*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ten

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos.

_____

10

.....Yayi kusan sau fin huɗu sannan ya dawo ya zauna. Cikin kaushin murya da dakewa ya furta, “Dole ne yarinyar nan ta mutu a asibitinki. Kuma a yau zuwa gobe nake buƙatar sanin daga inda ta fito? Miye dalilin Mashi'a na kawota?. Zaki cigaba da riƙeta har zuwa kwanaki uku da za'a gama min bincike na”.

Idanu Hajiya Ƙarama ta zubama mutumin zuciyarta na gudu da sauri-sauri a ƙirjinta. Cikin ɗan rawar lips muryarta na seizing ta ce, “Amma yallaɓai hakan fa zai

iya zama kuskure. Dan yarinyar nan gaba ɗaya komanta ya gama dai-daita raunin daya jimata ne kawai ya rage ya ƙarasa warkewa mu sallameta zuwa gobe idan ALLAH ya kaimu ko jibi. Sannan case ɗinta bama fa a hannuna yake ba doctor Larai ce ke kula da ita. Daɗin daɗawa Awwab. Yaron nan fa ya wuce duk inda kake zato da tsammanin sa kaima ka sani. Ni wlhy zuciyata ma ta fara bani kamar a ankare yake da abubuwa da yawa. Gashi sam baya jin tsoro ko shakkar kowa. Yanzu ka dubafa yarinyar mutane yama fyaɗe a cikin gidansu amma komansa bai canja ba face ma wani irin kulawa da yake bata ga girman kai sabo da yake ji da sam na gagara fassara al'amarin nasu".

"Mtsooww Lawusa, ke kin san dai idan na faɗi magana ko zartar da hukunci bana canjawa ko? Dukan waɗan nan hujjojin naki basa gabana. Gawar yarinyar nan kawai nake buƙatar gani fine and done". Ya ƙare maganar a wani irin hankali yana zazzaro mata idanunsa da sukai mugun kaɗawa saboda giyar da yake ta faman lodama cikinsa tun kan tazo. Yawu masu kauri ta haɗiye. Sai kuma ta shiga jinjina kanta. "Okay shike nan naji zan kashe yarinya bayan ansan wacece. Sai dai fa kaima ya kamata ka tuna lokaci yayi da zaka yi komai a wuce wajen. Nifa ina buƙatar shares ɗina, dan lokaci yayi da zan mora wahalata ta shekaru gaskiya. Tunda ba ƙuruciya nake ƙarawa ba. Yaron can Fahad banga amfanin saba ai, shima ya cancanci mutuwa. Sannan magana ta gaskiya mahaukaciyar matar nan na gaji da shiga da fita ina shan warin sashen ta itama. Ya kamata kayi wani abu, dan nasan dai zuwa yanzu kaima ka fanshe dukan alƙawarinka da alwashinka a kanta. Kaga sai muje next target wato Awwab. Dan Doctor Ram ya tabbatar min ko a yau muke son poison ɗin nan a shirye yake da aiko mana shi Nigeria."

Iska mutumin da tunda ta fara maganar ke kallonta yake ta faman furzarwa. Sai da ta kai har ƙarshe kafin ya ɗauka kofin giyarsa ya kai baki, ƙarasa shanye wanda ya rage a ciki yayi ya dire glass cup ɗin a saman Centre table ɗin gabansa yana wani girgiza kansa. Sai kuma ya maido jajayen idanunsa ya zuba mata. "Dont warry Lawusa. Komai da kika sani a tsare yana nan bai canja ba. Sai ma ƙarin shares da kowannen mu ya samu sakamakon sake hauhawar dukiyar nan. Dan yaron nan ba ƙaramin mahaukacin arziƙi ya tara mana ba. Shiyyasa nake son ki fahimceni akan kashe yarinyar nan. Dan sam na kasa jin nutsuwa akan barinta raye tun kan nasan wacece ita. Kije ki ƙarasa aikin ki a next zama zaki ji mina tsara game da Fahad ɗin shima".

"Shike nan yallaɓai ALLAH ya ƙara lafiya da nisan kwana. Na barka lafiya a huta gajiya".

Hannu kawai ya ɗaga mata da maida idanunsa luuu ya rufe cikin mayen barcin buguwar da yayi.....

Iska ta furzar mai zafin gaske. Tare da tura hannunta cikin hular kanta. A take hular ta zame ta faɗi, gashinta mai ƙarancin tsayi da cika ya bayyana. Bata damu

ba, dan abinda ya dame ta shi ya dameta. Tunda ta haɗu da Yallaɓai bai taɓa saka mata doka ko sanyata aiki ta gagara yinsa ba, saboda ra'ayinsu bai taɓa banbanta ba. Sai dai a wannan gaɓar an samu akasi. Dan yallaɓai ya sakata yin aikin da ita kanta tasan idan tayisa sai ta cutu. Matuƙar cutuwa. Domin kuwa ita kaɗai tasan irin son da takema yarinyar nan with all her heart. Duk da tana jin zafin abinda shegen yaron nan mai kama da ɗanyen attaruhu yay mata ɗigon sonta bai ragu a zuciyarta ba. Jinta take a yanda ta jure kwanakin baya akanta yanzu bazata iya ba. Dan wani irin mayataccen buƙatar son kasancewa da ita takeyi. A jiya kaɗan ya rage tabi dare a asibitin ta lalubeta. Sai dai ba haka take so ba. Tafi son su mori juna yanda ya kamata. Dan tana jinta a ranta banban da sauran waɗanda ta mu'amalata daga fara wannan harkar zuwa yanzun. Yarinyar akwai kayan marmari fresh a jikinta matuƙa da har wani sashe na zuciyarta na ƙin ganin bebekin Awwab akan abinda yay mata. Yo ita mace ma ta kasa nutsuwa balle shi namiji mai ji da shekarun ƙuruciya da hutu. Sosai tana jinta a tsaka me wuya...

“Yau ma wani ɗinne ya mutu da kika kasa nutsuwa?”.

Firgigit ta dawo hankalinta tare da juyawa tana kallonsa. Shima kallonta yake fuska babu yabo babu fallasa. Paah ya sake watsa mata kallo murya a kausashe ya furta, “Dan iskanci kinzo nan kin shanyani bayan ina can ina jiran ki kawo min coffee”.

Ajiyar zuciya Hajiya ƙarama ta sauke da ƙoƙarin controlling kanta. A hankali ta saki murmushi tare da canja yanayinta like she is innocent woman, cikin kwantar da murya ta ce, “Kayi haƙuri Abban Awwab. Ƙafata ce fa ta riƙe daga fitowa a bayi shine nake ɗan mammotsata. Amma wlhy kana raina tunda naga lokacin shan coffee ɗinka yayi. Amma ganin baka kirani ba yasa nai tunanin ko baku dawo daga masallaci bane”.

“Tunda nine limamin masallacin ba”.

Ya faɗa a gatsine cike da sake tunzura. Sake kwantar da murya tayi da shiga bashi haƙuri. Uffan bai sake cemata ba ya fita fuuuu yana harare-harare dan dama borin kunya ne kawai ya naɗe da hauka. Tun ɗazun yana a garden ɗin Maash tare da Siyama suna holewarsu. Dan tunda ya fahimci Maash baya gidan ya tura mata saƙo a waya kan ta samesa a garden ɗin Kasancewar yasan anan ɗine zasu iya zama safe fiye da ko'ina a gidan irin wannan lokacin. Sai yanzu ne yake fitowa dan yasan duk inda Awwab yake yana gab da dawowa gidan....

Itama da kallon harara ta bisa. Kafin taja tsaki da faɗin, “Nadai kusan yarda ƙwallon mangwaro na huta da ƙuda stupid man. Dan ɗauke beauty yarinyar nan zanyi mubar ƙasar zuwa can muyi aurenmu mu more rayuwar mu. (Umarnin yallaɓai fa?) Zuciyarta ta ayyana mata. Kanta dake wani irin sara mata ta dafe kawai zuciyarta na bugawa da sauri-sauri. Lallai dole ne tasan mafita a daren yau basai gobe ba. Dan tafi kowa sanin wanene yallaɓai akan duk abinda ya sa gaba. Amma bari taje ta bama wannan sakaran coffee dai ta dawo.....

(Tofa □ kaji kuma wani lissafin □□)

□□□□□

A gidan Abba Imamu rayuwa ta matuƙar juyama Mom baya. Dan sam ta kasa gane komai akan al'amarin Halime. Yarinya ce shu'uma matuƙa. Ga kalolin baƙin ciki da take tura mata iri daban-daban. Yanzu har takai Abba ya sallami mai aiki yace kowa tai aikinta ranar girkinta. Mom son jiki, Bibaa da Baby basu iya komai ba. Sai yazam a gidan duk ranar aikin Mom yini ake da yunwa, dan ko anyi abincin da wahala ya ciyu. Daga ƙarshe su ƙare da rigima ita da Abba. Dan ya tabbatar mata shi kam bazai ɗauki wannan banzan halin ba da almabazarancin abinci. Ashe da can duk wahalar gyaran gidan da abinci dama Samraah ce keyi ita kaɗai nata yaƴan na kwance. To ta sani bata cutar masa ɗiyar yar uwa ba kanta ta cuta. Dan ba baki ya mata ba yaƴanta in har a haka zata kaisu gidan miji to ta shirya kuwa za'a dinga koro mata su. Wannan magana tasa ta ƙona mata rai a ranar sai da suka tafka rigima sosai data kaisa da bata wan shika. Aiko dai tace babu inda zata. Kota kanta baibi ba yay ficewarsa.

Sam Halime bama tasan abinda ke faruwa ba ita. Dan kwanakin nan gaba ɗaya bata ganema kanta. Kullum bata da aiki sai barci, itama dai aikin gidan a ranar girkin nata ƙarfin hali kawai take yi wajen yinsa. Sai yamma taji zazzaɓi yace salamu alaikum. Bazata taɓa samun nutsuwa ba sai irin sha ɗayan nan na dare. A yau ɗin ma da aka tafka rigimar har ya bama Mom sakin tana barci bata san bikin da akeyi ba. Amma mi, Bibaa da Baby na ganin Abban ya fita suka afka ɗakin Halimen wai zasu daketa. Sun san itace ke ƙullama Mom ɗinsu munafunci. Miye-miye dai magana tsaff a bakunansu. Cikin barci kawai Halime taji an sauke mata uban dundu. A firgice ta farka tare da sakin ihu. Sai kuma ta tsaya cak ganin Bibaa da Baby tsaye kanta suna huci. Kallon mamaki ta bisu da shi, sai kuma ta tashi da ƙyau cikin dakewa ta tambayesu ko lafiya?.

“Uwarki zamu ci, shegiya annoba. Wlhy yau sai mun miki jina-jina a gidan nan dan ubanki”.

“Tofa babbar magana, wai kishiya taga abin cikin zanen kishiyarta”. Halime ta faɗa tana yayimar ɗan kwalinta ta aza bisa kai tare da sakkowa a gado. Waya ta ɗauka tana cigaba da faɗin, “Ai ku jira bani kaɗai ya kamata ku cima uwar ba, dole na kira Imamu kamar abin zaifi armashi. Kunga sai ku tuɓe ƙaton banza ku haɗamu ku lakaɗa mana dukan tsiya tunda shine ya kawoni gidan”.

Sororo Baby da Bibaa sukai suna kallonta. Kafin cikin ƙarfi hali da tsiwa Bibaa ta ce, “Badan Abbanmu ne ƙaton banza ba dan ubanki. Sai dai idan kece ƙatuwar banza. Kuma wIhy yau sai kin ban mana gidanmu”.

Dariya sosai Halime ta sheƙe da shi, kafin ta riƙe haɓa da faɗin, “Oh ni Halimatu. Gidanku dai gidanku dai. To ke banda abinki Habi wace sakarar mace ke alfahari da gidan tsohonta? Ai macen data kai mace gidan mijinta take ma fata da alfahari, dan acan ne idan ta tadda komai rigijif-jif-jif sai kiga ta gyara gidansu albarkar iyaye ta bata tsaro tako ina. Dan haka riƙe cika bakin nan naki wannan gidan Halime ne da Jalilah, Habi dai har yanzu bata da gida sai na raɓe-raɓe. Garama ita wannan galwalin ta kusa shiga daga ciki”. Tai maganar tana nuna Baby..

Cikin fusata Baby tace, “Waye Galwali? Aiko yau sai na tabbatar miki na fiki hauka da tashanci”. Fuuu tayo kan Halime.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eleven

11

.....Kafinma ta kai hannu kanta ita ta ɗauke fuskar Baby da maruka. Ta shaƙo wuyan Bibaa dake bayanta itama ta bata nata. Basu gama dawowa a hayyacinsu ba ta shiga musu dukan kan mai uwa da wabi. Yo har a gayawa Halime iya danbe. Ita da ake kira giwar dambe a wajen ɗibar ruwa a garinsu. Kai hatta a islamiyya duk wanda ya sake ta haɗosu da Halime aka haɗu a lungun kaci uwaka bayan an tashi to ranar kuwa sai yaci uwar tasa. Cikin ƙanƙanin lokaci ta musu lis da duka. Sai gasu

a ƙasa suna faman ribzar kuka. Itako ta ɗauki sabuwar wayarta da Abba ya siya mata kwanan nan tayi kiransa tana kuka wai yazo gasu Baby da taɓare zasu bigeta.

Bawan ALLAH sai gashi a haukace harda Alhaji Sadisu. Suka ko sameta kwance tana ɗan nishi ita adole ga wadda taci duka. Gashi ta kawo jan baki ta ɗan sassaka a wasu wurare na fuskarta da hannu wai duk sayin duka ne. Abinka da fara saika ɗauka haka ɗinne. Ido rufe Abba ya dinga sauke musu maruka abinda bai taɓa koda kwatanta yi ba. Sai dai ma idan Mom ta zugashi akan Samraah yana mata faɗa ita yana marinta suna dariya. Haukace masa Mom tayi da kuka da ihu, amma ada idan ta zuga aka mari Samraah daɗi take ji, ya kuma tabbatar mata idan har ta matso shi sai ya ƙara tsinke igiyar aurensu data rage. Dole taja birki tana kuka sai Alhaji Sadisu ne ya amshesu da ƙyar. Amma sai da yay musu lilis da duka ga wanda Halime tayi musu. Ya kuma tabbatar da ya matso da auren Baby nanda ranar juma'a ko daga shi sai mutanen anguwa ne za'a ɗaura ta tafi haka dan ta ishesa. Itama kuma Bibaan idan bata kama kanta ba zai aurar da ita ga duk wanda ya masa babu abinda ya shallesa da wani karatunta. Haka suka dinga kuka. Shiko ya kama Halimensa sukai ɗaki yana lallashi. Sai dai ita kuma duk jikinta yayi sanyi, dan harga ALLAH batayi zaton zai dakesu haka ba. Ita kawai tayi ne a tunaninta faɗa kawai zai musu a wuce wajen. Koda suka shiga ɗaki sai ta kasa haƙuri ta fito ta sanar masa gaskiyar abinda ya faru harda dukan datai musu. Tama nuna masa video data ɗauka dan sanda tace zata kirashi da farko bashi ɗin ta kiraba ashe video tajeyi.

Wannan halin nata shine abu na farko da yake sakashi jin ƙaunarta fiye da koda yaushe. Dan a ɗan zamansu sam ya fahimci Halime bata iya ƙarya ba. Sannan bata taɓa kawo masa ƙarar Mom ta mata wani abu a gidan ba idan baya nan kosu yaran sun mata. Sai dai ita Mom ɗin ta tonama kanta da kanta asiri ta hanyar gaya masa. Shiyyasa yau data kirashi ya taho a rikice. Amma Mom wani lokacin ma tun suna rigimar take kiransa ta sanar masa ƙarya da gaskiya cikin kunfar baki. Idan ya dawo gida yana jiran yaji Halime tace wani abu sai yaji shiru, ko yama samu tana firinfijimarta a gidan hankali kwance tamkar komai bai faru ba. Dan ita in har akwai wuta tv na kunne shikenan tace bata da sauran takaici a duniya. Balle ta haɗa uban shayinta cikin ƙaton kofi da burodi ta soya ƙwai ta zauna tana sha tana kallo ai ji take duniya babu ya ita. Har da rana da yamma shan shayi take saboda masifar ƙaunarsa da takeyi tun tana ƙaramarta. Abinci ma bai cika damunta ba in dai akwai shayi da burodi balle ga madara a ciki yaji da sauran kayan shayi ace kuma akwai soyayyen ƙwai wayyo jinta take kamar a aljanna. Yasha gwadata akan magana da Mom take sanar masa game da ita. Amma mutuniyar sai ta basar tama nuna ita yaushe akayi hakan, idan ma anyi to ta manta. Koda yake harga ALLAH bawai tanayi don makirci bane ko wani abu. Kawai ita har cikin ranta da halayenta da anyi abu ya wuce shikenan kawai sai wani ya taso kuma. Wannan dai ta gama da babinsa. Idan ko har kakaga Halime ta riƙe abu a rai ya dameta to lallai al'amarin babbane matuƙa. Dan wahalar data sha a hannun innarta da ace tana riƙewa a rai da tuni hawan jini da ciwon zuciya sun kai rayuwar yarinyar ƙasa....

❤❤❤❤❤

Ƙarfe sha ɗaya da wasu mintuna suke shigowa gidan. Har gaban dashensa TJ ya faka motar, da sauri Shu'aibu ya fito ya buɗe masa. Koda ya fita maimakon shiga sashen nasa sai ya koma ainahin ƙofar shiga babban sashen gidan. Babu kowa a falon sai Azizat dake dakon jiran dawowarsa. Yana shigowa kuwa ta miƙe zambar. Fuskarta ɗauke da murmushi ta nufosa tana masa sannu da zuwa cike da shagwaɓa. Sai da tazo gab da shi ya wani watsa mata mummunan kallo yayi wucewarsa upstairs. Kai tsaye sashen Ummie ya nufa ya barta nan tsaye baki sake tana binsa da kallo ga hawaye na gudu a fuskarta. Sai kuma ta kwasa da gudu tai sashen Hajiya Mammah itama. Sai dai tana murɗa ƙofar bedroom ɗin ta tajita a rufe gamm. Jingina tayi jikin ƙofar tana sake fashewa da kuka. Sai kuma wani ɗan nishi-nishi da take juyowa kamar daga cikin bedroom ɗin ya sata fara sassauta kukan nata tai tsai alamar saurare. Tabbas daga ɗakin mahaifiyar tata ne. Knocking ƙofar ta farayi da kiran sunan ta amma babu alamar za'a buɗe, sai dai kamar anyi shiru an daina nishin. Sake fashewa tayi da kuka tare da barin jikin ƙofar da gudu tai ɗakinta.

Wata shegiyar dariya Arwa dake laɓe tun ɗazun tana kallonta dan komai akan idonta ya faru ta saki, sai kuma cike da farin ciki ta furta, “Iska na wahalar da mai kayan kara” ta juya cike da takun girgiza jiki ta koma nata ɗakin dake a sashen uwarta Hajiya ƙarama. Dan su dukansu kowanne a sashen mahaifiyarsa yake har suma su Malika....

★ A ɓangaren Maash kuwa bai wani jima ba a sashen Ummie ya fito, dan ya samu tana barci ne alamar sauki na samuwa. Baya buƙatar wata matsalar ta sake samuwa a dalilin shigowar tasa dan haka ya juya ya fita a kan lokaci. Har zai wuce sai kuma yay tunanin shiga sashen Paah dan akwai maganar da yake sun suyi. Gobe in ALLAH ya kaimu kuma ya sanar masa da baƙi da zaiyi da wuri zai fita a gidan ba lallai su haɗu ba. Sashen Paah ɗin ya nufa da tunanin shi kaɗaine dan yasan da wahala Hajiya ƙarama idan tana a gidan kasancewar ya ganta a asibiti ɗazun. Knocking yay har sau biyu amma baiji motsin komai ba. Yasan Paah da kallon labarai yanzu haka hankalinsa nacan baima jisa ba. Dan barci dai yanada tabbacin baiyisa ba zuwa yanzun kam. Kansa tsaye ya tura ƙofar ya shiga kawai, sai dai kuma da saurin tsiya ya tsaya cak dai-dai yana ɗaga kafarsa zaiyi taku kusan na biyar a cikin falon sakamakon furucin da Paah ɗin yayi waya a kunnensa. Da ƙarfi yaja numfashinsa da ke neman fisgewa daga cikin ƙirjinsa. A wani irin harzuƙe da kaushin harshe ya furta, “Paah!!”.

A bala'in rikice Paah ya juyo tare da sakin wayar ƙasa yan zazzaro idanunsa. Fuuuu Maash ya juya ya fice a falon tare da bugo masa ƙofar da masifar ƙarfi har sai da ya zabura. “ Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un”. Ya shiga maimaitawa cikin tashin hankali. Shi ya haifi Awwab, amma wIhy zai iya rantsuwa da baya jin tsoron wani sama da yanda yake shakkar yaron nan. Kai hatta Baba prof daya haifesa baya jin yana shakkarsa kamar Muhammad. Koda wasa baya son Muhammad ya kamasa da wani laifi musamman akan abinda za'ace ya shafi mahaifiyarsa koda kuwa ɗan kaɗan ne...

Sashen Maash ɗin Paah ya nufa a ɗarare cikin kuma tashin hankali, dan Gara yaje suyita kawai baya son ya ɗauki fushin nan da shi. Kasancewar ta ainahin ƙofar shiga sashen ya fita yabi kansa tsaye ya shiga. Shu'aibu ya samu a falo da TJ. Cikin girmamawa suka shiga gaidashi. Da ƙyar ya iya danne yanayinsa ya amsa musu. Kafin ya ɗora da tambayar ogan nasu. Kai tsaye TJ ya amsa masa da, “Alhaji yana ciki”.

“Okay to bari na gansa ko?”.

Da girmamawa suka amsa masa da to. Shi kuma yay gaba kai tsaye sashen bedrooms ɗin Maash, suma sai suka fice dama abubuwan da suka dawo da shi a mota suka shigo da su ciki. A bedroom ɗin da yafi ƙyautata zaton samunsa yay knocking. Kusan mintuna biyu aka buɗe ƙofar. Ɗan zuba masa idanu Maash dake ɗaure da towel jikinsa na raɓar ruwa alamar daga wanka ya fito yayi. Sai kuma ya ɗauke kansa fuskarsa na sake zama kicin-kicin. Batare da ya ce komai ba ya saki ƙofar ya juya ciki. Bin bayansa Paah ɗin yay shima, a bakin katafaren gadonsa ya zauna, yayinda shi kuma yake daga ɗan lungun closet ɗin sa yana ƙoƙarin zira jallaniya fara tass mai gajeren hannu. Fuskarsa a tsananin ɗaure ya sake fitowa. Batare daya kalli Paah ɗin ba ya jingina da mirror daga tsaye yana kallon wani gefen. Kaɗan ya motsa lips ɗinsa wajen faɗin, “Good Evening”.

Karan farko Paah ya saki murmushin ƙarfin hali, sai kuma ya amsa da, “Evening dear, how are you?”.

Shiru Maash bai amsa masa ba. Sai ma ƙara ɗauke kansa da yay gefe. Shiru ɗakin shima Paah bai sake magana ba yana ƙulla ta inda zai fara. Kafin ya nisa a hankali ya sake furta. “Muhammad magana nazo muyi”.

“Ina jinka”.

Ya amsa masa a daƙile. Kai kawai Paah ya girgiza. Sai kuma ya cigaba da faɗin, “Kana fushi da ni ko? Akan abinda kaji ina faɗa. Haba Muhammad, kafa san yanda nake ƙaunar Ummu-Hidaya. Taya zan iya wofantar da ita saboda ta samu lalura”.

“Paah ka faɗi abinda ya kawoka kai tsaye Please”. Maash ya katsesa cikin zafin rai.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twelve

12

.....Zuru Paah yay masa yana kallo, sai kuma ya haɗiye yawu masu kauri yana jinjina kansa. “Muhammad wai sai yaushe zaka yarda dani akan mahaifiyarka ne? Kʼarshen maganata da kawai kaji baka san akan mi nakeyi ba, ba kuma kasan dawa nake yi ba”.

Fuska sosai Maash ya yamutse ransa na ƙara masa suya akan halin mahaifin nasa. Duk yanda yaso danne kar ya biye masa bazai iya ba, a fusace ya bashi amsa da, “Sai randa ka canja Paah. Sai randa ka ajiye son zuciya ka tuna da halacci. Bazan hanaka yin dukkan abinda kai niyya ba. Sai dai wlhy ina gab da ɗaukar mummunan mataki. Sannan yaronka na bashi nan da kwana uku ya sallami waɗan nan yʼan iskan yaran daya tara min a company, idan ba hakaba duk wani mai alaƙa dasu ya kuka da kansa. Kuma shima ya ajiye aiki da hannunsa kar ya bari na ziyarci Company yana ciki”

Cikin ɓacin rai da tsarguwa Paah ya ce, “Muhammad kana zargina ne?”.

Shiru yay yaƙi tankawa. Sai da Paah ya miƙe zuwa gabansa. Cikin sauke murya ya sake furta, “Muhammad miyyasa kai baka yafiya ne? Miyyasa kake da riƙo? Sai yaushe zaka yarda dani? Dan kawai kaji ina waya sai ka fasaarata da wata siga daban har kana tunanin sallamar waɗanda basu ji ba basu gani ba daga aiki”.

“Sai randa ka daina saka wannan ɗan iskan yaron na maka kawalcin yara ana kawosu da sunan wai ma'aikata. Paah na sanka fiye da yanda nasan kaina. Dama na jima ina zargin waɗan nan yaran zaman iskanci suke min a company. To wlhy na basu daga daren yau zuwa gobe su koma inda suka fito, in ma gidan karuwai zaka buɗe musu bai shafeni ba rayuwarka ce”.

Rumtse idanu Paah yayi da ƙarfi. Sosai kalaman ɗan nasa ke masa amsa kuwwa a cikin kunne. Yasan wanene Awwab idan yay fushi. Sam baya tauna magana yayin faɗarta balle shakka. Jin alamar zai bar wajen ya sashi buɗe idanunsa. Cikin ɓacin rai ya dakatar da shi da faɗin, “Miyasa baka tauna magana yayin furtata? Ina matsayin mahaifinka amma baka shakkar tauna magana yayin furta min ita. Komai ya zo maka a rai saika yaɓosa waje”

A daƙile da yanayin zafin rai shima Maash ya furta, “Ni ɗankane bani da hurimin hanaka duk abinda ka tsarama rayuwarka kam. Amma ka sani bazan iya cigaba da jurar ganin kana kana takamin mahaifiya a ƙarƙashin takalman ƙafarka ba Paah. Abinda na ɗauka kafin yanzu bazan iya ɗaukarsaba a yanzu. Idan da kace rashin mace ke saka aikata abinda kake aikatawa yanzu minene hujjarka kuma tunda kana da wata matar? Kai da kanka kamin alƙawarin dainawa, ashe baka fasa ɗin ba. Idan mace ɗaya ta maka kaɗan ka ƙara auren mana. Ka ƙaro uku su zama huɗu yafi min wannan mummunar ɗabi'ar taka mai zubar da mutunci ga zunubi wajen UBANGIJI.....” ya ƙare maganar cikin ƙaraji dasa hannu ya watso kayan saman mirror ɗinsa gaba ɗaya. Sai kuma ya kaima mirror ɗin naushi, a take kuwa ya shiga tsatstsagewa. Sake kai masa wani naushin yayi, ya kuma tsagewa tare da jimasa ciwo. Sai ga saman yatsunsa duk jini ya ɓata. Da sauri Paah ya kamo hannun nasa jikinsa har rawa yake. Amma Maash ɗin sai ƙoƙarin ƙwacewa yake yi. Dan so yake kawai ya ƙara kaima mirror ɗin duka ko zai samu sauƙin zugin da zuciyarsa ke masa...

“Please sweetheart relax. Dan ALLAH try to calm down. Jifa yanda kake jima kanka ciwo Muhammad”.

“Is not your business Paah. I beg you leave me alone”.

“Naƙi ɗin, nace maƙi na barkan! Miyasa kake da zuciya ne Muhammad. Fushinka yayi yawa. Taya zan Barka ka cigaba da jima kanka ciwo. Nace kayi haƙuri! Haba Muhammad”. Ya ƙare maganar cikin sanyin murya tare da jawoshi jikinsa ya rungume. Abinka da su duka dogaye, sai gasu kai ɗaya. Ƙarfi da cikar zati kawai Maash zai nuna masa saboda shi yana akan ƙuruciyarsa, shiko koba komai girma ya kamashi.

Luff Maash yayi a jikin mahaifin nasa, sai faman sauke zafafan ajiyar zuciya yake a jajjere. Yayinda Paah ke jin yanda zuciyar tasa ke gudu da ƙarfi. Sunfi mintuna uku a haka sannan ya ɗagosa. Kama hannun nasa yay suka nufi wajen gadon, zaunar dashi yay sannan yaje ya ɗakko first aid box ya dawo kusa da shi ya zauna. Hannun nasa dake ta tsatstsafo da jini ya kamo, cike da kulawa ya fara masa treating. Ko sau ɗaya Maash bai motsa ba, bai kuma kalla mahaifin nashi ba har ya kammala ya naɗe masa da bandage. Zama yay zai fara magana Maash ɗin kawai ya miƙe, da sauri Paah ya riƙosa ya maida shi ya zaunar. Bai musa ba ya zauna, sai dai yaƙi kallonsa yanzu ma. Shiru Paah yay yana kallonsa, sai kuma ya sauke numfashi a hankali yana sake tattaro abinda yake son faɗar. “Muhammad kayi

haƙuri, tabbas nasan bana ƙyauta muku, sannan ban yima kaina adalci ba. Bazan kira abinda nake aikatawa da ƙaddara kawai ba, harda sa kai. Shiyyasa tabbas a rayuwa ka guji aikata mummunan aiki a ƙuruciya, idan kuma ya zama jarabawarka ce ka fara kayi gaggawar tuba. Idan ba haka ba wannan abin zai ta bibiyarka ne a lokacin girma, a lokacin da kuma kake son ka daina ɗin amma abin yabi jininka. Wannan maganar mahaifiyarka tasha faɗa min ita da maimaita min a duk sanda ta sameni a halin rashin gaskiya. Amma mi a lokacin bana gane karatunta, gani nake ai duk sanda na shirya zan iya dainawa". Yay murmushin takaici, mai nuna ainahin ciwon da yake ji a zuciyar yasa. Cikin ɗan yarfar da hannu ya cigaba da faɗin, "Abubuwa da yawa sun faru, wasu ma suna kan faruwa da ni kaina ban san adadi ba. Ni ne ya kamata ace na tsaya muku, amma sam ban taɓa yunƙurin hakan ba koda sau ɗaya. Hatta da rashin Fahad a kusa da mu yana damuna. Sai dai ban san taya zance komai ba. Muhammad! Banso ace halin da nake ciki yayi nason da zai shafeku ba kamar yanda mahaifiyarku tasha yin fata. Sai dai a wannan gaɓar na fahimci zancen nan na masu iya magana da kance TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE. Wlhy bazan ɓoye maka ba, case ɗinka akan yarinyar nan ya tsaya min ta yanda na kasa haɗiyeshi, sannan yanda kake bama yarinyar kulawa tamkar ba abinda ake gudu bane ya shiga tsakaninku na sake ɗaga min hankali. Bana son ace sunanka ya ɓaci a duniya Muhammad, wlhy bana son abinda wani zai aibantaka da shi, koda bazan ce komai ba ina jin zafi, matuƙar zafi a cikin zuciyata. Dan ALLAH ina roƙonka idan an sallami yarinyar nan daga asibiti gobe idan ALLAH ya kaimu zan haɗa mata sha-tara ta arziƙi tare da siya mata ticket ɗin jirgi idan ba ɣar cikin garin nan bace ta koma garinsu. Idan kuma a cikin garin nan take da iyayenta nasan zata iya yiwuwa a gidan haya suke ko wani muhalli ƙaskantacce. Zan saya musu gida a ɗaya daga cikin jihohin arewa su koma can, kar su sake waiwayar Lagos har abad...."

Karan farko Maash ya zuba masa idanun kawai yana masa wani irin kallo mai wahalar fassara. Kallon ne ya dinga ratsa Paah sai ya gagara ƙarasa abinda ya faro ya ja bakinsa kawai yayi shiru. Wani irin murmushin ƙasaita da ɓacin rai Maash yayi, sai kuma ya ce, "Ya kayi shiru kuma, ina jinka Paah."

"Saurarena kawai kake amma ba jina ba Muhammad abar maganar kawai". Ya faɗa cikin ɗan borin kunya da kame-kame. "Ka kwanta ka huta dare yayi, zuwa safiya sai mu ƙarasa, amma ka daina kira min ƙara aure har ma na mata uku, kai ka sakar min Ummu-Hidaya ɗin ne da kake cireta a matsayin matata". Ya sake faɗa yana nufar ƙofa cikin ɣar sassarfa ya fice. Tsahon lokaci Maash ya ɗauka yana kallon ƙofar kawai. Sai kuma ya cije lips ɗinsa da masifar ƙarfi zuciyarsa na masa wani irin suya. Yasan mahaifinsa fiye da sanin da kowa ya masa a rayuwa. Amma bazai ce komai ba ALLAH mai ji ne mai gani. Yana kuma roƙonsa ya shiryeshi...

Humm, kai dai Paah ALLAH ya shiryeka dai to gaskiya😊. Yayanmu kayi haƙuri mahaifi mahaifine koda na banza ne😭.

□□□□□

Tun wucewarsa daga asibitin abubuwa suka sake cinkushe min kai. Kalamansa sai faman maimaita kansu suke a cikin kaina. Duk da nasha magani zafin zazzaɓin nan yaƙi bari na. Zaune na tashi ina kallon Mama Balki da barci ya ɗan fara figa. Sai kuma na miƙe cikin sanɗa na nufi ƙofar fita.

“Samraah ina zaki je?”.

Muryar Mama Balki a bazata ta daki cikin kunnena. Cak na tsaya tare da runtse idanuna. Sai kuma na juyo a hankali cikin son wayancewa zanyi magana ta dakatar da ni.

“Baki iya ƙarya ba Samraah, kada ki farata yanzu”.

Sosai furucin nata ya dakeni, dan haka na sauke ajiyar zuciya tare da dawowa a hankali na koma saman gadon na zauna. Kaina a ƙasa ina wasa da yatsun hanuna nace, “Kiyi haƙuri Mama. Ba wani abu zanyi ba. Reception zanje na samo pen da takarda zanyi amfani da su”.

“Amma a daren nan Samraah. Na kula tunda Alhaji ƙarami ya tafi baki da nutsuwa. Bana fatan ace kina son samo takarda da biron ne dan kiyi rubutun da zaki bar masa ki gudu”.

A karo na farko nayi murmushi tare da girgiza mata kaina. “Haba Mama, ai a yanzu wlhy koda shine da kansa yace na tafi gidanmu bazan je ba. Dan insha ALLAHU sai na sauke alkawarin dana ɗauka akan Ummie. Kawai zanyi amfani da sune dan ina son yin lissafi dalla-dalla. Ba kuma zai yiwu a cikin ƙwaƙwalwa ba dole sai da taswira a rubuce”.

Ajiyar zuciya Mama ta sauke. Batare da tambayata abinda zanyin ba ta miƙe. “Shike nan ki zauna ni bari na fita na samo miki. Kin san dai ba'a son ki yawaita motse-motse mai ƙarfi saboda ɗinkin jikinki”.

Bance mata komai ba sai duƙar da kaina dana sake yi. Itama sai ta fice abinta bayan ta zumbula Hijjab ɗin ta.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

*_Typing□*_Typing□_*

*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forteen

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

14

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

_____

.....Lokacin da suka iso airport ɗin su duka sai da ƙwalla ya cika musu idanu. Dan abune da basu taɓa zato ko tsammani ba a rayuwarsu. Sune yau da hawa jirgi daga Kano zuwa Lagos. UBANGIJI al-musawirru mai sassauya al'amura a sanda yaso ga kuma wanda yaso. Da suka shiga jirgin sai Hafizzullah ya rungume yayan nasa yana hawaye. Dole shi ya haɗiye nasa ya dinga lallashinsa. Bayan yayi shiru kuma ya dinga musu video wai dolene ya nunama Aunty Samraah yau sun hau jirgi. Dariya Musaddiq ya dinga masa har ALLAH ya saukesu lafiya garin Lagos. Sunyi mamakin ganin zuƙeƙiyar motar da tazo ɗaukarsu. Amma sai Musaddiq bai kawo komai a ransa ba tuna cewa dafa companyn Maash yake aiki, mai lamba ta ɗaya a Africa, na uku a duniya a matasa. Ai hakan ba komai bane ba. Sunyi da MD dama motar company zata daukesu daga airport ta kaisu duk inda zai je, sannan idan ya kammala gobe idan ALLAH ya kaimu zai kira aje can gidan ɣar uwar tasa a ɗaukesa zuwa wajen GM, daga nan zai wuce kuma....

□□□□□

Kamar kullum alarm ɗinsa ne ya tashesa. Hannu ya kai idanunsa a rufe ya lalubosa a saman side drawer ya danne wajen kashewar dan shifa ko yaya ƙara take damun rayuwarsa take. Shiyyasa bazaka taɓa ganin wayarsa da ringing ton ba. Kullum cikin vibration phones ɗinsa suke. Hakama television da wahala kiji ya buɗeta caaa tana surutu. Cikin mayen barcin da bai gama isarsa ba ya nufi toilet. Sai da yay wanka kamar yanda abun ke neman zame masa sabo saboda mafarki duk da ba kullum yake tashi a irin yanayin ba sannan ya ɗauro alwala ya fito. A ɗan gurguje ya busar da kansa ya shimfida sallaya yay raka'atainul fijir sannan ya fice masallaci. Ana idar da salla bai yarda sun haɗu da Paah ko Uncle Abdullahi ba ya dawo gidan. Jallabiyarsa ya zare ya ɗauka sports wear ya saka masu kalar blue da rashin white. Sosai kayan sukai masa ƙyau duk da baya sakasu ne domin kwalliya ba. Ya kama gashinsa ya haɗe a tsakkiya tare da ɗauresa da siririn baƙin band. Duk da gudu zai fita sai da ya sakama jikinsa turare ya maƙala bluetooth a kunensa sannan yay zaman saka takalma spots na companyn nike. Yana fitowa falo Laalah dake kwance ya miƙe ya nufosa. Kansa ya shafa cikin lumshe idanu da silent voice ɗin nan tasa ya furta, “Let's go my friend”. Cikin kaɗa bindi kuwa ya bisa abin cike da mamaki. Daka gansu kasan karen ya gama samun training na musamman a hannun uban gidan nashi. Gashi fari tass babu alamar wani dattin ƙazanta a tare da shi. Wanda ma bai sani ba sai ya ɗauka ba kare bane saboda yanda jikinsa ke duguzum da gashi. Yana nufar gate da ɗan gudu Laalah biye da shi ƙafa da ƙafa

dan a jere suke tafiya su Sha'aibu dake zaman jiran fitowarsa na take musu baya suka fice yana ɗagama ma'aikatan daketa faman gaishesa hannu. Gudun ya fara tun daga wajen gate ɗin a hankali Laalah a gefensa guards ɗinsa biye da su. Haka suka miƙe street ɗin nan. Sosai sukayi nisa bana wasa ba. Jefi-jefi suna gamuwa da mutane da suma suka fito jogging ɗin. Hannu kawai suke ɗagama juna kowa ya wuce. Sai wasu ƴammata ne da suka dai-daita gudun kusan da shi dan suna a ɗan gabansa kaɗan amma ko kallo basu ishesa ba. Sunyi nisa sosai ya jiƙe sharkaf da zufa har yana ɗiga sannan suka sake juyowa bayan ya kalla agogon dake a tsintsiyar hannunsa. Suna isowa kwanar da zata sadasu da gida ya tsaya cak. Nuni yayima Shu'aibu daya bashi ruwa cikin sauke numfashi da sauri-sauri. Da sauri ya nufesa tare da ajiye ƴar jakar da abubuwan da zai buƙata ke'a ciki. Kamar su bottle water, towel da abinda ba'a rasa ba. Ruwan ya amsa ya buɗe murfin haɗaɗɗiyar bottle water ɗin ya kai bakinsa. Kansa ya ɗaga sama ya shiga kwararawa. Wani irin kaiwa da komawa maƙoshinsa ya shiga yi, illahirin ƙofifin gashin jikinsa na buɗewa zufa na fitowa da gudu. Sai da ya sha fin rabi sannan ya sauke gorar yana sauke numfarfashi. Laalah ya zubama kaɗan a jiki, shiko yay wani irin matsawa yana girgiza jiki. Yanda yay ɗin ne ya saka Maash ɗin sakin wani ɗan guntun murmushi yana sake kai goran bakinsa ya ɗan kurɓa sannan ya rufe ta ya miƙama Shu'aibu da suma duk suke shan nasu ruwan tare da masa alamar ya bashi towel. Da sauri ya miƙa masa fari tass ɗin towel ɗin hannunsa dake a linke. Sai da ya fara gogo wuyarsa zuwa gashi dake kwance a kumatunsa sannan yay magana batare da ya kalli su Shu'aibu ba.

“Kira Tijjani ya samemu anan da mota”.

Duk da a hankali yay maganar sarai Shu'aibu ya jisan. Sai dai yayi mamakin jin abinda yace ɗin. Amma bashi da hurumin musawa. Sai ma waya daya zaro yay kiran TJ ɗin. Cikin ƙanƙanin lokaci motocin biyu suka iso. Ta farkon aka buɗe masa ya shiga shi da Laalah. Ta bayan guards ɗinsa ne. Sai TJ da Shu'aibu a gaba tunda ba Hayatu. A ɗan ɗarare TJ ya ce, “Sir ina zamu je?”.

Shiru kamar bazai ce komai ba. Sai kuma can a ƙasan maƙoshi ya furta, “Hospital”.

Da girmamawa TJ ya amsa da, “An gama ranka ya daɗe” yana tada motar. Kansa kawai ya kwantar jikin kujera ya kumshe ido. Har lokacin zufa na faman tsatstsafo masa. Bai ɗago ba har sai da suka isa asibitin. Shu'aibu ya buɗe masa da sauri ya fito. Sai dai banda Laalah shi an barsa a motar. Cikin takun nan nasa ya nufi cikin asibitin Shu'aibu da TJ biye da shi. Tako ina tsirarun ma'aikatan cleaners da ma Nurses da sauransu sai kalonsu suke. Koda suka shiga reception tuni yammatan dake a kan katan sun miƙe bakunansu a washe suna masu Barka da zuwa idanunsu a kansu kamar tsoffin mayu. Ko kallo basu ishesa ba sai su TJ suka amsa musu...

Kuka na gama zabgama mama Balki akan nifa yau ko su sallamen daga asibitin nan kona gudu gida. Dan bazan sake kwana banje naga halin da Ummie ke a ciki ba. Lallashina taitayi akan nayi haƙuri jikina ya ƙara ƙyau tunda doctor tace sai nan da kwana biyu, jikin Ummie kuma da sauƙi sosai. Tirjewa nayi akan nifa sai na tafi. Ganin yanda nake zabga uban kuka yasa Maman cewa shike nan naje nayi wanka idan Alhaji Ƙarami yazo anjima itama zata sake masa magana da kanta. Badan naso ba nabi umarninta. Kamar kullum sai da ta fara taimaka min na shiga ruwan zafi na mintuna goma sha biyar zuwa ashirin da nake yi sau uku a rana. Sannan ta fito akan nayi wankan bara taje ta dawo.

Wankan na ƙarasa batare da tunanin kowa zai iya shigowa ba na fito ɗaure da towel kawai. Dan masu shara tun sanda zan shiga cikin ruwa Mama Balki ke cemin sun shigo aikinsu. Haka dama sukeyi, kullum tunda sassafe zaki gansu, wani lokacin ma ana idar da sallar asuba. Daga nan kuma sai da rana, sai kuma yamma. Fes kuwa na samu ɗakin harda turaren wuta sun kunna. Jikina na goge da ɗan hanzari. Bana son Mama Balki ta shigo ban saka kaya ba duk da nasan ko tazo ɗin tsayawa take bakin ƙofa sai ta tambayi na shirya sannan ta shigo, dan kunyarta nake ji matuƙa. Ƴar jakar kayanmu na buɗe na ciro b&p da zan saka dan ni ina amfani da kayan asibitin ne. Bra ɗin na fara ƙoƙarin sakawa da sauri-sauri, na saka hannu ɗaya ina ƙoƙarin saka ɗayan kawai ya zaro ta baya. Fuska na ɓata kamar zan fasa kuka, abinda dai nake gudun sai ya faru, tunda dole na jira Mama Balki tazo ta maƙala min ko kuma na cire na sake sakawa tazo ta sameni, amma bari muga na gwada dai kozan iya nawa ƙoƙarin. Kicin-kicin maidawa na fara ina famar cizar lips, sai kawai naji saukar lallausan hannu mai bala'in sanyi akan nawa dake riƙe da hannun bra ɗin. Tabbas wannan ba mama Balki bace, dan wani irin mayataccen ƙamshi ne ya shiga ratsa ƙofofin hancina. A birkice na juyo gaba ɗaya na nama manta da wani batun saurin da nakeyi. Saukar idanuna cikin lulu cat ɗin nashi ya sani ja baya jikina har tsuma yake. Shiko ko gezau, sai ma wani irin kallon ƙurilla yake bina da shi idanunsa a shanye. Inda naga ya kafama idanun nima na kalla da sauri, ai da sauri na naɗe hannayena a wajen ina tura baki kamar zan fasa kuka. Kafaɗa ya ɗan ɗage tare da taɓe baki irin shi baiga abin kallo ba, ina ƙoƙarin sake juya masa baya sai kawai ya shiga takowa a hankali. Baya na sake jan jikina yana cigaba da biyoni duk na ruɗe. Jin na dangane da abu yasa na juya da sauri na kalla, sai naga bangone, tashin hankali anzo the end kenan inji bature. Banda zaɓin daya wuce kawai na juya masa baya na kalla bangon. Idanuna a runtse murya na rawa na ce, “Wai da ALLAH minene haka kake yi? Ni dai ka fita kayafa zan saka, sai Mama ta shigo ta ganka”.

Maimakon amsa min ko ya fitan sai kawai naji ya saukar hannunsa akan kafaɗata, da ƙarfi na sake matse idanun nawa jin yanda yake wani irin tafiya da yatsun kamar mai yi da gayya.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifteen

15

.....Hannun bra ɗin ya maƙala min a inda ya zare, a tunanina zai matsa ne sai naji saɓanin hakan. Matsoni ya sake yi ta yanda har nake jin saukar numfashinsa a saman wuyana, sai kuma ya saƙalo hannun nasa ɗaya ta saman cikina. Yanda na sake matsewa a bangon bai hanashi jawoni baya ba a hankali, kansa ya ɗoro a saman kafaɗata tattausan gashin kumatunsa dake da laimar da nake ƙyautata zaton zufa ce tunda sports wear ne a jikinsa na gugar gefen fuskata. Ɗayan hannun ya ɗaura a saman nawa dake rufe da ƙirjina har yanzu zai zame, aiko naƙi yarda na sake ƙanƙamewa.

“Na cire towel ɗin kenan?”.

Soft voice ɗin sa dake fita low sosai cikin maƙoshi ta ratsa kunnuwana. Kaina na girgiza masa alamar a'a idanuna na cika da ƙwala.

“Oya remove your hand kona ciresa tas”.

Nasan zai iya, dan kaɗan daga ƙaramin aikinsa ne. Dan haka na shiga zamesu a hankali hawayen da nake maƙalewa na sake taruwa cikin idanun. Sake matsesu nayi jin yanda yake jan towel ɗin a hankali, har ya gama sauke b ɗin kan jikina babu kunya babu tsoron ALLAH ya gyarata ta zauna da ƙyau sannan ya maida min towel ɗin a sama.

“I love white musamman yanda wannan ta miki ƙyau”. Ya faɗa cikin kunnena cikin raɗa.

Da sauri na toshe kunnena tare da ture masa kai dan bana ma son ji. Maimakon ya barni kamar yanda naso sai ma ya sake nanne ni da jikinsa tare da sumbatar wuyana da hannun dana toshe kunnen. Ni kaɗai nasan kalar masifaffiyar kunyar da nake a ciki da mamakin tasa rashin kunyar dan shi komai yana yinsa ne kansa tsaye. Mun kai tsahon mintuna biyu a haka sannan ya janye jikinsa a nawa tare da kama hannuna. Ban buɗe idanuna ba, sai alamar zaunar dani da naji yayi a bakin gado. Jin kamar ya jawo kujera ya zauna gab dani dan har ƙafafunmu na a cikin na juna ne ya sani buɗe idanuna dake mar-mar. Kamar yanda nayi hasashen hakanne kuwa. Ya jawo kujera gab da ni ya zauna hannunsa ɗauke da rigar asibitin da aka ajiye min a saman gadon. Idanunsa kan p ɗin dana ajiye. A zabure na kai hannu na ɗauke ina ɓata fuska kamar zan yi kuka na cikukuyesa a hannuna na tura ƙarƙashin cinyata. Mayatattun idanunsa ya zuba min tare da motsa lips ɗinsa a hankali ya furta, “Hand”.

Bani da zaɓin daya wuce miƙa masan kawai, dan nasan ko cewa nayi bana so bazai barni ba. Inaji ina gani ya saka min rigar sannan ya miƙar dani a gabansa kamar wata ƴar yarinya ya zare towel ɗin ya ajiye gefe. Hannu ya miƙa min wai na bashi p ɗin dana sake saurin ɗaukewa. Kafaɗa na maƙe masa ina juyar da kaina gefe. shima sai ya taɓe nasa bakin kawai. Turaren dana ajiye gefe ya ɗauka ya ɗan duba jikinsa, sai kuma ya ɗan sake taɓe baki kaɗan, batare da yace komai ba ya ɗan fesa min ya maida ya ajiye. Ni dai uffan bance masa ba, kaina a ƙasa ina wasa da yatsun hannuna. So nake na tambayesa yaya Ummie amma duk ya dabaibaye ni da salon da ban taɓa zaton gani daga garesa ba. Gashi duk abin nan da yake fuskar nan na'a tsukenta kamar bashi keyi ba. Da ƙyar na iya dauriyar faɗin, “Ina kwana? Yaya jikin Ummie?”.

Jin shiru bai amsa ba ya sa na ɗago idanu na a hankali kamar wata matsoraciya. Kamar yanda nayi zato shima nasan a kaina suke, dan haka da gudu nai yunƙurin kauda nawa amma sai ya riƙo haɓata da yatsunsa biyu.

“Ina miki aiki bazama kince kin gode ba”.

Baki na tura masa. Cike da ƴar jarumtar dana tattaro a tsiwace nace, “To ni dai ai bance ina so ba”.

Maimakon ya bani amsa sai naga ya saki wani shegen murmushi. Cike da suɓutar baki da mamaki na ce, “Lah yau ma kayi murmushi”.

Janye hannunsa yayi, tare da tsuke fuskar. Ni sai ma abin ya bani dariya. Sai kace wani ɗan yaro. Dariya nayi ina ƙoƙarin kare bakina na ce, “Ikon ALLAH, to kai baka so ace kayi murmushin ne? Sai kace wani abun mugun abu. ALLAH idan ma kayi murmushin kafi ƙyau. Amma kullum fuska a ɗaure kamar wani ma'aikin mutuwa.” na ƙare maganar ina haurawa saman gadon gaba ɗaya tamkar banga irin kallon da yake faman bina da shi ba. Sai da naja bargon na rufe ƙafafuna sannan na kuma marairaice fuska. A hankali na ce, “Yaya Awwab!”. Shiru yaƙi amsa min, sake maimaita kiran sunan nashi nayi a shagwaɓe. “Yaya Please answer me”.

Nan ɗin ma kamar bazai amsa ba. Na sake ƙoƙarin yin maganar cikin harara ya katseni da faɗin, “Ba kunni ke ji ba ne”.

Baki na tura sosai. Na ce, “To ai dai ba daɗi mutum yayi magana aƙi amsa masa.”

Banza yay min bai tanka ba. Nima sai na cigaba da faɗin, “Dan ALLAH ka taimaka a sallaman yau a asibitin nan. Idan ba hakaba ALLAH zan gudo gida. Ina missing ɗin Ummie sosai. Ni wlhy na warke fa”.

“Na gani”.

Ya faɗa kamar bashi ba yana ƙoƙarin yaye bargon dana rufama ƙafafun nawa. Da sauri na waro idanuna ina riƙe hannunsa. Kaji mun mutum to mizai gani?. Shanyayun idanunsa ya ɗago ya zuba min, ni kuma na marairaice fuska har idanuna na tara ƙwalla. Hannun ya janye kawai batare da yace min komai ba. Nima sai na sauke ajiyar zuciya dan al'amarin wannan mutumin yasha kan nawa ƙaramin tunanin gaskiya. Sake matsar da kujerar da yake zaune yayi gaban side drawer. Batare da yace komai ba ya shiga ƙoƙarin haɗa tea dan akwai babban basket mai murfi dake cike da kayan shayi kala-kala da su chocolate da kullum Hayatu baya gajiya da sayowa. Yo ni Hayatu ai zance tunda dai shine ke zuwa da su. Banda jiya da bai zo ba ɗayan yaron nan nasa da har yanzu ban san sunansa ba ya kawo snacks. Tea ɗin ya haɗa a zatona shine zai sha, har na fara gulmarsa a zuciyata sai naga ya miƙa min mug ɗin. Tsayawa nayi kawai ina binsa da kallon mamaki, dan haka muka ƙurama juna ido. Kusan minti ɗaya muna a haka kafin ya janye nasa da suke juyewa golden ƙwayar tsakkiya na zama siririya a wani irin salon yuuu ya ɗan lunshe su. Nima nawan na ɗauke da sauri ina haɗiyar wani yawu mai kauri dan gaba ɗaya jinai maƙogwarona ma ya bushe. Kofin ya ƙara miƙamin kansa a gefe, sai kuma ya miƙe.

Haka kawai kallon nima yay matuƙar min tasiri a cikin jiki da ma jinina, dan haka na gagara sake kallon inda yake har ya buɗe ƙofar ya fita. Ajiyar zuciya mai nauyi na sauke tare da rumtse idanuna na cije lips da ƙarfi. Tea ɗin na cigaba da sha da ɗan zafi-zafi batare dana san abinda nake ba. A haka aka sake buɗe ƙofar, a zatona shine dan haka na gagara ɗaga ido na kalli wajen. Sai da mama Balki ta rangaɗa sallama sannan na ɗago da sauri fahimtar itace.

Inda nake ta ƙaraso cike da tsokana take faɗin, “A lallai ɗiyata ta fara samuwa. Yau kece da haɗa shayi da kanki batare dana sha fama ba kina bata fuska da korafin bakinki ba bu ɗanɗano. To UBANGIJI ya ƙara sauƙi.”

A hankali nace Amin, dan a zatona bata haɗu da wannan pepper ɗin mutumin ba, sai naji hakan yamun daɗi. Sai dai me, bayan kamar mintuna biyar da zaman Mama Balki sai gashi ya sake dawowa tare da doctor. Miƙewa Mama Balki tayi fuskarta ɗauke da murmushi tana faɗin, “Har an kammala Alhaji ƙarami?”.

Cikin girmamawa, muryansa can ƙasa ya ce, “Eh mama sai ku shirya”. Jin abinda ya faɗa ɗin ya sani ɗagowa da sauri na kallesa. Sai muka haɗa ido. Da gudu na janye nawa na maida kan doctor dake min magana ɗan ji nake kamar ma kowa zai gane abinda ya faru tsakaninmu yanzu. Tambayoyi tamun tare da bani shawarwarin yanda zan kula da jikina yanda ya kamata har komai ya ƙarasa dai-daita. Duk bayan kwanaki biyu kuma zata zo har gida koni nazo asibitin za'a dinga sake dubani. Dan ba yau suka so sallamata ba. Sake ɗagowa nayi da mamaki sashen da yake. Yana tsayen dai har yanzu sai Mama Balki ce ke fita da kayayyakin mu tana dawowa alamar a iya ƙofa ake amsarsu. Yanda ya maida hankalinsa akan wayar hannunsa sai naji nutsuwa da alama baya jin duk abinda doctor ɗin ke faɗa. Taimaka min doctor tayi na sakko a saman gadon, hannunta riƙe da nawa ta ce, “Muje ki ɗan tattaka ƙyaji daɗin ƙafafunki tunda kwana da kwanaki kina zaune waje ɗaya babu ko babban motsi. Kaina kawai na jinjina mata, ta ɗauki hijjab da Mama Balki ta ajiye sabo ta saka min da kanta. Har ƙasa hijjab ɗin ya kaimin kamar wanda nake amfani da su a gida. Sai naji daɗi sosai dan yaushe rabo. Ta gabansa mukazo muka gitta bai kallemu ba bai kuma motsa ba har sai da muka fice gaba sannan. Kusan ƴammatan Nurses ɗin nan da suka dinga kulawa dani dasu aka ɗunguma min rakkiya har gaban mota. Sosai motar tai min ƙyau, banyi tunanin yana bayanmu ba, sai da muka iso ina sallama da Nurses ɗin da doctor naga an buɗe masa ya shiga, ba'a rufe ƙofar ba alamar ni ake jira. Ji nai kamar na fasa kuka, dan hakan na nufin a kusa da shi zan zauna kenan. Babu yanda zanyi, dan doctor da kanta ta taimaka min na shiga. Sai da aka maida ƙofar aka rufe har Mama Balki itama ta shiga gaba an ma tada motar muna shirin barin asibitin sannan na lura da shegen karen nan nasa dake tacan jikin waccan ƙofar. Wani irin fasa ƙara nayi tare da daka tsalle na faɗa jikinsa a matuƙar firgice, bazaki gane yanda nake masifar tsoron kare ba wlhy Bily.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixteen

16

.....Da uban sauri TJ ya taka birki dan shima firgita yayi, hakama Mama Balki, ya juyo zaiyi magana da sauri ya kauda kansa dan gaba ɗaya Samraah ta koma saman jikin ogan nasa ne. Mama Balki ma kallo ɗaya ta musu ta ɗauke kanta tana Murmushi. Shiko gogan tun faɗa masa jiki da tayi idanunsa kawai ya lumshe saboda ƙarar da tai har cikin tsakkiyar brain ɗinsa ya jita. Shi mutum ne da sam baya son hayaniya. Taɓasan da Laalah ya ɗan yi yana gurnani ya sa ya fahimci abinda take ma tsoro. Lumsassun idanunsa ya buɗe, ya ɗan kalli Laalah ɗin sai kuma ya kalleta. Tayi masifar cikuykuye sa daga ita har ƙatoton hujjab ɗinta. Shi sai abinma ya so bashi dariya. Amma sai ya danne baiyi ba.

Cikin silent voice ɗin nan tasa yay kiran sunan TJ. Amsa masa yay da girmamawa, sai kuma ya buɗe motar ya fita. Kasancewar glass ɗin ta inda Laalah yake an saukesa ya sa ya ɗan duƙo ta wajen sai dai kansa a ƙasa ba kallonsu yake ba. Maimakon amsa masa sai ya ɗan shafa kan Laalah ɗin tare da furta, “Maidashi wajen su Shu'aibu”. Kaɗa bindi Laalah yay alamar dai yaji ubangidan nasa. Tj na buɗewa ya dira da kansa.

Duk abinda suke ina jinsu. Ina jin ya fita na sauke ajiyar zuciya mai nauyi tare da zame jikina daga kan nasa. Ban yarda na kallesa ba na koma can jikin ƙofa na lafe. Ban kuma sake yarda na ɗago ba har muka iso gida. Sosai naji wani irin farin ciki da zaƙuwar ganin naje ga Ummie, dan bazan ɓoye miki ba har cikin tsakkiyar rai nake jin ƙaunar baiwar ALLAHr nan wlhy bily. Ƙagara nayi motar ta tsaya, amma sai bata tsayan ba sai da akaje har ƙofar sashensa. Muna fitowa ina zumuɗin tafiya na koma waccan ƙofar Mama Balki ta dakatar da ni, magana na ɗago zanyi ta dakatar dani, tare da jan hannuna muka shige sashen nasa dan shi tuni yama shige abinsa. Mamaki ne ya kamani, yanzu kam kasa haƙuri nayi sai da nai magana kamar zanyi kuka.

“Mama mi kuma zamuyi anan? Dan ALLAH mu tafi sashenmu ko wajen Ummie”.

Kanta tsaye ta ce, “Banda ikon yanke wannan hukuncin Samraah. Sai dai mu jira daga bakin Alhaji ƙarami”.

Sosai mamaki ya ƙara kamani, zan sake magana ta kama hannuna tai ciki dani. Zaune muka samesa a falo TJ na ajiye masa kofin coffee daketa tururi alamar yanzu nan ya haɗo masa shi. Tj ne ya amsa sallamar tamu, amma shi ko kallon ta inda muke ma baiyi ba. Wajen zama Mama Bilki ta nuna min, ban musa mata ba na zauna fuskata a kumbure. Kobi takaina batayi ba ta juya ta fita. A zatona wani abu zata ɗakko ta dawo, sai naji shiru har tsawon wasu mintuna. Ga TJ shima ya fice da ga ni sai shi. Karo na farko cike da ƙosawa na ɗaga kai na kallesa. Coffee ɗin sa yake sha hankali kwance tamkar ma bai san da zamana a wajen ba. Jinai raina ya sake ɓaci, amma sai na danne murya a sanyaye na ce, “Dan ALLAH zanje wajen Ummie na ganta”.

Kamar bai jini ba, sai da ya mula dan kansa sannan ya ɗan ɗago idanunsa ya kalla ta inda nake. Dai-dai na ɗan hararesa ni kuma batare da tunanin zai ɗago ɗin ba.

“Oh hararata ma kike?”.

Ya faɗa fuska a dake. Da sauri na marairaice fuskata kamar bani ba, cikin kalar tausayi na ce, “No ALLAH ba haka bane. Kawai an samu kuskure ne ni yazan harareka”. Na ƙare maganar a matuƙar karyar da kai. Ɗauke idanun nasa yay cike da basarwa ya cigaba da shan coffee ɗinsa. Naji tamkar na fasa ihu kona kamashi da duka. Amma duk babu dama. Sai kawai na dake tunda na fahimci yɗan wulaƙancin ne a kansa....

□□□

Kamar kullum tsaff ta fito cikin gayunta. Arwa ce riƙe da handbag ɗinta tana mata shagwaɓar ta bata kuɗi. Itako sai faman latsa waya take tana tafiya kamar ma bata jin ɗiyar tata. Sai da suka gama sakkowa da ga upstairs ɗin sannan ta miƙa mata hannu alamar ta bata handbag ɗin. Sake marairaicewa Arwa tayi da maida hannunta baya ta ɓoye jakar. “ALLAH Ummy ni bazan baki ba, just 200k fa nake so bawani kuɗi masu yawa ba. Gift da zan sayama Lubnah yau birthday ɗinta. Kuma motana fa nace miki duk friend ɗina sun sanni da shi, dan ALLAH ki bani baƙin naki, ALLAH bazanyi tuƙin banza ba i promise ”.

“Riƙe promise ɗinki. Dan bazan baki motana ba. Ga dai 100k nan na saka miki je kiyi manage da shi banda kuɗi yau. Give me my bag jare. Kuma ki tabbatar kin dawo gidan nan kafin ten na dare. Dan karna shigo ban sameki ba. Zan ɓata miki rai”.

Baki cike da iska Arwa ta miƙa mata handbag ɗin, babu ko godiya ta juya fuuuu ta koma sama. Kai kawai Hajiya ƙarama ta girgiza ta juya tai tafiyarta. Babu kowa a falon sai su A'i dake gyarawa. Gaisheta sukeyi cike da girmamawa. Itako tana amsa musu a nutsen nan nata babu alamar hayaniya a tattare da ita. Daka ganta kaga mace mai haƙuri da iya zama da mutane. Compaund ta fita, kai tsaye tai wajen motarta dan ita sam bata da driver. Bata yarda da kowa ba ita ke tuƙa kanta, tana ƙoƙarin ajiye handbag ɗinta a side ɗin mai zaman banza dai-dai nan Hajiya Mammah ke fitowa itama cikin wani shegen shiga na manyan mata dake ji da kansu. Kallon juna sukai, amma sai Hajiya Mammah ta watsar da Hajiya ƙaramar tamkar bata ganta ba ma. Lips Hajiya ƙarama ta cije tare da faɗin, (zanyi maganinki ne) a zuciyarta. A zahiri kam sai ta saki murmushi tare da nufar Hajiya Mammah ɗin cikin girmamawa ta gaisheta. A ɗage Hajiya Mammah ta amsa tana ƙoƙarin shigewa motar da drivern ta ya buɗe mata. Itama sai Hajiya ƙaramar tai murmushi ta juya

ga tata motar ta shiga. Kusan a tare suka fice a gidan. Sai dai suna fitowa babban titi kowa yay hanyarsa. Ita Hajiya Mammah gidan Baba prof ta nufa, itako Hajiya ƙarama asibiti ta nufa...

□□□

Gidane babba mai ƙyau kuma sosai. Ga masu aiki tako ina nakai kawo maza kai kace akwai wasu mutane da yawa a ciki. Guri drivern Hajiya Mammah ya samu yayi parking, sannan ya fito cikin rawar jiki ya buɗe mata, sai faman cika take da batsewa wa ma'aikatan dake ta faman gaisheta da girmamawa. Ko sau ɗaya bata amsa musu ba, sai ma tana fitowar tuni wani yazo ya amshi handbag ɗin hannunta dan sun san halinta sarai. A yatsine take bin jibga-jibgan motoci ukun dake fake a compaund ɗin wanda bata san da su ba a gidan da kallo. Cike da isa ta dubi wanda ya amsa mata bag ɗin ta ce, “Waɗan nan motocin fa?”.

Muryarsa har rawa take wajen bata amsa da, “Na baƙine da Alhaji yayi ranki ya daɗe”.

“Baƙi?”.

Ta maimaita da sigar tambaya, sai dai kuma kafin ya bata amsa tayi gaba bakinta a taɓe. Bayanta yabi da sauri. Kanta tsaye ta shiga ta main perlor ɗin gidan ta shiga ainahin falonsu. Babu kowa a ciki, sai ƙamshin air fresheners dake tashi da kuma ɗan sanyin ac kamar ba safiya ba. Baba kam akwai son tsafta. Duk da rayuwarsa yake shi kaɗai a gidan babu mace zaka samu komai tsaf-tsaf. Dan tunda mahaifiyarsu ta rasu bai sake aure ba. Suma kuma ko yace zai yi ɗin bazasu bariba wlhy. Dan yanda ba'ama uwarsu kishiya tana raye ba bayan ta mutu ma baza'ai mata ba. Zaune takai saman luntsuma-luntsuman kujerun falon. Tuni ta wani lume a ciki dan sunada bala'in taushi. Baban nasu ɗan gata ne, dan duk shekara sai Awwab ya canja komai na gidan an sake masa sabon fenti. Kukun gidan daya fito ne yana gaidata ya katse mata tunani, a ɗage shima ta amsa masa fuska a yamutse. Har zai juya ta dakatar da shi, umarnin haɗa mata breakfast ta bayar. Cike da girmamawa ya amsa mata yana komawa ciki. Babu jimawa kuwa ya kammala komai ya kawo ya ajiye gabanta. Zama ta gyara da ƙyau ta fara kwasar girki tana chart da Rubayya dake ƙara tsara mata yanda zata tunkari Baban. A haka Baba prof ya shigo falon ya sameta. Kanta dake duƙe ta ɗago ta kallesa, yana sanye cikin farar jallabiya tas data ƙara fiddo tsufarsa. Dan bashi da wani jikin kirki, gashi dogo masha ALLAH kamar dai su Paah dan duk shi suka biyo har su Maash duk tsahonsa ne. Kanta ta ɗan rissinar tare da faɗin, “Barka da fitowa Baba”.

“Yauwa Nafisatu kece a gidan?”.

Ya faɗa yana kaiwa zaune. Murmushi tayi, tare da sake rissinawa ta shiga gaishesa. Da kulawa ya amsa mata yana tambayarta mutanen gidan da jikin Ummie. Cikin ɗan ɗage kafaɗa ta ce, “Da sauƙi to Baba. But ba shiga nake ba dan tun dai randa ta faɗin nan gaskiya”.

Fuskarsa a ɗan ɗaure yace, “Ban gane ba?”.

Fahimtar katoɓarar da tayi yasa ta ɗan ƙaryar da kai gefe. “Baba ba wani abu nake nufi ba fa. Wlhy ina jin tsoro ne shiyyasa. Kasan idan Ummu-Hidaya na'a wannan yanayin akwai haɗari shiga inda takene. Amma nasan da sauƙi gaskiya, tunda kaga ba'ai kiranka ba”.

Kansa ya jinjina cikin nuna gamsuwa. Ita kuma ta sauke numfashi. Sai kuma tayi murmushi da sake ɗan dubansa. “Baba wai motocin suwaye na gani haka a gidan nan?”.

Hannunsa ya ɗan yarfar da taɓe baki, sai kuma ya ɗauka black tea ɗin da kuku ya kawo masa ya fara kurɓa, sai da yay kusan sau uku kafin ya kalleta. “Shugaban jam'iyyar ACC ne na ƙasa da wasu ministoci guda biyu. Suna damuna a kwanakin nan akan son na shiga siyasa. Ni kuma abinda bai taɓa birgeniba kenan Nafisatu. Yanzu ma shugaban ƙasa ne da kansa ya turosu. Ni dai na faɗa musu gaskiya ina akan bakana. Amma sun dage matuƙa. Shine nace suje zanyi shawara”.

Cike da zumuɗi da zamala Hajiya Mammah ta gyara zamanta. Gaba ɗaya 32teeth ɗinta washe suke. “Amma Baba mizai hana ka amshi tayinsu. Ni banga wani aibu ba a siyasa ai. Sannan kowane irin sharuɗɗa ka cikasu da ko ɗar bazakaji na shiga ba. Tayinfa kujera suke maka mai matsayin farko a jihar nan. Zamu kasance cikin matuƙar farin ciki a kiramu first family na wannan state mai girma irin Lagos. Baba dan ALLAH ka amsa”. Ta ƙare faɗa cikin shagwaɓa. Ajiyar numfashi ya sauke tare da gyara zamansa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_*_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventeen

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

17

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

_____

.....Tsahon lokaci muna zaune shiru batare da ya sake magana ba. Coffee ɗinsa kawai yake sha a hankali yana kuma daƙilar tab da ke a saman ƙafarsa da yay crossing.

“Wane hukunci kika yanke?”.

Tambayarsa ta iso cikin kunnena a bazata. Ɗan ɗagowa nayi na kalla inda yake, dan da farko ma banyi zaton shine yay maganar ba. Yanzu ɗin ma daƙilar tab ɗin kawai yake, dan haka na ce, “Wai kaine kayi tambaya?”.

Ɗago manyan idanunsa yayi a hankali ya kalleni. Sai kuma ya sake maidasu kan abinda yake yi. A taƙaice ya ce, “Uhmm”.

Ajiyar zuciya na sauke da faɗin, “Okay. Amma ban gane tambayar ba. Akan mi kake nufi?”.

“Komai!”.

Ya faɗa can ƙashan maƙoshi. Jimmm kawai nayi ina tunani bayan na sake maimaita komai ɗin a zuciyata. Kai gaskiya ban gane ba, dan duk da ina zargin ahalinsa ai nake ga bai dace na fito fili na nuna ba, tunda ba sanin nasan tarihin gidansu yay ba. Gara idan shine ya sanar min wani abu ai. Fuska na marairaice a sanyaye na ce, “ALLAH kuwa Ya Awwab ban gane ba”.

Komai baice min ba. Yanzu ma ko ɗagowa ya kalleni ɗin baiyi ba. Kusan mintuna biyu ya ajiye kofin coffee ɗin da yake sha sai kuma ya gyara zamansa. Da hannu yay min alamar nazo. Idanu na waro masa alamar mamaki, amma sai ya ɗauke kansa cike da basarwa yana sake tsuke fuska. Banda zaɓin daya wuce bin umarninsa. Dan sam bazan iya musa masa ba. Ina jinsa da wani irin girma da kima fiye da ko yaushe a yanzu. Sannan wani irin shakkarsa nake ji, kwarjinin sa gaba ɗaya ya cika falon har ina jin yama mana kaɗan. A hankali na miƙe kamar wadda tai laifi take tsoron duka. Dan da sanɗa na isa gabansa. Ƙoƙarin kaiwa ƙasan carpet nake ya min nuni da saman cinyarsa. Kaina na maƙe masa alamar a'a, sai ya ɗan taɓe baki ya nuna gefensa batare da yayi magana ba. Dole na canja na koma kan kujerar gefensa dai na zauna. Sai kuma na ɗan saci kallonsa ta gefen ido. Da sauri na maida kaina ƙasa dan dai-dai shima yana ɗagowa ne. Wani irin ratsawa muryarsa ta sake min har cikin kaina, duk da kuwa yayi maganar ne ba cikin tsawa ko hayaniya ba, dan ko a falon kake ba lallai ka jisa ba dan nima na kasance gab da shine. Amma ban sani ba, kodan sai da ya kamo yatsun hannuna cikin nashi tattausan hannun ne sannan yay magana oho. Sake matsa yatsun nawa yay a hankali ina kuma jin kaifin idanunsa har cikin jijiyoyin da jinina ke yawo.

“Idan nace komai ina nufin ina nufin komai da komai. Nasan zuwa yanzu kin san wanene Awwab a zahirance da baɗinance. Dan kinji komai a wajen Mama, kin kuma san komai a makwancinsa”.

Da sauri na ɗago ina ware idanuna duk da zancensa na ƙarshe ya bani kunya. Cikin ɗan rawar lips da nuna mamaki na ƙarara akan fuska na ce, “Ya akai ka sani mama ta faɗa min?”.

Wani ɗan makirin murmushi ya sakar min da lumshe idanunsa sai kuma ya buɗesu luuuu ya zuba su a cikin nawa. Ƙyaƙyƙyafta idanu na fara da ƙoƙarin janye

yatsuna dake a cikin nasa har yanzu. Amma sai ya hana hakan ta hanyar sake riƙesu da ƙyau yana girgiza min kansa. Sai kuma ya janye idanun kamar a kasalance ya ɗaura yatsarsa manuniya mai ɗauke da dogon farce fari tass har wani ƙyalli yake tsabar yanda yake fes, akan zobena ya saka yatsan yana wani zagayawa. Zoben na kalla da sauri nima dan sam ban gane inda ya dosa ba. Sai da ya gama zagayesa sannan ya zaresa a hankali daga cikin yatsata. Ɗan jujjuya min shi yay akan fuska, sai kuma ya runtsesa a cikin hannunsa yana kallona gira ɗaya a ɗage.

“Ke yarinya ne Samrh, tsiwanne kawai yayi miki yawa da shegen kauɗi. Shin bakiyi tunanin taya akai kika zo gidan nan ba haka kai tsaye bayan kin gudu min? Nasan hakan zai iya faruwa, amma dai abune da zai zama mai wahalar gaske musamman idan mukai duba da hannun da kika faɗa....”

Kasa haƙuri nayi, cikin tare numfashinsa na furta, “Dama da saninka nazo nan gidan ke nan?”.

Idanu ya ɗan lumshe ya sake buɗewa a kaina. A bazata naji saukar hannunsa kan hancina. Ya ɗan jashi kaɗan da faɗin, “Yanda kike stubborn ɗin nan ai sai da kula. In ba hakaba zaki ɓaro min aiki ne yar jarida”.

Duk da naji kunya sai da na ɗan tura masa baki. A shagwaɓe na ce, “Ai ALLAH kaine stubborn a gidan nan. Ni dama nata wasi-wasi, duk da nasan kaɗan daga ikon UBANGIJI hakan ta kasance. Amma dan ALLAH Ya Awwab ya akayi nazo?”.

Shiru yayi kamar bazai tanka min ba. Sai da na marairaice masa kamar zanyi kuka sannan. Yana a kwancensa jikin kujera idanunsa a lumshe yanzu. Hakan ya bani damar zuba masa idanuna ina kallon yanda yake motsa lips kamar abin dole. “Tun a guduwan farko nasan zaki iya maimaitawa. Shiyyasa na samar da zoben nan exactly irin naki ta yanda zan san duk wani motsinki. Kina asibiti a Abuja na sa miki, bayan dinga nuna kin inda kike har magana idan akayi ko kikayi zan iya jinki”. Ya ƙare maganar yana nuna min abinda ke a kunnensa kamar bluetooth sai dai shi ƙarami ne bai kai bluetooth girma ba

Cikin ɗan yarfar da hannu da mamaki na ce, “Bala'i, dama kaje asibiti ka duba ni ne? Wlhy naci kai. Taya ban taɓa ma lura da zoben nan ba nawa bane?”.

Idanu ya ɗan buɗe yana kallona. Kamar bazai ce dani komai ba sai kuma ya motsa small pinkish lips ɗinsa a hankali. “Saboda ke yarinya ce”.

Jinai kamar na harararesa amma bazan iya ba. Sai wani cemin yarinya yake. Amma duk da haka sai da na ɓata fuska. Hannu na miƙa masa na ce, “Bani zoben na gani dan ALLAH”.

Idanunsa ya maida ya lumshe. A taƙaice ya furta, “Ya gama aikinsa. Ina jinki mi kika yanke dan bani da lokaci zanyi baƙi”.

“Ni ban yanke komai ba, akan samun lafiyar Ummie kawai nake da plans”.

Idanu ya buɗe sosai yana kallona. Sai na ɗauke nawa daga kallonsa dan bazan iya jurewa ba. A hankali kamar mai jin tsoro na furta, “Ya kamata Fahad ya dawo gida kamar yanda kowa yake gida”.

“Nooo!!”.

Ya faɗa a tsawace yana ƙoƙarin miƙewa. Duk da yanda ƙirjina ya buga da rawar da jikina yake yi sai da nai saurin kamo hannunsa. Muryata a karye kamar zanyi kuka na ce, “Dan ALLAH kayi haƙuri ka zauna. Bafa kaji ƙarshen maganata ba Please”.

Ƙin zaman yay har tsawon lokaci. Sai faman huci ma yake yi abin mamaki da tsoro. Hatta da gashin jikinsa duk sun mimmiƙe. Muryata na rawa cike da magiya na sake faɗin, “Dan ALLAH dan ALLAH. Burinka fa shine samun lafiyar Ummie, kuma wannan hanyar da zan faɗa maka in sha ALLAHU ina fatan zata taimaka mana. Kayi haƙuri ka danne duk abinda kake ji game da ɗan uwanka. Dan wlhy komai bazai yiyu ba sai mun haɗa ƙarfi da ƙarfe. Ni, kai, shi, Hayatu, Mama, Baba, da duk wanda ka aminta da shi a cikin yaranka. Idan har wanda baka haɗa komai da su a duniya ba zasu ci arziƙinka yanda suke so har su bama yɗan uwansu kai mi kake jira akan naka gudan jinin ɗaya tilo. Kana ganin idan lafiyar Ummie ƙalau zata barku a cikin wannan halin? Ko a yanzu da take a cikin halin jarabawa wlhy maybe tana jin zafi da kewar rashin ganin ɗan uwanka dan bata san taya zata furta bane kawai. Karfa ka manta shima nan gidansu ne Ya Awwab. Yanda kake da iko da komai na cikinsa shima haka yake da iko da shi dan ko'a addinance matsayin magada masu kaso kai ɗaya kuke amsawa. Duk duniya fa baka da kamarsa, kamar yanda shima baida kamar ka. Duk mu ɗin nan da muke zagaye da kai son zuciya ko wani dalili zai iya sakawa mu gujeka, amma shi komi ka zama bazai daina jin ƙaunarka a zuciyarsa kamar yanda kaima nasan kana ƙaunarsa. Wannan ƙiyayyar dake tsakaninku ƙirƙirarriyar ƙiyayya ce, kune kuma ya kamata kuyi yaƙi da zukatanku wajen ganin kun canjama abokan gaba nasararsu. Kaifa ka tunatar dani ba'aima maƙiyi gaggawa, idan ba haka ba zai rigaka kai inda kake hari harma ya juyo kai baka kai ba. To kenan in har zaka tafin sai ka kasance mai kula gudun kar ya saka maka tarkon da zai riƙeka ya hanaka isar kafin shi ɗin ya iskoka kuma. Dawowar Fahad gidan nan shine first target ɗin mu akan kowa da komai wlhy. Amma na baka dama kaje kayi tunani ka gani, sannan ka nema zaɓin ALLAH. Ni kuma na maka alƙawarin duk abinda ka yanke zanyi biyayya a kansa sai muje plan na gaba, ni dai fatana kawai Ummie ta samu lafiya ne”. Daga haka na saki masa hannu a hankali. Kaina na duƙar na saki kuka. Dan harga ALLAH yanzu wani masifar tausayi yake bani. Bawan ALLAHn nan yana cikin wani irin bahagon ƙulli ne mai tsaurin gaske. Shiyyasa aketa amfani da shi ana azabtar da mahaifiyarsa da ɗan uwansa. Nayi zaton tafiyar tasa zaiyi, sai naga a hankali ya koma ya zauna cikin kujerar tare da dafe kansa da duka hannayensa yay masifar cije ɗan ƙaramin lips ɗinsa kamar zai hudashi da haƙori. Ha jima a haka kafin ya ringa sauke wasu irin zafafan huci da naji

ƙarin tsoronsa a raina. Dan tuni na maƙure a cikin kujera kamar mage taga ƙare a lungun mai hanya ɗaya tal.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighteen

18

.....Mun jima zaune a hakan kafin ya mike a fusace. Taku ɗaya biyu ya tsaya cak, batare da ya juyoba cikin kaushin murya ya furta, “Daga yau zaki cigaba da zama anan”.

Wani irin zabura nayi yan hanjin cikina na wantsalawa tare da bugun zuciyata. Bamma san sanda na furta, “Anan kuma?”. Ko kallon inda nake baiyi ba yayi wucewarsa hanyar bedroom ɗinsa. Wani irin bugawa zuciyata keyi diff-difff!! Dan har ga ALLAH maganar tashi tayi masifar ratsa min ƙashi da bargo. Wane irin neman bala'ine haka dan ALLAH. Taya zan cigaba da zama a side ɗinsa bayan Mama Balki ta sanar min babu wanda yasan akwai aure tsakanina da shi. Sannan yan uwansa ma abinda ya faru kallonsa suke ama tsayin fyaɗe. “Na shiga uku ni Samraah mutumin nan zai kasheni. Ni wlhy koma ba duk wancan ba bazan iya zaman anan da shi mu biyu kacal ba. Mutumin daya nema kusan kasheni ina gaskiya bashi yiwuwa. Gara ma tun kan wankin hula ya kaini dare na kama gabana. Inama laifin yace na koma sashen Ummie dan ALLAH. Zaram na miƙe, har haɗawa nake da sassarfa na nufi ƙofar fita. Sai dai kuma gam take alamar an kulle. Idanuna ne suka cika da ƙwalla. Ji nake kamar na saki ihu. Na jima a wajen kafin na yanke

shawarar zuwa na bashi haƙuri tare da fahimtar da shi illar wannan hukuncin nasa dan bazai haifar mana da ɗa mai ido ba daga ni har shi ɗin....

□□□□□

“Nafisatu ai ba amsar bane matsalar. Maganar kuma zamowarmu kuma family na farko a jihar nan a tunanina tuni muna ɗaya daga cikin masu wannan matsayin ama Nigeria ba jihar Lagos ba. Ɗanki ya jima da samo mana wannan sunan ama duniya ba'a ƙasar haihuwarmu kawai ba. Siyasa ta wuce duk yanda kike tunani, cike take da rikice-rikice da matsaloli iri-iri. Bazaki gane hakan ba sai mun farata. Amma dai ki bari zan tattauna da Awwab. Kin sanshi yanada experience akan irin waɗan nan abubuwan”.

“Baba yanzu nan duk mu yawan yaranka har mu huɗu cif babu wanda zaka iya shawara da shi a shekarunmu sai jika. Awwab har wani hankaline da shi wanda ko aure baiyi ba.”

“Humm Nafisatu, aure ai lokacine da shi ko?”.

“Baba yana da lokaci, amma kuma kaima ya kamata ka motsashi, yanzu irin wannan abun daya faru idan da maganar nan ta fita mi muke tunani? Ni yanzu ma tsorona ALLAH tsorona yaji daɗi ya cigaba da aikatawa tunda ba kunya garesa ba. Ballema yaga ba'a ɗauki wani mataki ba akai ai kaga abun bamusan kuma ina zai tsaya ba. Tun fa yana taɓa yɗan aiki wlhy wataran kan ƙannensa zai dawo. Dan Awwab yariga yayi gaurin da macen kawai yake buƙata fa. Ya kamata a duba wannan zancen Baba. Idan yana akan bakansa shi baiga wadda yake so ba ai ga yɗar uwarsa nan Azizat. A haɗasu mana kawai tunda Ita dai bazataƙi bin umarninmu ba. Shima kuma idan yaga kowa yaƙi saurarensa ai dole ya amince a wannan karon tunda koba komai yana son asirinsa ya rufu kar duniya ta sani”.

Jinjina kai kawai Baba yake. Sai da takai har ƙarshe sannan ya nisa. “Shawararki abar dubawace Nafisatu, kuma zan duba. Awwab ɗinne sai a hankali, yaro ne mai shegen taurin kan tsiya. Yanzu fa ki duba ki gani saboda yasan abinda yay ba dai-dai bane sam yaƙi zuwa gidan nan. Idan naje can duk yanda zai zame ya gudumin ya sani. Amma barshi nasan mi zanyi. Zanzo yau da dare na ritsashi in sha ALLAHU. Da zarar ya shigo gida ki kirani kawai”.

Cike da farin ciki Hajiya Mammah ta amsa da, “To in sha ALLAHU kuwa Baba. Amma maganar siyasar nan itama dai dan ALLAH a duba mana. Yaya kaga Nafisatu Adams K/Mashi ɗiyar gwamnan jihar Lagos”.

Yanda tai maganar tasa baba ƙyalƙyalewa da dariya. Itama dariyar takeyi....

❤❤❤❤

Kamar mai tsoron a jita a hankali nai knocking ƙofar, shiru babu motsin komai. Sake yi nayi har fin sau uku. Ganin dai bazai kulani ba na yanke shawarar buɗewa kawai ma shiga. A hankali na murɗa handle ɗin kuwa. Sai ko gashi ya buɗe. Sai da na sauke ajiyar zuciya tare da tsayawa na daidaita kaina sosai sannan na tura na shiga da sallama. Turus na tsaya ina kallonsa dan zaune yake akan sofa daga shi sai towel da waya a hannunsa yana magana cikin yanayin nan nasa a daƙile kamar wanda akama dole. A hankali na maida ƙofar na rufe ina mai duƙar da kaina dan bazan iya jurar kallonsa a yanda yake ba. Nafi minti biyu a wajen ina sauraren wayar tasa dana fahimci da Hayatu yake yinta. Sai dai abinda ya ɗan ja hankalina jin yana faɗin idan sun huta Hayatun ya kawosu nan gida. To ko su waye keda irin wannan matsayin haka. Dan na fahimci tunda nazo gidan nan ban taɓa ganin wani baƙo daya shafesa ba yazo. In banda ranar birthday ɗin nan da Bahijja tace min wanda suke zaune a waje ɗaya abokansa ne, kuma duk ba'a ƙasar suke ba idan ka cire ɗan sarkin Lagos ɗin. Ganin har ya kammala ya miƙe yana ƙoƙarin nufar mirror ya sani gyara tsaiwata. Dan ya wani basar tamkar baima ganni ba. Kuma na san yasan na shigo ɗin rainin hankalinsa ne kawai. Kaina a ƙasa daga ƙofar ɗakin na furta, “Dan ALLAH ina son muyi magana”.

Bai tanka min ba, bai kuma fasa abinda yake ba. Sai da ya mula dan kansa kusan minti biyu sannan ya magantu. Cikin silent voice ɗin nan tasa a daƙile ya furta, “Ki wuce wanka baƙi zasu shigo”.

Ji rainin hankali, ina masa wata maganar yana min wata. To ina ruwana da wasu baƙinsa. A zahiri kam sai na ƙara sauke murya har lokacin kan nawa a ƙasa. “Dan ALLAH kayi haƙuri ka barni naje can inda na saba. Ko kuma na koma sashen Ummie tunda dama a yanzu kusan acan ɗin nake. Ya Awwab taya zan dawo nan bayan kasan akwai matsala. Babu fa wanda yasan akwai wani maganar aure a tsakaninmu a gidan nan. Mi kake tunani zasu fassara zaman nawa?”.

“Su fassara duk yanda yay musu! Idan kuma kina buƙatar su sanin ne, yanzun nan sai na tarosu su sani”.

Da sauri na ɗago ina kallonsa. Yanda yay maganar kansa tsaye babu wani alamun ya ɗauki zancena da muhimmanci. Kai wlhy stubborn mutumin nan ya fara isata. Da ƙyar na iya dannewa muryata na ɗan rawa na ce, “Idan kai zaka iya fuskantar su ka kuma ɗauka komai wlhy ni bazan iya ba. Sannan ba wannan rigimar nake so ba yanzu lafiyar Ummie ce damuwata. Dan ALLAH ka duba zance na yana da muhimmanci...”

“Kin dameni Madam wuce wanka kafin nazo kanki”.

Ya faɗa da ɗan kaushin harshe yana ajiye cumb ɗin hannunsa yana barin wajen. Karan farko naji hawaye sun gangaro min.

“Karna fito na sameki a wajen”.

Ya sake faɗa dai-dai yana shigewa cikin cikin closet ɗinsa. Hannuna na dunƙule kamar zan kaima bango naushi sai kuma na tausayama kaina dai. Dan nasan nice zan sha wahalar a ƙarshe hannunna ya rugurguje a banza. Hararar inda ya shige ɗin nayi ina cizar lips ɗina da ƙarfi, ga hawaye share-share a fuskata. Jin motsin kamar zai fito ya sani zabura na nufi bathroom ɗin. Dole ina ji ina gani na haɗa ruwan wankan nai ƙoƙarin fara yi. Wankan nake ina hawaye da hango irin bala'in da zai iya biyo baya. Dan wlhy abin bazai zama mai sauƙin ba a gareni. Gara sashen Ummie da nake zama shi wannan suna ganin ai kamar ina cutuwane shiyyasa aka ɗagamin ƙafa. Amma nan fa? Ni kaina idan an titsiyeni ban san mizan ce ba. Dan nayi alƙawarin in har bada kansa ya fito ya bayyana musu wacece ni ba wlhy ko za'a kasheni bazan faɗa ba. Sai da na kammala wankan sannan hankalina ya tashi, dan ban san yaya zanyi da kayan sakawa ba kuma. Bathrobe ɗin sa na ɗauka na saka. Sallar walha da nake son zuwa nayi dan lokacinta yayi ya sani haƙura na fito, amma sai da na leƙa cikin ɗakin sannan. Shiru babu motsin komai, sannan a iya hangena ban hango alamar akwai mutun ba. Ɗan ajiyar zuciya na sauke na fito a ɗan ɗarare. Nannauyar ajiyar zuciya na sauke ganin tabbacin baya ɗakin, tunanin sauri na shafa mai yazo min, dan haka na nufi gaban mirror ɗin nashi. Zama nayi tare da bin kayan dake akai da kallo, cikin ɗan taɓe baki na furta, “Sai kace mace”. Da ƙyar na iya gane man shafawa, ina son na fara dubashi ina tsoron yin jinkirin da har zai dawo ya saman a wajen. Da sauri-sauri na shafa man da duk abinda zan iya amfani da shi a wajen. Na miƙe raina fal tashin hankalin kayan daya kamata ace na saka ya shigo. Daburcewa nayi dan abin yazo min a bazata. Rasa makamar riƙewa ta sani komawa kan stool ɗin kujerar na zauna tare da duƙar da kaina. Baiyi magana ba, sai madaidaicin akwati da yazo ya ajiye gab dani. Juyawa yay yayi ficewarsa yana faɗin, “Zanje wajensu, da munyi salla zasu shigo. Zaki iya zuwa duba Ummien kafin”. Daga haka yay ficewarsa. Da kallo na bisa duk kaina duk a ɗaure. Sai dai furta zan iya zuwa duba Ummie ne yay matuƙar wanke min zuciya. Mikewa nai cike da zumuɗi harda daka tsalle dan farin ciki, tuni na nema damuwata da tunanin wasu baƙi da ya ishi mutane da zancensu na ɗauki akwatin daya ajiye ɗin. Saman gado na kaisa na buɗe.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page nineteen

19

.....Kayane ɗinkakku har kala biyar, sai kayan ciki b&p 12-12. Sosai naji kunya ta kamani. Wani gefe na zuciyata kuma na mamakin inda yasan seize ɗina. Hatta da ɗinkunan dai-dai jikina cif. Zumuɗin tafiya wajen Ummie ya sani ajiye komai gefe na shirya cikin doguwar rigar lass pink mai ƙyau mara nauyi kuma. Komawa nayi gaban mirror ɗin ina kallon kaina fuskata cike da murmushi. Na dawo Samraah ta yʻar jarida yʻar gayu. A take yaya Musaddiq yazo min a rai. Hawaye naji sun cika min ido na kewarsu. Tunda abin nan ya faru bamuyi waya ba. Dolene idan na dawo wajen Ummie na roƙesa aron waya nayi kiransu har su aunty Zakiyya ma. Da wannan tunanin na ɗauki turarensa na fesa tare da ɗaukar ɗankwalin nai simple ɗauri. Mayafin cikin akwatin guda uku na ɗauka ɗaya nayi salla dan babu hujjab. Ina idarwa na miƙe cike da zumuɗi na tattare duk kayayyakin dana baza na maida bathrobe ɗin danai amfani da ita da towels ɗin daya cire na maida bayin. Sake ɗan gyara fuskata nayi da faran fauda ɗin dana gani sannan na fice.

Nayi mamakin ganin falon ƙal yanzu yana zuba ƙamshi ga sanyin ac duk da dai ɗazun ma ba wani datti bane. Amma daga gani yanzu kasan an sake gyarashi. Kaina tsaye na fito batare da jin damuwar idan na haɗu da wani yaya zanyi ba. Koda na shiga sai da na sauke ajiyar zuciyar jin daɗin ganin babu kowa a falon. Dama ba lallai na samu masu aiki ba, dan yanzu lokacin hutu ne an gama na safe sai kuma azhar tayi. Kaina tsaye na haye sama harda ɗan guduna.

Naji matuƙar farin cikin samun sashen Ummie fes da shi, ga ƙamshi na tashi tako ina. Da alama aikin Mama Balki ne kuwa. Ilai kuwa a ciki na sameta tana bama Ummie abinci. Da gudu na naje na faɗa jikin Ummie ina mai sakin kuka. Dariya Mama Balki ta sanya min, niko ko'a jikina murnar ganin Ummie kawai nakeyi. Sai da na gama murnata na ɗago ina kallonta. Itama kallona kawai takeyi kamar ta samu television. Murmushi na sakar mata idanuna cike da ƙwalla na ce, “Ummie na i miss you”.

A bazatar da ta bamu matuƙar mamaki mukaga ta saki murmushi tare da kai hannu ta shafa kaina. Sai kuma ta saki kuka. Ruɗewa mukai mu duka. Ƙoƙarin miƙewa nake a jikinta amma sai ta riƙeni da ƙyau, sai kawai na sake rungumeta nima ina kukan. Mun jima a haka kafin na ɗago jin kamar jikinta ya saki. Mama na

kalla, ta sakar min murmushi itama tana share ƙwallar idonta. A raunane ta ce, “Tayi barci. Dan tasha maganinta bayan na gama bata abinci. Gani nayi ga sake jawo kwanon sai nayi zaton bata ƙoshi ba shine na sake zaman bata kika shigo.”

Nawa hawayen nima na share. Sai kuma na tashi a jikinta muka taimaka mata ta kwanta. Zama nayi a kusa da ita hannunta cikin nawa ina jin matuƙar farin ciki da ganinta. Sai matuƙar tausayinta dake cimun rai da zuciya dan duk ta rame min a ido alamar ciwon ya bugeta sosai wannan karon...

□□□□

“Kamar ya an sallamesu? Waye ya sallame sun?”. Ta faɗa cikin daka tsawa. Ƙanƙame jiki nurse ɗin tayi jikinta na rawa. Cike da tsorata da birkicewar Hajiya ƙaramar ta ce, “Am sorry Maa. Wlhy ni ban san wanda ya sallamesu ba, naga kawai sun fito ne amma Dr Larai ce ta musu rakiya har mota. Muma ganin haka yasa muka rakasu”.

Wani irin tashi sama jijiyoyin Hajiya ƙarama sukayi, a fusace ta sake dakama Nurse ɗin tsawa. “Get out of my side!!”.

Ai da gudu Nurse ɗin ta fice kuwa. Har neman faɗuwa take, ALLAH dai ya taimaketa ta dafe bango. Tana fita itama Hajiya Ƙarama ta fice a fusace. Sai da taje ƙofar office ɗin Dr Larai sai kuma ta gyara yanayinta cikin jan numfashi da saukewa. Knocking ƙofar tayi, aka bata iznin shiga. Dr Larai na zaune da waya a hannunta da alama akwai abinda take yi. Shigowar Hajiya ƙaramar ya sata ajiye wayar tana murmushi. Da girmamawa matsayin Hajiya ƙarama na shugaba a asibitin ta ce, “Welcome Doctor ashe kin shigo? Yanzu nake tunanin zuwa na duba kafin na wuce gida ai dama”.

Murmushin yaƙe Hajiya ƙarama tayi, tare da jan kujera ta zauna. Hakan yasa itama Dr Larai komawa ta zauna. Gaisuwa sukai a mutunce. Kafin Hajiya ƙarama ta tambayi bataga petient ɗinta ba. Kota canja musu ɗaki ne?. Da ɗan mamaki Dr Larai ta ce, “Kunyi saɓani kenan? Dan sun wuce gida. Yaron nan naku rigimamme ne na bugawa a jarida. Dan har office ɗin nan yazo ta tirkeni sai na bama yarinyar nan sallama. Babu irin son fahimtar da shi ɗin da banyi ba dan ya barta ta ƙara samun sauƙi sosai amma fir yaƙi. Wai a dinga zuwa gida ana dubata. Ko kuma ya kawota asibitin kullum. Rikitaccen mutum ne na lura mai ra'ayin riƙau gaskiya.”

Da ƙyar Hajiya ƙarama ta ƙaƙaro murmushi. Sai kuma ta miƙe tana faɗin, “Ai in dai Awwab ne ƙyaga da yawa wlhy. Shike nan bari zanje gidan mu haɗu ai.”

Murmushi itama Dr Larai tayi da faɗin, “To shike nan hakan ma yayi, amma ina tausayama matarsa dan zata sha fama. Stubborn namiji irin wannan idan baka karancesa ba wahalar zamane da su. Dan su abinda suke so kawai za'ayi tilas.”

Murmushi kawai Hajiya ƙarama tayi dan ita abinda ya dameta shi ya dameta. Cikin wayancewa dai tace bara taje taga petient sun taru. Miƙewa itama Dr Larai tayi tana tattara kayanta. “Okay nima ai wucewa zanyi. Nasan Alhaji bazai wuce ba sai na koma.”

□□□□□

Tuni ganin Ummie yasa na manta da dokarsa ta kar na daɗe. Na shagala sosai da kwance mata gashinta bayan nayi sallar azhar, kanta na a saman cinyata ƙamshin turarensa ya cika ɗakin. Da farko ban maida hankali ba saboda nasan na saka wani a jikina. Sai da naji alamun mutum na nufoni sannan na farga. Shi ɗinne dai sanye cikin brown wando da ash ɗin riga mai gajeren hannu. Gashin nan a ɗaure ta can ƙasa sosai dan har yana taɓa bayansa. Saukar iska a cikin idanuna ya sani jan numfashi da ƙarfi na lumshe idanun, sai kuma duk kunya ta kamani irin wannan abin kunya haka na kure bawan ALLAH da ido. A zatona zaiyi maganar kallon sai naji baice komai ba. Sai ma hannunsa da ya ɗaura saman nawa dake tsefe kan Ummie. A hankali na ɗan ɗago na kallesa. Shima ni ɗin yake kallo. Ƙure juna mukai da ido ga hannayenmu akan Ummie.

“Kinga mamanki kin manta da umarni na ko?”.

Ya faɗa a hankali kamar mai raɗa. Fuska na ɗan marairaice masa da karyar da kaina gefe a shagwaɓe na ce, “Kanta ne fa ya tsufa”.

Idanunsa ya ɗan ja luuu kamar zai lumshe sai kuma ya buɗesu tar akan nawa. Bazan iya jurar salon kallon nasa ba a yanzu dan haka na janye nawa a hankali na duƙar da kan. Shima sai bai sake cewa komai ba ya ɗan janye hannun nawa ya ƙarasa tsefema Ummien. Dama ɗayan da nake yinne ya rage. Dan bana mata kitson da yawa. Koda ya kammala cumb dake saman cinyata ya ɗauka ya taje mata kamar yanda naima sauran. Sannan ya tattare gashin cikin hannunsa. Kallona yay a hankali ya furta, “Cire band ɗin kaina, idan kin dawo kwayi kitson”.

Kai kawai na jinjina masa. Kafin a kunyace na kai hannuna saman gashinsa dake kwance luff yana ƙyalli kona wata macen albarka na zame sililin baƙin band ɗin daya haɗe da gashin sai ma ka ƙura ido kake ganewa. Koda yaushe kuma zakaga da irinsa yake ɗaure gashinsa. Ina gama zarewa gashin nasa ya tarwatse a baya. Sai kawai na shagala da kallonsa har sai da naji saukar hannunsa cikin nawa zai zare band ɗin sannan na dawo hankalina. Duƙar da kaina nayi kunya duk ta isan. Yau dai na kula kamar ina sakin layi da yawa. Sai dai yanda ya basar yasa na ɗan ji

nutsuwa. Yana gama ɗaure mata ya gyara mata kwanciya shima ya miƙe yana faɗin, “Lets go”.

Dole na mike a hankali ina gyara mayafin jikina. Wani kallo ya dinga bina da shi daga sama zuwa ƙasa. Sai kawai nai gaba da sauri. A falo muka samu mama Balki ashe bata fita ba. Tana ganinmu ta saki murmushi da faɗin, “Har kun fito.” a kunyace na jinjina mata kaina. Shi kuma ya sanar mata akwai baƙi a gidan zuwa anjima zai kira wayarta tazo su gaisa. Ya kuma roƙeta ta rufe ƙofar falon ko Paah ne yazo karta barsa ya shigo. Maganar tasa ta ɗan ban mamaki, har na kasa haƙuri sai da na kallesa. Amma sai ya ɗauke kansa kamar ma bashi ne yay maganar ba...

A falon ƙasa muka ci karo da su Azizat. Tunda muka fara sakkowa duk suka miƙe tsaye tamkar waɗan da ke cikin shock. Dan su duka bakunansu a buɗe suke kallonmu idan ka cire wata farar budurwa da ban sani ba a gidan dake zaune ita bata tashi ba. Sai dai itama ta zuba masa ido kamar zata cinyesa. Kallo ɗaya na musu na ɗauke kaina. Kamar yanda shima naga baima nuna yasan da zamansu ba ya wucewarsa. Ina jiyo Malika na yin ashar a hankali. Ban san miya basu mamakin ba. Ganina a gidan? Ko kuwa ganina tare da shi?. Oho dai can ta matse musu. Dan ni su duka ukun a yanzu na shirya duk wadda tace zata shigo sabgata wlhy sai na mata zanen yarabawa a fuska.

Koda muka iso ƙofar shiga sashen nasa sai da na tsaya na ɗan gyara mayafina sannan na bisa dan shi har ya riga ya shiga. Da Hayatu na fara cin karo tsaye a ƙofa yana waya, muna haɗa ido ya wani rissinar da kai. Harara na balla masa na wuce ciki abuna. Bana ganin fuskar waɗanda ke a zaune, sai dai haka kawai zuciyata ke wani irin sanyi da jikina. Gani nike kuma kamar na sansu. Tamkar wadda ƙwai ya fashema a ciki na ƙarasa sosai cikin tsakkiyar kujerun ina sake yin sallama ƙasa-ƙasa batare dana kallesu ba. Turus na tsaya zuciyata na bugawa da ƙarfi sakamakon jin muryoyin da ko'a cikin barci bazasu taɓa iya su ɓace min ba. Jikina har rawa yake na ɗago dan tabbatarwa. Sai kawai naci karo da fuskar Yaya Musaddiq da ke faman min murmushi da ta Hafizzullah. Yanzu kam sosai rawar jikina sake bayyana tayi, ga lips ɗina na rawa kamar yanda hannuna ke rawa ina son nunasu amma na kasa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twenty-one

21

.....Suna gama ficewa cike da zumuɗi na maido hankalina kansu Yaya Musaddiq. Ƙoƙarin zama nake Hafizzullah ya ce, “Wlhy ji nake kamar a mafarki. Wai aunty Samraah kece matar mutum kamar Maash. Ya ALLAH Maash fa. Wai dan ALLAH Adda yaya akai haka ta kasance? Kodai dama ke kin san wa kika aura? Dan wlhy duk da sun sanar mana komai yanzu kuma a gabana komai ta faru lokacin auren sai nake ganin kamar dama dai kuna son junan ku ne ke da shi.”

Hararsa na ɗan yi, sai kuma na koma kusa da Yaya Musaddiq na zauna ina sauke ajiyar zuciya. “Yaya dan ALLAH mi sukace muku? Sannan dama kaima baka san shi bane?”.

Murmushi sosai Yaya Musaddiq yayi yana kallona. Sai kuma ya jinjina kansa. “Samraah wlhy har yanzu ni kaina ina a cikin yanayin da Hafizzullah ɗin yake ciki ne. Dan harga ALLAH ban taɓa sanin Maash ne mijinki ba, taya ma zan kawo hakan a raina to. Bama ni kaɗai ba, hatta su Abba babu wanda yasan wa kika aura. Koda aka ɗaukeni aiki a companynsa na amsa ne saboda dalilai uku. Na farko dai bazan iya bijirema umarnin ogana ba. Saboda yana treating ɗina like uba. Ko Abba dake ƙanin mahaifiyata muke a hannunsa tun bamu san kammu ba bana jin ya damu da tarbiyyata kamar yanda ogana ya tsaya a kaina. Hakan yasa babu abinda zai ce nayi a rayuwar nan naƙi yinsa sai dai ina na saɓama ALLAH ne ko cutar da wani. Wannan kam bazan masa biyayya ba. Na biyu maganar video ɗin nan. Na yarda zanyi aiki a companyn da tunanin ko zan fahimci wani abu dan na sanki da naci akan abu, komai tsahon lokaci da za'a ɗauka bazaki taɓa barin maganar video ɗin nan ba. Na uku amsar aikin kamar samun wata hanyar cigaban rayuwa ne yazo mana mu duka. Dan bamu da kowa sai junanmu. Dolene nayi aiki tuƙuru in har bana saɓama ALLAH bane domin cigaba da gina rayuwarmu. A lokacin da aka samu matsala game da aurenki, mahaifiyar Mansoor tazo har gida taci mutuncin su Abba akan ɗanta bazai taɓa ya aureki ba, su bazasu haɗa zuri'a da ke ba, idan kuma muka matsa zata iya ɗaukar kowane irin mataki dan ganin ta rabaki da ɗanta. Kin

san Kawu Musa da zuciya, dan haka shima ya balbaleta, sai kawai ta ɗaga hannu ta maresa. Kafin ta sauke hannunta mukaji itama an sauke nata marin. Ta gigita sosai, haka muma da mamaki muke kallon bawan ALLAHn daya maretan. Mutum ne cikin shigar kamala harda gemunsa, maganganun daya gayama mahaifiyar Mansoor a lokacin sun matuƙar birgemu. Sai muka ji sauƙin yanda kalamanta suka ƙona mana rai dama kowa na wajen a take muma mukace ko Mansoor ne autan maza kin barsa har abada. An gama duk wannan rikici Maman Mansoor ta wuce bawan ALLAHn nan shima zai wuce Kawu Musa ya dakatar da shi. Godiya ya masa muma haka. A mamakin mu sai kawai muka ji ya fara jera masa tambaya. (Yaro munene sunanka?) Yace masa Muhammad. Anan kake? Yace masa eh to yana aiki anan amma asalinsa ba mazaunin nan ɗin bane. Kana da aure? Sai da yay jim kamar mai tunani kafin yace masa a'a. Kana shirin yi ne? Nan ma ya amsa masa da a'a. Iyayenka fa? Yace suna nan a raye. Sai mukaga kawai Kawu Musa yayi murmushi. Batare da wani tunani ba kawai ya ce (kowa ya shaida. Ni Musa a matsayin yayan Abdul-wahab na bama wannan bawan ALLAHn Muhammad auren ɗiyata Samraah. Ina fatan bazaka taɓa watsa min ƙasa a ido ba. Ina fatan zaka tabbatar min da ƙyautata maka zato da nake yi. Ina fatan zaka riƙeta amana bazaka taɓa cin amanata ba. Idan kuma har akwai matsala ka fito ka sanar min wIhy zan fahimceka. Nima kuma badan bana son Samraah na baka ita ba. Ba kuma dan na zubar mata da darajanta nayi hakan ba. Yarinyata mai ilimin addini ce dana zamani. Sannan ƙyaƙyƙyawace mai tarbiyya. Kaga dai ban sanka ba, ban san daga inda ka fito ba. Komai daya faru daga UBANGIJI ne ba daga mu ba. Dan abinda kayi yanzu yasa nake ji a raina ko daga ina ka fito kai ɗin mutumin kirki ne, dan ɗan halak shike kare martabar tsoho a duk inda yaga za'a yaga masa rigar mutunci.”

“Wlhy Kandala ya matuƙar jimawa tsaye bai motsa ba a wajen. Har sai da Kawu Musa ya dafa shi da faɗin. Idan fa har kaga akwai matsala kada ka saka kanka a cikin damuwa. Mu duka dake nan babu wanda zai zargeka da rashin ƙyautawa har abada. Kuma mun ƙulla zumunci da kai kenan har abada. Murmushi yayi, sai kuma ya ɗan jinjina kai da roƙon a bashi wasu mintuna zaiyi waya. Kai tsaye Kawu Musa ya bashi dama. Tafiyarsa waya muka samu damar tattaunawa muma, Kawu Musa ya fahimtar damu dalilinsa na yanke hukuncin nan. Ni dai dan banda yanda zanyi ne bazan iya jayayya da su ba na amince. Hakama Hafizzullah atake yace shi dai dan ALLAH a barki. Amma sai Kawu Musa ya mana nasiha da nuna mana illar barinki ba'a ɗaura auren a ranar ba. Ya kuma ce mu cigaba da miki addu'a in sha ALLAHU sai kinci ribar wannan auren. Dawowarsa ta katse zancen mu. Ya tabbatar ma su Kawu ya amshi aure, sannan waliyyinsa na tafe in sha ALLAHU kafin lokaci yayi. Shima kuma zai je ya dawo. Badan muna da hope ɗin dawowar tasa ba muka barshi, amma abin mamaki na takaice miki sai gashi muna ƙoƙarin wucewa masallaci. Sunzo tare da babban malamin nan Sheikh Muhammad bin Khalipha Al-Hussain a matsayin waliyyinsa. Sai wannan Hayatu da suke tare yace ƙaninsa ne. Sheikh Muhammad dai ba ɓoyayyen mutum bane a garin Kano dama Nigeria baki ɗaya, dan haka duka damuwarmu da wani wasiwasi ya kau. Sheikh Muhammad ya tabbatar mana Muhammad tamkar ɗa yake a wajensa, kuma in sha ALLAHU

bazamuyi kukan haɗa jini da shi ba. Idan ma muna tunanin wani abu mu cire, dan wata hikima ce ta UBANGIJI shigowarsa rayuwarmu. Bai kuma ɓoye masa komai game da abinda ya farun ba. Kawu Musa yafi kowa shiga a farin ciki. Dan haka a take aka ɗaura aurenku bayan idar da sallar juma'a, aka kuma kwaso kayanki da aka kai gidan Mansoor aka maida gidan daya bada matsayin nasa. Bayan an kaiki kuma sai aka samu akasin ciwo da kika shiga har ya taho dake Abuja, daga baya ya sanar mana kuna Lagos wajen iyayensa. Koda yaushe muna waya da shi, amma bai taɓa gaya min komai da ya shafeshi ba. Sai a yau da muka iso an kaimu masauki kawai naci karo da fuskarsa matsayin mijinki. Bayan kuma ni sai a gobe zan gansa matsayin ogana bayan munzo wajenki. Kin san kuwa ruɗanin dana shiga Samraah. Har kusan faduwa nayi sai da Hayatu ya rikeni. Bayan sun bani ruwa nasha mun zauna a ɗarare Hayatu ya min bayani komai tun daga batun ɗaukar video har zuwa kidnapping ɗinki da mahaifiyar Mansoor tasa akayi, da karɓarki da yayi a hannunta sanadin bincike da yayi saboda kuɗi da aka nema a hannunsa da sunanki har 500m. Bayan ya gano bake bace amfani kawai ake son yi da sunanki ya kuma gano anyi kidnapping ɗinki shine ya kubutar dake. Yaso amsar video ɗin a hannunki lokacin kodan gudun kada ki sake shiga wata matsalar sai kikaƙi bashi. Sai kawai ya haƙura ya sake ki akan zai cigaba da bibiyarki har sai ya amsa dan in ba haka ba yasan wataran wani zai iya sake yunkurin cutar dake a kansa in har akasan da shi. Ya tabbatar mana shi ya kubutar dake daga auren Mansoor ne saboda kawai yasan bazaki taɓa samun farin ciki ba dan mahaifiyarsa da ƙanwarta ya tabbatar da zasu iya aikata komai akanki, yanda kuma basu samu kudin nan ba kema bazaki samu yanda kike so ba. Ko ran daurin auren da yazo ya biyo mahaifiyar Mansoor ne cikin ɓadda kama dan ya tabbatar tayi abinda auren zai fasu amma sai kawai tai abinda ya sashi tilas bayyana kansa garemu alhalin shi beyi niyyar hakan ba. Sai kuma kawai Kawu Musa ya masa ƙyautarki. Yace bazai iya watsama tsohon kasa a ido ba saboda sun bashi tausayi, koba komai shine ya saka auren rugujewa, idan bai amsa ba ai ya sake raunanasu kema kuma an cutar dake shiyyasa kawai ya amince. Sai kuma gashi auren shima ya zame masa alkairi, dan ya ce mana yanzu kin tallafi rayuwar mahaifiyarsa dake fama da jiyya shekara da shekaru. Nagode Samraah, Nagode matuƙa da kikayi haƙuri kika amshi ƙaddararki da hannu biyu, Nagode da kika kasance ɗiya ta ƙwarai, Nagode da kika cigaba da riƙe tarbiyyar ki. Dan tabbas naga tsagwaron jin daɗi a fuskar Maash game da ƙyautatama Mahaifiyarsa. Na tabbatar da koda a baya ba soyayya ce ta haɗaku ba yanzu kam yana sonki. Yana ƙaunarki, dan wannan alkairin naki ne muma ya jawo mana alkairin. Yanzu na fahimci dama Maash yaje garejinmu kai tsaye ne domin kawai ya ɗaukeni aiki, dan sai yanzu nake sake tariyo yanda aka ɗaukeni aikin cikin sauƙi ake kuma mutuntani da girmamani sama da ma'aikata da yawa. Gashi har an turani karatu wata ƙasa. Samraah tabbas ke ɗin alkairi ce. Gaba ɗaya halayen iyayenmu kin kwashesu. Dama ance TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE. tabbas na yarda da wannan batu na malam bahaushe”. Ya ƙare maganar yana share hawaye.

Da gani har Hafiz muma kukan muke. Dan labarin ya matuƙar girgizani. Ashe haka abubuwa suka faru ni ban sani ba. Ashe mahaifiyar Mansoor ce tasa akai

kidnapping ɗin a da farko. To amma tayaya akai hakan? Da sanin Mansoor ɗin kokuma? Idan bada saninsa ba taya akai tasan da videon nan? Shiyyasa ba'a son zargi, na daɗe ina zargin Maash akan ɓata min aure dan shi ya aureni ya cutar dani ya amshi video ashe abin duk ba haka bane ba. Kai jama'a, lallai masu iya magana sunyi gaskiya da sukace zato zunubi ne koda ya kasance gaskiya. Nagodema ALLAH da ban taɓa masa tambaya akan auren ba duk da nasha son yin hakan kwarjininsa da shakka na hanani. Sosai nake jin kimarsa na sake ƙaruwa a cikin zuciyata. Ashe shine ma ya kubutar da ni daga hannun mahaifiyar Mansoor. Kai ban taɓa zaton matar nan zata iya aikata irin wannan al'amarin ba. Wato mutum kai dai kawai gansa ka barsa yanda ALLAH yayisa, akan kuɗi baka iya banbance mutumin banza dana ƙwarai da wuri, dan sanin zuciya sai UBANGIJIN kawai.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twenty-two

22

.....Sai ƙarfe kusan uku mijin Baby ya iso gidan cikin ƙatuwar motar da ta sake haukace imanin su Mom. Sam ita bama damuwarta rabuwa da ɗiyar ba. Sai santin motar suke da sake kambama irin dukiyar mijin Babyn. Faɗa ma ta yarda akai baby iyayenta na Gwarzo su mata batayi ba. Sai sake shiryata da akai ciki wata alƙyabba mai ɗan karan ƙyau. Itako ido ƙemaƙayau ba ko ɗigon hawaye. Hasalima inda kwalliyarta batayi ba gyara abinta take ko tace a sake mata kaza bata son kaza. Su dai su Gwaggo Gudidi sunyi sororo suna kallon ikon ALLAH.

Abba baya nan ya fita, dan baiyi zaton mijin Babyn zai iso a lokacin ba kasancewar yasha jira kafin azhar amma shiru. Sai Alhaji Jafaru babban ɗan Gwaggo Gudidi ya jashi suka tafi wata gaisuwa a gyaɗi-gyaɗi. Su Gwaggo Gudidi

suna tunanin ai za'a jira Abban su dawo. Amma mi sai gani sukai an fito da amarya baby tana taku ɗai-ɗai ko irin rufe fuskar nan ta amare batai ba. Sai ma hirarsu suke da kakarta Umma suna dariya. Babu wanda aka kalla a cikinsu aka wuce da Baby ƙofar gida aka sakata a narƙeƙiyar motar da angon nata yazo a ciki. Abu mafi ban mamaki mijin ko kallonsu baiyi ba. Sai Mom ɗin da Umma ne suka gaisheshi yana amsawa cike da shan ƙamshi. Baki a washe Umma tace, “ALLAH ya tsare to Alhaji. ALLAH kuma yasa ku dawo lafiya da babbar tsaraba ta tattaɓa kunnena. Alhaji mu ya maganar tafiyarmu saudia ne?”.

Duk maganar da Umma take harararta Baby keyi, miye na wani tabbayar zuwa makka dan zubar da mutunci. Badai shine da kansa yace ya biya musu ba ai sai tayi hakuri taga lokacin yayi baice suje ba ko. Shikam ma ɗan mannin rainin wayon hannu kawai ya ɗaga musu a taƙaice ya ce, “A jira lokaci”. Daga haka ya ɗauke kansa tare da bama drivern sa umarni ko kallon amaryar tasa baiyi ba. Driver kam umarnin ogansa ya cika. Ya tada mota abinsa yay reverse har yana neman taka su Mom dake tsaitsaye. Ai tuni mutane suka shiga faman jinjina kawunan mamaki. Yʼan anguwa suka guntsa kowa da abinda ya fassara al'amarin. Dan kuwa dai sunga sabon salon ɗaukar amarya ganin idonsu.

Duk abinda ake Halime batama sani ba. Tana can tunda ta idar da sallar azhar ta kira Abba tace ya saya mata rake da gyaɗa tai kwanciyarta. Har aka tafi da Babyn kuma bata sani ba. Sai da hayaniya ta fara tashi ta yʼan gwarzo sannan ta farka...

□□□□□

Duk yanda Hayatu ke ƙoƙarin danne abinda ke cimasa zuciya ya kasa. Sai satar kallonsa yake ta cikin mirror har suka iso babban companyn da Ummie ta fara ginawa da hannunta tun mahaifinta na da rai wanda Paah ne ke riƙe da ragamar komai na companyn. Kʼatone bana wasa ba, sannan akwai ma'aikata jingim a cikinsa. A farkon ginashi ana sarrafa kayan suturu ne, bayan abubuwa sun kwaɓe akan ciwon Ummie companyn ya durƙushe harma ya daina aiki na tsawon shekaru. Sai daga baya Maash ɗin ya farfaɗo da shi tare da sake faɗaɗashi aka maida shi wajen sarrafa kayan abinci. Kusan kowane nau'i na kayan abinci har su mai magi duk companyn na fitarwa. Suga, gishiri, harsu omo da sabulai sannan kayan abinci tun daga kan shinkafa, taliya, fulawa, garin alkama, da ire-irensu, da dangoginsu. A yanzu dai a Africa babu companyn dake fidda kayan masarufi irinsa gaskiya. Dan tako ina suna kai abinci kuma sunada wasu reshika a wasu kasashen da dama.

Duk ta inda suka gitta gaisuwar girmamawa ake bama Maash. Shi ko yana mai amsa musu a daƙilen nan nasa dan motsin lips ɗinsa kawai suke gani sai kuma hannu da yake ɗaga musu. Duk wanda yayma Maash farin sani a rayuwa yasan

wannan halin nasa ba wulaƙanci bane yanayinsa ne kawai a haka. Dan magana inba ta zamar masa dole ba, da wahala kaga yana yinta. Idan ma yayin bazaka taɓa jin sautin muryarsa sama ba. Sai fa idan an ɓata masa rai yayi matuƙar iya hargagin da ke gigita mutum.

Kai tsaye office ɗinsa ya nufa Hayatu biye da shi dan shima yana da office a companyn. Har yanzu suna kan bincike game da case ɗin nan na samun yara a containers ɗin sa na kaya da suka tura Ghana. Monday ɗin nan zasu shiga court yau kuma zai sake zaman meeting da lawyers ɗin su da Paah, duk da dai kwata-kwata an nuna case ɗin bai shafesa ba duk da kasancewarsa shugaban companyn shiyyasa ma yake tsula tsiyarsa da matan da ake ɗauka aiki a ciki har Maash ɗin ya gano sa ranar yake tujara. Sun samu Paah ɗin baya nan, lawyers ɗin kuma basu kai ga ƙarasowa ba. Sai hakan ya bama Hayatu damar fidda abinda ke ransa.

Kallon Maash dake zaune cikin kujerarsa ta office ɗin yana daƙilar keyboard ɗin computer ɗin saman desk ɗinsa yayi. Sai kuma yayi ƙasa da kansa cikin girmamawa yace, “Yaya kamin afuwa, zan sake maimaita maganar nan dai ta kwanaki dana taɓa maka kaƙi cewa komai”.

Shiru kamar maash ɗin bazai amsa ba. Sai kuma can yace, “Uhumm ina jinka”.

Kai hayatu ya ɗan sosa yana sake ƙasa da kansa ya ce, “Nifa ALLAH yaya yau saina sake ganin kamanin Yayan Aunty sosai da Baba Abdull sun sake fitowa. Shi kuma ƙanin nan nasu Hafizzullah banbancinsa da Falaq kawai ita mace shi namiji. ALLAH tun ɗazu a ruɗe nake dauriya kawai nake yi. Ita kanta Auntyn yau sai naga suna fisgar kama da Falaq ɗin, kawai dan ita farace ita kuma aunty bata kaita has.....”

Ruff bakin Hayatu ya rufe batare daya ƙarasa faɗa ba saboda kallon da Maash ɗin yay masa. Sai ya wayance da faɗin, “Yaya ALLAH ka duba lamarin nan iya gaskiyata nake faɗa”. Ya ƙare maganar cikin shagwaɓa kamar ba Hayatu PA ba. (Wato na lura akwai lokacin da Maash matsayin oga yake a wajensa. Akwai kuma lokacin da yaya yake😀).

Hararsa kawai Maash ɗin yayi ya ɗauke kansa ya maida ga aikinsa....

□□□□

“Ban gane mi kike son faɗa ba? Kin san dai bana son rainin wayo ko”.

“Wlhy yallaɓai babu rainin wayo a maganata. Kai ma kasan bazan yi hakan a gareka ba. Naje na samu nima ta sallameta. Kuma shi Awwab ɗin ne yaje ya sakata yin hakan”.

Wata shegen ashariya Yallaɓai ya kutuntuma. Sai kuma ya miƙe zaram yana kaima Centre table duka har sai da Hajiya ƙarama ta zabura tana ƙanƙame jikinta. Sai kuma ya juyi a fusace yana nunata da yatsa. “Idan har na samu matsala a aikina saboda ke na rantse da ALLAH sai na koya miki hankali”.

Sosai hankalinta ya tashi, dan tasan mugun nan komai zai iya aikatawa akan buƙatarsa. Amma ba komai lokacinsa ne. Zata bisa yanda yake so gaba kaɗan zatayi maganinsa ai itama. Dan ta gama shirinta a kansa tun shekarun baya. Murya ta sauke cikin nuna tsorata ta furta, “Kayi haƙuri nayi kuskure, amma na samo hanyar gyara kuskuren nawa. Na tabbatar bazai kaita ko'ina ba sai gida. Koda yake nama bincika an tabbatar min suna gidan. A wannan karon zan nuna abinda ya faru ina jin tausayinta na dawo da ita sashena. Kokuma na nuna zan share mata kukanta akan abinda ya faru ta hanyar nema mata makaranta ta cigaba. Da ganan sai musan abinda ya dace, kaga munma samu sauƙi”.

Shiru ya ɗan yi alamar nazarin maganarta. Sai kuma ya kai zaune yana mai jinjina kai. “Hakan ma yayi, sai dai ina mai gargaɗarki ki kiyaye. Dan bana buƙatar wata matsala kuma.”

“In sha ALLAHU babu abinda zai faru, shi mai bincike a kantan ya dawo ne?”.

“Zuwa jibi ne ƙarshen kwanakin daya ɗiba min. Dan ko jiya munyi waya da shi ya kuma tabbatar min da aikin na tafiya yanda zanyi farin ciki”.

Itama murmushin ta saki duk da ba haka taso ba. Dan a nata ɓangaren tasa itama a bincika mata wacece Samraah ɗin?.

□□□□

Gaba ɗaya ganin yɜan uwana ya wanke min duk wata damuwata. Hirarmu muke cike da farin ciki suna bani labarin cakwakiyar gidan Abba ta yanzu da amaryarsa, tare da yanda auren Baby ya kasance, sun dai baro ana jiran miji yazo ya ɗauke ta. Matsama Yaya Musaddiq nai ya kiramun aunty Zakiyya. Daga nan fa mukaita gaisawa da mutane harda amaryar Abba da kawai naji matuƙar ƙaunarta. Daga ƙarshe jikina yayi sanyi jin batun zuwan mijin Baby yanzu babu jimawa da yanda tafiyar ta kasance. Mun cigaba da jimanta abun bayan katse wayar. A haka lokacin sallar la'asar ya riskemu. Ina tunanin yanda zasu fita salla sai ga guard ɗinsa yazo yace suzo boss yace ya kaisu suyi salla. Kafin su dawo nima nayi tawa, na sake gyara sashen naje kuma na gano Ummie. Alokacin nake cema Mama Balki tazo su gaisa da bakin da yace. Ta ce tana zuwa idan ta kammala abinda take yi. Harta bani abinci na kai musu. Duk da sunci sun ƙoshi dan acan inda aka fara saukesu sunce sunci abinci, nan ma kuma da Hayatu ya rakosu da kayayyakin ciye-ciye suma mukaita ci muna hira sai da na ɗauka musu abincin. Sake zaman hirar mukayi, dan

ji nake kamar mu dawwama a haka. Koda suɓutar baki ban sanar musu komai daya shafi gidan nan ba. Hirar abinda ya shafemu kawai mukeyi hankalinmu kwance. Hatta zancen alaƙar Mama Balki da nake zargi da baba ban gaya musu ba, shiyyasa ma na matsu tazo su gaisa. Dan duk wanda yasan mahaifinmu ya kallai Yaya Musaddiq yasan suna matuƙar kama, musamman yanzu da yake sake girma kamanin na sake fitowa sosai. Wajen ƙarfe biyar ina shirin zuwa na sake ganin Ummie da ga nan nayi kiran Mama sai gashi ya dawo. Sannu da zuwa su Yaya suka shiga yimasa da gaidashi. Ganin haka yasa nima na gaisheshi batare dana yarda na kallesa ba. Sai dai shi ina jin idanunsa na yawo a jikina, dan haka ma naƙi kallon nasa. Ciki ya shige yana faɗa musu bari ya ɗan watsa ruwa. Sukai masa fatan fitowa lafiya. Na gyara zama zan cigaba da hirata Yaya Musaddiq ya hararen, tare da mun nuni da ƙofar da ya bi.

Baki na tura cikin shagwaɓa nace, “Kai yaya mi kuma zanyi”.

Sosai yake kallona fuska a tsuke, “Oh kice karatun Mom kema kin ɗauka kenan?”.

Da sauri na shiga girgiza masa kaina. “Wlhy Yaya a'a”.

“Inafa a'a tunda gashi na gani da idona. Abba yakan dawo gida bai ishi Mom kallo ba. Kema ga mijinki ya dawo ko kallon inda yake bakiyi ba. Abba yakan dawo gida Mom bata bashi ruwa ba, ya shige yay hidimarsa. Kema kuma gashi mijinki ya dawo babu ruwa babu abinci, maimakon ki bishi kiji yaya ya dawo, miye matsalarsa kin gyara zama ke ga mai yɗan uwa sunzo ko. Haka kike so muma idan munyi aure matanmu suna mana?”.

Da sauri na sake girgiza masa kai idanuna na cika da ƙwalla. Ya ce, “Okay to aya maza tashi, haba Kandalata ina islamiyyan ya tafi? Mu kin bamu munci mun ƙoshi yan uwanki shi dake wahalar nema ko oho. Ko kina so Hafiz ya rainaki”.

Da sauri na sake girgiza kaina ina Hararan Hafiz ɗin dake kumshe dariya. Tashi nayi na nufi ƙaton freight ɗin dining room. Ruwa na ɗauka da lemo na sa a tray dana ɗakko a kitchen sai glass cup mai ƙyau. Ni sai ma naji abun banbara ƙwai wai namiji da suna Hajara. Haka dai na daure dan bazan taɓa iya bijirema Yaya Musaddiq ba.....✍

A fito lahiya matar yayanmu

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_Typing□_*

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twenty-three

---

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

=========

.....A hankali nake tafiya kamar kazar da ƙwai ya fashema a ciki, koda na isa ƙofar bedroom ɗin na yi kusan minti ɗaya kafin nayi knocking a hankali. Banji motsin komai ba balle na saka ran za'a buɗe min. Hannu na kai zan sake knocking ɗin aka buɗe ƙofar. Da sauri na janye hannun nawa na riƙe tray ɗin da ƙyau kaina a ƙasa. Jin shiru ya sani ɗagowa a tunanina juyawa yay ya koma. Amma sai na gansa tsaye kawai ya zuba min cat eyes ɗin nan nasa. Sosai tsigar jikina ta tashi, dan wani irin kallo yake min mai wahalar fassara gashi da ga shi sai guntun towel iya gwiwa. Kaina nai ƙoƙarin sake saukewa cikin ɗan rawar harshe na furta, “D... dama ruwa ne...”

Bai bari na ƙarasa ba ya matsa min hanya alamar na shiga. Raɓawa nayi na wuce, kai tsaye na ajiye tray ɗin saman Centre table na buɗe ruwan na tsiyaya a cup tare da ƙoƙarin ɗagowa. Ido muka haɗa da shi, yana tsaye jikin mirror ƙafafunsa a harɗe yay folding hannayensa a ƙirji ya zuba min ido kawai. Ƙasa nayi

da nawa, tare da takawa a hankali inda yake, batare dana kallesa ba na miƙa masa kofin ruwan. Shiru babu alamar zai amsa, dan haka na ɗago cikin yanayin kamar mai shakku na kallesa, har lokacin idanunsa a kaina suke, samun kaina nayi da marairaice face ɗina kamar zanyi kuka na ce, “Pleaseeee!”.

Ɗan luuuu yayi da idanunsa kamar zai lumshe sai kuma ya buɗe a kaina har sai da naji tsigar jikina ta tashi, hannuna dake riƙe da kofin ya ɗan fara rawa-rawa kamar zan saki kofin. Hannayensa dake harɗe a ƙirjinsa ya warware a kasalance, dan haka na ƙara ƙasa da kaina dan bazan iya kallonsa a yanda yaken ba. Jin saukar hannunsa a saman nawa mai riƙe da kofin ruwan ya sani lumshe nawa idon batare dana ɗago na kallesan ba. Ina ƙoƙarin sakar masa amma ya hana hakan, sai ma saukar ɗayan hannun nasa naji akan gefen cikina, a hankali ya fara tafiya da shi har zuwa bayana, kafin ya matsoni ya manne da jikinsa. Sannan ya kai ruwan da ke a cikin hannayenmu saman lips ɗinsa. Yasha kusan rabi ya zare kofin ya ajiye. Ni dai har lokacin ban sake yarda na kallesa ba. Sai dai na furta, “Nagode sosai Ya Awwab. ALLAH ya saka da alkairi, ya bama Ummie lafiya da tsohon rai mai albarka. ALLAH ya kareka da sharrin masu sharri. ALLAH ya yarda dakai”.

Jinai kawai ya ɗora ɗayan hannun nasa ta saman bayana shima ya mannoni da jikinsa gaba ɗaya ya kwantar da kaina a saman faffaɗan ƙirjinsa. Luff nayi ina mai shaƙar narkakken ƙamshinsa mai matukar tasiri da saka nutsuwa a zuciyar mai shaƙa. Munfi mintina biyar a hakan har wani bacci-bacci nake ji yana neman ɗaukata. Sai naji ya ɗagoni a slowly tare da juyamu na koma jikin mirror ɗin shi kuma ya koma inda nake da. Dagowa nai da nufin yin magana ya ranƙwafo ni gaba ɗayansa, daɓas na koma saman mirror ɗin na zauna, shi kuma yamun rumfa hannunsa ɗaya dafe da mirror ɗin, ɗayan kuma ya saukesa akan haɓata ya ɗago fuskata. Cikin matuƙar low voice ya furta, “Open your eyes”.

Jinai Sam bazan iya masa gardama ba, dan haka na shiga yin far-far da idanun kafin na buɗesu da ƙyar na saukesu akan ƙyaƙyƙyawar doguwar fuskarsa dake ƙawace da kwantaccen gashi baƙi siɗik. Kallon juna muke cikin ido da mu kammu bazamu iya fassara yanayin da muke a ciki ba. Sai wani irin tashi tsigar jikina keyi, a hankali a hankali idanuna suka fara tara ƙwalla. Kasa jurewa nayi na lumshesu slowly ina sauke tagwayen ajiyar zuciya. Dan mutumin nan zai kasheni da salonsa. A bazata matuƙar bazata naji saukar abu mai sanyi da taushi saman lips ɗina. Da sauri na buɗe idanuna. Ai babu shiri na maida su da gudu na kulle zuciyata na tsargawa. A salon da yake kissing ɗin nawa yasa gaba ɗaya jikina ya saki har ban san na kai hannuna saman kansa ba nariƙosa. Har ga ALLAH hakan da nayi kawai nayi ne amma bada wata manufa bane, tsabar na rasa ina zan dafa na samu sassaucin ruɗanin dana shiga ne yasa hannuna sauka a saman kan nashi batare dana shiryama hakan ba. Ashe shi hakan armashi ya ƙara masa, dan wajen kicin-kicin ganin na janyesa harda zame band ɗin dake ɗaure da gashinsa na tura yatsuna duk biyar cikin gashin ina yamutsawa. Munfi mintuna uku a haka, kafin ya janye lips ɗin nasa tare da ɗaura goshinsa saman nawa, hancinanmu na gogar juna, kowannenmu na sauke numfashi. Wajen minti ɗaya sannan ya ɗago kansa, kasa

kallonsa nayi, sai ma hawayen da suka cika min idone suka ɗan silalo badan ni kaina nasan dalilina nayin su ba, gaba ɗayana ya jawo ya rungume tsam-tsam a jikinsa. Nima samun kaina nayi da ƙanƙamesan dan jikina rawa yake yi.. nan ma mun kwashe wasu mintuna biyun a haka kafin ya kai bakinsa saitin kunnena cikin raɗa ya furta, “Kema baƙi ƙoshi ba ko? A ƙara”.

Ji nai kamar na tsaga jikinsa na shige dan kunya, sai kawai na sake ƙanƙamesa. Wani irin ratsa kunnena sassanyan sautin murmushinsa yayi a bazata. Sai kuma ya ɗagoni yana ƙoƙarin kallon fuskata amma naƙi yarda yay hakan....

A dai-dai lokacin da acan Maash da Sam-G ke a wata duniya anan falo Mama Balki ce ta iso domin gaishe da baƙi. Cikin fara'arta da kazar-kazar ta shigo bakinta ɗauke da sallama. Amsawa su Musaddiq sukayi dama ransu fal tunanin ganin wannan uba-uban ƙaton gida amma basuga giccin kowa ba sai masu aiki maza. Ɗagowa sukayi su duka a tare da nufin gaisheta, kawai saita ja birki da uban sauri har tana buge ƙafa da kujera. Kallon Musaddiq take kamar zata cinyesa da idanunta, jikinta sai rawa yake yi. Sai kuma ta sake maida kallonta ga Hafizzullah shima. Sai kawai gani sukai ta fashe da wani irin kuka tana faman jan jikinta baya.

A ruɗe duk suka miƙe suna tambayarta lafiya? Mike faruwa?. Sam ta gagara basu amsa, sai sake cin tuntuɓe da tayi da carpet hakan yasata tafiya gaba ɗayanta zata faɗi ta baya suka hau salati da nufarta su duka biyun suka tare a tare....

Cak Maash ya dakata daga yunƙurin sake maida lips ɗinsa da yake saman na Samraah. Itama sai ta buɗe nata idanun da sauri duk suka kalla ƙofar. Dan su dukansu sunji salatin su Hafizzullah ɗin Kasancewar da ƙarfi sukayi. Kallonta yay, itama ta kallesa, sai kuma a hankali ya zame hannayensa da ga jikinta ya ɗaga gaba ɗayanta ya sauke daga saman mirror ɗin daya ɗaurata.

Zan nufi ƙofa da sauri ya riƙoni, fuska na marairaice masa kamar zanyi kuka. Sai yay min nuni da gyalena da ɗan kwali dake yashe a ƙasa. Gyalen kawai na ɗauka dan hankalina ya tashi, kada wani ya cutar min yan uwafa a gidan nan? Da wlhy sunga ainahin baƙin halina dan saina gallabi kowa da kowa har uban gayyar tasu bazan bari ba. Dai-dai ina isowa falon suke ƙoƙarin zaunar da Mama Balki a kujera, sai nai turus ina kallonsu. Ruwa Yaya Musaddiq ya bata, yayinda Hafizzullah daya juyo ya ganni yake sanar min abinda ya faru. Da sauri na nufi Mama Balki. Zama nayi a kusa da ita cikin damuwa ina tambayarta mike faruwa?. Dai-dai nan ya fito shima sanye cikin baƙar jallabiya da tai masa wani masifar ƙyau. Muna haɗa ido na kauda nawa da sauri.

Mama dake kallonsa itama fuskarta share-share da hawaye ta nuna masa Yaya Musaddiq. “Alhaji ƙarami dan ALLAH kalla bawan ALLAHn nan. Kalla yanda yake

tsananin kama da Babanku. Inda ace mutum na mutuwa ya dawo da ƙuruciyarsa babu abinda zai sa bazan dage Abdul-wahab bane ya dawo Alhaji Ƙarami”.

Shiru kamar bazaice mata komai ba, sai kuma ya ɗan nisa a hankali tare da kaiwa zaune cikin kujerar dake facing ɗinta. Zaman ƙafa ɗaya kan ɗaya yay yana mai kwantar da kansa a jikin kujera tare da lumshe idanunsa. A haka ya furta, “Please Mama relax. Wannan ba Baba bane, dan Baba ya tafi ya barmu tafiya ta har abada.” ɗagowa yay da kansa ya ɗan zuba mana idanu mu duka sai kuma ya sake furzar da iska kaɗan yana ɗan mana nuni da Mama Balki. “Wannan matsayin uwa take garemu mu duka. Ban sani ba ko kun san Baba yana da mata a zamansa na Lagos harda yarinya ɗaya. Itace wannan”.

Da sauri Yaya Musaddiq ya kalla Mama, sai kuma ya juya ya kalla Maash ɗin. Sake gyaɗa masa kai yay cikin lumshe idanunsa tabbacin haka ɗin ne. Ni ko da Hafizzullah a ruɗani muke kallonsu. Gwarama ni dama na jima da wannan al'amarin a zuciya. Sai kawai mukaga Yaya Musaddiq ya duƙar da kansa yana hawaye. Kafin ya miƙe a hankali yaje gaban mama Balki ya tsugunna. Hannunta ya kamo cikin nasa hawaye na cigaba da masa gudu a fuska ya furta, “ALLAH na gode maka daka saka inada rabon ganin wannan rana kafin nabar duniya. Mama dan ALLAH kiyi haƙuri, kiyi haƙuri kiyi haƙuri. Tun daga randa nasan kaina, tare da labarinki a wajen Gwaggo Gudidi ban taɓa fashin addu'ar ALLAH yasa kafin nabar duniya na haɗu da ke da yar uwarmu da akace tana tare dake ba. A dalilinki sau biyu ina zuwa Lagos bayan na tuhumi iyayena akan kuskuren da sukayi suka nuna min nadamarsu suma, sai dai dan basu san ina zasu ganoki ba suma shiyyasa suka cigaba da zama da damuwar a rayukansu. Tabbas mama an cutar dake. Muma kuma an cutar damu, tunda da mun sanki na tabbatar bazamuyi kukan rashin iyaye a duniya ba. Dan ALLAH mama kiyi haƙuri ki yafema ahalinmu kada hakkinki ya cigaba da hanasu kwanciyar hankali a rayuwarsu. Kuskure ne sukayi a wata gaɓar da mu kammu bamu tsira ba. Dan mu ɗin ma komai sai da ya ƙwaɓe tsawon shekaru tsakaninmu dasu babu wani jituwa sakamakon amsata da ƙanin mahaifiyar mu yayi ya riƙe bai bar musu ba, duk da dama tun raduwar mahaifiyarmu ita Samraah da Hafizzullah suna a hannunsa ne. To nima sai yace zan koma hannunsa, amma suka nuna basu amince ba suma su Samraah sai a dawo musu da su. Kowa ya fahimci gadon da aka barmana sukemawa shiyyasa dangin mahaifiyarmu suka dage shine akai rabuwar tashin hankali suka manta damu sai da ga baya naita bibiyarsu har komai ya dai-daita. Zamma iya cemiki dawowarsu garemu sosai-sosai lokacin amsar kuɗin auren Samraah ne”. Kuka yaci ƙarfinsa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭_**_TSUTSAR NAMA....!!_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twenty-four

24

.....Muma kukan muke ni da Hafiz sosai. Hakama Mama kuka take har tana siƙewa. Sai da ya mana magana cikin gyaran murya sannan kowa ya ɗan tsagaita. Cikin yanayinsan nan na rashin son hayaniya ya furta, “Kuka ba shine alama ta godiyar ALLAH ba. Abinda ya faru ya riga ya faru, ku fuskanci wanda yake a yanzu itace rayuwa. Ya kamata bayan magrib itama Falaq kuje can dan ta ganku tunda tana fama da kanta bazata iya tazo nan ba. Gashi babu wani lokaci shi Musaddiq zai wuce gobe in sha ALLAHU”.

Duk mun gamsu da zancensa, yayinda Mama ke jinjina kai ta ce, “Alhaji Ƙarami dama kasan inda suke kenan? Shiyyasa ka auro Samraah?”.

Ɗan luuu yay da idanunsa kamar abin dole ya saki murmushi. Babu wanda ma yay zaton zai amsa a cikinmu saboda yanda ya jima baice komai ba. Sai kuma ya ɗan furzar da iska cikin sauke numfashi. Kansa ya girgiza a daƙile ya furta, “A farkon ganina da ita ban san ita wacece ba. Ban kuma taɓa kawo wani abu game da ita ba. Sai dai sunanta ya ɗan so ya ja hankalina har ya tunamin da Baba a ranar. Abubuwa ne da yawa suka faru da suka alaƙanta wannan auren Mama, dan har ga ALLAH ni banje da nufin ɓata mata aure ni na aureta ba. Kawai na hana wancan ne dan na kuɓutar da ita daga halin banza na mahaifiyarsa. Sai kuma Uncle nata yace ya bani, naso kawo musu wani dalili sai kawai naci karo da fuskar Musaddiq nima a lokacin, shine kawai nace na amsa. Bayan barina wajen kafin a ɗaura auren na saka akamin bincike shine na gano su ɗin yaran Baba ne”.

Sosai kowannenmu ke jinjina iko da hikima ta UBANGIJI. Hafizzullah da bai fahimci komai ba a zancen yay tambaya. Nice na masa bayani. Sai kawai ya hau murna wai muma ashe munada Mama. Abinda yay ɗin ne ya sakamu darawa mu duka. Hatta shi uban gayyar ina kallon sanda yay ɗan munafukin murmushin nan nasa dai-dai yana miƙewa. Ciki ya koma ya barmu anan da Mama. Aiko sai labari ya ɓalle a tsakaninmu, dan Mama wayayyar mace ce mai kuma tsananin kirki da dattako. Fita tayi sai gata tazo da Malam Baba. Mahaifin Hayatu kenan, mijinta kuma a yanzu, aminin mahaifinmu. Shi kansa ya shiga mamaki matuƙa, ya kuma yi

farin ciki da ganin yayan amininsa. Duk da ya jima zuciyarsa na masa wasi-wasi a kaina ashe. Shiyyasa tun ranar farko daya ganni agidan yake kallona. Dan duk da bana kama da Babanmu, gaba ɗaya komaina na mahaifiyarmu ne idan ka cire ɗan duhun da nake da shi dan mahaifiyarmu farace tass, su su yaya Musaddiq duk sun ɗakko farinta amma kamanin Baba. Maganar aure kuma dake a tsakanina da Maash ya sani Hayatu ya faɗa masu dama.

□□□□

Ganin har gab da magriba bai sake fitowa ba munata hirarmu da Mama a falo Yaya Musaddiq yay min nuni da hanyar bedroom ɗinsa cikin hikima. Jinai duk kunya ta gama kamani, sai dai bazan iya musa masa ba. Dan haka na tashi sum-sum na wuce. Yanzun kam ban tsaya knocking ba na murɗa handle ɗin ƙofar a hankali na shiga kaina a ƙasa. Dan har yanzu ina jin nauyi da kunyar abinda ya faru a tsakaninmu ɗazun. Jin ɗakin shiru kamar babu motsi ya sani ɗan ɗagowa ina kallon ko ina. Sauka idanuna sukai a kansa. Yana zaune a cikin sofa sanye da bathrobe alamar bai cire ba tunda ya fito wankan, bowl ne na glass a saman cinyarsa da uban chocolates a ciki. Da mamaki nake kallon chocolates ɗin kafin na ɗan ɗaga idanuna akan fuskarsa. Da farko na zata ma barci yake a hakan, sai da naga gashin idonsa dogaye sosai sun ɗan motsa alamar kallona yake ƙasa-ƙasa. Kauda nawa idanun nayi kamar zan juya naji ya furta, “Zo nan”.

Idanuna na ɗan rumtse, dan duk sanda saukar muryarsa zai shiga cikin kunnuwana sai na jisu har tsakkiyar brain ɗina. Sai da na ciza lips da sauke numfashi sannan na juya kaina a ƙasa na nufesa. Ban zauna a kujerar da yake ba doguwa sai na zauna akan ɗayar dake gefensa dan guda uku ne dama. Doguwa ɗaya sai biyu masu zaman ɗai ɗai a gefe da gefen ta.

“Mi kike buƙata?”.

Ya faɗa a daƙile yana kai sauran chocolate ɗin hannunsa ƙaramin bakinsa. Satar kallonsa nayi ina mamaki a raina, namiji da cin chocolate, ai kayan yara ne da mata, duk yau banga ni dai ya ci abinci ba, sai dai ko da suka fita yaci. Ganin ya zuba min ido na ɗan girgiza masa kaina da faɗin, “Ba komai, kawai na jika shiru ne baka fito ba. Ga kuma abinci duk yau naga baka ci ba”.

Shiru bai tanka min ba tsahon kusan mintuna biyu, kafin ya ɗago a nutsensa zaune sosai tare da ajiye bowl ɗin chocolates ɗin nashi a Centre table. Murya can ƙasa ya ce, “Gashi ina ci”. Yay maganar yana nuna bowl ɗin chocolates ɗin. Da mamaki na ɗago idanuna sosai na warosu a kansa. Tare da furta, “Chocolate ne abinci? Abin kwaɗayin yara ne fa. Kai kuma ƙatoto da kai ka zauna kana ci, kuma amma ce fa maza basa cin zaƙi hak.....”

Ganin yanda yake kallona da mayatattun idanunsa na kasa ƙarasawa, sai ma na miƙe cikin wayancewa na ce, “An kira magrib bari na shirya kar su zo suna jirana”. Na wuce bayi da sauri.

Da kallo ya bita harta shige, sai kuma ya girgiza kansa shima yana miƙewa zuwa closet ɗinsa yin shirin massalaci.

□□□

Bayan sallar magrib Hayatu da kansa yazo ɗaukarmu. Ogan nasa bai dawo ba. Amma tunda shi yace zamuje dama sai ban damu ba na shirya tsaff cikin atamfa riga da skirt a kayan daya kawo min. Ni da Hafizzullah da Mama a baya, Yaya Musaddiq da Hayatu a gaba. Yanda naga bakinsa yaƙi rufuwa saboda farin ciki nasan Mama ta gaya masa komai ko mahaifinsa. Nayi matuƙar mamakin ganin ƙayataccen gidan da shima yake a ciki. Sai na sake yarda da batun Mama Balki da tace su suna zaune a Maash Mansion ne kawai saboda Ummie. Shine gaba muna biye da shi, sosai ta ciki ma gidan yay ƙyau da tsaruwa. Sai da muka zauna ya kwala kiran mai aikinsu wata yar budurwar yarinya ta fito. Gaishemu tayi sannan ya bata umarnin kawo ruwa da abinci shi kuma yay sama. Babu jimawa sai gashi ya fito riƙe da ƙyaƙyƙyawar matashiya, gaskiya zata iya girmata koda shekara uku ne, da ƙyar take tafiya saboda cikin jikinta da yay girma sosai. Duk da fuskarta ta ɗan yi fushi irin na masu ciki hakan bai ɓoye kammaninta da Hafizzullah ba. Yanda muka zuba mata ido haka itama ta zuba mana nata. Lokacin da suke isowa gab da mu jikinta har rawa yake yi. Haka ta dinga bimmu ɗaya bayan ɗaya da kallo, kafin ta maida kan Mama da ke kallonta itama fuskarta ɗauke da murmushi. Cikin langaɓar da kai ta ce, “Mama ina ji a jikina su ɗin jinina ne. Dan ALLAH Mama kada kuce dani ba haka bane ba. Yaya Hayat yace bazai faɗa ba sai dai na gani da ido na”.

Murmushi mukayi mu dukanmu, kafin Mama ta gyaɗa mata kai. “Tabbas su ɗin jininki ne Falaq. Ga babban yaya Musaddiq, sai Samraah ban ƙanwa, sai auta Hafizzullah”.

Kuka ta saki a hankali idonta akanmu muduka ta ce, “Wlhy yaya kamar Baba, suna kama sosai”. Ta faɗa tana sake fashewa da kuka mai ban tausayi. Gaba ɗaya muka miƙe muka rufu kanta. Yaya Musaddiq akwai son yan uwansa, tuni ya janye ta daga jikin Hayatu ya kamata ya zaunar a kujera, gabanta ya durƙusa cikin lallashi yake mata daɗaɗan kalamai. Sai ta fara dariya ga hawaye. Ganin haka nima na zauna a kusa da ita na shiga share mata hawayen nata. Sai ta haɗamu ta rungume, tare da miƙawa Hafizzullah hannu alamar shima yazo. Ta ɗayan gefenta ya zauna shima muka haɗe kai waje guda muka bar Mama da Hayatu yan kallo. Mun jima a haka kafin Mama su dinga lallashinmu. Sallar isha'i data gitta ya samu miƙewa,

mazan suka fita mu kuma mukayi anan gida. Koda suka ɗawo sabon babin hira muka buɗe, Yaya Musaddiq da Mama nata bamu labarin Baba. Dan Hayatu fita yayi wai Maash ya kirashi akwai inda zasu je. Banyi mamaki ba, dan sukam ko aljanu haka suka gansu suka barsu saboda shegen yawonsu. Sai naji tausayin Falaq ya kamani, haka take haƙuri (kema haka zakiyi haƙurin) zuciyata ta ayyana min. Da mama ke sanarma Falaq ɗin ni matar Maash ce a yanzu wani irin ihun farin ciki ta saki tana rungumeni, koba komai yar uwarta ta dawo kusa da ita. Tsaff suka bata labarin yanda komai ya faru, ta dinga farin ciki da ƙorafin Hayatu ita bai sanar mata ba. Kamar wasa sai ga lokaci yaja. Dan sai da sha biyu tayi sannan Hayatu ya dawo, shine yake cewa ga Maash a waje yana jiranmu. Kuka Falaq ta sanya wai anan zamu kwana, ita bata gaji da ganinmu ba. Cikin dariya Hayatu yace, “Nikam babu ruwana Hubby, keda yayanki jeki gashi can”.

Aiko miƙewa tai tana ɗaukar mayafina, itako Mama Balki ta miƙe tana faɗin, “A'a nidai kam nayi nan”. Dariya muka sanya mata, dan muma ba son tafiyar muke ba, saboda hirar bata ishemu ba. Sai addu'a nake a zuciyata ALLAH yasa ya yarda. Kusan mintuna biyar sai gata ta dawo tana tuttura baki. Mayafina ta cire ta miƙamin tana faɗin, “Ya yarda da ƙyar su Yaya su kwana anan ɗin, amma wai ke kije lil sis...”.

Ɓata fuska nayi nima kamar zanyi kuka. Nace, “Amma baki roƙesa ba ko Aunty?”.

“ALLAH har kuka na masa. Kin san taurin kan Yayana kuwa. Idan yace a babu mai canja masa zuwa b. Cayay da ma wai idan na haihu zaki zo. Bama gobefa kenan”.

Dariya Hafizzullah ya fashe da ita, harara na balla masa da ɗaukar mayafina fuuu na nufi hanyar fita...

Shima dai Yaya Musaddiq da ke riƙe dariyarsa da Hayatu sai da suka dara, kafin su miƙe subi bayanta.

Sanda suka iso ina tsaye jikin motar ta saitin inda yake ina masa magiya amma ɗan mannin bai ko buɗe idonsa dake lumshe ba ya kallan bare ya tanka. Haushi da takaici ya sani balla masa harara na koma ta ɗayan side ɗin dan Mama ce a gaba kusa da TJ, da sauri TJ ɗin dake a waje ya buɗen ƙofar yana wani risinawa. Ko kallonsa banyi ba na shiga na zauna na juya ƙeyata. Koda su Yaya Musaddiq suka iso wajen inaji yana magana da su wai ƙanwarsa ta masa fin ƙarfi shi da baƙi ita da ƙwacesu su kwana. Ina jin yanda suke yar dariya da bashi haƙuri. Basu wani jimaba yace ma TJ muje Mama ta gaji. Suna min sallama ƙin kallonsu nayi, ina jiyo dariyarsu su duka ukun sai naji idanuna sun cika da ƙwalla.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twenty five

25

.....Koda muka iso gidan na gama shiryama raina abinda zanyi. Dan haka ina fitowa na zabura zanyi sashen masu aiki caraf aka riƙeni. A fusace na juyo, sai dai kafin ma na samu damar cewa wani abu camak ya ɗagani a cikin hannunsa ko kunyar su Mama Balki da TJ da sauran ma'aikatan dake a harabar gidan da basu yi barci ba baiji ba. Salati na ɗauka ina wawwaro idanu na da suka cika da ƙwalla waje. Amma sai yay biris dani kamar ma baiji ba, takunsa ma yake ɗai-ɗai like bai ɗauki komai ba. Tafi mukaji da salati, da sauri na ɗaga ido na kalla saman ginin dan tanan ne ake yi. Sai ko idanun nawa suka sauka akan Hajiya Mammah dake tacan sama a balcony na upstairs. Mutsu-mutsun son sauka na farayi, amma ko alamar zai taimaka ya saukenin baiyi ba. Bai kuma nuna shi yama jita ba balle ya kalla inda take. Bai kuma direni ba sai a gaban ƙofar sashensa. Yana riƙe da hannuna ya buɗe muka shiga. Muna shiga falon na sakar masa kukan shagwaɓa ina faɗin, “Ni ka sakan min hannu wajen Ummie zani, kuma ka daina bani kunya gaban mutane”.

Hanya ya nuna min alamar naje. Yanzu kam kasa haƙuri nayi sai da na kallesa. Sai kuma na shiga ƙyaƙyƙyafta idanu. Muryata na ɗan rawa na sake ɗagowa zanyi magana yay mun alamar zipping akan bakinsa tare da sake nuna min hanya. Kamar zan fasa kuka na shiga tafiya a hankali yana biye da ni har cikin bedroom. Koda

muka shigan ma sake nuni yay min ba bathroom. Nan ma sum-sum na wuce dan babu alamar wasa a tattare da shi. Gaba ɗaya a tsorace nake, idan yace abinda ya aikata zai maimaita nama san mutuwa zanyi kawai.. Wankan nayi tare da ɗauro alwala amma sai na kasa fitowa duk da bathrobe na saka. Ina tsayen ina faman ƙullawa da kwancewa kawai ya shigo shikin bayin, idanu na waro sosai na mamaki, sai ya wani lumshe min idanunsa yana nufoni, da sauri naja da baya na manne da bango, na gama sadaƙarwa kaina zai zo sai kawai ya wuce ni. Ajiyar zuciya na sauke mai nauyi tare da fita a hanzarce cike da sassarfa. Na ji dadin ganin kayan barci daya ajiye min wando da riga masu kauri, ɗauka nayi na saka a gurguje, tare da ɗaukar mayafina na yafa. Har na kammala abinda zanyi dan ya ɗan jima a cikin bayin sai kuma gashi ya fito sanye da bathrobe fara tas shima. Idanu muka haɗa, nai saurin ɗauke kaina ina sake ɓata fuska. Shima sai yay wucewarsa kamar bai ganni ba.

Ya jima a cikin closet kafin ya fito nan ma, ina kwance kan sofa ina game da wayarsa daya ajiye a Centre table sai gashi ya fito shima cikin kayan barci sky blue da suka masa ƙyau sosai. Batare da ya kallan ba yace, “Muje”. Wani ɗan karan dadi ne ya kamani, cike da zumuɗi na bisa dan a zatona ya barni naje can ɗin na kwana. Bare ma dana ganni a sashen Ummie ta hanyar da ban taɓa sanin yana da ita ba. Mun sami Ummie har tayi barci. Zama yay yana mata addu'a, ganin haka nima sai na zauna ina mata addu'ar. Tsahon mintuna goma sha muna a ɗakin ya fara riƙe kansa. Muƙewa yay a hankali tare da riƙo hannuna ya ce, “Lets go”. Tsoro naji yanda naga ya riƙe kan, dan haka banyi musu ba na bisa. Sai da naga zamu koma sashensa nai ƙoƙarin yin magana amma ya hanani hakan. Muna shigowa a bakin gado ya kai zaune, yana sake dafe kan nasa da hannu bibbiyu.

Tsoro ne ya kamani da tausayinsa, har bamma san naje gabansa na durƙusa ba ta tsakanin ƙafafunsa na dafa gwiwarsa ɗaya, ɗayan hannun kuma na kaisa saman nasa hannun daya dafe kai. A hankali na janye nasan muryata a raunane na ce, “Ya Awwab miya faru? Baka da lafiya ne?”.

Shiru kamar bazai kulani ba, sai kuma ya ɗago shanyayun idanunsa da launinsu ya sauya zuwa golden yana kallona. Cikin motsa lips ɗinsa kamar baya so ya furta, “My head”.

“Ciwo yake?”.

Idanunsa ya lunshe min alamar eh. Cikin damuwa nace, “Na maka kamu?”. Nan ma kan kawai ya jinjina min yana maida idanunsa ya rufe. Miƙewa nayi sosai dan na fara gajiya da durƙuson, hannunsa na janye, na ɗaura nawa a wajen na fara masa addu'a. Inayi ina kamun da tofa masa addu'ar. Har na kammala ina faɗin, “ALLAH ya ƙara lafiya”. Ya amsa min da amin akan lips ɗinsa, ƙoƙarin barin gaban nasa nake naji saukar hannunsa a saman ƙuguna. Da sauri na kallesa tsigar jikina na tashi.

“Ina zaki?”.

A raunane na ce, “Saman sofa”.

“Gadon fa?”.

“Amma....”.

“Shiiiiii!!!”.

Ya katseni tun kafin na ƙarasa faɗa. Tare da nuna min saman gadon babu wasa sam akan fuskarsa. Duk da shi dai ba banbance farin cikinsa ko damuwarsa kake dama a saman fuskar ba. Tunda akoda yaushe babu alamar fara'a a tare da shi. Sai idan shine ya so ya saki wannan munafukin murmushin nasa iya lips. Jikina har rawa yake wajen hawa gado. Idanuna kam tuni sun tara ƙwalla. Haka na kwanta ƙarshe gadon na wani naɗe jikina tamkar yar mage. Shiru banji ya hawo ba bai kuma tashi ba. Kaɗan na ɗan buɗe ido na kallesa. Yana zaunen har yanzu dafe da kan nasa alamar bai gama sauka ba. Jinai tausayinsa ya ƙara kamani, bamma san cikin raunin murya na furta, “Ko dai yunwa ce? Nifa duk yau banga kaci abinci ba”. Shiru baida alamar amsa min. Baima motsa a yanda yake ba har na gaji na maida idanuna na rufe. Mintuna baifi biyu ba ya hauro saman gadon, tuni zuciyata ya fara mutsu-mutsu, barema da ya kashe wutar ɗakin ya bar lamp ɗin side ɗinsa kawai itama ya maidata can ƙasa ba wani hasken kirki kasancewar muna a cikin net ne da yayma gadon rumfa gaba ɗaya. Jira kawai nake naji yamin irin na waccan ranar amma sai naji shiru baima ko matso inda nake ba. A hankali a hankali na fara samun nutsuwa har barci ya ɗan fara figata. Sai can na saki jikina sosai sannan na jisa a bayana. A ɗan firgice na farka, sai da ya riga har ya birkitoni na koma jikinsa

gaba ɗayana ya rungumeni. Kasa daurewa nayi, sai da nayi magana cikin rawar murya irin ta wanda ke cikin tsoro.

“Yaya wlhy akwai ciwo”.

“Nace zanyi wani abu ne”.

Ya faɗa cikin kunnena da wata irin muryar da sai da tsigar jikina ta tashi. Ƙam na runtse idanuna ban sake cewa komai ba. Shiru har kusan mintuna biyu muna a haka kafin a hankali ya dai-daita fuskata da tashi, goshinsa a saman nawa hakama hancinsa sai lips ɗinmu sai dai su ba'a haɗe ba. Duk da a cikin duhu-duhu muke yanda idanuna ke a rufe shima nasa a rufen suke. Cikin wani irin soft and low voice ya furta, “Yanzu dai so kike ayi wani abu ko?”.

Da sauri na shiga girgiza masa kaina hawayen da nake riƙewa na zubowa da gudu.

“To mi kike so?”.

“Barci”.

Na bashi amsa har ina taune lips ɗina jikina na tsuma.

“Ni kuma bana jin barci ya za'ayi?”.

A marairaice na ce, “Ka tashi kayi salla to ko karatun Alkur'ani”.

“Uhum-uhum. Ni matata nake buƙata”.

Har cikin tsakkiyar brain sai da naji saukar furucin. Muryata na matuƙar rawa na ce, “Ya Awwab wlhy akwai ciwo. Kuma doctor tace ba...bai...war...ke...b.....” Nama kasa ƙarasawa.

“Yanzu mi kike so ayi to?”.

Da sauri na sake maimaita, “Barci”.

“Kin tabbatar?”.

Kaina na shiga jinjina masa. Da sauri-sauri.

“Tom bari na saki barcin”.

Ya faɗa acan ƙasan maƙoshi. Kafinma nace wani abu naji saukar small lips ɗinsa kan nawa. Tun ina mutsu-mutsun ruɗewa da firgici har na nutsu luff, dan wani irin salo yake min mai shagaltar da gangar jiki, cikin ƙanƙanin lokaci na gama sallamawa gaba ɗaya na batare da ni kaina nama san minake ba. Ban tashi fahimtar kuskure na ba sai da aka ɗauki wani layi daban. Duk da a yanda yau yake bina a mugun nutse, cike da tattali da kulawa bamma san sanda na sakar masa kukan azaba ba jikina na matuƙar rawa.....

❤★❤★❤

Tun a balcony ɗin take faman jera manya-manyan ashariya wa Maash. Koda ta afka bedroom ɗinta gaba ɗaya ta kasa haƙuri saboda yanda zuciyarta ke mata hanƙoro. Wai mi yaron nan ke shirin maidasu? Yʼan iska ko mi? Yanzu har Ummu-Hidaya ta haifi abinda zaifi ƙarfinsu kenan. Yarinyar da aka haifa a gabansu, balle shi karan kaɗa miya. Kai wlhy bazai yiwu ba. Dole ne ta ɓaro aikin da dolema ayita ta ƙare a gobe. Ina dalili Rubayya ta sakata aikata abinda ke neman juyewa da ita. Banda yaron nan ƙwallon ɗan iska ne ka haikema yarinya amma ka koma kana wani abubuwa irin ga matarka ɗin nan kayi first night ko. To wlhy daga daren yau zuwa gobe sai ta tada hankalin kowa na gidan nan sai dai anyita ta ƙare. Munafukai kowa

yayi shiru da bakinsa irin komai ma bai faru ɗin nan ba. Waya ta jawo, ta shiga daddanawa. Number baba prof ta kira. Sai da ta kusa tsinkewa ya ɗauka cikin alamun wanda ya fara barci. Kuka ta fashe masa da shi a maimakon sallama. Cikin tashin hankali ya shiga tambayarta abinda ke faruwa?. Amma taƙi magana sai kuka. Sai da ya mata tsawa cikin tashin hankali kafin ta fara magana tana jan sheshsheka.

“Baba wace irin ƙazamar rayuwa kuma ke neman zuwa mana gidan nan. Mun shiga uku Awwab ya ɓalle. Baba kaga kuwa abinda na gani yanzun nan. Ya gama lalata wata gata can kwance a asibiti gashi can kuma yaja wata sashensa zai ƙara. Kuka yarinyar take tana roƙonsa amma bai barta ba. Har magana nayi masa amma ya hauni da zagi, wai bamun damesa yay aure ba, to haka zaita haye yʼayʼan mutane har yʼayʼanmu ma su jira zuwansa. Mu kammu idan bamu kama kammu a gidan nan ba sai layi ya biyo ta kanmu. Baba wlhy Awwab ya gama iskancewa, yaro ya tambaɗe ya lalace, kai ko jinin turawa na yawo a jikinsa. In baiyi bama ai bai cika jikan sifanawa ba (Spain 😂). Wayyo Baba mun shiga ashirin watan zubewar mutuncinmu yazo a duniya. Kʼilama a wannan karon har bbc saita bugamu...”

A rikice Baba yay mata tsawa, dan gaba ɗaya ta gama ruɗar da shi yama kasa yin tunanin daya dace. Kʼitt ta yanke kiran tare da kashe wayar gaba ɗaya. Dariya ta sanya cikin yanayin basanci ta ce, “A'a badai nice ba. Ai sai kaci baban uwarka Alonso Awwab. Gobe-gobe sai ka zama mijin Azizat ɗina. Kwantar da hankalinki yʼar albarka kukanki na kusa sharesa, nima kuma burina ya kusa cika.” ta sake ƙyalƙyalewa da dariya.....✍

Hummm munsha yajin aikin dole ko😂*_TSUTSAR NAMA....!!_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page twenty six

26

.....Fita tayi a sashenta, kanta tsaye tai sashen Paah shima. Wani irin mahaukacin bugu ta dingama ƙofar tana kuka da ihun da sai da kusan kowa ya tashi. A masifar

firgice Paah da Hajiya ƙarama suka fito. Ko bari su tambayi ma abinda ke faruwa batai ba ta hau rusar kuka da sanar musu kamar yanda ta sanar da Baba prof ta waya. Hankalin Paah da Hajiya ƙarama duk tashi yayi. Suka shiga salati da sallalami. Dai-dai nan sai ga kiran Baba prof ta wayar Uncle Abdullahi da suma bugun Hajiya Mammah ɗinne ya tashesu. Kururuwar da Hajiya Mammah keyi har yanzu ya sashi tsawatar musu kasancewar a hansfree Uncle Abdullahi ya saka wayar.

“Miyasa bazaku nutsu ba ne wai. Baku da hankali ne sai kowa ya fahimci abinda ke faruwa. Darene fa? Gida cike da ma'aikata. Idan abinda ke faruwa bai zama tonon sililin ba wannan shirmen naku da tatarako ai zai zama. Kowa ya wuce ya kwanta. In sha ALLAHU da safe zan shigo gidan zai ci ubansa ne ai”.

Kowa ya gamsu da bayaninsa, yayinda Hajiya Mammah ke kwasar dariya a zuciya. Paah kuwa jiri ma yake jin yana neman ɗibarsa. Sai da ya dafe bango dan tashin hankali. Ita kanta Hajiya Ƙarama zuciyarta sai mutsu-mutsu take a ƙirji. Ji take kamar tayi tsuntsuwa a sashen masu aiki dan ta tabbatar ita dai ba Samraah ɗinta yaron nan ya sake haikemawa ba. Sai dai babu damar yin hakan. Dole ma sai itace ta kama Paah suka koma ciki. Uncle Abdullahi da matarsa ma suka koma nasu sashe. Itama Hajiya Mammah ta juya tana dariyar ƙeta. Ranta fes wlhy dan gwara ayita ta ƙare.....

😂😂Hegiya Hajiya Mammah kin iya haɗa guri ko, to bari muga yaya wasan zai kaya.

❤❤

Ni a karan kaina ban san iya adadin kukan da naci ba. Dan gwara waccan ranar daga ƙarshe suma nayi, yau kuwa har ma fata nake ko zan suman na samu sassauci amma sumar taƙi zuwa. Azaba iya azaba da kwantata badai baki ba. Ban sani ba, ko hakan ya faru ne dalilin ina cikin tsoro da kuma ban gama farfaɗowa a waccan baƙar wahalarba oho. Duk da a yau komai yana yinsa gently ne ni banga wannan gentle ɗin ba sam. Kuka na gidan duniya na shashi har ina jin idanuna kansu sun min wani uban nauyi. Roƙo magiya harda cizonsa nayi amma bawan ALLAHn nan sai da ya kai inda yake buƙata. A Bathroom ma wani sabon kukan na sha, amma sam baiji tausayina ba sai da ya tabbatar ruwan zafin ya ratsani sosai yanda ya kamata sannan ya taimaka min na tsaftace jikina. Yanda ya ɗaukeni da kansa ya

kai haka ya sake ɗakkoni ya maido saman gadon. Da ƙyar na amshi magani daya bani, ina gama sha ya kwantar dani, bamma san barcin wahala yay awan gaba dani ba. Dan tun ina jinsa sama-sama yana salla har nayi barcin ban san ya dawo saman gadon ya kwanta ba sai asuba....

★★

Yanda Maash bai bari sunyi wani barcin kirki ba a wannan daren haka mafi yawan iyayensa basu runtsa ba. Hajiya Mammah dai na sake ƙulla abinda zata zo da shi gobe idan ALLAH ya kaimu. Paah na cikin tashin hankali da damuwa tare da nadamar abinda yake aikatawa. Dan shi kawai zuciyarsa na bashi TSUTSAR NAMA CE TA ZAMA NAMA. Ɓarnar da yake aikatawa ce tai naso wa gudan jininsa. Shiyyasa masu iya magana ke cewa ƊAN GADO HAR YA ZARTA. A wannan gaɓar kam ya yarda. Dama ance zina na bibiyar jini, idan kayi da yar wani sai anyi da taka. To shi bashi da ɗiya mace, shine ALLAH ya jarabci ɗansa babba da wannan ta'asar da ƙila zata zama sanadin tashi fallasar shima. Harga ALLAH bai taɓa fyaɗe ma kowa ba, amma fa tun yana secondary school ya fara neman mata. Saboda irin rayuwar da suka tashi, rayuwar turai. Uwa babu kwaɓa uba ba tsanani. Dan Ummansu nada faɗa, amma gasu yayanta soyayyace ziryan take musu. Garama mahaifinsu, yakan ɗan yi faɗan idan yaga abubuwan sunyi yawa. Shi kansa bai san adadin matan dayay mu'amala da su ba a rayuwarsa. Tun ma yanayin mai aji har gashi ya koma mu'amala da mai aiki. Dan da Siyama kawai yake mu'amala a gidan, hasalima ya santa ne tun kan ta fara aikin, koma yace saboda shi ta dawo aiki gidan, dan tace suyi aure yace a'a, shine ta zagaya ta samu aiki a gidan sai kawai ganinta yayi. Ya shiga matuƙar shock a lokacin, amma da yake yar duniya ce sai da ta maida shi ruwa a kanta duk da kuwa shi in har ya mu'amulanci mace ya rabu da ita da wahala ya koma. Amma akan Siyama sai tarihin ya canja, dan ta rantse masa in har yay sanadin data bar gidan sai ta tona masa asiri, shiyyasa ma ya barta saboda ya fahimci yarinyar hatsabibiya ce kwarai da gaske. Amma yau sai gashi ɗansa nayin yanda yaso a cikin gida batare da kunya ko shakkar wani ba.

Ita ko Hajiya ƙarama tashin hankalinta kada ace Maash ya sake haikema yar gaban goshinta Samraah ne. Har bayi ta shiga ta gwada kiran Mama Balki sai kuma ta fasa, saboda tunawa da Mama Balki nada miji fa. Ita dai damuwarta kawai kada Maash ya sake taɓa mata yarinya.

Acan Uncle Abdullahi da matarsa sun shiga wasi-wasi. Dan su zukatansu sun fara nusar da su anya kuwa ba magauta bane suka asirce Maash ɗin ke wannan irin

ta'asar babu kunya babu tsoron ALLAH a cikin gida kamar wata rayuwar kafurci. Kai da sakal fa. Yaron nan na buƙatar manyan malaman ruƙuya a kansa. Ita dai Maman Malika ma harta fara batun maida Malika Niger sai abubuwa sun dai-daita. Idan har abinda Hajiya Mammah ta faɗa Awwab ɗin ya faɗa to lallai basuga ta zama ba kuwa. Dole abar gidan da yammatan yaran nan guda huɗu zankaɗa-zankaɗa. (😂 Yayanmu kaga idi. Kowa zai fara killace ɗansa saboda kai, wannan aiki yayi tsamari).

A ɓangaren Baba prof shima ba barcin daɗin ran yayi ba. Dan ya jima ma bai runtsa ba bayan ajiye wayar da yayi. Har gwada kiran wayar Maash yay amma ba'a ɗauka ba (😂ina zai ɗauka kuwa kandala ta kanainayesa, danginta na murna an kwace mana Yayanmu). Haka ya dinga kai-kawo kamar mai Safa da marwa, sai da yaji ƙafafunsa na neman sagewa ya haƙura ya kwanta. Aiko asubar fari ya miƙe dan ko'a barcin nasa mafarkin Maash ɗin kawai yake yi ya haikema yarinyar mutane (kuji masifa. Yo banda sa kai a uku kai tsoho ina ruwanka😝).

□□□□□

Saukar iska mai sanyi akan idanuna ya sani buɗesu a hankali dan sun min nauyi jingim saboda kukan dana sha. Ga barci da nake ji matuƙa dan sam ɗan wanda nayi bai wadaceni ba. Dishi-dishi nake ganin abinda ke gab da ni, cigaba da huramin iskar ya sani ƙarasa buɗe idanun sosai. Fes suka shige cikin nasa da sukai wani irin fitowa blue sosai, hakama golden ɗin daya ratsasu ya sake yin garai-garai tamkar zinare na ƙyalli a cikin glass. A hankali na ƙoƙarin sake maida nawa zan kulle saboda wani irin kunya ne ya baibayeni.

Cike da karsashi ya ɗaura soft hannunsa saman fuskata yana sake matso da tasa fuskar gab da tawa, har hancinmu na gogar juna. Da silent muryar nan tashi mai fita acan ƙasan maƙoshi kamar abin dole ya furta, “No! Baby. Open your eyes”.

Baki na taɓe kamar zanyi kuka. Cikin shagwaɓa da ban san ni kaina nayi ba na ce, “I'm not baby”.

Sake manne fuskarsa da tawa yayi, tare da sake maida muryarsa can ƙasa ya ce, “Yes you are not ni shaida ne”. Yanda yay maganar yana kai hannunsa saman jikina da sauri na saka nawa na ɗan buge nasan ina sake ɓata fuska zan saki kukan. Na

kuma janye fuskata da ga jikin tasa na juya baya. Zafin da naji ya sani sakin yʻar ƙaramar ƙara. A hankali ya kwanto ta bayana duk da ma ya rufeni gaba ɗaya yʻar tsitt dani a jikin nasa. A cikin kunnena ya furta, “Still Pain?”.

Maimakon amsa kuka na sakar masa. Sautin murmushinsa naji a cikin kunnena, sai kuma ya saka hannunsa a saman fuskar tawa ya shafo hawayen. Hannuna nasa na ture nashin in ƙara ƙarfin kukan. Baice komai ba ya miƙe, har nayi tunanin ya barni ne sai naga ya zagayo ta gabana. Duvet ɗin da nake ciki ya yaye, tare da duƙowa ya ɗagani gaba ɗaya. Luff na kwanta a jikinsa tare da lumshe idanuna. Sai da muka shiga bayin na buɗe ganin yana ƙoƙarin cewa zai min wankan ma. Da sauri cikin shagwaɓa na ce, “Ni ka fita zan iya”.

“Kin tabbatar?”.

Ya faɗa cikin tsatstsareni da idanu. Kaina kawai na jinjina masa. Shima sai baice komai ba ya juya ya fita, yana gab da ƙarasa ficewar ya ce, “Ki tabbatar kin shiga ruwan nan”. Daga haka ya ficewarsa. Ajiyar zuciya na sauke mai ƙarfi, ni ba haushinsa nake ji ba. Tausayin kaina kawai nake ji, in dai haka zata cigaba da faruwa wlhy na kaɗe har ganye na. Dan al'amarin sam bashi da sauƙi. Ban cuci kaina ba na nutsu na gyara jikina yanda ya kamata, kamar kuma yanda Mama Balki ta koya min hakama Doctor. Sai kuma naji na ƙara jin nutsuwa. Wanka nayi na ɗauro alwala. Cikin sanɗa da jan ƙafa na fito. Naji daɗin ganin babu kowa a ɗakin, sai doguwar riga mara nauyi da hijjab dana samu a saman sofa. Ɗauka nayi cikin sauke ajiyar zuciya na saka dan har shida da wasu mintuna. Sallar asuba nayi, koda na idar duk yanda naso yin karatun Alqur'ani kasawa nai, anan inda nai sallar na ɓingire barci. Bamma san ya shigo ya ɗagani ya maida a saman gadon ba.....✍
*_Typing_*

*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page twenty- seven

27

.....Kamar yanda Baba prof yay alƙawari ƙarfe shida da kusan rabi a Maash Mansion ta masa. Sosai ma'aikatan gidan sukayi mamakin ganinsa da wannan uban safiya. A ƙasan rai kuma kowa na tunanin ko jikin Hajiya Babba ne ya sake motsawa. Dan in har ba ciwon Hajiya Babba ba baka ganin Baba prof ɗin a gidan sai dai wani babban dalili. Fitowarsa a mota dai-dai da fitowar Maash daga sashensa sanye cikin farare ɗin tas sports wear. Gefensa Laalah ne sai baƙin bluetooth daya manna a kunnesa ƙafarsa da sport shoes na kamfanin adidas. Kallon kallo aka tsaya tsakanin shi da Baba. Kafin shi Maash ɗin ya fara rissinar da nasa idon a yanayin nan nasa mai ban haushi. Inda Baban yake ya ƙarasa, ƙasa-ƙasa ya ce, “Good morning grandpa”.

Danne komai Baba prof yayi, cike da kulawa ya amsa masa da, “Morning dear, how was your night?”.

A takaice ya ce masa, “So good”.

“Hummm Masha ALLAH haka ake so ai. Amma inaga zaka bar fita Jogging ɗin nan kamar?”.

Cikin wani irin tsare kakan nasa da ido ya furta, “But why?”.

Haɗe fuska Baba prof yay dan karma ya masa gardama. Kai tsaye ya amsa masa da, “Nazo ne muyi magana mai muhimmanci”.

Shima fuska Maash ɗin ya ƙara tsukewa, tare da kallon agogon dake ɗaure a tsintsiyar hannunsa baƙi mai ƙyau. Kansa ya ɗan girgiza fuskar na sake komawa tamau. “No grandpa am sorry. Ka shiga ciki, jus 30minutes am come back”. Baima

jira mi Baba prof ɗin zai ce ba ya raɓashi ya wuce. Matuƙar sosuwa ran Baba prof yayi, dan ko iya cewa komai baiyi ba ya bisa da kallo kawai shi da karen nasa. Sai guards ɗinsa da suka take masa baya. Gefen lips ɗinsa ya ɗan cija kawai yana nufar hanyar babban sashen. Duk ta inda ya gitta masu aiki zubewa suke suna gaishesa. Ɗaya bayan ɗaya masu gidan suka fara fitowa suna gaishesa suma tunda duk sun san da zuwansa. Su dai yaran basu san mike faruwa ba dan ko barci ba tashi sukai ba balle ai batun yin sallar asuba. Hajiya Mammah tayi zaram zata wuce kiran Maash Baba ya dakatar da ita. Sanar musu Maash ɗin ya fita yayi, amma yanzu zai dawo. Sai a lokacin Paah ya ɗan sauke ajiyar zuciya. Tashi yay ya haura sama ya duba Ummie. Barcinta ma take hankali kwance. Sai mama Balki dake ɗan siɗaɗowa da tayi sallar asuba ta gyara sashen ta mata wanka ta bata abinci. Cikin girmamawa ta gaida Baban. Shiko yanata faman saka mata albarka da wannan ƙoƙarin nata. Murmushi dai ta dinga yi ita dai kawai.

Bayan ya dawo ƙasan suka ɗan fara tattaunawa akan al'amarin Maash ɗin. Hajiya Mammah nata sakko batun Azizat, acewarta hakan shine kawai maganin wannan matsala data kunno musu kai. Uncle Abdullahi ya bata goyon baya, shi dai Paah da farko shiru yayi, sai da Hajiya Mammah ta balbalesa da masifa ne ya ce shifa bawai baya so bane. Kawai yana tunanin ta yanda za'a sake tadawa Awwab ɗin maganar ne baya kuma anyita a watannin baya sai dai rai ya ɓaci kawai a banza. Kowa ya fahimci uzirin Paah ɗin, dan taurin kan Maash a bayyane yake ga kowa na gidan. Dan in fa har bashi yace zai yi abuba babu ubanda ya isa ya sanya shi ya yisa. Hajiya Mammah dai ta nuna musu wannan karon za'a masa zagir-zagir ne, dolene su nuna masa su suka haifesa ba shine ya haifesu ba. Domin kafa hujja aka aika Maman Malika wai taje sashen Maash ɗin ta duba wace yarinya ce ya kai. Taso noƙewa, amma girman suruki ya hanata dole ta miƙe ta tafi, babu jimawa ta dawo ta sanar musu yafa kulle ƙafarsa.

“Tunda yasan miya ajiye ba dole ya kulle ƙofa ba. Ai mudai Ummu-Hidaya ta haifa mana bala'i cikin zuri'a”.

Duk da furucin Hajiya Mammah ɗin baima kowa daɗi a wajen ba babu wanda ya tanka mata. Kusan a dai-dai lokacin ne kuma Maash ɗin yake dawowa gidan. Yayi zufa sosai sai furzar da huci yake. Dan yayi amfani da ƙarancin lokacin ne yay gudu sosai. Kai tsaye ƙofar babban sashen ya nufa, bayan ya amshi bottle water ɗin sa da towel a hannun Shu'aibu, Laalah biye da shi ya shiga da sallama ciki-ciki. Tuni su Afrah dake gyaran sashen sun fara zubewa suna gaishesa da girmamawa. Sau ɗaya ya amsa musu kawai yana ƙarasawa ƙaramin falon da iyayen nasa suke, wanda in ba irin meeting ɗin nan ba da wahala ma kaga wani a cikinsa. Kasancewar an rabashi da glass ne da babban yasa ko damuwa da kai-kawon masu aikin basu yi

ba. Dan ba'a jiyo magana, na waje kuma baya ganin na ciki, na ciki ne ke hango ma waje.

Kowa bai kalla a cikinsu ba ya kai zaune a kujerar farkon shiga falon da babu kowa a kai. Ruwansa ya ɗaga sama yana tsiyayawa a baki kamar daya shigo bai ga kowa ba. Sai da ya sha sosai ya ajiye a gabansa, karensa nata gefen ƙafafunsa ya kwanta shima yana huttan gudun da suka sha yau ɗin. Sai lokacin ya ɗan kalla iyayen nasa da duk suka zuba masa ido. A taƙaice ya janye yana cigaba da goge wuyansa zuwa ƙeyarsa ya furta, “Good Morning”

Paah ɗin ne kawai ya iya ƙarfin halin amsa masa da Uncle Abdullahi da Maman Malika. Amma Hajiya ƙarama da Hajiya Mammah wani shegen kallo suke binsa da shi. Na Hajiya ƙarama ba'a bayyane ba, amma ita Hajiya Mammah kamar idanunta zasu faɗo kansa. A masife ta ce, “Eh ai ba sai ka nuna mana kai tarbiyanka bai cikaba Awwab. Mune kakema gaisuwa like wasu sa'anninka ko. Kaje ai duniya ce zaka gani, wanda baima zo ba jiransa take”.

Ko kallon inda take baiyi ba ma. Sai zamansa ya gyara cike da ƙasaita yay crossing ƙafafunsa ya jingina kansa da kujera ya wani lumshe idanu. Takaici, baƙin ciki, haushi. Babu wanda bai kumesu ba. Sai dai babu wanda ya tanka sai Baba prof ne ya ce, “Awwab!”.

Batare da ya ɗago ba ko gyara zamansa ya ce, “Na'am”.

Sake danne zuciya Baba prof yayi ya cigaba da faɗin, magana ce mai muhimmanci ta taramu anan, kuma amsa muke buƙata daga bakinka, ba wannan shirun naka ba. Wancan karon kata mana zame-zame, na barka ne kawai dan na tabbatar da abinda akace kayin, ashe kuwa bazaka fasa ba tunda gashi ka maimaita. Kana ganin wannan rayuwar ta dace da kai kuwa Awwab, kaifa muka dinga fama da kai yin aure watannin baya amma ka nuna baka buƙata, why kuma yanzu ka zaɓi wannan rayuwar? Bayan tako ina ALLAH bai tauyeka ga yin auren ba? Na farko ya faru, anyi na biyu, to baza'a sake na uku ba, dan haka mun yanke shawarar daga nan zuwa next month za'a ɗaura maka aure da yar uwarka tunda a wata kusan tara ka kasa samo matar sai ka fara shiri”.

Wani shegen murmushi Maash ya saki a bazata. Dukansu sai da murmushin ya basu mamaki, hakan yasa duk suka zuba masa ido cikin ɓacin rai. Kasa haƙuri baba prof yayi yanzu kam cikin ɓacin rai ya furta, “Oh dariya ma na baka ko?”.

Murmushin ya sake saki yana mai buɗe manyan idanunsa a kansu. Yanda sukai wani tar-tar blue ɗin ya fito sosai zai tabbatar maka da baya tare da kowace irin damuwa. Cikin halin ko'in kula ya ɗan lumshe idanun ya buɗe, tare da motsa lips ɗinsa a nutsensa ya furta, “Shike nan zan iya tafiya?”.

Yanzun kam hatta Paah sai da ya zuba masa ido. Yayinda cikin masifa Hajiya Mammah ta shiga tafa hannaye da jera salati. Ta ce, “Ni Nafisa ALLAH kana gani, Awwab wai anya kuwa kai kam ba shaiɗani bane? Gaba ɗaya neman maida mu watsatstsu kakeyi ma dai na kula. Yanzu nan a duk zantukan nan da baba yay maka saboda sheɗanci da raini baka da abin cewa. Magana ta ALLAH Mu'azz ka haifa mana jaraba a family”.

Ko motsi baiyi ba balle yama nuna yasan mi take cewa, sai da yaja fin mintuna biyu sannan ya wani irin buɗe idanunsa, kai tsaye a kanta ya sauke su, cikin wani irin salon kallon raini, gaba ɗaya sai ta daburce ta fara kame-kame da zaginsa. Ɗauke kansa yay daga gareta ya maida kan Baba prof, cikin motsa lips a daƙile ya furta, “Daga farkon fara wasan har zuwa yau ai duk itace Director, ni ina amsa sunan actor ne kawai. Dukan amsoshin da kuke son ji a gareni ita ke da su.”

Wani irin kuka Hajiya Mammah ta fashe da shi tana zagin Maash da yaɓo maganar da duk tazo bakinta. Ko kallo bata sake isarshi ba ya miƙe abinsa yana mai ɗaukar bottle water ɗin sa. Da sauri Laalah ya miƙe shima. Cike da takun nan nasa na ƙasaita ya nufi ƙofa sai da ya kama ƙofa zai buɗe sai kuma ya ɗan dakata, kamar wanda yay mantuwa ya juyo, “Oh nace ba. Zan baki first and last warning. Idan kikace zaki cigaba da bin sawuna, wlhy wataran sai taɓo mai danƙo ya riƙe miki ƙafa ta yanda har sai naje na dawo daga inda zanje na sake dilmiyaki a ciki, kona datse ƙafafun kowa ya huta.” ya kare maganar cikin karkaɗa yatsarsa, daga haka yay ficewarsa kamar baiga kallon da suke binsa da shi ba.....✍

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

28

.....Tsuru-tsuru kawai sukayi suna bin ƙofar da kallo, sai Hajiya Mammah ce ke zazzaga masifa cikin borin kunya. Dan sosai maganarsa ta ƙarshe ta wani irin shigarta. Ganin kallon da Baba prof ke mata yasa ta miƙe. Murya a ƒan zafafe ya ce, “Koma ki zauna Nafisa”.

“Amma Baba kana fa jin abinda ya faƒa min, wlhy sai naci uwar yaron nan a gidan nan. Yanzu har lalacewar wannan gidan takai kamar Awwab ya gaya min baƙaƙen magana a gaban Mu'azz amma yay kamar baima ji ba. Ba shi ba hatta uwarsa a gabana aka haifeta.”

Cikin damuwa da ƒan ɓacin rai Paah ya ce, “Amma Adda mi kike so nace muku?. Duk dai mai hankali yaji wannan furucin na Muhammad zai fahimci akwai wani abu a tsakaninku ke da shi. Tabbas Muhammad bashi da ragowa, kuma in ransa ya ɓaci komai yazo bakinsa faƒa yake, amma tunda muke da shi bai taɓa maidama wani murtani ba a cikinmu sai yau. Duk kuwa abinda kiga Muhammad ya magantu a kansa to lallai wannan abun ya kai karen kure. Kuma ni kam gaskiya zuwa yanzu zuciyata ta fara bani akwai abinda yaron nan ke ɓoye mana, inda ace abinda ya faru a farko ne kawai zan iya yarda ƙaddara ta kaisa ga aikatawa. Amma muyi tunani, Muhammad fa duk da tsagerancinsa bazai zauna yana lalata yara ba irin haka a cikin gidan nan, dan duk da mahaifiyarsa na'a halin rashin lafiya bai haƒa mutuntakarta da komai ba. Mudai ƙara bincike gaskiya. Domin mu dukanmu mun san waye Muhammad”.

Da ga haka ya miƙe abinsa ya fice shima. Shiru falon yay babu wanda ya iya motsawa. Sai Hajiya Mammah dake wani irin cika da batsewa da famar jinjina kai. Ta bakin baba prof kowa ke son ji amma babu alamar zai ce wani abu. Sai ma miƙewa da yay shima ya fice a binsa. Ganin haka shima Uncle Abdullahi da Matarsa suka miƙe. Wani irin shegen murmushi Hajiya Ƙarama da ke kallon Hajiya Mammah ta ƙasan ido ta saki, sai kuma ta mike itama batare da tace komai ba ta fita. Dan ta ciki na ciki ne kawai.....

□□□□

Watanni huɗu kenan Mamy na gida, babu labarin Mansoor tako ina. Gashi Dad baizo gida ba kuma kowa bai sanar mata ya saketa ba ko bai saketa ba. Gaba ɗaya ta fige ta rame saboda damuwa. Dan har ga ALLAH tana matuƙar so da ƙaunar mijinta. Ta tura masa text message yafi sau dubu. Ta kirashi yafi sau dubu goma. Amma babu amsa babu reply na masseges ɗinta. Ga ciwo ya addabeta a tsaitsaye har dai sai da ta kaita da kwana asibiti ranar. ALLAH sarki Attahiru shine tsaye akan komai. Ganin fa yanda jikin Mamy yay tsamari a wannan karon yaje ga Dad ɗin su ya dinga kuka yana roƙonsa ya yafe mata, sannan ko sau ɗaya yazo ya ganta. Dan sam Mamy bata a cikin hayyacinta. Babu abinda take faɗi sai neman gafarar Dad ɗin. Da farko Dad koran Attahiru yayi, sai da yaga yanda ya riƙe ƙafafun nasa yana rabzar kukan abin tausayi sannan. Dan har ga ALLAH a yanzu tausayin babban ɗan nashi yake yi. Attahir akwai haƙuri, gashi da son yʻan uwansa. Ga biyayya a gare su. Yanzu tunda aka fara abin nan yazo neman ma Mamy afuwa ya masa gargaɗin kada ya sake masa maganar ta bai sake koda kwatantawa ba duk da abin na damunsa. Amma kullum dare yana lura da shi sai yaci kuka. Haka kuma zaita salla yana neman ɗaukin UBANGIJI da yima Mansoor addu'ar ALLAH ya karesa a duk inda yake. Shima sai hakan yaja hankalinsa yake tashi yin ibadar daren.

Yanzu da yake roƙonsa duk sai jikinsa yay sanyi, kamashi yay ya rungume. Sun jima a haka kafin ta ɗagosa yana lallashi. Ya kuma tasashi gaba suka je asibiti suka duba Mamy. Abinda Dad ɗin yayi ya faranta ran kowa. Dan duk wanda yasan Mamy yasan ta horu da horonsa matuƙa. Wannan zuwa na Dad shi ya kawo masalaha ga ciwon Mamy, ta dinga jin sauƙi har al'amura suka fara daidaita. Koda aka sallameta sai suka koma gida. Nan ma ta cigaba da roƙon Dad ɗin gafara yaran suka tayata har sai da yace mata ya yafe mata. Ya kuma kafa mata sharuɗa da dokoki. Ko guda ɗaya kuwa bata musa ba a ciki. Doka ta farko data fara bi shine shiryawa sukaje har gidan Abba suka bashi haƙuri tare da neman gafarar Abban da sauran mutanen Gwarzo da basu wuce ba da su Gwaggo Gudidi. Sun so ganin Yaya Musaddiq aka sanar musu ai ya wuce Chaina yau ne ma ranar tafiyar tasa zai bi ta Lagos. Abin ya basu mamaki. Sun kuma tayashi murna. Sun kuma yi alkawarin zuwa weekend zasu je har gwarzo domin bama su Kawu Musa haƙuri, dan su tunda suka zo aka ɗaura aure da su suka kama gabansu tunda bikin bana ɓangaren su bane ba.

Wannan ban haƙuri da su Mamy suka zo sukayi har gida ga ƙonama Mom rai, dama ga baƙin cikin tafiyar Yaya Musaddiq na cimata zuciya. Har ta kasa haɗiyewa sai da tai ta zabga habaici. Da yake dama Abba a ƙufule yake da ita akan tafiyar Baby basu bari ta masa sallama tama danginsa ba ya ce idan har Mom ta sake cewa ko uff a bakin aurenta. Dan ya tsinke sauran igiyoyin biyu da suka rage. Wannan magana ta matuƙar girgiza Mom da duk danginta. Nan fa suka shiga tausarta da

nuna mata kuskurenta. Daga nan akayi zaman sasanci aka sakata bama Abban haƙuri da su Gwaggo Gudidi....

□□❤□□

Tunda ya shigo ɗakin yay tsaye kawai yana kallonta nannaɗe a ƙasa kamar yar mage. Barcinta take hankali kwance. Kaɗan ya ɗan jaa idanunsa kamar zai lumshe sai kuma ya buɗe. Durƙusowa yay ya ɗauketa gaba ɗayanta ya maida a saman gado, kafin ya shiga ƙoƙarin zame mata hijjab ɗin. Firgigit ta buɗe idanunta dake jajur duk sun ɗan kumburo alamar anci kuka an gode ALLAH.

Sosai ƙirjina ya shiga bugawa da sauri-sauri ganin yanda ya ranƙwafo kaina, zaram nayi ƙoƙarin tashi jikina na rawa, sai dai zafin daya ratsani ya sani komawa da sauri na kwanta hawaye na ziraro min. Cikin ɗan jujjuya masa kai, lips ɗina da suka sha wahala a wajensa na rawa muryata a ɗashe na ce, “Please Ya Awwab don't do wahala for me again. Wlhy zan iya mutuwa. I'm just 23years only zakai child abuse fa”.

Shiru bashi da alamar cewa uffan, sai idanunsa masu tsananin kaifi da ya zuba min kawai kamar zai cinyeni da su. Cikin kuka sosai na sake buɗe baki zanyi magana ya ɗaura yatsarsa manuniya akan lips ɗin nawa yana mai sake matso da fuskarsa gab da tawa ya ce, “Shiii! Oya sleep”. Ya ƙare maganar can cikin maƙoshi da ɗaura hannunsa ya rufe idanuna. Babu musu na rufe ɗin duk da a cikin tsoro nake. Tun ina ɗari-ɗari har wani barci mai daɗin tsiya yay awan gaba da ni saboda yanda yake shafa kaina a hankali.

Ganin yanda ta fara sauke numfashi a hankali alamar tayi barci ya sashi yin ɗan guntun murmushi. A hankali ya furta, “You are a tiger, Samrh”. Sai kuma ya sake sakin murmushin gefen baki saboda tuno kalmar child abuse data faɗa. Sam yarinyar nan bata jin magana. Ga baki kaman parrot. Vibration ɗin da wayarsa keyi alamar shigowar kira ya katsesa da ga kallon da yake mata. Dan kallon wayar yay dake a kan side drawer. Sai da ta kusan tsinkewa kamar abin dole kafin ya kai hannu ya ɗauka. Ɗagawa yay ya kai kunnensa yana ƙoƙarin barin wajen. Koda Juliet da tai kiran ta gaishesa a taƙaice ya amsa mata. Bata damu ba ta fara masa bayani kan aikin da ya sakata. Ta tabbatar masa ta kammala komai yanzu haka jirgin da zai taho da shi ya ɗakko hanyar Nigeria. Cikin wani irin yanayi mai wahalar fassara ya lumshe idanunsa dake canja launi. Shi kaɗai ya san mi yake ji a zuciyarsa, amma

zai jure in sha ALLAHU. Sunayin sallama kiran Hayatu na shigowa. Gaisawa sukai shima sannan ya bama su Yaya Musaddiq suka gaisa. Kasancewar tafiyar ta Musaddiq sai dare ma ya bama Hayatun umarnin zagayawa da su suga gari zuwa anjima sai ya kawosu nan. Dan yau shi bazai fita ko ina ba zai yini a gida.

Murmushi Hayatu yayi da ga can, amma duk da haka sai da ya tambayesa ko baida lafiya. Dan yasan abinda zai iya hana ogansa kuma yayansa fita ba ƙarami bane. A taƙaice yace masa no kawai ya yanke wayar, Hayatu ya jima shiru yana nazari sai kuma yay yar dariya. Anya kuwa! Anya ogan nasa bai faɗa lobayyar pepper ƙanwar tasu ɗin nan ba. Rashin mai bashi amsa ya sashi haɗiye komai ya cigaba da sabgarsa.

Shi kam koda ya kammala wayar shiru yay a cikin kujerar lafe na kusan mintuna ashirin, kafin ya miƙe a hankali ya bi ƙofar dake sadashi da Ummie, ko'ina fes sai ƙamshi yake, ganin kwanikan abinci ya sashi tabbatar da har ta karya. Kusa da ita ya ɗan zauna ya shafa kanta dan barcinta take hankali kwance. Ga wani irin annuri da fuskanta keyi ƙyawunta da dauɗa ya dusashe na sake fitowa. Hawaye ne ya cika masa idanu, amma sai ya haɗiye su dan yan mazan maza ne akoda yaushe. Ya ɗan jima a ɗakin har Mama Balki tazo ta samesa duk da yanda kansa ke juya masa da ciwo. Bayan sun gaisa yana ƙoƙarin danne damuwarsa da ciwon da kansa ke masa yay mata bayanin a saka cikin yaran can wasu su gyara sashen Fahad. Yana gama faɗa ya miƙe da sauri ya fice a ɗakin kamar wanda ake tunzurawa. Da kallo Mama da har tsigar jikinta ke tashi da jin wannan batu ta bisa. Sai hawaye sharrr suka shiga ɓulɓulo mata, ga murmushin farin ciki. Wani irin ƙaunar Samraah na ratsa mata zuciya. Yarinyar nan ta cika alƙawarinta kenan. Dan dama ta mata alƙawarin sai ta masa maganar dawowar Fahad ɗin gida. Kasa haƙuri tayi sai da ta koma ta sanarma mijinta. Shima farin cikin ne ya dabaibayesa har murmushi ya gagara barin fuskarsa. Ranar da wannan farin cikin suka yini, tuni kuma an saka masu aiki gyaran sashen Fahad dake manne dana Maash ɗin batare da kowa ya sani a gidan ba. Dan su suna can ma ran kowa ɓace da abinda Maash ɗin ya musu yau.....✍ *_ TSUTSAR NAMA....!!_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page twenty-nine

.....A hankali Maman Malika da tun da suka dawo sashensu ta ɗago ta kalla mijinta. Shima dai zaune yake shiru da alama akwai abinda yake tunani. Agogo ta kalla sannan ta sake kallonsa. Murya a sanyaye ta ce, “Abban Muhseen yau bazaka fita aiki bane wai? Time fa yaja sosai”.

Numfashi ya sauke a hankali, kafin ya kalleta fuskarsa na nuna damuwa sosai. “Zanje Mubeena. Al'amarin gidan nan ne ya fara damuna wlhy. Daga wannan sai wannan. Ga yaron nan sam baya ganin girmanmu. Shi kuma Yaya baya ƙaunar laifinsa sai ma kiga kamar yana tsoron sa.”

“Humm Abban Muhseen ba tsoro bane ba. Sannan wlhy Awwab bawai baida mutunci bane ko kunya. Yaron yana cikin damuwa matuƙa. Ku kuma kun kasa fahimtar hakan. Kowannenku abinda ke gabansa kawai yake yi. Yanzu ko maganar nan daya gayama Adda fa abin a dubace. Dan babu rami miya kawo rami? Tabbas akwai abinda Addar ta sani game da abinda ke faruwa. Idan fa baka manta ba ko waccan ranar ita ta fara fasa zancen yama yarinya fyaɗe, duk da ana cikin tashin hankalin zuwa kamashi ita ba wannan bane damuwarta. Yau kuma itace fa ta tashemu a barci jiya. Kƙarfe sha biyu da wani abu bata kwanta ba mi take yi? A barshi ma batai barcin ba, miya kaita sashen Awwab har tasan yana aikata wani abu? Mufa buɗe zukatanmu mu kalla gaskiya a matsayin gaskiya in ba hakaba ALLAH zamu yi dana sani. Kadai san halin Adda ai da fitinarta, musamman daya kasance burinta a gidan nan Awwab ya auri Azizat. Baka tunanin zata iya shirya komai dan hakan ta kasance tunda an bisa ta lalama, an bisa ta tsiya duk yaƙi. Sannan na fara ji a jikina akwai abinda Awwab ke ɓoyewa a gidan nan. Babu yanda za'ai duk rashin kunyarsa ya dinga lalata yara a cikin gida mudai nemo gaskiya.”

Sosai maganganunta suka shigi Uncle Abdullahi. Yay shiru yana nazarin kowane harafi dalla-dalla da yi masa fashin baƙi....

□□□□□

Tunda ta iso asibitin ta gagara taɓuka komai. Sosai abinda ya faru a gidan keta mata faman kai kawo a zuciya. Kalaman Awwab sun farkar da ita wasu abubuwa. Tabbas sau biyu tana kama Hajiya Mammah ta fito a sashen Awwab, na farko ranar da ta aiki Yarinyar nan da abinci, na biyu daren ranar da abin ya faru kusan misalin

ƙarfe ɗaya ta fito daga ta backyard kamar wacce ke a firgice. Abinda yasa a lokacin bata maida hankalinta a kanta ba itama daga wani waje ta dawo. Abu na uku Hajiya Mammah ta damu akan zancen fyaɗen nan a safiyar ranar, sannan jiya ma itace tazo musu da zancen ga Awwab da wata. Da farko bata damu ba, sai yau da safe data bincika yarinyar nan a sashen masu aiki akace mata bata dawo ba ai. Bata samu damar ƙarasa binciken ba Baba prof ya iso gidan..

Mikewa tai tana mai girgiza kanta, dolene taje ta ƙarasa binciken data fara kafin wankin hula ya kaita dare. Daga nan tana buƙatar yin magana da Yallaɓai a wannan gaɓar. Handbag ɗinta ta ɗauka ta fice a office ɗin. Ko kallon tulin patients ɗin dake zaman jiranta batai ba dan hankalinta ma baya a kansu gaba ɗaya.....

□□□□□

Barci sosai nasha. Dan ban tashi farkawa ba sai wajen sha biyu. A hankali na buɗe idanuna bakina na ambaton sunan ALLAH da karanto addu'ar tashi a barci kafin na yunƙura da ƙyar na tashi zaune saboda ciwon da illahirin jikina ke mun. Sam banyi tunanin yana a ɗakin ba, dan haka na miƙe cikin ƙarfin hali saboda wani irin fitsari nake ji sosai. Wani irin motsawa zuciyata tayi sakamakon saukar idanuna a kansa. Zaune yake cikin sofa kamar wani saraki. Laptop ɗin jarabar a saman ƙafarsa sai dai ya saka throw pillow sannan ya ɗaurata. Ta gefensa a saman side table ɗin kujerar bowl ne da chocolate a ciki sai mug alamar ansha coffee ko tea. Ledojin chocolate ɗin da yaci ya zubar a ƙasan na bi da kallo, haka kawai sai naji tausayinsa ya kamani. Dan abinda na fara fahimta da shi kamar bai damu da cin abinci ba sai waɗan nan tarkacen kayan chocolate ɗin. Tabbas koda ace bai son cin abincin akwai ƙarancin gatan mai tsayawa ya bashi ya ɗin.. ganin ya ɗan dakata da danna keyboard ɗin computer ɗin alamar yaji a jikinsa ana kallonsa ya sani saurin kauda idanuna da ƙoƙarin son barin wajen, a ko dai-dai nan ya ɗago manyan idanunsa ya sauke a kaina. Basarwa nayi kamar ban gansa ba na wuce bathroom ɗin. Ina shiga na jingina da ƙofa ina mai sauke ajiyar zuciya mai nauyi da godema ALLAH da ya taimaken bai kamani ina kallonsa ba. Wanka nayi da ruwa mai ɗumi sosai na sake gyara jikina yanda ya kamata, dan har ruwan zafin na shiga. Yau banyin walha ba ina barci, alwala nayi dan naga har sha biyu da kusan rabi yanzu. Hankalina duk yana akan su Yaya Musaddiq shiyyasa ban zauna wani noƙe-noƙe ba na fito sanye cikin bathrobe ɗin sa sky blue. Inda na barsa anan na samesa. Sai da na zo gab da shi ya ɗago kai ya kallan. Murya a sanyaye alamar nasha kuka batare dana kallesa ba na ce, “Ina yini”.

Bai amsa min ba, sai idanunsa masu azabar kaifi daya zuba min. Ji nai duk ina neman daburcewa, dan haka nai ƙoƙarin barin wajen amma sai ya miƙa min hannu alamar nazo. Jinai kawai bazan iya musa masa ba, a hankali na fara takawa zuwa garesa, ɗan nesa kadan da shi na tsaya kaina a ƙasa. Soft hannunsa ya ɗaura akan nawa da nake wasa da su ya matsoni gabansa sosai, a bazata na jini zaune a saman cinyarsa alamar ya ajiye laptop ɗin da pillow ɗin. Sake matsoni yay cikin jikin nasa ya rungume tsam har ina iya jin bugun zuciyarsa kaɗan-kaɗan. Luff nayi wata nutsuwa na ratsani.

“Yaya jikin ya daina zafi?”. Ya faɗa cikin silent muryansa a cikin kunnena. Sosai kunya ya sake ƙamani, maimakon amsa masa sai na sake ƙanƙamesa ina ɓoye fuskana a jikin nasa. Kaɗan naji yunƙurin murmushin sa cikin ƙirjinsa. Shiru kusan mintuna biyu ya sake furta, “Kona duba ne?”.

Kafaɗa na maƙe masa da faɗin, “Uhm-uhm” cikin shagwaɓa ina ƙoƙarin tashi. Amma sai ya hanani yin hakan, hannayena ya kama cikin nashi ya zubama fuskata ido sosai yana kallo. Kasa kallonsa nayi ni dan bazan iya jurewa ba sam. A hakan ma ji nake kamar na gudu. Sake maida muryarsa ƙasan maƙoshi yay da kai hannu a haɓata ya ɗago fuskata da ƙyau ya ce, “Look at me”.

Da ƙyar na iya ɗago idanun na kallesan. Cikin ɗan ɗage gira ya ce, “Shin bakin ƴar mutan Gwarzo ya mutu ne kwana biyu?”.

Bakin na ɗan tura masa kaɗan. Girarsa ya ɗan ƙara ɗagewa da jinjina kai ya ce, “I see, bai mutu ba ashe. Yanzu idan su Ya Musaddiq suka zo mi zaki ce da su ya samu wannan idanun da ya kumbura?”.

Karan farko na ɗago na kallesa. Idanun nawa ya sarƙe cikin nashi, kallon juna muke cikin wani yanayi mai wahalar fassara. Jin yanda tsigar jikina ke tashi jinina na yamutsawa ya sani lumshe nawa a hankali. Murya ƙasa-ƙasa kamar mai koyan magana na ce, “Zan ce kai ne”. Na ƙare maganar in ɗan buɗe idanuna kaɗan.

“What a surprise, ni ne fa? To nayi me?”.

Ai babu shiri na buɗe idanun gaba ɗaya ina harararsa da tura baki. Sai kuma na yunƙura zan tashi ina ƙunƙuni. Sake maidani yay ya zaunar ya ce.

“Answer me”.

Shagwaɓe fuska nayi ina kaucema kallonsa na ce, “Ni dai ba ruwana. Ka sakan na saka kaya na je na ga Ummie na”.

Ɗan lumshe idanunsa yay ya sake buɗewa, sai kuma ya ɗan sauke numfashi, kamar wanda ke shirin sakin murmushi ya ɗan taɓe baki. Yatsun hamnuna dake cikin nasa ya ɗan matsa da murza farcen. “Shi wannan hannun yaushe za'a masa lalle?”.

Hannun na kalla nima, sai kuma a hankali nace, “Ai babu lalli ne. Da dai nasan su Yaya zasu zo da sunzo min da shi. Kuma ma ina son wanke kaina ya fara cushewa.”

Kansa ya jinjina min alamar amsawar kenan. Nima sai nai ƙoƙarin miƙewa. Taimaka min yay na tashi, ina shirin barin wajen shi kuma zai maida laptop ɗin sa a ƙafa ya ce, “Mi zaki ci?”. Kallonsa na ɗan juyo nayi muka haɗa ido, sai kuma na kalla ledodin chocolates ɗin da yasha batare da nayi magana ba na nuna su. Idanunsa ya ɗan ƙanƙance a kaina. Sai kuma ya girgiza min kai a daƙilen nan nasa. “Kince ba abinci bane ai”.

“To kaima ai shi kake ci”.

“Humm”.

Kawai yace ya maida kansa ga wayarsa daya ɗauka. Ganin ya kai kunne alamar wani ya kira ya sa na wuce abina dan na shirya. Ban wani jima ba na fito cikin skirt da riga na atamfa. Sosai kayan sun min ƙyau tare da fiddo ainahin surar jikina. Ni kaina sai da na sakarma kaina murmushi ta cikin mirror. Dauri nayi mai sauƙi bayan na shafa turarensa da mansa. Koda na juyo sai na samu ni yake kallo shima. Da

sauri na ɗauke kaina kunya na kamani. A ɗan daburce nace, “Zanje can sashen na ɗakko kayan kwalliyana Please Ya Awwab.”

Sai da ya maida kansa ga aikinsa kamar bazai kulani ba kafin a hankali ya ce, “No”.

Baki na ɗan tura batare dana sake cewa komai ba na nufi gadon. Tsaff na gyarashi, na tattare net ɗin. Dai-dai nan shima ya miƙe ya shiga bathroom. Babu jimawa ya fito alamar yin alwala.....✍*_Typing_*

*_Typing_*

*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page- thirty

30

.....Ina a inda ya tashi ina gyara wajen da tattare ledodin chocolates ɗin da ya zubar naji tsaiwarsa gefena. Juyowa nayi na kallesa, ya ɗan ɗage min gira alamar kallon fa, ƙoƙarin kauda kaina nayi ya kamoni, a bazata naji saukar sumbata a goshina. Idanuna na lumshe a hankali. Shi kuma ya kai lips ɗinsa kan kunnena a matuƙar low voice ya furta, “You are beautiful tiger girl”.

Da sauri na buɗe idanun a kansa. Kamar zan yi kuka na ce, “Tiger fa?”.

Ido ɗaya ya kashe min kawai yay gaba batare da ya amsa min ba. Yana buɗe ƙofar nima cikin shagwaɓa na ce, “Kaima Lion”.

Wani shegen murmushi kawai ya sakar min batare da yace komai ba ya buɗe ƙofar ya fita abinsa. Nima sai na samu kaina da sakin murmushin har haƙorana na bayyana. Sosai murmushinsa ke sakani farin ciki da nishaɗi. Dan yana bala'in ƙara ƙyau a duk lokacin da yayi sa. A gurguje na ƙarasa gyara ɗakin, nasa turare na fito falo bayan nayi salla. Fes na samu ko'ina anan alamar yasha gyara. Sashen Ummie na nufa ta hanyar da yabi da ni daren jiya. Na jima a can dan yau ma har sai da Mama Balki tace naje gasu Yaya Musaddiq nan zuwa harda Falaq. Cike da farin ciki da zumuɗi na tafin kuwa. Tuni na manta da halin da nake ciki saboda farin cikin ganin yɗan uwana duk uku. Nan fa na zauna muka buɗe sabuwar hira, har sai da Aunty Falaq ta tsareni naci abinci wai inji Yaya Awwab. Ni saima abin ya ban mamaki. Sai dai ban ja zancen ba na basar dan tunda na shigo na fahimci baya nan. Bayan sun tafi sallar la'asar nace mu shiga muma muyi a bedroom Aunty Falaq taƙi, nayi-nayi da ita tace ALLAH bazata taɓa iya shiga bedroom ɗin Yaya Awwab ba. Zata je sashen su Mama tayo. Sosai nake mamakin yanda suke mugun girmamasa, sai kuma hakan ya birgeni. Tare muka nufi sashen su Maman da ita. Bayan nama guard ɗinsa magana sun kulle sashen. A hanya muka gamu da Hajiya ƙarama ta dawo maybe daga asibiti ne oho mata. Sai dai muna gaisheta sai ga hajiyar nan data ɗakkoni da ga Abuja ta fito a mota itama. Sosai na zuba mata ido, dan tun ranar birthday ɗin nan ban sake ganinta a gidan ba. Itama kallona take kamar wata tsohuwar mayya. Dan haka na tsuke fuska ataƙaice na gaisheta naja hannun Falaq muka wuce. Har muka shige sashen Mama ina jin idanunsu a kammu su duka biyun..

Koda mukai sallar a sashen Mama Balki muka cigaba da zama. Suma su Yaya Musaddiq nan suka samemu. Sabuwar hira muka sake zamanyi yanzu kam harda Mama Balki da mijinta. Sunata bamu labarin Baba muna jin daɗi, sai gab da magriba Hayatu ya shigo yake cewa sun dawo. Yaya Musaddiq yazo suje ya ƙarasa kimtsawa jirginsa na nine ne. Gaba ɗaya kuma duk sai jikinmu yay sanyi, amma babu yanda muka iya tunda cigaba ne yazo mana. Sai kuma munyi haƙuri zamuci ribarsa. Anan mukai sallar magrib ɗin, sannan muka ɗan sake gyara jikinmu dan muma muna son masa rakkiya airport ɗin. Ana kuwa idar da sallar isha'i sai gasu sun dawo. Nasiha sosai Mama Balki da Baba suka sake ma Yaya Musaddiq, sannan muka haɗu mukai masa addu'a. Ya sake kiran su Abba yay musu sallama har nima muka gaisa. Mun fito muka samu har mitsocin da zamu tafi da su airport ɗin an shirya. Da farko nayi mamaki, sai da naga boss ɗin ya fito alamar da shi za'ai

rakkiyar sannan na fahimci dalilin shirya motocin da yawa haka. Dan kusan mota biyar. Biyu ta guards ɗin sa. Sai Mama da Baba da Yaya Musaddiq suka shiga ɗaya. Hayatu, Falaq, Hafizzullah suma suka shiga ɗaya. Sai ni da shi a ta tsakkiya duk da ba haka naso ba. Amma Falaq ta turani a motar da tsiya-tsiya tana dariya. Waya yake sanda na shiga, dan haka muna haɗa ido nayi saurin kauda kaina. Sai da mukai nisa da gidan sosai sannan ya kammala wayar, batare dana kallesa ba nace, “Ina yini”.

Bai amsa min ba, sai kaifin idanunsa da nake ji a kaina. Kasa jurewa nayi a hankali na ɗago na ɗan kallesa. Caraf kuwa ya cafke idanun nawa a cikin nasa kamar dama mai jiran hakan. Wani irin kallo yake mun mai tada tsigar jiki da saka jini tsinkewa. Bamma san sanda cikin rawar murya da shagwaɓa na ce masa, “Ni ka bar kallona”.

A hankali ya lumshe idanun ya sake buɗewa, sai kuma ya riƙo hannuna batare da yayi magana ba yanzu ma ya jawoni jikinsa kawai ya rungume. Luff nayi dan nima da alama abinda gangar jikin nawa ke buƙata kenan. Tuna bafa mu kaɗai bane akwai driver ya sani saurin yunƙurin tashi, amma sai ya maidani ya sake matsewa. A marairaice na buɗe baki zanyi magana ya dakatar dani.

“Bana son surutu”.

A hankali na sauke ajiyar zuciya tare da haɗiye abinda nake son faɗar kuwa. Dan ji nai bazan iya masa musu ba sam. A hakan muka isa airport ina a jikinsa. Munfi tsahon mintuna biyar bayan isowar tamu kuma kafin ya bari muka fita. Jinai gaba ɗaya kunya ta kamani ganin kowa ya fito ashe sai mune kaɗai a mota. Yaya Musaddiq yaja gefe sukai magana. Ban san mi suka tattauna ba dai naga Yayan nata murmushi da kallonmu. Sai kuma ya ɗan sosa kansa kamar wanda yaji kunya. Daga haka kuma naga shima Yaya Musaddiq ɗin yazo yaja Baba da Mama suka koma can. Anan ɗin ma sun ɗan jima, kowa fuskarsa ɗauke da murmushi idan ka cire uban gayyar da shi daman sai yaso yake murmushin. Shiyyasa da wahala ka gane farin cikinsa da akasinsa sai ka masa farin sani na haƙiƙa. Bayan sun gama zantukansu muma munata hirarmu suka dawo inda muke. Baifi mintuna biyar ba aka buƙaci ganin su Yaya a ciki. Tofa ai tuni kuma kuka ya tashi ni da Hafizzullah. Ganin haka itama Aunty Falaq ta fara. Mama Balki da Hayatu na ta mana dariya. Baba ko sai lallashinmu yake, shiko ai kamar ma bai san munayi ba. Haka dai muna ji muna gani Yaya Musaddiq ya wuce ya barmu da kewa.

Hafizzullah da Hayatu da Falaq can gida suka wuce. Mu kuma muka nufi gida muma inata mita dan nazata yau a wajenmu muma Hafizzullah ɗin zai kwana. Bai dai tanka min ba har muka isa gida. Hakan ya ƙara tunzurani. Dan haka nama rigashi fita a motar. Badan su Mama Balki dake wajen ba ma da bazanje sashensa ba. Nafi mintina goma da shiga sannan ya shigo. Lokacin har na shiga wanka. Na fito na sameshi zaune a bakin gado yana waya. Wucewa nai cikin closet ɗinsa na shirya. Ina fitowa yana shiga bayin shima. Sai na saka sallaya nayi shafa'i da wutri. Na idar na tashi na fita. A karo na biyu na shiga kitchen ɗin sashensa. Kai tsaye store na shiga na ɗakko catton biyu na bottle water na fito. Bedroom ɗin ba dawo dasu. Har lokacin kuma bai fito ba. Gaba ɗaya na fito da ruwan tare da buɗe musu murfi sai dai ban cire su a jiki ba sannan na ɗauka Alkur'ani na fara karatu. Surorin da duk akace suna karya sihiri nake karantowa ina tofawa a cikin ruwan bayan na ɗaɗɗaga murafan. Nayi nisa sosai a karatun sannan ya fito. Duk da nayi mamakin daɗewar tasa a ciki ban kula ba na cigaba da karatuna a nutse...

Sosai karatun nata ke ratsa masa zuciya. Ga yanda zazzaƙar muryarta ke fita cikin nutsuwa da bama komai hakkinsa na wani irin shiga masa har cikin jinin jikinsa. Cikin jin wata irin kasalar dake saukar masa ya ƙarasa closet ɗin sa. Shirin barci yayi shima, ya fito gaban mirror ya saka turare sannan ya ƙarasa saman sofa ya zauna yana satar kallonta ta gefen ido....

Barci nake ji amma tsoron abinda zai iya biyo baya ya hanani tashi naje na kwanta. Koda na kammala addu'oin ma sai na miƙe na kabbara salla. A mamakina sai naga shima ya miƙe ya saka sallaya ya kabbara salar. Mun jima muna miƙama UBANGIJI kukanmu dai sai wajen uku ya katseni cikin bada umarni yace naje na kwanta. Bazan iya masa musu ba. Dan sam banga hayar yin hakan ba a garesa, ga zazzaɓi ya rufeni haka dai na daure naje na kwanta. Duk yanda naso nayi barcin na kasa, sai dai nayi luff a kwancen har ya kammala tashi sabgar yazo ya kwanta. Lokacin da ya sakani a jikinsa wani irin dukan ɗari-ɗari zuciyata ta dinga min, na gama sadaƙarwa yau ma zansha wata azabar sai naji saɓanin haka. Sai ma tadani da yay ya bani maganin zazzaɓi ya sake maidani jikinsa muka kwanta. Babu jimawa kuwa mu duka barci yay awan gaba damu. Koda muka tashi a washe gari babu zazzaɓin, sai dai yanda nake tafiya da ɗan ɗingishi ya sashi min tambaya. Kasa bashi amsa nayi sai idanuna da suka cika da ƙwalla. Shima sai baicedani komai ba ya ƙyaleni kawai yama fita. Kusan ƙarfe goma na idar da sallar walha bayan naje naga Ummie sai gashi ya shigo, kaina a ƙasa na gaidashi, dan rabona da shi tun fita motsa jiki. Kai tsaye yace min ga Doctor tazo dubani. Sosai mamaki ya sani kallonsa, sai dai shi tuni ya ɗauke kansa ma. Ficewa yay abinsa kamar baiga kallon da nake masa ba. A dai-dai nan akai knocking ƙofar, tashi nayi na buɗe, sai ko ga Doctor naci karo da ita. Haka kawai nake jin nauyin matar, dan a haife ta haifi

waɗanda ma suka fini, kaina a ƙasa na gaisheta. Yayinda ta amsa min tana kama hannuna muka dawo cikin ɗakin.....✍

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page thirty-one

31

.....Ina ji ina gani dole na bar doctor ta dubani, kanta kawai naga tana girgizawa cikin damuwa. Sai dai bata iya cewa komai ba tamun allura da buƙatar ganin Mama Balki. Kaina a ƙasa na bata amsar cewar ba'a nan side take ba. Amma za'a iya kiranta a waya ta bari ya shigo. Babu jimawa kuwa sai gashi ya shigo kamar dama kunnensa a kammu yake. Kallo ɗaya na masa na ɗauke idanuna, sai ma kawai na zame na kwanta abina na juya musu baya.

Ina jin lokacin da Doctor ke sanar masa tana buƙatar ganin Mama Balki yace ta sanar masa koma minene ke faruwa karta damu. Ta ɗan jima shiru jimm kafin ta fara masa bayanin daya gama sakani a kunya. Dan bayani ta masa akan lallai ina buƙatar hutu da kulawa. Saboda ciwukan farko basu gama warkewa yanda ya kamata ba. Ga shi kuma an famasu shiyyasa ma nake jin zazzaɓi nake kuma ɗingishi. Badan ma jikina nada ƙyau ba ciwo na saurin warkewa da za'a iya samun matsala. Ta sake tabbatar masa da ina da dauriya, dan ba kowacce mace ke iya ɗaukar irin yanayin ba haka gab-da-gab gaskiya. Ko fargaba da tsotata ya ishi mutum ai. Ta dai jima suna magana da bashi dabarun daya kamata a kula dani domin samun dai-daiton komai yanda ya kamata kuma cikin ƙanƙanin lokaci. Daga haka ta sake bani wasu magungunan ta wuce bayan ta tabbatar masa zata dinga zuwa kullum dubani har na tsawon sati, kuma dan ALLAH na ɗan sami hutu kona satin ne.

Koda ta wuce ban iya motsawa ba. Sai dai ina jin kaifin idanunsa a kaina tsahon lokaci kafin ya shige bathroom. Kafin ya fito barci ya kwasheni. Ban tashi farkawa ba sai gab da azhar. Babu kowa a ɗakin sai ɗan short note da naci karo da shi ya ajiye min a gefen fillon da nake kwance. Na jima ina kallon rubutun mai ƙyau kamar

ba hannu yayisa ba kafin na saki murmushin daban shirya ba. Na ɗan ji daɗin jikina fiye da yinin jiya dana wuni a ƙuntace, kasancewar su Yaya Musaddiq kawai yasa na dinga dauriya. Wanka na ƙarayi na gyara ɗakin sannan nai zaman cin abincin da yace ɗin, kai tsaye na fahimci Mama Balki ce ta kawosa. Sosai naci na sha magani, sai da nayi salla sannan na tattara kayan abincin na fita zuwa sashen Ummie....

□□□□

Su amarya Baby an isa ƙasar California lafiya. Sai faman iyayi take da wani yauƙi ita a dole ga amarya. Ƙalubale na farko data fara fuskanta a wajen angon nata shine tun a airport ya sakata a taxi wai taje zai ƙaraso. Ya bama mai taxi address ɗin hotel ɗin daya riga yay booking musu tun kafin su iso. Hankalin Baby ya ɗan tashi, amma dai tai ƙoƙarin dannewa tunda yace mata uzirine daya shafesu. Batasha wahala ba kasancewar ta samu mai jiran isowarta cikin ma'aikatan hotel ɗin. Da alama dai mijin nata sananne ne a wajen. Sai ta sake jin kanta ya fasu sama sosai. Wani irin santi da sambatu ta dingayi ganin irin katafaren ɗakin da aka kawota, gashi ya jiƙu da kayan alatu. Dama tun a wajen hotel ɗin take faman sambatu a zuciyarta. Sai da ta gama taɓe-taɓenta da kalle-kalle da santi sannan ta kwanta barcin gajiya, babu batun salla ko duba lokaci, dan a cikin jirgi ko tuna tashi tai salla batayi ba. Yanzu kuma sun sauka maimakon tayi ƙoƙarin ramawa ko'a jikinta. Wankan ma tunda ta shiga tai fitsari taga ta kasa amfani da kayan bathroom ɗin shiyyasa ta haƙura. Tayi nisa a barci sosai aka tasheta. A firgice ya buɗe ido babu addu'a babu komai ta mike zambar tana ƙoƙarin ɓarka ihu. Tsawa ya mata da zabga mata harara da manyan idanunsa.

Sosai tsoro ya kamata da ganin yanda duk kamaninsa suka canja. Idanunsa sunyi wani irin jazur kamar ba mijin nata ba. Har ga ALLAH ba wani sonshi take ji ba, kawai kuɗinsa da zigar su Mom yasa ta amince da aurensa. Ta kuma gama shiryama ranta da shawarar ƙawayenta zaman shekara biyu zatayi da shi ta tara abinda ta tara tasa ya saketa ta samu dai-dai da ita yaro mijin wuce sa'a ta aura. Da ƙyar ta danne wata irin tsanarsa da ta sake ji na tsarga mata. Dan komawar idanunsa jajayen nan sai ya sake fito da tsufarsa. Duk da kuwa a fuska ƙyaƙyƙyawane, sai dai ƙaton cikin nan ya masa cikas da tsufa daya fara taso masa. Ɗan murmushi tayi cike da wayancewa da danne abinda ke ranta ta faɗa jikinsa ta rungumesa tana zabga masa kalamai wai tayi missing ɗin sa. Shiru bai rungumeta ba, bai kuma tureta ba, har sai da ta gaji dan kanta ta ɗago.

Matsawa yay daga gaban gadon yana ƙoƙarin cire kaya. Da sauri ta kauda fuskarta, dan tulelen cikinsa kamar na mace mai cikin yʼan uku dake gab da haihuwa. Tas ya gama sannan ya nufi hanyar bayi daga shi sai boxer. Yana gama shigewa ta sauke ajiyar zuciya. Itako taga takanta, wai tayaya zata iya dauriyar bin shawarar ƙawayenta? Tuna burikanta ya sata sauke numfashi. Tana nan zaune abin duniya ya isheta sai gashi ya fito. Yanzu dai towel ne a jikinsa. Zaram ta miƙe tana faɗin, “Bara nima nayi wankan to, dama gajiya tasa banyi ba na kwanta kawai ga yunwa kuma ina ji”.

“Okay”. Kawai yace mata ya cigaba da harkar gabansa. Da ƙyar ta iya samu ta kunna shower tai wankan, cikin son ta birgesa ta fito da ɗan guntun towel. Tako birgesan, dan duk inda tayi biye yake da ita da kallo kamar tsohon maye musamman bayanta. Bayan ta gama shiryawa cikin ƙananun kaya kamar yanda shima ya zuba yʼar shara da wando ta dawo kusa da shi ta zauna. Kamar abin arziƙi suka ci abinci tare tana faman masa shagwaɓa ita a dole ga amarya. Sai da yaci yay nak abinsa yay miƙar ƙoshi sannan ya miƙe a wajen. Barci ya ɗan fara figarsa a kujerar tana jikinsa akai kiran wayarsa. Janyeta yay ya tashi ya fita, kusan mintuna goma sai gashi ya dawo.. Da kallo ta dinga binsa, dan abinda aka ɗirka mata sai tsikarinta sukeyi. So take ko ɗan taɓata yayi, amma mutumin nan bashi da wannan niyyar. Ganin fa wankin hula zai kaita dare ga shi tun a yau take son fara tatsar kuɗaɗe dan Mom taci bashi sosai a bikin nan wajen shirya mata ɗaki tana son ta tura a biya kada asirinsu ya tonu. Tashi tai tsam ta nufi gadon da taga yaje ya kwanta. Cike da shagwaɓa ta faɗa masa a jiki. Shiru yay yana kallonta, itako babu kunya babu kawaici ta fara masa abubuwa. Barinta yay tai kiɗanta tai rawarta, kafin shi kuma ya fara maida mata murtani. Abinka da wadda tasha kayan iri-iri harda wanda bai kamata abama amarya irinta farin shiga ba. Gaba ɗaya ta gama sallama masa har bata ma san mi take ba. Hankalinta ya matuƙar gushewa taji kawai yana ɗaɗɗaureta. Da mamaki take kallonsa. Sai ya sakar mata makirin murmushi. Bata iya ta maida masa ba, dan a yanda ya kifata rufda ciki ya ɗaure ɗin ya sokar mata zuciya. Kafin ta samu damar neman ba'asi ya bita ya taushe. Duk da bata wani nutsu tayi islamiyya ba sosai hanyar da mijin nata ke neman bi a jikinta ya matuƙar firgitata. Cikin tashin hankali ta shiga tambayarsa mi yake sonyi haka? Abinda yake son aikatawa fa haramunne, taya zai yi ƙoƙarin mu'amalatar ta ta baya kamar wasu aladu. Ko kallo bata isheshi ba, tana ji tana gani ya aikata saɓon ALLAH da ita, maimakon bin hanyar da ALLAH ya halatta masa yabi wadda ya harta masa. Babu kuma tausayi babu imani sai da yay mata fata-fata. Tun tana kuka da roƙonsa da magiya harta ma suma dan azaba. Gashi ya ɗaureta duka hannayenta da ƙafafu babu damar koda kare kanta ne.....

❤❤❤

A ɓangaren Baba prof koda ya koma gida a jiya yaso bama al'amarin lokaci dan yay nazari, sai dai hakan na neman gagararsa. Washe gari duk da uziriri̇n dake gabansa bai iya fita a gidan ba har kusan sha biyu na rana, dan ya kwana da tunane-tunane ne ya tashi dasu. Wayarsa ya ɗauka har ya danna kiran number Maash sai kuma ya yanke yana mai girgiza kansa. Akalar kiran ya maida kan Hajiya Mammah. Harta tsinke ba'a ɗaga ba wai tana waya. Sake kiran yay dan bazai iya jira harta gama ta kirashi ba. Yanzun ma tana wayar, sai dai kuma tana gab da katsewa aka ɗaga. Cikin bada umarni ya ce, “Nafisa ki sameni a gida yanzun nan”. Daga haka ya katse kiran.

Shiru kawai Hajiya Mammah da tun jiya abin duniya ya isa tayi tana bin wayar da kallo. Ita bata motsaba ita bata ajiye ba. A haka kiran Hajiya Rubayya ya shigo mata. Da ƙyar ta iya ɗagawa takai kunnenta. Daga can cikin zumuɗi Hajiya Rubayya ta ce, “Miya faru? Ya kukayi da Baban?”.

“Ca yay na samesa a gida. Ni kuma bana jin zanyi hakan Rubayya. Dan ban san mizan ce da shi ba, kin dai san halin Baba akan ɗan iskan yaron nan”.

“Uhm uhm kar kice haka kije. Ai idan kikaƙi zuwa zai ma yarda da abinda ya faɗa kenan. Wannan fa wata gaɓace da zamu kama mu riƙe. Dan ita kawai ta rage mana yanzu. Dan haka tashi kije. Ki kirani ina jin abinda Baba ke faɗa zan dinga faɗa miki amsar da zaki bashi”.

Matuƙar yarda Hajiya Mammah tama Hajiya Rubayya. Dan haka bata kusa ba ta miƙa ta hau shirin tafiya. Ta fito cikin takun nan nata na isa da taƙama sai dai daka ganta kasan ranta a ɓace yake. Gaisheta ma'aikatan gidan keta faman yi cike da girmamawa. Sai dai gaba ɗaya hankalinta ba'a garesu yake ba. Dan dai-dai nan ɗaya daga cikin ƙosassun motocin Maash da ba kasafai yake fita da su ba sai abu mai muhimmanci ta shigo, sai motar guards ɗinsa ɗaya biye da ita. Da farko ta ɗauka Maash ɗinne ya fita yake dawowa, sai da aka buɗe motar taga wanda ya fito a ciki tai tsaiwar sojan badakkare kamar wadda ta suma a tsaye...

A hankali black beauty matashin saurayin dogo mai tsananin kammani da su Paah sai dai idanunsa sak irin na Maash ya wani yamutse fuska da bin gidan da kallo. Sam gidan baya wani birgesa a zahirance. Amma acan ƙasan ransa yana jin kewar

Ummien sa da son kasancewa da ita. Matsala ɗaya ke masa katanga da yunƙurin zuwa gareta, ɗan uwansa. In har Yayansa na waje komai buƙatar da yake ma wajen shi bazai taɓa iya kasancewa ba. Dan yana jin kamar ya soka masa wuƙa ko ɗaukar bindiga ya harbe masa kai kawai.

Sai da ya gama ƙarema gidan kallo batare da hankalinsa ya kai kan Hajiya Mammah ba ya ɗauka side bag ɗinsa irin ta maza matasa masu ji da gayu ya saka. Kansa tsaye babban ƙofar sashen ya nufa, dan sai ya fara zuwa yaga Ummiensa kafin ya ƙarasa sashensa. Yasan dai yanzu su Paah duk basa gida suna office.....✍
TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page thirty-two

32

.....Zaune nake cikin dauriya kan Ummie a saman cinyata ina mata kitso tare da raira karatun Alkur'ani a hankali. Duk da dai Alhamdullah yau ina jin jikina da sauƙi ba kamar jiya ba. Tunda na shigo Mama Balki ta sanar min ai Hafizzullah yazo da safe tare da Hayatu amma sun fita har da Maash sai kawai nace bara nai zaman yima Ummie kitsonta da tun jiya naso yi ALLAH bai ƙaddara ba. Muna fara kitson Mama tace bara taje ta duba su Aunty Falila a kitchen dake girkin rana. Da to na amsa mata na cigaba da kitson ina karatun. Fitar tata baifi da mintuna biyar ba aka buɗe ƙofar ɗakin, sai ban damu ba na cigaba da kitsona ina karatuna da tunanin ko itace ta dawo ɗaukar wani abu. Jin shiru bata ƙaraso ba bata kuma yi magana ba ga wani baƙon ƙamshin turare da ban santa da shi ba yasa na ɗago idanuna na kalla ƙofar.

Cak na tsaya da kitson ina bin black beauty matashin saurayin da kallon mamaki kamar yanda shima ya zubamun idanunsa sak irin na Yaya Awwab. Ganin kallon nasa na neman wuce gona da iri fuska a yamutse na ce, “Malam lafiya? Wanene kai? Miya kawoka nan?”.

Gira ya ɗan ɗage cike da salon iya shege sai kuma ya saki wani faffaɗan murmushi. Hannu ya kai ya ɗan shafi dan tsigigin gemunsa na ɗaukar magana ya wani karkace kai gefe tare da furta, “FAHAD EL-MU'AZZ ADAMS. Kefa ƙyaƙyƙyawa?”.

Maganarsa ta ƙarshe ta sani ƙin cemasa komai duk da naji wani daɗin jin sunan daya ambata ɗin . Sai ma ɗauke idanun nawa da nai na maida kan Ummie. Takowa yay shima a hankali zuwa inda muke. Zama yay kusa da Ummie ta ɗayan side ɗin, kamar wani ƙaramin yaro ya kwanto jikinta yana mai rungumeta. Cikin rawar marya ya ce, “I miss you mom. I love you with all my heart. You are my world and everything.” sai ga hawaye sharr, sake ƙanƙameta yay sosai a jikinsa. Sosai wani irin tausayinsa ya shiga ratsa min zuciya. Kaina na kauda daga kallonsu nima hawayen na zubo min. Da sauri na share su tare da ƙoƙarin cire kanta a jikina ya ɗago.

Da sauri ya ce, “Oh oh beauty sai ki tafi kuma? Ki bari na gama da Ummie na zan dawo kanki”.

Harara na zuba masa. Kafin na girgiza kaina da faɗin, “Ka kama kanka fa.”

Da sauri yako damƙe kan nasa. Sai kuma ya saki murmushi cikin komawa serious saboda hararar dana zabga masa. Hannayensa ya haɗe waje guda. Ya ce, “Am sorry. Barka da rana. Sunana Fahad El-Mu'azz Adams. Autan Ummiensa da Paah”.

Na kula akwaisa da shaƙiyanci, dan haka nayi murmushi da ɗan girgiza kaina. Cikin komawa serious nima nace masa sannu da zuwa. Sai dai yanzu ba kaine autan Ummie ba nice.”

Cikin marairaice fuska ya ce, “A'a dan ALLAH kada kimun haka. Na yarda ki zama aunty na kawai. Daga yanzu ma zan na ce dake aunty beauty”.

“Dama Auntyn taka ce ai”.

Muka tsinkayi muryar Mama a bayanmu. Da sauri ya juya, sai kuma ya miƙe cike da farin ciki ya nufeta. Babu kunya ya rungumeta. Dariya Mama ta shiga yi da ɗan bubbuga bayansa tana faɗin, “Oh ni maigado sai yaushe ne Fahad ɗina zai girma. Haba autan Ummie kafa isa aure”.

“Ina ban isa ba Mama. I miss you wlhy”.

“Muma munyi kewarka sosai Fahad. ALLAH yay maka albarka kaji.” ta faɗa tana ɗagosa. Daka gansu kaga waɗanda ke a cikin farin ciki sosai. Cike da girmamawa ya gaisheta, tare da tambayarta jikin Ummie yana mai bin sashen da kallo. Ta amsa masa da kulawa. Kafin ya tambayeta wai wacece ni dan ya matsu ya sani. Ƙaramar dariya Mama tayi, tare da faɗin, “A'a bakaji a bakina ba. Ka bari zaka sani”.

Cikin yanayinsa na mutum mai sauƙin kai a yanda na fahimta ni dai ya ce, “Okay Mama ba damuwa. Bari naje nayi wanka sai na dawo ALLAH yasa Ummie ta tashi ta ganni na ganta da ƙyau. Ina fatan kin min farvorite food ɗina dai?”.

“Sasai ma kuwa autan Ummie. Dan har sai kaci ka ture.”

Sosai farin cikin sa ya sake bayyana. Ya ɗaga min hannu yana maida bag ɗinsa da faɗin, “Bye Aunty beauty ki jirani nazo muyi hira. Dan sai kin faɗa min wacece ke zan barki.”

Sosai ya bani dariya. Hakama Mama Balki dariya take yi. Yana gama ficewa na dubi Mama fuskata da sauran dariyar na ce, “Mama wannan ɗan naki akwai dai rashin ji a jikinsa”. Dariya ta sake yi sosai tana kaiwa zaune. Ta ce, “Humm bar Fahad inda kika gansa ya dai so yin barkwancin ne. Amma shima da kike ganinsa wani lokacin akwai miskilancin. Sai dai bai kai Alhaji Ƙarami bane kawai. Halinsu ma sam ba iri ɗaya bane ba. Dan shi Fahad na surutu sosai, shiko Alhaji ƙarami maganar ma aiki ce. Nan fa ta shiga bani labarin Fahad da halayensa. Wani nayi mamaki wani nayi dariya wani al'ajabi. Surutunmu ya tada Ummie ma. Tana farkawa ta fara kiran “Yunwa Muhammad! Yunwa”. Aikin kenan yanzu, daga taci abinci sai barci. Idan kaga ta farka yunwar ce ta sake tashinta. Shiyyasa jikinta yake wani irin murjewa tana ƙiba kwarjininta na sake fitowa. Kwana biyu dai Alhmdllh bata wannan bige-bigen. Bamu sani ba ko hakan nada nasaba da canja mata magunguna da akayi ne. Dan a ranar da jikinta ya motsa sosai ina asibiti a yanda

Mama ke bani labari anzo da wani baƙon likita tun daga ƙasar RUMAN (Dole mu tuna Shahan-shan namu na Iffan😘😀). shine ya dubata tare da canja mata allurai da magunguna. Acewarsa a gwada waɗan nan sabin samfir ne da a shekarar nan aka samar dasu akan masu matsalar ƙwaƙwalwa. Ya bada wata ɗaya zai sake dawowa yaga idan an dace. Amma duk da haka a kullum sai doctors daya bari zasu ke kula da ita zasu dinga aika masa da cigaban da ake samu. Sannan ya dakatar da su Hajiya ƙarama da sauran doctors ɗinta a komai acewarsa shi baya haɗa aiki da waɗanda ba wanda yake tare ba.

Sosai naso ace sanda abin ya faru ina wajen. Dan ina buƙatar fahimtar yanayin kowa a cikin doctors ɗin nata na baya. Dan nasan ko suna da gaskiya hakan bazai musu daɗi ba. Amma ko yanzu na ɗauki ɗamarar yin hakan.....

□□❣□□

Ya ALLAH□ Wanda ke da rabon shiriya a masu ɗakkowa, da masu yaɗawa, da masu jiran a ɗakko su karanta a matsayin bati, ya UBANGIJIN al'ashi. Ya mai RAHAMA da jinƙai. Ya mai fidda rayayye a cikin matacce, ya fidda matacce a cikin rayayye. Nayi tawasalli da sunayenka masu tsarki, waɗanda ka kirayi kanka da su ka kuma sanar damu, da wanda ka barwa kanka saninsu ka keɓancesu gareka. Nayi tawasalli da ɗan gatan nan naka, wanda kace idan muka so shi, mukabi abinda yazo mana da shi na shiriya ka gafarta mana. Ina roƙonka ka shiryar dani da su. Ya rabbi kafisu sanin wahalar da nake sha a yayin rubutun nan. Nakan hana kaina barci domin sauke hakkin masu saya a lokacin da su suke barcin, nakan yini da ciwon kai, ina fama da ciwon idanu, ina fama da ciwon yatsu. Ina fama da ciwon baya. Wataran nakan wayi gari banama jin farin ciki ko sha'awar rubutun, wataran na tashi da uzirin baƙi ko fita. Amma duk nakan kuntata kaina domin naga nayi. Idan har ban kasance na cutar dasu da komai ba a rayuwarsu, ya rabbi! ya rabbi! ya rabbi!! ka shiryar dasu su guji taɓa hakkin daba nasu ba. Ka shiryar dasu su guji ɗaukarma kansu nauyin da zasuyi dana sani a ranar da ake fansa da lada da zunubi. Ya rabbi ka gafarta mana kurakuranmu. Ka shiryar damu, ka nisanta mu ƙuntata zuciyar kowa koda kuwa dabbace. ALLAH kasa mu samu sauƙaƙƙen hisabi batare da an jinkirta mana ba saboda hakkin wasunmu da mukaci a duniya. Dan ALLAH, dan ALLAH. Dan girman ALLAH mu saukaƙama kammu kunji bayin ALLAH. Ni kaɗai nasan a yanayin da nake wannan rubutun musamman a ɗan tsakanin nan, kada ki bari UBANGIJI ya kamaki da laifin hakkina nima bazan so haka ba. Dan bana son akai gaɓar da zan iya tashi tsakkiyar dare domin miƙama UBANGIJINA ƙararki ko ƙararka. Dan ALLAH, dan ALLAH, dan ALLAH. In har da gaske ke masoyiyar MANZON ALLAH ce kina fatan tashi a tawagarsa ranar da kowa ke fatan hakan, idan har da gaske kin yarda da mutuwa da ranar hisabi, idan har kin yadda wannan rubutun

hakkina ne ALLAH zai iya cirar min hakkina a jikinki, idan har kin yarda ban taɓa cutar dake da komai ba, idan har kina fatan kema ALLAH ya kiyaye hakkinki ko hakkinka, ku daina ɗakkowa a inda na killacesa, ki daina yaɗawa, kema ki daina karantawa. Wannan itace maganata ta farko kuma ta ƙarshe in sha ALLAHU, ALLAH ya yafe mana kurakuran mu baki ɗaya.

□□□□□

Ran Baba prof a ɓace yake kallon Hajiya Mammah dake gaishesa. Bai amsa ba, sai nuna mata agogon dake falon nasa mai shegen ƙyau da ɗaukar hankali yayi. “Kalla time, sai yanzu ne kike zuwa bayan tun 12 da wasu mintuna nai kiranki Nafisa?”.

“Kayi haƙuri Baba. Wlhy na fito zan taho sai ga Fahad. Bamma ko tsaya ya ganni ba na taho dan kar kaita jirana. Wlhy duk a tsorace nake, kada su sake ƙoƙarin ƙona mu a cikin gida kamar wancan karon. Ban san wace jaraba ce ta dawo da yaron nan ba ana zaune lafiya.”

Ɗan jimmm na wucin gadi ne ya riski Baba prof.. kafin tamkar mai koyon magana ya ce, “Wai wane Fahad ɗin?”.

Cikin rashin damuwa Hajiya Mammah ta ce, “Fahad namu mana Baba. Wlhy gashi can ya dawo abinsa. Abinda ma dai ya ɗan bani mamaki shine ganin a motar fitinannen ɗan uwan nasa aka ɗakkosa. Ko sun shirya ne bamu sani ba. Idan ma hakanne ta kasance ai mu abin farin ciki ne a garemu, dan wlhy tsoron tashin hankalin nan nasu nake suzo wataran su ƙonemu ƙurmus mu da gidan kana dai ganin wancan karon da ƙyar muka sha suka so sakamu a tara. Kai ai nikam wannan jini na Ummu-Hidaya ai ba'a cewa komai. Bala'i kala-kala daga wannan sai wancan”.

Yanda Baba prof yay shiru da alama ba fahimtar zantukan Hajiya Mammah yake ba ma shi. Dan sai da ta ɗan kai hannu ta taɓashi sannan ya dawo firgigit. Murmushi yayi zai yi magana dai-dai nan akai knocking ƙofa. Tsaki Hajiya Mammah tayi tana hararar ƙofar dan tasan bai wuce ma'aikatan gidan ba. Cike da wulaƙanci ta bada izinin a shigo. Ilai kuwa cikin ma'aikatan ne. Kansa a ƙasa da girmamawa ya kai durƙushe yana sanarma Baba prof yana da baƙo.

Agogo Baba prof ya kalla, cikin ɗan ɓacin rai yace, “Bani da apartment da kowa yau, koma su waye a sanar musu suje sa dawo next time”.

Kai hadimin ya jinjina. Har zai miƙe sai kuma ya koma ya durƙusa. Kansa a ƙasa cikin ɗari-ɗari ya furta, “Ranka ya daɗe Commando ne fa, kuma kaine kace ko baka gidan nan yazo nemanka a sanar da kai”.

Cikin masifa Hajiya Mammah ta juya zata fara danna masa zagi Baba prof ya dakatar da ita. “Uhmm Nafisa kinga barshi umarni na ne. Kinga jeki gida kawai idan na gama da shi zan zo na sameki. Komi ke faruwa ki dinga sanar dani ta waya. Sannan kiyi ƙoƙarin Mu'azz da Abdullahi su dawo gida gudun tashin hankali, idan kuma Awwab baya a gidan ki sanarma Mu'azz ya hanashi komawa gani nan zuwa yanzu nima”. Maganar yake yana tafiya, dan haka kafin ma ta bashi amsa har ya shige hanyar da zata sadashi da falon baƙi. Galala tai kawai tana kallonsa, can ƙasan ranta mamakin miya rikitashi haka take yi. Tare da mamakin girman wannan baƙo a wajensa. Amma dai koba komai ita hakan yayi mata. Dan ta kuɓuta daga abinda take gudu dai ke nan. Cikin taɓe baki ta miƙe, tare da saɓar handbag ɗinta ta fice hankalinta kwance. Ai garama taje taga show ɗin can gidan, dan babu wasu su Paah da zata kira sai abubuwa sun kankama.....✍*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

_Book three__Koo

_Page thirty-three

33

.....Abincin na fara bama Ummie bayan na wanke mata baki da taimakon Mama Balki. Ci kuwa take sosai kamar ko yaushe a kwanakin nan. Lauma biyu uku sai na bata ruwan addu'a ta sha. Ba ruwan addu'ar da nake mata bane kawai, Baba ma na mata, haka akwai wani da Hayatu ya kawo yace daga Sheikh Muhammad bin Khalipha Al-Hussain yake amsowa, tuni kuma ana kawowa masu kula da ita wai ke

bata. Dan haka dana tashi sai nake haɗesu waje guda ina bata, kullum kuma Mama Balki kan shafa mata sau uku a jiki, safe, rana da dare idan zata kwanta. Shi kansa Yaya Awwab daga jiya zuwa yau sune ruwan shansa batare daya sani ba. Dan kaf ruwan dake a cikin freight na kwashe na sanya masa na addu'oin a ciki, duk da ina ɗar-ɗar ɗin karya gane wajen buɗe murfin, dan haka nake ta kaf-kaf ɗin bashi ruwa yanzu da kaina. Dawowar Fahad ɗakin ya katse mana shirun da mukayi. Dan yana yin sallama yay tozali da Ummie dake zaune ina bama abinci ya ƙaraso cikin sassarfa ya wani rungumeta har sai da ta saki ƙaramar ƙara tana turesa. Ɗagowa yay cikin tsananin damuwa idanunsa share-share da hawaye yana kallonta. Itama kallon nashi take yi, sai kuma ta kauda kanta tare da zamewa ta kwanta ta juya mana baya. Ƙoƙarin komawa side ɗin data juya yayi, amma sai Mama Balki ta dakatar da shi ta hanyar riƙesa. Yayinda ni kuma ƙwallar tausayin ɗa da mahaifiyar suka cika min idanu.

Dai-dai nan aka turo ƙofar aka shigo. Tuni ƙamshin turarensa ya wani irin mamaye hancinanmu. Hakan ya samu ɗaga kai mu duka muka kallesa. Shima tsaye yay cak kamar wanda akama umarnin tsayawar. Yayinda Fahad yay wani kalar ɗauke kansa. Mama Balki ce tai ƙarfin halin masa sannu da zuwa. Da ƙyar ya amsa mata yanayinsa na ƙara komawa na ainahin stubborn ɗinsa. A cikin wani irin yanayi mai wahalar fassara batare da ya karaso ba ya juya ya fita abinsa yana jan sirrin tsaki dake bayyana fushinsa. Harara Fahad ya raka bayansa da shi shima yana jan tsakin mai kauri. Sai kuma a hankali ya furta, “Mugu kawai azzalumi”.

Har cikin tsakkiyar kaina naji shigar zagin nan. N bya ɗan kalla Fahad ɗin naga yanda yake wani cika yana batsewa. Maimakon naji haushinsa sai ya bani tausayi, dan hatta da jijiyoyin kansa duk sun fito raɗa-raɗa haka ma idanunsa sun wani bala'in kaɗawa jazur a ƙanƙanin lokacin nan. Kamar wanda aka tsikara shima ya miƙe zaram. Dai-dai nan Hayatu ya shigo ɗakin da sallama. Cak Fahad ɗin ya tsaya daga yunƙurin fitar da yake yi. Sai kuma murmushi ya ɗan kufce masa, da sauri ya nufi Hayatun yana faɗin, “Oyoyo sweet Yayana”.

Tuni shima Hayatu ya ajiye kayan hannunsa ya buɗe masa hannayensa suka rungume juna. Ajiyar zuciya na sauke a hankali, sai kuma na miƙe batare da nacema kowa komai ba na fita....

□□□□

Cikin yanayin gajiya ta shigo gidan. Ga damuwar dake a ƙarƙashin zuciyarta a kwanaki biyun nan game da rashin ganin Samraah. Tun a jiya bincikenta ya tabbatar mata da Samraah ce a sashen Awwab dai Hajiya Mammah da bata san an sallamota ba ta gani ba wata ba. Taso sanar ma Yallaɓai amma ta kasa hakan dan tana son ta fara sanin mi bincikensa ya samo masa akan yarinyar. In har wanda zata iya canja ra'ayinsa ne daga kasheta daya ambata sai ta fara shirinta. Idan kuma na wanda bazai iya canja ra'ayin nasa bane nan ma sai ta ɗauki mataki. Dan a wannan gaɓar bazata taɓa bashi goyon baya ba. Tanama Samraah wani irin mahaikacin so mai taɓa zuciya. Ita kaɗai tasan a halin matsanancin kishin da take ciki na Awwab a yan kwanakin nan musamman daga jiya zuwa yau.

Babu kowa a falon sai ƙamshi da sanyin ac. Tasan su Arwa sun fita yawonsu, dan Muhseen ne kawai ke zuwa makaranta yanzu a gidan sai Aneesa autar Hajiya Mammah ƙanwar Azizat kenan. Cikin rashin kuzari ta kama ƙarfen upstairs zata fara haura steps ɗin ta tsaya cak. Rawa jikinta ya nema fara yi sakamakon abinda idanunta ke kallo. Cikin wani irin bugawar zuciya da rawar baki ta furta, “Fahad!”.

“Yes Ummy. Surprise”.

Ya faɗa cikin fara'a yana ƙarasowa gareta. Cikin rashin kula da yanayinta ya bata side hug abinsa. Da ƙyar Hajiya ƙarama ta iya jan numfashi da kokarin controlling kanta. Amma ina jikinta karkarwa yake. Dan koda Fahad ya ɗago yana gaisheta sam bama fahimtarsa take ba. Sai da ya ɗan tanƙwaɓeta da zai gittata yana dariya sannan taji abinda yake faɗi na ƙarshe. “Oh Ummy mamakin ganina da alama ya sumar dake. Bari naje dai yanzu zan dawo karki faɗama su Azizat na dawo”. Daga haka yay wucewarsa ya barta a yanayin ƙaulani.

Sosai taji fitsarin dake a mararta na ƙoƙarin zubowa. Tuni ta saki handbag ɗinta a wajen ta juya ta fice a falon ƙafafunta na matuƙar rawa. Tana shiga motarta motar Hajiya Mammah na shigowa gidan. Ko bi takanta batayi ba ta wani irin yin reverse da mahaikacin gudu kamar ba'a cikin gida take ba ta fice har tana kusan takama ɗaya a cikin securitys ɗin ƙofar ƙafa ALLAH dai ya taƙaita yaja baya da sauri. Babu wanda ya kawo komai a ransa sai tunanin kiran gaggawa maybe ta samu daga asibiti. Dan sometimes takan yi irin wannan fitar idan hakan ta faru. Sai in ta dawo ta basu haƙuri da sanar musu abinda ya rikita tan. Shiyyasa kowa a gidan ke mata uziri da mata kallon innocent woman dako hannu ka saka mata a baki bazata ciza ba.

Wani irin mahaikacin gudu tayi ko'a titin. ALLAH dai ya taƙaita titin anguwa ne. Gashi kuma anguwan masu kuɗi ba wani yawan kai-kawon mutane ake samu ba, motocin ma sai jefi-jefi. Yanzu kam dama rana da wahala ka gani kasancewar duk ana wajen aiki. A cikin ƙanƙanin lokaci ta iso gate ɗin gidan yallaɓai. Horn ta dinga dannawa daya rikita maigadi, jikinsa har rawa yake wajen buɗewa. Ruɗanin da take ciki ya sata mantawa gaba ɗaya yau bata saka niƙaff ba. Sannan kuma da motarta ta amfanin ko yaushe ta shigo gidan bata ɓadda kama ba kamar yanda ta saba. Kasancewar a duka kamanni biyun na baɗini dana zahiri tana da power ɗin shigowa gidan yasa babu wanda yay mamakin ganinta sai dai mamakin yanda ta shigo. To amma idan suka auna da kafin zuwanta wadda tazo zasu iya kallon abin a wani abu daban kuma. A dai-dai ƙofar falon gidan tai parking, ko rufe motarta batayi ba ta afka ciki. Babu kowa a falon, sai tv dake magana ƙasa-ƙasa. Hannunta ta kalla da nufin neman waya, wayam babu handbag. Tunanin ta barta a mota ya sata jan tsaki. Juyawa tai da nufin ɗakko wayar dai-dai nan wanda zata fita ɗakowar dominsa ya fito. Baiyi mamakin ganinta ba, dan yasan zata iya zuwa ɗin dama..

Zaune ta kai dan wata irin hajijiya take ji na neman ɗibarta. Da ƙyar ta iya haɗa kalmar, “Fahad ya dawo, yanzu haka yana gida”.

Zaune ya kai shima a hankali batare daya ce mata komai ba. Sai ma file ɗin hannunsa daya ajiye yana mai dafe kansa da duka hannayensa biyu. Jin shiru baice komai ba ta ɗago ta kallesa. Muryarta har rawa take wajen sake faɗin, “Yallaɓai baka ji abinda na faɗa bane?”.

Wani irin murmushi ya saki, mai bayyanar da tsantsar ɓacin rai da tsufarsa. Ya ce, “Na jiki sarai, shima wanda ke bincike akan yarinyar nan ya kawo sakamakon yanzu”.

Bai gama rufe baki ba ta ɗauki file ɗin ta fara dubawa cikin rawar jiki. Abubuwa masu muhimmanci kawai take dubawa. Abu na farko daya fara jan hankalinta shine cikakken sunan yarinyar. Samraah Abdul-wahab Gwarzo. Na biyu aikin mahaifinta da sanadin rasuwarsa har ma da inda ya rasu. Na ƙarshe MATAR AURE. Rawa bakinta ya fara da ƙyar ta iya haɗa kalmar, “Ba...ban fahimci komai ba yallaɓai”.

Murmushi ya sake saki, sai kuma ya kalleta da idanunsa dake jazur kamar tsohon maciji. Musamman yanda tsufarsa ta sake fitowa fili sai taga har baƙinsa ma ya sake bayyana fiye dana baya mai tsananin shining ɗin hutu. Shima ɗin kallonta

yake cikin ido, batare daya janye ba ya furta, “Ita ɗin ɗiya ce ga Abdul-wahab Gwarzo (jirgin mota)”.

Kaɗan ya rage zuciyar Hajiya ƙarama ta ɓaro. Ta wani irin miƙe zambar jikinta na karkarwa tace, “What! Jirgin mota? Drivern mahaifin Ummu-Hidaya da kenan?”.

Kansa kawai ya ɗauke daga kallonta alamar tabbatarwa. Cikin kaushin murya ya cigaba da faɗin, “Tabbas nayi kuskuren ƙin bibiyar bayan Abdul-wahab kamar yanda nake biye dana Ibrahim Alonso. Idan baki manta ba nayi hira da yarinya shekara ɗaya data gabata a Kano sakamakon turamin program ɗin bikin buɗe Company da Awwab yayi. Zargin akwai dalilin da yasa ya amsa mata zaiyi hira da ita alhalin bai taɓa yi da ko manyan channels ba yasa na baro India nazo danna tabbatar da ko akwai alaƙa a tsakaninsu. Tako ina bincikena babu ta inda wata alaƙa ta alaƙanta su, dan haka ban maida hankalina ga cikakken sunan yarinyar ba....”

“Wai kana nufin itace yallaɓai?”.

Hajiya ƙarama da gaba ɗaya take a gigice ta jeho masa tambaya cikin katsesa. Iska ya furzar mai kauri tare da miƙewa tsaye. Taku ya fara hannayensa duka biyu a goye ya ce, “Of course itace yarinyar”.

“Tashin hankali. To amma tayaya tazo Lagos bayan ma'aikaciya ce? Ta yaya kuma Lagos ɗin ma take zaune a Maash Mansion? A ƙarshen zance shine tayi aure bayan fasa aurenta da saurayinta da suka jima a tare. Abin tambayar anan waye ya auretan? Waye kuma yay kidnapping ɗinta kafin auren har sau biyu? Tabbas akwai abinda ya kawota Maash Mansion, minene shi?. Yallaɓai wlhy zan haukace, wane irin ruɗani da tashin hankali ne haka yazo mana a rana ɗaya? Gashi mun gagara magance batun likitocin nan abu sai ƙara nisa yake, duk da dai ba wannan bane kaɗai hope ɗinmu wancan ma zasu iya mana illa tunda ko ganinta bamayi a yanzu balle sanin halin da take ciki”.

Amaimakon amsa mata dukkan tambayoyinta da maganganunta a mugun fusace yay wurgi da ɗan abin deco.. ɗin dake a saman Centre table ɗin gabansu.....✍ *_TSUTSAR NAMA....!!_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page thirty-four

34

.....Mugun tsorata Hajiya ƙarama tayi har sai da ta rumtse idanunta da toshe kunnenta jikinta na rawa. Shima nashi jikin rawar yake yi na tsantsar ɓacin rai. Kafin ya shiga maimaita kalmar, “Dole akwai abinda Awwab ya sani, dole shine ya shirya komai. Ta ya yarinyar dake a Kano zata dawo Lagos? Ta ya ɗiyar Abdul-wahab zata shigo Maash Mansion matsayin yʼar aiki? Ta ya?!!! Ta ya?!! Ta yaya?!!!!”.

Ya faɗa cikin wani irin ƙaraji da ya sake firgita Hajiya ƙarama. Dan bata taɓa ganinsa a irin wannan fushin ba duk da kuwa ita shaidace akan hatsabibancin sa tun ba yanzu ba. Da wani irin fushi ya danna gefen kujerarsa, zuuuu sai ga gurin ya buɗe. Wata yʼar loka ce ta bayyana, kwalaben manyan haɗaɗɗun giya masu tsadar gaske suka bayyana. Ɗaya a ciki ya ɗauka, batare da tuna akwai mai amsa suna surukarsa ba a wajen ya ɓalle murfin ya dasa a bakinsa ya shiga kwankwaɗar kayansa. Shike sha, amma Hajiya Ƙarama ita ke binsa da kallo kamar tsohuwar mayya. A yanda take jinta yau ɗin nan kamar fa ta amsa itama ta kora. Sai dai kuma tasan hakan zai iya ɓallo mata aiki ne a wajen Paah.

Tas ya shanye abinda ke ciki, tare da yin wurgi da kwalbar sannan ya koma cikin kujera yay wata irin lafewa yana sauke numfashi da ƙarfafan ajiyar zuciya tamkar wanda yay wani uban gudu a sahara. Sun kwashi mintuna biyar a haka shiru, kafin ya miƙe batare da ya kalleta ba ya ce, “Kije gida zan nemeki.”

Baki ta buɗe zatai magana ya ɗaga mata hannu alamar baya son jin komai. Kanta kawai ta jinjina tare da miƙewar ta fice. Da harara ya raka bayanta, yana jin a ransa amfaninta ya kusa ƙarewa a garesa. Juyayyun idanunsa ya maida kan ƙaton hotonsa dake a falon shi da mahaifin Ummie wato Ibrahim. Hoton yay matuƙar ƙyau musamman da suka kasance cikin manyan kaya, su sukansu kuma bakunansu ɗauke da murmushi. Hannayensu riƙe da jariri dake a cikin showal mai tsananin ƙyau da ɗaukar ido. An yi hoton ne a ranar sunan Muhammad Awwab. Shine kuma

jinjirin dake a hannun nasu suna kallonsa fuskokinsu ɗauke da murmushi. A fusace ya rarumi ɗayan deco ɗin saman table ɗin ya wulwula sai ko akan hoton. A take gilashin jikinsa ya tsatstsage. Yatsansa ya karkaɗa alamar gargaɗi ma hoton sannan ya wuce fuuuu zuwa bedroom ɗinsa....

A hankali Kukunsa dake laɓe yana kallon komai ya shiga jinjina kansa. Da baya-baya ya koma ya shiga ta cikin store. Stick ya ɗauka cikin dabara ya janye abinda ya kare cctv camaras ɗin dake a kitchen ɗin ta koma yanda take kamar komai bai faru ba. Dan duk leƙen da yay da naɗar abinda ke faruwa a rubuce camara ɗin bata ɗauka ba. Ba yau ya fara hakan ba, domin a ankare yake, ko it kanta camara ɗin babu wanda yasan ya fahimci akwai ta a kitchen ɗin fama cikin gidan baki ɗaya, sai dai bai taɓa cin karo da samun abinda yasan ogansa zaiyi farin ciki ba irin yau, dan koshi kansa a yau ɗin nan ya matuƙar girgiza da shiga mamakin ganin fuskar Hajiya ƙarama a matsayin wadda ta jima tsahon shekaru tana kawoma Baba prof ɗin ziyara amma bai taɓa ganewa ba saboda shigar ɓadda kama da take yi idan zatazo. Ba kuma su taɓa zama a wannan falon sunyi magana ba sai yau ɗin. Aikinsa ya cigaba dayi kamar yanda ya saba....

□★□★□

A hankali na murɗa handle ɗin ƙofar na tura kamar mai jin tsoron gamo da wani abun firgici. An rage hasken ɗakin ya koma dif sosai. Sai sanyin ac da ƙamshin fresheners dana saka kafin na fita. Ɗan dube-dube na fara kafin idanuna su sauka akansa. Yana can tsaye daga jikin window duka hannayensa goye a bayansa ya ƙurama waje kallo. Cikin sanɗa na ƙarasa shiga ɗakin. Tray ɗin dake hannuna na ɗaura saman Centre table dake a tsakiyar sofas. Kafin na ƙarasa takawa har inda yake cikin sanɗa. Cikin rufe ido da killace duk wata kunya dake cike da zuciyata na ƙarasa ta bayansa a hankali na warware hannayensa dake goye a bayansa na rungumesa ta baya, hannayena zagaye da shafaffen cikinsa. Dan abinka da dogo bawani na iya kai koda kafaɗarsa bane. Data samansa ne ma hannayena bazasu iya kullesa ba saboda yanda ƙirjinsa ke a buɗe alamar motsa jiki. Jikinsa akwai zafi sosai alamar zazzaɓi ko kuma duk ɓacin ran ne oho.

Duk da dabaibayin dana masa sam bai motsa ba, na ɗan ciza lips ɗina ina mamakin taurin zuciyarsa. A zahiri kam muryata na maida can ƙasa da yʼar shagwaɓa na ce, “My Lion!”.

Shiru bai amsa ba. Na ɗan yi jimm kafin na motsa hamnuna na mintsinesa a saman cikinsa kaɗan na sake faɗin, “My hot! Please answer me ko naita maka kuka”.

Nan ɗin ma kamar bazaice komai ba. Dan kusan fin minti ɗaya kafin naji saukar hannunsa saman nawa. Sosai shima ɗumin hannun nasa ya ratsa min nawa har sai da na ciza lips ɗina kaɗan. A hankali ya jawoni daga bayansa ya maidoni ta gabansa ya tsayar da ni. Har cikin jini da ɓargo na nake jin kaifin idanunsa na ratsani. Dan haka koda kwatance ban iya gwada ɗagowa na kallesa ba. Saukar hannunsa mai ɗumi naji akan haɓata, ya ɗago fuskata sama ta yanda zamu iya ganin juna. Amma sai na lumshe nawa idanun dan bazan iya kallonsa ba. Yafi minti ɗaya yana ƙarema fuskar tawa kallo, ina jin hakanne ta hanyar kaifi da tasirin ƙarfin idanunsa a kaina. Da wani irin ƙyar, tamkar wanda akama dole cikin maƙoshi ya furta, “Mi kike buƙata?”.

Sai da na ƙara runtse idanuna da ƙyau kafin na ɗaga hannuna na ɗaura yatsana manuniya akan jikinsa alamar shi. Ina ji ya ɗan furzar da numfashi mai ɗan sauti kafin ya furta, “Open your eyes”.

Kafaɗa na maƙe masa da faɗin, “Uhm-uhmmm!”. Cikin shagwaɓa.

“Why?”.

“Ina jin kunyan ka”.

“What is kunya?”.

Bamma san sanda na ware duk girman idanuna ba a kansa. Cikin suɓutar baki na ce, “Bama ka sanshi ba?”.

Kansa ya jinjina min kawai idanunsa da gaba ɗaya suka canja launi a cikin nawa, ya wani ƙankancesu da shanyesu sun koma wasu luu-luu da su tamkar mai son yin barci. Kasa jurewa nayi, na rissinar da nawa idanun a hankali ina maida fuskata

ƙasa. Sai kuma na ɗaura bayan hannuna akan hannunsa da har yanzu ke akan haɓata. “Yaya jikinka fa zafi, baka da lafiya ne?”.

Shiru kamar bazai amsa ni ba, sai kuma ya jawoni jikinsa a hankali ya rungume. Da ƙarfi na sauke ajiyar zuciya, dan wani ratsani zafin jikin nasa yayi har cikin ƙashi. Cikin kasa daurewa na sake faɗin, “ALLAH baka da lafiya. Please muje kasha magani”.

“Nooh!”.

Ya faɗa da ɗan kaushin murya yana sake ƙanƙameni. Tuno maganar Mama nayi da tace baya ƙaunar magani. Sai naji abin ya bani dariya ma. Namiji da shi babba amma yake tsoron magani. Mun jima tsaye a haka kafin na ɗago dan ƙafafuna sun fara gajiya. Cikin raunin murya kamar zanyi kuka nace, “ALLAH yaya ƙafafuna sun gaji ni dai”.

Baice komai ba, baima da alamar motsawa. Sai da ya mula dan kansa kafin ya ɗagoni. Ajiyar zuciya na sauke. A saman sofa ya kawoni ya zaunar, shi kuma ya wuce closet. Da kallo kawai na bisa ina mai sauke ajiyar zuciya. Sosai tausayinsu ya kamani shi da ɗan uwan nasa. Dan a kallo ɗaya zaka iya fahimtar tsantsar ƙiyayyar da sukema juna a bayyane take. Nayi nisa sosai a tunani har ya dawo ban sani ba. Sai da ya kama min hannu na dawo firgigit tare da ɗagowa na kallesa. Da sauri na kauda kaina, dan bathrobe ce a jikinsa blue black bai ko ɗaure igiyoyin ba, hakkan ya bama boxer ɗinsa damar bayyana da murɗaɗɗen jikinsa. Magana na buɗe baki zanyi yay min alamar zipping akan lips. Dole na haɗiye sai dai zuciyata sai faman dukan uku-uku take. Tsorona kar yace wanka zan masa. Wani wawan ajiyar zuciya na sauke ganin saɓanin hakan. Dan ƙofa ya buɗe muka fito, sai kuma na shiga wasi-wasin ina zamuje haka. Bamu fita ba a ta wajen bedroom ɗin nasa ya buɗe ƙofar da na daɗe ina tunanin ta bedroom ce itama, ashe ba haka bane. Dan gani nai kawai mun fito ta wani ƙyaƙyƙyawan waje da ƙaton swimming pool ne kawai a cikinsa. A yanayin kamar a ɗaki, sai dai ta saman ginin kana iya hango sararin samaniya, hakama ta jikin bango zallar gilashi ne da kake iya hango cikin garden ɗin nan. Ata ƙasa an matuƙar ƙawatashi da green carpet tamkar koriyar ciyawa farkon toho. Sai hakan ya bada wani irin ƙawa musamman da yanayin ruwan shi kuma ya kasance blue yana wani walƙiya da ƙyalli kamar kaci da haƙori. Sosai dogayen fararen kujerun da kallo ɗaya zakama tausasan katifun samansu kasan zasuyi laushi suka sake ɗaukar hankalina. Na shagala matuƙa da kallon wajen har ban san ma ya zame bathrobe ɗin jikin nasa ba. Sai da ya rungumeni ta baya sannan na ja ajiyar

zuciya. Yanda yake mun numfashi ata bayan kunne yay matuƙar saka tsigar jikina ta shi. Bamma san na ƙanƙame hannunsa dake saman cikina ba ina ƙara manne bayana da jikinsa idanuna a rufe. Cikin soft and silent voice ɗin shin nan yana wani irin mun salo a cikin kunne ya furta, “Za kiyi wanka a ciki?”.

Sosai na ƙara ƙanƙame jikina ina jujjuya masa kaina dake a saman ƙirjinsa.

“Why?”.

Ya faɗa yanayi kamar zai ciza kunnena. Jinai jikina yana neman fara rawa. Lips ɗina na rawa na ce, “Yaya wlhy tsoro nake ji. Ban taɓa shiga ruwa ba irin haka”.

Komai baice min ba, sai ɗan kwalina daya zame yana ƙoƙarin cusa hannunsa cikin gashin. Tanan kuma ɗayan hannunsa na yawo a jikina. Cikin ɗan ƙarfin da ya rage mun da sauri na janye jikin nawa dake ƙoƙarin fara rawa ina sauke numfashi da sauri-sauri. Komai baice da ni ba, bai kuma kallan ba, sai ƙarasa sakimmin hannun da yay a hankali. Idanuna na runtse, kusan minti ɗaya na buɗe su da sauri saboda jin ƙarar faɗawarsa cikin ruwan. Waro idanuwan nayi sosai ganin yanda ya wani nutse can ƙasa gaba ɗayansa sai motsin ruwan kawai kake gani ta sama.....✍

35 wazai tafo mana Please**_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page thirty-five

35

.....Mugun tsorata Hajiya ƙarama tayi har sai da ta rumtse idanunta da toshe kunnenta jikinta na rawa. Shima nashi jikin rawar yake yi na tsantsar ɓacin rai. Kafin

ya shiga maimaita kalmar, “Dole akwai abinda Awwab ya sani, dole shine ya shirya komai. Ta ya yarinyar dake a Kano zata dawo Lagos? Ta ya ɗiyar Abdul-wahab zata shigo Maash Mansion matsayin yʼar aiki? Ta ya?!!! Ta ya?!! Ta yaya?!!!!”.

Ya faɗa cikin wani irin ƙaraji da ya sake firgita Hajiya ƙarama. Dan bata taɓa ganinsa a irin wannan fushin ba duk da kuwa ita shaidace akan hatsabibancin sa tun ba yanzu ba. Da wani irin fushi ya danna gefen kujerarsa, zuuuu sai ga gurin ya buɗe. Wata yʼar loka ce ta bayyana, kwalaben manyan haɗaɗɗun giya masu tsadar gaske suka bayyana. Ɗaya a ciki ya ɗauka, batare da tuna akwai mai amsa suna surukarsa ba a wajen ya ɓalle murfin ya dasa a bakinsa ya shiga kwankwaɗar kayansa. Shike sha, amma Hajiya Ƙarama ita ke binsa da kallo kamar tsohuwar mayya. A yanda take jinta yau ɗin nan kamar fa ta amsa itama ta kora. Sai dai kuma tasan hakan zai iya ɓallo mata aiki ne a wajen Paah.

Tas ya shanye abinda ke ciki, tare da yin wurgi da kwalbar sannan ya koma cikin kujera yay wata irin lafewa yana sauke numfashi da ƙarfafan ajiyar zuciya tamkar wanda yay wani uban gudu a sahara. Sun kwashi mintuna biyar a haka shiru, kafin ya miƙe batare da ya kalleta ba ya ce, “Kije gida zan nemeki.”

Baki ta buɗe zatai magana ya ɗaga mata hannu alamar baya son jin komai. Kanta kawai ta jinjina tare da miƙewar ta fice. Da harara ya raka bayanta, yana jin a ransa amfaninta ya kusa ƙarewa a garesa. Juyayyun idanunsa ya maida kan ƙaton hotonsa dake a falon shi da mahaifin Ummie wato Ibrahim. Hoton yay matuƙar ƙyau musamman da suka kasance cikin manyan kaya, su sukansu kuma bakunansu ɗauke da murmushi. Hannayensu riƙe da jariri dake a cikin showal mai tsananin ƙyau da ɗaukar ido. An yi hoton ne a ranar sunan Muhammad Awwab. Shine kuma jinjirin dake a hannun nasu suna kallonsa fuskokinsu ɗauke da murmushi. A fusace ya rarumi ɗayan deco ɗin saman table ɗin ya wulwula sai ko akan hoton. A take gilashin jikinsa ya tsatstsage. Yatsansa ya karkaɗa alamar gargaɗi ma hoton sannan ya wuce fuuuu zuwa bedroom ɗinsa....

A hankali Kukunsa dake laɓe yana kallon komai ya shiga jinjina kansa. Da baya-baya ya koma ya shiga ta cikin store. Stick ya ɗauka cikin dabara ya janye abinda ya kare cctv camaras ɗin dake a kitchen ɗin ta koma yanda take kamar komai bai faru ba. Dan duk leƙen da yay da naɗar abinda ke faruwa a rubuce camara ɗin bata ɗauka ba. Ba yau ya fara hakan ba, domin a ankare yake, ko it kanta camara ɗin babu wanda yasan ya fahimci akwai ta a kitchen ɗin fama cikin gidan baki ɗaya, sai dai bai taɓa cin karo da samun abinda yasan ogansa zaiyi farin ciki ba irin yau, dan

koshi kansa a yau ɗin nan ya matuƙar girgiza da shiga mamakin ganin fuskar Hajiya ƙarama a matsayin wadda ta jima tsahon shekaru tana kawoma Baba prof ɗin ziyara amma bai taɓa ganewa ba saboda shigar ɓadda kama da take yi idan zatazo. Ba kuma su taɓa zama a wannan falon sunyi magana ba sai yau ɗin. Aikinsa ya cigaba dayi kamar yanda ya saba....

□★□★□

A hankali na murɗa handle ɗin ƙofar na tura kamar mai jin tsoron gamo da wani abun firgici. An rage hasken ɗakin ya koma dif sosai. Sai sanyin ac da ƙamshin fresheners dana saka kafin na fita. Ɗan dube-dube na fara kafin idanuna su sauka akansa. Yana can tsaye daga jikin window duka hannayensa goye a bayansa ya ƙurama waje kallo. Cikin sanɗa na ƙarasa shiga ɗakin. Tray ɗin dake hannuna na ɗaura saman Centre table dake a tsakiyar sofas. Kafin na ƙarasa takawa har inda yake cikin sanɗa. Cikin rufe ido da killace duk wata kunya dake cike da zuciyata na ƙarasa ta bayansa a hankali na warware hannayensa dake goye a bayansa na rungumesa ta baya, hannayena zagaye da shafaffen cikinsa. Dan abinka da dogo bawani na iya kai koda kafaɗarsa bane. Data samansa ne ma hannayena bazasu iya kullesa ba saboda yanda ƙirjinsa ke a buɗe alamar motsa jiki. Jikinsa akwai zafi sosai alamar zazzaɓi ko kuma duk ɓacin ran ne oho.

Duk da dabaibayin dana masa sam bai motsa ba, na ɗan ciza lips ɗina ina mamakin taurin zuciyarsa. A zahiri kam muryata na maida can ƙasa da ƴar shagwaɓa na ce, “My Lion!”.

Shiru bai amsa ba. Na ɗan yi jimm kafin na motsa hamnuna na mintsinesa a saman cikinsa kaɗan na sake faɗin, “My hot! Please answer me ko naita maka kuka”.

Nan ɗin ma kamar bazaice komai ba. Dan kusan fin minti ɗaya kafin naji saukar hannunsa saman nawa. Sosai shima ɗumin hannun nasa ya ratsa min nawa har sai da na ciza lips ɗina kaɗan. A hankali ya jawoni daga bayansa ya maidoni ta gabansa ya tsayar da ni. Har cikin jini da ɓargo na nake jin kaifin idanunsa na ratsani. Dan haka koda kwatance ban iya gwada ɗagowa na kallesa ba. Saukar hannunsa mai ɗumi naji akan haɓata, ya ɗago fuskata sama ta yanda zamu iya ganin juna. Amma sai na lumshe nawa idanun dan bazan iya kallonsa ba. Yafi minti ɗaya yana ƙarema fuskar tawa kallo, ina jin hakanne ta hanyar kaifi da tasirin ƙarfin

idanunsa a kaina. Da wani irin ƙyar, tamkar wanda akama dole cikin maƙoshi ya furta, “Mi kike buƙata?”.

Sai da na ƙara runtse idanuna da ƙyau kafin na ɗaga hannuna na ɗaura yatsana manuniya akan jikinsa alamar shi. Ina ji ya ɗan furzar da numfashi mai ɗan sauti kafin ya furta, “Open your eyes”.

Kafaɗa na maƙe masa da faɗin, “Uhm-uhmmm!”. Cikin shagwaɓa.

“Why?”.

“Ina jin kunyan ka”.

“What is kunya?”.

Bamma san sanda na ware duk girman idanuna ba a kansa. Cikin suɓutar baki na ce, “Bama ka sanshi ba?”.

Kansa ya jinjina min kawai idanunsa da gaba ɗaya suka canja launi a cikin nawa, ya wani ƙankancesu da shanyesu sun koma wasu luu-luu da su tamkar mai son yin barci. Kasa jurewa nayi, na rissinar da nawa idanun a hankali ina maida fuskata ƙasa. Sai kuma na ɗaura bayan hannuna akan hannunsa da har yanzu ke akan haɓata. “Yaya jikinka fa zafi, baka da lafiya ne?”.

Shiru kamar bazai amsa ni ba, sai kuma ya jawoni jikinsa a hankali ya rungume. Da ƙarfi na sauke ajiyar zuciya, dan wani ratsani zafin jikin nasa yayi har cikin ƙashi. Cikin kasa daurewa na sake faɗin, “ALLAH baka da lafiya. Please muje kasha magani”.

“Nooh!”.

Ya faɗa da ɗan kaushin murya yana sake ƙanƙameni. Tuno maganar Mama nayi da tace baya ƙaunar magani. Sai naji abin ya bani dariya ma. Namiji da shi babba amma yake tsoron magani. Mun jima tsaye a haka kafin na ɗago dan ƙafafuna sun fara gajiya. Cikin raunin murya kamar zanyi kuka nace, “ALLAH yaya ƙafafuna sun gaji ni dai”.

Baice komai ba, baima da alamar motsawa. Sai da ya mula dan kansa kafin ya ɗagoni. Ajiyar zuciya na sauke. A saman sofa ya kawoni ya zaunar, shi kuma ya wuce closet. Da kallo kawai na bisa ina mai sauke ajiyar zuciya. Sosai tausayinsu ya kamani shi da ɗan uwan nasa. Dan a kallo ɗaya zaka iya fahimtar tsantsar ƙiyayyar da sukema juna a bayyane take. Nayi nisa sosai a tunani har ya dawo ban sani ba. Sai da ya kama min hannu na dawo firgigit tare da ɗagowa na kallesa. Da sauri na kauda kaina, dan bathrobe ce a jikinsa blue black bai ko ɗaure igiyoyin ba, hakkan ya bama boxer ɗinsa damar bayyana da murɗaɗɗen jikinsa. Magana na buɗe baki zanyi yay min alamar zipping akan lips. Dole na haɗiye sai dai zuciyata sai faman dukan uku-uku take. Tsorona kar yace wanka zan masa. Wani wawan ajiyar zuciya na sauke ganin saɓanin hakan. Dan ƙofa ya buɗe muka fito, sai kuma na shiga wasi-wasin ina zamuje haka. Bamu fita ba a ta wajen bedroom ɗin nasa ya buɗe ƙofar da na daɗe ina tunanin ta bedroom ce itama, ashe ba haka bane. Dan gani nai kawai mun fito ta wani ƙyaƙyƙyawan waje da ƙaton swimming pool ne kawai a cikinsa. A yanayin kamar a ɗaki, sai dai ta saman ginin kana iya hango sararin samaniya, hakama ta jikin bango zallar gilashi ne da kake iya hango cikin garden ɗin nan. Ata ƙasa an matuƙar ƙawatashi da green carpet tamkar koriyar ciyawa farkon toho. Sai hakan ya bada wani irin ƙawa musamman da yanayin ruwan shi kuma ya kasance blue yana wani walƙiya da ƙyalli kamar kaci da haƙori. Sosai dogayen fararen kujeru a da kallo ɗaya zakama tausasan katifun samansu kasan zasuyi laushi suka sake ɗaukar hankalina. Na shagala matuƙa da kallon wajen har ban san ma ya zame bathrobe ɗin jikin nasa ba. Sai da ya rungumeni ta baya sannan na ja ajiyar zuciya. Yanda yake mun numfashi ata bayan kunne yay matuƙar saka tsigar jikina ta shi. Bamma san na ƙanƙame hannunsa dake saman cikina ba ina ƙara manne bayana da jikinsa idanuna a rufe. Cikin soft and silent voice ɗin shin nan yana wani irin mun salo a cikin kunne ya furta, “Za kiyi wanka a ciki?”.

Sosai na ƙara ƙanƙame jikina ina jujjuya masa kaina dake a saman ƙirjinsa.

“Why?”.

Ya faɗa yanayi kamar zai ciza kunnena. Jinai jikina yana neman fara rawa. Lips ɗina na rawa na ce, “Yaya wlhy tsoro nake ji. Ban taɓa shiga ruwa ba irin haka”.

Komai baice min ba, sai ɗan kwalina daya zame yana ƙoƙarin cusa hannunsa cikin gashin. Tanan kuma ɗayan hannunsa na yawo a jikina. Cikin ɗan ƙarfin da ya rage mun da sauri na janye jikin nawa dake ƙoƙarin fara rawa ina sauke numfashi da sauri-sauri. Komai baice da ni ba, bai kuma kallan ba, sai ƙarasa sakimmin hannun da yay a hankali. Idanuna na runtse, kusan minti ɗaya na buɗe su da sauri saboda jin ƙarar faɗawarsa cikin ruwan. Waro idanuwan nayi sosai ganin yanda ya wani nutse can ƙasa gaba ɗayansa sai motsin ruwan kawai kake gani ta sama.....✍

35 wazai tafo mana Please*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

_Page thirty-six

36

Tunda muka dawo daki na fahimci yanata faman dafe kansa. Ga jikinsa akwai matukar zafi har yanzu dan ya matsa saida na shafa masa mai. Black tea ya bukaci na bashi. Hakan yasa ni fita zuwa kitchen dinsa a karo na farko na dafa abinda ya umurceni, sai kuma na hada da dan spaghetti ko zaici dan naga kamar harda yunwa a al'amarinsa. Koda na dawo kwance na samesa yama ja bargo jikinsa. Har cikin rai saida naji gabana ya fadi. Tray sin na aje a side drawer na hau saman gadon. A hankali na daga bargon ta saitin kansa. Hannuna na daura a saman goshinsa. Zafi sosai da har saida tsigar jikina ta tashi. Jinai gaba daya na daburce. Cikin damuwa na shiga fadin, "Yaya awwab baka da lpy sosai dan ALLAH ka tashi

muje asibiti. Ko kuma na kira maka yaya Hayatu yazo kuje". Na kare maganar ina kokarin sauka a gadon.

Cak na dakata jin an riko hannuna. Juyowa nayi na kallesa zafin hannun nasa ma na ratsa jikina.

Idanuna na tara kwalla nace , pls yaya ka barni najena kirasu. Wlh bazan iya ganinka a halin ciwo haka ba na barka".

"Samrh".

Ya kirayi sunana a wani irin can kasan makoshi. Muryata na rawa na amsa. Bai sake magana ba sai jawoni da yay a hankali na fado jikinsa. Duk dˊakan bargon dake lullube jikinsa nake ina jin zafin zazzabin duk da kauri duvet din. Fuskata ya shafa a hankali yana wani lumshe idanunsa da gaba daya launinsu ya gama canjawa. "Banason kowa ya sani bani black tea din na sha."

"Amma Yaya".....

"Shiiii!!!!".

Ya fada yana mai lumshe idanun nasa da sake rikoni jikinsa da kyau bani da zabin daya wuce bin umarninsa. Dan haka na Mike jiki a sanyaye na zuba masa black tea din a kofi. Hannu ya Miko man alamar na kamashi ya tashi. Badan xan iya bana mika masa nawa sai dai koda na kama shi sai ya zam nice mana fada jikinsa alamar ya rinyaneni.

"My tiger ashe babu karfi".

Ya fada cikin kunnena kamar mai rada. Tashi da tsigar jikina tayi ya sani milewa zunbur ina tura baki. Shima sai bai sake magana ba ya tashi zaunen. Nuni yai min da filo, dan haka na dauka na sanya masa a baya jikin fuskar gadon ya zauna tare da jingina kafafuna a cikin duvet din. Zama nai daga bakin gadon a kusa da shi ina facing dinsa. Na dauka mug din na mika masa. Cat eyes dinsa masu tsananin tasiri a gareni na kaina ya amsa. Koda ya fara sha dinma bai janye ba sai nice na dukar da kaina kawai ina tunane -tunane. Tas ya shanye dan irin mitsitsin kofin nan ne na rowa. Cewar da yay a kara ya sani dagowa na kallesa. Amma sai na janye ina amsar kofin da girgiza kai nace, a'a ka barsa haka kadanci abincin ko kadanne. Allah ko zama da yunwa ya saka ciwo. Baice komai ba har na dauko tray din na aza saman cinyata na bude plate din. A take kamshin taliyar ya gama cika wajen. Ba wani dahuwar kakale na mata ba. Dan attarugu ne kadan sai vegetables da kifin gwangwani dana saka a ciki. Kodan yar kadan ce dama na dafa sai ya bani wani kalar kyau a idon mai kallo. Allah dai yasa tayi dadi ma a baki. Tray din na daga zan maida jikinsa ya dakatar da ni. Da mamaki na kallesa, shima kallona yakeyi. Cikin wani irin luu da idanun kamar zai lunshe hannayensa harde a kirjinsa ya min nunin na ajiye a saman jikin nawa. Nan ma kasa musa masa nayi, sake min nuni yai da spoon din shima. Nam m na dauka babu musu. Ya nuna min abincin tare da da bude

dan mitsitin bakinsa alamar na bashi. Sosai na dan waro idanuna waje. Sai ya dan bata fuska da kokarin zamewa zai kona ya kwanta. Rikosa nayi da sauri cikin maraicewa nace "Yi hakuri to zan baka" . Karamar harara ya dan mum sannan ya koma ya zauna. Niko sai mita nike a zuciyata. Mutum kamar kurma sai iya shege fal cikinsa. A zahiri kam abincin na fara bashi a nutse. Shiko ya zuba man idanun sa kawai yana wani taunawa tamkar bayaso. Sai da yay kusan lauma ukku sannan ya wani lumshe idanunsa cike da salo tare da hade babban yatsansa da manuniya alamar yayi

Bammasan na sakar masa murmushi ba nima. A mamakina shima saiya murmusa kadan, zuba masa ido kawai nayi ina kallonsa, dan tabbas murmushi yanama bawan ALLAHn nan kyau, sai kuma a kaf rayuwarsa, inaga abinda yafi masa wahala kenan sai magana.

"Samrh".

Ya kirani a hankali. Firgigit na dawo hayyacina. Sai kuma na dan bata fuska dan na fahimci na saki layi da yawa. Kokarin dojewa nake dan a tunanina zaimin magana nr akan kallon nasa. Sai naji sabanin hakan. Sake kiran sunan nawa da yay can kasan makoshi da silent muryan sa din nan yana sake marker da cat eyes dinsa kaina yasa n amsa nima idanuna a kasa.

"Minene burinki a duniya nan?".

Karamin murmushi nayi , tare da debo abincin nakai bakinsa. Budewa yay ya amsa, na dan janye hannuna batare dana kallesa badai nace "Yaya Awwab! Ina da burika da yawa. Sai daj dukansu sun ta'allaka ne a karkashin dai -daiton rayuwa da samuwar dunkulalliyar tafiya a yanzu. Dan na jima da shafe babin burikan da wauta da kuruciya ta kirjira a baya bisa wasu dalilai. Abincin na kara diba xan bashi ya girgiza kai alamar ya koshi, fuska na marairaice ina kallon abincin sannan na sake kallonsa nace," please kadan fa kaci. Ka daure ka dan kara sai kasha magan....."

Ai tun kafin in mana karasa kalmar maganin ya wani yamutse fuska da bata rai. Dariya naji ya bani , wai namiji babba kamarsa da tsoron magani. Bance dashi komai ba face rufe abincin na rufe na ajiye. Maganin dana riga na balla nasa a karamin plate na rufesa na bude na diba. Ina juyowa yaga abinda nayi kawai yay saurin Jan bargon zai kwanta na dane gadon ina dariya. A saman cinyarsa na zauna na hanashi kwanciyar tare da riko fuskarsa. Kansa ya shiga jujjya min kamar zaiyi kuka.

"Please my tiger wlh banaso . I hate medicine! Leave me alone I beg".

Hancinsa na dan ja da fadin, "No saifa my lion yasha maganin nan zan barsa. Ni inaso naga ka samu sauki, jikinka kara zafi ma yake".

"Please. "

Ya sakefada fuskarsa a yamutse kamar zai fasa ihu.

"Nima please manya fa basa tsoron magani. Haba dan ummiensa. Bafa wani wahala da yanzu ma kasha. Zakafi samun sauki da wuri".

No kawai ki rungume ni zan daina ji!."

A'a, sai kasha sannan zan rungumekan. Rufe idonka ka gani ka bude bakin haba mana. Be a good boy my lion hahhhh".

Kafada ya make mun duk ya marairaice abin dariya. Kamar ba stubborn maash din nan ba mai yin komai cike da rashin mutunci ba. Cikin kokarin sake dabara nace , to yanzu yaya kakeso ayi?".

Bakin ya bude zaiyi magana kawai na shammacesa na cusa maganin na danna masa kofin kan baki tare da rike masa hanci da yatsuna dole ya zuki ruwan. Sai da na tabbatar ya shanye ruwan maganin kuma ya wuce gaba sannan na saki masa hanci ina dariya. Ganin yanda yake rike dariyar dan na fahimci abin nasa fa na gaske ne. A hankali na rike fuskarsa da tafukan hannuna duk biyu tare da kai lips dina saman small nashi duk da yanda zuciyata ke dukan tamarin-tamanin ga kunya amma na daure. Cak kuwa ya tsaya da kakarin ya shiga sauke numfashi. Kusan minti daya na tabbatar nutsuwar shi ta dawo jikinsa dan harga ALLAH kunya naji sosai. Abu goma da ashirin gani a saman cinyarsa kuma zaune dane-dane kaini kandala ansha abin kunya. Saukar hannayensa akan bayana da yanda ya wani irin rungumoni tsamm ya sani lumshe idanuna dake rufe tare da jan numfashi a hankali mun kusa mintina uku a haka kowa na sauraren bugun zuciyar dan uwansa kafin ya kwantar dani a hankali shima ya kwanta yan Jan duvet ya lullubemu , sosai yanzu kam gabana ya fadi. Dan raba jikina nai kokarin yi da nashi ya girgixa man kansa cikin mugun low voice a kunnena ya furta "please stay! I need hakan babu abinda zanyi

Ajiyar zuciya na dan sauke mukai shiru. Harma na dauka barci ya kwashesa a bazata na sake jin muryasa a cikin kunnena. Tell me minene burinki.!

Saida nayi dan murmushi kafin na sake shigewa jikinsa dan yanzu kam zafin jikin nasa dadi yake man kasancewar nima kamar na fara jin sanyin abinka da wadda bata saba shiga ruwa ba. A hankali nima nace. "Yaya Awwab "

"No fadin yaya Awwab again. Sabon sunana nakeso

Da mamaki nace ," wane sabon suna ? Yashe ka samoshi".

"Yanzu da za'a mun mugunta bani magani mana In ba haka ba ni gsky zanbi takan dokan likitar nan .

Ai harda yar zabura nai amma sai ya maidani ya sake matsawa da fadin " Toki fada".

A shagwabe nace . Nifa nama manta".

Saida ya dan mintsineni sannan yace "Mai zafinki".

Jinai gaba daya kunya ta kamani ko yaushe nayi wannan irin baranbarama haka .....😂😂.....✍ *_Typing_*

TSUTSAR NAMA BOOK 3

Chapter: 37

Firgigit na dawo hankalina jin hannunsa a cıkın jıkina. Hannun na rike tare da marairaicewa na ce, "Please Yay... Uhmm uhmm My Hot" na fada kamar mai koyan magana ina kara cusa kaina cikin kirjinsa. Ina jin motsawar kirjinsa alamar yin murmushi. A zuciyata nace mugu dan masa

"You are my Hot too Aljannar duniyata. Fada min minene burin naki?".

Gaba daya jinai tsigar jikina na tashi saboda yanda yake min magana a cikin kunne a wani. kalar hankali. Ajlyar zuciya naja cikin dauriya da nuna juriya a hankali nima na ce, "Babban burina yanzu a duniya shine Ummie ta samu lafiya. Na biyu Yaya Musaddiq yay aure. Na uku ku daidaita kaida Yaya Fahad Please Yaya Awwab. Nasan ba son ranku bane. Amma Awwan Nasan na son ranku bane Ama kaine baba, kana amsa tamkar sursan uba ne a garemu baki daya Komi kake ja ranka ka dinga daurewa dan ALLAH Sannan ka yawaita ambaton sunan ALLAH da istigfan, salatin ANNABI da ambaton Hastinallatu wa-nimal wakil akoda yaushe. In sha ALLAHU zamuyi nasara. Dan haduwar kanku shine tsariin samuwar lafiyar Ummie, idan ba hakaba zamu cigaba da zama a karkashinigayar tufkada warwara ne. A varizu haka mataki na farko da hake so ka fara dauka bayan canja mata doctors din nan da kavi

shine maidota nan sashen. Tunda sananka balaukowa a maidata can, ko kuma kai ka koma catyta ta zauna nan kasa dan zafi mata sauki Haki za tamu damar kulle kowacce inin kofar hasarar cimma buri daga duk mai mummunar menuta Bank da wani burn a yanzu daya wuce tabbatuwar wadan nen abubuwan guda aku wihy

Wani irin matseni yay a jikinsa har sai da na saki karamar kara ya sassauta min. Yanda naji jikinsa na rawa yasa gabara fadowa. Da saun na dago tare da yaye duves din. Hannunsa yake kokarin karwe saman kansa ga wani irin juyewa da idanunisa ke neman yi. Da masifar saun no tashi zaune jikina na rawa. Gaba daya bargon na yaye, na wani irin daga kanisa na maida saman jikina tare da fisgar gorar ruwa na balle murfin. Diba nayi cikin hannuna na shafá masa a fuska, sannan na saka masa kan baki hawaye na rige-rigen sakko min. Da kyar na samu ya sha kadan, bariyi magana ba na fara karanto addu'or ina tofa masa Tamkar wani mai aljanu sai ya fara latawa a hankali a hankali har barcı ya daukesa. Tagumi kawal nayi na zuba masa ido, nama rasa wane kalar tunani zanyi. Ina nan zaune shiru na fara jiyo kamar hayaniya da dukan kofa. Jinai gabana ya fadi, a hankali na zame kansa a saman jikina na maida saman fillo tare da gyara masa bargon na sauka. Har nakai kofa na dawo, dan bathrobe ce a jikinmu daga ni har shi kasaricewar daga swimming pool muke, sai karamin towel da kaina ke nade a ciki Sauri-sauri na canja zuwa doguwar riga na saka hijjab kawai na fito. Babu kowa a falon, daga waje ne ake hayaniyar. Bude kofar nayi na fita gaba daya. Turus na tsaya jikina na rawa ina kallonsu, Fahad ne rike da wani shegen kaifaffen wuka irin na chinis din nan da zakaga suna fada da shi a films, sai faman rikesa ake yana rantsuwa sai ya kashe dan uwansa da hannunsa. Shi ya tsanesa, baya sonshi baya son ganinsa sai ya kashesa Abinda yay matukar bani mamaki kaf analın gidan idan ka cire Paah da Uncle din nan nasu kowa ka cire Paah da Uncle din nan nasu kowa yana nan. Amma duk sunyi tsaitsaye Baba ne kawai mijin Mama Balki ke kokarin ma Fahad magana, sai Mama dake rokonsa rama tana kuka. Sai kuma Hayatu da guards din Maash dake rirrike da Fahad din Sai Hafizzullah da ban san ma yana gidan ba na kokarın amsar wukar a hannun Fahad din cikin lallashi da dabaru Ido muka hada da Hajiya karama dake faman tabe baki, da sauri ta wayance ta gyara fuskar tata takai hannu tana sharar hawaye ita a dole kukama take yi. Kaina na girgiza na maida kan Hajlya Mammah. Waya ce a hannunta yanayınta da alamar damuwa da gani akwai wanda take son kira ko kuma tanata kiran ba'a daga ba Na maida kan Marman Malika: Kanta a kasa tana hawaye. Sai su Azizat da Arwa da yanayinsu ya nuna yanzu ma suke shigowa gidan suma sunyi tsuru-tsuru a cikin yanayi mai wahalar fassara. Sal masu alki da fuskokinsu ke nuna yanayi mabanbanta Bahijja dake kuka sosai kamar zata shide na zubama ido fiye da kowa, A'i na rike da itas itama tana sharban hawayen. Idanu na dan lumshe na bude ina mai sauke ajiyar zuciya.. Nayi alkawarin bakina bazai taba furta ni matar Maash bace, sai dai in har shine da kansa ya sanar musu Amma lokaci yayi da zan fara sasar musu. Arпта юкасı yayı da zar) rara buga

nawa acting din nima a cikin wasan nan. Sai da na karanto addu'a tare da dawowa ainahin Sam-G dita da kowa ya sani

Cikin dakiya fuska a daure da dan daga murya kadan na ce. "Ku sake shil"

A tare gaba daya, da wanda suka ganni tun dazu, da wanda basu san da fitowata ba duk suka dago suna kallona da matukar nuna mamaki a fuskokinsu. Çanin basu da niyyar sakin nasa a kausashe ha sake fadin, "Ku sakesa nace ko".

Hayatu ne ya fara sakinsa a hankali, sai Hafizzullah dake min wani irin kallo idanunsa duka a waje Bamma nuna na gansa ba ni sam, ganin Hayatu ya saki Fahad din suma guards din Maash duka sakesa, sai dai daka gansu kasan a tsorace suke. Hannayena na warware daga kirjina, kafin na shiga takawa a hankali na sakko a dan steps din dake gaban kofar sashen nasa. Dai-dai nan Hajiya Mammah ta wani irin zaburo a masife da nunani da yatsa ta ce. "Kail To ke kuma fa a waya kike wanhan maganar a gadarance haka?".

Ko kallon inda take bayi ba, na cigaba da takawa har gaban Fahad dake wani irin huci da karasa zaro wukar dake cikin kufenta dan dama hai gama cireta duka ba kasancewar dama bai gama cireta duka ba kasancewar Hafiz ya rike masa hannu. Saurın rikeni Hajiya karama tayı batare dana san sanda tama zo inda naken ba. Cikin girgiza kai ta furta, "No Please y'ammata. Zai iya jimiki ciwo baki ganin bashi da hankali".

Kaina na dan karkata na kalieta da ga sama har kasa cikin dage gira, sai kuma na dan girgiza kan nawa da gyara tsaiwata na ce "Avya ashe mahaukacine shima". Daga haka na dauke kaina na maida ga Fahad dake kokarin gittamu. Babu alamar wasa a tattare da ni na ce, "Yaya Fahad!"

Cak ya tsaya kamar wanda ake sarrafawa da remote. San banyi zaton zai tsaya din ba, kawai na gwada sa'ata ne kasan raina ina rokon UBANGIJI akan ya hanani jin kunya. Dan haka tsayawar tasa ta sakani wani irin jin sanyi a raina, ban damu da kallon da Hajiya Mammah da Hajiya karama kemun ba, kai dama kowa na wajen. Da baya na dan ja na koma gabansa. Ganin yanda yake hucin da cika da batsewa jikinsa na rawa ya sakani sakin murmushi. Batare da nayi magana ba na mika masa goran ruwan hannuna. Kin karba yayı, dan haka na sake sakin murmushin da

raunana murya nace, "Haba dai Autan Ummie ko sokake na saka riuma han varda da raunana murya nace, "Haba dai Autan Ummie, ko sokake na saka rigima ban yarda na bar maka autancin ba. Dan dama fa hakuri nayı kawai amma ina son autancina. Kasha kaji, muje mu duba Ummie na tabbatar tana matukar bukatarmu a kusa da ita. Shiko Yaya Awwab da kaina zan maka maganinsa. Yau sai ya bar mana gidan nan dan bazamu zauna da shi yana sakaka fushi ba Ina dalili ina dan mafari Yayana yafı gahan raini al, ungo kasha kay. Na kare maganar Ina kara mika masa rnuwan da mika dayan hannuna kuma alarmar ya bani wukar. Kamar mai shakkun yin hakan ya amshi ruwan ya bani wukar. Bamma san wani wawan ajiyar zuciya ya kufce min ba. Da kyar na danne hawayen da suka cika min ido ina satar kallonsa. Tuni ya balle murfin goran ya kai bakinsa yana sha da irin salon da dan uwansa yake shan ruwa a wasu lokutan. Sai da ya shanye tas ya mikomin roban. Amsa nayi ina murmushi da fadin, yauwa yayana you are the best Yaya in my life. Oya let's go wajen Ummien mu kafin kuda ya rigamu

A hankali ya saki murmushi. Muryarsa a dashe ya ce, "Kema you are the best kanwa in my life". Ya kare maganar yana mika min hannunsa wal na kama. Kafada na make masa tare da girgiza kai. A hankali na furta, "Wanan fare da girgiza kai. A hankali na furta, "Wanan hannun na sarki ne". Alamu yay min na bai ji minace ba wal. Sai kawal na sakar masa murmushi da nuna masa hanya. Kafada ya dan dage sama da tabe baki

"Na shiga uku ni Nafisa Wai mi nake shirin gani haka ne nikam? Ke kuma naki salon kenan kibi wa kibi kani Jama'a karuwanci a cikin gida

Kallontana dan yi na kashe mata ido daya lyeeeht Dan ubanki ni kike ma wannan abun? Kin san ko matsayına a wannan gidan?"

"Yar cin arziki mana

Na fada a hankali dai-dai zamu gittata Wani bala in zaburowa tai kaina tare da kai hannu zata fincikoni. Kamar walkiya Fahad ya sha gabanta. Cikin nuna tsantsar fusata ya ce "Mi zakiyi? Dukanta wai? Aiko da sai na datse wannan hannun naki ta yanda bazaki sake morarsa ba har abada Mammah

Wani inn tsuruu Hajiya Mammah tayı taqa kallonsa. Dan gaba daya fuskar yayansa take gari akan tashi fuskar. Mamaki take wal yaushe ma yaron nan ya zama kwalion dan iska haka shima. Ko duk karuwancin yarinyar nan ne dai halan?

TSUTSAR NAMA BOOK 3

QSe

Chapter: 38

Status

Ba Hajiya Mammah kawai ba, kowa chake wajen sai da mamalo ya nema kasheshi. Dan babu wanda bai saki baki ba. Sai ma Hayatu ne da abin ya beshi dariya. A zuciyarsa ya ce (pepper kanwar mu is back). A zahiri kam yana a layin yan kalo ne shima Hafizzullah ma dai dariya yake kokarin clannewa, shima a ransa ya ke gulamar (Humm Adda kartin halinki dabanne a rayuwa). Mama Ballo ma dai mamaki take, a kasan ranta kuwa jin wens alfahari take yi, lallai yanzu ne in sha ALLAHU aikin su zai tafi dai-dai. Blaba kansa murmushi yake a zuciyarsa, lallai ya sake tabbatar da yarinyar nan jinin Abdul-wahab ce, dan sam Abdul-wahab bal san wani abu tsoro ba a rayuwarsa. Shiyyasa ya kare rayuwarsa a bama ubangiciansu da bazasu taba mantawa be har abeda garkuwa...

A bangaren Hapya karama baki ta saki kawai, ga kafafunta na wani irin rava. Mamakin yarinyar da tu ajjibinta na neman halakata. Gaba daya hoton maharfinta ke dawo mata da abubuwan da suka dinga faruwa a tsakaninsu. Ta dayan gefen kuma shi kansa Fahad yaku ya goge mata hadda tas. Dan gaba daya ya juye Maash sak. (Yallabial muna cikin tashin hankali) ta fada a zuciyarta wata inin zufa na ketoma Ilahirin jikinta <

hankali) ta fada a zuciyarta wata irin zufa na ketoma n jikinta.

A bangaren ma'aikatan gidan musamman su Bahijja kusan suma a sumen suke da mamakın Kandalar, duk da dame a cikin shock din ganinta ma suke a gidan kasaricewar sunjikus-kus din da akeyi a gidan na wal Boss din su ya mata fyade. Duk da mali yawansu basu yarda ba sudal, dan wani irin kima da mutuncin Maash suke gani a rayuwarsu saboda ya musu abubuwa da yawan gaske da suka rasa a gidajen lyayensu...

Koda ya shiga dakin kai-kawo ya dinga yi tamkar mal safa da marwa kafin ya dauki waya ya danna kira. Kasancewar ba number Nigeria bace ya jima kafin ya samesa. Dan har ma ya fara tunanin komawa ta WhatsApp suyi video call, sal kuna akal sa a ta shiga. Bugu biyu aka daga, bai tsaya ko sauraren gaisuwar da yaron nasa ke masa da ga can ba ya wani daka masa tsawa

"Na baka awa ashirin da hudu na ganka a gabana. Idan ba haka ba, wihy! winy! Sal na saka an yo maka daukar amarya da ga UK zuwa Nigeria. Wawa kawal, har ni zaka yaudara, ina baka ci da sha da daukar bukatunka ashe sakarai ka maidani wanda baima san abinda yake ba.."ArewaBooks

turika ashe sakarai ka maidani wanda baims a Kayake ba... A

"Yallabei wihy! Wihy ba yanda kake zato bane. N Kaina ine a cikin tashin hankali. Tun dezun na rasa ta yanda zan kiraka na sanar maka yaron nan ya gudu. Wihy sai da aka tsara komal dan a yanzu haka akan yazo Dubai hutawa ne shida abokansa, kuma n sanar maka a ranar. Nima na sayi ticket din tafiya Dubai din kamar yanda kace ama jirgi daya zamu wuce aka samu matsala a airport din, na cigaba da kokarin ganin na samu next flight sai kawai na tsinta zancen wai Nigeria ya wuce da ga bakin abokin nasa. Nayi yurikurin biyosan tun a jiya jaman tsaro suka kamani ko awa daya banyi da fitowa ba, Yanzu haka cikin kokain ganin jirgin da zai tashi nan da awa daya dani ne dan na fahimci komai an tsara shi ne har kamani da akayi set-up ne kawai. Amma dan ALLAH yallabai ka gafarceni, ina nan tafe Kasa ya cewa da shi komal Baba prof yayı, sai ma wurga wayar da yay saman gado yay wan irin kawa zaune hannayensa duk biyu dafe da kansa dake wani kalar jujjuya masa kamar brain dinsa zata wulkice. Y jina a haka, sai da yaji bugun zuciyarsa na neman canjawa sannan ya kai kwance. Barci ya sha sosal, sal dai kafinma yayisa ya jima yana sambatun ambaton sunan Ibrahim Alonso da zuri'arsa. Sai da kyar barcin yay awan gaba da shi. Bai tashi farkawa ba sai yanzu kusan goma sha biyu na dare. Ya jima idanunsa akan agogon dakin nasa tamkar mai lissafa adadin dakikun da suka rage a rayuwarsa, kafin ta mika zuwo bayi. A cikin ma ya kwashe lokacı kafin ya fito ya rama salloli sannan ya zura jallabiya ya fito falo <

cilen ma ya kwashe lokaci kafin ya fito ya rama salloli n ya zura jallabiya ya fito falo Shine ya dari samu ya sha. Fitiler felon ya rage batare Tamkar fitowar tasa kuku ke jira, dan funi ya fito ya jere masa kayan abinci a gabansa kasancewar yasan da dare baye hawa dining cin abinci. Duk yanda yake jin matsananciyar yurwa bai ya cin abincin ba ma, sai black tea din nashi na fama ya bukaci a kawo masa da kunne tv ba ya zauna shiru yana nazartar abubuwa yanda ya kamata. Dan dazun gaba daya a birkice yake, shiyyasa hatta bayanin Commando bakwai komai ya gane ba. Dawowar nan ta Fahad ta matukar dagula lissafinsa. Sai batan yarinyar da bai taba

sake maida hankali kanta a lissafinsa ba tun randa ta gitta tamkar walkiya a tsakkiyar hadarin daya kankama zai zubda ruwa

Fie din da commondo ya kawo masa ya sake dauka, ya shiga binsa daki-daki dan dazun kamar sama-sama ya duba shi. Saida ya duba tsaff sannan ya fara lissafi, Tayi aure, an kaita gidan miji, har gidan da aka kaita commando yaje amma babu kowa sai maigadi. Ya binciki maigadi, amma bai samo komal ba, dan babu abinda ya sani face ogansa da yake lora da oga. Abinda ya kawo masa rudani a wannan gabar shine iwanan amaryar ogansa daya a gidan ta gudu da safe, har tai yunkurin fasa kansa idan bai bude mata kofa bo. A binciken Commando bata koma gidansu be, amma tayi jiyya a wani pravet hospital, Ya bibiyi asibitin amma bai samu komai ba sai sunan Ikitar data kula cia yarinyar tama kawota asibitin, a

yanzu kuma bata asibitin waj, bincike iya bincike na

commando kuma bai ganota ba ko inda take har

yanzu balle ita yarinyar sai lya kawai an mata transfer <

dacale, har tai yunkunn fasa kansa idan bai bude kofa be, A binciken Commando bata kom A

Upd

gidansu ba, amma tayi jyya a weni pravet hospital, Ya bibiyi asibitin amma bai samu komai ba sai sunan

QSe

Status

Tikitar data kula da yarinyar tama kawota asibitin, a yanzu kuma bata asibitin wai, bincike iya bincike na commando kuma bai garota ba ko inda take har yanzu balle ita yarinyar sai lya kawai an mata transfer zuwa Abuja. Abuja wane asibiti? Basu gano ba shima Kansa yay wani irin dafewa yana mai furzar da huci. Sai kuma ya jawo waya yay kiran Commondo. Bai tsaya armsa ko gasuwarsa tia yace ya samesa gida. Kawe ya yanke kiran.

Bako a cika mintuna talatin ciff ba sai ga amintaccense yazo ya sanar masa Commando yazu yana falon baki. Hannu kawai ya daga masa alamar yajn. Bayan ya woce sheria ya mike yabi hariyar da zata sadashi da falon bakın tanan cikin falonsa. Da saun commando dake zaune a kuera ya mike tsaye kansa a kasa domin girmamawa. Ba zamu kirashi yaro ba gaskiya. Dan shekaru kam zasu iya tasenma hamsin da wani abu. Sa dai yanayinsa ya nuna lallai a lokacin kuructya anyi rashin ji sosal, a yanzun ma bai zama fallai an bari ba. Nuni Baba prof ya masa kan ya zauna. Babu musu ya kai zaune sannan ya sak gaidashi, Nan ma kansa kawal ya daga masa sal kuma sukai shiru, Kusan minti daya kafin baba prof din ya dago yana sauke ajiyar numfashi

"Commando alkirika yayi kyau sosal, bance komai bane saboda rana a bace yake a dazun".

"Na sani boss, babu wani damuwa kayı komai ba

komai girmanka ne".<

dacale, har tai yunkunn fasa kansa idan bai bude kofa be, A binciken Commando bata kom A

Upd

gidansu ba, amma tayi jyya a weni pravet hospital, Ya bibiyi asibitin amma bai samu komai ba sai sunan

Tikitar data kula da yarinyar tama kawota asibitin, a yanzu kuma bata asibitin wai, bincike iya bincike na commando kuma bai garota ba ko inda take har yanzu balle ita yarinyar sai lya kawai an mata transfer zuwa Abuja. Abuja wane asibiti? Basu

gano ba shima Kansa yay wani irin dafewa yana mai furzar da huci. Sai kuma ya jawo waya yay kiran Commondo. Bai tsaya armsa ko gasuwarsa tia yace ya samesa gida. Kawe ya yanke kiran.

Bako a cika mintuna talatin ciff ba sai ga amintaccense yazo ya sanar masa Commando yazu yana falon baki. Hannu kawai ya daga masa alamar yajn. Bayan ya woce sheria ya mike yabi hariyar da zata sadashi da falon bakın tanan cikin falonsa. Da saun commando dake zaune a kuera ya mike tsaye kansa a kasa domin girmamawa. Ba zamu kirashi yaro ba gaskiya. Dan shekaru kam zasu iya tasenma hamsin da wani abu. Sa dai yanayinsa ya nuna lallai a lokacin kuructya anyi rashin ji sosal, a yanzun ma bai zama fallai an bari ba. Nuni Baba prof ya masa kan ya zauna. Babu musu ya kai zaune sannan ya sak gaidashi, Nan ma kansa kawal ya daga masa sal kuma sukai shiru, Kusan minti daya kafin baba prof din ya dago yana sauke ajiyar numfashi

"Commando alkirika yayi kyau sosal, bance komai bane saboda rana a bace yake a dazun".

"Na sani boss, babu wani damuwa kayı komai baA

sani boss, babu wani damuwa kayi komai ba girmanka ne

Upd Murmushi Baba prof yayı da gyara zamansa. Sa kuma ya dan furzar da numfashi, "Ya akai bincike tai Sea karana inda nafi bukata ba. Dan ina son sanin wanene mijn nata fiye da komar

Status

"Na sani boss, nima naso nakal har can din amma komal ya datse kansa. Sai dai duk da haka bawal na dakata bane. No kawo maka wannan din ne saboda naga ka matsu, Amma akwai yan swanta Maza guda bryu zan maida akalar aikina kansu, ai dole dai su san wanene ta aura? Sai shi wanda ya riketa shima yana cikin tisarmina. Kar har walliyin auren da sahala ya sira

RECENT

Murmushi mai fadi Baba prof yayi, dan yanda yaron nasa ke wani magana a ciccije yana birgesa, Kansa ya jinjina da gyara zamansa. "Shiyyasa kake birgeni sosal, dan nasan in har zan damka aikina a hannunka banda wata matsala a kai. Yanzu ma inada wani alka kasa, vana da olaka kuma da wannan din da kake y

"A to oga lafiya lau ne. Watso umarninka kawa a shirye nake na cafesa da hannu biyu

"Ina godiya. Zan dan baka alkın kadan a bude yanda zakafi fahimtarsa, ita yarinyar da kake wannan binciken a kanta yanzu haka tana a Maash Mansion ne

Wani inin dalalo ido Commando yayi waje. Tare da dafe bakinsa ya ce, "Kan ubancan kai. Amma ta barni naketa walankeduwa kamar wani shaho. A to lallai tana bukatar balli-balli a kan fuskarta kenan"18:08

6

naketa walankeduwa kamar wani shaho. A to lallai pukatar balli-balli a kan fuskarta kenan". A

Murmushi Baba prof yayi kawai, tare da cigaba da fadin, "Ai bamu zo nan ba Commando. Abinda nake son kamun a kanta biyu ne zuwa uku. Na farko ina son sanin mi tazo yi Maash Mansion. Na biyu ka tabbatar min da tanada alaka da Awwab ne tako wane irin fanni ko bata da? Na uku a cikin gidan tanada alaka da wani ne? Misalai, masu aiki, ko cikin masu gidan, ko masu hudda da gidan ta waje. Na karshe wanene ya shigo da ita Lagos dan a matsayin mai aiki take a Maash Mansion"

"Oga duka aikinka masu saukine a garan kaima ka sani, sai dai magana ta ALLAH tsaurin a waje guda yake. Nifa kasan in dai sabga da Zakin gidan nan naka a ciki tsoronta nake gaskiyar magana. Ka sani na sani aljani ma nan ya ga Maash ya barsa. Dan duk iskancina na tsawon shekaru yaron nan yakan goge min hadda tsaff. Kaga dai Jaga, duk yanda na gatanta yaron nan daga turashi aiki jikinsa sai da yaron

nan ya sabemin ya koma bayansa. Badan munyi wuff mun kaddamar mas ba da yanzu ya bude mana aiki fa. Boss kasan da haka ta faru fa babu tantama China Maash zai kaimu a markade namominmu da ranmu a durisa a gwangwanaye a dawo dashi Nigeria a dinga sayarwa matsayin naman tsakkiyar shawarma. Kai kanka yanda nake ganin idanunsa zai iya sawa a masa bandarka..."

"Commando!!".

Baba prof ya fada a fusace cikin daka masa matsanancinyar tsawa.....*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page thirty-nine

39

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

.....“Kaiyya oga sa'a dai sa'a dai. Kafa san ni a ɓangaren gaskiya ba ruwana feɗewa nake filla-filla. Amma dai tunda baka son ji bari nayi kurumm. Zanje na fara aiki amma dai ka ƙara tunani akan Maash, Nima zanyi tunani muga. Matsalar shi ba mata yake bi ba, baya hawa network kuma, amma da komai yazo da sauƙi ai”.

Gaba ɗaya Baba prof ya gamsu da bayanin Commando. Shi kansa shiyyasa yake a cikin ruɗani akan batun yarinyar nan da kuma abinda ya faru tsakanin Awwab ɗin da ita. Maash baya neman mata, shi shaida ne akan hakan. Sannan akwai wani dalilin da yasa baima kawo cewar shine ya aureta a ransa ba, dan yayi imani da shirinsa a kansa matuƙa. Shiyyasa ko fyaɗen nan har yanzu zuciyarsa bata gama yarda shine ya aikata ba. To amma abinda ya faru a asibiti fa? A gabansu fa yaron nan yay kissing yarinyar (Randa Maash ya samesu a asibiti, su a tunaninsu ma lokacin kissing ɗinta yayi). Dan ɗauka bai wani ɗauketa da muhimmanci ba, hakama kulawa a asibitin, komai zai iya yi dan yana da tausayi. Kai gaba ɗaya shi yama rasa ina zai kama gaskiya..

Waya ya ɗauka har zai dannama Hajiya ƙarama kira sai kuma ya fasa. Saƙo ya tura mata ya kashe wayar tare da miƙewa ya fita. Amintaccensa ya kira suka fita a gidan duk da kuwa dare ne dan har ƙarfe ɗaya ma ta gota....

□□□□□

Tunda na janyo ra'ayin Fahad muka nufi sashen Ummie ban sake bi takan ahalin gidan ba. Dan ko Hayatu da Hafiz anan suka samemu. Da yake muna a falon farko ne na shiga sashen sai muka baje munata hira abinmu harda Mama Balki. Kamar wasa abota ta ƙullu tsakanin Hafiz da Fahad duk da kuwa Fahad ya girmi Hafiz sosai. Dan koni ma ya girma balle shi. Da alama hakan ya faranta ran Hayatu, dan daga ƙarshe cayay su tashi suje yawo tunda yau boss na hutu. Har zasu fice na ma

Hayatu magana. Duk da dai yanzu kunyar abinda na dinga masa nake ji, amma dai na daure na ce, “Yaya Hayat dan ALLAH idan babu damuwa kuma oganka bazaiyi faɗa ba mizai hana a sayo kayan amfani na kitchen ɗin sashensa naga wanda suke ciki basu da wani yawa. Tare da kayan abinci sai na dinga mana girki acan. Naga sam bai damu da abinci ba sai kayan chocolate. Sannan ita kanta Ummie ya kamata ace nike mata abinci hidimar nama Mama Balki yawa. Ga kuma Fahad ma ya ƙaru”.

Sosai fuskarsa ta ƙawatu da murmushi. Ya ce, “Wannan shawara ce mai ƙyai Auntynmu. Kuma naji daɗi kamar yanda nasan Boss zaiji daɗi fiye ma da yanda naji ɗin. In sha ALLAHU ki bamu nan zuwa anjima duk abinda kike buƙata za'a kawoshi. Yanzu hakama zanyi waya da companyn da zasu zo su gyara kitchen ɗin su saka komai daya dace, kafin su gama mu kuma mun haɗo cefanen”.

“Nagode sosai Yaya Hayat”.

“Muke da godiya Auntynmu. Koba komai kwanan nan Yayanmu zaiyi kaurin wuya da tunbi”.

Dariya sosai zancensa ya bani, amma sai na murmusa kawai. Shima fita yay yana murmushin dan su Fahad tuni sun fice abinsu...

Kamar ko yanda ya faɗa ɗin haka ce ta faru. Dan na fita zuwa yin sallar la'asar daga nan na dubasu na samu drivern sa (TJ) da Guard ɗinsa da nake yawan ganinsu tare shima (Shu'aibu) tare da baƙi. Gaisheni sukai TJ ɗin ya bani waya. Jin Muryar Hayatu ya sani sauke ajiyar zuciya, shine yamun bayanin na basu damar shiga tare da masu company da zasuyi aiki. Duk da nayi mamaki ganin yammafa tayi yaushe har za'a kammala? Sai ban musa ba na basu dama ni kuma na shige ciki domin duba shi.

Da sallama na shiga ɗakin kamar mai jin tsoro, ganinsa tsaye gaban mirror yana fesa turare ya sani jin farin ciki. Ɗan kallonsa nayi na ɗauke kaina. Dan fesa turarensa yake kamar ma bai san da shigowata ba. Wannan halin nasa na shariya da ɗaukar kai na ban mamaki. Jinai kamar na watsar da shi nima na wuce abina. Amma sai na daure tunda koba komai na barsa babu lafiya. Muryata can ƙasa batare dana sake kallonsa ba na ce, “Ashe ka tashi, yaya jikin?”. Nai ƙoƙarin wucewa abina. Har na gittashi naji ba'a amsa min ba, sai na tsaya cak, dan magana ta ALLAH ban san wulaƙanci sam. Cikin ɗan yanayin jin haushi na ɗago manyan idanuna na kallesa. A mamakina sai na samu shima ni ya zubama ido. Dan ya daina fesa turaren ma ya jingina da mirror kawai yana kallona. Baki na tura masa tare da juyawa zan cigaba da tafiyata caraf aka cafke hannuna. Ƙin juyawa nai na kallesa. Sai dai ban ƙwace hannuna ba daga riƙon da yay min. Munfi sakan goma a haka shi bai sakeni ba shi baice komai ba. Jinai wani takaici ya sake kume mun zuciya, sai

nai ƙoƙarin jan hannun nawa. Sake riƙeni yay da ƙyau, tare da matsoni jikinsa ya juyoni gaba ɗaya na muna fuskantar juna. Ban yarda na kallesa ba, ban kuma ce da shi komai ba. Sai kawai ya ƙarasa jawoni jikin nasa ya rungume. A kusan tare ni da shi muka saki ajiyar zukata, kafin ya dagoni fuskata a cikin tafukan hannunsa duka biyu.

“Yau ba magana ne?”.

Ya faɗa da soft murya kuma can ƙasa da ni kaina dan yana a kusa dani ne na jisa. Ban kallensan ba, ban kuma ce komai ba sai kafaɗa dana maƙe masa.

“Oh! Why?”.

Sai da na ɗan murguɗa baki sannan nace, “Ai kaima baka yi ba”.

“Uhhmyim. Dan banyi ba sai kema ba zakiyi ba?”.

Kaina na jinjina masa alamar eh.

“Humm Aku na ta zama kurma kenan yau?”.

“Ni dai ba Aku bane”.

“To miye? Banan kike cika mana kunni da surutu ba ke a dole yar jarida”.

Farr nai da idanuna, tare da ɗan jujjuyasu, sannan na ɗan murguɗa baki na ce, “Kaima ai shaida ne tunda na karya maka record. Ko nayi ƙarya”. Na ƙare maganar ina waro masa idanuna sosai.

Maimakon ya tanka sai kawai ya saki murmushi, tare da kissing idanun nawa. Kunya ce ta kamani kuma. Dan haka nayi yunƙurin kwace fuskata amma yaƙi barina. Dole na haƙura amma na rufe idanuna naƙi yarda na sake kallonsa. Sai dai kuma shi ina cigaba da jin tasirin idanunsa a kaina sosai. Ganin bashi da niyyar barina a shagwaɓe na ce, “Gashi can za'a shiga salla fa”.

Tamkar wanda na dawo a hayyacinsa ya furzar da wani irin nannauyan numfashi. Sai kuma ya saki mun fuska a hankali. Jin kamar ba hanyar fita yayi ba na buɗe idanuna. Sai na hangosa zai shige bathroom. Mamaki hakan ya bani, sai dai bance komai ba na tsaya a wajen, babu jimawa kuwa sai gashi ya fito da alama alwala ya ɗauro. Har ya gittani zai wuce sai kuma ya ɗan dawo baya. Dawowar tasa ya sani ɗagowa na kallesa. Dai-dai da ya kawo fuskarsa gab da tawa, dan haka a bazata naji saukar sumba a saman goshina. Kafin ma nayi wani yunƙuri ya fice a binsa. Bamma san sanda na saki murmushi ba da kai hannu na shafi lips ɗina da goshina a hankali. Kasan raina kuma ina dariyar al'awar da ya sake, wato mutumin nan ja... Humm bari dai nayi shiru kada danginsa su min ca..

(Kin taimaki kanki kuwa, dan ba barinki zamuyi ba😎😉.)

Fitowarsa ya saka su TJ masu jagorantar companyn nan dake shigo da kwalayen kayan aikinsu rissinawa suna gaishesa. Kallonsu kawai yake batare daya amsa musu ba. Dan haka Shu'aibu ya fara masa bayanin cewa Hayatu ne ya turo companyn ya kuma kira su akan su sami Aunty ta basu izinin shiga da kayan. Shine yanzu da zata shiga suka sanar mata ta basu izini.. maimakon ya amsa musu bayanin da sukai masan sai ya ɗauke kai tamkar ma bai ji bayanin ba. Takunsa ya cigaba dayi cike da bajinta da mazantaka. Sai da yaje gaf da fita a daƙilen nan nasa ya furta, “Ina fatan dai kunyi salla? Su kuma aikinsu ya koma ta back door”.

Daga haka ya ficewarsa. Sanin basuyin ba ya sasu ajiye aiki suka bar wanda ba musulmai ba. Amma kamar yanda yay umarnin komawarsu ta back door sai suka kulle ƙofar tanan nan falo suka koma ta can ƙofar baya ta kitchen ɗin.....

❤❤❤❤

Jigatuwa iya jigatuwa Baby tayi, dan bata tashi farkawa ba sai a hannu Doctors. Su kansu likitocin ma firgitata sukayi. Dan daga ganinsu kaga irin manyan gawurtattun yan iskan turawan nan da akafi gani a cikin films matsayin criminals. Illahirin jikinsu ne tattoo baƙi da jaa. Ga wasu irin yan iskan abubuwa kamar stones sun manna a fuska harda haƙora babu ƙyan gani. Sun kuma irin zama ɓarka-ɓarka ɗin nan saboda workout. Idanunsu kam harda kwalli ga yan kunne. Kai tako ina dai basu da ƙyan gani. Tana ji tana gani sukai treatment ɗinta. Ba wannan ya tada mata hankali kawai ba. Sai da nishi ya isheta ta waiga ta gefenta kasancewar ko iya zama batayi sai kwance rigingine sai kawai tayi tozali da mijin nata na aikata irin abinda ya aikata da ita da ɗaya daga cikin yan iskan dake a kanta matsayin likitoci. Wani irin uhun tashin hankali ta saki. Sai dai a mamakinta ko'a jikinsu kamarma basu jita ba harkokin gabansu suke, sai wasunsu ne ma da suka kwashe da dariya. Haka ta dinga musu ihun kuka tana zaginsu da Hausa da turanci, tare da tsine musu ta uwa ta uba tana kiransu yan wuta.

Oho ita tama san mi take faɗa, dan hatta turancin nata babu alamar suna ganewa. (A Nigeria kuma sune wayayyu ma'iya turanci😝). Haka sukai kunnen uwar shegu da ita har suka gama hidimarsu sannan suka fice suka barta a ɗakin ita kaɗai sai mijin nata daya shiga wanka shi da ƙaton da suka gama aikata alfasha. Tana nan tana cigaba da cin kukanta suka fito riƙe da juna kamar wasu mata da miji. Sai kawai taji numfashinta ma na neman ɗaukewa. Dan duk iskancinta da ƙarancin rashin ilimi tasan wannan aiki ya ƙazanta.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ □TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty

40

.....Wato jama'a kuɗi! Kuɗi! Kuɗi!! Humm dole ma musha wahala akan kuɗi wlhy. Yo duk in kana son abu a rayuwarnan a yi maka shi tamkar ƙyaftawar idanu tofa lallai sai da kuɗi. Shiyyasa gasu nan sun zame mana masifar rayuwa. Talaka da baida su yafi kowa shan wahalar rayuwar. Karna dai cikaku da surutu. Ba komai ya sani muku sambatun nan ba sai da na fito ganin kitchen ɗin da aka shirya cikin abinda bai gaza awa uku ba. Tsaff an gama shirya duk wani abinda za'a buƙata a cikinsa kalar kitchen cabinet ɗin. Tuni ya canja kamar bashi ba a ɗazun tsurarsa sai cabinet. Ban sake tsinkewa ba sai da na shiga cikin store naga yanda aka ajiye wasu extra kayan aikin iri daban-daban. “Tab ɗin, ALLAH dai ya gafarta mana to. Ya bama kowa halalinsa ya kuma bamu tsahon ran mora da neman lahirarmu a cikin duniyarmu”.

Na fito inata ƙara jinjina al'amarin na sameshi a falon da alama shigowarsa kenan. Dan tun fita massalaci sallar la'asar bai dawo ba sai yanzu da ake shirin gab da magriba. Cike da ɗauki na ƙarasa inda yake na zauna ta kujerar gefen. Duk da kunyar yanda ya wani zuba min idanunsa nake yi haka na fuske abina.

“Hummm Yaa Awwab kaga kuwa yanda suka maida kitchen ɗin nan? Tab ɗin jan aljannar duniya. ALLAH yanda kasan mutum ya koma can ya saka gado kawai ace canne ɗakinsa. Gaskiya mutanen nan sun iya aiki tabb”.

“Shi kuma wannan bakin ya iya surutu”.

Ya faɗa yana wani lumshe idanu da buɗewa tamkar wanda ya sha yay marisa. Ɓata fuska nayi tare da tunzura bakin na ce, “Namayi fushi, dama ka samu nake baka labari ko”. Na tashi fuuu zan gudu. Ji nai kawai an fisgoni, sai gani daɓar a

saman cinyarsa. Kʼoƙarin ƙwace kaina na shiga yi ina kukan taɓara da faɗin, “Ni ka barni babu ruwana da kai. Kowa yay sabgarsa, ni wajen Ummiena ma zan koma”.

Tsam ya matseni a jikinsa yana mai cusa fuskarsa a gefen wuyana. Yayinda numfashinsa ke shiga cikin kunnena da sautin dan murmushinsa. Ban fasa yunƙurin sauka a jikin nasa ba har sai da ya ɗan cizar min kunne, gaba ɗayana na naɗe masa jiki tare da sakin yʻar ƙara, a shagwaɓe na ce, “Wayyo Ummie King zai cire min kunni. ALLAH ni bazan yarda ba sai na rama cizona”. Na faɗa ina mai hayewa jikin nasa gaba ɗaya nima na shiga kokawar laluben kunnensa ni a dole saina ciza..

“Oh my god, yarinyar nan baki son zaman lafiya sam”. Ya faɗa kamar zai saki kuka yana kare kunnensa duka biyu da hannayensa. Oho bamma nuna na jisa ba, na shiga cigaba da ƙoƙarin zame hannunsa da hannu ɗaya, ɗayan na kaisa gefen cikinsa ina mintsina. Hannunsa ɗaya dake a saman kunnen ya cire yana ƙoƙarin buge nawa dake mintsininsa. Ai ko sai na samu caraf na cafke kunnen. Kaɗan na ciza amma mutumin nan ya wani saki yʻar ƙara da faɗin, “Ouchhh! Ummie kunnina, tiger ta ciresa”.

Sosai na ƙyalkyale da dariya. Na yunƙura zan gudu ina faɗin, “Sai tsoro ga jan faɗa”. Caraf ya riƙoni yana ɓata fuska. Marairaice tawa fuskar nayi kamar zanyi kuka na ce, “Ayya Yaa Awwab ayya!. Nifa yʻar ƙararrama ce kar kace zaka rama”. Harara ya zuba min yana sake ɓata fuska da murza kunnensa da hannu alamar har yanzu yana masa zafi ko kuma shagwaɓa ce ta motsa abinka da Ajebota. Ganin yanda ya zuba min idanunsan nan na maguna kamar zai cinyeni da su, ga fuskarsa babu alamar fara'a ya sani sake narairaicewa. “Na tub...”

“Shii!!!” ya katseni yana sake ƙanƙance idanun da shanyesu kamar mai jin barci. Sai kuma ya ɗan yamutse fuskar da motsa lips ɗinsa a hankali ya furta, “Sai fa na rama”.

“Mi ɗin?”.

Na faɗa cikin waro idanuna. Hararata ya ɗan yi, da sake matso da fuskata gab da tashi, sosai na sake waro idanun da marairaice fuska zanyi magana a hankali ya wani irin sauke small pinkish lips ɗinsa a kan nawa. A salon daya cafka lips ɗin nawa yasa bamma san na ƙanƙamesa ba.....

“Yau na shiga uku! Mizan gani haka ni Nafisatu Adams”.

A bazata muka ji saukar muryar Hajiya Mammah a saman kammu. Kici-kicin ƙwace kaina na shiga yi duk da shi bashi da niyyar yin hakan kuma sarai yaji abinda naji. Amma bawan ALLAHn nan sai ya wani sake matseni da komawa wani irin salo na taƙadarin namiji da sam babu ɓarɓashin kunya tattare da idanunsa. Ina jin ta sake saka salati har muryarta na rawa...

Ba muryar Hajiya Mammah ba hatta jikinta rawa yake yi. Ba komai ya firgitata ba sai ganin ko kallo bata ishi Maash ɗin ba ma. Sai ma wani sabon salan iskanci da yake yi a jikin Samraah ɗin. Duk da iskancin ɗan iska akwai a inda idan akai wani iskancin shi da kansa kunyar kansa da kansa yake. Dan haka Hajiya Mammah taga abinda zai tsiyayar mata da idanun ganinta batama san lokacin da tai wufff ta fice waje ba jikinta na ɓari, mamaki ma take wai yaushe Maash ɗin yay irin wannan fitsarewar ne? Dama yaron nan bayan iya wulaƙanci da raini ma mutane tantirin ɗan hau ne?. Ai ko baiji kumyar kansa ba ya tuna ita ɗin yayar ubansa take fa... Fuuu-fuuuu take wucewa kamar wadda ake controlling da remote. Ko kallon masu gaisheta batayi ta afka ɗakinta ta kulle kanta. Jingina tayi da murfin ƙofar tana sauke numfashi a gwagwgwame. Ita wannan yaron zaima tantiranci haka? Daga ta nuna masa hanya shike nan abu na neman zama bala'i. Tayi barazana wa hukuma amma ko'a jikinsa ma. Hasalima sai ya bita yana gasa mata magana. (Yi baga yarinyar ba ma ɗazun ta gasa miki) wani sashi na zuciyarta ya ayyana mata. Tab ɗin jan, babbar magana ɗan sanda yaga gawar soja. Shin ko dai bayan abin farko ya faru yaron nan zuwa yay ya zagaye aka ɗaura masa aure da yarinyar nan? Yo inba auren ba taya za'ai ma wai a dinga wannan kwamacalar ne haka. Ko yar iskar yarinyar nan dai dama ta saba da harkar nan ita ke ƙara kanainayesa. Ko kuma ta masa barazana idan bai cigaba da mata ba zata tona shi. Kai yafa kamata su dawo cikin hankalinsu...

Laluben waya ta shiga yi, cikin Sa'a kuwa ta samota a aljihun doguwar rigarta. Har rawa jikinta yake wajen son kiran Baba prof. Sai dai har ta yanke ba'a ɗaga ba. Kiran ta sake yi nan ma shiru. Sai kawai ta tura masa saƙo tasan dai idan ya gani zai kirata. Daga haka taja ƙafafunta da ƙyar zuwa kan sofa ta zauna ta zabga tagumi. Iskancin Maash na mata kai-kawo a cikin idanu da ba shegiyar yarinyar nan mai kama da afiruwa.....

□□□□□

Ram jami'an tsaron Dubai sukayi da Mansoor batare da bashi damar yin wata magana ba wai sai a office. Duk yanda yake son kare kansa da tabbatar musu gaskiyar al'amari sunƙi saurarensa. Sai ma tabbatar masa da sukai duk da abinda ya faɗa shine zai zama hujja garesa a wajen alƙali a court. Yana ji yana gani kuwa suka sakayashi a cikin cell cikin manyan criminals.. Abin kamar wani wasa sai gashi kusan sati uku shi ba'a kaisa court ɗin ba, ba kuma a yarda an samar masa da lawyer ba. Sun kuma hanashi neman kowa a waya dan dama sun amshe tasa a hannunsu. Sannan ko buga wayar cikin station da suke da ita sun hanashi wannan damar. Ganin tun komai zai iya zama labari amma ya gagara zaman ya fara tada ma Mansoor hankalinsa. Ance duk wanda yabar gida gida zai barsa, to lallai hakance ta fara faruwa da al'amarin sa. Dan kuwa gadai shi cikin masifar rayuwa da

yake kallonta ba komai ba a farko amma rashin wani nashi da zai san halin da yake ciki na neman dulmiya rayuwarsa a masifar da babu wanda yasan iya ina zata tsaya kuma. Iyaye ba wasa ba, ko da ɗan iska zaka zama idan da albarkar iyaye wlhy kafin cin ribar iskancin (idan har masuyi na ganin akwai ribar a ciki fa kenan. Dan kar ace Bilyn Abdull tace iskancin akwai riba da albarkar iyaye bance ba😂😵). A ranar cikarsa wata guda suka fara kaisa kotu, musawar da yay a zama na farko da dagewa akan shi bai aikata abinda ake tuhumarsa da shi ba yasa aka ɗage Shari'a aka miƙashi ajiya prison. Cikin amincin UBANGIJI a wannan zama wata baiwar ALLAH yar Nigeria taci karo da shiri'ar. Haka kawai tun a ganin Mansoor ɗin ta fahimci lallai akwai lauje cikin naɗi, sannan kishin juna na baƙin fatar da kasancewarsa ɗan ƙasarta ya sata shiga da fita har sai da ta samu damar ganinsa a prison ɗin bayan kwana biyar. Da yake akwai ilimi sai da ta samu nasarar yin hakan.....

□□□□□

Duk yanda naso kuɓuta daga hannunsa a wannan gaɓar bai bani wannan damar ba sam. Sosai hankalina ya tashi da tsoron kar wani ya sake shigowa ya samemu a wannan halin kamar yanda Hajiya Mammah ɗin tayi. Amma bawan ALLAHn nan ko'a kwalar rigarsa bidirinsa yake yi. Sai da yayi yanda yake so sanan ya barni tare da rungumeni tsam-tsam a jikinsa. Duk da nima riƙen nake da shi fatana ya sakeni na sauka a jikin nasa. Amma bashi da niyyar hakan. Da ƙyar nayi ƙarfin halin fisgo furucin dake bakina na furta, “Yaya Hajiya Mammah fa”.

Ya jima shiru babu alamar yama ji mina faɗa, dan har na fidda rai da samun amsa ko samun damar barina sai naji a hankali ya fara sassauta min riƙon. Sai da na fara murnar zan samu dama na tashi sai naji muryarsa da tai matuƙar shaƙewa can ƙasan maƙoshi a cikin kunnena.

“Waye ita?”.

Tsabar mamakin mutumin nan bamma san na manta da wata aba kunya ba na ɗago manyan idanuna da suka gama shigewa ciki suka canja launi na zuba masa. Cikin suɓutar baki na ce, “Hajiya Mammah ɗin?”.

Fuskarsa a yamutse ya ɗaga min kai alamar eh. (Mutumin nan zai kasheni da halinsa) na faɗa a zuciyata ina mai ƙura masa ido. A zahiri kam sai na yunƙura kawai zan sauka daga jikinsa. Amma sai ya hana hakan, sai ma a ɗan kausashe da daƙilalliyar muryar nan tasa da ke fita so silent ya furta, “Idan kika tashi ALLAH sai na ɗauke ki naje da ke har cikin ɗakin barcinta na miki abinda yafi wanda ta gani ɗin. Idan kuma baki yarda ba bissmillah”.

Sosai na saki baki da hanci da idanu dama gangar jiki duka ina kallonsa uwa wata saƙago. Yako wani kashe min ido ɗaya da shegen salonsa na manyan shegun

yara da suka gogu da sanin duniya. Ni sai ma abin ya bani kunya. Tuni na rissinar da kaina a cikin ƙirjinsa kawai dan banda abin cewa kuma. Shima kawai sai ya sake rungumeni tsaff. Tare da furta, “Shiyyasa nace miki you are tiger”.

“Ni ba damisa bace, kai ne dai Zaki da baya banbance na gida dana waje”.

Na faɗa cikin ƙunƙuni ina sake cusa kaina jikinsa hannayena duka biyu zagaye da shi. Ina jin alamun murmushinsa, nima sai na ɗan murmusa kaɗan. Dan a duk sanda yay murmushi wani irin nishaɗi nake ji a raina nima.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-one

41

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

.....Kamar ko yanda Hayatu yay alƙawari bayan sallar isha'i sai gasu niƙi-niƙi da kaya shi da Fahad da Hafizzullah. Lokacin shi ogan baima dawo massalaci ba. Da yake ina falo a lokacin sakamakon jini dana gani, dama dai ina ɗan jin alamunsa hakan tun safe. Alhamdullah tun maganin da yasa aka bani lokacin da yay kidnapping ɗin nan nawa bana azababben ciwon marar nan, sai kuma a wannan karon nafi samun sauƙi fiye da ko yaushe. Dan duk da na rage yin mai zafi idan lokaci yayi musamman randa zai zo nakanji ciwon. Amma yau alamarsa kawai naji sai ɗan karen ƙwaɗayi dake damuna, ashe zancen Ruƙayya gaskiyane data taɓa faɗa min idan kayi aure kakan daina duka. Kasancewar ta ƙofar baya ma'aikatan gidan ke shiga da kayayyakin yasa ban tashi a falon ba. Nayi mamakin yanda Fahad ya sake daya shigo. Dan zama sukai rashe-rashe suna bani labarin wuyar da suka ciwo. Niko ina musu sannu da kumshe dariya. A ɗan abinda na fahimta game da matsalar sa da ɗan uwansa a yanzun nan shine waje ɗaya ne kawai basa iya zama. Idan kuma har ɗaya na waje koda basa ganin juna suna jin zafin kansu. Amma idan babu ɗaya normal ne. Dan gashi dai Fahad kamar bashi ba anan duk da kuwa yasan a sashen wa yake. Munfi awa guda da shigowarsu dan har inata mamakin a ina ya tsaya shi tunda anyi salla dai tuni sai gashi ya shigo Hayatu biye da shi. Kamar amma Fahad allura zaram ya tashi tsaye. Tuni kuma murmushin dake fuskarsa ya ɓace ɓat. Hannun Hafizzullah ya kama da faɗin, “Dude lat's go”.

Kallonsa Hafizzullah yay zaiyi magana na girgiza masa kai. Sai kawai ya miƙe ɗin. Amma sai da ya gaida Maash da shima yay wani irin masifar kicin-kicin da fuska cikin girmamawa. Kai kawai ya ɗaga masa alamar amsawa, kafin ma ya fahimci a yanda ya amsa masan har Fahad ɗin ya ja hannun nasa sun fice. A hankali na sauke ajiyar zuciya, sai nima na miƙe jiki a sanyaye ina masa sannu da zuwa. Nima ɗin kai kawai ya jinjina min yana kaiwa cikin kujera. Ban damu ba na sake ma Hayatu sannu tare da godiya sannan na wuce ɗaki.

Banfi mintuna goma da shigar ba ina ƙoƙarin canja channel a tv sai gashi ya shigo. Kallo ɗaya na masa na ɗauke kaina. Shiko ma bana zaton ya kallan ɗin. Sai da ya gittani na ɗan bisa da kallon ƙasan ido. Mutum dai gashi nan sundum-sundum😎 kamar wani kurma. Kai ina zan iya ƙuntata kaina haka. Duk da nima sai naso dai nake magana amma nashi yayi yawa wlhy. Shifa a rana zaka ma iya lissafa furucin bakinsa tsaff.....

“Oya zo nan”.

Silent muryansa ya katse min tunani. Ɗagowa nai na kallesa. Ganinsa tsaye tacan bakin closet ya canja kaya yasa na miƙe ina ajiye remote ɗin hannuna. Koda na karasa garesan bai yi magana ba ya dai kama hannuna muka shige ciki. Babu wani bayani ya hau zame min kayan jikina. Koda na kallesa zanyi magana sai ya girgiza min kansa yana wani lumshe ido. A zuciyata na fassara abin nasa da (bansan surutu. Koba haka ɗan uwan naku ke faɗa ba Bliy😎?). Oho shi dai bai fasa abinda yake ba. Ga kunya kamar na nutse. A bazata matuƙar bazata naji kawai a cikin kunnena ya furta, “Time for Menstrual pain ba”. Da sauri na ɗago cikin waro idanun waje sai ya wani ɗage min gira. Cike da salon iya shege ya furta, “Duk zufan nan da nasha ashe ban farauto baby ba. Ba komai thanks you my ALLAH. Ina addu'a da roƙon samun little Ummu-Hidaya a next”.

Gaba ɗaya jina nai a rikice. Dan haka nai ƙoƙarin janye jikina a nasa, amma sai naci karo da kunyar da tafi ta farko dan babu kaya a jikina. Sai kawai na sake komawa na ƙanƙamesa. Yunƙurin murmushinsa kawai naji a ƙirji, amma ina da tabbacin a zahiri babu alamarsa a kan fuskarsa. Bai sake cewa komai ba shima sai ƙoƙarin saka min wasu kayan da ban san daga ina ya samosu ba. Wani shegen ƙyaƙyƙyawan abaya ne mai azabar ƙyau milk da kwalliyan golden a jikinsa. Ƙamshin ma da take kawai abin ɗaukar hankali ne. Kasa haƙuri nayi sai da na kallesa fuskata da murmushi na ce, “Woow Yaya ina ka samo a bayar nan ta haɗu wlhy”.

Banyi tunanin zai amsa min ma, amma sai kawai ya ɗan ranƙwafo ya lakace min hanci kaɗan, cikin raɗa-raɗa ya ce, “Ƙanwata BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING mana. Indai kina son Abayoyi yan yayi da fidda kwalliyar kece raini jeki can kawai My Tiger, har masu sari suna kawoma kaya tun daga ƙasar Egypt akan farashi mai sauƙi da kai ma zaka sayar ka samu taka riban 09032345899”.

“Woow, gaskiya madalla da Bilyn Abdull online shopping da ya sauƙaƙa mana wahal halun neman abayoyi muna a gidajenmu kwance. Jiba dai yanda rigar nan ke wani wal-wal na fito kamar jinin sarauniya Aminar zazzau.”

A hankali ya saki murmushi da kanne ido ɗaya ya ce, “Bilyn Abdull online shopping ai duniya ne”.

Jikinsa na faɗa na rungumesa. Na ce, “Tabbas na shaida hakan”.....

Koda muka kammala shiryawa tsaff hannunsa riƙe da nawa muka fito. Babu abinda kake ji sai mayataccen ƙamshin turarensa. Dan ni kam sam ba'a jin nawa. Da kansa ya kulle ƙofar ya saka mata security. Ko'ina na gidan akwai haske sai kace a turai. Kasancewar ba dare ne yay ba tako ina ma'aikatan da basa barcin wuri nata kai kawo. Sosai nake jin kunyar yanda ya riƙe hannuna ram kamar zan gudu masa. Suko duk wanda ya mana kallo ɗaya baya sakewa sai yay ƙasa da kansa yana gaishe mu kawai. Muna gab da isa parking space mukaci karo da Hajiya ƙarama

dake fitowa a mota. Da alama shigowarta gidan kenan dai itama. Yanda ta ke kallonmu kamar wata gunki ya sani ɗan risinawa na gaisheta. Lips ɗinta na rawa ta amsa min. Shiko gogan ko kallon inda take banga yayi ba muka gittata muka wuce. A gaban wata motar dake rufe da tempol muka isa. Sai ga TJ kuwa da ɗan gudinsa ya iso. Yaye tempol ɗin yay. Wata arniyar farar dunƙulalliyar mota da ban san yaya zan siffanta muku ƙyawunta ku gane ba. Gashi naci kai ban san sunayen motoci ba. (Su o'e yᵊar uwarku bata san mota ba fa😆) ta bayyana. Kasa daurewa nayi sai da nace, “Woow” a hankali ina sake damƙe hannunsa dake riƙe da nawa. TJ na gama yaye tempol ɗin yabar wajen, ɗan kallonsa nayi, dai-dai da ya ciro key ɗin motar ya ɗan ɗaga min shi sai tin fuskata. Murmushi na sakar masa har haƙwarana na bayyana. Dan na fahimci dai da kansa zai yi driving ɗin kenan abinda ban taɓa gani ba. Hannuna kuwa ya ja har gaban motar yana mai danna key ɗin tai yᵊar ƙara. Sai ko ga murafanta sun wani shiga ɗagewa sama kamar fukafukai. Tofa yau naga jalalar rayuwa. Mota dai dana sani buɗe mata murfi ake kamar ƙofar ɗaki. Amma wannan al'amari haka tab ɗin. Ina kallon yana murmushi, nasan kuma bai wuce yanda yaga na saki baki ba ina zuba ƙauyanci. Da kansa ya sakani a motar, sannan ya zagaya ɗaya side ɗin ya zauna. Wani abu ya danna a hankali murafan suka shiga komawa yanda suke. Wani irin ƙamshin motar da sanyin ac daya kunna suka fara ratsani. Juyowa yay ya kallan cikin wani irin shanye cat eyes ɗinsa.

“Are you like it?”.

Yanda yay maganar cikin motsa lips ɗinsa a wani kalar hankali yasa tsigar jikina tashi, nima a hankali idanun nawa a cikin nasa na furta, “Fiye ma da yanda kake tunani Yaya”.

“I'm not your Yaya, change this name for me. I no like it”.

Fuska na ɗan shagwaɓe kamar zan yi kuka nace, “Yaya Musaddiq ƙaninka, Aunty Falaq ƙanwarka. Hafizzullah ƙanwar ka. Hayatu ƙaninka, Fahad ƙaninaka, sai ni ce kaɗai za'a ware a dangi. To ALLAH ma nayi yaji da ga yau zan koma wajen Ummiena”. Na ɗauke kaina.

“Ai nasan bama zaki iya ba, yin nesa da ɗan santalelen mijin nan naki tab. Asibiti mafa matsawa kikai a sallameki dan ki dawo kusa da ni”.

Da wani masifar sauri na juyi na kallesa. Ya wani tsatstsareni da idanu hannayensa harɗe a ƙirjinsa, sai wani ƙara shanye idanun yake ƙasa-ƙasa. Kafin ma nace wani abu, a saman lips ya furta, “Ki rantse ba haka bane Kandala”.

“Ni ALLAH bance ba. Kuma ni ba Kandala ba, in ba haka ba ALLAH kaima Yaya to”.

Karan farko naga yayi murmushi mai wahalar gani akan fuskarsa. Dan haƙoransa har sai da suka bayyana. Ya dunguremin kai da faɗin, “Kema Yaya to”.

Dariya na ƙyalƙyale da ita. Shima sai ya wani shafa kansa yana mai ma motar key. Sosai mamaki ya kamani ganin har lokacin Hajiya ƙarama na tsaye a inda muka barta ɗazun idonta a kammu. Kaina na ɗauke abina kawai har lokacin fuskata da murmushi.

Yanda yake juya steering cike da gwaninta ya sani kasa haƙuri sai da na furta, “Dama ka iya mota amma kullum ake tuƙaka”.

Baice komai ba sai ɗan murmushi kawai ya cigaba da tuƙinsa. Nima sai nayi shiru kawai na sake maida hankalina a kallon gari. Dan yau itace rana ta farko da nake ganin birnin Lagos da ƙyau duk da ma dare ne. Tabbas Lagos ta cancanci zama cikin citys na duniya. Dan adai ta inda muke zaka ɗauka ma a turai kake ba Nigeria ɗinmu ba. Jinai na sake so da ƙaunar ƙasata sosai. Isowarmu bakin katafaren ruwan nan na Lagos da muke ta jin labari ya sa kaina sake susucewa. Duk da darene akwai mutane sosai anata harkokin arziƙi. Kai da ka gani kasan duk wanda ke'a wajen yaci ya tada kai. Yo wannan irin holewa haka ina talaka yaga lokacin yinta. Sosai mamaki ya kamani ganin mu anzo an taremu cikin tsaro da matuƙar girmamawa. Sannan maimakon wajen taron mutanen nan mu can ta gefe aka mana rakkiya mu kaɗai a wajen ƙwallin ƙwal. Sai dai akwai haske sosai da zaka iya ma yarda allurarka a cikin yashin nan ka ɗauki abinka. Sai ƙarar ruwa dake wani irin ambulowa na hanƙoro a gaɓa, sai kuma ya janye ya koma. Na zata nan kawai zamu tsaya mu kalla ruwan mu koma, sai kawai ga wani ɗan madaidaicin jirgi fari tass mai masifar ƙyau ko'a kallonsa ya iso gaɓar ruwan. A hankali ya juyo ya kallan ta re da motsa lips ɗinsa kaɗan ya ce, “Les't go”.

Idanu na ɗan waro waje da faɗin, “Cikin jirgin?”.

“Yerhhh”.

Ya bani amsa a taƙaice yana jan hannuna.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_

Typing□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-two

42

.....Tamkar wata shasha haka na koma wajen kallo har muka shige ciki. Jinai har numfashina na sama da ƙasa saboda haɗuwar cikin jirgin da kayan alatun da aka shirya masa. Zaune ya kai cikin lallausan wajen da aka shirya tamkar falo, tare da kamo hannuna a hankali ya jawoni saman cinyarsa ya zaunar. Ajiyar zuciya na sauke nima a hankali, tare da juyawa na kallesa. Sai kawai ya saka soft hannunsa cikin nawa ya ajiye min key ɗin motar nan. Hannun nawa na kalla na ɗago shima na kallesa. Ya wani irin kashe min ido ɗaya da ɗage gira sama.

Tashi tsigar jikina tayi, dan haka nai ƙasa da kaina ina jujjuya key ɗin, muryata na ɗan rawa na ce, “Key! Karfa na yarda”.

Sake rungumoni yayi jikinsa tare da ɗaura kansa a kan wuyana yana wani shinshinawa sannu-sannu har ya kai saman kunnena. A hankali ya kama kunnen da haƙori ya ɗan ciza. Jikina na ƙanƙame lips ɗina na rawa alamar son yin magana amma na kasa. Sai ƙoƙarin ɗaura hannuna da nai akan nashi da yake yawo a saman cikina. Raɗar da yake min akan kunnen ta sani ƙanƙame hannun nasa da masifar ƙarfin da ban san daga ina yazo ba.

“It's yours”.

Kasa magana nayi tsabar yanda yake neman haukata min jiki da salon sa. Sai kawai na saki hawayen da suka cika idona na, lips ɗina na rawa na ce, “Mota fa?”.

“Uhhmm!”.

Ya faɗa yana ƙara cusa hancinsa cikin wuyana. Kasa jurewa nayi, dan jikina ya fara rawa. Sai kawai na birkito na faɗa jikinsa na ƙanƙamesa kawai tsam-tsam ina sauke numfashi a gwame...

Wani irin shegen murmushin mugunta Maash ya sake yana sake turata a cikin jikinsa da ƙyau. Shi kaɗai yasan mi yake ji akan wannan yar ficilar yarinyar mai wayon tsiya....

😎Humm su Yayanmu fa to□Bara dai nayi ciluuu.

□□□□□

Sosai jikinta yay sauƙi a ɗan tsakanin nan, sai ma wata irin murjewa da ƙyawu da cikin ya ƙara mata. Ga haskenta ya sake fitowa bazaka taɓa cewa Halimen yʏan tumaki bace ba. Yawan kwaɗaita mata karatu da Aunty Zakiyya keyi ya fara jan hankalinta. Aiko Abba na zuwa yau da dare ta ce masa tana son komawa makaranta. Kallonta yake da mamaki, itako ta shagwaɓe masa fuska kamar zatai kuka. Dole ya saki murmushi da faɗin, “Haba Halimatussa'adiyya, karatu kuma? Keda ke fama da jikinki wane karatu”.

“Ni dai naji sauƙi, ina son komawa na samu ƙarin ilimin addini dana zamani kodan nasan ta yanda zan cigaba da bautama UBANGIJINA na kuma shiga duk inda nake so a duniya. Yanzu dan ALLAH ina daɗi kamarka ace matarka bata iya ko karanta sunanta ba balle ta rubuta. Dan ALLAH ka duba dai Dalin”.

Murmushin ya sake saki yana ƙumshe dariya, dan yasan idan yayita a waje to za'a samu matsala shi da ita. Saboda cikin nan fushi yake sakata sosai ga masifar tsiya. Gwaggo Gudidi dake saurarensu daga waje ce ta shigo, zama tayi itama ta saka baki akan maganar komawar Halimen makaranta. Dan in ta koma ɗin ko abinda zata zauna da Mom ta samu ai anci riba. Saboda ita kanta ta fahimci Halimen na buƙatar ilimin zamani sosai kodan zama da irin su Mom. Shiyyasa ma da Zakiyya na zugata bata ce musu komai ba. Cikin hikima duk tama Abba bayani sai ya fahimta...

Yin maganar nan da kwana baifi uku ba kuwa sai ga Abba da form ɗin wata makaranta. Suna boko da safe islamiyya da yamma. Sosai Halime ta shiga murna. Hakama Gwaggo Gudidi. Nan dai Abba ya cike mata Form ɗin ya maida, tare da ɗan yin duk abinda ya dace. Randa suka bukaci a kaita su mata interview ya zo ya ɗauketa ya kaita. Tsabar yanda ya matsu da son kasancewa da ita sai ya wuce da ita gida. To ita kanta dai tana buƙatar, dan haka ko musa masa batai ba. Sun samu Mom bata gidan, sai Aunta kawai da sabuwar mai aikin da Mom ta kawo. Haka Abba ya saka mai aikin ta gyara ma Halimen sashenta tsaff. Koda Gwaggo ta kirashi akan ta jisu shiru sai yace mata ai suna gida Halimen zata ɗan ɗakko wasu kaya ne. Har Gwaggo ta yarda, sai kuma zuwa can ta sake kira bayan tayi wani tunani tace Halimen tai zamanta kawai tunda ma ta samu sauƙi. Ba ƙaramin daɗi hakan yayima Abba ba kuwa. Aiko ba kunya ya ɗaga halime sama yana juyi da ita...

Mom bata san wainar da ake toyawa ba, suna can yawan leƙe-leƙensu da Ummanta. Sai dawowa tayi da yamma sosai ta samu part ɗin Halime da hasken fitila. Hankalinta ne yay masifar tashi, dan ta gama zagaye gari da labarin ai Abba ya saki Halime ya korata garinsu. Miye-miye zantuka gasu nan dai barkatai tako ina. Sai kuma ga Halimen ta dawo kamar an jehota daga sama. Shin yaya akai ne haka ta faru, ba malamin nan ya tabbar musu da anyi an gama ba. Haka dai taita ƙullawa da kwancewa ita kaɗai, gashi dare yayi balle ta fita. Ta kira wayar Ummanta bai shiga ba sai daga baya ta tuna bata da caji....

□★□□□★□

Cikin ƙosawa da zaman shirun da suke tun ɗazun Hajiya ƙarama ta sake kallon Yallaɓai ta gefen ido. Har yanzu dai yana a yanda yake zaune. Sosai takaici ya fara kamata. Ta rasa mi yake tunani haka. Shin maganganun data gaya masa akan abinda ya faru yau a gidan ne komi? Ko kuwa fitar su Awwab data gani yanzu da itama yasa ta kasa zaune ta kasa tsaye sai da ta fito a daren nan. Numfashi da ya furzar tare da ajiyar zuciya yasa ta kallesa da sauri. Sai taga shima ita yake kallo. Murmushin ya sakar mata dake bayyana ainahin wanene shi, dan duk wanda yaga murmushin yasan na baƙin mungunta ne. Dan haka cike da zumuɗi itama ta ce, “Yallaɓai ka samo mana wani abu ne?”.

Kai ya jinjina mata yana ƙara sakin murmushi. Sai kuma ya gyara zamansa da ɗaukar waya yay kira, shiru yay yana sauraren bayanin da akai masa da ga can. Sai da aka gama sannan yay ɣar gyaran murya cikin bada umarni ya furta, “Ina son video ɗinsu da hotuna daga yanzu har sanda zasu baro bakin ruwan.”

“An gama ranka ya daɗe”.

Katse wayar Baba prof yayi, tare da juyawa ya kalla Hajiya ƙarama data tsaresa da idanu. Kafin ma yay magana ta taresa da faɗin, “Amma yallaɓai mi kuma zamuyi da hotonsu ko video? In dama a club ne ko wani wajen daban sai muce munada alamar tambaya a kansu. Amma yanzu minene wani bakin ruwa”.

Ƙaramar dariya ya saki da faɗin, “Ai ke wani lokacin idan kina abu kamar mara wayo. Bari na baki a buɗe. Har yanzu bamu da matsayar sanin alaƙar Awwab da wannan yarinyar. Duk da dai a duk mai hankali zai iya bama alaƙar suna da abinda muketa ƙoƙarin ƙin yarda ko ɗauka saboda wasu dalilinmu. Idan na ɗauki kalmar yarinyar tayi aure, na haɗa da Awwab ya mata fyaɗe amma ko damuwar hakan babu a tare da shi duk da kasancewarsa mutum mai kiyayewa, a mahanga ta hankali mi zai iya baki?”.

Ɗan jimmm Hajiya ƙarama tayi na tunani, sai kuma kamar wadda aka tsikara ta zaburo tana mai waro idanunta gaba ɗaya waje ta ce, “Mun shiga uku ni Lawusa. Yallaɓai kodai yaron nan yaje ya binciko yarinyar ne dan ya aureta. Anya ba shine ke aurenta ba kuwa? Sai dai ta yaya zai yi aure bada saninku ba sai kace mahaukaci. Yo wama zai masa walicci? Sannan shi ba ɓoyayyen mutum bane, babu yanda za'ai yaje neman aure ba'a gane shi ɗin wanene ba? Kai bama wannan ba, Awwab bazai taɓa yin aure bada sanin ku ba tunda bawai wani abu kuka taɓa masa da zai ji a ransa zai yi hakan ba. Ko Jaga da yaso ɓata mana shirin an kawar da shi”.

“Humm Lawisa Kenan. Nima daga daren shekaran jiya zuwa yinin jiya da daren jiyan zuwa yau, duk nayi irin wannan lissafin naki. Har ina tilasta kaina ƙin gaskatawa dan bana jin akwai wata hujja da Awwab zai iya yin hakan. To amma dai yanzu ina da plan, shiyyasa ma nasa commondo ya samo min hotunan da video ɗin”.

Da mamaki ta ce, “Wane irin plan?”.

Wani makirin murmushi Baba prof ya saki da maida kansa ya jingina da kujeran. Kansa tsaye ya ce, “Ki jira zaki gani ai”.

“Amma nake ga kamar ya kamata ace na sani”.

“Zaki sani, amma ba yanzu ba. Give me just one day”.

“Okay ba laifi, ni bara na tashi na wuce. Kasan gidan namu yanzu baya rabo da labarai. Komi kenan zuwa safiya dai ina saurarenka. Dan dole na taƙaita zuwa gidan ka saboda kar a fara mun wata fassara kuma daban gaskiya. Daga suriki...”

“Hakan nada ƙyau. Idan ma ina son ganinki zaki dinga ganin address ɗin wajen haɗuwa”.

“Okay ba damuwa, na barka lafiya”. Ta faɗa cikin girmamawa har da ɗan rankwafawa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_*_ *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

43

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

.....Sosai nake kallonsa ina ƙara jujjya key ɗin motar, shi ko yana zaune zama irin na ƙasaita ya wani yi crossing ƙafafunsa, tare da folding hannayensa a ƙirji ya zuba min ido kawai shima. Idanun nawa na ɗan rissinar, tare da sake kallon key ɗin sannan cikin ƙarfin hali na ce, “Amma Yaya Awwab motar nan ta mun girma, duk da ban san mota ba, kuma zan iya maka rantsuwar yau na fara ganin irin wannan ɗin ma. Mizai hana ma dai ace yar ƙarama haka dai-dai ni”.

Shiru baida alamar cewa komai. Sai ma jingina kansa da yay da jikin kujerar ya wani lumshe idanu. Jinai gaba ɗaya na ƙagara yace wani abu, amma bawan ALLAHn nan baida alamar cewar har kusan mintuna goma. Sai da ya mula dan

kansa yana a yanda yake zaune batare daya tashi ba ko buɗe idonsa ya ce, “Samrh”.

Ya kirayi sunan nawa so soft. Nima sai na samu kaina da amsa masan a can ƙasan maƙoshi ina ɗan sauke ajiyar zuciya.

“Kin san wa kika aure kuwa?”.

Kaina na ɗan ɗago na kallesa. Kansa ya jinjina min a hankali tare da cigaba da faɗin, “Idan irin wannan motar kike so guda goma za'a kawo miki. Idan wadda ta fita kike buƙata ko kwana biyu bazasu wuce ba batare da an kawo miki ita ba. Ke ko zana hoton mota kikayi da hannunki, kika ce so kike a miki irinta da sunan ki ki zama ta farko kuma ta ƙarshe mai irinta kisa a ranki an gama kawai.”

Sosai na sauke ajiyar zuciya ina mai lumshe idanuna, da gudu hawayen da suka cika shi suka shiga rige-rigen sakkowa. Sake damƙe key ɗin nayi a cikin hannuna, kafin na miƙe a hankali har zuwa gabansa na durƙusa. Muryata na rawa na ce, “Yaya ban san taya zan fara maka godiya ba, bamma san taya zan musalta maka abinda nake ji a raina ba.....”

Ɗagowa yay a hankali tare da mun alamar zipping akan bakinsa. Gashi ya wani kalar zuba idanunsa a cikin nawa. Tashi tsigar jikina take yi saboda mayataccen kallon da yake min a cikin tsakkiyar idanun sosai nake jin tasirin su. ALLAH ya saka baiwa da tsantsar kwarjini a cikin idanun bawan ALLAHn nan. Kuma kamar yasan da wannan baiwar shiyyasa yake yanda yaso da idanun akan mutane. A hankali ya fara motsa lips ɗinsa ta yanda badan kallonsa nake ba, babu yanda za'ai na fahimci mima yake faɗa, dan sam babu sautin murya sai motsin lips ɗin kawai..

“A farin ciki kawai nake buƙatar ki kasance”. Ya ƙare maganar da salon kashe min ido ɗaya tare da wani kalar jan su shuuuu kamar zai lumshe, sai kuma ya miƙe abinsa. Cikin takun nan nasa dake tabbatar da shi a ingarma kuma jarumin namiji ya ƙarasa can ƙarshen jirgin ta inda zai iya kallon ruwa hannunsa riƙe da glass cup dake ɗauke da non alcoholic wine. Hannunsa ɗaya ya dafe ƙarfen jirgin da shi, ɗayan na riƙe da kofin yana kallon uba-uban ruwan da ya isa ka sake yarda cewar ALLAHn fa ALLAH ne, dan duk da dare ne yanda ruwan ke ƙara da ɗan walƙiya ta gefe gefen da fitilar jirgin ta haska shi ya isa ka ƙara godema UBANGIJI. Sai wani irin kaɗa gashinsa iskar keyi tana maidosa baya. A hankali na sauke ajiyar zuciya da ɗan kauda kaina a kallon nasa. Sai kuma na miƙe nima na nufesa. Duk da ina tsoron kallon ruwan haka kawai zuciyata ke ingizani kan na matsa kusa da shi. Duk da ina da tabbacin yaji motsin isowata wajen bai ko kallan ba. Nima sai ban damu ba, dan zuwa yanzu na fara fahimta da haddace halin kayana. Jikin ƙarfen na jingina. Sai dai na juyama ruwan baya ina facing cikin jirgin ne. Batare dana kallesa ba nima hannayena a ƙirji nayi shiru kawai ina kallon cikin jirgin daki-daki. Nafi minti biyu a wajen kafin ya ɗan juyo kaɗan ya kallan. Duk da naji kaifin idanunsa a kaina ban kallesan ba ni.

“Hummm!” ya faɗa yana mai ɗauke kansa tare da kai kofin lemon nan daya kasa shanyuwa bakinsa. Kaɗan ya sha ya sake janyewa. Duk ta gefen ido nake kallonsa ina mamakin baƙin halinsa. Kasa daurewa nayi, dan sai nake ji a raina kamar haushi yaji, dan haka cikin dakiya da marairaita na ce, “Yaya fushi kayi?”.

Nan ɗin ma kamar bazai tanka ba. Sai da ya mula dan kansa kafin a daƙilen nan nasa kamar wanda ya gaji da magana ya ce, “for what?”.

“Saboda nace mota tamun girma.”

Tsaye ya tashi sosai, sai kuma ya kamo hannuna ya maidoni gabansa sosai. Kallona yake sosai ta yanda har nake jin ni banzan iya kallonsa ba. Dan haka na kasa ɗagowa ina dai tsayen a gabansa kaina a ƙasa. Saukar hannunsa saman haɓata ya sani ɗan ɗagowa, muna haɗa idon na maida nawa na rissinar. Sake ɗago kan nawa yayi da kawo fuskarsa gab da tawan ya haɗe goshinmu waje ɗaya, kaɗan na so buɗe idanun nawa, sai dai da gudu na maida su na rufe saboda jin saukar mincili lips ɗinsa akan nawa. Sam ban san akwai abu a bakinsa ba, sai da naji ya fara juyemun lemon cikin bakina a hankali da wani shegen salo mai tada kan mutum. Ya Arrahaman, guy ɗin nan bala'i ne. Ni dai kodan irin wannan rayuwar baƙuwace yanzu gareni shiyyasa nake jin duk wannan oho. Abinda kawai na fahimta nima banda juriya, ja'irar kaina ce, in har yay knocking sai na buɗe masa ƙofar batare dama nasan mi nake ba. Maybe wasu su kalla hakan gazawa, sai dai ni a karan kaina nasan ba hakan bane. Ɓoyayyen sirrin dake a raina ne ke kasa cigaba da bizne kansa. Maash ya cancanci a soshi, sai dai kawai ka basar saboda tunanin bazaka samu ba. Ga marasa iya juriyar riƙewar ne ke kai masa tallar kansu. Tun ban maida hankali akan abinda yake yi ɗin ba har na fara maida masa murtani. Tsabar taɓara da tasirin da hakan ya masa sai kawai naji muku mutumin nan ya saki kofin hannunsa tsulum cikin ruwan. Ya wani ɗaukan camak. ALLAH ya rainani, yanda akoda yaushe yake mun ɗaukar amaryar nan. In sha ALLAHU sai na dage na ƙara ƙiba ko zanyi maganinsa (Sam-G fa na magana. Ashe dai ƙibar nan abin so ne. Mune fa ake yayi yanzu😉😂).

Cusa kaina nayi kawai a jikinsa. Dan wata kalar matsananciyar kunyarsa nake ji har tsakiyar brain. Ashe wannan wasa ne farin girki. Dan daga wannan ɗaukar kawai jina nayi a tsakiyar wani shegen lallausan abu, dole na ɗan buɗe idona sai naga ashe gadone a kuma cikin jirgin ne a wani ɗan ɗaki da akai matuƙar ƙawatawa da wasu irin fitilu da furanni masu azabar ƙamshi. Kai kai duk yanda zan musalta muku ba lallai ku gane ba. Kawai dai anyi babu ku kudai. Kusa rigima kawai kuma mazanku su kaiku wajen nan ku kashe kwarkwatar ido😝. (Kuji min mata da iyayi, anata Masara da hinkafa wake ta wani holewa a jirgi😏, bammu tabarma ma a tsakar gida aka kunna hitilar kwai ya ihemu cin soyayya😑. Yo ALLAH na tuba mu harma... Bara dai nayi hiru amma abar ziga mu ehe😣).

Da farko hankalina ya tashi musamman dana tuna karo biyu wahalar dana sha. Amma dana tuna halin da nake a ciki sai naji nutsuwa. A hakan ma dai ban tsallake

ba, dan na cuɗu matuƙa har sai da ya samu yanda yake so ko nace muka.... (😎 Zancen ya tsaya iya nan to😊).

Na jima ban yarda na ɗago koda wasa na kalla sashen da yake ba. Dan wata irin matsananciyar kunyarsa nake ji fiye da yanda kuke zato. Hummm kar kuga laifina, Ni kaɗai nasan karatun da aka ɗaura min a cikin wajen nan. Koda aka kawo abinci ma ya ce na tashi naje nayi wanka na ci, ƙi nayi, dan shi ya riga yayi wankansa. Sai ma sake shigewa cikin lallausan farin duvet ɗin nayi na nutse a katifar da ƙyau. Sai da yace idan na bari ya hauro sai na yabama aya zaƙinta sannan na tashi ina tuttura baki. Cikin shagwaɓa batare dana kallesa ba nace ya ban kayana to. Sai ya miƙamin wata shegiyar rigar baci fara, wadda da iya da babu duk ɗaya. Duk da kuwa a tsaho nasan zata iya kai fin har gwiwa. Kawai yanda take shara-shara ne abin zakkunya. Sauka nai jikina gaba ɗaya nannaɗe a duvet ɗin, ganin zan tafi a haka a daƙilen nan nasa na magana kamar dole ya ce, “Kima dawo ki ajiye musu duvet, in ba haka ba ke da su ne ni zan wuce ne na barki a wajensu”.

Kʻafa na fara bubbugawa a ƙasa ina kukan taɓara. Sai ya ɗauke kansa tamkar bai san inayi ba ya fara kai coffee ɗin da ya sa aka kawo masa baki. Nikam dai na gama shiga ɗari tara da cassa'in da tara, ni kam ina mutumin nan ke son kaini ne?. Ganin bashi da niyyar cewa komai dole na ajiye musu duvet ɗin na kwashi rigarsa da idona ya kai kai na saka sannan na wuce bayin ina murguɗa baki da jajjan rigar ƙasa dan rabin cinyoyina duk a waje. Haka kawai naji a raina yayi murmushi, aiko ina shigewa nace “Fitinanne kawai, shiyyasa yʻammata suka dameka”. (😎Kishi phone store).....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-four

.....Koda na shiga bayin naji wani irin daɗin ganin p&pad a ciki. Duk da nayi mamakin hakan sai kawai nai tunanin ko suna ajiyewa ne dama in case. (Ko kuma shine yasa aka ajiye miki ba) wani sashe na zuciyata ya ayyana min. Sai abin ya sake bani kunya. Mutumin nan ɗan duniya ne sai dai kawai a barsa. Nima bathrobe ɗin na saka na fito fara tas kamar tashi, ko da wasa ban yarda na kallesa ba, duk da shi bana raba ɗayan biyu kallon nawa yake dan kujerar dana zauna tana facing ɗinsa ne. Su kaɗaine kuma a wajen sai wannan gado. Mugun ƙwaɗayin da nake ji ya sani cin gasashen kifin da aka wani ma gashi na musamman sosai. Sai naji na samu nutsuwa. Duk wata samuwar kwaɗayina ta tafi. A karan farko na ɗan ɗago na kallesa. Ganin yanda hasken screen ɗin laptop ɗin da yake dubawa ya haske masa fuska ya sani shagala kallonsa. Tun inayi a sace har na tafi direct abuna na shagala sosai. Ko kaɗan banyi tunanin hankalinsa na'a wajena ba, dan yanda yay serious a daƙilar computer ɗin ko kaine zaka ɗauka baya tare da duniyar mutane, sai kawai a bazata naji cikin silent voice ɗin sa ya furta, “Kina buƙatar wani abu ne?”.

Kaina na kauda, kamar bazance da shi komai ba dan naji kunya. Sai kuma na fuske nima ƙasa-ƙasa na furta, “Ba zamuje gida ba?”.

Cak ya tsaya da abinda yake yi, sai kuma ya ɗan ɗago ya kallan. Rissinar da nawa idanun nayi ina wasa da yatsun hannuna. Shima sai ya ɗauke kansa ya cigaba da abinda yake yi. Sai da ya mula dan kansa a taƙaice ya furta, “Next tomorrow”.

Da sauri na ɗago tare da gwalalo idanu waje. Na ce, “Zamu tafi? Ummie fa?”. Ɗan dakatawa ya sake yi, sai kuma ya cigaba da aikinsa batare daya tanka min ba. (Tab ɗin, aiko bazan iya zama anan har jibi banga Ummie ba. Sai dai kai ka zauna) na ayyana a zuciyata ina miƙewa. Bayin na koma na saka rigar barcin nan daya bani sai na lulluɓo gyalena dana shiga da shi. Fitowa nai na haye gadon abina tare da jan bargo na shige ciki. Addu'ar barci nayi dan shi nake ji sosai, duk da wani gefe na zuciyata duk gana akan can gidan saboda Ummie, sai dai idan na tuna Mama nan ga Fahad sai naji sanyi a raina. A haka barci mai nauyi ya kwasheni ban san sanda ya baro latse-latsen nashi ba yazo ya kwanta....

□□□□

Idan ma tace abin duniya bai isheta ba a ɗan tsakanin nan wlhy tayi ƙarya. Tama rasa ina zata kama. Gaba ɗaya haushin Rubayya take ji, shiyaysa ma ta daina amsa mata waya a kwana biyun nan. Tunda ita ta bata shawarar da gashi nan ta rubza a ciki. Anya kuwa bazata tafi plan bi b ba. Shegen yaro sai jarabebben taurin kai. Ga wannan yɗar iskar yarinya sheɗaniya sun nuna mata hanya itama tana neman zame musu ƙalliƙalallah. Dolene ma ta ɗauki mataki akan yarinyar nan itama. Amma sai plan ɗin ta ya gama kankama. Shima Fahad tunda ya fara koyon tsagerancin ɗan uwan nasa zata gyara masa zama. Dole ne fa itace kaɗai zatai

mulkin Maash Mansion. Kuma dole Awwab ya auri Azizat ta hakane kawai zata cigaba da mallakar kowa na gidan. Koda wataran ALLAH ya bama Ummu-Hidaya lafiya bata isa jaa da ita ba tunda dai a yanzu Maash shine mai dukiyar.

Murmushi ta saki har haƙoranta na bayyana. Cike da izza ta furta, “Baba tunda ku bazaku iya komai ba kuna tsironsa, ni Nafisatu bint Adams zan ƙwatama kaina abinda ku kanku anan gaba sai naso ku samu. Dan ɗaya bayan ɗayanku sai na maida muku murtani wlhy. Musamman ma Mu'azz. Sai na tabbatar masa da ni suka haifama Awwab shi da Ummu-Hidaya. Badai ni ya ɗagama murya ba, hahahahaha sai ka koma ƙasan ƙafafuna kuwa muje zuwa”. Ta wani miƙe tana juyi kamar ƙaramar yarinya..

Ni sai ma abin ya bani dariya😂😝.

□□□□□

Washe gari kamar yanda Maash ya bama Hayatu umarni akan gyaran sashensa bisa shawarar Samraah sai ko gashi da companyn da zai yi aikin. Bayan sun shiga sun dudduba ko ina da gwadawa aka shiga fitar da komai da ba'a buƙata. Bedroom ɗin Maash ɗin ne kawai ba'a taɓa ba sai kitchen da akama gyara jiya. Aikin bai tsaya anan ba harda sashen Fahad shima. Sai da suka kammala kwashe komai aka fitar tsakar gida sannan suka fara aikin fenti da canja wasu abubuwan duk da kuwa babu abinda gidan yayi, amma abinka da masu kuɗi, a duk sanda za'ai sabon gyara ana ƙoƙarin ya tafi da irin wannan zamanin ne ko tsarin kayan da za'a canja ɗin. Mutanen gida basu san mike faruwa ba sai gani sukai kawai anan aiki. Yayinda ake maida kayan sashen Maash ɗin sashen su Mama Balki dan kayan sabbine ko shekara basuyi ba. Kawai dai anso ciresun ne saboda ba'a matsalar kuɗin canjawar. Wannan abu ya sake harzuƙa zuciyar Hajiya Mammah, harta gagara haƙuri sai da ta tsare Hayatu da masifa dan duk shekara biyu ko ɗaya da rabi ita ake bama kwangilar canja kayan gidan, duk da dai ta karɓi hakan ne da ƙarfin tsiya dan da Hayatun ne. Sai kuma abinda taso za'a sakama kowa iyakaci ta tambayi kalar da kake son kawai. Sai gashi wannan karon taga ana aikin kuma ko shekara batai da canja kayan ba. Abin ma takaicin banda nasu sashen. Komai Hayatu baice da ita ba, sai da yaga azabar tayi yawa ya sanar mata umarnin boss ne. Shi nashi kawai tsayawa kan masu aikin.

Sake tunzurata zancen yayi, take ta hau neman layina Maash. Sai dai switch off. Wani irin tuƙuƙi taji yana sake turnuƙeta. Ita a ganinta taya za'a hau canja kaya yanzu bayan ga biki na tahowa, dan tana nan akan bakanta yanda Baba yace nan

da wata ɗaya za'ai bikin Maash da Azizat babu fashi sai hakan ta tabbata. Shiyyasa ma zata ƙulla plan b domin masa ɗaurin goro shi da kowa na gidan. Fuuuu ta nufi sashen su Paah. Yana zaune dan yana kallon wani program da alama yau bazai fita office ba ta shigo. Kallonta kawai ya tsaya yi har sai da ta iso gabansa sannan ya ɗauke kansa tare da gaisheta a fisge. Dan wannan ɗabi'ar Tata ta shigama mutane ba sallama na ƙona masa zuciya. Ya tabbatar idan bata fasa ba wataran sai taga abinda zai dameta wlhy. Yanda yay mata ɗin yasa ranta sake ɓaci, a take ta balbalesa da masifa akan laifin Maash kamar wani ɗanta ba ƙani ba. Ƙanin ma fa sako bawai na can-can nesa ba. Banda ma ta raina masa wayo a yanzu duk wanda ya kalleta ta kallesa baza'a taɓa cewa ta girmesan ba saboda shi namiji ne. Amma bai sani ba ko wannan linda-lindar jikin nata ne ke kwasarta tana ganinta shirum kamar matar sarkin yarabawa. Karan farko da ya fara manna mata hauka har taci jarabarta ta tsire bai tanka mata ba. Sai Hajiya ƙarama ce data fito da shirin fita asibiti ta ke bata baki. Bata kulata ba, hakan kuma ba sabon abu bane ba. Dan tun tana ma amarya basa shiri, duk da kuwa da farko farkon auren babu wata matsala saboda Hajiya Mammah na murna amma Ummie kishiya, kasancewar a lokacin akoda yaushe cikin saka ran zata warke suke. Sai dai a dalilin wani abu da su suka san tsakaninsu ya saka su ƴar walle-walle. Duk da kuwa ita Hajiya ƙarama taƙi nuna akwai matsala kowa laifin Hajiya Mammah kawai take gani da tunanin itace tama Hajiya Ƙaramar koma minene.

Rai ɓace Paah ya tashi ya bar mata falon. Ai ko sai ta hayayyaƙo masa harda shan gabansa tana daka masa tsawa. Ai ko shima ya daka matan cikin matuƙar fusata da hargagin da bai taɓa koda kwatanta mata ba ya nunata da yatsa tare da faɗin, “Addah! Leave me alone!. Get out of my side kafin na nuna miki ainahin true color ɗina wlhy. Kin isheni! Kin isheni!!. Haba wai ƴaƴana sune kaɗai ƴaƴa a family ɗin nan da kullum dai sai ance sunyi-sunyi. Musamman Muhammad bashi da wani filin shaƙar iska mai daɗi a gidan nan. Kullum cikin wahalar nema da kai kawo yake na ganin ya ƙyautata rayuwarmu da ingantata amma bazamu masa addu'a ba mu gode masa sai zaman lissafa kurakuransa. Kuskuren ma daba kuskure ba dai Muhammad. Yanzu ki duba Fahad tunda ya iso gidan nan wlhy ko kallo ban ishesa ba. Yama nuna gaba ɗaya bai san dani a cikin gidan nan ba. Shekara nawa ban gansa ba, ko naje ƙasar da yake guduwa yake baya barin ma mu haɗu sam. Shi kansa Muhammad idan bai so ba sai ya shafe wata biyu ban gansa ba kuma yana cikin ƙasar koma cikin gidan. Miyyasa wai bazaku tausaya min bane ku barni da damuwata. Shin da halin da uwar ƴaƴana data zama sanadin rufin asirina da ku zan ji ko da fitinarki Addah?!!. Ke wane kalar iskanci ne yaranki basayi kin ma taɓa nuna kin san suna yi ɗin. Please! Mind your business and leave me alone!!!!”.

Ya wuce abinsa fuuu cikin bedroom. Ba Hajiya Mammah da Paah yayima ihun ba. Hatta da Hajiya ƙarama sumar tsaye tayi. Dan abune da bai taɓa kwatanta faruwa ba a gidan koda a mafarki. Mu'azz na ɗaga murya ma wani. Kai kai koda ƴan aiki bata taɓa ji ba. Shi mutum ne mai shiru-shiru, dan zata iya cewa ma rashin magana kamar a wajensa Awwab ya gado shi. Sannan shima wani lokacin akwai

miskilanci, dan in bai gadama ba sukan iya gaɓar sati biyar ita da shi wlhy bata ishesa koda kwallo ba. Sai dai ita ta gaji ta sauka. Amma jiba yau ya koma kamar wani mafaraucin zaki..

Ido suka haɗa da Hajiya Mammah data suma a tsayen itama. Sai kawai ta wani balla mata uwar harara tai gaba abinta.. sai kawai murmushi ya suɓucema Hajiya ƙaramar batare data shirya ba. Wayar dake hannunta ta kalla, sai kuma ta kwashe da dariya, tare da shiga WhatsApp ta turama Baba prof recoding ɗin da tayi na duk abinda ya faru. Tana turawa ta kashe wayar gaba ɗaya ta koma cikin ɗaki dan ga fasa fita aiki kuma. Sai taga ƙarshen wasan.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:Opay

BANK ACC NO:9060576116

ACC NAME:MUSAA ABDULLAHI SALEH

ATURA SHEDA ZUWA;09060576116

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09060576116

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-five

45

.....Koda kiran salla ya farkar da mu da asuba nayi mamaki. Sai daga baya na fahimci daga wayarsa ne ya saita hakan. Tashi yay ya shiga bayi. Bayan ya fito ya kabbara salla nima sai na shiga domin gyara jikina na kuma yo wanka. Sai dai ƙasan raina ina cikin damuwar kayan sakawa. Koda na fito sai da na gyara gadon sannan na zauna. Wayarsa na ɗauka na duba naga ko akwai app na Alkur'ani. Nayi sa'ar samu kuwa, dan haka nayi zaman yin karatu, shi kuma da alama azkar yake yi dan yana dai zaune a inda yay sallar idanunsa a lumshe ya jingina bayansa da kujerar wajen. Mun jima a hakan har sai da gari yay haske sosai ya miƙe, nima sai na ajiye wayar batare dana kallesa ba kaina a ƙasa na gaishesa.

“Kin tashi lafiya?”.

Ya amsa min a taƙaice. Numfashi na ɗan sauke a hankali ni ma nace masa, “Alhamdullah”. Fita yay, ni kuma na ɗan sauke ajiyar zuciya. Ina a wajen zaune babu jimawa sai gashi ya dawo riƙe da wata ƴar ƙaramar bag mai shegen ƙyau. Kusa da ni ya ajiye batare da yayi magana ba ya wuce bathroom. Da kallo kawai na bisa har sai da ya shiga na ɗauka jakar na buɗe. Abinda ko nayi tunanin ganin ne wato kaya. Har cikin raina naji sanyi, dan haka na miƙe a gurguje na shirya cikin doguwar rigan mai ƙyau sosai. Yana fitowa ɗaure da towel kallo ɗaya na masa na ɗauke kaina, har ya kammala shiryawa ban sake maimaitawa ba. Sai da yazo har inda nake ya kama hannuna sannan na ɗago na kallesa. Da ido yay min nunin na tashi, ban musa ba na miƙe, sai dai a raina ina mamakinsa. Gurin jiya muka fito, ganin da nai masa na yau sai naji ya sake ƙayatar da ni. Gamu a gaɓar ruwa yanzu kam al'amarin zabbirgewa da ƙayatarwa, sai dai bata inda muka baro bane nan ɗin

ma babu kowa shiru sai kukan tsuntsaye. Bamma san na saki murmushi ba. Ganin yana kallona nayi ƙoƙarin ɗauke kaina ina gimtse abina. Nima gwara ai na koya irin halin nashi Aita zaman kuramen kawai. Ƙayataccen breakfast ɗin da aka shirya mana mukai zaman ci. Koma nace naci, dan shikam ma tsakurar komai yake kamar abin dole. Na fahimci sam baya son abinci, ya dai fi ganewa kayan ƙwalam ɗin nan da maƙulashe...

Ana kiran wayarsa ya tashi a wajen, can ya koma ya tsaya. Ban tsaya jiransa ba na ƙarasa cin abincin na tashi. Ciki na koma ban jima ba na dawo. Na samu ya gama wayar, ma'aikatan jirgin ma na tattare kwanikan da mukaci abincin. Kallona naga yayi kamar mai nazari, sai kuma ya ɗauke kansa da maidawa kan wayarsa dage vibration dan shi sam baka jin ƙara a duk wayoyinsa.

“A ƙaraso da su”.

Kawai yace yana mai yanke wayar. Mamaki ne ya kamani, na kalla gabas da yamma kudu da arewa naga dai a tsakiyar jajeji muke sai ruwa. To ta'ina ma wani zai samu damar zuwa nan ya same mu. Bari dai naga ikon ALLAH. Aiko na gani, dan ba'a cika minti biyu ba sai ga ma'aikacin jirgin ya shigo bayansa da mutane guda uku. Ɗaya babban mutum ne mai cikar kamala da mutumtaka. Ni sai ma naga kamar nasan fuskar. Sai matashin saurayi da bazai wuce sa'an Hayat ba, shi kansa saurayin kamanninsa da Bahijja sosai ya mugun jan hankakina. Sai dai na cije kawai na kame kaina, sai Hayatu dake biye da su. Araina nace (bindin Maash kenan). Ganin Maash ɗin ya miƙe cike da girmamawa yana ma dattijon barka da zuwa da kiransa da Abbah yasa nima suna zama na gaishesa cikin girmamawa kaina a ƙasa. Sosai yake murmushi, kafin cikin jinjina kai ya ce, “Masha ALLAH, abu yayi ƙyau Muhammad Awwab. ALLAH kaine abin godiya, ALLAH ya ƙarama wannan aure albarka”.

A mamakina murmushi naga yayi yana ɗan rissinar da kai alamar jin nauyi, nace (tofa, dama akwai wanda Maash kejin kunya a duniya ashe). Gaisuwar da saurayin nan ya mun cike da girmamawa ta katse min tunani na. Na amsa masa shima ina ɗan murmushi. Muka kuma gaisa da Hayatu na tambayesa aunty Falaq yace tana lafiya.

“Samrh!”.

“Na'am”.

Na ɗago ina amsawa da ɗan kallonsa. Inda dattijon nan yake ya ɗan kalla, tare da sake maido idanunsa a kaina ya ce, “Wannan shine Malamina kuma kamar Abbana. Shiyya fara koyar da ni ilimin addini kamar yanda ya koyar da kakana mahaifin Ummie kenan da ALLAH yayma rasuwa tare da Baba. Shine kuma ya amsar min walliccin aurenki. Nasan dan da wahala ace baki san wannan fuskar ba. Dan Sheikh Muhammad bin Khalipha Al-Hussain ba Nigeria ba a Africa ma sananne ne”.

(Haba no wander nifa nace nasan fuskar nan) a zahiri kuma sai na jin jina kaina da sake rissinawa na ce, “Sannu da zuwa Abba. ALLAH ya ƙara lafiya da nisan kwana masu albarka”.

“Amin ya rabbi ɗiyata. ALLAH yay miki albarka. ALLAH kuma ya jiƙan mahaifinki Abdul-wahab da rahama. Mutumin kirki mai gaskiya da riƙon amana. Mai sadaukarwa. Ina fata da addu'ar ALLAH ya gadar da ƙyawawan halayensa ga ku zuri'arsa. Dan masu iya magana kance TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE. Nayima mahaifinki ƙyaƙyƙyawan sani gaskiya. Har takai ina jin kunyarku matsayin zuri'ar daya tafi ya bari da ya kasance bamu taɓa bibiya ba har sai a gaɓar da UBANGIJI ya zartar da ikonsa. Amma tabbas nasha yin hasashe a kanki a duk lokacin dana ganki a tv. Saboda iyalan gidana na bin program ɗin da kike gabatarwa. Tun ina faɗa da yawan kallon tashar har dai na nutsu nima naga abinda suke kallon a wata rana. Amfanin shirin da hikimar iya zance da ALLAH ya baki yaja hankalina matuƙa. Sai kuma a raina nake jin kamar na taɓa saninki amma a ina shine na manta. Har dai randa Muhammad ya kirani da bayani akan rikicin aurenki da hukuncin kawunki. Kasancewar yana faɗin min wadda yay hira da ita a Alheri tv yasa na gano kece. Abinda yay matuƙar sake ɗaukar hankalina kuma hoton da ya tura min na ɗan uwanki dake tsananin kama da mahaifinku, kema ashe jininsa nake gani a jikinki shiyyasa nake ganin kamar na sanki. Dan haka na buƙaci yazo ya sameni. Mun tattauna sosai akan abinda bamu tabbatar ba, a take nan ya saka aka masa bincike aka kuma tabbatar mana ke ɗin jinin Abdul-wahab ce. Madalla da ƙyaƙyƙyawan tsiron alkairi. ALLAH ya gafartama Abdul-wahab Gwarzo”.

Sosai nake kuka. Yayinda Malam ya cigaba da zabgama Baba addu'a har ma da kakan Maash ɗin. Maash na amsawa da Amin, dan Hayatu da saurayin nan suna can gefe sun bamu wuri. Nima dai ina amsawar sai dai kuka yaci ƙarfina. A hankali naji saukar hannunsa saman nawa kasancewar muna zaune ne a kusa da juna. Na kuma ɗan dafe kujera da hannun, ina sharar hawaye da ɗayan. Sosai ya runtse hannun cikin nashi tare da ɗan murzawa alamar lallashi. Sai kuma ya zato tissue a cikin kwalinsa dake saman Centre table ɗin kujerun wajen ya miƙa min. Ban musa masa ba na amsa. Hawayen na share, sai kuma ya miƙa min ruwa. Nan ɗin ma amsa nayi na sha kaɗan na ajiye. Sai da na ɗan samu nutsuwa kafin Malam ya cigaba da faɗin, “Samraah kinyi ƙoƙarin, ALLAH ya saka miki da alkairinsa. Mijinki yana min duk bayani akan kula da mahaifiyarsa. Tare da cigaban da ake samu yanzu sosai. Waɗan nan halayyar sune halayen mace ta gari. Sune irin halayen da kowane namiji zai so samu ga matarsa koda kuwa akwai wani special abu da yafi so ga mace. Ki cigaba da yanda kika fara kar ki canja kinji. Kema in sha ALLAHU ALLAH zai kula dake. Ba kuma zai taɓa taɓar dake a ƙarƙashin ƙafafuwan ƙasƙantattu ba masu bijirema gaskiya”.

“In sha ALLAHU Abba Nagode sosai. ALLAH ya ƙara rahama da jin ƙai a gareka.”.

“Amin ya rabbi ɗiyata, tare dake da zuri'armu baki ɗaya. Akwai magunguna da nazo da shi da ruwan addu'a duk suna a motarku. Idan kun koma gida sai a cigaba

da yimata amfani da su. Hatta kuma zaku iya sha da amfani da su ɗin ba komai bane, har a girki kina saka muku musamman ruwan addu'ar zaki iya abinci da shi. Sai kuma a ƙara dagewa da addu'a da sadaƙa. Kiyaye dokin ALLAH, kiyaye hakkokin mutane. Azkar, karatun Alkur'ani. In sha ALLAHU muna fatan nasara a wannan gaɓar. Sannan Bahijja ta sanar min dukkan abinda ya faru a ɗazun akan Fahad, shima kar ai wasa dan abinda ke jikinsa a yanzu yafi na ɗan uwansa ƙarfi sosai gaskiya, dolene zai fishi zafi da son ayima duk wacce za'ai. Jarabawa ce ALLAH ya bamu ikon cinye wa baki ɗaya".

Sosai nayi mamakin jin sunan Bahijja a bakinsa. Amma dai na daure na amsa da "Amin ya rabbi. ALLAH ya tabbatar Abba. In sha ALLAHU shima komai zai tafi dai-dai". Na faɗa fuskata cike da murmushi. Shima murmushin ya min tare da faɗin, "Kina mamakin nace Bahijja ko?".

Kaina dake a ƙasa na jinjina ina murmushi. Shima sai ya sake murmusawa. Tare da nuna saurayin da suke tare da Hayatu. "Wancan yarona ne shima. Sunansa Hameed. Yayane ga Bahijja mamansu ɗaya. Mijinki shine ya kawo Bahijja gidan nan domin yimana wani aiki, kuma Alhamdullah ana cin nasara. Sai dai itama ban sanar mata ke ɗin matar Yayan nasu bace ba."

Kasa daurewa nayi sai da na ɗago na kalla Maash da hankalinsa gaba ɗaya ke a kan wayarsa yana daƙila. Mamakin duniya ya kasheni, amma sai bance komai ba na sake maida hankalina kan malam da fuskarsa ke a ƙawance da Murmushi. Ya ce, "Karki damu, a hankali zaki fahimci komai. Dan gidan nan naku sai mijin naki ne ya iya musu ai. ALLAH dai ya shiryar camu".

"Amin" na amsa masa a hankali, ina sake mamakin mutumin nan. Tabbas na yarda shi ɗin yafi Aljani taƙadaranci kamar yanda Hayatu ya taɓa faɗa min...

Daga haka suka cigaba da tattaunawa da Maash, a tattaunawar tasu ne na fahimci shima Hameed ɗin an kawosa ne yin wani aiki a asibitin da Hajiya ƙarama ke aiki. Abin ya bani mamaki, sai dai ban iya saka musu baki ba tunda zancensu ne. Amma wai abu dana taɓa ji a asibitin nan sanda nake jiyya sai Sosai wannan zama ya jamu lokaci mai tsayi, dan sallar Azhar ce ta tashemu.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-six

46

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

.....Malam shine ya ja musu sallar azhar a cikin jirgin. Maash da malam ɗin sun sake sabon zama da ga shi sai malam ɗin daya jasu har zuwa la'asar, kai da kaga zaman zaka san abu mai muhimmanci suke tattaunawa, nan ma ya jagorancesu sallar la'asar sannan suka tafi. Ni lokacin ma ina ɗaki kwance ya kirani mukai sallama. Bayan tafiyarsu na zata muma zamu wuce sai naga wasa farin girki. Dan kuwa zama daram mai naƙuda ta samu katifa. Haka ina ji ina gani muka sake kwana a cikin jirgin nan dake ta faman shawagi kawai a cikin ruwa. Daren ranar ɗin ma dai

bai ƙyaleni ba nasha jagwalgwala har sai da nayi laushi a hannunsa. Kai jama'a mutum ina ma prioud ɗin ban tsira ba. Kamar yanda ya faɗa kuwa washe garin cikarmu kwana biyun gabanin magrib muka bar cikin jirgin. Sai kuma naji du kamar kar mu wuce. Dan rayuwa a cikin jirgin nan rayuwace mai tsayawa a zuciya da bazamu taɓa mantawa da ita ba da ga ni har shi. Ga wata shaƙuwa ta musamman data shiga tsakanina da shi. Duk da kuwa yana nan da halinsa da kuka sani na rashin son magana babu abinda ya canja. Wani lokacin ma idan na gaji da shirun nasa sai na ɗauka wayarsa naita game abina. Dan zuwa nai na dinga ɗakkosu a play store iri-iri. Wani lokacin ma ina a jikinsa zanta abina yana kallona. Kokuma yana aikinsa a computer ni kuma ina game ɗina ko kallon films tunda ga datan banza. Yo ta banza mana tunda shi koyaushe data ɗinsa a buɗe yake.

A motar da mukazo dai muka koma. Sai dai maimakon gida ma wani wajen yay dani. Ganin ƙaton companyn da muka zo ya sani tambayarsa ina ne nan. Bai bani amsa ba sai da ya gama shan ƙamshinsa ya ce, “Na Ummie ne. Shine ta fara ginawa”.

“Woow Masha ALLAH”. Na faɗa tare da cigaba da yaba haɗuwar companyn da girmansa. Har ciki muka shiga a office ɗin dana fahimci nashi ne. Dan babu kowa sai masu gadi a ciki da waje. Kujera ya nuna min shi kuma ya shiga bayi, koda ya fito ficewa yay da alama zaije massalaci. Ina jin ya kulleni ta baya. Ban damu ba na miƙe ina bin hotunan saman desk ɗinsa da kallo. Kusan biyar duk shi da Ummie ne da Paah da wani da aka rufema fuska da wani emoji kwalliya. Mamaki ya kamani na ɗan kware ɗaya sai naga fuskar Fahad. Murmushi kawai nayi tare da jin tausayinsu. Dan masifa ma ace a hoto ma basa son ganin juna. Duk inda fuskar Fahad take ya rufeta. Da ga shi sai Paah da Ummie sai wani ƙyaƙyƙyawan baturen dattijo dake tsananin kammani da Ummie da shi kansa Maash ɗin daya ɗan ɗebe wasu abubuwan da ƙyaƙyƙyawar mace baka. Tabbas wannan shine Ibrahim (Alonso) kenan, ita kuma macen Rabi'ah. A take naji ƙaunar dattijon ya shiga raina yayinda na shagala a kallon Rabi'ah, wlhy ji nake kamar na san fuskar nan. Addu'ar samun rahama na musu tare da mahaifina sannan na maida hotunan a yanda suke na koma na zauna inata son tuno a inda na san fuskar Mama Rabi'ah. Zamana baifi minti biyu ba ya dawo. Zama yay tare da ɗaukar wayarsa dake vibration tun ɗazun ya kai kunne.

“Office”.

Kawai ya faɗa yana mai yanke wayar. Ɗan juyowa yay ya kallan, sai kuma ya ɗauke kansa tare da nuna min wani ƙofa ya ce, “Jeki ciki”.

Kamar zanyi magana sai kuma na fasa. Mikewa nai na nufi inda ya nuna ɗin, a cikin raina ina mitar ALLAH ko'a jikin ƙofa ne sai na maƙe naga wanda zai shigo. Ai ko hakan nayi, ina maƙe a jikin ƙofar ina kallo da ido ɗaya ta ɗan wajen nan mai kamar camara. Saurayine matashi ya shigo, sai dai fuskarsa kusan a rufe take da hirami, sai gilashi daya rufe idanunsa tas ba'a iya ganin komai. Idan ka gansa saika

ɗauka baida gaskiya. Cike da girmamawa ya rissina ya gaishesa. Ina kallo ya amsa masa da alamun jinjina kai. Sai kuma ya nuna masa kujera. Zama yayi, tare da yaye hiramin ya cire gilashin. Ban sanshi ba, bamma taɓa ganinsa ba. Oho su suka sani wannan kuma. Ganin bazan iya jin abinda zasu faɗa ba na ɗan buɗe ƙofar kaɗan. Dai-dai nan ko saurayin ya miƙa masa wani abu kamar yana faɗin,

“Alhamdullahi Sir, naci nasarar ganin fuskar ɗaya daga cikin masu zuwa gidan da ɓoyayyar fuska. Sai kuma ita Hajiya Nafisa kwana biyun nan tana yawan zuwa gidan gaskiya. Guy ɗin nan mai suna Commondo da muka bibiya kwanaki shima kwana biyu nan yana zuwa akai-akai gidan. Sauran baƙin kuma da suka ɗan zazzo duk akwai sunayensu da fuskokinsu anan zaka gani. A jiya tattaunawasu da commondo ya bada damar a bibiyar masa brothers ɗin wata yarinya da suke zargin tana anan cikin Mansion ɗinka kamar mai something suna Samraah. Wadda naji Hajiya Nafisa ma tazo da batunta. Sai ita mai ɓoyayyar fuska data bayyana itama tazo da batunta. Kamar dai itace ya bada umarnin a kashe a asibiti ranar.”

Shiru Maash ɗin bai ce komai ba. Har kusan mintuna biyar kafin ya buɗe baki da ƙyar ya furta, “Ya akai ka fito kai yanzu?”.

“Baya gida tun around 11am ya fita. Amma dai akwai abinda yake ƙullawa gaskiya, sai dai bai faɗi komai ba akan shirin dan an sanar masa kun fita a gida tun shekaran jiya, lokacin suna tare da ita matar nan yace zai yi wani abu amma itama yaƙi sanar mata, amma a randa kuka fitan aka sanar masa. Jiya ma bai yini a gidan ba, yau ma gashi kusan hakan”.

“Kai mi kake tunanin yana shiryawa?”. Ya faɗa a daƙile.

“Eh gaskiya bazan ce ba kai tsaye. Amma dai ina hasashen koma minene tabbas zai iya shafarka. Dan haka ma na saka abu a jikin driver ɗinsa. Idan har an dace bai farga ba ya cire to zamu iya ganin wani abu koda ba duka ba ta nan. Sai dai gaskiya Sir ya kamata ka ƙara ninka tsaro a mansion. Dan shirin nan na musamman ne kuma daɗaɗɗen shiri kamar yanda Jaga ya faɗa. Sannan har yanzu kowa ba abin yarda bane a gidan nan. Ita kanta yarinyar da suke magana na fahimci a al'amarin nata akwai lauje cikin naɗi, musamman yanda naga al'amarinta na ɗaga musu hankali matuƙa, dan a nasu bincike sun gane tana da aure, amma sun gagara binciko ainahin mijin nata. Shiyyasa nake ga muma kamar ya kamata mu binciko ita ɗin wacece kafin su su binciko”.

“No wannan ba aikinka bane. Yanzu abinda nake so da kai shine. Ka tabbatar Hameed ya samu karɓuwa a wajensa hundred percent ta yanda samun aiki a asibitin bazai masa wahala ba. Akwai yarinya mai suna...” ya ɗan yi shiru alamar tunani. “Oh na manta. Ka kira Bahijja zata faɗa maka. Ina son kama oganka bayani ya kamata daga nan zuwa sati biyu. Kaima bazan sake ganinka ba sai nan da four to five weeks haka. Dan zan yi tafiya gobe in sha ALLAH”.

“Ba komai Sir, ALLAH ya kaimu. In sha ALLAHU kuma komai zai cigaba da tafiya fiye da yanda muke fata. Zan kuma sanarma oga saƙonka in sha ALLAHU. Komai da kake buƙata zaka gansa a flash ɗin nan ga kuma bayanai a file ɗin shima oga na bashi copy ɗin komai”.

Hannu naga ya bashi, sukai musabaha wancan ɗin ya fice. Kasa motsawa nayi a wajen. Dan tunda suka fara magana komai ke mun kai-kawo a zuciya..

“Idan kin gama laɓen ki fito”.

A bazata matuƙar bazata na ji saukar furucinsa tsakiyar kaina. Sosai na waro idanu waje. Tare da dafe ƙirji na kallesa. Yana zaune a yanda yake. (Kambu, yaya akai ya san ina laɓen? Ka jimun aljani) na ayyana a zuciyata. A zahiri kam sai na tunzura baki ina danne kunyar da naji na fito. Hankalinsa na akan file ɗin da aka kawo masa, dan haka na ɗan hararesa da murguɗa baki kaɗan. Har zan zauna gefe sai wata zuciyar ta ƙwaɓeni zama kusa da shi kodan naga mike a file ɗin. Sai dai me, ina zaman naci karo da hoton Hajiya ƙarama da shima ya ƙurama ido...

“What!?”.

Na faɗa cikin tsananin mamaki ina mai kai hannu na amshi hoton. Bai motsa ba, bai kuma ce dani komai ba. Sai da na ƙarema hoton kallo ciki da bayansa na sake tabbatar dai da ita ɗin ake maganar sannan na kallesa. Sosai naga jijiyoyin kansa sun wani irin tashi, yanayinda gaba ɗaya ya sauya. File ɗin na zame gaba ɗaya daga jikinsa nima nawa jikin na rawa na shiga dubawa daki-daki.

“Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un”. Na faɗa wani irin abu mai nauyi namun kai-kawo. “Tabbas biri yayi kama da mutum. Dama matar nan tana a cikin suspect ɗina a gidan, ashe kuwa. Amma Yaya abinda ban gane ba wane Baba prof ake magana? Wlhy kaina ya kulle gaba ɗaya, zuciyata bugawa take da ƙarfi”.

Shiru bashi da niyyar motsawa tsahon lokaci. Sai kuma ya ɗago a hankali ya kalleni. Sake firgita nayi zuciyar tawa na ƙara ƙarfin gudu da ganin idanunsa da sukai wani kalar masifar juyewa. Gaba ɗaya sun koma golden kai kace irin gawurtattun zakunan nan ne da suka addabi jeji tako wacce kusurwa. Ga wani irin tsananin fusata dake nuna ainahin stubborn Maash ɗin nan da bai san komai bace rashin mutunci. Rawar jikina ƙaruwa tayi, na shiga girgiza masa kaina hawaye na cika min ido. “Please Yaya ka daina kallona idanunka tsoro nake ji”. Shaaa hawayen da nake maƙalewar suka zubo. A hankali yay wani luuu da idanun, sai kuma ya miƙe murya a matuƙar shaƙe ya ce, “Les't go”.

Kasa tashin nayi dan har sai da yaje ƙofa kafin na miƙe jikina na rawa ina sharar hawaye. Har muka isa motar ma kukan nake, gaba ɗaya komai ya ƙwace mun. Sam bana son yarda Baba prof ɗin su ake nufi ya ce a kasheni. Idan fa har shine shima akwai lauje cikin naɗi a tattare da al'amarinsa kenan. Kai mun shiga uku wannan duniya to waya kamata mu YARDA da shi?. Waye zamu YARDA MASOYINMU ne na

gaskiya? Wai kenan da gaske anzo zamanin da zakama mutun ALKAIRI ya maida maka da SHARRI ke nan? Da gaske ne maganar malamin nan da yace wannan al'ummar na wannan gaɓar tamu sune MAFI SHARRIN AL'UMMA?. Mu zauna mu auna mana. Wlhy da wahala, matuƙar wahala a yanzu ka ƙyautatama mutum biyar ka samu ɗaya ƙwaƙwƙwara za dai maido maka da ALKAIRI. Mai ɗan sauƙi a ciki ne sanda ka masa zai nuna jin daɗin yimasan da kayi zuwa anjima ya manta. Wani ma kana bashi, bakinsa a washe a gabanka yana matsawa ya zageka da nuna ai dole ma kayi masan. Haba mutane why! Why! Why! Mukafi buƙatar yima WUTA tanadin kammu tun a duniya saɓanin ALJANNA. Why muka fi yarda da rayuwa da ruɓaɓɓiyar ZUCIYA saɓanin tsarkakakkiya?. Ni gaba ɗaya ma zuciyata ta cure waje ɗaya.....✍

To adai ji tsoron ALLAH kar a samu naman salla a manta dani.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-eight

48

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

*_WhatsApp_*

https://chat.whatsapp.com/LkRMFFQZakP55c7xK0QaMG

https://chat.whatsapp.com/D1Ki9jt2lNkKVetOWNuFN5

.....Shigowarsa gidan kenan yaci karo da commondo na jiransa. Duk da a gajiye yake tiɓis ga dare yayi hakan bai hanashi zaman saurarensa ba. Kamar ko yaushe cikin girmamawa commondo ya gaida shi. Tare da ɗorawa da bayaninsa.

“Boss bayani ne nazo da shi dan na kasa haƙurin haɗiyewa har na kammala binciken nan.”

Cikin ƙara nutsuwa Baba prof ya ce, “Tofa ina saurarenka miya faru?”.

“Akan ahalin yarinyar nan ne, brothers ɗinta biyu da nake faɗa maka bincike ya tabbatar da suna anan Lagos. Ɗaya makanike ne. Watanni bakwai da suka wuce sabon companyn Maash dake Kano sun ɗauke sa aiki.....”

“Whatttt!!! Maash Company?”

“Humm boss ai ban kai the end ba. A yanzu haka zancen da nake maka ma sun turashi karatu ƙasar ƙetare, ban dai gano ƙasar ba. Kuma jirginsa ta nan Lagos ya tashi ma. Abinda kawai bamu tabbatar ba shin da sanin Maash ɗin ne ko kuwa companyn ne tunda sun ɗauki yara kanikawa aiki da yawa bashi kaɗai ba. Shi kuma ɗayan yana cikin Lagos ɗin nan har yanzu, a ina yake shine ban sani ba. Amma dai inaga ka bincika a cikin Maash Mansion tunda har yarinyar na gidan to tabbas shima dole za'a sameshi a ciki”

Rasa ma abin cewa Baba prof yayi tsabar shock ɗin da yake a ciki. Da ƙyar ya iya motsa hannunsa ya ɗauki wayarsa domin tabbatarwa. Layin Hajiy jia Mammah ya kira. Bugu*_*_Typing_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page forty-nine

.....A mamakina murmushin Baba prof ɗin ya ƙara saki, sai kuma ya kai hannu saman kan Maash ɗin ya wani ɗan birkita sumar da yau bai ɗaure ba. Cike da son danne komai da fuskarsa ke son bayyanawa ya ce, “Ja'iri, dama sai wani abu ya faru nake zuwa da sassafe?. Kwana biyu ban zo naga daughter ɗina bace. Nayi busy da yawa shiyyasa yau dana samu chance nace bari na shigo”.

“Hummm”.

Kawai Maash ɗin yace.

Bakin Baba prof ɗin ne ya motsa kamar zai yi magana sai kuma yay shiru sakamakon shigowar Hajiya Mammah. Mu duka kallonta mukai banda gogan. Harara ta zuba mana ta ɗauke kanta. Niko sai na fuske nace mata “Mammah ina kwana”.

“Daban kwana ba zaki ganni yɗar tsirku. K! K! Ki kiyayeni ki fita idona. Wlhy idan kika bari na waiwayo kanki tofa kin shiga dubu bama uku ba. Idan su waɗan nan sihirinki ya cisu to ni bai cina. Dan nafi ƙarfin iyawarki nima shegiyar kaina ce nan da kike gani. Haba wace irin masiface wannan yarinya kin zame mana ƙadagangaren bakin tulu. Kiri-ƙiri kin mallake uwa da yɗayɗanta ke ga ƙwalluwar tantiriya. To wlhy yau sai kin bar gidan nan da ƙafafunki”.

“Ko kuma ke ki bar mata ba. Wai ke Mammah minene matsalarki? Masifa dai masifa dai kamar grandma. Ita mun samu ta mutu mun huta da nata jaraban ashe ta bar mana gadon ki. Can kin ishi mijinki ya koroki kin zo nan kin dame mu. Ina ruwanki, ba mallakewa ba tama haɗa wuta tayi farfesunmu ta cinye a cikinta ai dai yɗar uwarmu ce. To bari na baki labari wannan tana da matsayi mai girma a wajen mu. Dan har abada bazamu taɓa wulaƙanta zuri'ar Uncle Abdul-wahab ba. Ke kwanan nan ma zaku ganta matsayin matar aure a gidan nan kin ishe mu”. Ya wani ture plate ɗinsa ya bar wajen yana jan hannun Hafiz. Mu dukanmu da kallo muka bisa, a raina tausayinsa na kamani, dan na fahimci shi Fahad sona yake.

A mamakina sai naga gogan da tun da aka fara ihun yake ma latsa waya ya wani saki murmushi. Yayinda Hajiya Mammah ta kira sunan Fahad da ihu sosai. Amma tsabar wulaƙanci sai da yaje ƙofa ya juyo ya hararetа da faɗin, “Kin je kin kira Grandpa to shima sai dai ya sake share musu waje dan yasan muhimmanci Uncle Abdul-wahab idan ke baki sani ba. Amebo woman a canja hali.” ya mata gwalo ya fice.

Haukacewa ne kawai Hajiya Mammah batai ba saboda azabar masifa. Dan har sai da takai Paah da Uncle Abdullahi sun zo sashen, can sai ga Maman Malika da Hajiya ƙarama. Kuka sosai Hajiya Mammah keyi wai Fahad ya zageta ta uwa ta uba kuma nice na sakashi. Sannan Awwab na zaune baice masa komai ba. Ita wlhy yau bazata yarda ba sai ta bar gidan nan. Har kamar ita Fahad zai wulaƙanta saboda tana zaune a gidan uwarsa. Ta ma fahimci Paah ne ke sakasu musu rashin mutunci.

Rai a ɓace Paah ya ɗaga mata hannu da faɗin, “Point of correction Addah, nifa ki daina sakani a sabgarki da yaran nan yanzu. Dan kin fimu sanin mike tsakaninku. Bafa rami babu abinda zai kawo rami. Dan haka a can da kuka ƙulla ku warware kanku.”

“Ni kake gayama haka Mu'azz? Ni kake gayawa magana akan yayanka?”.

“An gaya miki Adda, wai yaya kike son nayi ne nikam. Dan ALLAH ku barni da abinda ya dameni. Nifa gaskiya nama fara gajiya da zaman kowa a gidan nan. Idan akwai matsala ne kowa ya koma inda ya fito mana. Ai nan ɗin su gidan mahaifiyarsu ne. Bamu da wani dalilin kuma zuwa mu tare a cikinsa. Koni da nake auren Ummu-Hidaya idan bata yarda na zauna mata gida ba bani da wani ƙarfin ikon yin hakan. Idan ance Awwab nada taurin kai kowa yasan Fahad a gidan nan na kowa ne. Amma gashi nan shima kuna neman kangarar min da shi bai shakkar kowa bai kunyar kowa a yanzu. Baba ya kamata kayi wani abu a wannan karon, idan ba hakaba magana ta ALLAH ka cigaba da shiru ana cigaba da aibanta min yara tofa ni da kaina zan ɗau mataki wlhy, dan ina sonsu fiye da komai, zan kuma tsaya na kare musu mutuncinsu kamar yanda kowa ke kare mutuncin nasa ɗansa. Da ɗin ma ina muku kawaici ne kawai amma na fahimci Adda bata san kawaici ba. Kai kuma a matsayinka na babba baka taɓa ganin laifinta balle ka tsawatar mata. Sai kace wai a barta da halinta ta gado Mama ne. Mama ai uwace a garemu zamu iya haƙuri da ita amma ita ɗin fa. To na gaji kowa ya koma inda ya fito kawai a barsu a gidan mahaifiyarsu su huta suma”. Yana gama faɗa ya fice fuuuu harda bugo ƙofa da masifar ƙarfi.

Yanda falon yay tsitt zai baka tabbacin kowa yayi sumar wucin gadi ne. Idan ka cire mai gayya da aiki da har yanzu yake faman latse-latsensa a waya daɗa duniya baya a wajen ne. Fuskokin kowa na fara bi da kallo. A mamakina Uncle Abdullahi murmushi yake yi. Hakama matarsa. Amma Hajiya Mammah, Hajiya ƙarama, baba prof ba'a magana. Hajiya Mammah dai hawaye take sharewa (gaskiya sai anyi shari'a, taya za'a saka gimbiya mandiya Hajiya Nafisatu bint Adams kuka

😂😝). Hajiya ƙarama kam kamar jikinta rawa yake, ga wata irin zufa ta jiƙeta kamar ba ac a falon. Haka ma Baba prof zufa kawai yake har jikin hularsa ta nuna shatin laima, kansa dai a ƙasa baka ganin idanunsa da fuskarsa da ƙyau. A hankali na zare jikina daga wajen na shige ɗakin Ummie, a laɓe na samu Mama da alama itama show ɗin take kallo. Murmushi ta sakar min dan haka nima na maida mata murtani. Sai tamun jinjina. Dariya abin ya bani na ce, “Kai Mama. Ai ɗanki ne abin jinjina. Jibafa yanda yake zaune kamar baima san ana komai ba ya bama banza ajiyar kowa. Ga kuma Auta ya tunzura ya gudu. Ashe shima haka yake?”.

Ƙaramar dariya tayi da faɗin, “Ai hakan shine dai-dai. Dama shi Alhaji Ƙarami haka yake musu ya manna musu hauka ya watsar da su musamman a tsakanin nan na rasa miyasa. Fahad kuwa ai da zafinsa ya dawo da alama addu'armu na karɓuwa. Alhaji Mu'azz bai taɓa birgeni a rayuwa irin yau ba. Bawan ALLAH ashe shima yana ƙaunar yayansa. Ni kam zargina ya fara barin kansa. Amma bakiga murmushin da Alhaji Abdullahi da Maman Malika suke ba”.

“Na gani sarai, amma abinda zai baki mamaki su kamar babu wata damuwar komai tare da su sai ma daɗi da suke ji”.

“Tabbas naga hakan. Amma mutum ne baka yarda da shi sai yazo ya maka kwaf ɗaya. Shi kansa Paah ɗin sai fa naga ƙuru-ƙuru baida laifi zan yarda”.

“Haka ne kuma gaskiya Mama, ALLAH dai ya daidaita Yaya da Fahad a fara aikin Maja”.

“Amin ya rabbi yar albarka. Ai kece ginshiƙin komai”

Hannu nasa na rufe fuskata ina murmushi.

Jin shiru alamar sun bar falon yasa na fita. Har yanzu gogan na wajen zaune. Tattare kayan na shigayi. Batare dana ce masa komai ba nima. Ina kitchen ina wanke kwanikan da muka ɓata ɗin sai gashi ya shigo. Ni tsoro ma naji da farko. Dan yazo gab dani ne ya tsaya. Koda na juyo har karo muka ci. Da ga ni har shi sai da kowa ya dafe inda ya bugu. A ɗan shagwaɓe na ce, “Yaya ALLAH ka bani tsoro. Mi kake so?”.

Cikin tsareni da idanun nan nasa ya nuna min lips ɗina. Sosai na waro nawa idanun, sai ya ɗaga min gira. Kunya ce ya kamani. Nai ƙoƙarin juyawa amma ya hana hakan. Mun ja kusan minti uku a wajen dan sai da yay yanda yaso sannan ya janye lips ɗin nasa daga nawa. Hakan ya sani faɗawa jikinsa na rungumesa dan ƙafafuna ma ji nake sun gagara ɗaukata. Nan ma munja kusan minti biyu kafin na ɗago a hankali. Ina ƙoƙarin juyawa ya dakatar dani. Muryarsa a shaƙe ya ce, “Inaga zamu wuce yanzu”.

Da mamaki na kallesa na ce, “Ina?”.

“Nema mana”.

Sosai naji gabana ya faɗi, ni har ina murna ya ɗan rage tafiye-tafiyen tsiyar tashi ashe ba haka bane ba. Kuma tsabar manni irin na mutumin nan ace zakai tafiya amma sai yanzu kake sanarma matarka. Jinai raina ya sosu. Amma sai na daure na danne na masa murmushi. Dan na fahimci nice zan canjasa, amma yanzu ban isa cewa ga yanda nake so ba tunda a haka ya tashi komai sai a hankali. Addu'a na shiga masa da fatan nasara. Yanda yake lumshe idanunsa nasan addu'ar ta masa daɗi. Sake rungumeni yay kusan na mintuna biyu kafin ya kamo hannuna muka fito. A falo muka samu Hayatu da Mama na magana. Dan haka nai ƙoƙarin zame hannuna a cikin nasan amma ya hana hakan. Gaba ɗaya naji kamar na nutse, da ƙyar na iya gaida Hayatu da tun kallo ɗaya da yay mana ya ɗauke kansa. Mama ko bama ta nuna taga mi muke ciki ba, sai addu'a take kwarara masa. A hankali ya amsa mata da amin tare da godiya. Sannan ya ɗora da faɗin, “Mama Falaq zata dawo gida ta haihu. Inaga sai a saka a gyara mata bedroom ɗin nan na kusa da Ummie. Sannan za'a kawo sabbin masu aiki nan sashen.”

Murmushi Mama tayi da satar kallon Hayatu da ya ɓata fuska yana kallon Maash ɗin. Kamar zai fasa ihu ya ce, “Yaya nace maka a camma fa babu wata matsala”.

Hararsa yayi da faɗin, “Na gama magana. Idan ta haihu ka ɗauketa kuma tafi bangon duniya, yanzu dai zata dawo gida ta haihu”.

Dariya abin nasu ya bani, nai ƙasa da kaina ina murmushi. Mama ma ina ganin tana murmushin, yayinda Hayatu ya cika yay fam.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty

.....Hannuna yaja muka shiga wajen Ummie, tana zaune shiru abinta ta zubama television da ake karatun Alkur'ani ido dan yanzu haka muke yini da kwana da karatu. Har gabanta mukaje muka durƙusa, ya kamo hannunta ya riƙe cikin nashi. Juyowa tayi ta kallemu, sai kuma ta kalla hannunsu ta kuma maida ta kalla nawa da nashi dake a haɗe. Ta jima tana kallon hannayen namu kafin ta ɗauke kanta. Yanda yake mata magana da roƙon ta masa addu'a sai da naji hawaye sun cika min ido. Haka dai muka fito batare da tace masan komai ba. Sai dai har cikin raina naji daɗi da banji yayi complain kansa na ciwo ba yau. Alhamdullahi hakan na nuna ALLAH na amsar addu'armu...

Har waje haka ya fita hannuna a cikin nashi. An gama shirya motoci harda ƙyamishashshiyar baturiyar nan. Ashe har lokacin Baba prof na gidan. Dan muna fitowa shima yana fitowa tare da Uncle Abdullahi da Hajiya Mammah. Ko kallon inda suke baiyi ba, sai ma jinginani da yay jikin motar ba kunya ya sunkuya ya sumbaci goshina da lips ɗina. Inaga tunda nake a rayuwata ban taɓa shiga cikin kunya irin yau ba. Tabbas na yarda mutumin nan bai san kunya ba. Compound ɗin da mutanene sosai. Masu aiki, su baba prof, su Hayatu kai jama'a ina cikin jalala ni dai.

“Hafiz zai biyomu zuwa jibi in sha ALLAHU. Dan na canja masa school. Barinsa a Nigeria yanzu akwai haɗari saboda za'a iya amfani da shi domin cin dundumiyar mu. Ta ko ina bana san ya cutu akan laifin da ba nasa ba. UBANGIJI ne bangona. Ke kuma kece Hope ɗina Samrh. Dan zan barki ne matsayin tarko. Ga Ummie nan, ga Fa.. ha ..d nan”. Ya fadi sunan a rarrabe da ƙyar. “Dan ALLAH motsin kowannensu na dinga sani, suma tarko ne. Duk abinda kike buƙata ga TJ nan ga Shu'aibu. Ki faɗama Fahad zai samesu. A yanzu tako ina a sashen nan akwai camara da securitys, da ɗin ma dan bana zama ne babu kowa shiyyasa. Yanzu ko nasan ina da Tiger a gida na ko?”.

Yanda ya ƙare maganar ne ya sa nayi dariya. Shima sai ya murmusa. Ba ƙaramin shock na gani a fuskokin wasu da murmushin nasa ba. Koda ya shiga mota da aka buɗe mosa sai naji kuma duk babu daɗi, kaina a ƙasa na sake jera masa addu'a. Lips ɗinsa ne kawai ke motsawa alamar Amin. Kafin a hankali yace, “Wuce kije ciki”. Banyi masa musu ba na juya na tafi, sai da naje zan shiga na juyo, a kan iska na rubuta masa (I miss you) na shige abina ina murmushi idanuna cike da ƙwalla. Tabbas na yarda sabo ake ma kuka ba mutuwa ba. Cak na tsaya ina kallon Ummie dake jikin window ɗin falon tana leƙen komai. Harga ALLAH sai da naji shock. Amma sai na dake na nufeta ina share hawayen nawa. A mamakina ina zuwa gab da ita ta buɗe min hannayenta alamar nazo gareta. Ai da gudu na ƙarasa na shige jikin nata ta rungumeni tsam. Tana jin motsin tahowar mutane ta sakan da sauri ta nufi ɗaki. Sagade nayi a wajen uwa wadda ta suma. Har sai da Mama Balki ta taɓani sannan na dawo hayyacina. Murmushi tamun da faɗin, “Ko dai nace ya dawo ɗiyata zata bisa”.

Kaina na duƙar ina murmushi yaƙe, sai kuma na nufi ɗakin Ummie da ɗan gudu. Tabbas naji kunyar maganarta, amma ba shine maƙasudin gudun nawa ba. So nake naje na sake tabbatar da abin al'ajabin dana gani. Shin Ummie ɗin ce ko kuma gizo tamun yanzun nan. Kwance na sameta tamkar mai barci, sai gaba ɗaya na sake jin kaina na neman juyewa. Koda mama Balki ta shigo ta tambayan barci take. Kaina kawai na iya ɗaga mata dan ban san abinda zance ɗin ba nikam. Da ga ƙarshe ma sai na fito a ɗakin na haura sama.....

□□□□□

Maimakon gida guesthouse ɗinsa ya wuce. Inda yakan daɗe baije ba saboda wasu dalilai. Gaba ɗaya ko gani bayayi da ƙyau. Yana shiga ciki Hajiya ƙarama ma na isowa. Dan biye take da shi a baya batare da ya sani ba. Koda ta shigo falon da farko shiru yay baima nuna yasan da zuwan nata ba, sai da taga shirun yayi yawa ta fara magana cikin muryarta dake nuna tsantsar tashin hankalinta.

“Tabbas yallaɓai muna a cikin tashin hankali. Gaba ɗaya a kwanakin nan abubuwa taɓarɓarewa suke neman fara yi. Irin wannan na guda shiyyasa tun samun lafiyar Ummu-Hidaya na farko nace maka muyi abinda ya dace, amma kaƙi fahimtata. Wlhy idan bamuyi wani yunƙuri ba a wannan gaɓar da wuri to fa lallai wankin hula na gab da kaimu dare. Dan zuciyata ta fara kaini ga zargin anya kuwa yaron nan Awwab baya biye da mu? Dan take takensa a wannan gaɓar sun fara bani tsoro. Sannan kaga wannan ifiritiwar yarinyar daya kawo ya ajiye wlhy shaiɗaniya ce. Kuma tabbas aurenta yayi, idan har abinda ya faru a farko ya zama kuskure to bayan faruwar hakan ya aureta dan ya binne abinda ya faru. Idan kuma zamuyi tunani na hankali ance tana da aure, dan ya mata fyaɗe a kuskure kuma zai aureta ne da aurenta? Duk yanda muke son sakama ranmu ba haka ba to tabbas fa tun farko Awwab shine mijin yarinyar nan. Shi kansa Mu'azz abunuwansa na kwanakin nan sun fara bikita min lissafi da har nake ganin dole akwai abinda ya sani, sai dai ban sani ba ko ya shafemu ko ba haka ba. Ka duba yanda yaron nan shima Fahad ya dawo a fetsare kai kai lallai muna buƙatar dawowa cikin hankalinmu, dan wlhy ɗayan biyu ne. Kodai aikin dake jikin kowa ya fara barinsa, ko kuma sun san abinda ke faruwa....”

Wani irin watsi da kayan saman Centre table ɗin Baba prof yayi, kafin cikin matsanancin tsawa ya ce, “Lawusa!! Get out of my house now!!”.

“Yallaɓ....”

“I say get out!!!!”.

Jitai gaba ɗaya illahirin jikinta na rawa. Dan idanun baba prof ɗin sun gama jirkicewa sun juye gaba ɗaya. Fuskarsa ta wani irin canja gaba ɗaya tsufansa ya

bayyana kansa. Tunda take da shi bata taɓa ganin matsanancin fushisa irin na yau ba. Tafiya take a gwagwgwame tana waigensa. Tana zuwa compound ta afka motarta ta tada. Ai a guje tabar gidan batare da ita kanta tasan mima take yi ba. Sai da tayi nesa da gidan ta samu waje tai parking. Ruwa ta fisga ta hau kwankwaɗa, sai da ta sha fin rabi kafin ta kifa kanta jikin steering tana sauke numfashi a harɗe. Mike damun tsohon nan ne? Shi indai yana a cikin fushi gaba ɗaya sai kiga ya juye mahaukaci. Tun fa da sauran ƙuruciyarsa haka yake da wannan halin mahaukatan. Ya kamata ace ya nutsu mu tattauna musan mafita amma haukar tashi na neman motsawa. Magana ta gaskiya idan naga zata ƙure bafa zan zauna ta kife da ni ba. Amma shike nan duk wahalar da nayi ta tsahon shekaru ta tafi a banza kenan. Kai impossible.

A zuciyarta take ta faman ƙullawa da kwancewar nan ita kaɗai. Tafi awa guda a haka kafin ta tada motar ta cigaba da tafiya. Ba gida ta nufa ba, kai tsaye cikin Agege ta nufa. Ta ɗan yi zurfi a anguwa sosai kafin ta samu waje tai parking. Wayarta ta ɗauka tayi kiran layin Commondo. Kamar bazai ɗauka ba sai tana gab da tsinkewa gashi ya ɗaga.

“Ina anguwarku, ta wajen wani shagon saloon ka sameni Please idan babu damuwa. Gashi zan ɗauka hoton wajen na tura maka ta WhatsApp”.

Banji mi akace da ita tacan ba. Ta dai yanke kiran bayan ta amsa da okay gashi zan tura. Mintuna kaɗan kuwa wani mai sanye da p-cap daya rufe fuskarsa sosai ya buɗe motar ya shigo. Ajiyar zuciya Hajiya ƙarama ta sauke, tare da kallonsa dai-dai yana cire p-cap ɗin. Shima kallonta yayi tare da kashe mata ido ɗaya cike da salon taƙadaranci ya ce, “Yau tsohuwar love ce ta tashi halan Lawy Baby”.

Hararsa ta ɗan yi ta ɗauke kai. Ya wani kwashe da dariyar mungunta tare da kaima kafaɗarta duka ya ce, “Ki gama zagaye-zayenki kema kin san bazaki taɓa ƙara samun jarumi kamar ni ba Lawusa. Dan tunda kike tare da ni kin taɓa kallon wata mace da suffar da kike kallonta yanzu. Jarumi kennan ba irin wannan lusarin mijin naki ba da ko ciki ya kasa baki kusan 18years. Kima shirya aikin nan na zama done no more mata a cikin rayuwar mu”.

“Kai dai ka sani”.

Ta faɗa cikin taɓe baki.

“Kema zaki sani ai. Ina my sweet daughter? Ina fata baki takura min yarinya ko? Dan duk duniya a yanzu banda kowa sai Arwa. Itace farin cikina itace nishaɗi na a itace mafarkina. Dan a yanzu duk wahalar da nake wajen ganin na tara dan ita ne. Ina son duk randa zata kalleni a matsayin mahaifi tasan cewa eh na cancanta.....”

“Hummm kaga ba wannan ya kawoni ba. Akwai matsala fa. Wawan tsohon nan nason raina mana hankali. Tana neman ƙwaɓewa amma ya zauna fushin banza da wofi a maimakon mafitar da zata ɓulle”.

Yanzu kam serious commando ya koma.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fivty one

51

.....A cije ya ce, “Miya faru kuma?”.

“Humm! Miye ma bai faru ba”.

Tsaff Hajiya ƙarama ta kwashe labarin komai ta bashi. Har korar da Baba prof ya mata yanzun nan. Ta ɗora da faɗin, “Nifa na fara tunanin tafiya plan b. Kawai mu kauda tsohon nan dan na gaji da harkar nan wlhy. Ina buƙatar zuwa na huta. Tuni da mun gama aikinmu amma tsohon nan sai raina mana hankali yake yana jammu a ƙasa, shi banda ma kansa a toshe yake a shekarun nan nasa an gama barbaɗa masa gishirin mutuwa uwar mi zaiyi da kuɗin nan? Amma yabi duk ya maidamu yaransa, garama kai dama yaronsa ne, amma Ni dan uwar ubansa ba aiki mukeyi kai da kai ba, nafa fara gajiya da raina min hankalin da yake dan yana ganina mace, wlhy na fisa bushewar zuciya”.

“Bake kaɗai bace kika gaji da aiki da wannan mutumin, ni kaina na fara gajiya. Dan na fahimci kansa kawai ya sani. Sannan kuma tunaninsa sam baya tafiya yanda ya kamata. Yanzu ko akan zancen yarinyar nan da ake tayi da kuma Maash na bashi ƙafa ne naga ko zaiyi tunani irin na masu hankali. Sai dai da alama giya ta cinye brain ɗinsa. Sam baya tunani irin na masu hankali. Maash fa ba shashasha bane ba, dan shi yana aiki ne da ƙwaƙwalwa da zuciya a lokaci ɗaya. Idan da bai san wanene shi ba tabbas da alama yanzu ya fara farga, dan idan har zamuyi lissafi irin na masu hankali a bayanin da kikamin yanzu akwai lauje cikin naɗi. In babu rami to miya kawo rami. Ya ɗauke mahaifiyarsa ya maida sashensa duk da azababben asirin da oga ya musu. Ƙaninsa ya dawo, a gaba ɗaya yanda yaron ya dawo kuma an tsarata ne. Mi hakan ke nufi”.

“Abinda naso ya fahimta kenan ai amma shi jaki ya wani kironi. Nifa yanzu wannan duk matsalarsa ne. Kawai mu tafi plan b. Dan bazamu cigaba da zama yana juyamu ba. Idan bai sani ba shine a tafin hannunmu ba mune a tafin hannunsa ba. Sannan muke juyashi, ba shike juya mu ba. Duk randa kuma yasan su waye mu wlhy sai zuciyarsa ta buga”.

Dariya sosai Commondo ya kece da ita, sai da yayi mai isarsa kafin ya kalleta yana wani rausayar da kai irin na manyan ƙwari. “Barsa wasa yake da wuta, amma bai san itace zata ƙona shi ba. Na yarda dake kaiwa mu tafi plan b”.

Idanu ta kashe masa tare da bashi hannu suka tafa. Sai kuma ta ce, “Kai tsaya! tsaya! Kayi maganar akwai alaƙa tsakanin yarinyar nan da Awwab. Kana nufin akwai abinda kake ɓoyema yallaɓai akan binciken daya sakaka akan ta ne? Danni fa na gama yarda da gasken gaske yarinyar nan Awwab ya aureta”.

Wani shegen murmushi Commando ya saki, a zuciyarsa yace (Shegiya tsuntsuwar kanari mai wayo. Ai kema bazaki sani ba dan da wannan makamin zan yaƙeki. Yanda zamu haɗu mu kauda yallaɓai haka nima zan kaudaki, kudai gama yimin wahalar, ɗiyata kuwa sai ta dawo hannuna) a fili kuwa sake faɗaɗa murmushin yayi har haƙoransa na bayyana ya ce, “Karki damu zaki sani idan ma akwai in babu sai nan gaba. Yanzu dai ina da uziri. Amma mu haɗu zuwa gobe kamar zai fi.”

(Matsiyaci tabbas akwai abinda kake ɓoyewa. Amma zanyi maganinka. Mudai gama da Yallaɓan kaine next. Dan ku dukanku sai na goge muku hadda. Badai Arwa ce mai gadonka ba, ka gama amsar kason ka kaima na kaudaka dan har abada yɗata bazata san kaine mahaifinta ba. Kamar yanda na sanarma iyayena ka jima da mutuwa da itama kanta har abada a haka zamu cigaba da tafiya) Hajiya ƙarama ce ke wannan zantuka a zuciyarsa. A zahiri kuwa sai ta saki murmushi da faɗin, “Yanda kace ai haka za'ayi Abban Arwa. Kadai tabbatar ka kirani da wuri dan muyi mu gama kasanshi baya tsayawa waje ɗaya. Dan yana ganin yanzu tana neman ƙwaɓewa wata hanyar zai nemo balle ga Awwab ɗin yayi tafiya”.

“Baki da matsala kema kin sanni ai. Na barki lafiya”. Ya ƙare maganar yana buɗe ƙofar ya fice abinsa. Yana gama fita ta dallama bayansa harara tare da taɓe baki. Mamaki ma take yanda akai ta auri guy ɗin nan. Babu yanda Ummu-Hidaya bata bata shawara ba amma a lokacin ta dage akan itafa taga miji. Haka tayi zaman shekaru kusan biyu da shi suka haifi Arwa. Arwa nada shekara ɗaya aka kamashi akan laifin kisan kai. Prison aka kaisa ɗaurin rai da rai. Hakan yasa kawai ta yanke hukunci da tsarama iyayenta da duk danginta cewar yayi haɗarin mota ya mutu dan ba'anan Lagos aka kama shi ba a arewa ne. Kowa ya yarda da ita dan yanda ta tsara komai dole ne ma a yardan, balle ita ba cikakkiyar bahausa bace tana da yare. Anyi zaman makoki da komai da akema mamaci tayi basajar yin takaba. Bayan nan da shekara ɗaya da wasu wattani sannan Arwa nada kusan shekara uku ta auri Alhaji El-Mu'azz, kusan shekara huɗu da aurensu kwatsam sai ga Commondo ya

dawo, ba kuma kowane ya fiddosa ba sai Baba prof.. fitowar commondo taso zame mata matsala, dan ya ta mata barazana akan indai bata bar Paah ba sai ya tona mata asiri ya kuma halaka ta. Barazanar nan yasa ya dinga cin kuɗi a hannunta na hauka, har sai da taga abin ya tasarma gurguntata sannan ta zauna ta sanar masa planning ɗinta na auren El-Mu'azz. Tun daga lokacin suka shirya sabon plan akan yallaɓai kasancewar shi commondo yaron yallaɓai ne na ammana kusan ma yana ɗaya a cikin waɗanda suka ƙara kangarar da shi a sanda ya fara rashin ji. Dan haka ɗan amana ne na Baba prof matuƙa shiyyasa suke ganin zasu kadashi cikin sauƙi. A mafi yawan lokuta idan ya ƙulla sukan warware masa batare daya sani ba. Hakama Hajiya ƙarama idan ta ƙulla commondo na warware mata batare data sani ba. Shima kuma commondo ɗin Hajiya ƙaramar kan warware masa. Haka dai suke wannan rayuwa tacin amanar juna amma a zahiri su amintattun juna ne....

□□□□□

Ranta a ɓace yake har ƙololuwar zuciya. Ta kuma gama yankema kanta koyama Fahad da yarinyar nan dama Awwab ɗin hankali. Hatta da ɗan uwanta bazata ƙyale ba. Waya ta ɗauka tai kiran Auta. Kamar itace ta mata laifin cikin masifa ta zayyane mata komai. Mashi'a sam bata da son fitina. Sai kawai ta shiga bata haƙuri da tabbatar mata cewar tana nan tafe in sha ALLAHU. A satin nan zata shigo Nigeria dan sutukarta ma babu lafiya. Jin hakan ya ɗan sakama Hajiya Mammah nutsuwa. Amma duk da hakan sai da tai kiran Rubayya da rabon da suyi waya harta manta. Da farko Rubayya masifa ta balbaleta da shi. Sai da itama Hajiya Mammah ɗin ta hayayyaƙo mata sannan suka koma dai-dai. Amma duk da hakan ita Rubayya tace bazata zo Maash Mansion ba sai dai ita taje gida ta sameta. Da yake itace ke so kuma a ƙage take ko gardama batai mata ba tace tana jirata gata nan zuwa.

Hakan kuwa akai, ta tashi tai shiri cikin shiga ta alfarma da fariyya data saba ta fita drivern ta ya jata suka wuce gidan aminiyar tata....

To ALLAH yasa a ƙulla alkairi ƙawar o'e□😮.

□□□□□

Na jima a kwance ina ƙullawa da kwancewa akan rayuwa da kwamacalar gidan nan, tare da abinda na gani game da Ummie. Sai kewar mijina data addaban, dan kona faɗa kona ɓoye haka dai al'amarin yake ina jin kewarsa matuƙa. Hirarsa ta jiya

da mutumin nan a office ce ta sake dawo min. Tuna abinda ya bashi flash da file yasa na miƙe na fito. Ɗakinsa na shiga, komai tsaff kamar yanda na gyarashi a ɗazun. Bincike na fara a closet ɗinsa dan tabbas ina son sanin mike a cikin flash ɗin nan. Duk inda nai hasashen zai iya ɓoyesa ban ganshi ba, sai a ƙarshe a banza na samosa ata inda ma mutum bazai taɓa tunanin an ajiye ba. Ganin harda file ɗin yasa na yarda shine. Iya flash ɗin kawai na ɗauka, dan nafi damuwa da son ganin abinda ke'a cikinsa. Sai dai yanzu damuwar a ina zan samu waya ko laptop na kallonsa? Badan babu wayoyi a gidan ba, sai don komai na son sirri ai a rayuwa. Musamman ma wannan shima bazai so ace na saka a wayar wani na kalla ɗin ba. Ban samu makamar kamawa ba. Dan haka na maidashi na ajiye a wajen na fito akan sai na samu mafita. Ƙasa na sauka domin nema mana abincin lunch, amma sai da na leƙa Ummie. Na samu Mama na kwance mata kai sai kawai na fito nima na shiga kitchen ɗin. Ban jima da farawa ba sai ga Fahad da Hafiz. Nan fa sukai zaman tayani munayi muna hira. Ni harma mamakin shaƙuwar Hafiz ɗin da Fahad nakeyi. Sai ka rantse sun san juna tuntuni. Muna kammala abincin salla muka nema, daga nan kowa yayo wanka muka fito.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-two

52

.....Bayan mun kammala lunch su Fahad suka tafi ɗakko Aunty Falaq. Basu wani jimaba kuwa sai gasu. Matuƙar farin ciki duk muka tsinta kammu. Yanda naga Falaq ta rungume Ummie tana kuka da yanda Ummien keta faman shafa kanta da cikinta yasa na sake shiga ƙaulani. Tabbas akwai shaƙuwa a tsakaninsu daka gani, amma duk mai hankali zai iya sakama yanayin Ummien alamar tambaya. Daga baya kuma da taga kamar zamu farga sai ta canja yanayi tama kwanta. Dole muka dawo falo aka buɗe babin sabon hira, salla kawai ke tada mu. Kamar wasa da dare sai ga TJ da saƙo wai inji boss. Ina buɗewa sai ga waya, harda sim card a ciki da cajinta da komai. Nayi farin ciki sosai kowa kuma ya tayani har Mama.

Samun wayar nan ya matuƙar sakani a farin ciki. Dan ji nai kamar na taka rawa. A falon na barsu nacema aunty Falaq zanje nayo shirin barci nazo a ɗakinta zan kwana. Kai tsaye ɗakinsa na wuce na ɗakko flash ɗin nan. Ɗakina na koma jikina har rawa yake. Kamar mai tsoron a kamata sai da na kulle har windows bayan ƙofa sannan na haye gado na saka flash ɗin jikin wayar.....

□□□□

Karan farko a rayuwarsa da tun cuɗewar abubuwa ya zauna yin nazari. Sosai abubuwan dake faruwa a gidan ke dawo masa dalla-dalla. Tabbas lokaci yayi da zai gyara mu'amalarsa da yʻayʻansa. Ya kuma tsaya tsayin daka wajen ganin lafiyar matarsa rufin asirinsa. Baya ganin laifin Awwab da Fahad, dan suna da hujjojin da zasu juya masa baya a rayuwa. Suna son mahaifiyarsu, babu kuma wani ɗa na kwarai da za'a wofantarwa da mahaifiya ya iya kawaici koda kuwa mahaifinsa ne. Tun suna masa alkunya da tunatar da shi muhimmanci mahaifiyarsu a garesa har sun daina sun wofantar da shi kawai. Dan gara-gara ma Muhammad na ɗan rangwanta masa sai idan ta ƙurane yake magana. Amma Fahad ko kallo bai siheshi ba. Yanzu haka tunda ya dawo ko hangosa yay sai ya canja hanya. Jiya ne ma data ƙure suka haɗu babu yanda zai yi ya ce masa ina yini. Bai ko jira ya amsa ba yayi wucewarsa...

Shigowar kira ya katse masa tunaninsa. Kamar zai share sai kuma dai ya kalla wayar. Ganin Baba ya sashi sauke ajiyar zuciya. Ɗagawa yay cike da girmamawa ya gaishesa duk da kuwa bai jima da barin gidan ba. Baba prof kam dako amsawa baiyi ba kai tsaye yace yazo ya samesa a gida yanzu nan. Ya amsa masa nan ma da girmamawa. Bai kuma ɓata lokaci ba ya shirya ya fita amsa kiran mahaifin nashi...

Kusan a tare suka shigo gidan, har shi Paah ɗin ma yayi mamaki dan da'alama tunda Baban yabar Maash Mansion sai yanzu ne yake dawowa gidan. Sai da ya dakata Baban ya fara shiga ciki sannan shi yabi bayansa. A falo ya samesa, duk da basu jima da rabuwa ba ya sake gaishesa yana mamakin ganin yanda duk fuskar mahaifin nasu ta birkice. Daga ƙarshe ma kasa haƙurin yayi sai da ya tambaya.

“Baba kana lafiya kuwa?”.

Murmushin yaƙe Baba prof ya ɗan yi, sai kuma ya jinjina ma Paah ɗin kai cikin furzar da numfashi ya ce, “Idan nace da kai babu komai Mu'azz na maka ƙarya.”

Cikin tashin hankali paah ya ce, “To baba miya faru?”.

“Ba daga ni bane Mu'azz daga kune. Al'amarinku ya fara tayar min da hankali musamman kai da yʻar uwarka. Sai kuma Awwab. Yanzu kuna ganin a matsayina na mahaifin ku da mahaifiyarku ta tafi ta barni da ku kun min adalci kenan ku dinga cima kan ku mutunci?. Yanzu har kun kai girman da zaku dinga gorantama kanku akan yʻayʻanku. In ce kamata yay ni da ku mu nutsu mu fuskanci abinda Awwab ke ɓoye mana dangane da yarinyar nan. Ko kuna ganin zancen fyaɗen nan ba komai bane....”

“Baba kayi haƙuri bana katseka bane. Amma bana tunanin Muhammad zai aikata wannan mummunan aikin da gangan. Mu zauna mu auna maganganun Addah da abinda ya faɗa mata ranar. Dole akwai abinda ya kamata musani.”

“Humm banƙi ta taka ba, amma dai ni da kai duk munsan wacece Nafisa ko. Tunda mun san ita fitina bata mata wahala mizai hana mu mata uziri. Ƙaramin abu kaɗan daga aikinta ta maida shi babba.”

“To amma Baba su kuma sai a dinga musu adalci ai. Bai kamata ace muna ƙara musu zafi ba a rayuwarsu. Sun rasa mahaifiyarsu tun suna ƙanana. Duk da bawai ta bar duniya bane amma banbancin kaɗan ne. Ni kuma a matsayina na mahaifi son zuciya ya hanani fuskantar su, na kasa rungumarsu na zame musu madadin uwa na kuma amsa sunan uba. Birinƙyaɗuwata kawai nake yi kuma a matsayinku na iyayena da ita dake matsayin yaya a gareni kun kasa nuna min kuskurena. Badan ALLAH ya kiyaye yaran nan ba wlhy tuni sun iya faɗawa criminals rayuwa. Dan kaine ma mai ɗan jan Muhammad a jiki da, sannan ya samu tattalin Abie kafin yabar duniya. Amma Fahad sam bai samu gatan nan ba. Baba mufa duba al'amarin nan da mahangar adalci.”

Kai kawai Baba prof ke jinjinawa kamar tsohon ƙadangare. Sai da Paah yay shiru kafin yaja gwauron numfashi da faɗin, “Shike nan na yarda duk munyi wannan kuskuren. Sai muyi fatan haɗuwa mu gyara mu duka a yanzu. Amma ita wannan yarinyar da Fahad yace ɗiyar Sarkin mota ce ita da ɗan uwanta kai dama kasan da hakan?”.

“Wlhy sam ban sani ba sai yanzu nima daya faɗa ɗin na sani. Amma nakega ai hakan ba komai bane ba. Dan Abdul-wahab ya cancanci kowane irin ƙyautatawar mu. Ka kuma san shaƙuwar dake tsakanin Abdul-wahab da Muhammad zai iya yin komai domin ganin ya binciko sauran zuri'arsa. Tunda mu bamuyi hakan ba. Da kuma Ummu-Hidaya na lafiya na tabbatar da tuni tayi hakan. Shiyyasa ni sam ban wani yi mamakin hakan ba sai ma daɗi da naji dan sun tabbatar da su yayan halak ne da basa manta alkairi”.

“Hakane”.

Baba Prof ya faɗa cikin ɗacin rai. Kafin ya nisa da cigaba da faɗin, “Hakan da Awwab yayi na jawo yaran jiki abin a jinina masa ne kam. To amma batun maganar fyaɗen da ake zargin ya mata kuma fa?”.

“Wannan batun Baba yana buƙatar bincike. Kuma shine maƙasudin zargina akan akwai abinda ita Adda ta sani akan al'amarin. Ya kamata kuma ka binciketa, tanan ne kawai zamu iya kamo bakin zaren.”

Nanma kai Baba prof ɗin ya jinjina. Yana dai ta danne zuciyarsa. Sai can yace, “Amma baka tunanin aurenta Awwab yayi?”.

“Aure fa Baba? Yayi aure shi Muhammad ɗin batare da mun sani ba? To waye zai masa walicci? Minene kuma dalilin da zai sa ya aikata hakan? Tunda yasan mu dukanmmu burinmu shine yayi auren?”.

“Nima irin waɗan nan tambayoyin naka sune a raina Mu'azz. Amma tabbas mu zauna muyi tunani irin na masu hankali. Idan har mun tabbatar Awwab zai iya nemo zuri'ar Sarkin mota dan ƙyautatawa taya zai haikema yarinya batare da dalili ba. Gashi nan yin hakan ya zame masa matsala, ya kuma zame mana muma ahalinsa. Duba nan ka gani, na tabbatar zuwa gobe wannan labarin shine zai zama latest”.

Jikin paah har rawa yake wajen amsar magazine ɗin da Baba prof ɗin ke bashi. A shafin farko yaci karo da abinda ya nema rikito masa zuciya waje. A take rawar jikinsa ta ƙara ƙarfi. Idanunsa suka kaɗa jazur. Muryarsa na rawa da yatsarsa dake nuna abinda Mujallar ta rubuta da kuma hoton Maash da yarinyar (Samraah) ya ce, “Bab....ba ya akai wannan maganar ta fita?”.

“Taya zan sani Mu'azz, ni kaina wannan tashin hankalin yasa Poland ka ganni haka. Ina fitowa da Mansion na samu kira. Wani ma'aikacin Mujallar ne ya min gulmar tare da turo min ita. Ya kuma tabbatar min nayi gaggawa kafin su saketa yau ɗin nan. Sai dai ashe na makaro, dan ya turo saƙon ne tin daren jiya ban lura ba sai a yau. Koda na isa gidan Magazine ɗin aikin gama har ya gama.”

“Aiko wlhy Baba sun takalo rigimar da bazasu iya maganinta ba. Dan yau ɗin nan ba gobe ba sai na saka an kama duk wani shege dake aiki a gidan wannan mujallar” ya miƙe a matuƙar fusace ya fice batare da ko sallama ya sake ma Baba prof ɗin ba. Wani shegen murmushi baba prof ɗin ya saki har haƙoransa na bayyana. Sai kuma ya jawo waya ya hau danne-danne tare da kaiwa kunnensa. Ana ɗagawa cike da bada umarni ya furta, “Duk su saki labarin. Ina son daga yanzu zuwa safiya kaf Nigeria dama duniya su san da wannan labarin”. Ƙitt ya yanke kiran, tare da kwashewa da dariya tamkar ba baba prof ɗin nan ba da tsufa ya gama cinyema rayuwa gaba ɗaya sai abinda ya sara kuma. Kai duniya ɗan adam abin tsoro. Idan har jininmu basu tsira daga zaluncinmu ba, to waye kuma zai tsira daga garemu. ALLAH ka gafarta mana kurarenmu, ka hanemu son zuciya da zalunci ga waninmu koda dabba ce😭.....✍

Masha ALLAH kowa na buƙatar samun lokacin kwalliya a gobe idan ALLAH ya kaimu, jibi kuma suyar mama😊, (to kar dai a manta da ni gaskiya ɗan hanji-hanjin nan na gobe ina jira). ALLAH ka karɓi ibadunmu da wanda sukaje hajji, ALLAH ya dawo mana da su gida lafiya. ALLAH kuma ya maimaita mana da rai da lafiya. ALLAH ya rufama kowa asiri ya hana kowa cin bashi. Mata yan uwana dan ALLAH kada a takurama maza yin abinda basu da shi. Duk abinda suka kawo mu amsa kuyi haƙuri mu sanya albarka, ALLAH sai ya bamu ladan haƙuri.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

*

Typing□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-three

53

.....Wani irin suya ta bala'i zuciyar Paah keyi. Kai tsaye ya bama driver ɗinsa umarnin wucewa da shi DSS office. Sai dai me suna ɗaukar hanyar a tafiyar da bata fi ta mintuna biyar ba kawai wata mota tasha gabansu, ga titin baida yawan mutane haka sosai sai jefi-jefi. Rai ɓace Paah ya fito ganin drivern sa na ma mai motar magana amma bashi ma da niyyar gyara musu balle fitowa ya basu haƙurin ɓarnar da yay musu dan ya gogi musu mota sosai. Saitin drivern yaje yay knocking glass ɗin wajen. Ana buɗewa kawai aka huro masa abu a fuska. Babu shiri ya haɗiye abinda yake son faɗa ɗin yay baya yana kai hannu a fuskarsa ya share abinda aka huro masan, yana ɗagowa kawai luuuu ya tafi zai faɗi. Ihu drivern sa ya ƙwala yana yo kansa da kiran, “Alhaji! Alhaji!!” kawai suka harbesa har sau biyu. Kafin wani lokaci mai tsayi sun saka Paah a mota sun bar layin driver kwance cikin jini yana magowar mutuwa dan sun samesa ne a ƙirji da cikinsa.....

□Waye da wannan aiki kuma??.

❤❤❤❤❤

Gaba ɗaya ji nake tsigar jikina na tashi sosai. Dan har ga ALLAH zuciyata ta ƙara girgiza da ganin Baba prof ɗin da Hajiya ƙarama. Duk da ba komai na fahimta ba game da zantukansu. Amma kenan hirar da yaje nayi da ni a wancan lokacin tana da manufa kenan. No wander naji duk zuciyata bata aminta da shi ba. Shine harda zuwa ya dinga ɓarin kuɗi harda kuma bani mota. Bama wannan ba, a cikin zantukansu shi da Hajiya ƙarama akwai wajajen da nake buƙatar yima nazari. Kamar...

(Tabbas nayi kuskuren ƙin bibiyar bayan Abdul-wahab kamar yanda nake biye dana Ibrahim Alonso...) “Abdul-wahab dai Baba fa kenan. Alonso Abie ɗin Ummu. To miye ribarsa idan ya bibiyi bayanmu?. Sannan su kansu bayan Abie dai na nufin Ummie, Maash, Fahad ko. Ikon ALLAH to mi hakan ke nufi kuma? Tunda dai Fahad da Awwab ai jikokinsa ne da ɗansa na cikinsa ya haifa”. _(Yallaɓai wlhy zan haukace wane irin ruɗani da tashin hankali ne haka yazo mana a rana ɗaya?. Gashi mun gagara magance batun likitocin nan abu sai ƙara nisa yake, duk da dai ba wannan bane kaɗai hope ɗinmu wancan ma zasu iya mana illa tunda ko ganinta bamayi a yanzu balle sanin halin da take ciki)._ Furucin Hajiya Ƙarama ya sake min amsa kuwwa a zuciya. “Sun gagara magance batun likitoci, sannan basa ganinta, Ummie kenan ko wa? Anya kuwa mutanen ba sune keda hannu akan al'amurin Ummie ba?”. _(Dole akwai abinda Awwab ya sani. Dole shine ya shirya komai. Ta ya yarinyar dake a Kano zata dawo Lagos? Ta ya ɗiyar Abdul-wahab zata shigo Maash Mansion matsayin yar aiki? Ta ya! Ta ya! Ta yaya?!)_ “Wannan magana ma alamar tambaya gareta, Maash nada dalilin ɓoyeni matsayin matarsa kenan?. Ya ALLAH wai wannan wane irin ruɗaɗɗen gidane haka? Na gagara fahimtar komai, gaskiyar Mama da tace kowa ma abin zargi ne, gida kamar jinin sarauta, koda yake miye banbancin gidan masu dukiya da sarautar. Su waɗan can mulki da dukiya suke ma farauta da yaƙi. Su kuma waɗan nan dukiya da ƙarfin iko suke ma farauta. Idan za'a auna ai ɗan juma ne da ɗan jummai. Gane mai gaskiya kuwa ta hanyar bincike ne kawai dan nasan Maash bazai faɗa min ba. Dole ne zuwa gobe na ziyarci asibitin can, amma bari na fara magana da aunty Falaq....

Da wannan tunanin nai shirin barci. Wayata kawai na ɗauka sai hijjabin salla na wuce. Na samu kuwa Mama har sun kwanta. Aunty Falaq ce kawai ke zaman jirana. Muma sai muka kashe komai muka wuce ɗakin da akai mata masauki. Ɗaki ne babba da komai na buƙata a cikinsa. Zama nayi saman gado ita kuma ta wuce bayi. Kamar jira ina zama kira na shigowa wayar hannuna. Shiru nayi ina kallon no ɗin dan bata Nigeria bace, sai da tana gab da tsinkewa na ɗaga dan zuciyata ta gama bani Maash ne. Koda na kai kunne shiru babu magana, nima sai kawai nayi shirun.

Munfi minti ɗaya a haka ganin baida niyyar magana na ce, “Assalamu alaikum wanene Please? Dan kana kiran matar aure ne”.

Nan ma shiru kamar bazai tanka ba, sai can ya ɗan motsa a ƙasan maƙoshi sosai dan da ƙyar nake iya jinsa ma ya ce, “Nima mijin aure ne”.

Murmushi nayi a karo na farko, a fili kam na bashi amsa da, “Uhhyim to wa kake nema?”.

“Mrs Maashhhh”.

Ya wani jaa h ɗin ƙarshe har sai da naji tsigar jikina ta tashi. Da ƙyar na iya saita kaina na ce, “kayi ɓatan kan number wannan Mrs Muhammad Awwab ce”.

Ina jiyo sautin murmushinsa sai dai baice komai ba. Dan haka nima na murmusa ina kaiwa kwance. Yaja wasu sakanni kafin ya amsa ni da, “Miya hana ki barci har zuwa wannan lokacin?”.

A hankali na ce, “Ba komai”.

“Kin tabbatar?”.

“Uhmm! Kai miya hana to?”.

Ɗan shiru yayi sannan ya ce, “Kewarki”.

yanda ya faɗa ɗin ya sakani ɗan lumshe idanu, gudun karya fara ɓaromin manya-manyan magana ya sani cewa,

“Naga waya nagode sosai ALLAH ya saka da alkairi ya ƙara buɗi mai albarka. Ya yaye maka dukkan damuwarka. Ya maida maƙiyanka ƙasan takalman ƙafafunka. Ya ɗaukaka darajarka a duniya da lahira”.

Maimakon amsa ƙitt naji ya yanke kiran. Mamaki ya kamani nai zuru ina kallonta kawai. (To addu'ar ce baya so ko mi) kafin na samo amsata sai ga video call ya shigo. Ajiyar zuciya na sauke kafin na tashi zaune na jingina da gadon sannan na ɗaga. Ƙaramar ajiyar zuciya na sauke da ɗan binsa da kallo. Kafin na ɗan rissinar da idanuna ƙasa dan babu riga jikinsa sai raɓar ruwa da yake alamar wanka ya fito. A hankali ya furta, “Cire wannan hijjab ɗin”.

Idanuna na ɗago cikin ɗan warosu waje na ce, “Saboda mi?”.

“Haka nake so”.

Ji nai kamar na kwafɗesa, amma yaya na iya dole na cire ɗin bayan na kalla ƙofar bayi kada aunty Falaq ta fito. Da ga baya ma sai na miƙe na fita gaba ɗaya na koma falon sama. Sai da na zauna sannan na kallesa na ce, “Sorry”.

Komai baice min ba sai wani shegen kallo da yake bina da shi har ina jin kunyar kaina da kaina duk da rigan ba wani ya nuna min jiki bane, wando ne da riga amma ta ciki best ce sai yar jacket ɗin samanta da take har gwiwa. Ta cikin ta kama min jiki sosai saboda ta wajen a buɗe take. Baki na ɗan tura na ce, “Wai mi kake kallo?”.

Maimakon bani amsa sai ya ɗan sakin murmushi da faɗin, “Ina jinki maimaita”.

“Mi kuma?”.

“Du'a”.

Sai naji kunya ma duk ta kamani. Amma sai na daure na maimaita masa kamar yanda na faɗa a farko. Ajiyar zuciya ya ɗan sauke mai nauyi lips ɗinsa na motsawa. Dai-dai nan na fara jiyo hayaniya na tashi sosai a gidan, hanyar down stairs na kalla da sauri, kafin na miƙe da sauri ina faɗin, “Ya Awwab gidan nan fa kamar babu lafiya”. Banma jira amsawarsa ba na katse kiran na sauka da sassarfa. Na samu har Mama da Aunty Falaq ma sun fito, har buge juna muke wajen ƙoƙarin fita. Sosai hankalinmu ya tashi lokacin da muke ƙarasa fitowa ganin police ne sai ma'aikatan gidan zagaye da wani abu, mace ce ke kukan da alama itace aka zagaye. Kusan a tare muka iso da Hajiya Mammah. Sai yazam tsawar da tayi ma'aikatan sun buɗe hanya. Hakan ya bamu damar ganin abinda ke faruwa. Falilah ce rungume da mijinta tana kuka kamar ranta zai fita. Jikinsa duk jini har mayafin da aka rufa masa data yaye. Sosai gabana yay mummunar faɗuwa. Ita kanta Hajiya Mammah idanu ta waro sosai da maida kallonta ga police ɗin, sai dai ta kasa cewa komai sai Baba ne yay ƙarfin halin tambayar lafiya..

Kai tsaye ɗan sandan ya bashi amsa da sun tsincesa ne a bakin hanya yashe a ƙasa babu jimawa. A dalilin number motar suka gane daga gidan nan yake. Dan da zasu wuce da gawar ta shi asibiti suga dai ya dace su fara zuwa da shi nan ɗin su tabbatar.

Muryar Baba na rawa ya ce, “Tabbas na nan ne. Drivern Alhaji ne, kuma tare suka fita ɗazun ai. Ina shi Alhajin?”.

“Gaskiya shi kaɗai muka samu, kuma harbinsa akayi”.

Sosai hankalin kowa ya tashi, Hajiya ƙarama ta fashe da kuka tana kiran ta shiga uku. Driver tare yake da Paah. A take aka fara neman layin Paah amma yaƙi shiga. Yan sanda da sukaga abin na gaske ne fa suka ce to zasu je office ai tracking layin Paah ɗin, gawar kuma za'a aikata asibiti domin ayi bincike, zuwa da safe sai a samesu a can office. Idan kuma Paah ya shigo kafin safiya a kira su su sani....

ALLAH sarki da ƙyar aka iya ɓanɓare Falilah a jikin gawar. Haka suka wuce aka barmu jugum-jugum. Nayi ƙoƙarin kiran layin Maash back amma yaƙi shiga. Dole na

haƙura. A wannan dare duk wanda yace yayi wani barci to lallai yayi ƙarya. Sai dai in ɓarawo dan babu Paah babu labarinsa. Hatta Baba prof ya zo gidan tun a daren shima hankalinsa a tashe.....✍

Wai ni mima zance anan ne??? Mu tattauna a comment kawai😩😩

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-four

54

.....Zan iya cewa rashin barci da kwanan tashin hankali ya haifar min da zazzaɓi mai zafi. Haka na lallaɓa nayi wanka da asuba ganin baƙona ya wuce. Na ɗan yi mamakin hakan amma sai banbi ta kansa ba nayi salla. So nake na kwanta amma bazan iya hakan ba. Koba komai ina buƙatar son samun Maash a waya duk da nasan manyan gidan bazasu ƙi kira su sanar masa ba. Miƙewa nayi kawai jiri ya wani kwasheni, babu shiri na faɗa saman gado na kwanta. Sai kawai naji hawaye na zubo min. Sannu a hankali barci ya dinga rinjayar idanuna har mai nauyi yay awan gaba dani batare da na shiryama hakan ba.

Nayi nisa sosai a barcin wani irin mahaukacin bugun ƙofa ya farkar da ni. A firgice na tashi har ina ɗimaucewa na rasa hanyar ƙofa sai da lalube na samota. Ina buɗewa kawai aka ɗauke min fuska da mari, ban gama dawowa a hayyacina ba aka sake ɗauke ni da wani marin, tare da fisgar hannuna ƙeyyy akai waje dani har falo. Sai a lokacin ne na fahimci Hajiya Mammah ce. Dan wani irin ihu tamun a saman kai da ya neman toshe min jina gaba ɗaya tana mai min nuni da television. Juyayyun idanuna na kai ga tvn, dai-dai ana nuno hotona dana Maash a cikin jirgin nan. Ba hoton bane ya bani mamaki, ganina riƙe da bindiga, na nuna Maash ɗin da ita daka ganni kaga yar daba. Dan wando ne ma da riga a jikina na rashin tarbiyya. Bayana

wasu mugayen zaratan maza ne abin tsoro suma sun nuna Maash ɗin da bindugun hannunsu. Sai kuma na gaba guntun video ne na harba masa wani ɗan abu kamar kibiya da ɗayan hannuna dake a ɓoye sai kawai a kan maƙoshinsa, kafin ya yunƙura cikin ƙattan nan dake bayana ɗaya a bayansa ya kai masa yanka da wuƙa a saman hannun da yake ƙoƙarin kaima maƙoshinsa zai cire kibiyar. Kaina na shiga girgizawa da wani irin sauri jikina na rawa.

“Wlhy wannan duk ƙarya ne ba gaskiya bane ba. Ba abinda ya faru kenan a cikin jirgin nan ba. Wlhy bani bace, waɗan nan mazan ma ban sansu ba, ba kuma suje inda muke ba ni da Yaya Awwab. Taya zan cutar da Mijina da hannuna to”.

“MIJIIII?!!! A gidan uban naki ya zama mijinki munafukar yarinya. Yallaɓai oya ku kamata idan taje can tayi bayani. Munafuka ce dama tunda tazo gidan nan muke zargin akwai abinda ya kawota, dole ma itace tai kidnapping Mu'azz. Dan tun bayan da Awwab yay hira da ita shike nan ta saɗaɗo ta biyosa”. Hajiya Mammah ce mai maganar a zafafe. Kuka na sake fashewa da shi dan gaba ɗaya na ruɗe. Gashi bani da wani ƙarfi jiri nake ji sosai fiye da ɗazun. Sai waige nake ko zanga Fahad da Hafizzullah amma babu su a wajen. Sai Mama da ke kuka tana son yin magana amma sun hanata. Ga aunty Falaq a gefe ta zube tana murƙususu da alama naƙuda ce. Banma san sanda nace “Mama aunty Falaq! Aunty Falaq!!”. A gigice Mama ta juya ga aunty Falaq, dai-dai nan matan yɗan sandan suka kamani suka fice da ni a falon.

A tsakar gida na samu an tattare yɗan aikin duka waje guda har su Shu'aibu duk an saka a mota da su TJ, su Bahijja har Falilah dake fama da raɗaɗin mutuwar mijinta ba'a bari ba. Haka nima aka tausani dan inda suke wajen ya mana kaɗan. Gashi an gwamutsa mazan da matan duka. Halin da nake a ciki yasa numfashina ya fara fisga, tun ina ƙoƙarin janyo shi har hakan ya gagara. Ban tashi tsintar kaina a ko'ina ba sai a cikin cell yashe a ƙasa an saka min drip....

□□□□

Ganin Mansoor na mintuna goma da Salimah ta samu tayi shine ya taimaketa dawowa Nigeria neman iyayensa. Dan bata tambayesa komai ba sai inda ya fito da address ɗin gidansu. Duk da dai da ƙyar ta samu ya faɗa mata dan shi yace yama fi son dawwama a can. Sai da ta takurashi har lokacin da aka bata na neman ƙarewa sannan ya sanar mata shi ɗan Nigeria ce a Kano state. Bako tayi ƙasa a gwiwa ba ta garzayo. Sai dai kafin ta taho ɗin ta nema taimako wajen shahararren matashin ɗan kasuwar nan da yay matuƙar ƙarfi a Dubai ɗin wato Maash. Duk da dai bata samu ganinsa ba ta gana da makusancinsa. Shine ya taimaketa ya haɗasu a waya sukai magana ta minti biyar ko kuma tace ta masa bayani, dan akaf mintuna biyar ɗin nan bataji yace da ita ko ci kanki ba. Ko gaisuwa da tai masa kawai yace Uhmm ne.

Bayan ta gama faɗar ne wanda ya haɗasun ya amshi wayar yace ta jirashi. Kusan awa ɗaya ya kirata back. Ya sanar mata Maash yace taje ta nemo iyayen shi guy ɗin, idamasu hali ne suzo Dubai tare, idan marasa ƙarfi ne ta kira ta sanar za'a tura mata kuɗin jirginsu da duk wani shigi da ficin shigowa wata ƙasa. Sosai taji daɗi tanata ma Maash addu'a da shi daya taimaketa. Yace mata babu damuwa ta dai yi ƙoƙari dan Maash zai shigo Dubai a nan da kwanaki uku, kuma kwana biyu zaiyi kacal, ba lallai kuma ta sake samun damar ganinsa ba.

Ita asalinta yar medugiri ce. Harkar kasuwanci ta kai Babanta can Dubai shine ya maida su can. Dan mahaifiyarsu ta jima da rasuwa daga ita sai ƙanwarta yanzu sai Babansu da shima girma ya fara kamawa. Tayi karatu mai zurfi a fannin Shari'a, tana kuma harkar kasuwancinta daga Dubai zuwa ƙasashenmu na nan masu makwaftaka da Nigeria.

A randa Salima ta iso aranar batai ƙasa a gwiwa ba sai da ta samu gidan su Mansoor. Inda ta fara cin karo da Attahir zai kai Mamy asibiti ganin doctor. Da farko bai saurareta ba sanin halin matan zamanin nan (Su wai mazan nan sun ɗauka kowace mace ma irin su Azizat ne😒). Sai da ta ambaci sunan Mansoor sannan ya saurareta bayan ya jawota daga cikin asibitin suka yo waje da Mamy na ganawa da doctor kasancewar har asibiti Salima ta bisu. Bata wani ja masa aji ba ta warware masa komai dake faruwa da ɗan uwansa. Hankalinsa yayi mummunan tashi, babu shiri yay kiran Dad ya masa bayani. Dan baya son Mamy ta san komai kodan yanayin jikinta a yanzu. Shima hankalin Dad ya tashi sosai. Dan haka yace a kawo Salima office ɗinsa shi kuma Attahiru yaje ya maida Mamy gida ya samesu a office ɗin.

Hakan kuwa akayi, sai dai anan asibitin Attahir yace Salima ta jirashi ya je ya kai Mamy gida ya dawo sannan ya ɗauketa. Suna tafiya yana ƙara mata tambayoyi har suka iso office ɗin Dad ɗin. Tsaff ta kwashe duk yanda ta sanar ma Attahir shima Dad ɗin ta sanar masa. Har neman taimakon da tayi wajen Maash dan ta tabbarar in har ya saka baki a maganar Mansoor zai iya kubta. Musamman da ya kasance ba gaskiya bane set up ne. Daga Attahir har Dad sun girgiza da jin sunan Maash. Amma yaya zasuyi tunda ta riga ta kai zancen can, sun kuma san taimakon nasa ne kawai zai fidda Mansoor da gaggawa. Cikin gaggawa suka fara shirin wucewa Dubai batare da Mamy ta sani ba. Dan basu sanar mata komai ba sai shi Dad ɗin ne yace mata zai je Dubai wani Bussines zai kuma je da Attahir. Bata kawo komai a ranta ba dan yanzu daga ita har Dad ɗin jan Attahir ɗin sukeyi jikinsu sosai. Hatta aurensa da ke gabatowa shiri suke masa na musamman. A shekaran jiya suka isa Dubai. Basu kuma samu ganin Maash ba sai a daren jiya ɗin nan. Sam shi bai wani gane Attahir da Dad ba. Saboda ba dasu yay waccan harƙallar ba Mamy ce. Saima ɗaukar hankalinsa da kammanin Dad ɗin sukai ya zuba masa ido ƙasa-ƙasa, sai da Attahir ya katsesa da bayanin fitowa filo ya gaya masa gaskiyar zance gudun kada sai ya je fiddo Mansoor ko ganinsa yaga shine yace bazaiyi ba. Amma a mamakinsu sai sukaga ko shock ma fuskarsa bata nuna ba. Face bada umarnin kira masa lawyers ɗin sa da yayi. A take kuma PA ɗin nasa ya aikata yanda ya buƙata.

Ya gana Da lawyers ɗin nashi da Attahir da Dad sai shi Hayatu na mintuna ashirin, kafin su ɗunguma zaman court ɗin da za'ayi na biyu akan case ɗin Mansoor ɗin. Sai dai shi banda shi. Suna wucewar ne ma ya shiga yay wanka, ya fito ya nema no ɗin Samraah. Bayan kuma ta yanke bata sake samunsa ba shi kuma duk da yaji mita faɗa bai nemota ba har yanzu.

(Anya kuna ganin lafiya kuwa? Kumu dai je zuwa muji ina Maash ya shige ne haka to? Duk da yaji batun Samraah na cewar gida babu lafiya).

□□□□

Tun bayan wucewar motocin police da duk ma'aikatan gidan harda Baba mijin Mama Balki baban kuma Hayatu gidan yay tsitt, sai magowar Falaq mai naƙuda. Da farko duk fita sukayi batare da kowa yazo takanta ba har Baba prof. Sai kuma ga Hajiya ƙarama ta dawo wai Mama Balki ta tashi ta shirya falaq ɗin a wuce da ita hospital. ALLAH sarki Mama Balki a ruɗe take, dan haka ta amsa mata da to. Jiki na rawa ta tashi ta nufi ɗakin da akama falaq ɗin masauki. Ita kuma Hajiya ƙarama ta juya ta fita akan suyi sauri tana jiransu. Tana fita tai kiciɓus da Baba prof shima yay sau da baya. Kallon kallo suka tsaya yima juna tamkar wasu zakaru ko ragunan da suka gama tara ƙahunna da basu da aikin yi sai son yin dabbe. Kallonsa take kamar yanda yake kallonta. Kafin shi ya basar cike da ɓoye abinda ke barazanar bayyana akan fuskarsa. Ciki ya shigo, itama sai ta biyoshi. Mama Balki na'a kan Falaq dan harta wuce ɗaki da dawo da baya, ganin irin kallon da suke mata su biyun batare da sunyi magana ba ya masifar tayar mata da hankali, kafin Baba prof ɗin ya furta, “Su waɗan nan mi sukeyi a gidan nan da ba'a wuce da su ba?”.

Cikin marairaice fuska kamar ta ALLAH Hajiya ƙarama ta ce, “Baba yarinyarta naƙuda take yi, asibiti zamu wuce yanzu da ita kayi haƙuri dan ALLAH”. A mamakin Mama Balki baiyi magana ba, sai wani irin kallo da Baba prof ɗin yama Hajiya ƙaramar ya ɗauke kansa, sai kuma ya juya ya fita yana mata wani irin inkiya da hannu. Bin bayansa tai da sauri itama tana sake tabbatar ma da Mama Balki ta tashi ta shirya falaq ɗin su wuce asibiti.....✍

(Ya kamata nayi tambaya anan ma ko na wuce???)

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

Typing□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-five

55

.....Cikin ƙanƙanin lokaci labari ya zagaye ƙasa. Dan ta ko ina yan media yaɗashi suke abinka da babban mutum. Gashi daɗin daɗawa an tabbatar da zuwa yanzu Maash na gadon asibiti ne ma a wajen ƙasar. Ga batun mahaifinsa da ba'a gani ba. Ma'aikatan jirgin da aka nuna wancan guntun video sun fito sun tabbatar ma duniya duk abinda aka gani ya faru, dan a yanzu haka suma suna a asibiti ne saboda raunikan da aka ji musu, biyu da ga cikinsu ma sun rasu. Mugun kiɗimewa Sheikh Muhammad bin Khalipha Al-Hussain yayi da gani wannan labari. Dan shi bai san mike faruwa ba yau ya tashi baya jin daɗi ko television bai buɗeba balle redio, hakama waya. Sai da Hameed ya kira shi yana sanar masa sannan ya buɗe tvn yaga wannan ƙulli. Dan daga gani kasan an shirya komai ne ma'aikatan jirgin nan kuma su ci kuɗi. Number ɗin Maash ya fara nema sai dai kuma bata shiga. Hayatu, nan ma bata shiga. Haka ya dinga bin duk wani yaron Maash makusanci dake a ƙasar da wajen ƙasar dan so yake yaji ina Maash ɗin yake wannan al'amari ke faruwa haka? Ko da gaske yana a gadon asibitin ne?. Amma amsa ɗaya yake samu suma basu san inda Maash yake ba. Hayatu ma an nemesa an rasa tun barowarsa prison da suka sami damar fitar da Mansoor bayan an tashi a shari'ar da lawyers ɗin

Maash ɗin suka kawo ƙarafafan hujjoji da ya tabbatar da komai shiryashi akai akan Mansoor. Abinka da komai akan tsari a ranar suka saki Mansoor ɗin aka cafke abokin nasa...

Su kansu su Attahir ɗin a kiɗime suke da jin abinda ke faruwa. A take Attahir ya fito yay magana a media. Bayan ya kira wani abokinsa ma'aikacin BBC. Zancen Attahir ya fara saka mutane a ruɗani, ba'a gama hakan ba sai ga Sheikh Muhammad shima ya fito ya ƙaryata batun abinda ya faru a jirgi. Ya kuma tabbatar da Samraah matar Maash ce shi da kansa ya amshi walliccin aurensa, ya kuma bada hotuna da bidiyo da akayi a wajen ɗaurin auren dama saboda gudun abinda zai iya zuwa ya dawo kasancewar aure ne na babban mutum da akai kamar a sirrance tunda babu wanda ya sani har family ɗinsa. Tofa, zantuka sun fara canja salo, dan an rasa ina za'a ɗauka a yarda. Batun farko na Maash na asibiti bayan Samraah da yaranta sun nema halakashi? Ko kuwa batun Attahir da mahaifinsa da suka tabbatar da a yau ɗin nan sun gana da Maash a Dubai kuma lafiyarsa ƙalau. Harma da taimakon da yay musu basu ɓoye ba. Hakama Salima da lawyers nashi, sun kuma tabbatar da shima Hayatu ko awanni biyar ba'ai da ɗaukesa ba. Dan lafiya Lau suka fito a prison da shi suka shiga mota ya shiga sun iso gidan Maash ɗin sukaga babu motar da yake ciki a tare da su. Nan kuma gidan Maash an zagayesa da securitys. Basu sani ba Maash na cikin gidan har yanzu, ko kuwa? Amma dai sun tabbatar lafiyarsa ƙalau su dai akwai dai abinda ya faru? Ko batun babban malami da kowa ke mutuntawa da gani girma daya tabbatar da shi da kansa ya amsawa Maash auren Samraah harma ga shaidu?.

Kasancewar Samraah sananniya ce a baya, da irin yanda zancen kidnapping ɗinta da batun fasa aurenta da aurenta na biyu ya zagaya media sai aka dinga dawo da labarin yanzu. Sai dai abinda ya so raba kawunan mutane ko'a baya ba'a san takamaiman mijin Samraah ba. Wanda akaita haɗata da su editing hotunan akayi. Amma sanin waye malam yasa da yawa aka amince da wannan zance.....

□□□□□

Gaba ɗaya Mama Balki ta rikice. Ta rasa miya kamata tayima Falaq, ga shi bata son tafiya asibiti da ita tabar Ummie ita kaɗai a gidan nan akwai haɗari. Dan tabbas komai zai iya faruwa. Hawayenta ta ƙara sharewa, tare da bubbuga fuskar Falaq da ke neman shiɗewa. A dai-dai nan aka fara taɓa ƙofa alamar za'a shigo. Hankalinta ne ya sake tashi, dan tayi alwashin data bar Ummie gara ta haƙura ta rasa Falaq ɗin. Ta gama sallamawa a bazata taji ana kulle ƙofar, da wani irin sauri ta ɗago dan

tasan dai da ga ita dai Falaq sai Ummie da tun ɗazun ma take barci bayan likitocin ta sun zo sun dubata sun mata allura. Sai dai a mamakinta sai taga Ummie ce ke rufe ƙofar, bata gama dawowa a sumar wucin gadin da tayi ba Ummien ta baro ƙofar ta iso garesu. “Bilkisu Kamata” ta ce kawai tana ƙoƙarin kama Falaq. Duk da maganar bata fita sosai harshen ma a karye yake kamar mai koyon magana Mama Balki taji abinda ta faɗa. Tuni wani ƙarfi yazo mata ga hawaye na kwarara tana kuma kallon Ummie ɗin suka ɗaga Falaq. Jin yanda ake buga ƙofar da wani masifar ƙarfi ana ƙwala kiran sunan Mama Balki yasa Ummie sake faɗin, “Mubar gidan nan Bilkisu”.

Ta wajen swimming pool ɗin nan suka fita, ita dai Mama Balki sai kallon Ummie take hawaye sun gagara tsaya mata.

Da wani irin ɓacin rai Hajiya ƙarama ta koma, Baba prof na tsaye a babban falon sashensu yana kai-kawo su Azizat cirko-cirko Hajiya Mammah na zaune na sharar hawaye, hakama Maman Malika kuka take. Uncle Abdullahi dai ya fita tun ɗazun a gidan akan batun Paah. Iya su kaɗai ne a gidan sai police a ƙofar gate biyu da aka bari, amma da securitys ɗin ƙofar, da na gidan, da duk wasu ma'aikata maza da mata an tattaresu zuwa police station. Babu ma wanda yabi takan batun Fahad da Hafizzullah da basa gidan duk wannan dambarwar da ake yi. A yanda Hajiya ƙarama ta faɗo falon ne yasa duk suka ɗaga kai suka kalleta. Cikin shashsheka da sauke numfarfashin gudun da ta ɗan yi ta ce, “Ta kulle ƙofa fa matar can. Ina tsoron ba wani abu take shiryawa akan Hajiya Babba ba”.

Su dukansu babu wanda bai zabura ba. Cikin matuƙar ihu Baba prof ya ce, “Ubanwa yace ita su barta ita da yar tata. Idan wani abu ya samar min Ummu-Hidaya sai na kashe matar nan. Ni dama sam ban yarda da ita ba itama...”

Babu wanda ya iya cewa komai akan maganar tasa. Sai rige-rigen ficewa da sukai a sashen zuwa sashen Maash ɗin. Wani irin mahaukacin jijjiga ƙofar suka dinga yi su duka suna zagin Mama Balki. Ruɗewa Mama Balki da duk suke iya jiyosu kasancewar sun zagayo ta can baya ta sake yi. Ga Falaq ta sume musu ta ƙara nauyi. Jikin Ummie ba wani ƙarfi yake da shi ba. Amma ta daure matuƙa duk da itama jikin nata rawa yake yi. Jin motsin ana nufo inda suke dan su Baba prof na ƙoƙarin zagayowa ne su biyo ta baya tunda duk sun san da ƙofar cikin garden har biyu yasa cikin kuka Mama Balki da jikinta ke ƙara ƙarfin rawa ta ce, “Ummie ki gudu ke kawai, bari na kira Isma'il amintaccen Alhaji ƙarami ne in sha ALLAHU zai taimakemu ya kaiki wajen da wani bazai taɓa sani ba har Alhaji ƙarami ya dawo. Amma zamanki anan akwai haɗari”.

Kai ta girgiza mata, tare da mata nunin su ɗauki falaq ɗin. Babu yanda Mama Balkin ta iya haka suka sake ɗaukar Falaq, cikin flowers suka shige hannayensu dafe da bakunansu. Daga ta inda suke suna iya hango Baba prof da Hajiya Mammah dake ƙoƙarin shiga ta ƙofar swimming pool da suka bari a buɗe. Dai-dai nan Falaq ta kawo wani irin bahagon mummunan numfashi da ya saka Baba prof dake ƙoƙarin

shigewa tsayawa cak. Jikin Mama Balki na wani masifar ɓari ta cire ɗan kwalin kanta ta toshe bakin Falaq dake zabura. Garrr wata ƙatuwar baƙar kunama ƙirin ta fito daga ƙarƙashin Falaq ɗin ta shige tsakanin Mama Balki da Ummie. Hakan na nufin kunamar ce ta sari Falak. Su duka kasa motsi sukayi, musamman Ummie da dama tun can fil azal tana masifar tsoron kunama a rayuwarta da maciji da ƙadangare. Kuma Mama Balki ta san da hakan. Ga shi in har suka sake wani motsi Baba prof da har yanzu ke'a tsaye sai ya gane. Haka suka zauna zukatansu na bugawa ga wata irin zufar tashin hankali data gama jiƙe Falaq babu tantama haihuwa ce ga azabar kunama.....

□□□□

A can Kano kuwa ɓangaren Abbah kam neman yanke jiki yayi zai faɗi a lokacin da yaci karo da tashin hankalin da ke faruwa. Dan illahirin jikinsa karkarwa ya shiga yi. Baima san sanda ya fara ƙwala kiran Mom da duk abinda ake tana a kusa da shi tana gani ba daɗi kamar zai kasheta. Ƙin amsawa Abba kiran da yake matan tayi sai ma murmushi da ta saki duk da wani ɓangare na zuciyarta na mata raɗaɗin jin Maash wai Samraah ta aura. Amma babu komai tunda ga a yanda aka ƙare hakan ma nasara ce. Halime da sam ita bama tasan wainar da ake toyawa ba jiyo muryar Abba dake kamar rawa ya sata tashi a ɗan firgice daga kwanciyar da tayi a kujera. Dan yau bazata fita makaranta ba bata jin daɗin jikinta. Da ƙyar ta iya lalubar ɗan kwali ta ɗaura, a karo na farko da tun zuwanta gidan matsayin matar Abba ta shiga sashen Mom. Dai-dai nan Abba yayo baya zai faɗi da sauri ta saka hannayenta biyu ta tarosa ya faɗa a ciki. Duk da nauyin da yay mata, ga ƙaton cikinta daya ƙara fitowa haka ta daure jikinta na rawa ta kai durƙushe da shi. Kuka take tamkar ranta zai fita, UBANGIJI gafurin rahimun sai ga Alhaji Jafaru da Gwaggo Gudidi tamkar an jehosu gidan. Kukan Halime da neman temako da take yaja hankalinsu sashen Mom ɗin suma suka nufi can da sassarfa.

Mom ɗin najin motsi itama ta fara kuka tana kaiwa durƙushe gaban Abba ta kamoshi daga jikin Halime ta maida nata jikin. Salati Gwaggo Gudidi da Alhaji Jafaru suka shiga yi suma suna nufar kan Abban da gaba ɗaya numfashinsa ya gama ɗaukewa.....✍

□□□□□

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

Typing□

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-six

.....Baba Prof ya ɗan jima yana waige-waige kafin ya ƙarasa shigewa ganin baiga komai ba. Yana shigewa Ummie ta miƙe jikinta na rawa saboda azababben harbin kunamar daya ratsata har tsakkiyar kanta itama. Cikin ƙanƙanin lokaci zufa ta gama wanke mata jiki. Ƙoƙarin nufota Mama Balki tayi, amma sai ta mata nuni da su kama falaq kawai, hawaye ne suka ciwo idanun Mama, dan ta tabbatar cizon kunamar nan ya shigi Ummien amma ta nuna dauriya. Haka suka kamata da ƙyar sai nishi take saboda babu damar yin kuka kasancewar ɗan kwali da Mama Balki ta saka mata a baki, yayinda ita kuma Ummie keta faman taunar lips ɗinta. Ta cikin garden ɗin Maash daga can ƙarshe da filawoyi suka lulluɓe bangon gaba ɗaya Ummie tayi da su. Mamaki ya kama Mama Balki lokacin da Ummie ta saka hannu ta shiga yaye filawar wajen duk da ƙayoyin dake famar fasa mata hannu, ƙofa ce ta bayyana da bazaka iya taɓa yarda akwaita a wajen ba saboda ta mugun sajewa da katanga matuƙa. Da ga gani kai kasan an tsara wajen ne sosai. Dan ƙafa, ce ta gasken gaske. Wani abu daga can ƙasa Ummie ta danna sai ga ƙofar na buɗewa da ƙyar, dan wani irin mugun ƙarfi ne da ita gata ta zallar ƙarfe. Dai-dai suna gama fita suka jiyo Arwa na ƙwala kiran su Baba prof. Suna ɗaga kai suka hangota ata can saman Maash ta balcony. Tabbas ta gansu, kamar yanda suka ganta. Dan haka Ummie taja ƙofar da masifar sauri ta datse. Kuka Mama Balki ta sanya tana neman number ɗin Isma'il. Amintaccen Maash da ke matsayin Kuku a gidan Baba prof, duk da dai itama Mama Balkin bata san da hakan ba, bama yasan cewar Isma'il ɗan sanda bane kawai dai yakan zo amsar bayanai a hannunsu na wani abu idan ya faru gidan lokaci-lokaci. Harta tsinke bai ɗaga ba. Hankalinta ya sake tashi, dan ta tabbatar suka zo ga ƙofar nan bata buɗe ba zasuyi yinƙurin zagayawa ne, ga Ummie dake shan azabar kunama, ga Falaq data haɗa biyu naƙuda da kunama utama. Kiran ta sake yi, sai data masa uku sannan ya ɗaga, batama zauna saurarensa ba ta shiga masa bayani. Shima can hankalinsa ne ya sake tashi, dan dama a tashin hankalin rasa inda Maash yake suke shi da duk ɓoyayyayun da ba

kowa ya sani ba. Ya tabbatar musu su ɗan bar wajen kaɗan gashi nan zuwa, dan dama yana kusa da gidan yaje kasuwa ne. Ko tahowa su Baba prof sukai daga cikin gidan kafin su su zagayo shi ya iso. Hakan kuwa akayi, dan cikin ƙanƙanin lokaci ya iso kasancewar su su Baba prof na can suna kokarin neman ƙofa da Arwa ta tabbar musu ta gani da idonta an buɗe su Mama Balki sun fita harda Ummie da suka duba basu gani ba a kaf sashen. Ganin fa babu ko alamar kufan ƙofa a wajen wasu suka fara ƙin yarda da Arwa ɗin. Yayinda Baba prof yace bazasu tabbar da hakan ba sai sun zagaya ta baya dan ga sayin ƙafafun su Mama Balki nan ɓaro-ɓaro a garden ɗin. Dan haka aka bar su Hajiya Mammah da yaran, shi kuma shi da Hajiya ƙarama suka zagaya. Isowarsu dai-dai da tashin motar Isma'il daya kwashi su Ummie sai number ɗin motar da ƙurarta suka gani. Wani irin mahaukacin reverse Hajiya ƙarama tayi tare da ƙarama motar wuta suka bi bayansu. Gaba ɗaya hankalin su duk ya tashi, da ita Ummie ma duƙar da kanta kawai tayi dan juya mata yake yi sosai. Isma'il na ganin zasu ƙure musu ya wani irin yin reverse shima ya dawo baya, kasancewar ita kuma ta riga ta kwashi motar da yawa domin ƙoƙarin cimmusu sai ta kasa tsayawa. Da wannan damar ya samu shigewa wani layi da bashi da tabbacin yana ɓillewa ko a'a...

Wani kalar taka birki da dukan steering Hajiya ƙarama tayi. Shima Baba prof ya kaima glass ɗin window ɗin gefensa naushi. Gaba ɗaya idanunsa sun gama kaɗewa jajur, wayarsa ya fisga a take ya shiga kiran number DCO ɗin da case ɗin Paah ke hannunsa. Yana ɗagawa ya masa bayani akan kidnapping Ummie da aka sake yi tare da bashi number ɗin motar. Yana ajiye wayar Hajiya ƙarama dake masa kallon tashin hankali ta ce, “Yallaɓai amma fa wannan ganganci ne. Tunda kaima kasan ba kidnapping ɗin nata akai ba. Nifa na kasa ganema gaba ɗaya wannan shirin naka dake neman harmutse komai.”

Ko kallon inda take baiyi ba bare ya amsa mata ya buɗe motar yay ficewarsa. Jitai kamar ta shaƙo shege ta farka mar wuƙa kowa ma ya huta. Motarta itama ta fisga a fusace ta bar wajen batare data sake kallonsa tsaye a gefen titi yana waya ba. Tasan Commando yake kira, ita ma kuma tana buƙatar ganin commondo ɗin yanzun nan. Dan su ya kamata su ɗauki Ummie kafin shi.....

❤❤❤❤

An miƙa Abba asibiti da gaggawa. Halime sai kuka take yi Gwaggo Gudidi na lallashinta. Har yamma basu ji wani ƙwaƙwƙwaran bayani akan al'amarin nasa ba. Sai kusan bayan isha'i doctor ya ɗan kwantar musu da hankali tare da son ganin

Alhaji Jafaru. Dagewa Halime tayi akan saita bisa, da ƙyar Gwaggo ta dinga lallashinta Alhaji Jafaru ya fita ya tafi shi kaɗai. Babu jimawa sosai sai gashi da takardar magunguna. Wayarsa daya bari ya ɗauka ya fita. Gwaggo na tambayarsa yaya ake ciki yace mata kawai da sauƙi ayi masa addu'a. Gaba ɗaya jikin Gwaggo ya ƙara yin sanyi, yayinda Halime ke kwasar kuka. Ita kanta Mom duk tayi wani sukuku dan zuwa yanzu ta fara jin hankalinta na tashi. Gashi su Gwaggo duk sun ƙi kulata sam....

❤□❤□❤

Tun a mota faya ta fashema Falaq, da ƙyar ALLAH yasa suka isa gidan da Isma'il yake rayuwa kafin fara aikinsa a gidan Baba prof.. dole shi da Mama Balki suka kamata zuwa ciki, dan Ummie kam bazata iya ba zuwa yanzu ƙarfin ta ya gama ƙarewa. Ita kanta sai da suka komo suka kamata suka fita da ita a motar zuwa ciki. Suna shigowa kukan jariri na jaraɗe gidan. Da sauri Mama ta nufi ɗakin, har ta shiga sai kuma ta dawo jikinta na rawa ta buƙaci sabuwar reza da ko towel ne. Zuwa Isma'il yay ya ɗako, yana kawo mata ta koma ciki. A mamakinsa sai ya ga Ummie ma ta miƙe. Ƙoƙarin dakatar da ita yayi amma sai ta masa murmushi kawai cikin ƙarfin hali ta shiga ɗakin itama. Mama Balki na hanata amma a hakan cikin yanayin da take sai da ta taimaka mata suka amshi haihuwar Falaq ɗin. Dan ma Alhamdullah komai yazo da sauƙi. Dan suna gama yanke cibi sai ga uwa itama ta biyo. Mama ce ta cigaba da gyara Falaq, yayinda Ummie ke rungume da jinjiri a jikinta hawaye na sauka mata da alama akwai abinda ta tuna ko yake dawo mata da irin wannan yanayin. Haka dai Mama ta gama tsaftace komai ta gyara jariri da uwarsa ta kuma taimakawa itama Ummie ta gyara jikinta daya ɓaci. Bawan ALLAH Isma'il sai gashi da kayan da duk zasu iya buƙata na sakawa harda na jinjiri sai likitan Ummie. Yana ajiye musu tare da abinci ya nunama Mama Balki komai yay, likita ya duba Falaq duk da yace ba aikinsa bane aka kuma duba Ummie su duka akai musu allaurar dafin harbin kunama sannan suka musu sallama akan zai koma kan aiki kar a nemesa. Addu'a Mama balki ta masa Ummie dai na kwance rungume da jariri kamar mai barci....

□□□□□

Dole Isma'il yay hanzarin shiga kasuwa yay cefane sannan ya kama hanyar komawa gidan Baba prof. Yana zuwa kuwa motar data ɗakko baba prof na isowa. Gaishe shi yayi kamar yanda kowa ke gaishe shi a ransa yana mamakin ganin yanda duk Baba prof ɗin ke'a hargitse. Haka dai ya lallaɓa ya shige kitchen ganin

Commondo ya iso shima. Yana shiga kitchen ɗin ya ɗauka ruwa da lemo ya kai falo, in da ya samu har commondo ya shigo. Yana ajiyewa ya juya ya koma kitchen ɗin. Inda ya saba laɓewar ya laɓe yau ma. Aiko sai ga muryar Baba prof ɗin cikin tashin hankali...

“Daga nan zuwa dare ina buƙatar ganin gawar Lawisa a Maash Mansion ”.

A wani kalar firgice Commondo ya juya ya kallesa. Batare da yasan ma mi yake ba ya ce, “Yallaɓai saboda me?”.

“Saboda daman hakan shine plan ɗina, sai dai ba a yanzu naso yin hakan ba. Amma naga tana neman shiga min hanci dolene kuma na fyatota.”

“Eh bazan ƙi baka goyon baya ba ranka ya daɗe. Sai dai inaga ya kamata mu dai sake nazari. Lawisa nada sirrikan ka a hannunta da yawa. Sannan ko babu komai kana buƙatarta a yanzu.”

“Duk wani sirri dake a hannunta bashi da wani amfanin da zai min. Kawai a kaudat.....”

“Niko keda sirrin da zai maka amfani Adams”. A bazata sukaji muryar Hajiya ƙarama a kansu. A tare duk suka kalleta, a yau babu kunya babu tsoro ta nuna Baba prof da yay galala yana kallonta. Dan sam baiji ko alamar shigowarta falon ba ma kodan a gigice yake.....✍

Tofa. Manyan shegu yaya dai?.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-seven

.....“Lallai kai ka tabbata ɗan kunama Adams, har ni kake bada kwangilar a kashe yau? To lallai kayi babban kuskure, dan Lawisa da kake gani ƙadangaruwar bakin tuluce. A barni na ɓata ruwa, a karni kuma a kar tulu. Kuma wlhy kayi kuskuren barin abinda ke ranka ya fito fili har na jisa. Wato dama planning ɗinka kenan kasheni. Kai wannan tsohon ban taɓa ganin asararre irinka ba tsohon najadu da zai ƙare rayuwarsa a rumfar asara. Koda yake bazanyi mamaki ba, tunda har hassada ta kaika ga cin amanar wanda ya ɗaukeka daga rana ya kaika inuwa dama nima nasan za'azo wannan gaɓar, sai dai kuma ita wannan Lawusar ba Alonso bace. Ba kuma Ummu-Hidaya bace da ka raina. Wlhy sai naga bayanka. Baƙin azzalumi, dama wannan ruɓaɓɓen plan ɗin ka shirya shiyyasa kaketa wani ɓoyema mutane ko, to kaje ka samu likitoci su maka wankin brain, dan naga alamar taka dattin giya ya cikashi. Na kuma maka alƙawarin ni Lawisa sai na fara ganin bayanka. Kai kuma ɗan koranka an saka ka kasheni ko, idan zaka gwada bissmillah”.. ta ƙare maganar da karkaɗa yatsunta a gaban fuskar Commondo ta juya fuuuu ta fita a falon. Babu wanda ya iya motsawa a cikinsu. Dan kowa da abinda yake tunani. Sai zuwa can Commondo ɗin ya ja numfashi ya fesar. Cikin yanayin nan nasa na ciccijewa ya fara magana.

“Oga kafayi kuskuren saka mace a wannan sabgar taka. Musamman ma wannan mai buɗaɗɗen idon, dan wannan daga ganinta kaga hatsabibiyar da zata iya aikata komai dan cikar burinta. Tabbas da ace ina nan ka shirya ƙulla alaka da ita da bazan bari ba. Amma karka damu, ko yanzun saina nuna mata babba babbane. Badai duk abinda take taƙamar da shi a ƙarƙashin ikonka yake ba. Sai na koya mata darasi kafin na kaudata. Amma saka batunta a gefe, ina son wannan abun dake neman ƙwaɓewa mu gyarashi da shiri na musamman dan na fara zargin itace ma ta kuɓutar da matar nan a gidan”.

Karo na farko da tun bayan fitar Hajiya ƙarama Baba prof ya ɗago ya kalla Commondo. Kai ya jinjina masa alamar tabbatarwa. Tare da faɗin, “Yes oga ka auna mana. Idan babu rami miya kawo rami?”.

Sosai Baba prof ya gamsu a wannan gaɓar, domin kuwa ya ɗan buɗe mata wani abu a lokacin da sukai kiciɓus a ƙofar sashen Awwab ɗin kallon data masa ya kamata ya saka masa alamar tambaya, amma duk da haka ya mata nuni da ta kauda matar da yarta, shine tai amfani da Ummu-Hidaya ta fitar kenan a gidan?. To anya kuwa ba itace ma tai kidnapping masa Mu'azz ba?”.

Kallon Commondo yayi cikin jinjina kai ya ce, “Zan iya yarda da zancenka dan yarta ce ta ankarar damu sanda suke guduwa. Sannan itace taja motar sanda muke binsu. Ta kuma kasa cimmusu har suka gudu. Sannan na fara zargin Mu'azz na hannunta. Dan idan ka haɗa 1+1 amsa guda zai baka. Dama tana da shirin cin amanata kenan?”.

“Bazamu tabbatar da haka ba sai mun bita a sannu. Idan ta tabbata cin amanar taka take shirin yi kuma. Aiko sai tayi nadama Boss. Ka bani nan da zuwa dare zanyi tunani. Amma kaima kayi wani abu guda. Yana da ƙyau na dinga sanin mi ka shirya saboda gudun samun matsala. Dan tun farko da nasan abinda ka shirya kenan baza'a saki wannan maganar data karaɗe lungu da saƙo ba har sai mun fara yin abu biyu. Sannan zamu rushe uku a ciki”.

Kai Baba prof ɗin ya kaɗa masa. “Dama banyi aikin don yin wani abu ba. Nayi ne kawai dan ɗauke hankalin mutane. Dan nasan zancen zai ɗauki lokaci ana tattaunashi”.

“Hakane kuma oga. Amma abinda ya fi tsaya min a rai shine batun Maash na asibiti. Taya hakan zata kasance bayan lafiyarsa ƙalau?. Sannan Maash FURAR DANƘO ne akan shekara ana damunsa bashi farau-farau.”

“Lafiya Lau yake. Yana Dubai a cikin gidansa. Na saka an katse network ɗin gidanne kawai da wuta da ruwa, an kuma zagaye da securitys yanzu haka shi baima san mike faruwa ba sam. Yaronsa kuma na hannunmu.”

Kasa magana ma Commondo yayi, dan yasan wanan ramin sam bai ginu ba. Gaskiyar Lawisa wannan tsohon dattin giya ya gama cinye masa ƙwaƙwalwa wlhy. Jiba wani wawan shiri dan ALLAH. Amma ba damuwa, shi bari yayi wasa akan nashi wasan dana Lawisa. Tunda yanzu ya fahimci tun a duniya ake fara nafsi-nafsi. “Oga ka bani nan zuwa dare zanyi tunanin mafita. Kaima ya kamata kayi wani tunanin mu haɗa plans kamar biyu mu gani. Yanzu mu dukanmu muna buƙatar hutu”.

Sosai Baba prof ya gamsu da hakan. Dan tabbas kansa ma shi gaba ɗaya a juye yake. Sannan ya yarda da Commondo fiye da ɗari bisa ɗari a rayuwarsa. Baya taɓa kawoma ransa zai iya cin amanarsa. Kallan Commondo ɗin yayi, cike da yarda ya ce, “Suma ahalin yarinyar nan ya kamata muyi tunani a kansu. Dan nayi tuya na manta da albasa kasancewar ban san makirin can ne ya karɓi waliccin auren ba. Bana son maganar nan ta lafa da ga nan har zuwa randa zan saka a buɗe Awwab. Dan ina son lokacin da zai fito kansa yay matuƙar ɗaukar zafi ya rasa ina zai fara kamawa, ta hakanne kawai zan iya cimma burina a kansa. Sai maganar Ummu-Hidaya, bana son akai safiya bamu san inda suke ba. Hakama Mu'azz”.

“Ka ɗauka wannan matsalar na maganceta ma. Dana fita daga nan zan fara samar da masu binciken ne ta ɓangarori biyun”.

Kai kawai Baba prof ya jinjina masa. Sallama commondo ya masa, shi kuma ya samu giyarsa ya kwankwaɗa sannan ya tashi ya shige ciki....

Commondo na barin gidan Baba prof gidansa ya wuce. Bai yi mamakin samun Hajiya ƙarama ba, gaba ɗaya ta hargitse masa falo da hayaƙin shisha. Ɗ'ar dariya yayi tare da kaiwa zaune. Dan yasan dai bata shan komai yau kuma gata da shisha.

Lallai ran manyan mata ya ɓaci kenan. Yanda take bulbula hayaƙin sai kawai yaji yana buƙatar kasancewa da ita. Miƙewa yay ya shige ɗakinsa. Babu jimawa ya fito da allura. A kusa da ita ya zauna tare da kama hannunta kawai ya fara mata. Kan shisha ɗin ta wurgar tare da juyowa a fusace. “Oh har ya baka allurar guban da zaka mun ɗin na mutu ne?”.

Murmushi yayi tare da rungumota jikinsa yana magana ƙasa-ƙasa kamar ba commondo ba. “Haba kema kin san bashi da wannan matsayin, ya sani na kashe uwar yaƴata da hannuna. Never for ever sai dai shi ya wuce. Cool down na miki allurar nan ne dan ki samu nutsuwa musan miya kamata muyi. Dan na jiyo mana komai akan plan ɗin nasa”.

Jikinta ta janye tana mai sauke ajiyar zuciya. Daga haka barci ya fara rinjayar idonta. Wata shegiyar dariya yayi da ɗaukarta gaba ɗayanta duk da tana da jiki badai can sosai ba yay cikin ɗakinsa da ita. Duk tana jinsa, sai dai bata da ƙarfin hanashi. Daga ƙarshe ma allurar na fara mata aiki a jiki da kanta ta fara kai masa kanta. Haka ya shiga yin yadda yaso da ita. Ya kuma tabbatar daga nan har zuwa gobe allurar zata iya kaiwa jikinta, dan haka daren yau na party ne gaba ɗayansa kawai...

□□□□□

Matsanancin ciwon cikin dana farka da shi ya sakani fara fisge-fisge. Tuni na fincike ruwan da aka saka min. A dai-dai nan naji wata muryar da nake da tabbacin nasan mai ita tana ma yaƴan sandan dake bakin cell ɗin da aka sakanin tsawa. Har rige-rigen buɗe ƙofa suke su shigo. Ciwo yaci ƙarfina bamma tantance maza bane ko mata suka ɗaukan, sai da aka shiga da ni mota na iya kallon mutum ɗaya a cikinsu wadda mace ce. Da ga haka na maida idanuna na lumshe gaba ɗaya.

Sama-sama nake jin kai-kawon komai har isarmu asibiti da taimakon da likitoci suka shiga bani. A ɗan maganarsu nake jin wai ina zubar da jini. Daga haka ban sake fahimtar komai ba sai farkawa nayi na ganni kwance a gadon asibiti police mace a gefen gadon da nake zaune. Sannu tayi min, tare da kiran likita. Ya ɗan dudduba ni ya tabbatar ma da yaƴar sandar yana buƙatar ganin mijina ko wani a cikin ahalina. Kai tsaye ta bashi amsa da ina a ƙarƙashin kulawar su ne. Za'a iya sanar musu minene matsalata.

Ɗan jimm likitar tayi kamar mai tunani sai kuma ta ce, “Mijin nawa dai tafi buƙatar gani. In har za'a iya yi mata wannan alfarmar zata so hakan”.

Cikin rashin damuwa jami'ar tace zata duba. Daga haka likitar ta sake fita ni kuma barci ya sake rinjayata. Ban sake farkawa ba sai cikin dare sosai. Na tashi da wata masifaffiyar yunwa. Tun ina juye-juye har na fara kuka da roƙon a bani abinci.

Tsaki yar sandar tayi cikin masifa take faɗin itafa na takura mata na hanata barci, a ina zata samo min abinci yanzu cikin daren nan. Ban iya amsata ba na cigaba da murkususu na kawai. Sai kawai ta tashi ta fita rai ɓace. Tun ina saka ran zata dawo harna fidda rai, ga cikina yay wata irin masifar ƙullewar yunwa na cure waje guda ina hawaye. A hankali wani irin daddaɗan ƙamshi ya dinga ratsa min cikin hanci, tun yana a nesa da inda nake har na fara jinsa a gab-gab da ni. Ƙoƙarin buɗe idanuna dake alumshe nayi jin saukar hannun mutum akan jikina. Bana iya ganin ko waye da ƙyau, sai dai a tsaye yana da tsayi, akwai kuma facemask a fuskarsa, gashi ya ɗaura hular rigar jikin nasa a saman kai ta yanda har ba'a iya gane ainahinsa, dan hatta idanunsa akwai glass.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-eight

58

.....Kamani yay gaba ɗaya ya tada zaune, shima ya kai zaunen tare da sakani a jikin nasa ya rungume. Wani kalar nutsuwa ce ta fara ratsani, irin wadda nake ji a tare da mutum ɗaya kacal a duk sanda ya rungume ni irin hakan. (Tabbas bana tantama wannan Maash ne, Awwab ɗina ne). Na faɗa a zuciyata hawaye masu zafin gaske na gangaro min suka sauka a kan ƙirjinsa, sake ƙanƙameni yayi sosai. Munfi mintuna biyu a haka kafin ya ɗagoni ya gyara min zama da ƙyau, wani ɗan mitsitsin flaks ya ciro a jikinsa mai ƙyau sosai ya buɗe. Sai da ya ɗan kalla abinda ke ciki kafin ya kawosa saman lips ɗina, ganin na tsaya kallonsa ya jinjina min kai alamar na sha.. kamar wadda ake bama umarni a hankali na ɗaura nawa hannun akan nashi dake da handglove na gyara zaman flaks ɗin a bakina da ƙyau, ai ko tunda na kafa kai ban janye bakina ba sai da na shanye shayin dake a ciki mai matuƙar daɗi da kauri duka. A take wata irin zufa ta shiga karyo min tako ina a jikina. Sake kwantar da kaina nai a jikin nasa ina sauke numfashi, na jima a hakan kafin na ɗan

ɗago ina kallonsa. Hannu na kai a hankali saman fuskarsa zan cire facemask ɗin fuskar tasa ya hana hakan ta hanyar riƙe min hannun yana ɗan jujjuya kansa gefe.

Cikin dasashjiyar muryata na ce, “Why?”.

Maimakon bani amsa kafaɗuna ya kama da hannu biyu ya kwantar dani a gadon tare da jamin bargo ya rufa min. Sai kuma ya min nuni dana rufe ido batare da yayi magana ba har yanzu. Babu musu nayi hakan, kamar abin tsafi sai wani irin barci ya sake yin awon gaba da ni da alama dama yunwar ce ta tada ni....

*_WASHE GARI_*

Yana tsaka da aiki a kitchen kusan shidda na safe kira ya shigo wayarsa. Ringing ɗin da yaji wayar nayi ya nema birkita masa lissafi. Dan ya tabbar ringing ne daya saka shi domin mutum ɗaya. Sai ogansa ma nasa daban. Sai dai kuma mai wannan kiran a daren jiya ya gama jin cewar baya ma ƙasar, shima kuma ya shaida hakan. Da ƙyar ya iya ƙundunbalar ɗaukar wayar ya duba. Tabbas shine kuma da no ɗin Nigeria. To mi hakan ke nufi kuma? Rashin samun amsa ya sashi ɗagawa kafin ta tsinke. Yana kaiwa kunne tare da yin sallama aka katsesa da faɗin, “GGC GARDEN yanzu” daga haka aka yanke wayar ƙittt. Shiru yayi yana mai nazari tare da mamaki. Shi jami'in tsaro ne mai matuƙar fiƙra na sirri. Yasan kaɗan da ga aikin mutanen banza tsara komai. To amma kuma tabbas wannan muryar mai number ɗin ce. Kenan mi hakan ke nufi? Wani ne ya kwaikwayi muryar? Bayan ya samu nasarar samun wayar. Ko kuwa dai su Baba prof sunyi BONONO ne rufe ɗaki da ɓarawo kamar yanda yay zato. Sun shuka ne an tone. Kai shi kam dama dai yayi mamaki ace Maash aka rutsa a Dubai. Duk da hakan zata iya faruwa kasancewar shiri ne babba amma kuma idan za'a haɗa 1+1 ai amsa ɗaya zata bada. Dan shima Maash ɗin shegen kansa ne akwai hatsabibanci... Wayar ya sake ɗagowa ya ƙura ma number ɗin ido, da ga ƙarshe dai ya yanke shawarar fara neman ogan nasa ya sanar masa. Yana ko ɗagawa ya zayyane masa komai. Shi kansa ogan nasa yayi mamaki ƙwarai da gaske da jin wai Maash a Nigeria. Amma sai yace ya dakata bari suyi bincike. Yana nan zaune cikin shirin kira da tafiya ba'a cika mintuna biyu ba kuwa ciff ogan nasa yay kiransa yace yaje Maash ɗin ne dai. Rasama abin faɗa Isma'il Kuku yayi. A ransa kam faɗi yace, (anya Maash ɗin nan kuwa ba aljani bane, anya).....

(😂Nima dai Isma'il na fara tsoron Yayan nan namu gaskiya😝😝).

Koda ya isa GGC GARDEN ƙoƙarin sake kiran Maash ɗin yayi, sai dai harta tsinke ba'a ɗaga ba. Sai ma knocking window ɗin side ɗin da yake akai masa. Sauke gilashin yayi, batare da wanda yay knocking glass ɗin yayi magana ba yay

masa nunin ya sakko. Kamar zai yi magana sai kuma ya fasa. Fitowa yay ya kulle motar yabi bayansa. Duk da akwai yɗar tazara a tsakaninsu bazaka taɓa ma tunanin tare suke tafiya ba. Sai dai a ransa yana mamakin a maimakon su bada umarni matsayinsu na jami'ai sune ake bamawa, lallai ƙarfin dukiya na nuna iko a wannan tafiyar. Can cikin vip na garden ɗin ya kaisa, bai kumayi magana ba anan ma ya juya ya fita. Wajen yayi ƙyau sosai, ga haske tako ina kamar rana. Idanu ya ɗan zubama bayan wanda ke tsaye ya juya ma ƙofar shigowar baya. Baƙaƙen kaya ne a jikinsa hatta da hannunsa dake zube a cikin aljihun wando da alamun handglove a tare da su. Hakama kansa yaja hular rigar. Sallama ya sake yi a karo na biyu, zuciyarsa na masa ɗari-ɗarin Maash ɗin ne ko kuwa ba shi ɗin bane. Shiru har fin minti ɗaya kafin ya juyo. A hakan ma fuskar a rufe take da facemask ga gilashi ga hular ta taimaka wajen hana ganin fuskarsa da ƙyau, batare da yayi magana ba ya nuna masa wajen zama shima yana kaiwa zaune. Hannayensa ya harɗe a ƙirji ya zubama Isma'il ɗin ido na tsawon sakanni. Kafin a hankali cikin silent voice ɗin san nan ya furta, “Gaba ɗaya wasan ya canja a gaɓar da banyi zaton fara yaƙin ƙarshen ba.”

A karo na farko Isma'il ya saki murmushi, dan tabbas yanzu ya sake yarda da Maash yake magana. Ajiyar zuciya ya sauke mai nauyi, tare da faɗin, “Ranka ya daɗe wlhy gaba ɗaya zuciyata a ɗari-ɗari take, na kasa gaskata kai ɗin ne ko waninka.”

Hannayensa ya warware da ga ƙirjinsa, tare da kai yatsu biyu saman fuskarsa ya zame mask ɗin zuwa ƙasan haɓarsa. A daƙilallen yanayi ya furta, “Ina Ummie na da Mama da ƙanwata?”.

Mamaki ne ya ɗan kama Isma'il amma sai yay niyyar latsashi. Cikin ɗan nuna firgita ya ce, “Ranka ya daɗe ban gane ba?”.

Shiru yay kamar bazaice komai ba kansa a duƙe, kusan mintuna biyu sannan ya ɗago yana kallonsa. Duk da idanun sakaye suke a cikin gilashi sai da Isma'il ɗin ya dinga jin kaifinsu, dan haka shi ya ɗan rissinar da nashi. Da wani irin taurin zuciya ya furta, “Isma'il ni ba jami'in tsaro bane. Amma brain ɗina da zuciyata na aiki fiye da ta wasu jami'an tsaron dake a cikinku. Ba kuma dan na kasance na daban ba. Sai dai na rayu ne a matsayar ƙin yarda da kowa hatta kaina.”

Kai Isma'il ya jinjina yana mai sake rissinar da kansa. Cike da girmamawa ya ce, “Suna gidana. Ƙanwarka kuma ta haihu namiji. Ina mai farin cikin kasancewa wanda zai fara maka albishir guda biyu. Na haihuwa dana alamomin samuwar lafiyar Ummie. Dan da taimakonta suka fito a gidan kamar yanda Mama ta sanar min.”

Wani shegen murmushi daya saka Isma'il tsayawa kallonsa ya saki, batare da yace komai ba. Sai da ya ɗan bubbuga table ɗin gabansu da yatsa sannan Isma'il ɗin ya kawo numfashi, sai kuma yaji kunya. Ɗauke kai Maash ɗin yayi da faɗin, “Bayan nan fa?”.

Ajiyar zuciya ya sauke mai ƙarfi. “Abunuwa da yawa sun faru a cikin gidan, nasan kuma ƙarin bayani kawai kake son ji, dan in har baka sani ba a yanzu kana da hanyar saninsu ko anan gaba. Sun ɗauke Alhaji, amma abinda na fahimta ba Prof.. bane ba.....”

“Nasan inda yake”.

Ya faɗa a daƙile. Sai Isma'il kawai ya saki baki yana kallonsa. Sannan cikin in ina ya ƙarasa faɗin, “Anyi uwar watsi tsakanin Hajiya Lawisa da Prof...”

Sake sakin murmushi Maash ɗin yayi a karo na biyu, kafin a wani kalar soft voice ya ce, “Miya haɗasu?”.

Tsaff Isma'il ya kwashe komai ya sanar masa. Kafin ya ɗora da faɗin, “Amma ranka ya daɗe naji yana sanarma yaronsa Commondo cewar kana Dubai ya maka tarko, yasa an yanke wutar gidan da kake ciki, da network, da ruwa. Sai kuma gaka a Nigeria. Wlhy ni gaba ɗaya ma sai na raina kaina. Anya yallaɓai baka cancanci zama jami'in sirri ba”.

Maimakon ya amsa masa sai ya miƙe yana mai maida mask ɗinsa. “Zaka iya tafiya, da ga yanzu zuwa asuba zan tura a ɗauka su Ummie”...

Da kallo kawai Isma'il ya bisa, sai da ya ga ya ɓacema ganinsa ya sauke wani nannauyan numfashi yana miƙewa. Kamar ɗazun yanzu ma rakashi akai har mota, yana barin wajen office ya wuce. Dan bazai iya haɗiyewa ba sai ya gana da ogansa....

A ɓangaren Maash ma Isma'il yana gama ficewa ya ɗaga waya yay kira. Cikin bada umarnin ya furta, “Ina son scorpions dake rayuwa a cikin yashi mai zafi kamar guda ashirin nau'i daban-daban daga nan zuwa gobe in ALLAH ya kaimu”. Da ga haka ya maida wayar cikin aljihu batare da ya kashe ba ya shige yʻar bukkar dake a wajen da aka yi ta domin hutawa kawai. Abu ya ɗakko ya fito suka bar Garden ɗin.....✍

Munga idi. Yayanmu kunamai kuma😷? Mi zakayi da shi□? To gaskiya kowa yay ta kansa ni dai ba ruwa na□□□□□□□□□.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page fifty-nine

59

.....Duk wanda yace yayi barci mai daɗi a daren jiya tako wane ɓangare yayi ƙarya. Dan kowa da abinda ya damesa. Daga masu shiryawar har waɗan da aka shirya mawa ɗin. A Maash Mansion dai an samu cigaban isowar Aunty Mama (Aunta Mashi'a) da duk labari ya sameta ta kuma ga komai. Abinda ya tada mata hankali shine rashin sanin inda Ummie take da Paah. Sannan ance Hajiya ƙarama da Baba prof sun bi bayansu suma har yanzu basu dawo ba. Da yake hankalin su Hajiya Mammah ɗin a tashe yake ita da Maman Malika basuyi tunanin bincika gidan Baba prof ɗin ba sai Aunty Mama ɗin ce tai tunanin hakan. Sun ji daɗin jin ya koma gida, itama Hajiya Ƙaramar sai sukai tunanin ko tana asibiti damuwa ta hanata dawowa gidan. Abu na biyu da aunty Mama ɗin tayi shine haɗuwa ita da Uncle Abdullahi da abin duniya yama yawa dan shima dai sai dare ya shigo gidan yanayinsa yasa Maman Malika bashi maganin barci aka samu ya runtsa. Police station sukaje suka fito da duk ma'aikatan gidan da aka rufe. Anan ne suke jin Samraah babu lafiya tana ma asibiti ita. Kasa magana ma Aunty Mama tayi dan ɓacin rai, sai Uncle Abdullahi ne ya balbalesu da masifa. Itama dai sunje asibitin sun ganta. A lokacin tana barci suka gana da likitar dake kula da ita.

Bata basu a ɓoye ba ta sanar musu Samraah nada ƙaramin ciki ne, sai dai akwai ɗan matsala dan yaso fita sai dai ALLAH ya taimaka tana fara bleading ɗin aka kawota asibitin. Sunyi nasarar tsaida shi amma tana buƙatar bed rest gaskiya. Sannan duk wani abu da zai tayar mata da hankali ba'a sonshi. Akwai Ummie da take yawan kira ya kamata tazo asibitin ko hakan zai bata nutsuwa. Sai mijinta shima da suke buƙatar gani.

Sosai Aunty Mama ta nuna farin cikinta da har ya bama Uncle Abdullahi mamaki. Dan shi dai yasan cakwakiyar da akeyi akan batun yarinyar nan a gidan. Amma yaga autar tasu ita ko'a jikinta ma. Bai daiyi magana ba sai da suka fito daga asibitin. Gefen titi ya samu ya faka motar yana kallonta. “Auta wai halan baki san mike faruwa bane? Duk fa wannan tashin hankalin akan batun yarinyar nan ne”.

Murmushin itama tayi tana mai fuskantarsa. Ta ce, “Yaya nasan komai. Sai dai hakan bazai hanani murnar samun ƙaruwar da mukayi ba. Dan koba komai cikin dake jikin yarinyar nan jininmu ne.”

“Amma bata hanya mai ƙyau aka samar da shi ba ai kin sani”.

“Kamar ya?”.

“Fyaɗe fa Awwab ya mata”.

Karo na farko dariya ta suɓucema Hajiya Mama. Ta ce, “Humm yaya kenan, wai ku har yanzu kuna akan keken ɓeran da Awwab ya sakaku kenan? Zuwa yanzu ya kamata ace kun gama haddace halayyarsa sai dai ku bama na waje labari kuma. To wannan yarinyar matarsa ce da gaske. Duk abinda kaji Sheikh Muhammad bin Khalipha Al-Hussain ya faɗa shine gaskiyar magana. Abinda keta kai-kawo kuwa shirine kawai na magauta bana raba ɗayan biyu kuma abokan kaduwancisa ne”.

“To ke ya akai kika sani?”.

“Yaya labari ne mai tsaho, amma bari na gajarce maka shi. Tiryan-tiryan ta bashi labarin komai tun bayan ɗaura aure, ciwon Samraah da kawota asibiti Abuja har zuwa guduwar da tayi ta faɗa hannun Madam Jannifer da sakata amsota da Maash yayi, da kawota gidan matsayin yar aiki kamar yanda ya buƙata. Rasama abin cewa Uncle Abdullahi yayi, dan harga ALLAH zancen ya girgizashi. Sai tausayin yaron ya sake kamashi. Tabbas matarsa ta faɗi gaskiya da tace basu damuwa da damuwarsa sai ayyukansu kawai. Haka ya tada motar jiki a sanyaye suka koma gida.

Sun samu Hajiya Mammah nata masifa akan dawo da masu aiki da akayi, sai da Hajiya Mama ɗin ta mata bayanin sune suka je suka saka aka sakosu. Cikin masifa Hajiya Mammah ta ce, “Amma banda waccen shegiyar yarinyar ko?”

“Saboda mi Adda?”.

“Saboda bata da gaskiya, ita dake matsayin yar jarida a Kano ubanmi ya kawota nan? Dan ko kunsa an fiddota wlhy sai na maidata. Sai ta faɗi inda Mu'azz yake”.

“Addah kina kwantar da hankalinki idan abu ya faru dan ALLAH. Samraah bata da hannu akan kidnapping Yaya sam saboda ita ɗin matar Awwab ce da gaske, kuma shine yasa na kawota nan gidan a wancan lokacin” tsaff ta kwashe labarin komai ta basu kamar yanda ta bama Uncle Abdullahi. Gaba ɗaya falon yay wani irin tsitt tamkar ruwa ya cinye kowa. Hatta da Baba prof dake ƙoƙarin shigowa ƙamewa yay a ƙofar duk da ya jima da yarda da hakan, ya kuma ji bayanin Sheikh Muhammad ɗin, amma jin komai a bakin autar tasa da yanda Maash ya shigo da yarinyar gidan sai yafi jin labarin kamar shine ainahin na gaskiya. Daɓar Hajiya Mammah ta kai a kujera, yayinda Malika da Azizat suka fasa ihu a tare. Da ga ƙarshe ma Azizat zubewa tai a wajen wai ta suma.....

□□□□

Wani irin kallo take ma jikinta da Commondo dake a gefenta kwance. Bama tasan lokacin data fasa ihun masifa ba a kanshi. Firgigit ya tashi fuska a yatsine. Kafin cikin jin haushi ya ce, “Haba Lawy baby, miyyasa kike abu kamar wata ƙaramar yarinya. Ina barci na mai daƒi da nishaƒi kin wani tadani”.

“Nayi ƈin, amma baka da hankali ko? Mika mun?”.

Dariya ya kwashe da ita harda ƙyaƙyƙyewa. “Ka jimun yˇar iska. Mi kika kawo kanki na miki dai. Naga keda kanki kika dinga jawoni kina roƙon nayi. Shegiya kinji mazan ƙwarai ko. To miye ma in nayin, naga dai har yanzu matata kike. Kona sake ki ne? Karki manta da aurena kika je kikai aure. Dan haka inada hakki a kanki. Yanzu ba gashi kin tashi fresh ba, basar kawai hajjaju kije kiyi wanka muzo mu tattauna abinda ya dace kafin shegen tsohon nan yasan ina mahaukaciyar matar can take. Dan mune yafi cancanta mu samota mu haƌa da Mu'azz dan uban Maash tsoffinsa duka na hannunmu ai dole ya bamu abinda muke so.”

Takaicinsa ne ya hanata yin magana. Batare data tanka masa ba ta miƙe ƙawai ta hau saka kaya. Shiko dariya kawai yake kwasa ta wulaƙanci. Fuuu ta fito a ƌakin sai jin tashin motarta yaji. Baki ya taɓe dan ko'a jikinsa, shi dai ya samu abinda ya ke so. Kuma ya jisa fiye da yanda yay fata. Ya kuma san da kanta zata dawo dan yanzu a tafin hannunsa take neman mafita kawai ce hanyar binta....

□□□□

“Isma'il lafiya na ganka haka kamar wanda aka koro?”.

“Humm oga am sorry, ai badan ma na riƙe kaina ba zaka iya ganina a fiye da hakan. Tabbas Maash yana gari, dan daga wajensa nake yanzu. Anya mutumin nan bashi da aljanu? Shifa aka nuna bashi da lafiya a asibiti sannan da kunne na naji prof.. na zancen yasa a yanke wutar gidan da yake da network da ruwa, aka kuma zagaye gidansa da jami'ai. Kuma yana da tabbacin yana a cikin gidan fa. Kuma mu kammu mun tabbatar ya shiga Dubai a shekaran jiya. Amma gashi yau alamu sun nuna a Nigeria ya kwana. Wlhy ni a karan kaina da nake amsa sunan jami'in tsaron sirri al'amarin sa ya fara bani tsoro. Irin waƌan nan ne idan suka zama cikin jami'an tsaro suke aiki mai ban mamaki, idan kuma suka kasance criminals suke mummunar ɓarna dan suna da matuƙar wayo da fiƙra. A yanzu haka bana raba

ɗayan biyu dama yasan da shirin duk za'a masa haka a Dubai ɗin shine ya basu ƙafa, dan ya tabbatar min yasan inda mahaifinsa yake ma”.

“What?!”.

“Wlhy oga haka yace ya sani, kaga tabbacin duk motsinsu kenan yana sane. Sai dai abinda ya ɗan ruɗar da ni anan prof ba shine yay kidnapping Alhaji Mu'azz ba, kuma bana jin Maash ɗin zai yi hakan saboda kisan da akama drivern. Anya kuwa matar nan ko Commondo ɗin nan basa cin dundumiyar prof ta ƙarƙashin ƙasa?, dan bana raba ɗayan biyu Alhaji Mu'azz na hannunsu”.

Nannauyan numfashi ogan nasa ya sauke dan tabbas maganar yaron nasa abar a duba ce. Idan kuwa haka ne lallai wannan wani point ne da zaisa su sami Commondo ko Hajiya Lawisa a hannu. Dan dolene su kama ɗaya a cikinsu. Lokacin da zai fara motsi shima yayi a garesa. Maganar ɓoye kai da ainahin matsayi ta ƙare. Sun cigaba da tattaunawa musamman akan takun da Maash ɗin yazo da shi. Shi kansa ogan nasa kai kawai yake jinjinawa da hatsabibancin yaron. Dan tunda suka fara aiki akan wannan case ɗin matsayin jami'an sirri da yawan bayanai shine ke basu kafin su su binciko. Dan ba ƙaramar gudunmawa yake basu ba akan aikin nan, hatta baza mutane cikin family ɗin shine ya bada shawarar da ƙirƙirarta. Kuma har yanzu bai san ainahin shine ogan ba saboda wani dalilinsa da ya barma kansa sani. Shi kansa Isma'il ɗin sai kwanan nan ya sanshi, kuma shima bai san ainahinsa ba balle alaƙar data alaƙantashi da Maash ta zahiri.....✍

To oga kai waye? Muma ya kamata mu sani ai koya kuka ce?.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty

.....Ba ƙaramin shock ta shiga ba lokacin da take shigowa gidan taci karo da duk ma'aikatan sun dawo gida. Ga batun auren Maash da Samraah zance dai ya fito. Ko kallon inda Baba prof yake batayi ba. Ita ta duba Azizat tai mata allura aka maidata ɗakinta. Tana ƙoƙarin tashi ta shige yan sandan dake bincike akan ɓatan Paah suka zo gidan kusan tare da Uncle Abdullahi da ya fita. An samu wayar Paah da sukai tracking, sun sameta a gaba kaɗan da inda aka sami gawar drivern sa, da alama an yardata ne daga baya. Dan a yanzu haka suna kan yin wani bincike na duk inda aka shiga da wayar a jiya kafin a yardar da ita suna fatan samun nasara. Sannan an samu sayin yatsun hannu har na mutum uku a jiki shima suna kan bincike, shiyyasa zasu bibiyi duk inda yaje ɗin...”

Tamkar jira Baba prof keyi cikin nuna jin daɗi ya ce, “Idan ko hakanne officer ya kamata a fara da duka sayin yatsun hannayenmu mu da muke gidan nan, tunda daga nan ya fita zuwa gidana. Can ma kuje ayi komai yanda ya dace kafin shegun su farga su ɓadda sawu” ya ƙare maganar yana wani sakin murmushin mungunta da kallon sashen da Hajiya ƙarama ta ke. Da sauri ta gyara yanayinta tana mai watsa masa wani mugun kallo ta ɗauke kanta. Sai ya sake sakin wani murmushin da cije lips ɗinsa. A ransa yace (ƙaramar shegiya zanyi maganinki. Sai na dafaki a tsaye ai. Zaki tabbatar da ni Uban ubanki ne a iya hatsabibanci).

Ɗari bisa ɗari ɗan sandan ya yarda da batun Baba prof ɗin, sai dai yace zasu je su dawo dan babu kayan aiki a tare da su yanzu. Duk kuma wanda ya fita daga gidan zuwa kafin su dawo yana cikin suspect nasu. Daga haka suka fice.. Fitar tasu bai fi da mintuna ba wayar Hajiya Mama ta fara tsuwwa. Ganin mijinta yasata ɗagawa cike da zumuɗi. Duk idanu suka zuba mata. Wani irin miƙewa tayi cike da tsantsar farin ciki ta furta, “Alhamdullahi ALLAH mun gode maka. Yanzu haka kuna a cikin gidan nashi kenan?”.

“To Masha ALLAH muna zaman jiran ji daga gare ku, dan fatanmu kawai asan ina Awwab yake yanzun”. Ɗan jim tai alamar saurare kafin ta yanke kiran ta dubi duk wanda ke a falon da wani irin zaƙuwa ta ce, “Ana fatan samun Awwab a cikin gidan nan. Ashe an katse masa duk network da wutar gidan ne da ruwa. A yanzu haka Daddyn Irfan ya tabbatar min sunata shiga da fitar ganin an ɓalle ƙofofin gidan, idan har yana a ciki zuwa dare zasu taho Nigeria da shi”.

Wani irin makirin murmushi Hajiya Ƙarama ta saki tana kallon Baba prof da zufa ta gama jiƙema gaban goshi. Da yatsa ta masa alamar 1-1 tana kashe ido ɗaya. Sai kuma ta miƙe zumut tana faɗin, “Alhamdullahi, mun godema ALLAH”. Yanda tayi ɗin ya saka kowa maimaita kalmar Alhmdllh ɗin Maman Malika da Hajiya Mama harda rungume juna. Ita kanta Hajiya Mammah ta nuna farin cikinta duk da har yanzu batun auren nan na Maash ya kasa haɗiyuwa a wuyanta. Zancen Baba prof ne ya katse musu murnar tasu.

“Anya kuna ganin ya kamata Awwab ya dawo ƙasar nan babu iyayensa a gidan nan, babu matarsa, babu Fahad?”.

Gaba ɗaya murnar tasu ta koma ciki, dan gaskiya Baba prof ɗin ya faɗa. Wayarsa ya ɗauka yana miƙewa da faɗin, “Abdullahi bamuga ta zama ba muje ko”.

Miƙewa Uncle Abdullahi yayi yana faɗin, “Baba bara na ɗan canja kaya” ya nufi hanyar sashensu, yayinda Hajiya ƙarama ta saki murmushi dan ta gane wayo ne kawai ya sashi barin gidan. Duk da kuwa wanda aka lissafa ɗin duk bai san inda suke ba. Amma jin za'a buɗe Maash yake son zuwa ya nemo mafita....

Uncle Abdullahi na shiga bedroom ɗinsa ya ɗakko wata yar ƙaramar waya. Kunnawa yayi sannan yay kira. Ana ɗagawa. Daga can cikin bada umarni ya ce, “Ku saki yaran nan daga nan zuwa awa ɗaya da kwata. Sai dai ku tabbatar basa a hayyacinsu”. Daga haka ya yanke wayar yana wani makirin murmushi. Kasheta yay gaba ɗaya ya maida inda ya ɗakkota sannan ya canja kayan ya fita kamar bashi ba...

Bashi kaɗai ba, a ɓangaren Hajiya ƙarama ma a hargitse ta wuce ɗakinta. Kira ta dannama Commando. Yana ɗagawa zai fara mata surutun banza a tsawace ta ce, “Akwai matsala fa. Mun manta wayar nan duk mun taɓata da hannayenmu kafin a jefar da ita, sannan bamu kasheta ba. Yanzu yan sanda sun samo wayar kuma shirinsu shine bibiyar sayin yatsun mutane uku da suka gani a jiki. Kaga kuwa akwai nashi, nawa, naka. Ga shi wannan tsinannen tsohon yace a fara da nan gidan kuma nasan danni yayi haka. Sai dai da yake bani da hakkin matsiyaci yanzu ake sanar ma Mashi'a ana ƙoƙarin buɗe gidan Awwab ashe sakawa yay aka yanke masa wutar gida da network da duk wani abinda zai iya tabbatar da yana a gidan sannan yasa jami'an tsaro suka zagaye gidan kamar dai yanda ya taɓa sawa akama Shamsu. Shine ya wayance da wai bai kamata Awwab ya dawo babu iyayensa babu Fahad ba. Kaji makiri fa, nasan neman mafita ya tafi dan in har aka samu Maash a gidan nan ya kuma fito a yau kashinsa ya gama bushewa”.

Yar dariya commondo ya saki daga can da faɗin, “Cakwakiya kenan. Yanzu yaya za'ayi to?”.

“Ya kamata dai musan mafita kam. Dan in ba hakaba tofa wasan zai canja salo in har Awwab ya fito. Kai dai kasan halin mutumin nan kansa kawai ya sani. Duk kuma yanda zai yi yaga ya fidda kansa a wannan gaɓar zai yi ɗin tunda babu wata alama data tabbatar da shine ya ƙulla duk wannan harmutsin jiya zuwa yau ɗin. Shi kuma Awwab ba kanwar lasa bane ba”

“Ya kamata kizo ki sameni. Dan bamuga ta zama ba.”

Daga haka ya yanke kiran.....

□□□□□

Alhamdullah jikin Abba yayi sauƙi, yan Gwarzo da labarin komai ya sama suma ta ɓangaren su Gwaggo Gudidi da ɓangaren mahaifin su Samraah ɗin su kawu Musa kenan duk sun shigo ganinsa. Basuyi ƙasa a gwiwa ba kuma suka haɗa community zuwa gidan Sheikh Muhammad bin Khalipha Al-Hussain. Sai dai basu sami ganinsa ba ance ya wuce Lagos. Haka dole suka haƙura suka koma gidan Abba da shima aka sallama. Sun sake zaman meeting kan zuwa can Lagos ɗin. Dan har yanzu basu san halin da Samraah take ciki ba su. Sun kira no bata shiga, an kira ta Hafizzullah duk ba'a samu. Ga Musaddiq da yaga komai a Media yanata faman kiransu cikin tashin hankali. Dan har yana tabbatar musu da shifa zai dawo gida. Sai da sukaita tausarsa dai....

A yayin da su suke cikin wannan damuwa da tashin hankali ita Mom ranta fari ƙal. Sai ma siɗaɗewa tai tabar gidan zuwa gidan Ummanta. Cike da nishaɗi sukaita tattauna batun. Duk da zaka iya fahimtar tsantsar hassadar su a cikin zancen game da jin wai Samraah Maash ta aura. Sai da suka gama ƙulle-ƙullen sharrinsu sannan suka koma kan tattauna batun Baby dake matuƙar ɗaga musu hankali. Abu kamar wasa kwanaki nata sake tafiya. Bata ba mijin nata babu batun zuwa makarsu bayan sun gama baje gari da zance. Dan su har yanzu hankalinsu bai fara basu akwai babbar matsala ba, balle su fara ƙoƙarin neman ahalin mijin baby ɗin. Bata jima ba ta koma gida tunda ta baro shi cike da mutane. Sai Halime baiwar ALLAH dake ta fama da kanta keta hidima da su ga hidimar Abba shima. Dan ma su Aunty Zakiyya na tayata.....

□□□□

A guje ɗaya daga cikin securitys ɗin ƙofa yazo yana sanar ma su Hajiya Mama dake cikin gida duk da ita tana ma ƙoƙarin wucewa duba jikin Samraah ne ita da yaranta. Haka itama Hajiya ƙarama ta fito ne zata wuce wajen commondo amma da shirin asibiti kamar can ɗin ta nufa.

Yanda jikinsa ke rawa ya gagara iya cewa komai ya saka Hajiya Mammah daka masa tsawa. Da ƙyar ya iya nutsuwar shaƙar numfashi da fesarwa sannan ya sanar musu ga wata mota ta ajiye su Fahad a ƙofar layin nan. Yanzu nan securitys ɗin farkon layi suka kawosu wasu kuma sunbi mai motar. Kafin ya gama rufe baki ma'aikatan gidan suka shigo ɗauke da su Fahad da ke cikin yanayin barci. A saman kujeru aka shinfiɗar da su, hakan yasa kowa yin cirko-cirko kawai ana kallonsu. Musamman ma Hafizzullah da Hajiya Mama ta zubama ido. Sai zuwa can tai ƙarfin

halin tambayar shi wanene?. Maman Malika ce ta bata amsa da bayani gamsashe. Murmushi ta saki tana mai jinjina kanta.. Sai kuma ta juya ta zaro waya tai kiran Baba prof. Kamar wanda ya daburce ya shiga amsa mata harshe a cuɗe, ita harma yanda ya ruɗe ɗin yaso bata mamaki. Amma dai batace komai ba.

Babu jimawa kuwa sai gashi ya iso. Dai-dai nan suma yɾan sandan nan suka dawo. Su kansu sunyi mamakin dawo da su Fahad ɗin, duk da dai su dama ba'a ma san ainahin abinda ya faru da su ba. Tunda aka fara dambarwar nan babu su a gidan. Hajiya ƙarama ce ta dubasu domin tabbatar da lafiyarsu.

Yanda ta ɗago tana wani jijjiga kai ya sakasu zuba mata ido. Cikin nuna damuwa ta ce, “Babu abinda ya samesu da alama ma shaye-shaye sukayo.”

“Shaye-shaye?!!”.

Kusan atare kowa na falon ya faɗa. Sai da taji zuciyarta tayi wani irin tsargawa amma ta dake tace eh. Masifa Hajiya Mammah ta fara akan Hafizzullah ne ya koya ma Fahad to, dan Fahad dai baya shaye-shaye duk sun san da wannan. Babu wanda ya iya cewa komai a falon. Sai Baba prof dake a cikin ruɗani. Sai kuma Uncle Abdullahi daya kafe Hajiya ƙarama da kallon mamaki. Dan a wannan gaɓar dai shi shaidane tayi ƙarya.. Ma'aikatan gidan aka kira suka ɗaukesu suka maida sashen Fahad ɗin, daga haka kowa ya kama gabansa tunda su ana ganin babu wata matsala a tattare da su sunje sun shawo kayan maye ne.....✍

Uhhmmm Uncle Abdullahi??? To bance dai komai ba□□

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

61

.....A hankali na dinga buɗe idanuna da sukai min matuƙar nauyi, ɗakin na fara bi da kallo. Take komai ya shiga dawo min dalla-dalla. Ciki harda abinda ya faru a daren jiya. Waige-waige na fara yi, sai dai babu ko alamar wanda nake son ganin, sai yʻar sandar nan kaɗai zaune a kujerar gaban gadon da nake tanata zabga game a waya. Wani irin rauni naji zuciyata tayi, dan na fahimci tabbas nayi mafarki ne a daren jiya kenan. A cikin mafarki Maash ya kawo min ziyara harda shayar dani shayi mai daɗi. Hakan na nufin koda bama tare zukatanmu na tare. Idanun kawai na maida na kulle, sai da na ɗan sake jimawa a hakan kafin na yunƙura na tashi zaune. Dai-dai nan Nurse ta shigo. Da sauri tayo kaina batare data damu da yʻar sandar nan ba. Zanyi salla nace mata. Babu ko musu ta kamani zuwa bayi. Ita ta taimaka min nayi al'awar ta sake fito da ni. Ganin bazan iya tasowa ba ina ganin jiri tace nayi sallar a zaune. A zaunen kuwa nayi ta, ina idarwa na zame a wajen na kwanta dan babu abinda kuma nake buƙata yau sama da waje mai sanyin. Dai-dai nan Alaja ɗin nan data ɗakkoni daga hannun Madam Jannifer wadda Mama ta sanar min autar su Paah ce ta shigo da sallama. Likita biye da ita sai wasu yara masu ƙyau sosai daka gansu kaga yʻan hutu. Wani kalar faɗuwa gabana yayi, babu shiri na zabura na tashi tsaye. Da sauri doctor ɗin ta kamani ta zaunar a bakin gadon tana faɗin, “Please calm down kada ki ruɗar da kanki. Dan yanzu yin wani babban yunƙuri a gareki haɗari ne..

Murmushi itama Alaja ɗin tai mun, tare da zama a kusa da ni ta rungumoni jikinta. “Cool dawn my Daughter cool down.”

Sai a lokacin na sauke ajiyar zuciya. Zancen Yaya Awwab na wancan ranar na dawo min akan batun shine ya sakata ta ɗakkoni ai da ga gidan Madam Jannifer. Gaisheta nayi, ta amsa min da kulawa, tare da tambayata jikina. Na tabbatar mata da Alhamdullah. Suma yaran suka gaisheni. Amsa musu nayi, tare da miƙa musu hannu cikin ƙarfin hali ina murmushi. Babu musu kuwa duk suka zo gareni.. sai da taga suna neman haye min jiki ta dakatar da su. Baki suka dinga turawa cikin shagwaɓa. Ni sai ma suka bani dariya dan su duka sun kai kusan 12years da 10years. Amma Abinka da rainon madara.

Hajiya Mama da kanta ta bani abinci naci, doctor ta shigo ta dubani ta bar Nurse ta bani magunguna sannan suka fita. Duk yanda naso daurewa na kasa. Sai da na tambayeta Ummie na lafiya, sannan anga Paah. Aunty Falaq kuma ta haihu?.

Sai da tayi ɗan jim kafin ta saki murmushi da faɗin, “Everyting Alhamdullah daughter. Yanzu ki kwanta ki huta, idan kika samu lafiya duk zaki ji komai, za kuma ki gansu.”

Kaina na ɗan jinjina mata kawai. Ina son tambayar ta Maash ko ya kira waya amma ina jin kunya. Dan ban san yanda zata fassara al'amarin ba tunda koba komai matsayin suruka take a wajena. Haka na haƙura na kwanta ina mai lumshe idanuna....

□□□□□

Gaba ɗaya komai ya ida daburcewa Baba prof.. suna isa gida yace driver ɗinsa ya biyosa dan tun a can Maash Mansion suka rabu da Uncle Abdullahi. Ya turashi wani waje akan shima zai je wani waje. Cikin rawar jiki kuwa ya bisa har falo. Wasu azababbun maruka har huɗu ya dinga sakar masa. Kafin ya shaƙe mas wuya ya buga kansa da bango. Wahalalliyar ƙara ya saki jikinsa na rawa. Sai da prof yaga numfashinsa na barazanar barin jikinsa sannan ya wancakalar da shi gefe aiko ya faɗa akan hannunsa ji kake ɓasss alamar karaya. Wata ƙarar ya sake saki da ko fita batayi, sai ga zufa na wanke masa jiki. Babu ko tausayi a idanun Baba prof ɗin ya take hannun daya karye ɗin tare da duƙowa kansa ya sake shaƙar wuyarsa ya ce, “Ya akai waɗan can yaran suka fito??”.

“Wlhy! Wlhy ban sani ba yallaɓai. Na rantse da ALLAH inda kace na kaisu can na kaisu. Kuma ko daren jiya na kai musu abinci. Yau ne kawai ina shirin fita da safen nan zuwa wajensu kace min zamu fita shine na bari akan sai in mun dawo naje ɗin. Amma wlhy ban san tayaya akai hakan ba. Ban san wanene ya fito da su ba, babu kuma wanda na saka ya tayani aikin balle nace wani yaci amanata”.

Sake falleshi da mari yayi. Ya mutsika hannun da ƙafa har sai da ya saki fitsari. Cikin azababbiyar murya ya ce, “Idan baka faɗa da arziƙi ba zaka faɗa ta tsiya ai dan ubanka. Sai kayi dana sanin sani na”. Ya ƙare maganar yana kai waya kunnesa. “Commondo ka sameni yanzun nan a gida”.....

Kallon Hajiya ƙarama da ke tsaye Commondo yayi, cikin taɓe baki kasancewar taji komai ta ce, “Wannan wawan fa ya fara haukacewa wlhy. Jeka dai ka jiyo mana mike faruwa zan jiraka. Dan nina a haukacen nake. Dolene fa yau muyi wani motsi”.

Kamar Commondo zaiyi magana sai kuma ya fasa. Miƙewa yay yana murmushi, sai kuma ya kai mata runguma ta kauce tana harararsa. Dariya ya kwashe da ita yana ajiye karan sigarin hannunsa a ɗan bowl ɗin daya tarasu da yawa ya fice. Raka bayansa tayi da harara itama tana kaiwa zaune. Wayarta dake ringing ta ciro a jaka tana kaiwa kunnenta. Bayan sun gaisa ta ce, “Jannifer ki kasance cikin shiri fa, da zarar na tura miki text ko na kiraki ku shiga gidan. Dan ina gama jin cikin wawan nan shima yanzu aikinmu zai fara”.

“Baki da matsala hajjaju na. A yanzu haka na shirya tsaff ni da yarana”. Jannifer ta faɗa daga can cike da nishaɗi. Wayar Hajiya ƙarama ta yanke itama tana murmushi. Dan ita kaɗai tasan nata plans ɗin, daga Commondo har Prof a tafin hannunta suke.....

A ɓangaren Commondo yana isa ya samu Baba prof cikin bikitaccen yanayi, ga driver ɗinsa kwance a tsakkiyar falon hannu ya kumbura sosai, bawan ALLAH har yayi sumar wahala. Kallo ɗaya commondo yay masa ya ɗauke kansa. Kan Baba prof ya maida yana mai faɗin, “Ranka ya daɗe gani”.

Wata irin iska mai masifar nauyi baba prof ya furzar. Kafin cikin shaƙaƙƙiyar murya ya ce, “Commondo akwai matsala. Wannan wawan ya jiƙa mana aiki ɗaya”.

“Aiki? Wanne kenan a ciki ranka ya dade?”.

Kallon Commondo ɗin yay da juyayyun idanunsa ya furta, “Yaran nan sun kuɓuta. Fahad da ƙanin yarinyar nan”.

“What?!!”.

Commondo ya faɗa yana wani miƙewa. Dan shi kansa yanada babban target akan Fahad a daren yau. Dan tunda Prof ɗin ya sanar masa suna a hannunsa sune farkon plan nashi. Hannu baba prof ɗin ya yarfar shima cikin zafin rai ya ce, “Wai mike shirin faruwa ne? Tabbas ana bibiyar bayanmu”.

“Yallaɓai waye zai bibiyi bayanmu amma? Kafa ce Maash yana ƙarƙashin ikonka shi da jarababben PA ɗin nan nashi. Yarinyar nan tana asibiti a ƙarƙashin kulawar likita da jami'an tsaro. To kodai Mahaifiyar Maash ɗin ce? Dan tabbas ina ji a jikina matar nan ta samu lafiya.....”

“Noooooooooo!!!! Bazai yiwu ba Commondo bazai yiwu Ummu-Hidaya ta taɓa samun lafiya ba har sai idan nine naso hakan. Kuma zanyi hakanne a gaɓar dana shimfiɗe gawawwakin yaranta biyu a gabanta na durƙusar da ita bisa gwiyawunta ta damƙa min dukiyar da tai min gadara a kanta sannan, dan banaso Ummu-Hidaya ta mutu yanzu. Sai ta wulaƙanta, ta rasa inuwaf raɓawa taji sanyi. Idan har kuma wani ya bata wannan inuwar wlhy sai ta gwamci GARA RANA DA ITA...”

Kai kawai Commondo ya jinjina masa, sai kuma cikin sauke numfashi ya ce, “Banƙi ta takaba oga. Amma yakamata fa zuwa yanzu mufara tunani irin na mutane guda biyu. Idan ba haka ba taya akai ta gane hanyar da zasu gudu a ranar? Sannan da suka gudun shi wanda ya taimakesu wanene shi?. Oga akwaifa tufƙa da warwara a al'amarin nan na wannan karon. Anya kuwa? Anya Maash bai baka ƙafa ba? Ka kuwa tabbatar guy ɗin nan zai yarda ya faɗi ƙasa irin haka da sauri. Maash ba ba wawa bane kansa na aiki fiye da gudun sakannin agogo. Ina baka shawarar kayi bincike shin da gaske ne har yanzu Maash na'a gidan can? Hakama PA ɗinsa. Idan

har mun samu wannan tabbacin to dolene a cikin yaranka bayan Maash akwai wanda yasan wani abu kuwa. Ko kuma dole mu yarda Ummu-Hidaya ta samu lafiya. Dan kowowar su Fahad gida kam akwai ayar tambaya akai....”

Kasa magana Baba prof yay, sai idanu da ya tsurama Commondo tamkar mai nazarin zantukansa. Jirin dake neman yadda shi ƙasa ya sashi kaiwa zaune. Hannunsa har rawa yake wajen ƙoƙarin ɗaukar wayarsa. Danne-danne ya shiga yi tare da kai wayar kan kunensa. Sai dai layin ɗaya kira yaƙi shiga. Sake gwadawa yay har sau fiye da goma amma bata tafiya. Kallon Commondo ɗin yayi cikin ɗan rikicewa.

Kafin ma yay magana Commondo ya ce, “Miya faru? Waka kira?”.

“Zain bin Abideen. Kuma layinsa yaƙi shiga. Dole ne nai shirin tafiya Dubai daren yau da sunan duba jikin Awwab”.

“Shawara mai ƙyau sir”.

Commondo ya faɗa cike da bashi ƙwarin gwiwa. Daga haka suka cigaba da tattaunawa. Bayan sun kammala Commondo ya ɗauki drivern na baba prof ya fita da shi zuwa mota. Shi kuma sai ya miƙe yana mai cigaba da neman number Zain bin Abideen. Ganin bazai samu ba yay kiran airport cewar yana buƙatar ticket ɗin Dubai. Sun tabbatar masa yau jirgi bazai tashi ba sai gobe dan sunada matsalar hazo. Bai damu ba dan a haukarsa yana da isashen time ɗin kaiwa goben zai dai cigaba da neman Zain....

□□□□□

A ɓangaren Maash kamar yanda ta faɗa bayan sallar la'asar shi da Hayatu da isowarsa ƙasar kenan suka ɗunguma zuwa gidan Isma'il Kuku. Lokaci Ummie na zaune bayanta goye da jinjirin Falaq da Mama taima wanka. Yayinda Falaq ke kwance kanta a cinyar Ummien tanata mata surutu akan Awwab da Fahad Ummie na murmushi kawai dan bata iya doguwar magana. Da ga Maash har Hayatu sumar tsaye sukai. Dan harga ALLAH shifa Maash ba yarda yay da maganar Isma'il ba ɗazun. Duk da yasan kaɗanne daga hukunci UBANGIJI ace Ummien ta samu lafiyar. Duk da dai tun kwanaki ya ɗan so gano wani abu game da ita amma taƙi bashi kowace irin ƙofa. Wani kalar tsuma jikinsa ya farayi jijiyoyin kansa na miƙewa lokacin da take kai hannu saman kan falaq ɗin ta shafa tana Murmushi. Cikin karyayyen harshenta ta ce, “Muhammad ɗina bai canja ba dai”.

Yʼar dariya Falaq ɗin tayi da faɗin, “Tabb Ummie ai Yayana bazai taɓa ya canja ba ALLAH. Kinga yanzu yʼan gidan nan duk tsoronsa suke fa. Shi dai kinga sai ya gadama in kayi magana goma ya amsa maka ɗaya. Baka isa gane ainahinsa b....”

Ta kasa ƙara sawa sakamakon kaiwa ƙasa da Maash yay rijiff.....✍

Zazzaɓi□□□□□.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-two

62

.....A firgice duk suka juya suka kallesa. Da ga Ummie har Falaq sai da suka ji shock, bare ma Mama Balki dake kitchen tana haɗa musu abinci dan babu wanda yaji motsin shigiwarsu. Jikin Ummie rawa ya fara yi, duk ta daburce, ƙoƙarin kwance Babyn bayanta take da alama so take ta koma yanayinta na da amma Mama Balki ta riƙe hannunta. Kuka ta fashe da shi tana mai girgiza mata kai. Ta ce, “Dan ALLAH Aunty karkiyi haka. Kada kice zaki cigaba da ɓoyema Alhaji ƙarami wannan ni'imar. Ɗan ZAKI ya riga ya girma aunty. Wannan ba Muhammad Awwab ɗin da kika sani bane da zaki iya zama da yanayin wahala domin bashi kariya. Wannan na yanzu ke zai bama kariya da ƙarfin ikon ALLAH”.

Wani irin kuka Ummie ta fashe dai-dai Maash na kai goshinsa ƙasa yay sujidar shukur. Ya jima dirƙushe a hakan shi da Hayatu da tuni ya bisa shima yayi. Yana ɗagowa Hayatu ya faɗa jikinsa ya wani kalar rungumesa yana sakin kuka tamkar ba Hayatu ba. Ca yake “Yayanmu Ummie ta dawo garemu. Ummie ta dawo? Ummie ta dawo Yayanmu. Dan ALLAH kar kuce mafarkin dana saba yi ne”. Sai kuma ya sake ƙanƙamesa kamar yanda shima Maash ɗin ya wani matsesa a jikinsa dan gaba ɗaya ma shi baya a hayyacinsa.

Karan farko Ummie ta share hawayenta tare da sakin Murmushi tana mai miƙewa. Goyon Babyn ta gyara sannan ta nufesu. A hankali ta kamo kan Maash ta

rungume, tare da riƙo hannun Hayatu ta sumbata. Sai kawai ta sake fashewa da kuka. Da gudu itama Falaq ta taso ta rungume Ummie. Miya rage, itama kawai sai Mama Balki ta nufosu. Sun jima a haka suna kuka su dukansu. Yayinda idanun Maash suke a rufe har yanzu dan shi babu ɗigon hawaye a cikinsu. Sai dai jijiyoyin kansa sunyi wani kalar masifar tashi dama na illahirin jikinsa kasancewar rigar jikinsa mai ƙaramin hannu ce. Hatta gashinsa duk sun mimmiƙe.

Wani irin sakin Hayatu yayi ya damƙe Ummie ya rungume tare da sakin kuka mai ƙarfin gaske. Abinda Hayatu da Fakaq basu taɓa gani ba kenan tunda suke a rayuwarsu. Gara Mama Balki ita tasan ƙuriciyarsa. Duk da Maash tun yana yaronsa duk abinda kaga yama kuka lallai wannan abu ya kai intaha kuwa. Fashewa suma sukai da kukan Hayatu na kama hannun Falaq suka shige bedroom suka rufo. Itama Mama Balki dake kuka kamar ranta zai fita sai kawai ta wuce kitchen da sassarfa...

Kuka sosai Ummie keyi da Murmushi a lokaci ɗaya tana mai shafa kan Maash dake kwance a kan ƙirjinta. Sai kuma a hankali ta fara raira masa waƙar da take masa lokacin yana ƙarami. Tare da ɗago kansa tana kama kumatunsa duka biyu ta ja. Dariya kuwa ya saki irin wadda da yawan mutanen da suka sanshi zasu iya rantsuwar basu taɓa ganin yayi ba. Itama Ummien dariya ta fara tana dungure masa kai da jan hancinsa sannan ta fara goge masa hawayen da manyan yatsun hannunta biyu. Sai da ta gama taass sannan ta jingina goshinta akan nasa tana murmushi.

“U...m...m...ie”.

Ya kira sunanta a wani irin rarrabe.

Da harɗaɗɗiyar muryarta ta ce, “Na'am Muhammad Awwab ibn Ummu-Hidaya Ibrahim”.

Dariya ya sake yi da rungumeta da ƙyau. Dan sunane da yake kiran kansa da shi yana yaro a duk sanda ya fahimci Paah ya ɓata mata rai. Duk da tana ƙoƙarin ganin basu fahimta ba amma ƙulafucin Awwab sai ya gano. Dan ko yaya ya ga fuskarta ta canja yata bin ƙwaƙwƙwafinta kenan har sai yasan waye ya ɓata mata ran. Idan Paah ne bazai sake masa magana ba. Zai kuma ce sunansa ya koma Muhammad Awwab ibn Ummu-Hidaya Ibrahim...

Sake ƙanƙameta yay da faɗin, “Da gaske ba mafarki nake ba kamar yanda na saba Ummie na?”.

“Ba mafarki kake ba my heartbeat. Ummien ka ce. Itace a gabanka. Kayi haƙuri Muhammad, kayi haƙuri. Nayi komai ne dan ku. Na karɓi komai ne dan ku. Nayi haƙuri da komai dan ku. Duk da bani da tabbacin zaku rayu ko ni na rayu har zuwa wannan lokaci. Amma ina fatan hakan a raina a duk lokacin da hankalina ya dawo jikina kafin magauta su farga su maida ni ruwa. Nayi haƙuri da rasa Abie a dalilin rashin fahimtar gadar zare, amma bazan iya haƙuri da sadaukar da ku ba a lokacin

dana banbance baƙi da fari. Muhammad ina Fahad, ina Autana yake. Ina yarinyata take. Dan ALLAH ka kaini naga Fahad da Samraah yanzun nan”.

Da sauri ya ɗago yana kallonta. Sai kuma ya motsa lips ɗinsa a hankali ya furta, “Samrh!”.

“Yes dear. Ina son naganta?”.

Kafe Ummie yay zuciyarsa na bugawa da sauri-sauri. So yake yay magana amma ya kasa. Fahimtar hakan ya sata sakin murmushi. Ta ɗan girgiza masa kanta tana mai kaiwa zaune dan ta gaji da durƙuso akan gwiyawun nata. Da sauri ya kamata ya zaunar da ƙyau, murmushi ta sake sakar masa da kama fuskarsa ta sumbataci goshinsa. Sai kuma ta lakace masa hanci da faɗin, “Kallon fa. Kana mamaki ne?”.

Kasa cemata komai yay sai idanu daya kafeta da shi. Murmushi ta sake yi da faɗin, “Nifa bana son miskilanci”.

Murmushi ya sake mata a hankali yana kai rissinar da idanunsa. Itama sai ta saki murmushin tana mai sauke numfashi.

“Ummie tun yaushe kika warke?”.

“Muhammad kowane labari nada nashi tushe. Kamar yanda gini ke farawa da tushiya, tsirrai ke farawa da mafari. Ɗa a cikin uwa ke farawa da gudan jini. Samraah na cikin mutanen da suka shigo rayuwata a ƙarshen labarina. Amma tana cikin mutane masu muhimmancin da kwatantashi bazai yiwu da baki ba. Ka bar batun su Bilkisu, waɗan nan sunansu JINI NA, kamar yanda kai da Fahad kuke JINI NA. Amma tabbas warkewa ta ta fara ne daga lokacin da Samraah ta shigo rayuwata bisa hukunci da amincin UBANGIJI. Muhammad ka tashi, maza tashi ka kaini ga Mahaifinku da Samraah da Fahad. Ko kaje ka kawo min su na gansu, ina son mu bar ƙasar nan mu duka a yau kafin maƙiya su farga da mu na roƙe ka”....

“Kinfi ƙarfin barin ƙasar nan saboda WAWAYE Ummie. Sai dai su su GUDU su barta, dan a yau zaki kwana a cikin MAASH MANSION ne ma”.

Ya faɗa da wani irin salo mai nuna gwarzantaka da tsantsar bajinta da babu ɗigon tsoro a cikinta.

Kai Ummie ta girgiza masa cikin rauni. “No Muhammad. No. Bazan sake komawa gidan can ba, kasan kuwa su wanene ke cikin gidan nan? Kasan kuwa ƙarfin bushewar zukatansu? Kasan kuwa ƙarfin rashin imaninsu da abinda zasu iya?.”

“Ummie!!! Please. Kar kice na BARI. Dan kansu kawai suka sani, kisa a ranki kawai yanzu ne WASAN ZAI FARAAAAAAAAA!!!!”.

Yanda yay maganar yana bubbuga yatsarsa a ƙasa jijiyoyin jikinsa na wani irin masifar tashi ruɗu-ruɗu abinka da mai buɗaɗɗen jiki, ga idanun gaba ɗaya sun gama birkicewa. Sai da Ummie ta firgita. Wata irin amsa kuwwa Muryar mahaifinta ta shiga mata a cikin kunne. A lokacin da suka je Spain harda Abie kawai sun fita yawo shi da Abie ɗin sai gasu sun dawo wuyan Awwab zane da tattoo ɗin fuskar zaki a gefen wuyarsa da har yanzu shine dai. Da mamaki ta kamashi tana dubawa. Hankalinta ya tashi ta fara masa faɗan waye ya masa Tattoo? Abie yana ina aka masa. Babu shakka ko tsoro ya ce, “Ni naje aka mun Abie ya biya saboda ni ZAKI NE”.

Haushi ya saka Ummie mangaresa. Sannan rai ɓace ta tafi wajan Abie ta kai ƙara duk da yace mata Abie ɗin ne ma ya biya kuɗin Tattoo ɗin. Sai kawai Abie ɗin ya ƙyalƙyale da dariya da faɗin, “An masa ne saboda yana so. Dan JIKANA ZAKI NE!!!”. Sai kawai tama rasa abin faɗa a lokacin, dan yanda Abbie ɗin yay magana babu alamar damuwa tattare da shi sai ma ƙarfi da karsashi...

Kuka ta fashe da shi tana mai ƙanƙame Maash ɗin a jikinta ta ce, “Yeess Abie JIKANKA ZAKI NE”.....

😂YAYANMU ZAKI NE muma mun yarda Abbie😊, dangin Kandala ma sun shaida😆😂.

□□□□□

10:12pm na dare da abubuwa da yawa ke kan faruwa wanda ya damalmale na kowa ya faru. A ɓangaren su Fahad da Hafizzullah sun farfaɗo tun bayan Magribar da tai dai-dai da isowar Sheikh Muhammad ibn Khalipha Al-Hussain Maash Mansion bisa jagorancin Baban Hayatu da kaɗai yasan da zuwansa. Dan haka suka kasance a ƙarƙashin kulawarsa dan kai tsaye sashen Fahad ɗin Baba ya kai Sheikh Muhammad ɗin batare da kowa na gidan ya sani ba sai Shu'aibu da TJ. Hakan ta farune kasancewar ma'aikatan gidan yau jikinsu duk a sanyaye yake. Hajiya ƙarama bata gidan. Hajiya Mama na asibiti wajen Samraah. Hajiya Mammah tana sama tare da aminiyarta Rubayya data kawo mata ziyara suna tattauna cakwakiyar gidan. Wanka Baba ya sakasu sukayi aka basu abinci sukaci Sheikh ya basu ruwan addu'a sannan yay musu tambayoyi akan ina suka je. Amsa ɗaya suka bashi shine su dai sun kwanta barci daga haka suka farka suka gansu a wani waje daban an ɗauresu. Sai wani dake kawo musu abinci sau biyu a rana. A kuma daren shekaran jiya aka zo aka canja musu wajen zama. Sosai baba da Sheikh suka jinjina zancen, dan haka suka buɗe musu komai dake faruwa harda videos ɗin da aka saki akan Maash da Samraah, dana Maash a asibiti. Wani irin rawa jikin Fahad ya fara, kafin cikin kuka

ya fara roƙon su kaisa Dubai ya ga Yayansa. Yanda yake ambaton yayan nasa duk a rikice yasa suka fahimci al'amari fa da alama ya dai-daita. Kallon juna Baba da Sheikh sukayi, kafin su zaunar da Fahad suka lallasheshi shi da Hafizzullah dake kuka sannan a nutse suka warware musu ainahin gaskiyar abin duk shiri ne. Sai dai ba'asan inda Maash yake ba yanzu taka maimai. Suka kuma warwarema Fahad alaƙar Maash da Samraah, yayinda Hafizzullah ya ƙara masa bayani dalla-dalla. Ai kawai gani suka Fahad ya miƙe a fusace, suna kiransa ko saurarensu baiyi ba ya nufi ainahin baban sashen. Sai kawai ihunsa da hargaginsa suke jiyowa yana ƙwala kiran sunan jama'ar gidan ɗaya bayan ɗaya. Ƙoƙarin miƙewa Baba yayi Sheikh ya hanashi yana mai girgiza masa kansa yana murmushi. A dai-dai lokacin Hajiya ƙarama da yau ma Commondo yayma fata-fata ta shigo ranta a ɓace. Cak ta tsaya kamar wadda aka dokama guduma a kai. Hakama Hajiya Mammah ta fito daga ita sai ɗaurin ƙirji Hajiya Rubayya biye da ita ta cikuykuye jiki da zanin gado. Dan irin mafaraucin kiran da Fahad kema kowa na gidan ko a bayi kake zaka iya fitowa a guje tsirara batare daka fargaba musamman idan kanada wani tabon laifi tattare da kai. Hatta su Azizat sun fito. Maman Malika ce kawai ta fito a nutsenta tana ƙoƙarin kiran mijinta da Hajiya Mama akan suzo gida fa ga abinda ke faruwa. Hakama Hajiya Mammah jiki na rawa ta koma ɗakinta ta ɗauki waya tai kiran Baba prof.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-three

63

.....A dai-dai lokacin Baba prof ke waya da Teacher ɗinsa dake ƙasar Togo sai ga kiran Hajiya Mammah ya shigo a ɗayar wayarsa. Yanzu baya wasa da kiran kowa, dan haka bama ta gama ringing biyu ba ya ɗaga yana kaiwa kunne da ajiye kiran teacher ɗin nasa. Cike da tashi. Hankali Hajiya Mammah tace, “Baba dan ALLAH

kazo gida yanzu babu lafiya. Shima Fahad ya ɓalle gashi nan da zandareren takobin nan nashi ya ce wlhy idan bamu fito masa da Awwab ba da Mahaifiyarsu sai ya ma kowa yankan rago yau a gidan nan". Bata ta jira cewarsa ba ta yanke kiran ƙittt.

Kasare yay yana kallon wayar. Dan yama rasa yanda zai fassara zancen nata ko hasaso wani abu sai jikinsa ne ke rawa. Sai kuma ya tura wayar a aljihu da sassarfa ya fito yana haɗa hanya da ƙwalama driver ɗinsa kira yama manta ya kaishi fagen rabin mutuwa ɗazun. Sai da ɗaya a cikin ma'aikatan gidan ya iso ya sanar masa ai driver tunda suka shiga ciki tare bai fito ba. Kansa ya dafe tare da masa nuni da mota ya ce, "Kaini Maash Mansion"....

Cikin in ina ya ce, "O...ga ai ban iya mo..ta ba".

Wani firgitaccen tsawa Baba prof ɗin ya masa cikin ƙara ji yace, "Nace ka kainiiiiii!!!".

Rawa sosai jikin dattijon ya fara dan tsawar ta ratsashi. Dai-dai nan ɗaya daga cikin guards ɗin sa ya iso ya amshi key ɗin motar.....

Suna fita a gidan Isma'il ya saki murmushi, tare da ciro wayarsa ya ɗanna ma Maash kira. Ya ce, "Ranka ya daɗe saƙo ya samesa. Yanzu haka ɗaya daga cikin guards ɗinsa ya tafi kaisa Maash Mansion kuma zaku iya tafi".

Sai da yay ɗan jimmm alamar saurare sannan ya saki murmushi da faɗin, "Thanks you Sir ina kan aikina ne". Daga haka ya yanke kiran.....

□□□□□

A hankali Maash dake rungume da Babyn Falaq ya sauke wayar tare da sake rungume jinjirin yana mai kaima goshinsa sumbata. Sai kuma ya juya ya kalla Ummie da tai sabon shirin cikin wani ubansu lass da aka kawo mata mai shegen tsada da ƙyau. Ga gwala-gwalai Falaq ta mata ɗan simple kwalliya da ya sake bayyana ainahinta na UMMU-HIDAYA IBRAHIM ɗin ta. Sai wani uban ƙamshi da take bulbulawa. Gaba ɗaya wannan shirin an ƙirƙiresa ne daga ɗazun bayan sun gama kukan samun lafiyar Ummie sun koma murnar samun sabon Baby da atake Hayatu yace yaba Ummie wuƙa da namar zaɓa masa suna Maash kuma ya masa huɗuba. Babu ko wani kwana-kwana tace MUHAMMAD AWWAB. hakan kuwa akai masa huɗuba da shi kuma Maash ɗin ne yayi duk da baya jin daɗin jikinsa amma ya kasa gaya musu. Bayan ya kammala yace su tashi su wuce Hayatu ya ce, "No Yaya ba'a haka ba. Sai Ummie ta kimtsa ku bani awa uku kawai." baima saurari amsar Maash ɗin ba ya fice. Kamar ko yanda ya buƙata awanni ukun ma basu gama cika ba sai

gashi da duk kayayyakin da Ummie ɗin ta saka. Kawo kayan ya saka Maash haɗa sabon plan shima. Dan haka yay kiran Sheikh da ya sauka Lagos babu jimawa yay masa bayinin akan Fahad. Dan yana fatan yanda yake jin sakawai game da ɗan uwan nasa a yanzu babu wannan ƙiyayyar shima ta kasance hakan. Kuma ko shi abin bai sakesa ba ya san ko akan Ummie da Samraah zai iya yin duk abinda suke so. Sai gashi kuwa komai ya tafi musu dai-dai a ƙanƙanin lokaci Fahad ya haye dokin da suka azashi....

Ummie taso ganin Samraah kafin shigarsu Maash Mansion amma Maash ɗin ya lallaɓata akan tayi haƙuri, akwai dalilin da yasa baya son su haɗu a yanzu dan zata iya shiga shock ɗin da matsala zata iya afkuwa. Dole ita tana buƙatar a bita mataki-mataki yanda komai zai zo mata da sauƙi. Amma ya mata alƙawarin yanda zata kwana a maash Mansion itama Samraah a ciki zata kwana in sha ALLAHU yau.. wannan ne ya bata ƙarfin gwiwar haƙuri suka tafi...

Rikicin daya ɓarke acan babban falon gidan da kowa yay cirko-cirko yana kallon Fahad dake garzaza tsiya da rantsuwar idan har basu fiddo masa Yayansa da Ummiensa da Paah da Samraah da Hayatu da su Mama Balki da Falaq kamar yanda suka fiddosu shi da Hafizzullah ba. Ya rantse da ALLAH yau sai kowa ya kwana da zanen yarbawa a fuskarsa kafin da safe yasa a kwashesu zuwa police station gaba ɗayansu yasa basu ko ji motsin shigowar motar su Maash ɗin gidan ba. Tun a main perlor suke jiyo hargagin Fahad. Wani irin makirin murmushi Maash ya saki yana mai lumshe idonsa baby har yanzu na'a hannunsa ya kwantar da shi a kafaɗarsa ya riƙe Ummie da hannunsa na dama. Mama Balki ce ta fara shiga da sallama mai ɗan ƙarfi. Hakan yayi dai-dai da juyowar Fahad yana nuna Baba prof dake tsaye kawai zufa ta gama jiƙesa dan kalaman Fahad wani masifar ratsashi suke, ballema yanzu da yake nunasa da takobin yana faɗin, “Wlhy da kai zan fara Baba. Dan ma su san da gaske nake yi babu ruwana da kai ka haifi Paah zaneka zanyi da takobin nan tsaf da zanen yarbaw.....” yay ɗiff ya gagara ƙarasawa yana kallon Mama Balkin kamar yanda take kallonsa tana murmushi. Baki ya motsa zaiyi magana sai kuma ga Hayatu, kafin yace tak Falak ta shigo da sallama itama. Ya yunƙura zai nufesu kamar yanda Hajiya Mama da Maman Malika suka yunƙura suma sai ga mai gayya da aiki Muhammad Awwab El-Mu'azz Adams riƙe da hannun Ummie ga abu dake a kafaɗarsa dake tabbatar da Baby kuma.

Yanda kuka san an saka remote an tsaida Film ɗin dake tsaka da aiki haka kowa ya tsaya cak a yanda yake. Musamman Hajiya ƙarama da Baba prof. Yayinda karyayyen harshen nan na UMMIE daya rangaɗa sallama ya ratsa kunnen kowa tamkar yanda sautin kiran salla kan ratsa kunnen mai barci a bazata. Karo na farko Baba prof ya wani zabura ya manne da bango. Hajiya ƙarama ma tai baya tana mai sakin handbag ɗin hannunta zuciyarta na wani girgiza a cikin ƙirjinta. Hajiya Mammah dai baki ta saki da waro idanu waje gaba ɗaya. Haka Maman Malika sai da ta ɗan ja baya.. Fahad kuwa wani kalar suɓucewa takobin hannunsa tayi tare da ƙafafunsa ya tafi ƙasa ragwafff ya dire gwiyawunsa a ƙasa tamkar irin tsohon raƙumin nan daya galabaita a tsakkiyar sahara... Yaran kam da su ganin Hajiya

Babba cikin ado kuma tana sallama ne ya hargitsasu duk sai suka cure waje guda suka ƙanƙame juna. Dan tuni an gama cusa musu zancen Hajiya Babba mahaigakciya ce tuburan da zata iya kisa ba kuma lallai ta warke ba...

Da wani kalar sassarfa Ummie ta ƙarasa ga Fahad, tarosa tayi gaba ɗayansa dan neman rasa numfashi yake tsabar firgita. Wani irin ƙanƙamesa tayi a jikinta cikin matuƙar dakiya ta furta, “Oh my sweet Auta don't fall down” dan tayi alkawarin bazata sake barin maƙiya suka gazawarta ba. Ina Fahad fa ya shiɗe farin ciki ko firgici sun sakashi suma. Hayatu ne yay saurin ɗakko ruwa ya kawo. Ɗago Fahad ɗin yayi daga jikin Ummie da nauyinsa ya sata zama dole ya shafa masa ruwan. Nannauyan numfashi ya kawo mai azabar ƙarfi. Sai kuma ya kalla Hayatun da Maash dake tsaye a kansa. Muryarsa na rawa hawaye na kwarara ya ce, “Yaya mafarki nayi Ummie ta warke harta shigo ta ganni na ganta fa. Dan ALLAH miyyasa kuka tadani ku barni na koma ko magana muyi da ita”. Ya faɗa yana sake rumtse ido.

“Ba mafarki bane kiddo. Da gaske ne buɗe idonka”.

Tamkar matsoraci jikin Fahad ya fara rawa, hatta idanunsa mar-mar sukeyi yana buɗesu a hankali har ya buɗe gaba ɗaya kan ƙyaƙyƙyawar fuskar UMMIE da ke kallonsa tana hawaye itama. Hannunsa dake rawa ya shiga ɗagawa a hankali a hankali har ya isa saman fuskarsa ya ɗora. Da sauri ya janye tamkar wanda ya dafa wuta. Sai kuma ya miƙe zaune daram ta sake kai hannun yana kallonta yana hawaye. Caraf ta riƙe hannun tare da ɗorawa saman fuskar tata ta ƙanƙame. Sai ga hawayen da taketa riƙewa sun zubo sharrrr. Wani irin firgitattacen ihun da faɗin “Ohhhh Myyyyy Goooood!!!” Fahad ya fasa yana rungumeta gaba ɗayanta sai kuma ya fashe da kuka.

A hankali Maash ya kauda kansa gafe na tsawon minti ɗaya kafin ya maidosa kansu. Hayatu ya miƙama Babyn sannan ya kai duƙe a slowly tamkar wanda baya so ya ɗago Fahad daga jikin Ummie. Miƙar da su yay tsaye su duka ya kama fuskar Fahad da hannu biyu ya fara share masa hawayen da yatsunsa manya yana wani ɗan jujjuya masa kansa”.

Jikinsa kawai Fahad ya faɗa suka wani ƙanƙame juna da iyakar ƙarfin ƙwanji. Cikin kuka Fahad ya ce, “Yaya dan ALLAH da gaske UMMIE ta samu lafiya? Da gaske ba mafarki nake ba kamar yanda na saba?”.

Ɗagoshi Maash ɗin yayi ya tsurama fuskarsa ido. Sai kuma ya sakar masa wani shegen murmushi daya kusan ɓaro zukatan wasu tare da motsa lips ɗinsa kaɗan, cikin silent voice ɗin nan tashi ya furta, “Ba barci kake ba Kiddo. Ummien ce a gabanka da lafiyarta. Dan haka ga saƙo ka faɗama MAƘIYA GASKIYA!!!” ya ɗan ɗaga sautinsa anan ta yanda kowa sai da ya jisa. “Su fara gudu, gudu na ceton rayukansu. Gudu na cigaba da bizne abinda suka shuka. Idan ba haka ba. Bayan ka musu zanen Yarabawa. Ni Muhammad Awwab El-Mu'azz nayi musu alƙawarin sai

nayi gunduwa-gunduwa da kowanne gaɓa ta jikinsu ta yanda ba za'a iya iya banbance kowanne ɓangare na halittar su ba!!!”.

Tamkar wani abun shirin Film kawai Fahad ya bushe da wani ɗan iskan dariya. Sai da yay mai isarsa kafin ya kalla yayan nasa. Cike da jin sabuwar izza ya ce, “My sweetheart yayana. Idan ka fatattaka namansu. Na maka alƙawarin siyo ƙatuwar tukunya da ƙatin iccen nan na dahuwan naman raƙumi, na bama Aunty Samraah ta mana DABGENSU mu baje a ƙaton tray UMMIE da MAMA su dinga bamu a baki muna taunawa da korawa da ruwan kamfanin MAASHHHHHHH”.

Dariya abin ya bama Falaq. Tako kasa haɗiyewa ta fara ƙyalkyatawa. Sai kawai Hajiya Mama da itama abin ya birgeta ta shiga yin dariyar. Ai kawai sai su Mama da Hayatu da Maman Malika suka hau tayasu. Gogan kan sai ya wani lumshe idanu kawai yana mai tura hannayensa duk biyu a cikin aljihu. Da wannan damar Hajiya Mama da Maman Malika suka sami damar tahowa rungume Ummie. Tsabar makirci sai itama Hajiya ƙarama ta taho da gudu tana kuka zata rungume Ummien wai. Ajiyar zuciya Hajiya Mammah ma ta saki tana sakkowa. Ganin hakan yasa su Azizat fara sakkowa daga upstairs da suka maƙale a guje suma duk da bawani saninsu Ummie ɗin tayi ba duk suna ƙananu sosai, sai ɗan sanda ta samu lafiyar nan lokacin kuma ba'a tare suke ba. Suma duk nufar rungumetan sukayi. Amma mi duk kafin su isa gareta sai kawai Fahad yasha gaban kowa ya tare ta. Cak duk suka tsaya suna kallonsa kamar yanda shima yake kallonsu cikin wani irin ɗage kan rainin waye da girgiza hannu ya ce, “Inaa ai babu mai taɓa Ummie a gidan har sai anyi searching”. Yana gama faɗa yaja hannun Ummie yay hanyar sashen Maash da ita dake ta cikin falo yana wani kalar takun buɗewa daka gani kaga tsageran matashin zamani mai shirin a mutu ko ai rai😂.

Shi kansa Maash a wannan gaɓar sai da yay gajeren murmushin da kowa zai iya gani a kan fuskarsa yana mai ɗan girgiza kan kaɗan. Batare da yace ma kowa komai ba yay ma Falaq nuni da hanya ita da mama Balki. Gaba kuwa sukayi ya bisu a baya bayan ya juya ya kalla Baba prof cikin ido ya sakar masa murmushi, ya sake juyawa ga Hajiya ƙarama ita kuma ya mata wani shegen kallon da su duka sai da suka nema zubewa ƙasa. Cikin nashi takun bajintar shima yay gaba. Yayinda falo yake tsitt har yanzu tamkar an jera gunkunaye. Kowa da abinda yake rayama zuciyarsa.

Rawar da ƙafafun Baba prof keyi yana shirin zubewa a ƙasa ya maidosa hayyacinsa daga sumar tsaye da yayi sakamakon kallo da murmushin da Maash ya masa. Yay taga-taga zai faɗi sai da Hayatu ya taroshi yana faɗin faɗin, “Subahanallahi Baba”.

Cikin wani irin jan numfashi dake shirin ƙwace masa a hankali ya ce, “Kaini na zauna Hayatu zaunar da ni.”

Babu musu Hayatu ya kamashi har kan kujerar dake kallon ta Hajiya ƙarama da itama ta kai zaune sakamakon jirin dake neman yarda ita ya zaunar. Sai kawai ya

ƙara yin shakaff a kujerar dan kaɗan ya rage zawayin dake ƙoƙarin ɓarke mas ya samu ƙofar fara tsirarowa.....✍

(😂😂😂😂Baba prof sannu kaji, abin tausayi wlhy□□□).

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-four

64

.....Shigowar Uncle Abdullahi gidan da labari ya kaimawane ta dawo da kowa a hayyacinsa. Sai tarin da ya sarƙe Baba prof. Su duka su kansa sukayi, banda Hajiya ƙarama data samu hanyar hayewa sama. Kallon kallo sukaima juna ita da Hajiya Rubayya da har yanzu ke tsaye tana kallon komai. Sai kawai suka sakima juna murmushi. Cikin rawar murya Hajiya ƙarama dan ita kaɗai tasan halin da take ciki itama ta ce, “Ki tattara su Falilah subar gidan nan zuwa gobe bayan kowa yasan wacece Nafisa”.

“An gama ranki ya daɗe”.

Hajiya Rubayya ta faɗa cikin kashe ido tana sakin wani makirin murmushi. Gaba Hajiya ƙarama tayi zuwa sashensu. Sai da ta tabbatar ta dannama ƙofar key kafin ta wurgar da bag ɗinta bayan ta ciro wayarta. Kira ta dannama Commando, yana ɗagawa bata jira cewarsa ba cikin bushewar zuciya ta furta, “Wasa ya canja gaba ɗaya. Dole ne a mutu har liman. Uwar tafiya ta dawo hayyacinta, yanzu kam kan mai uwa da wabi kawai. Ka canjama Mu'azz wajen zama a daren nan. Shi kaɗai ne makamin mu a yanzu”.

Tana gama faɗa ta yanke wayar. Jannifer ta kira, itama tana ɗagawa tace, “Bana son kuskure. Idan har naga kiranki ya zama Mu'azz da Commondo na a hannunki ne”. Wayar ta wani irin jefa saman gado. Sai kuma ta ƙyalƙyale da dariya ta kuma fashe da kuka duk a lokaci ɗaya, tamkar itama dai kan nata ya fara taɓuwa.

Hajiya Lawisa sorry woohoo😂😂□□.

□□□□

Commondo ya jima zaune da waya a hannu shi bai ajiye ba shi bai motsa ba. Dan shi kansa ba ƙaramin dukan zuciyarsa zancen Hajiya Ƙarama ɗin yay ba. Yanzun nan fa yake ganin text message ɗin wani yaronsa da tun ɗazun ya turo masa kasancewarsa da Hajiya ƙarama yasa bai lura ba. A saƙon yana sanar masa cewar ya gano inda Mahaifiyar Maash take. Har ya tura masa address yanzu haka shirin da yake kenan na zuwa su ƙwamusota ransa fari ƙal zai fara aiwatar da nasa plans shima. Kansa ya girgiza, dan haka kawai yaji kamar bai yarda da batun Hajiya ƙarama ɗin ba. Wayar ya fara daddanawa, yana zuwa kan sunan da yake nema ya danna mata kira.

Siyama da tun ɗazun take a bayan window laɓe ita da wasu ma'aikatan gidan mabanbanta suna kallon komai dake faruwa dan tun isowar su Maash duk wanda idonsa ya gansu bai zauna ba ya biyo saboda son tabbatar da Hajiya Babba ɗin ce ko watace ke musu gizo wayarta ta hau tsuwwa. Da sauri tabar wajen ganin Commondo ne. Sai da ta shige cikin garden sosai sannan ta ɗaga tana mai maida muryarta can ƙasa ta ce “Boss”.

“Siyama mike faruwa a gidan nan?”.

“Hummm! Boss ai komai ma ya faru ko nace yana kan faruwa. Jira nake kawai akai ƙarshen Film ɗin na kiraka na baka bayani.....” tsaf ta zayyane masa komai fiye da yanda Hajiya Ƙarama ta sanar masa. Sannan ta ɗora da faɗin, “Mutuniyarka ta haye sama kamar zata zube. Dan numfashinta ma kamar siezing yake. Kakansu ɗin nan da yau na ɗaura alamar tambaya a kansa gashi nan za'a wuce da shi gida naji suna kiran likitansa”.

Murmushi Commondo yayi, dan yasan Siyama bata san komai akan Baba prof ba. Ya turata jikin Paah ne domin ɗaukar fansa da sanya masa ido akan duk wani motsin Hajiya ƙarama. Tunaninsa ya katse tare da yin gyaran murya. Sannan ya ce,

“Zamanki ya kusa ƙarewa a gidan nan. Sai dai ki saka min ido akan Lawisa sosai-sosai a tsakanin nan. Koda tari tayi na sani”.

“An gama Boss”. Ta faɗa cike da girmamawa. Dan commondo ya cancanci fiye da komai a wajenta. Ya taimaketa a lokacin da kowa ya ƙyamacesu akaƙi taimakonsu ita da mahaifiyarta. Ita kaɗai ta tashi gaban uwarta batare da sanin kowa a danginta ba da mahaifinta. Tunda tai girma tayi wayo takan tambayi mamanta ina babanta saboda ganin sauran yaran da iyayensu ke haya a gidan da suke duk suna da Baba. Maman tata bata bata amsa. Sannu-sannu idan faɗa ya haɗata da yara sai a dinga zaginta da kiran mamarta karuwa ita kuma yƴar shege. Tun abin baya mata zafi harya fara. Ta dinga tsare mamarta tana kuka amma bata cewa da ita uffan. Daga ƙarshe ma suka bar gidan. A anguwar da suka koma ɗin ma komai bai canja ba, dan nan ɗin ma dai Hausawa ne. Tasha kama mata a lokuta da dama na gulmar mamanta akan ita munafukar karuwa ce. Kullum tana nuna ita ta ALLAH ce sai dare yayi ta fita aikata aikin ta. Tun abin baya mata tasiri har itama ta fara tsarguwa da fara sakama Maman nata ido. Sai dai hakan ya gagara dan barci na hanata rawar gaban hantsi. Tunda tai wayo bata iya wuce takwas na dare batai barci ba, takan kuma rasa dalilin hakan. Sai daga bayan nan data duƙufa bincike ta gano Maman nata ce ke bata abinda ke sakata barci ashe a cikin wata FURAR ƙaddara data sabar mata sha tun tana yarinya. Dan haka tafa canja taku itama. Furar ta fara sayowa tana ɓoyewa a duk sanda Mamanta ta bata wadda keda maganin sai ta ƙi sha ta canja da wadda ta sayo ta ɓoye waccan. Haka zatai likimo har Maman tata ta gama shirinta cikin ƙazamar shiga irin ta karuwan dare ta zabga hijjab har ƙasa sannan ta fita. Randa ta fara gani tayi kuka sosai, daga baya ma sai ta sha furar nan barci dole ya ɗauketa. Sai da sukai haka da mamanta fin sati sannan a cikon kwana na takwas tabi bayanta. Hankalinta yay mummunan tashi da abinda ta gani, dan tabbas Mamanta Karuwa ce. Karuwarma ƙazamar karuwa da ake nema ta gaba da baya. Kaɗan ya rage a ranar Siyama bata bar duniya ba. Dan har jiyya ta kwanta na wasu kwanaki. Bata da aiki sai kuka. Ko kallon Mamanta bata ƙaunar yi. Kwatsam a washe garin da aka sallameta asibiti sai ga Mamanta an kawo jage-jage da jini wai wata ta soketa da kwalba a club. Duk yanda taso barinta zuciyarta bata yarje mata hakan ba. Haka ta rungumeta tana kuka da roƙon a taimaka mata. Amma mi kaf anguwar babu wanda ya taimaketan sai Commondo. Shi ya saka yaransa suka ɗauki Mamanta aka kai asibiti, ya biya kuɗin komai harna gado. Tsahon sati uku da tai a asibitin nan har nauyin abincinsu shiya ɗauka. Sai dai me tunda suka dawo gida sai sabon ciwo ya tashi ma Maman tata. Bata ɗauki hakan komai ba sai tunanin wajen yankan ne bai gama warkewa ba. Sannu-sannu suna zuwa asibiti ganin likita kwatsam randa jiki ya rikice sai aka tabbatar mata Mamanta fa nada ƙanjamau. Ga tsutsa na fita mata ta baya Sakamakon abin da take aikatawa dan bata amfani da maganin da masu wannan ɓarna ke sha. Hankalinta ya tashi, taje domin sanarma Commondo ya sake taimaka musu ta samu baya nan yayi tafiya wai. Hankalinta ya tashi, dan asibitin basu riƙesu ba dole suka dawo gida. Wata sabuwar ƙyama da tsangwamace aka fara musu, bataga laifin mutane ba dan ko ita dauriya take saboda warin da mahaifiyarta ke fitarwa ta

bayanta daya zazzago. Takai ko zama bata iyayi ma sannan toilet baya iya riƙuwa gareta. Babu kalar kukan da batai ba da magiya amma ina abinci da zasu ci ma ya gagaresu balle omon da zata tsaftacema Mamanta jiki. A haka suka kwashi watanni uku. Kwatsam wata rana zuciyarta ta ayyana mata zuwa wani company neman taimako anan bayansu. Dan haka ta shirya taje. Securitys basu barta ta shiga ba duk da magiya da kukan data dinga musu. Dole ta tsugunna a bakin gate ɗin ta cigaba da kukanta. Tafi minti talatin a haka sai ga wata dalleliyar mota mai azabar ƙyau. Harta gotata aka dawo baya. Magana driven ya mata, hakan yasata miƙewa zaram jikinta na rawa ta nufoshi. Cikin tsawa-tsawa ya tambayeta mi take yi a wajen?.

Jikinta har rawa yake dan tsoro ta sanar masa taimako take nema. Sai da ya gama saurarenta yay mata tsawa tabar wajen. Har ta juya zata tafi tana kuka sai kuma ya dakatar da ita. Hotonta ya ɗauka yay danne-danne a waya. Babu jimawa taga ya ɗago ya kalleta da murmushi. “Yarinya kakarki ta yanke saƙa shiga mota oga yace zai taimakeki a kaiki”. Cike da farin ciki ta shiga motar, shi kuma yay reverse ya koma batare da ya shiga companyn ba. Wannan shine mafarin haɗuwarta da Paah. Dan an kaita garesa wani gida, Maimakon ya taimaka mata bayan ta gama zayyane masa damuwarta kamar yanda ya buƙata sai ya nuna mata sai idan ta biya masa buƙatarsa. Da farko taƙi har tai fushi ta tashi zata fita. Sai dai tuna halin da mahaifiyarta ke'a ciki ya sakata komawa garesa. Babu ko tausayi kuwa ya keta mata haddi, a kuma ranar ta fara sanin namiji. Bayan ya gama abinda yaso ya bata kuɗi har naira dubu ɗari biyu. Haka ta tafi tana kukan baƙin ciki da na farin cikin samun kuɗin da zata kai mahaifiyarta asibiti. Sai dai me tana zuwa ta samu mahaifiyarta ta mutu an jehota ma bakin bola mutane yayyaɓe da ita suna kallo da zagin gawarta. Wannan al'amari ya ɗimautata. Ɗimautawar data yanke jiki ta faɗi bata tashi farkawa ba sai a gadon asibiti. Bayan ta farfaɗo ta fahimci commondo ne ya kawota asibitin... Wannan shine sanadin komawarta hannunsa. Ta bashi labarin komai daya faru, ya nuna ɓacin ransa tare da tabbatar mata ita da kanta sai ta ɗauki fansa dan yasan wanda yay mata wannan aikin saboda sunan companyn data faɗa. Commondo ne ya kawota Maash Mansion a sanadin Jannifer da ya jima da sani ta sanadin Hajiya ƙarama. Da farko Paah ta firgita da ganinta, dan ta tabbatar masa saita tona masa asiri a wajen ɗansa da abinda yay mata. Aiko fa ya rikice yace ta faɗi duk abinda take so. Sai da ta gama ja masa rai sannan tace zata cigaba da zama a gidan, duk wata kuma zai yanka mata albashin naira miliyan ɗaya. Hankalinsa ya tashi ya nema ta sassauta masa dan miliyan ɗaya duk wata tayi yawa ai. Badan baida kuɗin bane ko hanyar samunsu. Sai dai gudun kar Awwab ya gano shi ne. Dan dole de kuɗin zai dinga fiddasu ne daga asusun company. Da ƙyar ta yarda da 200k duk wata. Dole kuma hakan yake biyanta. A hankali kuma ya fara jan ra'ayinta suka cigaba da mu'amala. Koda ta sanarma Commondo sai yace ta cigaba da biye masa ta hakane ai zata cimma burinta itama.. ta cigaba da biye masa, tare da cigaba da ɗibama Commondo bayanan duk da yake so a gidan musamman akan Hajiya Ƙarama da zuwa yanzu ita kanta ta gama gane alaƙarsu, ta kuma san Arwa yɗarsa ce. Sai dai bata taɓa tunanin bama wani bayanan nan ba dan

da iya gaskiyar zuciyarta take ƙaunar Commondo matsayin Yaya daya taimaketa a lokacin da kowa ya gujeta.....✍

(Hummm ALLAH ya rabamu da mummunar ƙaddara. Da yawan yaranmu idan mummunar ƙaddara ta gitta ma rayuwarsu nakasassun zukatanmu suka gagara taimakonsu a matsayinmu na al'ummarsu, sheďancin mutane irin su Paah yay tasiri a kansu ko muka dinga musu hisabi da laifin iyayensu ko wasu ahalinsu sai irin su Commondo da akema kallon gurɓatattu su rungumesu, su tallafesu, komi tsarkin zukatansu sai su koma irinsu suma. Kamar dai Siyama. A yanzu zuciyarta ta gama bushewa. Ko kisa Commondo yace tayi wlhy zata aikata saboda shi kaďai takema kallon girmamawa. Dan ALLAH mutane mu gyara, mu kiyayi hukunta wasu da laifin wasunsu. Hakan na maidamu bayane da sake raunana al'ummar mu da fiddo gazawarmu a fili. ALLAH ka yafe mana kurakuranmu baki ɗaya. Ka shiryemu ka shirya mana zuri'a. ALLAH ka rabamu da mummunar ƙaddara. Ka kiyaye mana mutuncin mazajenmu karsu jawo ma yayanmu da mu abin kunya ta hanyar aikata mummunan aiki😭. Yanzu idan Awwab yasan gaskiyar irin waďan nan abubuwan da Paah ya aikata dan akwai ire-iren hakan da yawa da wace kalma zai iya kare kansa. Ummie Ummie Hummm ya rabba😭)

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-five

65

.....Kuka sosai Fahad yaci a jikin Ummie itama tana taya shi da sake jin tausayinsa, dan kiyayewar UBANGIJI ce kawai tasa yaronta bai lalace ba. Sai Mama ke

lallashinsu. Dan Maash ya fita zuwa asibiti ɗakko Samraah kamar yanda yay ma Ummie alƙawari.

Ina zaune a saman abin salla dana idar da shafa'i da wutri hannayena biyu tallafe da fuskata na afka duniyar tunani. (Ko ina Yaya Awwab ya shiga ne? Ina Fahad da Hafizzullah? Da har yanzu ko mai kama da su ban gani a asibitin ba. Shin Ummie fa? Aunty Falaq kota haihu?) Waɗan nan tambayoyin sune fal zuciyata. Sai kuma zancen ɓatan Paah ɗin nan yana cimun rai da saka tunanina rarrabuwa akan Matarsa da Kakansu. Saukar soft hand mai sanyi akan nawa ya sani ɗago idanuna. Sosai naji shock ɗin ganin wanda banyi zato ba. Dan sam ba ƙamshinsa bane dana sani kamar dai ranar nan. Sai kawai raina ya bani yau ma na sake yin mafarkinsa kenan. Numfashi na ɗan sauke da cigaba da kallonsa dan na gama yarda mafarkin nakeyi ɗin.

Cike da wani irin salo ya ɗan ɗage girarsa duka biyu da mun alamar kallon fa?. Samun kaina nayi kawai da ɗan ɓata fuska. Cikin ɗan ƙunƙunin da nai zaton duk a mafarkine kawai na ce, “Ni ka bar min gizo”.

Idanu ya ɗan lumshe a hankali. Tare da rungumeni a jikinsa. Gaba ɗaya naji jikina ya wani mutu. Musamman da ya ɗaura mitsitsin bakinsa akan kunnina can ƙasan maƙoshi ya furta, “Kona mutu sai na dinga zuwa miki a fatalwa ma”.

Da sauri nayi ƙoƙarin janye jikina zuciyata na harbawa da sauri-sauri. Amma sai ya hana hakan yama sake ƙanƙameni da ƙyau yana sakar min numfashin sa a cikin kunne. Dole na sake ƙanƙamesa muryata na rawa na ce, “Please Ya Awwab mafarki nake ko gaske kai ne?”.

Baiyi magana ba, sai mintsinin da ya sakar min a gefen cinyata babu shiri na ɗan gantsare tare da faɗin, “Ouch!!”. Ina ɗan kai masa duka a bayansa. Ɗagoni yay yana kallona cikin ido, kafin ya motsa lips ɗinsa a hankali ya ce, “Kin yarda ido biyu ne?”.

Murmushi na sakar masa nima tare da faɗawa jikinsa na ƙanƙamesa. Cikin rikicewa nake jera masa tambayoyi. “Yaushe ka dawo? Ina ka shige ne? Ina Ummie na? Aunty Falaq ta haihu ne? Anga Paah? Ina Fahad da Hafizzullah ban gansu ba.....”

“Shiiii!!!. Wanne zan amsa a'a ciki to? Ammien unborn”.

Ya faɗa cikin kunnena da raɗa. Ajiyar zuciya na sauke tare da ɗagowa ina kallonsa. Idanuna cike da ƙwalla na ce, “Please My Lion duka ka amsa min, waye kuma Ammien Unborn ɗin?”.

Nunani yay da yatsa.

Sai naji gabana ya ɗan faɗi, muryata har rawa take na ce, “Ban gane ba ALLAH Yaya”.

Ido sosai ya zuba min kawai yana kallona. A hankali na fara ganin ƙyalli a cikin idanunsa alamar hawaye na taruwa. Sai kuma ya ɗan duƙo ya sumbaci idanuna dake kallonsa da hancina da baki na. Kafin ya riko hannuna shima ya sumbata. Murya can ƙasan maƙoshi lips ɗinsa na motsawa a hankali ya furta, “Samrh! ALLAH ya mana ƙyauta da abinda kuɗi ko ƙarfin mulki basa badawa. Naso yin kuskuren wasa da rayuwar ƙyautar da UBANGIJI yay mana. Am sorr...”

Da sauri na kai hannu na rufe masa bakin ina girgiza masa kai. Hawaye na silalo min na ce, “Baka min laifin komai ba Yaya. Dan ALLAH karka bani wani haƙuri. Komai daka gani a rayuwar bawa ƙaddararsa ce tazo da hakan. Ina tayaka murnar samun ƙaruwa”. Na ƙare maganar da shigewa jikinsa sosai na ɓoye fuskata dan kunyarsa naji tana sake shigata mai tsananin. Ga wani irin farin ciki na matuƙar ratsani wai ni Samraah ke ɗauke da ciki irin na haihuwa. Nima zan zama Mama”.

Sake ƙanƙameni yay sosai a jikinsa shima kamar zai maidamu abu ɗaya cikin kunnena ya furta, “Nima ina tayaki murnar samun ƙaruwa Aljannata”.

Dariyar na sake ƙyaƙylƙyalewa da shi ina sake ɓoye kaina a cikin jikinsa. Sosai naji motsin fitar sautin nashi murmushin shima a cikin ƙirjinsa. Mun jima a haka kafin ya ɗagoni ya sumbaci lips ɗina. Tare da nuna min nashi alamar nima nayi masa. Kafaɗa na maƙe masa alamar naƙi ɗin.

Fuska ya ɗan yamutse yana wani ɓata ta. Hakan ya sani kai yatsana manunuya na ɗalli small pinkish lips ɗinsa ina murguɗa baki da faɗin, “Dan kurma kawai”.

Ƙaramin murmushi ya ɗan saki da alamunsa kawai na gani ya ɗauke kansa. Batare da yayi maganar ba dai ya miƙe dani a haka ya nufi ƙofar fita. Mamakine ya kamani, da sauri na ce, “Yaya bafa a sallaman ba. Ina zaka je da ni”.

“Saidawa”.

Ya faɗa a taƙaice yana ficewar dani. Dole sai nice na lumshe idanuna tare da ɓoye fuska a ƙirjinsa saboda kunyar mutane. Dan muna fitowa a ƙofar ɗakin mukaci karo da yar sandar nan. Mugun sandamewa tai tana kallonmu, sai da muna gab da gitttata ta ɗan dawo hayyacinta tana gaishesa. Amma bai ko kalleta ba balle naji ya amsa yay gaba. Sai jina nai ya saka a mota shima ya shiga. Kwantar dani yay kaina a saman cinyarsa. Bamma san wanda ke janmu a motar ba sai da Hayatu ya ce, “Auntyn mu yaya jikin?”.

Da sauri na buɗe ido muryata har rawa take na ce, “Yaya Hayat da ma harda kai?”.

Ƙaramar dariya yayi da faɗin, “Eh mana”.

Ajiyar zuciya na sauke mai ɗan nauyi. Ban sake magana ba sai yunƙurin tashi zaune. Sai dai gogan ya maidani ya kwantar yana tsuke fuska. Dole na haƙura na koma na kwanta. Daga ƙarshe ma na lumshe idanuna tare da juyar da fuskata ina facing cikinsa. Daga haka nayi luff sai sauraren wayar da aka kirashi yake amsawa nakeyi. Sai dai furucinsa yay matuƙar ɗaukar hankalina. Dan cikin kaushin harshe yake faɗin, “Ko waye ya taɓa koda bangon gidan ne a cikinsu ku kamashi yallaɓai”.

Ban san mi'akace masa daga can ba. Na dai ji ya yanke wayar kamar a ɗan fusace ya wurgata sit ɗin gaba na gefen Hayatu dake driving. Daga haka ya kwantar da kansa shima jikin kujerar ya lumshe idanu. Babu wanda ya sake magana har sai da naji alamar gida muka dawo. Bamma san na ware idanu ina kallon ikon ALLAH ba. Har ƙofar sashensa Hayatu ya faka motar. Duk yanda nake masa kallon mamaki shi yaƙi yarda mu haɗa ido, sai ma taimaka min da yay na fita a motar, kafin nai wani yunƙuri ya ɗaukeni cak babu ko kunyar Hayatu dake a wajen ya nufi sashensa da ni. Ni dai na riga na faɗa a hannun yᵛan sari sai a hankali. Dan kunya dai kam wala a idanun Maash. Banyi zaton akwai kowa a sashen ba sai da muka shigo falon, jin ya tsaya cak yaƙi saukeni yaƙi magana kuma yasa na buɗe idanun nawa. Haɗa ido mukayi, dan haka na ɗan ɗaga gira da kaɗa idanun nawa alamar yaya dai.

Nasa kan shima ya jinjina da cat eyes ɗinsa ya mun nuni da cikin falon. Ai babu shiri na kalla falon da sauri wlhy duk zatona wani abu yake nuna min. Amma mi sai caraf idanuna akan Fahad, Hafizzullah, Aunty Falaq. Ummie, Mama Balki. A wani irin ruɗewa na dirgo jikin nasa. Na koma bayansa da sauri na ɓuya ina jin tamkar ƙasa ta tsage na shige ciki. Dariya Falaq da Hafizzullah da Fahad suka kwashe da shi. Hakan ta sani sake maƙalewa a bayansa ina jin kamar na saki ihu.

“Haba yᵛar Ummie yaya da ɓuya kuma?”.

Wani karyayyen harshe mai nuna rauni da sanyi ya ratsa cikin kunnena. Fuskar Ummie da tai min kamar gizo a kallon dana musu ɗazun ce ta shiga dawo min. Da sauri na ɗan leƙo kaina daga ta bayan nasa zuciyata na harbawa. Sai kawai Maash ya damƙoni ya kawo gabansa. Rawa jikina ya fara ganin tabbas fuskar Ummie ce zaune Hafizzullah da Fahad sun sakata tsakkiya ga baby a cinyarta. Da ƙyar na haɗiye busashen yawu na na furta, “Ummie!”.

“Yes dear”.

Ta faɗa fuskarta na sake ƙawatuwa da fara'a. Sake daburcewa nayi, na juya na kalla Maash dake bayana a tsaye har yanzu. Sosai idanuna suka firfito. Sai dai na gagara magana. Hannuna ya kama tare da fara tafiya da ni a hankali har gabanta. Bamma san na ƙwace hannun ba na zube a gaban nata gwiyawu biyu a ƙasa jikina na rawa. Hannunta ta miƙomin, ai da sauri na ɗaura nawa akai ina ƙarasawa jikinta da jan gwiwa. Sai kawai na samu kaina da fashewa da kuka na faɗa jikinta na rungume ita da jinjirin saman cinyarta. Itama ƙanƙamenin tayi da ƙyau a tare muka saki kuka. Munfi mintuna biyu a haka har sai da yay yᵛar gyaran murya Mama Balki

tazo ta ɗagomu Hafiz ya zare jinjiri da muka matse sannan muka tsagaita. Fuskata Ummie ta riƙe a cikin tafukan hannayenta cike da nuna ƙauna ta ce, “Yaya jikin naki?”.

Kuka na sake fashe mata da shi da rungumeta sosai na ce, “Ummie na warke. Ummie dama kin gama ibadar ALLAH shine babu wanda ya sanar min. ALLAH kaine gagara misali. Ikonka da hukuncinka zartaccene akan komai. Ya rabbi muna godiya da dukkan ni'imokinka garemu. Ya ALLAH ka hanamu saɓa maka akan son zuciya”. Sai kuma na zame a hankali nayi sujidar shukur. Naja tsahon mintuna kafin na ɗago ina mai jera godiya ga UBANGIJI. Kafin na sake ɗagowa na rungumeta.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□ *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-six

66

.....Zuwan likitan Ummie ya taƙaita zaman namu. Duk da dai an ɗan taba hira da zaka iya rantsuwa da ALLAH mun jima da sanin juna musamman ma Ummie da ke jan kowa jikinta. Barcin da allurar ke saka Ummie yasa dole taje ta kwanta. Mu kuma muka dasa sabuwar hira duk da dai akan abinda ya faru ne ga kowannenmu a kwanakin nan uku. Mama Balki ce da taga dare na ƙara zurfi dan Maash tunda ya raka Ummie ɗaki ya haye sama abinsa bai sakko ba tace nima na tashi na wuce tunda ba lafiya gareni ba. Badan naso ba dole nabi umarninta dan dama ƙarfin haline kawai sam bana jin daɗi. Shima kuma Ya Aawab koba komai nayi kewarsa. Sai da na leƙa na duba Ummie dake barcinta hankali kwance sannan na haura saman. Banyi mamakin ganin ko'ina babu datti ba. Har na nufi ɗakina sai kuma na fasa na maida akalata ga nashi ɗakin. Nayi mamakin samunsa tsaye a bakin window tsaye yana kallon waje. Ko kayan jikinsa bai cire ba. Sai da na masa kallon tsaff na gane waya yake yi dan akwai bluetooth a kunnensa. Kamar zanyi magana sai na fasa. Jikina a sanyaye dan wani masifar son kwanciya nake a waje mai sanyi na kai zaune kan carpet. Cikin dabara na kwanta tare da jan jikina na koma saman tiles na kwanta. Aiko sai na shiga sauke ajiyar zuciya a jajjare dan jin daɗin samun

abinda nake so. Na lumshe ido kenan naji kawai an ɗagani a wajen. Buɗe idanun na nayi da sauri ina ɓata fuska sai ya harareni. Baice dani komai ba ya wuce dani bathroom. A bazata kawai na jini a cikin ruwan ɗumi. Kafin nai wani yunƙuri shima ya shigo cikin bathtub ɗin. Jikinsa kawai na shige na rungumeshi. Shima hannu biyu ya amshe ni sai kuma ya fara laluben lips ɗina ya haɗe da nashi. Tuni ya shagaltar da ni har ya cire kayan jikina ma ban farga ba. Sai da ya sakar min lips ɗin kuma naji kunya. Shiko ko'a jikinsa sai ma wanka da ya shiga mun.....

Da zamu fito kam ban yarda ya ɗakkoni ba. Dan nama rigashi fitowa shi ya tsaya alwala. Gaba ɗaya na fice a ɗakin zuwa nawa. Dan nasan babu wanda zan samu a saman namu. Tsaf nai shirin barci na ina mai tsayawa kallon kaina a mirror. Gani nai kamar na canja ma ni a kwanki ukun nan kar kuce na cika ƙarya. Maimakon ni da nasha jiyya a asibiti aga na fige na fita a hayyacina sai na ganni ma na murje fata ta ta wani yi kalar ɗan golden brown kaɗan mai haske bamai duhu ba. Haka dai na shirya na haye gadon na kwanta dan bana jin zan sake komawa ɗakinsa. Sai dai a mamakina ina kwanciya yana shigowa. Daga saman gadon na ɗago ina kallonsa har ya ƙaraso inda nake. Laptop bag ɗinsa ya ajiye tare da wani ɗan bowl mai ƙyau idanunsa shima a kaina. A kusa da ni ya zauna tare da kamo hannuna cikin nashi cikin low murya ya furta, “Baƙya jin yunwa kika zo nan kika kwanta?”.

Kaina na jinjina masa. Sai kuma na yamutse fuska tare da faɗin, “Tea kawai zan sha sai anjima kuma.”

“Why?”.

“Yanzu bana jin yunwa barci ma nake ji.”

Kansa ya jinjina min tare da ɗan shafar kumatuna ya sakko da hannunsa saman cikina nan ma ya shafa. Sai kuma ya yunƙura zai tashi. Hannun nasa na riƙe, hakan ya sashi komawa ya zauna yana kallona. Duk da tsigar jikina ta tashi dan bana jure kallonsa cikin ido haka na daure. Cike da ƙarfin hali naja kumatunsa. “Please My Lion Smalling kodan murnar samun lafiyar Ummie. Ya kamata a yau fuskar nan ya zama tamkar buɗaɗɗen sabon fire mai ƙamshi”.

Idanunsa ya ɗan lumshe sai kuma a bazata ya ɗan saki murmushin. Cike da farin ciki na rungumeshi ina faɗin, “Thanks you my Handsome.” yanda nayi maganar ina hura masa iska a kunne sai kawai naji ya birkitoni. Banyi zaton halin da ake ciki zaisa ya nuna wata buƙata ba. Amma mi sai labarin ya canja salo. Duk yanda naso zame kaina bai fa barni ba sai da abinda nake gudun ya kasance. Sai dai fa misalta muku yanda yau ɗin ta kasance hummmm abine da bazai yiwu ba. Dan wannan sirrina ne, amma dai ta shiga cikin jerin wasu kwanaki masu matuƙar muhimmanci da bazan taɓa mantawa ba a rayuwa ta. A shi kansa nasan hakanne, sai dai ba lallai ka gane ba kasancewar halittar sa ce kamar hakan yakan iya shanye

komai a zuciyarsa shi kaɗai. Da yawan miskilai akance idan abin farin ciki ya samesu kakan iya gani koda a fuskarsu ce shi dai bawan ALLAHn nan sam ba haka bane, zai iya haɗiye miki farin ciki da damuwa ka kasa gane masa. Duk da dai kam na jigata sosai, dan da ƙyar na iya yarda ya taimaka min muka gyara jikinmu saboda barcin da ya gama cinye idanuna ga zazzaɓi. Bamma san yaya akai ya sakan wani kayan barcin ba sai can fitsari ya tadani na gansa ya baje takardu a saman carpet shima yana daga kwance ruf da ciki yana faman daƙilar laptop, gefensa akwai sallaya da Alkur'ani alamar salla ya idar ya kuma dawo wannan aikin. Nayi mamaki, dan banyi zaton zai iya sake wani abu ba musamman a yanda komai ya kasance. Shine ya taimaka min nayi fitsarin dan jiri nake gani, ya sake maidoni ya kwantar. Gabannin asubahi na farka da ciwon ciki. Kafin kiran salla sai amai nake yi ga zazzaɓi sosai a jikina. Hankalinsa yay matuƙar tashi. Babu shiri ya nemo doctor Larai ta asibitin su Hajiya Ƙarama bayan an idar da sallar asuba. Cikin ƙanƙanin lokaci kuwa sai gata. Sama-sama nake jiyo muryar Ummie da Mama Balki da doctor Larai ɗin a kaina... Sai da Ummie ta riƙoni jikinta ta rungume sannan na ɗan buɗe idona, da ƙyar na iya furta “Ummie ruwa zan sha”.

Fuskarta cike da damuwa ta ce, “Ruwa kike so?”.

Kaina na ɗaga mata hawaye na zubo min. Dan sam bana jin daɗin jikina. Har Mama Balki ta ɗakko ruwan Dr Larai ta hana su bani, ta tabbatar musu amai zanyi idan nasha. A ɗan samu na ɗumi dai a bani kafin ta gama haɗa ruwan da zata saka min. Haka dole akayi, sai dai ni ruwa mai sanyi nake so. Dan haka na sanya musu kuka. Dai-dai nan Maash ya shigo da abu a hannu. Tunda yay sallama idonsa a kaina ƙyam, kai tsaye in da naken ya ƙaraso, Ummie nata ƙoƙarin lallashina nasha ruwan ɗumin. Da ƙyar dai na yarda nasha maƙwarwa biyu kawai. A hakan ma sai da nai yunƙurin aman ALLAH dai yasa banyi ba.

Bayan doctor ta gama haɗa ruwan ta buƙaci a gyara min kwanciya. Nayi zaton zai bar Ummie da Mama Balki sumin amma babu kunya ya kamani da kansa daga jikin Ummie ya kwantar da ni saman dagon duk yanda doctor ɗin ta buƙata. Yana zaune a gefena shi da Ummie sun sakani tsakkiya hannunsa riƙe da nawa aka ɗaura min ruwan. Da farko yamutse-yamutsen fuska na dingayi da ruwan ya fara shigata, sai da ya fara gauraye jikin nawa sannan na fara sauke ajiyar zuciya.

Ummie ce cikin sauke numfashi ta dubi Dr Larai, da karyayyen harshen nan nata ta ce, “Doctor kodai asibiti zamu koma ne. Yarinyata na buƙatar text gaskiya musam dalilin ciwon cikin nan da take ta complain.”

Murmushi Doctor Larai tayi, cike da girmamawa ta ce, “Ranki ya daɗe in sha ALLAHU nai miki alƙawarin samar da duk wata kulawa gareta anan gida. Text kuma ina ganin basai mun sake mata ba. Dan result ɗin da wancan asibitin suka bada game da ciwon nata babu wani kuskure. Sai dai kamar yanda suka faɗa tana buƙatar bed rest sosai gaskiya. Dan cikin nan har yanzu bai zauna da ƙyau ba.”

Idanu sosai Ummie ta waro da ga ita har Mama Balki. Duk da ita Mama Balki taso zargin hakan. Itama Ummien taso zargin hakan amma dai tafi son ji a bakin likitar dai. Murmushi Dr Larai tayi da faɗin, “Oh baku sani ba ashe. Da alama Alhaji ya shirya muku bazata ne dai kenan”. Ta ƙare maganar tana ɗan kallon sashen da Maash yake kamar yanda Ummie ma ke kallonsa. A mamakinsu sai suka ga ya ɗan kauda kai yana murmushi.

Kasa haƙuri Mama Balki tayi sai da ta sanya dariya. Sannan ta ce, “Kai Masha ALLAH. Alhaji ƙarami kuma sai a ɓoye mana mijin? Ko dai kishiya ce shiyyasa ba'a son mu sani?”.

Ɗagowa yay ya kalla Ummie, sai kuma ya maida idonsa akan Mama har lokacin da guntun murmushin a fuskarsa. A nutsen nan nasa ya ce, “Ni Mama ba ruwana. Ita ce tace nayi shiru da bakina tana jin kunyarku, tana son kuma mu rama yanda Ummie ta ɓoye mana samun lafiyarta muma”.

Bamma san na buɗe idanuna da sauri ba duk da nauyin da suka min. Fuskata a marairaice kamar zanyi kuka. Da wani shegen salonsa ya kashe min ido ɗaya tare da motsa lips ɗinsa a hankali ya ce, “Koba haka kika ce ba?”.

Tsabar kunyar da naji bamma san na saki kuka shagwaɓa da faɗin, “Ummie kin gansa ko. ALLAH ni sharri yake mun”.

Ranƙwashi Ummie ta kai masa bisa kai, kafin hamnun nata ya sauka a kan nasa ya miƙe yana murmushi yay hanyar ƙofa. Dariya Dr Larai da Mama Balki suka sanya. Itama Ummien sai ta girgiza kai tana murmushi da kamo hannuna cikin nata ta ce, “Ƙyalesa kinji. Nasan shine bake ba. ALLAH ya baki lafiya, ya saukeki cikin aminci kinji”.

Kasa amsawa nayi da Amin, dan sai naji gaba ɗaya kunya ta lulluɓeni fiye da farko. Wlhy Maash na neman sakani taɓarewa. Ban sake yarda na buɗe idanun nawa ba, ina dai saurarensu sunata cigaba da murnarsu Ummie harda sujidar shukur tayi, lallashin da Mama Balki naji tana mata yasa na fahimci hawaye take yi. Ban san yaya suka ƙare ba dan barci ya fara cin ƙarfi na. Ko shigowar Fahad da Hafizzullah sama-sama na jiyo barci yay gaba da ni.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-seven

67

.....A ɓangaren Baba prof sai da likitansa yaje gida ya dubashi. Dan Uncle Abdullahi na tare da shi. Doctor ya tabbatar masa da jininsa ya hau sosai. Ya kamata kuma ya kwantar da hankalinsa koma mike faruwa dan bugun zuciyarsa har ya canja. Nan dai ya bashi shawarwari tare da masa allurar barci dan ya ce yana buƙatar hutu na awa kamar goma. Baba prof ɗin bai musa ba. Dan shima a karan kansa yana buƙatar hakan kam gaskiya...

Uncle Abdullahi bai baro gidan ba sai da yay barci ko nace aka kira wayarsa. Yanda ya baro gidan a gaggauce yana bama ɗaya daga cikin ma'aikatan umarnin kwanciya a falo dan ya dinga ankare motsin Baba prof ɗin zaka tabbatar da kiran da akai masa mai muhimmanci ne. Wanda aka saka kwanciya a falon yana ganin Uncle Abdullahi ya fita ya wani faɗa saman kujera ya kwanta, koba komai banza ta faɗi yau. Dan har wani barbaje ƙafafu yake ransa fes. Bai wani bi takan Baba prof ya hau barcinsa harda minshari. Da wannan damar baƙon da basu san da shi ba a gidan tun ɗazun ya sami damar shigowa ya wuce har bedroom ɗin Baba prof ɗin. Tsaye yay a kansa yana kallonsa, sai kuma yay dariya da faɗin, “Mugu kenan uban mugaye”. Ƙaramin kwandon kaba dake a hannunsa ya buɗe yana kallon kunamin ciki manya-manya har guda uku. Baƙa, sai fara tass tamkar mara jini. Ga kuma mai kamar gold. Yanda suke ta faman ɗaga bindina sama zai baka tabbacin dama kawai suke jira. Murmushin mungunta kawai ya saki tare da ɗaukar su ɗaya bayan ɗaya da hannunsa dan shi yasha maganinsu babu abinda suke masa, Safar ƙafar prof ya buɗe ya saka ɗaya. Ya buɗe wandonsa😷 ya saka ɗaya. Sannan ya ɗakko hula a gefensa tsabar iya mungunta ya saka ɗaya a ciki ya kifama Baba prof hular a ka. Hancin sa ya kama ya ɗan ja cike da shaƙiyanci ya ce, “Barci lafiya tsoho, ni JAGA ina gaisuwa”. Ya juya yay ficewarsa yana dariya....

Jaga😷??????.

□□□□□

Kai kawo kawai take tana faman lissafa mintuna. Kaɗan-kaɗan kuma ta kalla wayarta dan babu abinda take fatan gani a yanzu sai kiran Jannifer. Rawar da ƙafafunta keyi da jin zuciyarta kamar zata wantsalo saboda ƙaguwa ya sata faɗawa

saman gadonta. Kirjinta ta dafe tare da shaƙar numfashi ta fesar. Ita likita ce ta san irin wannan saka abu a rai yayta azalzalarka zai iya kawo heart attack ma. Dan bugun zuciyarta yay masifar ƙara ƙarfi. Kamar da wasa taji abu ya soketa. Jimm ta ɗan yi sai kuma ta share. Kara sukar ta akayi a wani wajen da ban. Azabar data ratsata ta waje biyu a lokaci guda yanzu kam ya tilastata tashi zaune tana kai hannu wajen da ɗan wawwaigawa amma babu komai a inda taken. Tashi tai ta fara ɗage-ɗagen filos da duvet, ɗayan hannun kuma tana taɓa inda zugin ke ƙaruwa mata har waje biyu. Kamar wasa sai da azaba ta sata sake kaiwa kwance, nan ma aka sake ɗalla mata. Ina bazata iya jurewa ba, da sauri ta mirgina ɗayan gefen tana sakin ihu. Aka ƙara bata wani harbin. Kafin dai ta fasa ihun da aka kawo mata ɗauki an mata ɗalli yafi bakwai. Zufa kuwa ta gama jiƙeta ta sharkaff harda sakin fitsari. Da sauri Bahijja dake laɓe ta fice tana dariya.

Kusan cin karo sukai da Rubayya dake ƙoƙarin zuwa ta sanar mata plan ɗin su fa na neman rugujewa dan Hajiya Mammah na tare da yar uwarta Mashi'a a ɗakin Mashi'ar bata san mu suke tattaunawa ba, ko kallonta Bahijja batai ba tai wucewarta. Da kallo ta bita ita kuma zuciyarta na ayyana mata itama nemanta Hajiya ƙarama keyi, shiga tai ranta a ɓace, sai ta sameta cikin wannan hali. Kamata tai ta riƙe dan yanda jikin Hajiya ƙarama ke rawa ga zufa ta mata sharaf ya isa baka amsar babu lafiya. Neman shiɗe mata take, dan haka ta rungumota jikinta sai ko ta samu nata rabo itama aka bata har harbi biyu. Tuni ta saki Hajiya ƙarama a ƙasa ta ƙwalla ƙarar data jawo hankalin mutanen gidan. Har rige-rigen shigowa Hajiya Mammah da su Arwa akeyi. Mamaki ya kama kowa yanda Hajiya Rubayya ke birgima a ƙasa tana ihu da rike inda aka harbeta. Ga kuma Hajiya ƙarama kwance a ƙasa tai sharkaf da zufa tama kasa kukan ita dan abinda ke harbin nata fa na jikinta kuma basu daina ba. Arwa ce ta fara nufarta, hannu tasa ta kamo mahaifiyar tata zuwa jikinta, kafinma ta gama mannata an bata rabonta. Kara ta ƙwalla da sakinta timm a ƙasa tai baya tana ɓalla ihu da riƙe hannunta.

Da sauri Hajiya Mama ta ce, “Ya Salam mike faruwa ne haka? Ke Arwa lafiya?”. Tai maganar tana kaiwa zata taɓa Hajiya ƙarama Hajiya Mammah ta riƙeta da jawota baya. “Auta! Baki da hankali ne. Kina ganin daga taɓa da yarta tayi itama tana ihu ga Rubayya kwance ke sai ki kai kanki?”.

“Amma Adda ya kamata musan mike faruwa ai”. Hajiya Mama ta faɗa cike da damuwa. Masifa Hajiya Mammah ta fara mata dan ita wani irin kishi ne ya taso mata. Ganin Rubayya a ɗakin Hajiya ƙarama sai zuciyarta ta ayyana mata amanarta suke ci ALLAH ya saka mata. Duk yanda Hajiya Mama taso taimaka musu Hajiya Mammah ta hana. Ashe shi tsautsayi baya wuce ranar sa. Dan Azizat na maƙale a baya sai ji sukai ta ƙwalla ƙara. Juyowar nan da zasuyi kanta sakamakon tsallen data buga gefe kawai Hajiya Mammah ta maye gurbin ƙafarta akan baƙar narƙeƙiyar kunamar data ɗalli Azizat ɗin a ƙara. Itama ƙarar ta fasa tana mai yin tsalle gefe dan har cikin tsakkiyar kai taji harbin nan. Ai ko kaɗan ya rage Hajiya Mama data firgita itama ta taka ALLAH dai ya kiyaye Ilham ta riƙeta da sauri tana faɗin “Mama Scorpion”.

Garrrr kunamar dake neman ceton ranta itama ta shige ƙasan gado Hajiya Mama na kallonta da Ilham. Sai yanzu suka fahimci abinda ke faruwar...

Dole fa aka kira ma'aikatan gidan. Anci sa'ar akwai wanda suka sha maganinta. Dole sune sukai kama-kamar ɗaga su Hajiya ƙarama zuwa mota. Anan ne wasu kunamun har biyu suka faɗo ashe a jikin Hajiya ƙaramar suke. Asibiti aka wuce da su su duka biyar din. Su sunata ihu Hajiya ƙarama kuwa tuni ta suma ma ita dan azaba. Wannan al'amari ya matuƙar bama kowa mamaki. Duk da ana shan kashe kunamu a gidan harma macizai a wasu lokutan saboda garden amma ba'a cikin gida ko ɗaki irin haka ba. Abinma tambayar miya kawo kunama har cikin jiki haka? Ba kuma ɗaya ba har uku, Babu mai basu amsar tambayar nan dan basu sani ba.

Duk wannan bidirin da akeyi fa babu wanda ya sani a ɓangaren su Maash. Sai Hafizzullah ne dake salla ya ɗan fito. Ana wucewa da su asibiti kuma ya koma ciki shima abin na bashi mamaki. Shine ya samu Fahad ya tashi. Tambayarsa yayi ina yaje? Ya bashi amsa da “Gidan ne fa babu lafiya. Kunama ta harbi har mutum biyar gasu can an wuce asibiti da su.”

“Ikon ALLAH kunama kuma a gidan nan? Dawa-dawa?”.

“Wlhy nima abin yaban mamaki. Hajiya Mammah da wata mata baƙuwa sai budurwar nan mai iyayin tsiya mai kama da sadakar yalla da kuma wadda ka saka ranar ta kawo mana abinci baƙar nan da Mamanta ita tama suma”.

Dukansu ya gane su, idan ka cire baƙuwar da bai san wacece ba. Haka kawai sai baiji komai a ransa ba ya ce, “ALLAH ya ƙyauta” kawai ya tashi ya shige toilet. Alwala yayo shima dan yanzu ya dage ta tashi sallar dare saboda Hafizzullah da ya ga yanayi. Dan Hafiz akwai ibada gaskiya. Training ne kuma daya samu daga Yaya Musaddiq tun yana ƙaraminsa. Dan tun sanda ya fara wasa da salla ganin Mom nayi da yaranta Musaddiq ya dage a kansa har sai da yaga ya dawo hankalinsa. Daga nan kuma abin ya shigesa sosai bai sake sakaci ba sai ma Alhmdllh....

□□□□□

Masu iya magana kance rana dubu ta ɓarawo ɗaya rak take zama ta mai kaya. Tabbas hakanne ta faru a daren yau da mutane guda biyu da yaransu. Dan jami'an tsaro sun samu nasarar cafke Commondo da yaransa biyu. Sai Madam Jannifer da yaranta huɗu harda dattijuwar tsohuwar nan ta gidanta Mama. Su dukansu kuma an cafkesu ne a lokacin da suke shiga gidan da suka ɓoye Paah batare da shi Commondo ya san da zuwan su Jannifer ba. Amma su su Jannifer sun san da zuwansa dan sun mayi shirin ƙwamushesa ne shima bisa umarnin Hajiya ƙarama.

Sai dai basu san an saka tarko a gidan ba tun yammaci sakamakon bayanin da Maash ya bama su Isma'il akan inda su Commondo ɗin suka kai Paah.

Gaba ɗayansu hankalinsu ya matuƙar tashi. Duk da dai shi Commondo yana ganin kamar duk iya ma miza'ayi zuwa safiya sai Baba prof ya fitar da shi. Itama dai Jannifer ɗin tana da ɗan nata hope ɗin na ganin manyan ƙwarin da take huɗɗa da su zasu fitar da ita zuwa gobe. Yaransu ne dai hankalinsu ke matuƙar tashe musamman yaran Jannifer da irin haka bai taɓa faruwa da su ba. Wasu ma a cikinsu kuka sukeyi. Abinda kuma ya sake ɗaga musu hankali da akaje station ɗin da su gaba ɗayansu rarrabasu akayi babu wanda aka haɗa da ɗan uwansa...

Kai tsaye asibiti aka wuce da Paah duk da babu wani rauni a jikinsa. Sai dai yunwa ta galabaitashi dan ko sun bashi abinci baya wani ci sosai sakamakon azababben yajin da suke cika masa. Gashi yana da urlser. Taimakon gaggawa aka shiga bashi, sai dai ba'a sanar da kowa a gidansu ba kasancewar dare ya riga yayi. Garama Isma'il ya turama Maash text message sai dai shi kuma hankalinsa bai kai ba dan lokacin kam yana wani tsagin daban kuma. Da safe suka tashi da tashin hankalin yanayin Samraah. Sai da doctor ta dawo duba jikin Samraah da azhar suke jin ai su Hajiya Mammah na asibitinsu an kaisu jiya da dare kunama ta harbesu. Musamman ma Hajiya ƙarama har yanzu tana cikin azaba. Tana tsaka da musu wannan bayani aka kirata wai tazo asibiti akwai matsala ga Baba prof an kai shima kunamu sun masa kaca-kaca da harbi har a saman kansa. Yanzu ma'aikatan gidansa suke kawosa...

A firgice tama su Ummie bayani ta fice akan tana zuwa. Abin mamaki Maash ko tari baiyi ba sai ma hayewarsa yay sama kamar ma bai ji mi aka faɗa ba.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

.....Da kallo kawai su Ummie suka bisa har ya ɓacewa ganinsu. Uwa uwa ce koda kuwa sakarai ce. Dan a take kan Ummie ya kawo mata haske. A zuciyarta ta raya (Anya ba Muhammad bane?) Sarai tafa sanshi idan aka masa sai ya rama. Wannan halin nasa tun yana mitsitsinsa yana matuƙar damunta. Tasha masa addu'ar ALLAH ya yaye masa shi. Ganin ya lafa daga baya sai tayi tunani ai ya barsa gaba ɗaya. Ashe-ashe.

Falaq ce ta fara ƙyaƙykyalewa da dariya da faɗin, “ALLAH yaja kwana Yayana”.

Kallonta duk sukayi, ta ɗauke kanta kamar ba ita tai maganar ba. A take itama Mama kanta ya kawo haske. Lallai kam zata iya yiwuwa Awwab ɗin ne. Wato ya rama musu abinda ya faru da su. Kai jama'a wannan hatsabibin yaro sai a barshi. Itama dai sai da ta murmusa. Hafiz da Fahad basu fahimci komai ba. Dan haka sukabi Falaq suna mata nacin tambaya. Cikin raɗa ta faɗa musu komai da abinda ta fahimta. Idanu Hafiz ya waro, yana haɗa 1+1 a ransa. Eh lallai biri yayi kama da mutum. Idan ba haka ba tayaya kunamar sai selecting mutanen data harba harda ma wanda bai kwana a gidan ba. Wato Maash abin tsoro ne. Dariyar Fahad ta maido Hafizzullah hayyacinsa. Sai kawai shima ya fara dariyar suka tafa.. ita Falaq ma sai ta koma yar kallo, dan ta kula sun fita iya shege...

Sai da sukai mai isarsa Hafizzullah ke faɗin, “Ya Fahad anya kuwa ba yarinyar nan bace tai aikin nan? Dan lokacin da ake fita da su gidan nan na ganta tana dariya acan baya laɓe”.

Cikin zaro idanu waje Fahad ya ce, “Kuttt wace yarinya?”.

“Kamar Bahijja naji suna kiranta cikin masu aikin nan”.

Salati Fahad yasa kafin yaja hannun Hafizzullah suka fita. Kai tsaye sashen masu aiki suka nufa. Karo na farko kenan tun zuwan Hafizzullah ya shigo nan ɗin, iyakarsu sashen su Mama Balki. Shi kansa Fahad ɗin zai iya rantsuwar bai fi sau biyu ya taɓa shiga ba. Cikin sa'a ma suna buɗe ƙaramin gate ɗin sashen suka hangota tana shanya kaya da alama wanki tayi sai raira yan wakoƙinta take. Kiran da Fahad ɗin ya mata yasa ta ɗan juyo a firgice, sai kuma duk ta daburce dan ya tsuke fuska hakama Hafizzullah. “Biyomu”. Ya faɗa murya a dake yaja hannun Hafiz suka juya. Gaba ɗaya sai ta ƙara rikicewa. Haka tabi bayansu hawaye na taruwa mata a ido. Itafa tana shakkar Ya Awwab sosai saboda baya wasa da yara. Amma wannan Ya Fahad ɗin tafi tsoronsa barema yanda yake cewa zai ma mutane yankan rago.

Ganin sun nufi sashen Fahad ɗin ta sake ruɗewa. Dogarewa tai ƙoƙarin yi a bakin ƙofa Fahad ya daka mata tsawa. Ai babu shiri ta shigo tana hawayen da take dannewa. Ƙasa ta durƙushe daga ɗan bakin ƙofa. Yanda duk take a ruɗe dariya ke bala'in cinsu. Amma duk suka danne Fahad ya ɗakko takobinsa ya ajiye. Murya a dake ya ce, “Kece kika sakama yan gidan nan kunamu jiya ko?”.

A wani mugun firgice ta ɗago tana zabga salati kamar tsohuwa. Zata fara rantse-rantse ya zaro takobin a cikin kufanta. Hafiz ya kalla ya ce, “Broth rufe min ƙofar falon nan ka riƙe min ita idan bata faɗa ba saina cire mata harshe.”

“Lahhhh ina ha illahu.... Ni Bahijja na shiga uku. Dan ALLAH Uncle Fahad kar muyi haka da kai.”

“Idan baki son muyi hakan faɗa min yanda akai kunama taje jikinsu?”.

Kuka Bahijja take sosai dan ta shiga tsaka mai wuya. Tunda take abubuwanta a gidan nan wani bai taɓa kamata ba sai yau. Bata son faɗa amma tana tsoron Fahad ɗin nan. Ganin dai Hafiz ya rufe ƙofar falo ta ƙara sakin kuka da faɗin, “Wlhy ni ce. Na sakama Hajiya ƙarama a kayan barcinta data ajiye saman gado ne tana wanka. Na saka biyu a aljihun wando biyu a aljuhunan rigar. Shine shine na laɓe, to bata fara cizonta ba sai bayan kusan mintuna goma, su kuma sauran taimakonta suka zo yi suka sami rabonsu....”

Kafinma ta kai ƙarshe Fahad ya bushe da dariya. Ganin haka itama sai kawai ta fara dariyar saboda tuno yanda Hajiya ƙarama ta dinga yin ƙaramin disko. Cikin dariya Fahad ya nuna Bahijja yana faɗin, “Yarinyar nan ALLAH ke muguwa ce. Ina kika samo kunama da bata cijeki ba?”.

Sai da ta ɗan sosa kanta sannan tace, “Ai nasha magani. Na kuma ramawa su Uumie ne ranar da suka sa ta cijesu”.

“Oh woow! Aiko nima dole a bani maganin nan kodan irin wannan ranar. Fantastic”.

Haka dai sukaita nishaɗin su ita dai Bahijja ma sai ta zama yar kallo....

★★★

Zuwan likitan Ummie yasa bata nema Maash dan taji gaskiyar magana ba. Ga zancen cikin nan na Samraah ya ɗaukaka farin cikinta yau matuƙa. Kasancewar suna mata allura tasha magungunanta sai barci yau ma hakanne. Doctor kuma ya sake tayata murna da in sha ALLAHU bai wuce ya ƙara shan magunguna na watanni uku zuwa huɗu ba abubuwanta su dai-daita. Abinda yasa ma zai kai haka saboda an jima ana mata allurorin da suka so jawo mata babbar matsala. Sai dai Alhamdullah

komai zai zama labari. Shima bazai basu bayanai bane saboda akwai abinda yake shiri kan likitocin da suka kula da ita ɗin ta bayan fage. Sai ya kammala bincikensa sannan zai mata cikakken bayani. Ummie ta gamsu, ba kuma ta matsa da sai taji ɗin ba. Barci ne ma ya rinjayeta har doctor ɗin suka ƙarasa abinda suke suka fice bata sani ba kuma....

❤❤❤

Ban tashi farkawa ba sai gabannin azhar. Yana kwance a kusa da ni da alama shima barcin ne ya kwashesa. Nauyayyun idanuna kawai na zuba masa tsahon lokaci, kafin na sauke ajiyar zuciya da kai ɗayan hannuna saman tattausan gashin kumatunsa na shafo. Janyewa nayi ƙoƙarin yi ya riƙe hannun tare da buɗe idanunsa a hankali ya saukesu kaina. Idanu muka zubama juna cikin wani bahagon yanayi kafin ya lumshe nasa tare da matso da fuskarsa daf dani har hancinanmu na gogar juna.

“Kin ta shi?”.

Ya faɗa yana ɗaura hannunsa akan wuyana. Idanuna na ɗan lumshe masa na buɗe alamar eh.

“Mike ciwo yanzu?”.

Kaina na ɗan girgiza masa alamar babu. Numfashi ya ɗan sauke da sumbatar lips ɗina kaɗan, sai kuma ya janye hannunsa dake saman wuyana ya maida saman cikina. Yanzun ma da raɗa ya ce, “My Baby fa?”.

Hannunsa na ɗan mintsina cikin tura baki na ce, “Ni ban santa ba”.

“Jealous ba?”.

Yay maganar da ɗan goga hancinsa kan nawa.

“Ba wani jealous nima ai Ummie na na sona. Ga kuma Mama”.

“Kidai tsaya a Ummien taki banda ƙwacen Mamana. Dan kin san ita ɗin tawace ni kaɗai. Falaq ma sammata nake”.

Murmushi nayi a karo na farko. Na ce, “Yaya!”.

“Uhhmyim My Tiger”.

“Har yanzu ba'a san inda Paah yake ba? Ina ka shige duk wannan dambarwar baka zo ba sai daga baya?”.

Shiru ya ɗan yi kamar bazaice komai ba. Sai kuma ya buɗe idanunsa yana kallona. Yayinda hannunsa ke saman fuskata yana shafa gashin girata da yatsarsa babba. Muryarsa can ƙasan maƙoshi ya furta, “Paah dama nasan a inda yake, na barsu ne kawai naga iya gudun ruwansu Samrh”.

Idanu sosai na waro da faɗin, “Yaya da gaske?”.

Kansa kawai ya jinjina min.

Murmushi nayi tare da sumbatar mitsitsin bakinsa kaɗan, ina ƙoƙarin janyewa ya riƙe lips ɗin nawa da nashi. Sai da ya tabbatar ya samu yanda yake so sannan ya barni. Muryarsa a shaƙe cikin kunnena ya furta, “Kema kina buƙatar mijinki ba?”.

Maimakon na bashi amsa sai kawai na shige jikinsa na rungumeshi dan kunya maganar tashi ta bani, shi ba ruwansa kai tsayensa yake magana ba kwana-kwana. Sosai ya riƙeni shima batare da ya sake cewa komai ba. Daga haka ɗakin yay shiru tsawon lokaci tamkar barcin muka koma amma duk idonmu biyu. Kiran salla ya sakashi sauke ajiyar zuciya, tare da ɗagani a hankali zai gyara min kwanciya na yunƙura nima. Sai kawai ya zaunar dani na jingina jikinsa. Yanda ya tsareni da kallo yasa na kasa kallonsa ni. Sai naji ya ɗan furzar da numfashi. Sauka yay tare da ɗagani cak a gadon. Fuskata a marairaice na ce, “Nifa ina iyawa”.

Komai baice dani ba har sai da muka shiga ciki bayin ya direni a bathtub sannan ya kamo jaw ɗina. Ɗago idanuna nai nima ina kallonsa. Yanda yake wani bina da narkakken kallo yasa tsigar jikina tashi, har sai da na sauke ajiyar zuciya a hankali. Shima iska ya ɗan furzar kaɗan, tare da furta, “In dai ina cikin gidan nan kin daina komai sai kula da ni shima a be.....” da sauri na kai hannuna saman bakinsa na rufe. Janyewa yay yana murmushi.

“Kin san mizan faɗa ne kika wani rufen baki”.

Bakina na ɗan tura nima da faɗin, “Nidai ba ruwana. Ga abinda nake son ka faɗa min ka tafi wanda ba'a sakaka ba”.

“ALLAH yarinyar nan kin lalace. Toni mi nace zan faɗa kike neman fassara min zance?”.

Kaina na juyar ina murguɗa baki na ce, “Ni dai ba ruwana”.

Murmushi ya sake saki mai ƙayatarwa da kai hannunsa saman cikina ya shafa. A mamakina sai jinai ya ce, “My blood kada kiyi rashin jin Ammien ki kinji”.

Harararsa nayi nima na ɗora hannuna saman cikin na ce, “My blood kada kayi miskilancin Dadaan ka kaji”.

Dariya muka saki a tare, ya dunguremin kai. Nima hancinsa naja da alama mun manta a bayi muke.....✍

(Nima dai na fara tunanin kun manta a bayin kuke□□□□).

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page sixty-nine

69

....."Wai kai lado yau mike damunka ne? Motsi kaɗan sai ka wani kwashe da dariya. Kai ko damunka abinda ya faru da oga kamar baiyi ba ma. Alhalin idan binciken inda aka samo kunamu aka zo yi wlhy kai zasu kama tunda kaine ka kwana da shi".

Dariya wanda aka kira lado ya sake kecewa da ita, sai da yay mai isarsa sannan ya ce, "Bazaka gane ba Hamisu. Wlhy ko kaine zakai dariyar da tafi tawa ma. Ka koga wani gigitaccen ihu da Yallaɓai yayi, ai ni nasha kallo. Da gudu fa ya fito falo ya kwaɓe wandon sai ɗan panti. Hannunsa kan jikinsa ya damƙe yana rabga ihu. Badan Kuka ya taimaka ya rufe ƙofaba da har tsakar gidan nan zai fito a haka hhhhhh!!!!" ya ƙara kwashewa da dariya. Da ƙyar ya cigaba da faɗin, "Kama-kama mukayi da Kuku wajen kamashi amma ina sai rawar disko dansa yake. Ashe bawan ALLAH abune goma da ashirin ya ishe shi. Kunama a wando, kunama a cikin hula ga wata a ƙafa tana bashi wuta. Haka dai muka dannesa muka cire panti da ƙyar shegiyar ta manne kuwa tanata aikin da aka sakata. Shiyyasa jikinsa fa ya kumbura tunkan a bar gidan nan sai bargo aka lulluɓa masa. Bakaga har mukaje asibiti dubasa da alama babu wandon ba hhhhhh!!! ALLAH alhakinmu ne anƙi bamu albashinmu, ALLAH yay ma wanda yasa kunamar nan albarka hhhhhhhh!!!!".

Duk yanda Hamisu yaso ƙin biyewa lado hakan ya gagara. Shima sai da ya shiga kwasar dariyar.....

Baba prof ashe haka abubuwa Suka kasance harda rawar disko dansa😆😆, Sai munzo dubiya dai to, ALLAH yasa sannan ka fara saka wando😂□□□.

□□□□□

Kusan lokaci ɗaya Ummie da Samraah zamuce sun farka. Wanka ta farayi dan in dai tai barcin nan sai ta jita Alhamdullah jikin kuma yay mata sakayau. Kasancewar Mama Balki na yawan shigowa dubata sai ta kawo mata abinci ganin ta tashi. Bata wani zauna ba dan tana acan sashensu ne tana shiryama Baba abincin da zai kaiwa Malam can masaukinsa. Koda Ummie ta fito salla ta farayi, ta yi karatun Alqur'ani sannan ta zauna cin abincin dan yanzu kam tana cin abinci saboda magungunan na sakata jin yunwa. Tana farawa Fahad da Hafizzullah suka shigo. Cike da farin ciki take kallonsu. Dan har cikin ranta take jin son Hafizzullah. Duk da har yanzu babu wanda ya faɗa mata wanene shi sai take zargin Mama Balki ce ta haifesa saboda tsantsar kamarsa da Falaq. Zama sukai suka sakata tsakkiya. Fahad ya amshi spoon ɗin hannunta ya cigaba da bata abincin, itama saita dinga basu a baki Fahad nata tsiyaya mata surutu akan halin da su Baba prof ke ciki na harbin kunama dan su da sai da sukaje asibiti dubiya ko nace sa ido, shi dai Hafizzullah nashi dariya ne. Sai in anzo gaɓar daya sakosa ko yace koba haka ba? Dan tabbatarma Ummie sannan Hafizzullah ɗin ya bada amsa. A haka Maash ya shigo ta samesu. Sanye yake cikin baƙar jallabiya mai gajeren hannu data masa ƙyau sosai. Idanu duk suka ɗago suna kallonsa, kafin Hafiz ta fara gaishesa. Shima Fahad sai ya gashesa tare da faɗin, “Yaya irin wannan ƙyau haka, kamar kaine ma ke rainon Babyn wlhy”.

Idanu Hafizzullah ya waro sosai akan Fahad, dai-dai Maash na ɗaukar gwangwanin turare akan mirror ya wulwulo masa. Da gudu Fahad ɗin ya miƙe ya fice. Hakan yasa Hafizzullah dake ƙunshe tashi dariya shima miƙewa ya fita da gudu. Ummie ma dariya take yi, cikin dariyar ta ce, “ALLAH ya shiryeka Fahad”.

Fuska Maash ya narke a marairaice ya ce, “ALLAH ya rainani Ummie. Ranar fa ina jinsu wai zaimun yankan rago”.

Dariya Ummie ta sake kwashewa da shi. Dan itama a ranar komai a kan idonta akayi tana leƙensu ta balcony ɗin sashenta batare da su sun lura da ita ba. Sai dai a tunaninta ma shi baya gidan a lokacin tunda bataga ya fito ba sai Samraah. Sosai dariyar Ummien ke sakashi farin ciki. Dan Doctor ya tabbatar masa duk cikin nasarorin samun lafiya ne. Yanda ya zuba mata idanunsa da ɗan ruwan hawaye ta cika yasata miƙewa ta buɗe masa hannayenta alamar yazo gareta. Babu musu kuwa ya iso. Shigewa yay ta rungumesa. Sai kawai ta sakar masa kuka. Daburcewa

yay ya ɗago da sauri jikinsa har tsuma yake. Fuskarta cikin tafukan hannunsa muryarsa na ɗan rawa ya ce,

“Ummie miya faru kuma?. Kar kuyi kuka dan ALLAH”.

Murmushi ta saki tana mai kai nata hannun itama ta shafa fuskarsa. “Muhammad ina kukan farin ciki ne barni nayi. ALLAH ya muku albarka kaji. Gaba ɗaya zancen cikin nan na matarka ya wanke dukkan dattin zuciyata. Na godema UBANGIJI da ya bani rahamar samun waraka tare da ƙyautar zuri'a daga tsatsonka. Ka saka a ranka wannan itace ƙyauta mafi girma da kuka fara bani bayan samun warakata.”

Rungumeta ya sake yi shima cike da farin ciki yana mai ƙoƙarin haɗiye hawayen da suka cika masa ido. A hankali ya furta, “In sha ALLAHU Ummie zamu cigaba da baki irin wannan ƙyautar har sai kince sun isheki da amincewar UBANGIJIN rahama mai badawa a sanda ya so ga kuma wanda yaso.”

“ALLAH ya tabbatar Muhammad ɗina.”

Daga haka suka zauna. Sai kallonta yake yi yanaji kamar ya haɗiyeta dan tsananin ƙaunar da yake mata a rayuwarsa. Kamar yanda itama take jin matsanancin ƙaunar gudan jinin nata. Muryarta a sanyaye ta ce, “Ya kamata muje muga su Baba asibiti. Amma harbin nan na kunamu ya bani mamaki kamar an tsara musu hakan”.

Kauda kai Maash yayi kamar baiji ba. Sai da ta ce, “Nasan ka jini ai. Na kuma tabbatar a yanzu cewar kai ne”.

“Ummieeee!”. Ya faɗa fuska a narke.

“Ba wani Ummie anan. Miyyasa kayi haka?”.

Murmushi ya ɗan yi da faɗin, “Kai Ummie sa ido ne fa wannan”.

“Nayi saka idon ja'iri”.

Ƙaramin murmushi yayi kawai, sai zuwa can ya ce, “Yanzu ma aka fara, har sauron da suka saka ya cijeki sai na rama miki”.

Salati Ummie ta sanya tana tafa hannaye. “Oni Ummu-Hidaya kai ɗin ne dai kenan Muhammad. Ya ALLAH ka shirya min wannan yaron da ya girma bai san ya girma ba. To ai basu suka saka kunama ta harbemu ba ALLAH dai ya ƙaddara”.

Ƙin cewa komai yayi sai fuskarsa daya tsuke kamar bashi ba. Juyawa yay ya fuskanci Ummien da ƙyau. Cikin dakewar nan ta shi ya ce, “Ummie ina son na san gaskiyar komai a yau?”.

Murmushi tayi mai ƙyatarwa. Tare da kamo hannunsa ta sumbata. “Karka damu My dear zaka sani amma ba yau ba. Kai nake son ka sanar min abinda duk ya faru da ga lokacin dana sake komawa halin haukar nan har zuwa yau? Amma kafin hakan ina son nasan Companyn dana ce ka buɗe a Kano ya fara aiki?”.

Kansa ya jinjina mata..

A hankali ta saki murmushi mai ƙayatarwa tare da lumshe idanunta ta furta, “Alhamdullahi ya Rabba. Muhammad ALLAH yay maka albarka. Hakan na tabbatar min zuwa yanzu kasan ainahin fuskar kowa a wannan family naku”.

“Tabbas Ummie. Dan komai ya fara buɗewa ne daga ranar bikin buɗe Company. Sai dai komawarki a halin ciwo a lokacin ya sake tayar min da hankali. Sai dai koba komai na fara fahimtar daga ina ainahin komai yake, duk da anyi yunƙurin daƙileni da sihiri fiye dana farkon daya raba tsakanina da ke. Aka kuma sake ta'azzara ƙiyayyata da Fahad. Sai kuma ALLAH ya shigo da Samrh rayuwata a lokacin...” tiryan-tiryan ya kwashe komai ya bata labari hatta aurensa da Samraah. Har zuwa wannan rikicin da ya faru na kwana biyun nan. Kuka sosai takeyi kamar yanda Fahad dake laɓe yana saurarensu yake yi shima. Hakama Samraah da ko Fahad bai gani ba kuka take yi. Dama tazo gaida Ummie ne, saɗaf-saɗaf ta koma da baya tunda ALLAH yasa kowa bai ganta ba.

Daga ƙarshe dai shima Fahad ya faɗa ɗakin. Rungume Maash yayi da Ummie yana mai basu haƙuri. Murmushi Maash da gaba ɗaya yanayinsa ya canja yayi yana mai shafa kansa.

“Kai zan bama haƙuri Fahad, dan na maka abubuwa da yawa marasa daɗi, na kasa riƙe amanar Ummie. Na kasa kula da tarbiyyarka. Ban san cinka ba bansan shanka ba balle muhallin da kake rayuwa. Duk da ina son yin hakan a ƙasan raina amma bazan iya ba. Akwai lokacin danai yunƙurin neman inda kake amma hakan ya gagara, sai da nayi jiyyar sati biyu. A randa nai maka mugun dukan daka bar gidan nan sai da nayi kuka naji sanyi a raina. Ka yafe min kaji Kiddo, dan wlhy ni kaina ban san duk taya nayi waɗan nan abubuwan ba sai da Abbah ya fargar da ni shi da Baba (Sheikh Muhammad ibn Khalipha Al-Hussain da Baban Hayatu). Amma duk da haka na gagara basu haɗin kan shan maganin da suka tabbatar min in sha ALLAHU suna fatan ya zama waraka a garemu”.

Kuka sosai Fahad ya sake fashewa da shi shi da Ummie. Sosai ya rungume Maash fiye da farko. “Ni Yaya bakamin komai ba. In ma kamin na yafe maka. Dan koda baka yimun da hannunka ba Yaya Hayat na mun komai. Kuma koda zanji haushi yana sanar min da kuɗinka yamun. Wlhy bazan taɓa yafema mutanen nan ba. Kuma ni dan ALLAH ku gaya min waye-da-waye ALLAH sai na musu yankan kifi”.

Dariya Ummie ta sanya, yayinda Maash yay murmushi da dungure masa kai. “Kai bakinka baya gajiya da ambaton yanka mutane?”.

Cike da shagwaɓa Fahad ya ce, “To yaya ai kaima dai jiya kace zaka yanka min”.

Yanzu kam dole sai da Maash ya ɗan dara da faɗin, “ALLAH ya shirya min kai. Ni tadani naje na duba Matata kaji”.

Cike da shaƙiyanci Fahad ya ce, “Uhhm su Yaya fa an zurma da yawa. Ummie ki ƙara godema Aunty Samraah ita babbar yar su ce tunda ta kamo babban kifin nan naki a kogi cikin ƙanƙanin lokaci”.

Mi Ummie zatai banda dariya. Maash ya kama kunnen Fahad ya murɗa har sai da yay ƙara sannan ya sakar masa ya fice yana murmushi kawai...

Rungume Ummie Fahad yayi cike da farin ciki ya ce, “Wlhy Ummie da gaske yana bala'in sonta. Kigafa yanzu murmushi baya masa wahala.”

“Kaima saika dage ka samo min wadda zata maka irin wannan kamun kaji Autana”.

“Kwantar da hankalinki ke dai Ummie ai ni biyu ma zanyi rana ɗaya”.

“Biyu fa Auta?”.

“Yes Ummie na, ba gara na more da ƙyau ba”.

“ALLAH ya shiryeka”.

Ta faɗa tana dungure masa kai. Dariya yayi, sai kuma ya marairaice mata wai ta bashi labarin abinda ya faru a bayan dan shi bai taɓa tunanin ciwonta nada alaƙa da wani abu ba. Saboda babu wanda ya taɓa zama ya nuna masa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy

70

.....Kˈarfe biyu da rabi na rana bayan jami'an tsaro sun gama bincike-bincikensu suka saki labarin kama Commondo da Madam Jannifer. Tare da samo Paah da aka tabbatar da Commondo ɗin ne yay kidnapping ɗinsa ya kuma kashe drivern sa. Ita kuma Jannifer suna kan bincike domin sanin dalilinta na yunƙurin sake zuwa domin ɗaukar Paah ɗin a daren jiya.

Sakin wannan labari dai-dai da isowar tawagar motocin Maash har bakwai asibitin. Dan gaba ɗayansu suka taho hatta da Falaq mai jego ba'a bari ba. Samraah ma ce yaso hana ta biyosu. Aiko ta saka masu kukan taɓara. Sam baya son ganin damuwa a tattare da ita, dole ya barta ta biyosun amma ya saka TJ yin tuƙi a hankali. A waje wajen motocin suka bar wasu guards ɗin nasa. Wasu kuma suka take masu baya har ciki. Ummie da Mama Balki ne a gaba su Sha'aibu na jagorantarsu. Sai Falaq da Samraah biye da su, Samraah na ɗauke da Baby Awwab. Maash da Hayatu sai Fahad da Hafizzullah na take musu baya. A ƙarshe sauran guards ɗin. Tako ina suka ratsa daga yˈan dubiya har ma'aikata da patients kallonsu sukeyi. Ɗakin da aka kwantar da Baba prof suka shiga. Yana kwance sharkaf, a kallo ɗaya zaka fahimci ya jigata da cizon kunamar nan. Ga wani uban ƙullutu a goshi da alamu suka nuna ya buga kanne a bango maybe waje neman ceton kai. Kˈafafunsa a wawware suke an yafa masa duvet kamar dai babu wando ne ta maganar Lado(🤣).

Ummie ce ta fara gaisheshi da masa yaya jiki. Idanu kawai ya zuba mata batare daya iya amsawa ba. Ba kuma dan baya magana ba sai dan bakin nasa ya gaza koda motsi ne, sai kallon tsana da gargaɗi yake mata kamar zai cinyeta da idanun. Murmushi ta sakar masa tamkar bata fahimcesa ba ta ce, “ALLAH ya kiyaye na gaba”.

Sai su Mama da su Samraah suka gaidashi a jimlace. Fahad kam ko kallon inda yake baiyi ba. Maash ma dai da farko bai tanka ba, sai da ya mula dan kansa ya wani taka cike da ƙasaita da izza hannayensa duka a aljihu ya matsa gaban gadon. Zama yay a kujerar gabansa yay crossing ƙafafunsa tare da folding hannayensa a ƙirji ya wani zuba masa cat eyes ɗin nan nashi masu kaifi da kwar jini. Ji kawai baba prof yay wani abu na tsarga masa. Dan gaba ɗaya kamanin Awwab ɗin rikiɗa masa sukai tamkar Ibrahim Alonso.

A daƙilen nan nashi cike da manners ya furta, “Ya kake?”.

(Ya kake?) Baba prof ya maimaita a zuciyarsa, zuciyarsa tasa na masa zogi. Da ƙyar ya iya buɗe bakinsa ya bashi amsa da, “Awwab kasan a gaban wa kake kuwa?”.

Murmushi rainin wayo Maash ɗin ya wani saki. Sai kuma ya kalla haɗaɗɗen agogon hannunsa mai shegen tsada yana ɗan wani laɓe small pinkish lips ɗinsa. Hannun ya sauke yana ɗan juya idanunsa ya maidasu ga Baba prof ɗin. Kansa tsaye ya furta, “Mahaifin Paah ɗina”.

“Mahaifin Paah ɗin ka?”.

Baba prof ɗin ya sake maimaitawa a fili yana wani tsare Maash ɗin da idanunsa. Ta cikin wando kuwa saboda harbi da wajen ya sha baya iya riƙe fitsari sosai yanzu ma sai da ya tsillo. Dan wani banzan kallo Maash ya sake masa yana faɗin,

“Bayan hakan ko akwai wata alaƙar? Oh sorry ashe yaron Grandpa ɗina ne kuma, sorry Mr Adams K/Mashi”.

Tsuuuu!!

Fitsari ya ɗan sake kufcewa Baba prof again. Jikinsa ko har ɗan rawa yake duvet ɗin da aka lulluɓa masa ne kawai ya rufa asiri. Ashe tsugunne bata ƙare ba. Dan Maash na rufe baki Fahad da idanunsa ke kan television ɗin ɗakin ya ce, “What!! Uncle Abdullahi!!”.

Yanda ya ambaci sunan da ɗan zabura yasa hankalin kowa komawa can banda Maash da bai ko motsa ba. Uncle Abdullahi ɗinne kuwa ke bayani matsayin babban ɗan sandan sirri da yaransa suka samu nasarar cafke Commondo da Madam Jannifer a daren jiya. Ta re da tabbatar da sun amso Alhaji El-Mu'azz k/mashi. Babu wanda baiyi mutuwar tsaye ba a ɗakin, wasu ma har murza idanu suke domin son ƙara tabbatarwa. Kasa haƙuri Fahad yay jikinsa na tsuma ya tako gaban Maash da ke zaune baida alamar nuna yasan mike faruwa. Amma kuma kunnesa na jin dukkan bayanin Uncle Abdullahi ɗin. Riƙo hannunsa Fahad yayi murya na karkarwa ya ce, “Kaga fa Uncle Abdullahi wai ɗan sandan sirri. Imagine”.

Karo na farko Maash ɗin ya ɗago. Idanu ya zubama Fahad ɗin, sai kuma ya janye a hankali ya maida ga television ɗin. Fuskar Uncle Abdullahin kawai ya zubama idanu, sai kuma ya saki murmushi tare da lumshe idanunsa ya sake buɗewa akan Fahad. A taƙaice ya furta, “Na gani”.

Ba Fahad ba hatta Ummie sai da ta waro idanunta waje. Mama Balki kam ai baya tai ɗan mamaki sai da Hafizzullah ya ɗan riƙota. Babu zato suka ji an faɗo ƙasa timm. A tare duk suka juya, mi zasu gani Baba prof ya sulmiyo ƙasa dan kiɗima. ALLAH ma ya taimaka jikinsa cikuykuye yake da duvet da anyi abin kunya. Rawa jikinsa yake sosai yana nuna television da yatsansa. Magana yake son furtawa amma ko harafi guda ya gagara fita a bakin nasa. Sai kawai ya zube gaba ɗaya raƙwam alamar suma.

Hayatu ne yay ƙarfin halin kiran doctor, akai kama-kama aka maida Baba prof saman gado. Dole kowa ya fito aka barsa da doctor. Daga nan suka shiga inda aka haɗa su Hajiya Mammah su duka. Sukam da sauƙi dan tunda akai musu alluran kashe dafi ta sauka. Barcin da aka sakasu yine ya jasu har zuwa yanzu. Sai Hajiya ƙarama ce dai ansha wahala. Sun samu suma duk sun ɗimauce da labaran da ake nunawa a television. Ba labaran ne yaja hankalinsu ba ganin Uncle Abdullahi a matsayin ɗan sanda. Sun samu itama dai Hajiya Ƙarama na mazarin jiki. Dan abu biyu ne ya ɗimautata zuwa uku. Ganin an kama Commondo da Madam Jannifer, sai Uncle Abdullahi matsayin ɗan sanda babba kuma na sirri. Ƙarin tashin hankalin ma wai shine ya kama su commondo. Itama dai sai da aka nemo likita kanta. Daga nan ɗakin da aka kwantar da Paah muka fara shiga. Ɗakine na musamman dake zagaye da tsaro na musamman. Barci yake shi kam hankalinsa kwance. Duk da ya rame alamar yasha wahala. Rawa jikin Ummie ya fara. Ta ƙarasa gaban gadon da sassarfa. Tuni ta manta da wanda ke tare da ita batama san ta kai dirƙushe ƙasa ta kamo hannun Paah ɗin ba hawaye masu zafi na rige-rigen sauka mata a kumatu. Karyayyar muryarta na rawa ta furta, “Azz! kaine haka? Ya Arrahaman”. Sai kawai ta saki kuka tana mai rungumesa.

Da baya-baya na koma na fice a ɗakin, dan haka kawai naji tausayin Ummie ya masifar shigata. Karo naci da mutum, dan haka na ɗaga kai da sauri na kalleta ina mai ambaton ban haƙuri gareta. Itama dai-dai ta ɗago zata bani haƙurin. Ban iya na ƙarasa ba ni, sai idanu dana zuba mata zuciyata na wani irin sauka a hankali. Raɓani tai zata wuce na damƙo hannunta, sai ta juyo a girgice zatai magana nai azamar girgiza mata kaina da zipping ɗin bakina alamar tai shiru. Cikin rawar jiki ta haɗiye maganar da take son yi kuwa. Ni kuma naja hannunta muka bar ta wajen duka. Sai da muka bar ƙofar ɗakin na tabbatar ba idon kowa ata inda muke sannan na ce, “Miye sunanki?”.

Sosai fuskarta ya nuna alamar mamakin tambayar da nai mata. Amma ganin na haɗe fuska babu alamar wasa a tattare da ni, ga shi na tabbatar tasan wacece ni dan yanda muka shigo suna kallonmu ko ita bata gammu ba nasan za'a bata labari, ga kuma tranding da hotunana dana Maash sukai a kwanakin nan koma nace suke kanyi. Amma duk da haka sai da na ƙara mata da faɗin, “Sunana Samraah Abdul-wahab Gwarzo, Mrs Awwab El-Mu'azz Maash. Nasan kin sani. Minene sunanki?”.

Kanta ta shiga jinjina min tana yɑan waige-waige, mutyarta na karkarwa ta ce, “Murjanatu Usman”.

“Masha ALLAH Murjanatu kwantar da hankalinki ba wani abu bane ba, magana nake son nayi da ke amma bazai yiwu anan ba. Ko zaki iya bani number naki?”.

Yawu masu kauri ta haɗiye da ƙyar. Cikin ƙara daburcewa ta ce, “Dan ALLAH Maa kiyi haƙuri idan akan turekin nan da nayi ne. Wlhy ban san kin tahoba sam shiyyasa”.

Murmushi na mata dan naga ta firgice. Cikin son dai-daita yanayi na na ce, “No kwantar da hankalinki ba wannan bane ba. Tambaya zan miki akan wani abu daya shafi mace mai ciki, amma bana son yi anan shiyyasa”.

Da masifar ƙarfi ta sauke ajiyar zuciya, sai kuma ta sake sauke numfashi da faɗin, “Wlhy ranki ya daɗe harna tsorata. Kin san abunne akwai tsoro balle ku manyan nan. Na zata ko na miki wani laifine. Ba damuwa ko gida kike son nazo zanzo na same ki ai. Sai dai matsalar baza'a barni na shiga ba”.

“No karki damu zansa azo har nan ɗin a ɗaukeki. Ko zaki iya bani number ɗinki?”.

Cike da zumuɗi ta amsa min tana amsar wayar hannuna. Ni saima taso bani dariya. Dan hannunta har rawa yake wajen loda number ɗin. Amsa nayi nai saving. Da murmushi na ce mata, “Zaki iya ji kirana akoda yaushe in sha ALLAHU. Amma fa maganar nan ta tsaya iya ni da ke kawai. Dan na fahimci kina da hankali da nutsuwa tun wancan kwanciya asibitin da nayi shiyyasa”.

Sosai ta sake washe baki cike da farin ciki tana Murmushi. Da ga haka muka baro wajen. Sai da naji shock da hango Maash tsaye da alama ta inda zan fito yake son gani. Amma sai na dake abina a nutsena na ƙarasa inda yake. Batare da nayi magana ba na zare wayar da yake dannawa daga cikin hannunsa. Sai da yana wani sakanni kafin ya ɗan ɗago cat eyes ɗinsa ya kallan. Ido ɗaya na kashe masa cike da salon basar da shi na ce, “Tsaiwa anan kamar wani dogari”.

Maimakon tanka min sai ya wani cigaba da kallona, kusan minti ɗaya sannan ya motsa lips a hankali ya furta, “Let's go”. Yana kama hannuna. Banda zaɓin daya wuce bin nasa. A haka muka dinga keta mutane ana kallonmu. A karan farko naji banji kunyar hakan ba. Sai dai a raina ina jin wasu fa zasu iya ɗaukar hotonmu musamman a wannan gaɓar da dama ake neman labari a kammu. Kamar ko ina gani har hanji, dan bamu ƙarasa gida ba sai ga hotunanmu sun fara yawo a media. Sosai na tsarkake sunan UBANGIJI da jinjina halin gulamar mutane da ƙaikayin hannayensu nason yaɗa abinda sam bai shafesu ba. Dan su birge ne ko dan ace a bakinsu aka fara ji oho musu.....✍

Zazzabi ya tasani gaba posting yanzu sai a slow. Ayi hakuri dai in sha ALLAHU muna gab da tsargewa kowa ya huta.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-one

71

.....Washe gari tunda Baba prof da Hajiya ƙarama suka dawo hayyacinsu duk sai suka matsa a sallamesu a safiyar. Iya ƙoƙari doctors ɗin sunyi dan ganin sun fahimcesu musamman ma Baba prof da tai masa illa a inda ya kamata ya samu kulawa amma sam hakan yaƙi yiwuwa. Dole suka haƙura suka sallamesun. Dama shi Paah tun a daren Maash yasa aka sallamesa saboda Ummie ta tada hankalinta akan zataje asibitin zaman jiyyarsa. Shiko bai amince da hakan ba. Shiyyasa ya yarda da a dawo da Paah ɗin gida likitan ya cigaba da zuwa dubashi anan.

Kai tsaye sashen Maash ɗin aka kaisa ɗakin da Ummie take. Sai ganinsu kawai tayi. Sosai ta nuna farin cikinta taita sanya musu albarka. Su dai basu ce komai ba musamman ma Maash da ke matuƙar jin zafin Paah har yanzun. Isma'il ne yay kiran Maash ya sanar masa ai an sallamo Baba prof gashi a gida. Baiyi mamakin hakan ba, dan haka baice komai ba sai murmushi. Lokacin da kuma yake fitowa ya shiga ya duba Paah ya fito zasuyi break fast su Fahad ke sanar da itama Hajiya ƙarama ta dawo gida yanzun nan. Dama su su Hajiya Mammah tun jiya aka sallamosu. Uffan shi dai Maash baice ba, sun kuma san bazai ce ɗin ba daman....

□□□□

Iya faɗin yanayin da Baba prof ke ciki kawai sai dai kintace, dan a matuƙar harmutse yake. Duk da yanda yake jin rashin ƙarfi a jikinsa suna isowa gida wanka yay tare da yin shiri cikin manyan kaya. Sai da ya fito sannan ya tuna babu drivernsa fa a gidan yanzu. Gashi bai san ina Commondo ya kaisa ba. Zaune ya kai cikin kujerar falon kawai yay shiru. Sai da yaja tsahon lokaci a haka kafin ya ɗauka waya yay kira. Ana ɗagawa da ga can batare da ko sallamar da akai masa ya amsa ba cikin bada umarni ya furta, “Ka sameni a gida yanzun nan”. Ƙitt ya yanke kiran.

Sake zabga tagumi yayi na wani lokaci, sai kuma ya miƙe ya fara safa da marwa a falon cikin rashin ƙarfin jiki. Tsahon awa ɗaya ciff sannan Uncle Abdullahi ya iso gidan. Ya nuna mamakin ganin mahaifin nasa a gida, kasancewar duk sun san bai isa a sallamesa ba haka da wuri dan jikin nasa da saura. Ga Doctors ɗin ma sun tabbatar da yana buƙatar hutu..

“Baba ina kwana? Yaya ƙarfin jikin?”.

Ya faɗa cikin ƙoƙarin danne komai dake a ransa. Shiru Baba prof bai amsa ba, sai da yaja lokaci mai tsaho sannan ya juyo a wani irin yanayin mai wahalar fassara yake kallon sa. Kasa jurewa Uncle Abdullahi yay ya duƙar da kansa ƙasa, ya san minene laifinsa, ya kuma shirya amsa komai da za'a tuhumesa da shi. Kamar ko yanda yay zato a zafafe Baba prof ya furta,

“Abdullahi!! Wanene ni a wajenka?”.

Sosai tambayar ta bama Uncle Abdullahi mamaki, amma ya daure kansa a ƙasa ya amsa da, “Baba mahaifina ne kai, wanda yay sanadin kawoni duniya, ya tarbiyyace ni ya tufatar da ni da ciyar dani a lokacin ƙuruciya da kula da ilimina duk bisa amincewar UBANGIJI”.

“Ban yarda da hakan ba Abdullahi. Ƙarya kake yi!. Da ace ni ɗin mahaifinka ne da baka zaɓi wata rayuwa bayan idanuna ba. Da ace ka yarda ni Adamu ni na ciyar da kai, na tufatar da kai, na biya maka kuɗin makarantar da har kayi kaurin wuyan

aikata abinda ka aikata to lallai fa da baka kasance wani abu a bayan ganina ba. Abdullahi idan ban manta ba ni da kaina na hana ɗan uwanka aikin interpol a sanda ya ƙwallafa ransa. Amma shine kai ka zagaye ka zama jami'in sirri bada sani na ba. Hakan na nufin akwai wani abu a ranka ke nan ko kake shiryawa".

Hankali tashe Uncle Abdullahi ya ke girgiza ma Baba kai. "Wlhy Baba sam ba abinda kake zargi bane ba. Kuma a lokacin daka hana Yaya Mu'azz zama jami'in interpol na ɗauka wannan aikinne kawai baka ra'ayin muyi. Zama wannan jami'in kuwa wasu dalilai ne suka kaini ga zama hakan. Ban kuma ɓoye ba domin wata manufa tawa sai dan yanayin aikina kenan. A jiyan ma dole ce ta tilasta ni fitowa har duniya ta sanni da wannan matsayin. Amma idan har na ɓata maka rai ka gafarceni dan ALLAH".

Shiru Baba prof kamar bazai tanka masa ba. Sai da ya mula dan kansa kafin cikin bada umarni ya furta, "Bazan taɓa aminta da kai ba Abdullahi a yanzu sai na tabbatar. Sai dai a matsayina na mahaifi ina baka umarnin ka saki wannan yaron Commondo...."

A bala'in firgice Uncle Abdullahi ya ɗago yana kallonsa. Har bai san sanda ya furta, "Baba saboda mi? Akan mi kuma zanyi hakan bayan shi ɗin mai laifi ne. Dukkan bincikenmu ya tabbatar mana da cewar da hannunsa a yin kidnapping ɗin Yaya Mu'azz. To wai kai minene ma haɗinka da shi da har kake so a sakesa Baba?".

"Babu ruwanka da alaƙar dake tsakanina da shi. Kidnapping Mu'azz kuwa ni da kaina zan hukunta shi na kuma ji ba'asinsa nayin hakan".

Wani murmushin ɓacin Rai Uncle Abdullahi yay da faɗin, "Baba to ai kai ba jami'in tsaro bane. Dan mi zan barka kayi hakan? Sannan babu ta inda dokar ƙasata ko aikina suka bani damar sakin Commondo a halin yanzu. Saboda yanzu haka ana kan binciken mugayen ayyukansa ne ma. Shawarar dazan baka ma shine Baba kai gaggawar barranta kanka da shi idan ma wata alaƙa ta taɓa alaƙantaku. Dan wannan mutumin mugayen ayyukansa zasu iya kaisa ƙasa dama duk wanda yake tare da shi. Ka gafarceni Baba na barka lafiya". Ya ƙare maganar yana miƙewa ya fice. Dan gaba ɗaya kansa juya masa yake. Idan bai bar gaban Mahaifin nasa ba zai iya rasa control ɗinsa ne gaba ɗaya...

Ko sau ɗaya Baba prof ya kasa motsi. Sai kalaman Uncle Abdullahi ne ke masa wani irin amsa kuwwa acikin kunne har bai ma san ya fita a falon ba. Cigaba da jin sautin muryar Uncle Abdullahi na masa ihu cikin kunne ya sakashi fassa wani ihu shima yana wancakalar da Centre table ɗin gabansa. A guje wasu a cikin ma'aikatan gidan suka fara rige-rigen shigowa ciki harda Kuku da ke lafe yana jin komai. Sai dai shi kansa a yau ba ƙaramin girgiza zuciyarsa tayi ba da ganin abinda bai taɓa zato ba. Yanzu nan duk irin aibanta Baba prof da tsiyatakunsa da ya dinga yi a wajen ogan nashi ashe mahaifinsa ne. Kan bala'i jan. Wannan wace kalar

cakwakiya ce haka. Sai yanzu ya fassara sunan Uncle Abdullahi da ƙyau. *_Abdullahi A.KM_* wato (Abdullahi Adams K/Mashi) kenan dai. Jiyyar gaba ɗaya haddarsa ta gama gogewa. Jiyay kawai buƙatar ganin Maash yake, shin shima yasan ogansa kawunsa ne ko kuwa sai a jiya da yay bayani?.

Da ƙyar suka samu Baba prof ya zauna. Haka suka shiga kimtsa falon shi kuma ya shige bedroom. Giyarsa ta samu ya kwankwaɗa ya zube ƙasa sai barci. Dan inba hakan yayi zuciyarsa zata iya bugawa a yanzun nan.....

□□□□□

Da mamaki Uncle Abdullahi ke kallon Maash da ke shigowa office ɗin nashi. Sam baiyi zaton shi bane ba. Dan shigowarsa station ɗin kenan rai a ɓace daga gidan Baba prof. Baifi zaman mintuna biyar ba akace yayi baƙo. Da farko yace baya buƙatar ganin kowa. Sai kuma yanda yaga yaron nasa ya yi shiru kamar mai son cewa wani abu yace yaje ya shigo dako waye. Amma mintuna goma kawai zai iya bashi. Shine fa kawai sai ya ga Maash ya shigo alamar shine dai baƙon da aka nemawa iso kenan.

Da ƙyar ya iya ɗaga hannu yay masa nuni da wajen zama. Shima sai Maash ɗin ya kai zaune batare da yace komai ba. Sai da yaron Uncle Abdullahi ya fita a office ɗin sannan a hankali Maash ya furta, “Good morning Uncle”.

Murmushi Uncle Abdullahi yayi da faɗin, “Morning Awwab. Daga ina haka?”.

Ƙaramin murmushi shima Maash ɗin ya saki a karo na farko. Sai kuma ya ɗan kalla Uncle Abdullahi ya ɗauke idanunsa a daken nan nashi ya ce, “Daga gida, kuma wajenka nazo”.

“Dama nasan zan ganka, amma banyi zaton da wuri haka ba. Kar dai na jaka da nisa mike tafe da kai?”.

Numfashi mai nauyi ya sauke da gyara zamansa da ƙyau babu alamar wasa tattare da shi. “Uncle basai munja komai da nisa ba tsakanin ni da kai kamar yanda ka faɗa. Nasan kasan abubuwa da yawa da suka shafeni wanda ba kowa ya sani ba a gidan nan. Wasu ma da kaina na buɗa maka saninsu saboda na jima da sanin kai ne ogan Isma'il da Shu'aibu. Nasan hakanne tun lokacin da ka bada su Shu'aibu matsayin guards ɗina....”

“What a surprise!.”

Uncle Abdullahi ya faɗa cikin nuna matuƙar mamaki da al'ajab har yana miƙewa. Ƙasa kawai Maash yay da kansa yana furzar da isa. Ɗan bugar desk Uncle Abdullahi

ya ƙara yi yana sake jinjina al'amarin sosai. Kallonsa Maash kawai yay ya sake ɗauke kansa kamar mai ɗan jin nauyin Uncle ɗin nasa.

Zama Uncle Abdullahi yayi zuciyarsa na sake mamakin hatsabibancin yaron nan. Amma sai ya dake.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

😭□_* *_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-two

72

.....Cikin girgiza kai ya ce, “Nama rasa mizan ce Awwab. Kenan da ban fito a wannan gaɓar na bayyana kaina ba haka zamuyita tafiya ina maka kallon biri kana min na ayaba?.”

Murmushi Maash yay da faɗin, “No Uncle! No! Just forget. Hakan ya kasance ne saboda wasu dalilai. Kamar yanda yanzu ma dalilan ne suka kawoni nan. Isma'il ya sanar min duk yanda kukayi da Baba. Duk da bai kamata ace ya sanar min ɗin ba. Sai dai ruɗanin da ya shiga shima na gane cewa munada alaƙa har haka mai ƙarfi ya kaisa ga hakan. Uncle Please ina riƙonka ka bama wani case ɗin nan. Saboda....”

“Saboda ban cancanta ba? Ko saboda Baba ya kasance mahaifina kai kuma ɗan ɗan uwana?”.

“No Uncle Understand me. Abin zai zamar min wani iri nima. Shiyyasa ba kowane imformetion zakaga nake baku ba, wasu lokutan nake yin wasu abubuwan da kaina ta bayan fage. Magana ta gaskiya case ne da bazan iya bari ba, ba kuma zan so sarƙaƙiyarsa ta shafi har waɗanda bai kamata ta shafa ba irinka.”

Sosai Uncle Abdullahi ke jinjina kai idanunsa da suka canja launi akan Maash. Murya a shaƙe ya ce, “Muhammad Awwab!”.

“Yes Uncle”.

“Kasan mi nake so da kai?”.

Kai kawai Maash ya girgiza masa.

“Kasa a ranka sunana Abdullahi A.km. da yay rantsuwa wa UBANGIJI zaiyi aiki tuƙuru domin kare ƙasarsa dayin adalci wa mutanen cikinta walau talaka ko mai arziƙi, ko mai mulki. A tsarin aikinmu babu zancen family. Babu zancen kasuwanci, babu zancen abota ko makwaftaka. Tabbas a lokacin dana amshi wannan case ɗin ban san nasu wanene ba. Sai da aka hari rayuwarka ta farko sannan har na yanke komawa cikin Maash Mansion. Bayan nan ne na zauna nayi bincike mai zurfi tare da saka mutane da yawa a cikin ku. Abinda yasa na ɓoye kaina gareka dan ka samu damar sanar min komai batare da kaji wani ɗar ba. Ashe ma nayi shuka a idon maƙwarwa ɗan nawa ƙwaron kansa ne”.

Murmushi nan ɗin ma Maash ya ɗan yi kaɗan batare da ya yace komai ba. Uncle Abdullahi bai damu ba ya cigaba da yin maganarsa. “Ina son kamar yanda kayi kawaici ƙin nuna kasan nine a da yanzu ma ka cigaba da tafiya a hakan kawai na baka san ni ɗin waye ba. Dan tunda na fara aikin nan sai fa na kaisa in sha ALLAHU”.

“Uncle Amma....”

“Chapter is closed Awwab”.

Uncle Abdullahi ya faɗa cikin katseshi. Numfashi Maash ya furzar da faɗin, “Shi ke nan. Yanzu wane taimako kake buƙata. Dan duk yanda kake tunanin abun ya wuce hakan”.

“Nasani Awwab. Dan laifukan da masu laifukan sun kasance rassa daban-daban. In dai akwai wasu imformetion a wajenka ka bani su kawai zakaga yanda aikin zai cigaba da tafiya. Na kuma maka alƙawarin komai gareka zai zama a buɗe. Hatta da shawara zamu iya nema ta wajenka dan na fahimci kai bana wasa bane”.

Girgiza kai Maash yayi kawai batare da yace komai ba. Sai daya ja kusan minti ɗaya kafin ya ɗago. “Baka da matsala ina sha ALLAHU. Sai dai ina son ka bama Baba damar ganin Commondo dan hakan nada matuƙar amfani. Musamman ga ita matar nan dan akwai abinda take ƙoƙarin shiryawa kenan da ya kamata muyi saurin ganota”.

“Okay na fahimceka. Wato shiyyasa taje ta shirya ma Baba wancan ƙazon kuregen kenan na cewar Commondo ne yay kidnapping Yaya? Duk da ni inama zargin kamar tasan komai”.

Ɗan wani luuu da idanu Maash yayi sai kuma ya buɗe akan Uncle Abdullahi. “Tare da ita sukai komai”.

“What! Kana nufin harda ita akai kidnapping Yayan? Kenan itama tana da alaƙa da Commondo ɗin?”.

Ƙaramar dariya data bama Uncle Abdullahi mamaki Maash ya saki. Sai kuma ya ɗan taɓe baki da ɗage kafaɗa. Kansa tsaye ya ce, “Uncle wannan zaren tsayinsa yafi na igiyar wutar lantarki. Idan nace zan maka bayani yanzu akan komai, bama zaka iya fahimta ba. Amma ka bani lokaci”.

Ya ƙare maganar yana miƙewa. Cikin girmamawa yay masa sallama ya fice abinsa yana wani makirin murmushi. Dan kuwa shi kaɗai yasan mi yake shiryama ransa. Zuwansa nan kuwa nada dalili da nasaba da son sanin ainahin abinda ke a ran Uncle ɗin nasa da kuma son tantance a wane matsaya yake yanzu...

Da sauri Jaga da Hayatu dake zaman jiransa duk suka miƙe. Gaba yay suka take masa baya. A waje ma su Shu'aibu na jiransa. Nan ma TJ ne ya buɗe masa mota. Jaga da anan suka haɗu da shi dama Maash ya ce ya shiga gaba. Shi kuma Hayatu ya dawo kusa da shi.. guards ɗin kuma duk suka shiga motocin su suma....

□□□□□

Kamar yanda Baba prof ke a hargitse haka Hajiya ƙarama ke a harmutse. Dan ita koma wankan bata nema yi ba tana isowa gidan ta shige ɗaki ta kulle kanta. Bige-bigen wata ta fara. Ana ɗagawa ta ce, “Please ina son mu haɗu”.

Ban san amsar da aka bata daga can ba ta dai jinjina kan ta yanke kiran. A gurguje ta canja kaya dan yanda take jinta bata jin zata iya wani zaman yin wanka. Cike da fatan ALLAH yasa kada ta samu kowa a falon ƙasa kamar yanda ta shigo bataga kowa ba tayi. An koyi Sa'a babu kowan, dan akwai sauran safiya duk basu tashi barci ba masu gidan. Mota ta shiga ta fita a gidan duk da yanda take jin jikinta babu daɗi. Yanda take ɗibar motar yasa ta isa inda take harin zuwan da wuri. Can gefen gari ne wani ɗan ƙauye ko kuma ma mu kirashi club kawai dan mahaɗace ta gawurtattun yan iskan criminals ɗin Lagos ɓoyayyu da wasu manya suka ɗaurema ƙugu. Mata ne da maza a wajen ana ashararanci. Sai cinikayyar mugayen abubuwa na maye dana ta'addacin da ake gudanarwa. Mafi yawan waɗanda suka san wannan waje yan ɓadda sawune. Kasancewar safiya ce tsirarun mutane ta samu dan ansha shagalin dare duk sun zube barci wasu kuma sun kama gabansu. Sai masu kula da wajen ne keta aikin tsaftacesa sai kuma irin ogan da sunci dubu sai ceto kansu na iya ɗaukar kowane kalar kayan maye yanzu batare da sun jigata ba.

Kamar yanda ƙa'idar take sai da aka binciketa tsaf sanan aka nema mata iso wajen boss ɗin. Mintina kusan ashirin aka shiga da ita ciki. Ƙaton falone da yaji kayan more rayuwa dan an shirya liyafar duniya a cikinsa. Gini ne to iya gini aka zuba a cikin jejin nan. Sai kuma aka bisa da iccen bamboo aka rufe ta yanda zaka ɗauka da shi aka yi san. Tana nan zaune kusan mintuna biyar ma sannan ya fito. Fari ne tass ƙarfaffan gaske jiki duk ya buɗe ya kuma sha zanen tattoo. Rantalelen kansa sai ƙyalli yake saboda yanda aka ƙwalƙwale gashin tsaf. Sam fuskarsa babu walwala amma yana ganin Hajiya ƙarama ya ɗan saki murmushi yana kaiwa zaune da faɗin, “Manyan ƙasa yau dai aƙalla an tuna da ni kenan?”. Cikin harshen turanci

Murmushin yaƙe ta saki da faɗin, “Hummm Marcel dama ban manta da kai ba. Kawai dai abubuwa ne suka min yawa. Ya naka?”.

“Komai normal muna nan muna zubawa? Da alama ta ƙwaɓe dan naga an kama mutuminki. Sai dai abinda ya ɗauran kai kamar wanda kike zaune a wajensa yanzu naga ance yayi kidnapping ko har yanzu dai yana sonki?”.

“Hakane Marcel. Sai dai duk abinda ya faru tare mukayisa. Abinda yasa na nemoka saboda Jannifer itama dai yarinyarka ce. Nasan kuna harkar bussines sosai batun yanzu ba. Na kuma san a tsarinka duk wanda ke tare da kai in har ya faɗa hannun jami'an tsaro kasheshi kake sawa ayi. Shiyyasa nazo neman alfarmar shima Commondo a kawar da shi kawai a lokacin kawai da Jannifer”.

Wata shaƙiyyyar dariya Marcel ɗin ya saki, sai da yay mai isarsa sannan ya tsagaita da faɗin, “Ada Jannifer ke yarinyata. Amma tuni na saidata ga Bancy. Shiyyasa bani da wata alaƙa da abinda ya sameta yanzu”.

Da mamaki Hajiya ƙarama ta ce, “Amma bata taɓa faɗa min ba”.

“To wannan tsakaninku ne kuma. Yanzu dai idan kina son aiki akan Commondo sai muyi ciniki kenan. Sannan batun Jannifer ki samu Bancy ɗin dan tabbas bazai barta a hannun jami'an tsaro ba. Daga nan kuma zuwa dare zai iya sakawa a saketa dan shi kinsan ba irin tsarinmu yake ba.....”

Sosai hankalin Hajiya ƙarama ya tashi, dan tsakaninta da Bancy fa sam babu jituwa. Idan kuma har yasan akan yimata aiki Jannifer ta shiga hannun kwalawa tabbas ya samu makamin yaƙarta kenan. Ina bazata faɗi ƙasa haka wanwar a tsakkiyar ƴan iska ba. Dan haka kai tsaye ta fito fili ta ce, “Akwai matsala kenan Marcel. Dan kasan bama shan inuwa ɗaya da Bancy yanzu. Idan har ban kawar da Jannifer ba zai yi amfani da wannan damar domin fallasa ni.”

“Eh kema kince wani abu. Sai dai gaskiya zan gaya miki dan kin san ni bana ɓoye-ɓoye a aiki. Ni da Bancy akwai yarjejeniyar da ta hana mana yin aiki a tsakanin mutanenmu. Dan haka banda lasisin kashe miki Jannifer sai dai Commondo kawai. Dan haka kije ki sake sabon tunani akan Jannifer saboda kin santa bakinta reza ne.”

Sosai hankalin Hajiya ƙarama ke'a tashe. Amma sai ta danne ta amsa masa da “Babu damuwa. Ka faɗi ko nawa kake buƙata akan Commondo, sannan yaya maganar poison ɗin nan na wajen doctor Khunal?”.

“Ki nemesa kuyi magana. Tunda kema kin san laifinki ne. Tun 3 to 4years ya haɗa abunnan amma kina jan jiki. Ki dai yi fatan bai saidama wani ba kawai. Dan kin sanshi dai akan kuɗi baya wasa mugun ba indiyen mam”.

“Ba damuwa zan nemesa. Lokacin amfani da abunne bai taso ba sai yanzu. Miye kuɗin aiki na? Dan bayan an gama da shi akwai wasu har huɗu. Idan kuma su haɗuwarsu zai zama wahala ko a rarrabe a ƙaddamar dan bana son a wuce kwanaki uku nan to a sakama gidan duka wuta. Sai dai kafin hakan ina buƙatar Maash, Mu'azz & Ummu-Hidaya a raye”.

Dariya sosai Marcel yayi da faɗin, “Fantastic. Wai har yanzu kina wahala akan wannan project ɗin? Koda yake bakiyi jiran banza ba, tunda ta ƙara mai kam. A bazan ji tausayinki ba kawai naji babban alert. Ta shi kije kawai daren yau labarin mutuwar Commondo zata zo gareki. Sauran aikin kuma ma ƙarasa zancensa a waya”.

Murmushi kawai Hajiya ƙarama tayi tana miƙewa. Sai kuma ta miƙa masa hannu sukai musabaha sannan ta fice.....✍

Matar nan ko?..

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_*_□TSUTSAR NAMA....!!□_*

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-three

.....Kasancewar yau ma sharkaf na tashi har sai zuwa ƙarfe ɗaya saura na samu zazzaɓin jikina ya sauka yasa ni bansan wainar da ake toyawa ba a gidan. Cikin ƙarfin hali na taƙarƙara nayi wanka nayo alwala. Koda na idar da sallar ban wani damu kaina ba na saka doguwar riga mara nauyi na ɗan saka turare. Ina ƙoƙarin fitowa wayata ta hau tsuwwa. Ɗauka nayi na duba sai naga shine. Zaune nakai kafin na ɗaga. Saukar sassanyar muryarsa cikin kunnena ya sani sauke ajiyar zuciya. Sallamar tashi na amsa masa tare da gaisheshi. Shima cike da kulawa ya tambayan yaya jikin?.

“Alhamdullahi, Yaya shine ka fita ban sani ba”.

A hankali Maash ya lumshe idanunsa dan shagwaɓar tata ya jita har tsakar kansa. Cikin sake sauke murya shima ya ce, “Am sorry. Uzirin fitar ne ya taso min dole My Tiger. Ina fatan dai yanzu babu zazzaɓin?”.

“Ya sauka, har nayi wanka zanje wajen su Ummie yanzu ma”.

“Masha ALLAH, ki daure kici abinci to, nima anjima kaɗan zan dawo.”

Cikin sake narke murya da shagwaɓeta na ce, “Karfa ka daɗe”.

Ina jin saukar sautin murmushinsa cikin kunnena, sai kuma ya ce, “Okay bye” ya yanke kiran. Ajiyar zuciya na sauke tare da kafe wayar da kallo, sai kuma na ɗan sumbaceta. Duddubawa nai naga miss call nashi ritutu, sai na Gwaggo Gudidi da Abba. Ya Musaddiq ma yamun ɗaya. Sai Fahad da Hafizzullah da Aunty Falaq. Ajiyar zuciya na sauke nayi kiran Abba muka gaisa harda amaryarsa. Ya sake tabbatar min da yana nan tafe in sha ALLAHU shi da Kawu Musa. Nayi murna sosai ya bama Auta shima muka gaisa yau baije school ba wai babu lafiya. Gwaggo na kira itama muka gaisa, mun ta hira da ita har na sauka ƙasa. Acan mukai sallama. Babu kowa a falon dan haka na shiga ɗakin aunty Falaq mai jegon yan gayu. Yo jegon yan gayu mana tunda sabgoginta taketa zubawa ba kamar yanda naga masu jego na nutsuwa waje ɗaya ba ko ɗan suna ayi sannan. Amma ita yau kwana shida ko ina ƙafarta zuwa take a gidan nan. Na samu tana barci. Dan haka banyi magana ba na fito. Ina son shiga na gaida Ummie amma na kasa saboda yanzu ba ita kaɗai bace a ɗakin. Har na nufi kitchen dai na daure na koma ƙofar ɗakin. Knocking nayi kamar mai jin tsoro sannan nayi sallama. Bammayi zaton za'a jini ba sai naji an buɗe ƙofar. Hajiya Mama ce, tana ganina ta saki murmushi da faɗin, “A'a Masha ALLAH daughter ce? Jiki yayi sauƙi kenan”.

Murmushin nima na sakar mata kaina a ƙasa na rissina na gaisheta. Ta amsa min da kulawa tana jan hannuna ciki. Paah na zaune ya jingina da fuskar gadon Ummie a kusa da shi tana bashi magani a baki. Jinai nutsuwa ta ƙara ratsani ganin Ummie jiki dai nata ƙara sauƙi, gashi itama har tana jiyyar wani. Har ƙasa na durƙusa na gaishe da Paah ɗin tare da tambayarsa jikinsa. Ya amsa min a hankali dan muryar tasa bata fita sosai. A mamakina nima sai ya tambayen yaya nawa jikin? Sake ƙasa nayi da kaina kawai ban iya na amsa ba. Dan haka kawai naji

kunyar amsawar. Ƙaramar dariya Ummie da Hajiya Mama sukayi. Sai kuma Ummie ta ce, “Zo nan Babyna”.

Babu musu na tashi zuwa gareta, zan durƙusa ƙasa ta kamoni ta zaunar kusa da ita. Duk sai naji na daburce. Amma ta hanani saukar da nake son yi. A haka na gaisheta da tambayarta jikinta dana Paah. Ta ce duk Alhamdullah yaya nawa nima. Itama kasa amsa mata nayi sai tai murmushi kawai. Cikin basar da zancen tace, “Ai munje dubaki ni da Mashi'a amma kinata barci.

Kaina a ƙasa na ce, “ALLAH Ummie bamma san kunje ba”.

Cikin murmushi ta amsa ni da faɗin, “Shiyyasa dama bamu tadaki ba. ALLAH dai ya ƙara afuwa. Mi kike son ci yanzu?”.

“Ummie bana jin yunwa”.

“No bazai yiwu ba. Rabonki da abinci tun daren jiya. Faɗa min mikike son ci?”.

Kafin na bada amsa akai knocking ɗin ƙofar, ba kuma a jira anyi magana ba ko anyi sallama kawai aka shigo. Hajiya Mammah ce. Sai da ta gama kallemu sannan cikin harzuƙa ta ce, “Eh lallai. Mu an hanamu zuwa amma Mashi'a na nan. Wai ko dai zancen Fahad ɗin gaskiya ne mune ake zargin mun haukata kin Ummu-Hidaya?”.

Murmushi kawai Ummie tayi batare da tace mata komai ba. Sai Hajiya Mama ce ta ce, “Kai Adda wane zancene haka kuma?”.

“K! saurara min da'alla auta. Wai shin gaskiya a buɗe sai muƙi faɗa saboda muna tsoron wa? Yo inba da gaske mune dai ake ganin mun haukatatan kamar yanda ɗan ta ya faɗa ba wane take-take ne wannan? To idan ance ke kada mu dubaki ai ya kamata ma musan shi ɗan uwanmu yana gidan muzo mu gansa muji daɗi ko. Ni narasa wannan al'amari haka komai a munafunce. Yaranki sun rainamu a gida, kowanne sai ya gasa mana magana. Ƙarshen raini ma da nuna mu ba'a bakin komai muke ba aure Awwab yaje yayi a ɓoye saboda gamu mayu kada mu sani mu cinye matar ko? Ko miye abin ɓoyewa ga yar drivern gida? To fa gaskiya ni ina son gidan nan ayi zama, dan bazan bar waɗan nan abubuwan da suka faffaru su wuce a banza ba nan gaba a sake samun hanyar wulaƙantamu ehe. Dan haka ALLAH ya baka lafiya Mu'azz sai anyi zama wlhy. Shima Abdullahi naga ashe ya fara zama almunafunfun, yo inba munafunci ba dan ya zama ɗan sanda sai ya wani ɓoye fisabilillahi. Gida dai gaba ɗaya babu saiti kamar an koro mu da ga dawa kowa ruɓaɓɓe”.

Babu wanda yace da ita komai. Ita Ummie ma ta maida hankalinta kaina ne kamar bata san tanai ba. Sai na fahimci itama fa tana da irin shariyar Yaya Awwab. Sai Paah ne ya kalleta cikin mamaki ya ce, “Abdullahi kuma Addah?”.

“Ƙwarai kuwa Mu'azz Abdullahi dai daka sani. Ni ba zamansa ɗan sandan bane ya ɓatan rai ba, yanda ya ɓoye mana sai kace abun wani mugun abu. Ko miye a cikin ɗan sanda kuma mtsoww!!”.

A mamakin kowa sai Paah ya saki murmushi. Bai kuma sake cewa komai ba ya zame ya kwanta abinsa. Nima kama hannuna Ummie tayi muka fita a ɗakin muka barsu.....

□□□□□

Kai tsaye gidan Baba prof ta wuce. Dan ta gama tsara dole ta sake neman kusanci da shi in har tana son aikinta ya tafi yanda ta tsara shi. Tako yi sa'adar samun farkawarsa a barcin da giya ta sakashi kenan. Zuwanta yasa aka isar masa da saƙo. Ya jima baice komai ba dan mamaki, sai da ga baya kawai ya jinjina kansa da yin alamar ta shigo.

Tunda ta shigo cikin takun ƙasaita da izza yake kallonta kamar yanda itama shi take kallo. Sai da ta kai zaune ta saki wani murmushi da faɗin, “Barka da rana”.

Maimakon amsa mata gaisuwar sai ya ce, “Miya kawoki nan?”.

Murmushi ta sake saki tana langaɓar da kai gefe sai kuma ta daidaitashi. “Da gani har kai ka sani na sani muna buƙatar juna a wannan gaɓar”.

“Haka tunaninki ya baki”.

“Kaima haka naka tunanin yake yallaɓai. Kada kai wasa da wannan damar. Daga ni har kai muna yaƙi akan abu guda ne, sannan maƙiyanmu guda ne. Idan munce yaƙin ne bazamu iya tare ba lallai munyi kuskure. Kafin kuma cimma burinmu da kai maƙiyanmu ƙasa to sune zasu fara kaimu domin sun ɗakko hanya. Commondo da ga ni har kai ya shirya cin amanarmu ne. Dan yayi kidnapping Mu'azz batare da mun sani ba, bai kuma sanar mana ba saboda yana da wata manufa a zuciyarsa game damu. A binciken dana gudanar yanzun na tabbatar da shine ya gayyaci Jannifer domin su canja ma Mu'azz wajen zama shine aka kama su”.

“Lawisa! Kinsan ko mi kike faɗa?”.

“Niko na sani Yallaɓai, idan baka yarda ba kalla wannan video ɗin”.

Tai maganar tana miƙa masa wayarta. Amsar wayar yay, yayi playing video ɗin data latso masa. Rai-rai kuwa abinda ta faɗa ne a video ɗin. Dan ga Commondo zaune tare da Jannifer suna tsara komai. Dunƙule wayar Baba prof yay a cikin hannunsa zai yi jifa da ita Hajiya ƙarama tai saurin tashi ta riƙe kayarta.

“Please! calm down, yanzu fa ba lokacin fushi bane ba. Lokacin yin faɗan ƙarshe ne kawai. Idan ba hakaba wahalarmu ta shekara da shekaru kuwa zata tafi a banza. Muna da ƙalubale daban-daban dake zagaye damu. Na farko dai Ummu-Hidaya ta warke, na biyu yaƴanta Awwab da Fahad dan shima yaron tsagera ne abinda kai musu ya warware. Ga Abdullahi matsayin jami'in tsaro kuma shinema case ɗin su Commondo ke a hannunsa. Ga Commondo ya juya mana baya. Sai dai ban sani ba ko kasan dama shi ɗin Abdullahi ɗan sanda ne?”.

“Ya kamata nasan tun yaushe Commondo ke cin dunduniyata”. Baba prof ya faɗa a kausashe maimakon amsa zantukan data lissafo masa. Tasan wannan mutumin ya gama zarewa, amma bazatayi sake ba dan mugune, dan haka kawai ta saki murmushi. Cikin ɗan laɓe baki ta ce, “Wannan duk mai sauƙine zamu iya bincike. Amma dolene muyi duk yanda zamuyi mu gansa a yau kafin gobe, in ba hakaba yayi magana mun kaɗe”.

Kai kawai ya jinjina mata tare da tabbatar mata karta damu zuwa anjima zataga kiransa akan hakan. Amma ta kasance cikin shiri.. cikin gamsuwa tai masa sallama ta wuce tana wani makirin murmushin nasara. Tana fita daga nan gida ta wuce ranta fes. Dan kaso arba'in cikin ɗari na damuwarta ya kwaranye. Koda ta iso gidan wanka ta farayi, dan zuwa yanzu ta samu ƙwarin gwiwar yin hakan. A'i ta saka ta kawo mata abinci, ta ɗan ci tasha magungunanta sannan ta nemo Rubayya a waya. Ta sake tabbatar mata kada ta bari aikinta ya wuce gobe. Dan haka tayi ƙoƙarin zuwa ta kwana a gidan yau. Bata jira cewarta ba ta yanke kiran.

Tana gama wayar ɗakin Arwa ta shiga domin dubata. A bakinta take jin ai an sallamo Paah a asibiti tun jiya da dare ma kafin su amma yana sashen Awwab suma duk an hanasu ganin sa. Kasa cewa komai Hajiya ƙarama tayi sai idanu data zubama yaƴar Tata na tsawon lokaci. Kafin taja numfashi ta fesar tare da miƙewa kawai ta fita.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

Typing□

*_Typing□_**_Typing□_*

*_Typing_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-four

.....Daga station Maash guesthouse ɗinsa suka wuce. Da ga shi sai Hayatu da Jaga suka shiga ciki. Sun fi zaman mintuna talatin Maash ɗin baice komai ba yana dai zaune ƙafafunsa a harɗe ya jingina kansa da kujera idanunsa a lumshe da alama ya tafi dogon nazari ne. Jaga zaiyi magana dan ya matsu Maash ɗin yace wani abu Hayatu yay masa nunin yay shiru cikin alamar yin zipping lips nashi. Ajiyar zuciya Jaga ya saki da rufe bakin nasa ruff ya koma ya zauna yanda yake. Maash ya jima a haka har akai kiran sallar azhar sannan ya buɗe idanunsa. Miƙewa yay ya nufi bedroom yana ce musu suma suje suyi alwala. Hakan kuwa sukayi, bayan sunyo duk suka wuce massalaci.

Koda suka dawo daga massalacin ma sai da yay waya da matarsa babu ko kunya a gabansu kuma. Shi dai Hayatu murmushi kawai yake. Yayinda Jaga keta wani sinne kai shi ga ɗan duniya (😂😝). Wayar Maash ya ajiye fuskarsa da alamun murmushi, yana kallonsu yaga yanayinsu sai ya gimtse cike da basarwa ya gyara zama da faɗin,

“Muktar!”.

Ɗan sosa kai Jaga yayi dan in ba Maash ɗin dake kiran ainahin sunansa yanzu ba mantawa ma yake da sunan sa wani Muktar can. Cike da girmamawa ya ce, “Na'am babban yaya”.

“Ina ganin lokacin da zaka fara naka aikin yayi”.

Wani irin miƙewa Jaga yay ya taka rawa sai kuma ya ware baki zaiyi ihu. Da sauri Hayatu yay gyaran murya. Baki jagan ya dafe da hannu biyu shima da sauri yana waro idanunsa waje. Sai kuma ya koma ya zauna kansa a ƙasa ya ce, “Afuwan babban yaya. Kasan hankalin bai gama zama ba sai kun haɗa da addu'a”.

Komai Maash baice masa ba sai ma maida hankalinsa da yay akan tab dake hannunsa. Sai Hayatu ne ya ƙumshe baki yana yʻar dariya ciki-ciki. Shima ɗagowar Maash ya sashi saurin haɗiyewa ya daidaita yanayinsa.

“Wa zaka fara kaima ziyara?”.

Cike da zumuɗi Jaga ya ce, “Commondo”.

Murmushi ya nema suɓuce ma Maash amma sai ya gimtse yana mai ɗan taɓe baki cike da basarwa ya ce, “Okay good and fine. Kanada damar yin hakan a yau. Dan Iyayen gidan nasa na shirin ganawa da shi a daren yau suma. Kana da damar basu assignment lokaci ɗaya.”

Wani irin daɗi ne ya ratsa zuciyar Jaga. Nan take ya shiga sambatun godiya kamar wanda aka yima wata ƙyauta. Ga shi dai a zahiri da shiga kamar ba shi ba ya shiryu. Dan bayan an gama jiyyarsa daga suƙar wuƙa Maash da kansa ya kaisa Rihab akan matsalar shaye-shayensa. Ya zauna tsahon watanni har ALLAH yasa aka dace batun shaye-shaye ya zama tarihi. Shine ya sake ɗaukarsa zuwa ƙasar Canada aka sakashi wata makaranta domin fara sanin minene ma amfanin rayuwa. Yayi wata biyu acan aka sake maidashi ƙasar Saudiyya a yanzu haka yana ɗaukar karatun addini dana zamani. Wannan zuwan nashi Nigeria ma anyi amfani da hutun makaranta da suka samune. Yanzu kam a rayuwarsa ji yake babu ya Maash. Shine uwa shine uba. Komai ya sakashi zai iyayi barema akan waɗan nan mutanen da shi kansa burinsa ɗaukar fansa a kansu musamman ma Commondo da ya zama sanadin ta'azzarar lalacewar rayuwarsa. Sannan ya shirya kashesa a gaɓar da yake ganin zai kuɓuce masa duk da wahalhalun bashi kariya daya kasance yana yi a tsahon shekaru.

A duk ta yanda zai ziyarci cell da taimakon Isma'il Maash ya tsara masa. Da ga haka suka ɗan ƙara tattaunawa sannan suka fito. Wani wajen suka sake zuwa shi da Hayatun, shi kuma Jaga ya tafi masaukinsa. Daga nan gida suka wuce, inda suka tarar su Fahad baje a falo anata tsara yanda shagalin bikin sunan gobe in sha ALLAHU zai kasance. Dan zasuyi walima kawai anan cikin Mansion ɗin. Duk sannu da zuwa sukai musu. Hayatu ne kawai mai amsawa. Mai gayya da aiki kam hannu ya ɗaga musu kawai idonsa akan Samraah dake goye da baby a baya tana cin abu a bowl da bai san ko minene ba. Itama dai ɗan kallonsa tayi, sai kuma a hankali ta sauke idanunta muryarta can ƙasa ta ce, “Sannu da zuwa”.

Kai kawai ya jinjina mata tare da janye idanunsa a kanta a wani kalar slowly. Sai kuma ya nufi ɗakin Ummie cikin takun nan nasa.....

□□□□□

Tun Commondo da Jannifer na saka ran zuwan iyayen gidansu har al'amarin ya fara basu mamaki. Musamman ma Commondo. Dan yayi tsammanin in har ya kwana Baba prof bazai barsa ya yini ba. Amma sai gashi har ana shirin fuskantar wani daren babu Baba prof babu Lawisa. Koda yake yasan ita bazata zo ba. Saboda gaba ɗaya ya haɗa lissafinsa akan shirinta na turo masa Jannifer. Tun kuma daren jiya ya gama kitsama kansa yanda zai wargazata. Har shine zata shirya ma tarko. Ashe shirin nata ba'a kan yallaɓai kawai yake ba har da shi. Lallai zata san ta taɓo gidan rina wlhy. Dan ko bai fita a wajen nan ba akan lokaci yayi alƙawarin sai ya tarwatsa rayuwar Lawisa tazo ta samesa anan kusa...

A ɓangaren Jannifer ma dai hakanne. Dan zuciyarta ta fara bata Hajiya ƙarama na shirya wani abu ne tayi amfani da ita. Idan kuma ba haka ba tsautsayine ya faɗa mata. Amma ya kamata ace Hajiya ƙaramar tazo dan fitar da ita. Sai kuma gashi shiru wai malam yaci shirwa gashi oganta bai san tama amshi wannan aikin ba. To wlhy ta ɗauki alƙawarin in har Hajiya ƙarama batayi wani abu daga nan zuwa gobe ba har wani daga cikin sirrinta ya fito lallai itama sai ta kaita ƙasa dan sai dai suyi mutuwar kasko wlhy.....

□□□□

Muna zaune a inda ya barmu sai gashi ya fito. Narasa miyyasa yanzu idan ya shiga ɗakin Ummien bai wani jimawa. Kuma haka zai fito fuska ciɗin-ciɗin. Ina ji a raina kamar hakan nada nasaba da Paah dake a ɗakin yanzu. Ko saboda mi babu jituwa tsakaninsu da mahaifin nasu oho? Dan in batun sihiri ne zuwa yanzu ai Alhamdullah. Amma in sha ALLAHU shima Paah ɗin zanyi ƙoƙarin fara shayar da shi ruwan addu'ar da muke sha tunda ALLAH ya dawo da zamansa nan ɗin. Ganin bai kalla kowa a cikinmu ba ya haye sama nima sai na miƙe riƙe da bowl ɗin madara da sugern dana haɗa waje ɗaya nake sha. Dama Ya Hayat ya amshi Baby. Ruwa na ɗauka nasa a tray sannan na nufi ɗakin nasa. Tsaye ba samesa da ga shi sai dogon wandon jeans ɗin jikinsa ya cire rigar har singlet ɗin ciki. Wandon ma ya kwance belt ɗin amma bai zaresa ba. Wayata ce a hannunsa yana dannawa, da mamaki na ɗan kallesa na ɗauke kaina. Dan wannan jikin nasa a bubbuɗe sam bana son ganinsa sai inji duk ina ƙara tsorata da shi. A hankali na ajiye tray ɗin ruwan ina faɗin, “Sannu da dawowa.”

Wayar ya ajiye tare da ɗan kallona ni da tray ɗin. Ban damu da kallon da yake min ɗin ba na kai zaune ina ɗaukar bowl ɗin madarana da shuga na cigaba da sha. Shima zaman yayi yana mai ɗaukar goran ruwa dana ajiye na addu'oi ya ɓalle murfin ya kai bakinsa. Sai da ya shanye tass ya ajiye goran sannan na kauda kaina

a kansa. Yunƙurin miƙewa nake na wuce bathroom haɗa masa ruwan wanka a bazata matuƙar bazata naji saukar muryarsa yana furta, “Wacece ita?”.

Sosai naji ƙirjina ya motsa. Amma Abinka da ɣar jarida sai na dake na kallesa cikin nuna mamaki da rashin fahimta na furta, “Wake nan?”.

Shiru bai da alamar sake tanka min, sai kuma ya ɗago ya zuba min idanun nan nasa masu firgitarwa. Babu wasa a tattare da shi ya ce, “Samrh! Who is she?”.

Baki na murguɗa kaɗan, sai kuma na marairaice fuska da faɗin, “My hot ban ga gane wa kake magana ba Please. Naga dai tunda ka shigo iya mu kaɗai ne ka samu zaune”.

“Hummm!”.

Yace kawai yana miƙewa. Murmushi na saki a karo na farko, sai kuma na matso inda yake nasha gabansa ganin niyyar barin wajen yake. Kallona ya tsaya yi kamar yanda nake kallonsa nima cike da shauƙi. Sai kuma na matsa a hankali na shige jikinsa na rungumesa. Ajiyar zuciya muka sauke a tare, na sake ƙanƙamesa da faɗin, “Yarinyar jiya kake magana?”.

“Uhmm!”.

Ya faɗa acan ƙasan maƙoshi.

“Labarin mai tsada ne. Sai idan nima zaka gaya min wanda nake son ji na maka alƙawarin faɗa maka. Dan tabbas abinda ya shafi yarinyar a garemu mai muhimmanci ne”.

Shiru kamar bazai ce komai ba. Har ma na fidda ran ji sai naji saukar hannayensa saman bayana ya sake rungumoni da ƙyau. A cikin wani kalar salon rikita ni ya fara shinshinar wuyana. Ji nai ina daburcewa dan haka na mintsinesa ta re da ƙoƙarin janye jikina na ce, “Wayyo ni My Lion please”.

“Anƙi please ɗin faɗa min”.

“Anƙi wayon nima sai ka fara faɗa min”.

Numfashi ya ɗan furzar tare da ɗagowa ya sake rungume ni. “Naji”.

Ya faɗa a takaice kamar abin dole. Duk da naji haushi sai na daure. Musamman ma ganin la'asar ta gabato. Kamar yasan mike a raina shima sai ya kalla agogon. Kallona yay idanunsa a ƙanƙance. Cikin motsa lips ɗinsa ya ce, “Salla first”..

Nima sai na ce “Wanka fa?”.

“Na gaji ki mun”.

Kafaɗa na maƙe masa alamar a'a.

Kansa ya nuna alamar wai shi ɗin?

Na ɗaga masa gira ina murmushi. Hannu ya kai zai damƙoni na goce da sauri ina dariya. Sai ya ɗan ciza lips irin zaki gane idan na kamakin nan ya wuce bathroom ɗin.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

Typing□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-five

.....Bayan idar da sallar la'asar ɗin ya jima bai shigo ba. Harma nai zaton ya gudu ne sai gashi ina falon saman zaune ina waya da Gwaggo Gudidi da miss call ɗinta dana sake gani ya sakani kiranta naji ko wani abu ne ya faru. Bedroom ɗinsa ya wuce babu jimawa sai gashi ya fito. Zama yay a kusa da ni tare da zame jikinsa ya kwanta kansa a saman cinyata. Ɗayan hannuna ya kama ya riƙe kan nasa ya ɗaura a saman shafaffen cikinsa ya harɗesa cikin nashi da yay folding a ƙirji. Jinai gaba ɗaya wayar ma na kasa cewa komai. Amma dai na dake har muka kammala. Sallama nake ƙoƙarin mata ya buɗe idanunsa da mun nunin na bashi wayar. Sai da na waro ido sosai amma sai bai sauraran ba ya kai wayar kan kunnensa. A mamaki na sallama yay cike da girmamawa da gurɓatacciyar hausarsa da sai anyi da gaske ake gane wasu kalmomin. Shiyaysa ma ni nafi ganewa muyi magana da turanci a koda yaushe. Shima yama fi yin hakan. Amma a raina na ɗauri ɗammarar koya masa Hausa in sha ALLAHU.

Nasan ba gane maganarsa Gwaggo keyi ba dan haka hirar bai tsaho ba ya bani wayar. Sallama nai mata batare dana saurari tsogumin da take akan rashin gane

abinda yake fada ba na yanke kiran. Wayar na ajiye da kai hannun nawa cikin sumarsa daya warware na fara tausa masa kan nasa da yin wasa da gashin. Idanunsa ya lumshe da ƙanƙame hannuna dake a cikin nasa har yanzu. Cike da sanyi na ce, “My Hot!”.

A can ƙasan maƙoshi ya ce, “Umyim”.

Ban damuba na ce, “Abinci fa?”.

Kansa ya girgiza min alamar bazai ci ba. Cike da damuwa na ce, “Miyyasa?”.

Idanunsa ya buɗe ya kafeni da su. Sai kuma ya lumshe da sake buɗewa cikin motsa lips ɗin sa ya furta, “later”.

Kaina kawai na jinjina masa da gyara zamana. Dan nasan tunda yace bazaicin ba ba cin zaiyi ba fa ko miza'ayi. Sakin batun abinci nayi na kama mai muhimmanci. A ɗarare na ce, “Na maka laifi fa. Amma dan ALLAH kayi haƙuri ka yafe min tun kan na faɗa”.

Shiru kamar bazai ce komai ba sai zuwa can ya ɗan buɗe idanunsa da suka sirka yanayi, sai kuma ya sauke ajiyar zuciya da miƙa hannu ya ɗauka laptop ɗin sa daya ajiye saman Centre table. Filo ya ɗauka ya ɗaurata a saman cikinsa duk yana daga kwancen, sai da ya fara ƙoƙarin kunnata ya ce, “Ai nasa zaki ɗauka ki sake dubawa shiyyasa na ajiye miki inda zaki gani”.

Da mamaki na ce, “Kasan akan mi kuwa nake magana? Flash ɗin ranar fa?”.

Murmushi kawai ya saki da ɗan jinjina min kansa batare da yace komai ba. Gaba ɗaya sai ma na gagara cewa komai dan mamakinsa. Harga ALLAH mutumin nan ya fara bani tsoro, sai kuma can da nai tunanin camara ya saka a ɗakin nashi yasa na ɗan ji nutsuwa. Abinda ya kunna a laptop ɗin ne ya ɗauka hankalina. Sai na nutsu ina kallo. Gaba ɗaya abinda ya faru jiya ne lokacin da suke shigowa gidan da Ummie. Kasa daurewa nayi sai da nayi dariya, tare da jan hancinsa ina faɗin, “Oh My Lion ashe kaima bakinka ya iya magana haka. ALLAH ya shirya Yaya Fahad wlhy, harda wani faɗin a dafasu a tukunya a baku kunci kuna kora ruwan companyn Maashh.”

Murmushi kawai yayi baice komai ba. Nima sai na cigaba da faɗin, “Amma Ya Awwab ka kalla yanayin Baba kuwa? Da Hajiya ƙarama? Sannan video ɗin waccan ranar ka kallesa?”.

Kansa ya jinjina min. Sai kuma a hankali ya furta, “Mi kika fahimta ke?”.

Ɗan jimmm nayi alamar tunani, dan bazan iya katoɓarar fitowa fili na sanar masa ainahin abinda ke'a raina ba gaskiya. Kakansa ne fa, tab ɗin ba ruwana.

“talk”.

Ya faɗa yana matsa hannuna.

Murmushi na ɗan masa da faɗin, “Uhmm inaga mubi a hankali kawai watarana zaka fahimta. Dan zata iya yiwuwa abinda ni nake tunani daban wanda yake gaskiya daban. Amma dan ALLAH ka amsa min abin nan ɗaya kuma yana cimun zuciya. Shin mutumin nan da naga ka zare wuƙa a jikinsa lokacin bikin buɗe Companyn ka kai ne ka kashe shi? Ko miya faru?”.

Ɗan murmushi ya saki a karo na farko, tare da kai hannuna dake cikin nasa kan mitsitsin bakinsa ya sumbata.

“Yau kuma aikin jaridar ne ya tashi?”.

Cike da shagwaɓa na ce, “Oh ALLAH daga tambaya”.

“Nima ai bance bazan amsa ba”.

Ya faɗa yana ɗago ido ya kallan. Sai kuma ya gyara kwanciya da maida su ya lumshe. Numfashi ya ɗan furzar da fara magana a hankali. “Mama ta baki tarihin gidan nan dan haka zan faɗa miki daga dalilin buɗe Company.”

Kaina na jinjina masa cike da zumuɗi. Cigaba yay da faɗin, “A tsakanin da Ummie ta samu lafiya aka ƙirƙiri samar da companyn Kano. Kusan ma itace ta zo da shawarar hakan dan mace ce mai matuƙar experience akan Bussines. Sai dai koda najema Baba da batun sam bai bada goyon baya ba shi. Sai ma illolin yin hakan daya nuna min game da yan arewa. Abin ya tsayan a rai na sake samun Ummie da batun amma sai ta balbaleni da faɗa tare da cewar umarni ai ita ta bani ba shawara ba. Dan haka nabi Umarnin aka fara samar da Company. Ban sani ba ko hakan ne ya ɓatawa baba rai sai ya fita daga batun gaba ɗaya. Ana gab da gamawa jikin Ummie ya ɗan fara motsawa. Hankalinmu ya tashi matuƙa muka shiga neman mai maganin nan na Togo amma babu shi babu alamarsa. Tun muna ɗaukar komai zai dai-daita har abu ta ɓaci sosai, abubuwa suka ƙara rikicewa. Haka dai cikin dauriya na ƙarasa gina wannan gidan na muka tare. Sannan na shirya batun buɗe Companyn Kano. Tun bayan sakowa da ga batun auren Paah da Hajiya ƙarama yanda take nuna damuwarta akan Ummie da ni yasa nake ɗan sakewa da ita. Har itama na koma kiranta da Ummy, ko bana gida takan kirani ko na kirata a raina ina jin bayan Mama kamar itama uwa ce. Dan hatta cin abinci takan nuna damuwarta da naci ko ban ci ba a duk sanda ta kirani. Hakama idan ina gida ko asibiti ta dawo a gajiye takan tsaya ta samar min abinda zanci hakan yasa na ƙara bata muhimmanci fiye ma da Paah da nake matuƙar jin zafi. Sai dai me a gaɓar bikin buɗe Company duk sai suka ƙi shirin halarta har Baba dan barin ma ƙasar yay shi. Raina ya sosu nai fushi na fita batunsu da ga ni sai su Hayatu da yarana muka tafi. Kwatsam an fara gudanar da taro lokacin da kike barin wajen akai kiran hayatu a waya. Ta gefen ido nake kallon yanda yake amsa wayar yan zufa, kafin ya sauke a daburce ya matso inda nake. Sai dai yana ta ƙoƙarin ganin ya saita kansa dan kar a fahimta. A kunne ya gwargwaɗa min kiran da Jaga yay masa da abinda ya faɗa

masa, dan haka nai excusing kaina na shiga ciki Hayat ya biyo ni. Da taimakon wayar hayatu muka gano ɗakin da Jaga yake. Da farko na ɗauka set up ne akayi, sai da Jaga ya shiga sanar mana wanda ya sokesa da aikin da ya kawosa jikina da abinda aka aikosa yi a yau amma ya canja shawara shine aka kawosa nan ɗakin dan a kasheshi a kuma maida abun kaina. Dan haka cigaba da rayuwarsa nada muhimmanci garemu dan yana da muhimman abubuwa da zai faɗa mana da zasu amfane mu. Wannan daliline yasa nai ƙoƙarin cetonsa duk da Hayatu na nuna min na barsa ƙarya yake yi. Amma ban saurarensa ba. Ina ƙoƙarin zare wuƙar da aka saka masa ke kuma kika iso batare da mun sani ba. Ashe har muka fita da shi kina biye damu. Duk da dai a lokacin da nake fitowa a ɗakin ƙamshin turarenki yasa naso na farga da ke, amma hankalina ba'a wajen yake ba dan haka na fice kawai. Ansha matuƙar wahala kafin samun rayuwar yaron, sai dai da yake ALLAH ya ƙaddara akwai sauran kwananasa gaba yasa ya warke kamar komai bai faru ba.. Ambatar sunan Grandpa ɗina a wannan ranar da shi Muktar Jaga yayi da ita Lawisa yasa na tabbatar da gaskiyarsa dalilin zuwan sa Kano a bazata har hirar da yay da ke. Tun daga lokacin nai doubling question mark ɗin dana sakama kowa a kansu. Nasa ya zama biyu. Na kuma janyema Lawisa sosai . Wannan video kuma ya tabbatar min da inahin fuskar ita Lawusar dai ce ba wata ba..”

A hankali hawayen da naketa riƙewa suka silalo min. Muryata na rawa na ce, “Hajiya ƙarama?”.

Kansa ya jinjina min alamar eh kawai. Wasu hawayen ne suka sake ɓulɓulo min. Cikin sake ƙanƙamesa na ce, “Yaya Awwab kayi haƙuri, amma wlhy zuciyata na bani sune suka kashe Abie da Babana.....”

Da wani irin mugun sauri ya ɗago idanunsa da launinsu ya canja gaba ɗaya ya kalleni. Kaina na jinjina masa nima cikin tabbatarwa na ce, “Tabbas Yaya akwai ƙamshin gaskiya a magana ta. Dan na bibiyi videon ɗin nan da ƙyar tare da tankaɗesa da rairaiye sa. Kuma alamu sun nuna Ummie tasan wani abu shiyyasa ya durƙusar da rayuwarta zuwa wannan yanayin”.

Ai sosai ya tashi zaune gashin jikinsa na wani mimmiƙewa. Muryarsa har rawa take wajen faɗin, “Samrh miyyasa kikayi wannan tunanin?”.

“Yaya hujjoji da yawa. Dan kasan jami'in tsaro, da lauyoyi, da likitoci, da ƴan jarida al'amarinsu na kamanceceniya da juna. Saboda komai nasu yana tafiya ne a bigiren bincike. Shiyyasa zakaga a mafi yawan lokuta indai masu wannan ayyukan sun san abinda suke basu da wahalar fuskantar case irin wannan da saurin kama bakin zaren sa.”

Hannu ya kai saman yay wani kalar shafosa tamkar mai sharce ruwa ya yarfar. Bawai yau ya fara irin wannan tunanin ba shima. Sai dai a kaf bincikensa bai taɓa samun wanda ya ƙarfafa wannan hasashen nashi kamar ita ba a yau. Dan yanda ta fassara abin da confidence abin a duba ne..

Yunƙurawa yay zai tashi na riƙosa da sauri. “Yaya ina zaka je?”.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-six

.....“Ina son naga Ummie”. Ya faɗa da alamar ran yaɗan maza ya ɓaci. Kaina na girgiza masa da sake damƙe hannun nasa na ce, “No Ya Awwab ba yanzu ba. Ummie da bata bukatar kowane irin matsi daga garemu akan son sanin gaskiyar al'amarin kamar yanda doctor ya faɗa al'amarin ta daki-daki yake buƙata. Dole mu cigaba da haƙurin binta mataki-mataki dan akwai abinda itama take shiryawa, kar kuma ka manta ya sanar mana ba komai ya dawo kanta yanda ya kamata ba a yanzu. Sannan tanama naka takun tankaɗa da rairaya ne shiyyasa taƙi fitowa fili ta gaya maka koda abinda ya rage a zuciyarta ne. Dan haka mizai hana muyi wani abu domin gabato da komai a gaggauce”.

Idanu kawai ya zuba min batare daya amsa ba. Ban damu ba na cigaba da faɗin, “Ban san tsare-tsaren ka ba. Amma a nawa tunanin ya kamata kayi wani abu saboda dalilai biyu. Na farko matsayin Baba prof mahaifin Paah. Bafa abune ƙarami ba fiddo da ainahinsa ta ɓangarenka kai tsaye ko ɓangaren Ummie. Hakan zai kawo rabuwar kan family ɗin nan, dan koba komai sunan mahaifi yake amsawa a garesu. A kai kanka ma bar ganin ba komai bane wlhy sai ka jigata matuƙar jigata dan jini ya wuce wasa. Sannan babu alfanu duniya ta raja'a akan rikicinka da Family ɗinka. Hanya zaka bama abokan gaba na bayan fage suci tuwo a kanka tako wane fanni. Kasan dai masu iya magana sunce, DAUƊAR GORA CIKI KA SHATA. Dan haka kamar yanda ka fara yaƙin ta hanyar sunƙuru, tofa mafitar ɗayace a ƙarasashi ta hanyar TURNUƘU FAƊAN IBILISAI. yaro bai gani ba balle ya raba. Ma'ana mu zuba kamar

yanda suka ɗauki shekaru suma suna zubawa. A maimakon baƙin fenti ya shafe ka, ruwan sama ne zai wankeka tatas ya kuma wanke Ummie su da bakinsu su faɗi ainahin abinda suka shuka, idan ma tonama kan nasu asiri sukai wa duniya sune suka zaɓi hakan. Ya kaga wasan zai kasance”.

Na ƙare maganar da kashe masa ido ɗaya. A mamakina sai naga kawai ya saki murmushi da cije lips ɗinsa. Hannunsa ya dunƙule tare da miƙo min□□ Nima kawai sai nayi yanda yay ɗin muka buga. Da sauri na janye nawa ina yarfarwa da faɗin, “Shiiii azaba wanan hannu kamar rodi”.

Ƙaramin murmushi yayi da ɗan ɗallamin lips kaɗan da yatsarsa. Sai kuma kawai ya jawoni jikinsa ya rungume tsammm. Ajiyar zuciya muka dinga saukewa a tare. Na ɗan motsa zanyi magana a hankali ya ce, “Shiiii bana son surutu”. Sai kuma ya ɗaukeni cak yay bedroom da ni. (Ba sai kunji miya faru ba kuma ehe😉 dan naga fans ɗin bily kun cika sa ido😉□😝□)

Lallai yau Samraah taci tuwo a kammu bari mu ware□□□□, danginta kuma har daku shinnnnnn😂😝?.

□□□□□

Ƙarfe goma na dare Baba prof da Hajiya ƙarama suka kama hanyar station. Dan dama tana asibiti tun bayan sallar magrib. Ta can ma Baba prof ɗin ya ɗauketa kasancewar da kansa yay driving abinda ya jima baiyi ba. Amsar tuƙin hajiya ƙarama tayi. Kasancewar al'amarin hanya ce daga babban jami'in da yafi Uncle Abdullahi faɗa aji yasa tun a gate aka tarbe su. Baba prof ya yankema zuciyarsa sai ya fara jin tabakin commondo da tabbatar da gaskiyar Hajiya ƙarama sannan ya fitar da shi, dan ba fitar da shi ɗin ne mai wahala ba, amma maganganun Hajiya ƙarama suka canja wancan tunanin nasa. Yana son tabbatarwa, idan gaskiya ta faɗa shi da kansa zai saka a ɓatar da Commondo tun a daren yau. Idan kuma ƙarya take zai saka a fiddashi batare da saninta ba. Daga ƙarshe hukuncin da yay niyyar ma Commondo zai sa Commondo ɗin ya maidashi a kanta.

Kamar yanda yake nasa tsarin a zuciya itama yana yin nata ne. Dan tayi waya da Dr Khunal yanzu haka zuwa gobe abinta data biya maƙudan kuɗi ita da Baba prof ɗin domin Maash zai iso a daren yau. Za kuma tayi aiki da shi akan Maash kamar yanda suka tsara tun farko, da shi Baba prof ɗin da Mu'azz. Ummie kuwa nata tanadin na musamman ne. Shiko Commondo ta riga ta gama bada kwangilarsa. Jannifer ma Baba prof zai ƙarasa mata ita shiyyasa ta azashi a keken ɓera.

Tunaninta ya katse lokacin da aka shigo da Commondo da Jannifer hannayensu duk da Handcuffs. Ga raunuka a jikinsu dake tabbatar da Dukansu akai babu jinawar nan. Dan bayan la'asar Uncle Abdullahi ya bada umarnin fara tuhumarsu amma su duka sunƙi cewa komai saboda damar da duk suka ƙudiri aniyar bama iyayen gidan nasu na yau kawai. Idan basu zo ba zuwa gobe zasu fara buɗe aiki. Shiyyasa suka jure da dukan bawai dan basa jin zafi bane ba ko ciwo...

Cikin tsawa jami'in daya kawosu ya nuna musu ƙasa matsayin wajen zama. Sannan ya koma daga ƙofar ɗaki ya tsaya dan yasan basu da wata hanyar guduwa tako ina office ɗin zagaye yake da jami'an tsaro irinsa. Daga Hajiya ƙarama har baba prof kallon Commondo da Madam Jannifer sukeyi kamar yanda suma suke kallonsu kallo irin na ƙurilla...

Kusan mintuna biyu kafin Baba prof ya janye nasa idon cikin gyara zama da kafe Commondo da ido ya ce, “Commondo ya akai aka faɗi a ragaya?”.

Murmushi Commondo yay da jinjina kansa. Sai da ya kalla gefen Hajiya ƙarama ya furta, “A ɓaɗinance talalace! A zahirance kuma ɗaurin goro ne!”.

“Akasin lissafi kenan fa”.

Baba prof ya faɗa cike da waro idanu.

“Na dukkan lissafi ne ma aka samu a wannan gaɓar oga. Dan shi macijin cikin ciyawa idan har yay kala da ciyawar sai yayi illa batare da ma'abocin taka ƙafa ya farga ba. Rafi da kogi zasu iya haɗa tafiyar wucewar ruwan cikinsu a hanya ɗaya. Amma shi kududdufi da gulbi koda suna maƙwaftaka akai rami a tsakaninsu ba lallai ruwan ɗaya ya ɓulla a cikin ɗaya ba. Dan ramin su baya kogo kamar na rijiya”.

Cikin ɓacin rai Hajiya ƙarama ta tare numfashin Baba prof dake ƙoƙarin yin magana. “Amma kun san magana cikin duhu haramunne a wannan tafiyar tamu. Anan duk ɗaya muke. Dan itama Jannifer abokiyar cin mushe ce. Banga dalilin ɗaure zance ba bayan muna neman hanyar gudu tare mu tsira tare ne a wannan gaɓar. Idan kuma har kukace wasan na nuna zalama ne, to karfa ku manta ku duk biyun nan linzamin dokin Lawisa ne. Musamman ma kai ɗin nan”. Ta ƙare maganar da nuna Commondo.

Wani shegen murmushi Commondo ɗin ya saki. Cikin ɗage gira ya furta, “Lawisa! Ke ƙaramar giwace, ragon layya kawai yay dogon miƙi zai iya yaddaki a dokar jeji. Ashe baki shirya wasan ba da ƙyau amma kikayi tunanin tararsa. Shi zuciyarki bata baki tabbacin ko Giwa ta faɗi tafi ƙarfin wawason yayan damisa ba. Shike nan, tunda kince muje a buɗe, muje ɗin, kin san dai ni bishiyar dabino ne wlhy bani yayan banza. Dan ko a ɗanyena nake rububin cina akeyi”.

“Kamar yanda kasan nafi ƙarfin damisar takarda. Sannan ni uwar bakirikice ba yarinya ba. Duk wanda ya sanni a cikinta ya ganni ba raino na akai ba. Miyyasa ka shirya cin amanata?”.

“Saboda kema naki shirin kenan?”.

“Amma kasan komi nayi akwai dalilinsa?”.

“Kamar yanda kika san nima bana komai sai da dalili. Miyyasa na ɗaukeki Hadari zaki maidani hazo?”.

“Ohooooooh!! da ƙyau!”.

Baba prof ya faɗa yana wani kwashewa da dariya da tafa hannaye. Gaba ɗayansu juyawa sukai suka kallesa. Duk kuma sai suka sha jinin jikinsu. Cikin daina tafin da musu nuni da hannu ya ce, “Ku cigaba mana, miyyasa zaku bari kuma?”.

“No oga relax. Kada ka ruɗar da kanka kadai san makircin wannan wawuyar”. Cewar Commondo da sauri. Da saurin itama Hajiya ƙarama ta cafe da faɗin, “Sai dai wawaye. Kai ni fa a wannan gaɓar banƙi a mutu ba har liman wlhy. Dan na gaji da tafiya da maciya amana waɗanda kansu kawai suka sani. Na kuma gaji da barin jakai ina dukan tanki.”

“Oh really?! To ai Lawisa ke ce babbar mai cin amana a cikinmu. Dan kece kika nunama kowa tashi ta fisheshi. Oga shine ya jawoki a wannan tafiyar ya kuma maidaki abinda kike a yau amma har kike tunanin watsar da shi...”

“Hahahaha!!! Commondo! Commondo!! Commondo!!. Lallai kai jaki ne na yarda. Wai shin kana yin duk wannan ne saboda tunanin wannan abun zai iya fiddaka a wannan wajen? To lallai kayi kuskure dan anzo gaɓar jifar gaffiyar ɓaidu. Dan anzo gaɓar da shi ɗin ma takansa yake bazai iya maka komai ba. Idan ma lissafin barin nan ɗin kake to ka bari, dan zama daram mai naƙuda ta samu katifa hahahaha!!!”.

Wani irin kallo Commondo yake ma Baba prof. Cikin zafin rai ya ce, “Oga!!”.

“Don't call me Oga again!!”.

Baba prof ya faɗa a matuƙar zafafe. Wani shegen murmushi Commondo ɗin ya saki da jinjina kansa. Tabbas badan handcuffs ɗin hannunsa ba babu abinda zai hanashi raunata mutanen nan guda biyu, har shi zasu haɗema kai. Amma babu komai zai musu abinda sai sun gwammace inama raunin yaji musu. Cikin tsantsan tsana ya kallesu ɗaya bayan ɗaya, “Lallai ku sani ku dukanku zaku tafka babban kuskuren da sai kun dawwama kuna nadamarsa a rayuwarku. Dan ni Commondo tauraro ne mai wutsiya. Sannan cinnaka nake ban san na gida ba. A tafiyata kuwa bana GUDU DA WAIWAYE. Idan har kaga nayi, abu mai matuƙar muhimmanci na dawo ɗauka. Kada ku taɓa tunanin ƙarfin iko ko faɗa ajin da kuke taƙama da shi zai

tserar da ku daga tarkon Commondo. Dan *_TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE_*. Kusa a ranku yanzu ne wasan zai faraaaaaa!!!!”.

Daga Hajiya ƙarama har Baba prof sai da suka ja baya saboda yanda Commondo ya ƙarasa magana ta ƙarshe a kausashe kuma da tsawa. Yayinda Jannifer ta kece da dariya. Sai da tayi mai isarta duk suna kallonta sannan ta dubi Hajiya ƙaramar.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-seven

....."Hajjaju wannan duk damuwarku ce dan ku kuka san kanku. Ni a wane matsaya nake? Dan bana buƙatar sake kwana a wannan wajen da ga ni har yara na. Kin san fa ni ba irin Commondo bace, da an cigaba da takura min bakina buɗewa yake caaaaaa!!!!! Da magana".

Fushin Commondo yasa Hajiya ƙarama watsama Jannifer harara. A harzuƙe ta furta, "In bakin naki bai buɗeba baki cika yɑr halak ba Jannifer. Shashasha kawai ana batun masu hankali kina sako ruɓaɓɓen bakinki. K! har kina da bakin ma jefama mutane maganar banza batare da an sakoki ciki ba".

"Oh yeer! Hajiya Lawisa amma dai kin san ni tururuwace bana jidon banza ko?".

"Duk jidon naki kiyi dan iyakarki tsintar gero da dawa amma ƙashi ko nama ƙaryarki".

"Haka kika ce?".

"Nama ce fiye da haka. Dan ku dukanku anan zan iya da ku".

“Ai ba abin mamaki bane dan MAGE taci amanar KARE!!”.

Wata murya a bazata ta daki dodon kunnensu. Gaba ɗayansu suka juya ga ƙofa da basu san yaushe aka buɗeta ba har mai maganar ya shigo musu babu notis. Kusan a tare Hajiya ƙarama da Baba prof sukai baya. Yayinda Commondo yay wata irin zabura da ga zaune yana ƙwalalo idanu waje. Jannifer da bata san ko waye ba kuwa ta ce, “Wannan gaskiya ne ɗan uwa”.

Murmushi Jaga ya sakar mata tare da kashe ido ɗaya yay mata alamar jinjina. Sai kuma ya wani ɗan jujjuya kai yana mai gyara tsaiwa cike da gadara ya bisu da kallo ɗaya bayan ɗaya. Kafin ya tsaida idanun kan Commondo. Rawa jikin Commondo ya farayi sosai. Da ƙyar ya iya furta kalmar, “Jaga! Fatalwa?”.

“Yes I'm. Amma ni ba fatalwa bane JAGA!!!! ne”. Ya ƙare maganar da wani irin kashe ido ɗaya cike da salon iskanci. Lokaci ɗaya Hajiya ƙarama da Commondo suka saki ihu. Yayinda zuciyar Baba prof kawai ta tsarga lokaci ɗaya cikinsa yay wani irin kalar bada sauti sai gudawa tsuuuuuu!!! Daga tsaye. Dariya Jaga ya kwashe da ita. Sai kuma ya nuna Baba prof da yatsa, ya nuna Commondo, ya nuna Hajiya ƙarama sannan ya kai hannunsa kan wuyansa yay alamar yankawa. Tuni itama Hajiya ƙarama fitsari ya ɓalle mata ƙafafunta suka fara rawa.

Cike da mamakin abinda ke faruwa da yanda zakunan dake hanƙoro kusan na mintuna talatin babu mai jin wani duk suka gigice Jannifer ta kalla Jaga cike da rashin damuwa ta ce, “Ɗan uwa halan kai ɗin waye dan ALLAH?!”.

“JaGa!!!! Gawa ta ƙi rami kenan. Sun gina naƙi shiga, ɗan Badamasi ke nan ajiyar ALLAH, mutuwarka sai cikar kwanakinka. Namiji ƙi gudu sa maza gudu. Ki basu shawara, yanzu ba lokacin gardama bane ba lokacin GUDUN CETON RAI NE. Domin gab ZAKI na gaskiya yake da fitowa shawagi. Dan haka mun shiga ƙarnin MAI RABON GANIN BAƉI YA GANI. Maƙiyanka fadawanka. A kafta Yaya Maaaaashhhhhhh!!!”.

Ya faɗa yana tafa hannunsa sai ko ɗiffff wuta ta ɗauke duhu ya bayyana. Wani irin masifaffen ihu Hajiya ƙarama ta fasa dan a zatonta fa Maash ɗinne ya shigo, itama sai gudawa zuuuu. Yayinda Baba prof ya yanke jiki ya faɗi kawai. Commondo kansa a gigice yake dan shi fa kamar su duk sun ɗauka fatalwa jaga yay musu, sannan ganin Maash anan ɗin tamkar ƙarshen numfashinsu ne. Ita kanta Jannifer da bata fahimci tushen zancen ba jin sunan Maash ya saka ƙirjinta fara karkarwa ta kawai fashe da kuka. Ga duhu office ɗin.....

😂Wai miyyasa mutanen ke tsoron Yayanmu haka. Koda yake shifa mara gaskiya ko a ruwa jiɓi yake

□□□□□

Gaba ɗaya ya hanani sake sauka ƙasa. Sai shine yaje massalaci. Bai dawo ba sai da akai isha'i. Da wannan damar nai amfani na sauka na haɗo masa abinci. Ummie na ciki saboda Paah, su Hafizzullah ma da alama suna masallaci tare da shi. Aunty Falaq ma na ɗaki dan haka harna gama abinda zanyi babu kowa a farlon. Ina idar da sallar isha'in na kwanta a wajen dan ɗan sanyi-sanyi nake so. Daga azhar har zuwa gabannin asubahi zaka sameni lafiya Lau kamar banda wata damuwa. Ana ce miki asuba tayi da ƙyar nake yin salla sai zazzaɓi da amaye-amaye har sai rana ta ɗaga kuma. Jin an ɗagani na buɗe idanuna, dan nasan mai mun hakan sai dai shi. Kallonsa nayi tare da ɗan tura baki gaba. Cike da shagwaɓa na ce, “Please My Hot ALLAH can yafi daɗi”.

Bai tanka min ba sai da ya sauke ni saman gadon. Yana ranƙwafe a kaina idanunsa cikin nawa yana bina da wani kasalallen kallo da zuwa yanzu na fara fahimtar fassarar halin da yake ciki a duk sanda yake mun shi. Cikin motsa lips ɗinsa kaɗan ya furta, “Kina son ki haifar min yara da sanyi?”.

Kai na girgiza masa a marairaice kamar zanyi kuka na ce, “ALLAH yafi min daɗi ne fa”.

Bai ce komai ba ya kwanta ta gefena yana mai rungumeni a jikinsa. A tare muka sauke ajiyar zuciya. Nima sai na sake shige masa da sake ƙanƙame shi. Mun jima a haka kafin ya fara canja salon kwanciyar tamu zuwa wani abu daban. Mamaki ya sani ɗagowa na kallesa. Ɗazun nan fa barowarmu falo ya.... Tunanina ya katse jin saukar mitsitsin lips ɗinsa kan nawa. Yanda ya iya bin hanyoyin mantar da mutum kansa yasa tuni ma na saki ragamar duk da nasan wahala ce dai bazan fasa shanta ba. Dan shi ɗin bana wasan yara bane. Marmarine da ga nesa....

Nako ji a jikina, haka na lafke masa wanka ma sai da taimakonsa. Dan ma yunwar da nake ji ta sa na kasa kwanciya na ce masa abinci zanci. Da kansa ya zubo abincin yazo ya zauna ya dinga bani. Nima sai na amsa ina bashi. Hakan ya ɗan taimaka min na ɗan ci shima yaci. Ina cewa na ƙoshi shima kuwa yace ya ƙoshi. Mamaki yake bani dan ban taɓa gamo da wanda bai damu da zaman cin abinci ba irinsa. Kwance zan kai ya kamani ya zaunar yana girgiza min kai alamar karna kwanta. Cikin shagwaɓa na ɗan tura baki dan kwanciyar nake so. Bai kulani ba sai jinginani da yay da jikinsa kawai ta ɗauki wayarsa yana latsawa. Ajiyar zuciya na sauke kaɗan, idona akan wayar nima nace, “Ya Awwab”.

“Uhhyimm”.

“Yarinyar nan ya kake ganin zamuyi da ita?”.

Shiru kamar bazaice komai ba. Sai kuma ya ajiye wayar yana furzar da numfashi. “Ki bar komai a hannuna dan zuwa yanzu haka ma tana hannu”.

“What! Ya akai hakan?”.

Na faɗa ina tashi zaune da ƙyau. Kallona yay shima sai kuma ya ɗan lumshe ido ya sake buɗewa akaina. Akan lips ya furta, “Bana wasa da DAMA”.

“Ni shaida ce”.

Na faɗa cikin kashe masa ido ɗaya da kai baki a hankali na sumbaci kumatunsa. Murmushi ya saki mai ƙayatarwa ya jawoni jikinsa ya rungume. Kiran wayarsa ne ya katse mu. Ɗauka yay, kasancewar muna a kusa da juna yasa naji duk abinda Hayatun ke faɗa. Yana ajiye wayar ya miƙe nima na miƙe. Kallona yay na ɗaga masa gira da faɗin, “Lokacin da zan taimaki mijina da tawa basirar yayi. Let's go”.

“My baby”.

Ya faɗa da soft murya yana kallon cikina.

Nima ƙasan nayi da muryata ina mai ɗora hannuna saman cikina na furta, “Yana tare da kariyar UBANGIJI”.

Baice komai ba yay gaba. Nima sai na juya na fita zuwa nawa ɗakin. Babu jimawa na fito, sai naci karo da shi a ƙofa yana niyyar shigowa. Batare da yace komai ba ya kama hannuna kawai.....

□□□

Sai da taimakon Isma'il Baba prof ya koma gida. Tsabar ɗimuwar da yake ciki yasa baima fahimci wanda ya maida shin ba. Hakama Hajiya ƙarama ita kanta bata san a yanda ta dawo gidan ba. Kawai dai ta tsinta kanta a bakin gate. Batako saurari mai taxi daya kawota ba ta afka ciki sai securitys ɗin ƙofa ne dake binta da kallo suna toshe hancin qarin kashin da take suka biya shi. Da ga Maash har Hayatu da Samraah da TJ dake jan motar da zasu fita da kallo suka bita suma.

Nannauyan numfashi na sauke da faɗin, “To ita kuma wannan ƙalau take kuwa? Jibafa jikinta kamar wadda tai kashi, gashi sam bata a hayyacinta”.

Hayatu ne cikin yar dariya ya karɓe da faɗin, “Babu tantama aikin Jaga ne wannan”.

“Jaga kuma?”.

Na faɗa ina kallon Maash da yay kamar ma bai san abinda ake yi ba. Yanzun ma bai tanka ba. Sai Hayatun ne dai ya bani amsa da, “Eh, ya kai musu ziyara ne. Kinga ko yanda suke tunanin ya mutu ganinsa a raye ai cakwakiya ce babba. Amma bari na taɓa Isma'il”.

Wayar Isma'il ɗin ya kira. Yana ɗagawa da dariya ya fara daga can. Hayatu shima sai ya fara dariya. Da ƙyar dai cikin dariyar Isma'il ɗin ya bama Hayatun labarin duk abinda ya faru batare da yasan a Hansfree wayar take ba. Shi kansa Tj dariyar yake yi. Yayinda ni kuma nai ƙasa da kaina kawai inayin tawa can cikin maƙoshi. Dan yanzun ma mai gayya da aiki bai tanka ba bai kuma kulamu ba. Cikin ƙanƙanin lokaci muka iso gidan da yay matuƙar ƙayatar dani. Dan ya ginu iya ganin mai kallo, sai ma ka iya ɗauka gilashi ne kawai gaba ɗayansa. Ni dai a zuciyata naita santina har muka shiga ciki.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-eight

.....Da sauri saurayin da muka samu zaune a falon ya miƙe tsaye cikin nuna girmamawa. Sai budurwar dake ƙasan carpet bakinta a ɗaure da seletep hannunta ma a ɗaure. A kallo ɗaya da nai mata na gane Murjanatu ce. Sai da na ɗan waro idanuna waje ina kallon Maash. Amma sai ya ɗauke nasa cike da basarwa ya cema saurayin da ya kira da Muktar ya kwance mata abin hannunta dana bakinta. Kamar yanda aka bashi umarni yayi, sannan ya koma ya zauna yana mai dakawa Murjanatu data sanya kuka tsawa alamar taima mutane shiru. Shirun kuwa tayi tana hawaye da kallona. Duk sai naji ta bani tausayi. Murya a sanyaye na cema Hayatu

su bata ruwa. Babu musu kuwa yaje ya kawo mata. Tako sha sosai tana sauke ajiyar zuciya.

Sai da naga ta ɗan samu nutsuwa sannan na tashi na koma kusa da ita. “Murjanatu”. Na kira sunanta a taisashe. Amsawa tayi muryarta na rawa sosai da jikinta. Kafaɗarta na dafa da kulawa na ce, “Ki kwantar da hankalinki. Bamu kawoki nan domin cutarwa ba. Sai domin mu kuɓutar da ke. Kamar yanda kika sani na faɗa miki sunana a waccan ranar. Sannan kin mun sani na tsakanin mai jiyya da ma'aikaciyar asibiti a wancan karon.”

“Hakane Aunty”.

Ta faɗa muryarta na rawa. Kaina na jinjina da kallon Hayatu na ce, “Yaya Hayat ko zamu samu hoton matar can a wajenku”.

Kai tsaye ya ce, “Abu mai sauƙi”.

Tab dake gefen ogan nasa ya ɗakko, yay ɗan danne-danne ya miƙo min. Hoton Hajiya ƙarama ne rangaɗaɗau kuwa. Anci ado na fariyya kamar kai mata magana ta amsa. Janye idanuna nayi daga kan hoton na maida kan Murjanatu da har yanzu ta kasa nutsuwa da ƙyau. “Murjanatu ina son ki kwantar da hankalinki ki kuma amsa min dukkan tambayar dazan miki. Hakan da zakiyi shine zai kuɓutar da a halinki dan bamu kawoki nan ba sai da muka san komai a kanki”.

“Dan ALLAH aunty kuyi haƙuri kada ku cutar dani, wlhy zan amsa muku duk abinda kuke buƙata. Bana son komai ya samu iyayena”.

“Babu abinda zai samesu. Sai dai ki sani a yanzu haka suna a hannunmu. Idan kin amsa mana abinda muke buƙata babu gargada to tabbas zaki samesu cikin aminci harma mu fidda mahaifinki ƙasar waje yaga likita akan ciwonsa.”

Da sauri ta jinjina min kai cikin ɗokantuwa. Hoton Hajiya ƙarama na nuna mata. Duk yanda taso dakewa sai da muka fahimci razanarta. Muryarta na ɗan rawa ta ce, “Shugabar asibitin da nake aiki ce. Sunanta Doctor Lawisa.”

“Micece alaƙar dake tsakaninki da ita bayan wannan?”.

Baki ta buɗe zata fara rantsuwa na girgiza mata kai da faɗin, “Gaskiya kawai Murjanatu. Dan da kunnena naji tana cin mutuncinki saboda kin sanar da wani cewar an cirema patient appendix. Wlhy kinji na rantse miki, idan baki faɗan gaskiya ba zan tafi na barki da su”. Na ƙare maganar ina nuna mata su Hayatu da Maash da yay wani zaman kasaita yanzu ya kwantar da bayansa da kujera ido a lumshe sai ka ɗauka ma barci yake. Amma ni nasan idonsa biyu mu yake kalloma. Cikin ruɗewa ta shiga roƙona akan karna barta da su zata faɗa. Zama na gyara alamar ina saurarenta.

Sai da ta shaƙi numfashi da kukan da ke mata kai-kawo sannan ta ce, “Aunty zan faɗa miki komai dana sani. Amma dan girman ALLAH ki taimakeni da iyayena in ba hakaba wlhy zata iya halakamu. Dan akwai wani da yaso yin irin wannan kuskuren na fallasa sirrinta har yanzu bamu sake jin labarinsa ba. Hakama mahaifiyarsa wayar gari akayi ta ƙone a gidansu ƙurmis akace gobara ce. Again wata ta taɓa bijirema umarninta a gabanmu ta mata allurar poison ta faɗi a wajen ciwon ciki ranar batai kwanan duniya ba sai akace wai ciwon hanta ne ya kasheta dama ta daɗe da shi a jikinta. Still wata mata ta taɓa fahimtar an cutar da yarinyarta a asibitin tazo na rantse miki tana barin asibitin basu isa gida ba mota ta take napep ɗin da suke ciki sai gawarwakinsu aka dawo da shi asibitin.”

Ba ƙaramin tashi hankalina yayi ba. Amma cikin dauriya nace mata, “In sha ALLAHU Murjanatu mun miki alƙawarin baki dukkan tsaro da kariyar UBANGIJI. Shiyyasa ma muka ɗauke iyayenki kafin ma mu kawoki nan ɗin”.

“Shike nan aunty zan faɗa muku komai. Kamar yanda na faɗa muku sunana Murjanatu Usman. Teachen practice ne ya kaini asibitin kasancewar a bayyane duniya ta shaidashi da taimako wa talaka. Koda yake dama hakan shine burina. Dan a dalilin aikin ido da aka taɓama mahaifina ƙyauta a asibitin naji ƙarfin gwiwar yin karatu a fannin lafiya. Tare da alƙawarin neman aiki anan idan na gama domin hidima ga ɣan uwana talakawa nima. Hakan kuwa akayi, ana bamu zaɓin inda zamuyi practical ɗin na cike sunan asibitin. Na kumayi sa'ar aka turani can. A farkon farawa ban fuskanci kowace irin matsala ba, sai da na kusa cika watannin da suka kai gab da ƙarasa abinda ya kawoni, wani al'amarin daya gigitani ya faru. Mu huɗu ne baƙin masu koyon sanin makamar aiki, Dr Lawisa tai zaman meeting damu a satin kusan ƙarshe da zamu gama. Ta mana alƙawura masu yawa tare da ɗaukar mu aiki na dindindin da wasu abubuwa na ƙyautata rayuwa idan mun kammala karatun mu. Ƙarshen zancen shine tana son yin aiki tare da mu saboda ƙwazonmu. Harga ALLAH da farko bamu fahimci manufar aikin nata ba. Dan haka muka miƙa wuya. Rashin wayo kuma da jin ɓoyayyen aikin taimako ne da bata son kowa ya sani yasa data bamu takardar yarjejeniya akan da mun kammala karatu nan zmauyi bamuyi wani musu ba muka saka hannu itama ta saka tare da wasu mutane biyu da bamu san matsayinsu a wajenta ba. Tun daga nan muka fara aiki tare da ita. Sai dai a zahiri muna ma asibiti aiki ne kuma. Bayan kammala karatun mu muka dawo aiki gaba ɗaya, a kuma lokacinne aikin data buƙaci muyi taren muka fara shi. Tsagwaron tashin hankali muka shiga mu duka a ranar farko da muka fahimci minene aikin data kira na taimakon. Dan ba komai bane face cire ƙodar bayin ALLAH da basuji ba basu gani ba. Musamman ma talakawa da ke cikin matsanancin yanayin ciwon da ke buƙatar taimako. Sai ta katantance tace zata taimake su ta ɗakko wata cuta mai alaƙa da cikin ciki tace kana da shi sai an maka aiki. Idan aka saka kuɗin aikin ta yanke kaso biyu tace ka biya ɗaya asibiti zata biya sauran, sai ai amfani da wannan damar a cire maka ƙoda batare da ka sani ba. Nuna borenmu akan wannan al'amari yasa taima Safina allurar poison ta mutu. Ta kuma ɓatar da Pemi har yanzu babu wanda yasan inda yake. Kowa ɗauka yake ya mutu a gobarar

data cinye gidansu. Ni da Sajida mun matuƙar razana, ta yanda har muka gagara iya nuna sake borenmu. A tsahon shekaru biyu kenan dana kasance a asibitin wlhy Ni kaina bazan iya faɗar adadin da matar nan ta cirema ƙoda ba. Tun daga kan yara ƙanana, manya, mata da ma tsoffi. Aikin kanso ya tashi wani lokacin asiri yay kamar zai tonu, sai dai tasan duk hanyar da zata bi ta daƙile komai ta cigaba da bizne mummunan aikinta. Badan muna so ba muke mata biyayya, dan wlhy yanzu haka Babana itace ta maida shi haka, hakama Yayan Safina ta maida shi gurgu. Dukkan motsin rayuwarmu tana biye da shi. Kusan mu goma ne ma'aikatan asibitin dake ƙarƙashin wannan mulki nata wanda dai na sani a bayyane, sai dai gaskiya sauran duk da amincewarsu sukeyi. Ni da Sajida ne kawai bama so. Rashin ƙarfi da hanya da tsoro ya hanamu fiddo zancen. Ba wannan bane kawai, hatta da mutun idan ya mutu akan yi saurin cire wasu sassan jikinsa sai dai wlhy ban san mi take yi da su ba. Hatta da ƙodar ban san wanda ake bamawa ba idan an cire. Sai dai akwai wata mata dake yawan zuwa wajenta Madam Jannifer, tana kawo yara itama ana cirar ƙodar tasu, a ɗan bincikena na gano itama tana safarar yarane daga arewaci da sunan aikatau. Sai dai idan ta kawosu sai ta saka wasu a karuwanci, wasu kuma ta rabama manyan mata yan lesbians. Wasu kuma a fita da su ƙasashen ƙetare. Ita ɗin matar wani babban soja ne daya rasu shekaru kusan goma sha bakwai. Tana da yara biyu amma duk basa Nigeria. Bayan mutuwar mijin nata ne tayi ridda daga musulimci ta koma kirista. Asalin sunanta Munnira ne, daga ita har mijin yan jihar Zamfara ne. A yanzu haka ma naga tana hannun hukuma an kamata da zargin kidnapping mijin ita Dr Lawisa. Sai dai abinda na fahimta tabbas da sanin Lawisa komai ya faru, dan shekaranjiya naji tana waya da ita sai dai ba komai na fahimta ba a zancensu. Sannan ana shigo da mugayen ƙwayoyi ana ajiyarsu cikin store ɗin asibitin nan da sunan kayan asibiti ne, ana kuma saida abubuwan asibitin masu muhimmanci suma. Wannan shine abinda na sani kawai Wlhy”.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page seventy-nine

.....Mu dukanmu salati kawai mukeyi da mamakin hatsabibanci irin na wannan mata. Sai kace ba mace da aka sani da taushin zuciya da tausayi ba. Lallai al'amarin na matar nan babbane. Tsahon lokaci babu wanda ya iya cewa komai hatta shi mai gayya da aikin. Sai da Jaga ya ce, “Humm ai dama na faɗa maka babban yaya. Akwai abinda take yi a asibitin nan shiyyasa ta bashi muhimmanci sosai. Dan matar nan ANGULU ce wlhy bata jewar banza. Shi kansa Commondo ɗin amfani kawai take yi da shi. Ai ko yanda kuɗaɗe ke shigar mata duk da tana ɓoyewa tuni ya kamata a zarge ta da hakan”

Cikin jinjina kai Hayatu ya ce, “Tabbas maganarka haka take Jaga. Dan ko shi kansa Baba yanzu na fara tunanin anya matar nan ba itace ke amfani da shi ba”.

“Zata yiyu bazata yiwu ba oga Hayatu. Saboda magana ta gaskiya shima tsohon nan hatsabibin kansa ne. Ko maganar saka yara a containers ɗin babban yaya na kwanaki wlhy ina da tabbacin yana da hannu a ciki. Dan ni na faɗa muku wannan Mr Paul fa abokin huɗarsa ne sosai. Sune ma suketa son jansa ya shiga siyasa yana ƙi, bakuga yanda aketa jan shari'ar ba ma. Yanzu dai gasu can na barsu a halin ruɗani da ƙaulanin kasa banbance ni fatalwar ne ko kuwa ina raye. Duk da dai nasan zuciyarsu tafi karkata ne a ni fatalwa ne. Amma a taron sunan nan na gobe zan tabbatar musu ni mutum ne. Ruɗanin da zasu shiga shi zai sa su fara neman hanyar tabbatar da gaskiya, babban Yaya kuma sai yay amfani da wannan damar. Ni wlhy so nake ma Babban yaya yasa a saki Commondo nifa nafi son na kashesa da hannun....”

Ya kasa ƙarasawa saboda kallon da Maash ya masa. Murmushi na ɗan yi da girgiza kai. Hakama Hayatu sai da ya murmusa kaɗan. Sai TJ ne ya furta, “In sha ALLAHU bazaka sake aikata wani mummunan aiki ba Muntari. Na baya ma ALLAH ya yafe maka tunda Alhamdullah bama ka taɓa yin kisan ba dai”.

“Hakane kuma Yaya Tijjani”.

Jaga ɗin ya faɗa fuska a marairaice kamar zai yi kuka.. Ni sai ma abin nasa ya bani dariya.....

□□□□□

Gaba ɗaya lissafin Baba prof ya gama rincaɓewa. Dan tunda Isma'il daya kawosa ya rakashi har Bathroom ya fita sai ma ya gagara yin wankan. Ga warin gudawar da

yay a jikinsa na matuƙar damunsa. Amma ruɗanin ganin Jaga ya mantar da shi komai. Tabbas da farko zuciyarsa ta bashi Jaga fatalwa yay musu. Sai dai yanzu daya haɗa lissafi ya fahimci maganar Hajiya ƙarama gaskiyace kenan. Commondo na son cimma wata manufa shiyyasa bai kashe Jaga ba. Shiyyasa a yanzu ma da yake a hannun hukuma bai damuba, saboda yanada wanda zai masa aiki a waje. To amma Jaga sunan Awwab ya ambata ai. Ya ilahil alami. Shin ko dai Commondo shima ya koma ɓangaren Awwab ɗin ne? Tabbas idan hakanne zama fa bai gansa ba. Dole ne a gobe ayita ta ƙare kawai. Zaiyi amfani da taron da Nafisa ta sanar masa za'ayi a Mansion. Ƙasaitacen murmushi ya saki a hankali tare da sauke nannauyan ajiyar zuciya. Sai yanzu ne yaji yɤar nutsuwa na dawo masa. A gurguje yay wankan duk da jikinsa babu wani ƙarfi. Yau babu zancen shan barasa. Ɗakin sirrinsa ya shiga ya dinga haɗa duk wasu abubuwansa masu muhimmanci waje guda. Haka ya raba dare, sai da ya gama tsaff sannan ya bincika jirgin da zai iya tashi koma na wane ƙasa ne a gobe idan ALLAH ya kaimu ƙarfe huɗu. Yako samu mai zuwa Saudiyya, a take ya sayi ticket ta online ɗin. Bindigarsa daya jima bai yi amfani da ita ba ya ɗauka yayma zubin bullet taf sannan yay zaman yin dogon rubutu a takarda daban-daban kowanne da sunan yɤayɤansa. Suma ya kammala gab da asuba ya haɗasu ya ajiye. Sai lokacin ya samu giyarsa ya kwankaɗa son ransa sannan ya haye gado yay male-male.....

□□□□□

A lokacin da Baba prof ke wancan shiri anan Maash Mansion ma Hajiya ƙarama tunda ta samu ta sheƙama kanta ruwa akan batun Jaga sai ta fara samun yɤar nutsuwa. Ita dai tunaninta na nan akan Jaga fatalwa yay musu. Dan haka ta tabbatar ma kanta yin abinda ya dace kafin komai ya buɗe. Dan ta fahimci a yanzu Madam Jannifer da Commondo komai zai iya fita daga bakinsu. Hakama Baba prof a shirye yake da yin komai a kansu. Idan ko haka ne to batun ta kwanta a barci baima taso ba. Ita dama ta kammala dukkan shirinta game da kaf dukiyarta da harƙallolinta ta shirya ta yanda kota bar ƙasar zata cigaba da gudanar da komai a maɓoyarta. Hatta da sace Samraah ta gama da wannan matsalar, dan bazata taɓa barma Awwab ba, babu ruwanta da batun wani yɤar Abdul-wahab jirgin mota ce har yanzu tana sonta da kwaɗayin kasancewa da ita, ko cikin jikinta bai dameta ba zata zubar da shi da zarar sun bar ƙasar. Arwa kuwa da abarta zata tafi. Itama dai ticket ta siya ta online amma na ƙasar Dubai, daga can zata wuce ƙasar data gama tsarama kanta rayuwa da wani bazai taɓa tunanin tana a can ba saboda ƙasar ba wani wajen yawan zuwan mutane bane. Gaba ɗaya yaranta da ta gama shiryawa domin wannan yaƙi ta kira. Sai Marcel da shine uban tafiya. Abinda kawia ya banbanta shirinta da Baba prof ita sai nan da kwana biyu take shirin wucewa. Amma dai a gobe take son ai mata kidnapping duk wani wanda ke cikin list ɗinta. Saƙonta daga wajen Dr Khunal kuwa a daren yau zai iso Nigeria kamar yanda ya

tabbatar mata. Dan tun ɗazu da sukai waya yace mata bazai ƙara minti goma da shi ba a hannu amma ya sake ninka mata kuɗin kuma a haka ta biya. Jirgin da ya taho da saƙon kuma da ayanzu haka yana a bisa hanya na tashi yay mata text da _Done_. Wannan ne ma ya bata ƙwarin gwiwar tunkarar Baba prof a ɗazun....

□□□□□

A nan ɓangaren Fahad da Hafizzullah kuwa su shirin shagalin sunan gobe in sha ALLAHU sukeyi hankalinsu kwance. Dan su kawai a rakwashe a ƙwalle a girgije shine nasu shirin. Ga mutanen Kano su Abba da wasu a cikin yɞan gwarzo na a hanyar zuwa a goben domin ganin Falaq da kuma halartar bikin suna duk da taso ace itace ta fara ziyartarsu amma sun dai ce sune zasu zo domin neman afuwar mama Balki. Dan hakama suka kwaɓeta gaya mata, hatta da Samraah ma bata san da zuwan nasu ba. Amma Maash da Hayatu duk sun sani, a jirgi ma zasu zo.

Abin da farko kamar wasa sai gashi dai gagarumin taron suna na niyyar haɗuwa. Dan daga abincin mutane ɗari da sukai niyyar yi sai Ummie tace a ninkashi ya zama na mutane dubu ɗaya za'a bada wani sadaka. Duk da ma bata san da zuwan baƙi daga Kano ba kasancewar har yanzu bata san alaƙar Hafizzullah da Samraah ba. Ba kuma tasan Samraah ɗiyar Jirgin Mota bace. Su Hayatu sun tsara sai a gobe zata sani in sha ALLAHU wajen taro. Koda Hajiya Mammah ta zagi Samraah da sunan ɗiyar driver a jiya kawai ta ɗauka hakanne amma hawai ta ɗauki abun da muhimmanci ba. Dan ko ɗiyar mai bara Awwab da Fahad suka kawo mata matsayin matansu zata goya musu baya kuma taso matan musamman idan sun kasance mutanen kirki masu tarbiyya.

Bayanin likitanta akan ba komai zai dawo mata kanta lokaci ɗaya ba kamar da, ba kuma komai zata zurfafa nazari ko maida hankali akansa ba yasa yanda take ɗaukar Hafizzullah ɗan Mama Balki yasa suka barta a hakan kawai. Dama kuma bata tambayi kowa ba akan hakan ma.....

□□□□□

Zazzaɓin dana fara ji yasa muka baro guesthouse ɗin nasa muka nufi gida. Muna shigowa gidan muka tadda wani bala'in kuma. Dan tun a compound muka samu ma'aikatan gidan cirko-cirko maza. Daga ciki kuma ihu da kurkurwa ke tashi kamar muryar Hajiya Mammah. Har Maash yaja hannuna alamar muje ciki na girgiza masa kai. Murya a marairaice nace muje muga muke faruwa. Yaso tirjewa na sake shagwaɓe masa kamar zanyi kuka. Mun girgiza matuƙa da abinda muka samu yana

faruwa. Wai baƙuwa Hajiya Mammah tayi tun safe sai kuma ga ƙawarta Hajiya Rubayya da daren nan. Babu wanda yasan miya haɗasu aka jiyo hayaniyarsu. Tun sunayi a ɗaki har takai an fito waje tare da hankaɗo baƙuwar Hajiya Mammah waje tsirara. Ita ma Hajiya Mammah ɗin daga ita sai zanin gado data cikuykuye jikinta a ciki. Yayinda Hajiya Rubayya ke riƙe da wuƙa tana rantsuwar sai ta kashe Hajiya Mammah tunda taci amanarta.

Cikin tashin hankali Maman Malika ke tambayar cin amana kamar ya. Babu ko ɓatan harshe Hajiya Rubayya ta saki baki tana kwarara bayanin aure sukai ita da Hajiya Mammah shekara biyar kenan. Amma sai gashi yau ta kamata da yaɗar ƙanwarta da take riko a gado ɗaya. Babu wanda bai razana da wannan batu ba. Falon yay tsitt zuciyar kowa na bugawa da ƙarfi. Baka jin komai sai hayaniya da banbamin Hajiya Rubayya dana Hajiya Mammah da ke faɗin itama wlhy sai ta kashe Rubayya. Kafin kace mi sun farama juna fallasa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty

.....Hajiya Rubayya ta shiga faɗin, “Amma dai kin san ke ƙaramar yʼar iska ce Nafisa. Sannan a tafin hannuna kike wlhy. Ko kin ɗauka nima zaki iya yimin irin asirin da kikayi ma Mu'azz da babanku na mallaka domin gidan nan da komai ya dawo hannunki ki dinga juya kowa na cikinsa. Kullum cikin bankawa Maash asiri kike dan ya auri yʼarki ku mallake dukiyarsa sai wanda kika so yaci. Da kikaga kinƙi samun damarsa akan auren kin buga kin buga ya gagaresa sai kikaje kikayo masa asirin da yayma yʼar mutane fyaɗe. Kika kuma shirya tozarta shi wa duniya sai da kikaga kin gagara samun hanya kika dakata. Dai-dai da ubanki asiri kike masa ko na miki ƙarya?”.

Wani shegen zabura Hajiya Mammah tayi kan Hajiya Rubayya cikin kukan kura da wuƙa tsirara. Fashewa duk mukayi dan tsabar tsorata. Dan kowa ya gama sadaƙarwa za'ai kisan kai. Abunka da taron mata.

Wani ihun da Hajiya Mammah ta sake saki da faɗin, “Ka sakeni Awwab ka sakan. Wlhy sai na kashe wannan matar yau”. Yasa duk muka fahimci shine ya riƙeta. Duk abinda taken kuwa bai sake ta ba. Yana tsaye cak itako tanata fisge-fisgen son ƙwace hannunta. Sam ba ita yake kallo ba. Sai da mukabi abinda ya kafe da ido muka fahimci Paah ne tsaye a wajen ashe. Tsabar mamakinsa da firgici sai kawai mukaji Hajiya Mammah ta ƙwalla gigitacciyar ƙara, koda muka dawo da kallonmu kansu hannunta daya riƙe mukaga ta riƙe da ɗayan hannunta tana ihu ga hannun na jale-jale alamar ƙaryata yayi. Ko kallon inda wani yake kuma baiyi ba ya keta ta tsakkiyarmu ya gitta Paah ya wuce a binsa. Sai da yaje fita a kausashe ya furta, “Hayat! Securitys su kwashe min matar nan da dukkan muƙarrabanta” yay ficewarsa.

Razana matuƙa muka gani a fuskar Hajiya Rubayya. Ta zabura cikin masifa tana faɗin bataga ubanda zai kamata ba kawai securitys ɗin gidan suka shigo. Abinda ya ɗaure kan kowa da bada mamaki babu wanda ya musu bayani suka nuna Kubrah, Falilah, Afrah sai yarinyar da ake rikicin a kanta da Hajiya Rubayyar. Dai dai nan Hajiya ƙarama ke fitowa da alamun bata cikin nutsuwarta ko wadda ke cikin wani yanayi. Dan duk tayi wani firingai-firingai kamar wadda bata samu isasshen barci.

Ƙoƙarin magana Hajiya Rubayya tai mata amma sai ta wani ɗauke kai. Wata muguwar ashariya Hajiya Rubayya ɗin ta lailayo, sai dai kafin ta dire securitys ɗin sunyi waje da ita. Baki ta taɓe kawai ta juya ta koma. Babu wanda hankalinsa ke kanta sai ni. Dan haka na sakama yanayin nata ayar tambaya. Cikin sauke numfashi na maida kallona ga Hajiya Mammah da aka rasa wanda zai ƙarasa gareta, sai ihu take abin tausayi. Sai naji kawai na sake girmama rashin mutuncin Ya Awwab ɗin, amma dai maybe yana da dalilin karyatan. Karo na farko Azizat da yar uwarta suka bani tausayi, dan sun haɗe kai can gefe suna faman kuka. Hakama Hajiya Mama hawaye take yi, da alama abinda yar uwar tata ke aikatawa ya ɗimautata kamar yanda ya ɗimauta kowa. Ummie da Paah da Mama Balki dake can gefe na kalla suma. Sai naga Ummie ta juya ta koma abinta, shima Paah ya take mata baya. Mama Balki kam babu wani alamun razani a fuskarta da alama tasan abinda Hajiya Mammah ɗin ke aikatawa tuni.

Jiki a sanyaye na kalla Hayatu. Na ce, “Yaya Hayat ko za'a kaita asibiti ne dai. Kaga hannun har ya fara kumbura”.

Ɗan jimm yay kamar mai tunani, sai kuma ya jinjina kai da faɗin, “Boss ya iya ɗori, ko dai kije ki lallaɓashi ko zai ɗorata, dan yanzu dare yayi ɗaya saura fa”.

Cikin mamaki na ce, “Yaya Awwab wai kake nufi?”.

Kai tsaye ya jinjina min kai alamar eh. Ajiyar zuciya na ɗan sauke da kallon Fahad da Hafizzullah dake latsa waya hankalinsu kwance suma. Sai bance komai ba na fita kawai ina addu'ar ALLAH ya sa a dace ɗin yazo yay ɗorin tunda dama shine ya karya...

Sosai nasha mamakin samunsa zaune a falon ƙasa hannayensa duk biyu dafe da kansa. Gefensa na dama Paah ne zaune, haggu Ummie. Suma dai sunyi jugum-jugum. Juyawa nai da nufin komawa Ummie ta kirani. Dole na ƙarasa garesu kaina a ƙasa na durƙusa a gabanta. Hannuna ta kamo cikin mata, dole na ɗago na ɗan kalleta. Da ido tai min muni da shi. Sai na waro idanuna cikin marairaicewa. Kanta ta girgiza min tana sake lumshe idanunta alamar kar naji komai naje. Babu yanda na iya dole na rarrafa gaban nasa, kamar mai jin tsoro na ɗora duka hannayena biyu a saman nashi da ya dafe kai da su. Shiru babu alamar zai motsa ko nuna yasan da zamana. Sai naji na sake jin shakkar tasa. A marairaice na juya na kalla Ummie. Sake jinjina min kai tai cikin ƙarfafa gwiwa. Sai kuma ta miƙe, shima Paah miƙewar yay suka bar falon.

Na ɗan ji sauƙi kaɗan dan ina jin kunyarsu. Dan haka na daure da rawar murya na ce, “Yaya Awwab!”.

Shiru. Na saka faɗin, “My Lion!”. Nan ma shiru, ban gajiya ba na ce, “My hot please mana. Kayi haƙuri dan ALLAH kaje ka duba mata hannun kafa karyata. Bai kamata ba ko yaya ita ɗin uwa ce. Bai kuma zama lallai gaskiya bane abinda matar can ta faɗa, kama sani ko sharri aka ƙulla mata. Bai kamata mu yanke mata hukunci batare da wani bincike ba.....”

“Samrh leave me alone and get out of here!!”.

Har tsakkiyar raina naji tsawar nan. Amma na dake na sake buɗe baki zanyi magana ya sake daka min tsawar.

“I say leave!!”.

Takaici yasa na saki masa kuka, miye nawa daga roƙon alfarma irin wannan tsawa haka kamar wata dabba. Abunka da mai ciki zuciya a kusa. Tsabar taurin kan mutumin nan har naci kukana na tsire bai kulanin ba. Bamma san lokacin dana tashi a fusace nabar wajen ba ina jin kamar zuciyata zata fashe. To irin wannan wulaƙanci har ina dan ALLAH. Idan ya gadama kar yaje ya ɗorata ai yayar babansa ce sunfi kusa. Haba bana son taurin kai wlhy. Ɗakina nai shigewata na kulle kaina ban kuma sake bi takansa ba. Wanka nayi nai kwanciyata sai zazzaɓin nawa na fama yay mun rijif kuwa. Da ga haka na koma takaina nima.....

*_WASHE GARI_*

Washe gari safiyar suna. Daga tashi sallar asuba da nayita da ƙyar na sauka ƙasa. Can ɗakin da Aunty Falaq take naje na kwanta dan zazzaɓi ne sosai a jikina. Tambayar duniya tamun na ganina anan da asubar nan nace mata ba komai anan kawai nake son kwanciya. ganin yanda nake rawar sanyi dole ta bar ni. Sai ma blanket data ƙara min. Kamar kuma yanda yake ga al'adar bahaushe an raɗama baby suna a masallacin nan Mansion Muhammad Awwab. Sama-sama naji su Fahad sun leƙo suna faɗama Aunty Falaq ɗin. Kasancewar basu shigo ba yasa basu san ina ciki ba. Sau biyu ina tashi yin amai kafin barci mai nauyi ya ɗaukeni. Na roƙeta kuma kada ta gayama kowa karma ta faɗama kowa ina a ɗakin.

Shaƙiyancin da take min yasa na fahimci ita tana fassara yo yajin nawa zuwa nan da wani abune daban. Sai kawai na barta a hakan ne wai ina gudun Ya Awwab. Harda cemin itama farkon cikin nan haka ta dinga yi, sai da ya shiga wata uku sannan. Ni dai ban kulata ba....

★ A sauran ɓangarori kam kowa ya tashi da shirinsa a yau ɗin. Baba prof, Hajiya ƙarama, Maash da muƙarrabansa. Sai su Fahad masu shagalin suna. Hajiya Mammah dai yau babu kanta. Dan Maash dai bai ɗorata ba a daren nan aka kaita asibiti, sai sune sukai mata ɗorin. Tsabar fitina kuma tace a sallameta zataje gida tai jiyya. Basu ƙi hakan ba suka sallamota. Wajen ƙarfe goma drivern ta da Maman Malika datai mata rakkiya suka dawo. Zuwa lokacin gida ya fara ɗaukar harama dan masu tsara decorretion a cikin garden har sun fara aikinsu.

Dai-dai lokacin da su Hajiya Mammah ke dawowa Hajiya ƙarama ce daga can ta ɗakin da gen ɗin gidan yake da wani matashin saurayi dake aiki a gidan Baba prof matsayin mai shara da goge-goge. Wani ɗan akwati mai ƙyau ta buɗe tare da nuna masa cikin akwatin. Ƙaramar kwalbace ɗauke da ruwan allura sai syringe a gefenta. Fuskarta ƙawace da murmushi ta ce, “Kaga wannan allurar ita zakaje ka masa yanzu da gaggawa kafin giyar ta sake sa. Ka tabbatar a kan jijiya ka masa ita. Kada kai min wasa da abun nan. Idan ba haka ba, kaima kasan mizan iya yi Labaran”.

“Babu abinda zai faru maa, dan har video ma zan miki ko kuma na kiraki ta WhatsApp video call dan ki tabbatar”.

“Hakan ma idan kayi babu laifi, zan fiyin farin ciki ma.” tai maganar tana bashi akwatin. Da hannu biyu ya amsa ya saka aljihu, sai kuma ya gyara hiramin kansa da ƙyau ya fice. Sai da ya fita da fin mintina goma sanan itama ta fice ranta fesss. Tana komawa ɗaki Marcel ta kira akan karfa suyi wasa. Dan ƙarfe huɗu za'a fara taron. Ya kamata ace zuwa ƙarfe biyu sun gama da batun DJ ɗin da aka ɗakko su su maye gurbinsa yaransa su iso da kayan kiɗan. Ya tabbatar mata komai sun gama

tsarawa. Nan ma ta yanke wayar tana Murmushi. Cike da nishaɗi ta shirya ta fita saloon. Dan yau so take ta fito a hajiyarta.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-one

.....A ɓangaren Baba prof kam sai kusan sha ɗaya ya tashi saboda giyar da yasha. Zuwa lokacin yaron Hajiya ƙarama har ya zabga masa allura yama bar gidan dan ya gama nashi aikin kuma. Sai dai da yake ba take zata fara aiki ba, bai ji komai a jikinsa ba lokacin. Wanka yayi yay sallar asuba data suɓuce masa. Bayan ya idar break fast ya fara zaman yi sannan ya koma bedroom ɗin sa yay zaman yin waya da yaransa akan su kasance duk cikin shiri. Dan shi anayin azhar zai wuce Mansion. Suma sun tabbatar masa da komai done. Lokaci kawai suke jira. Amintaccen guard ɗinsa ya kira ya dinga kwasar kayyakin da yay packeging a daren jiya yana kaiwa mota. Sai da ya gama lodesu tsaf sannan ya faɗa masa inda zai kai masa su. Guard ɗin na wucewa yay kiran ma'aikatan gidan. Albashi ya babasu tare da sanar musu zaiyi tafiya, amma sai nan da gobe ko jibi. Su cigaba da kula da gida kamar yanda suka saba. Sun amsa masa da gurmamawa tare da addu'oin dawowa lafiya sannan ya sallamesu. Isma'il nakomawa kitchen ya turama Maash da Uncle Abdullahi

dukkan bayanin. Shima ya fara shirya inasa-inasa dan yau ne aikinsa zai ƙare a gidan. Zai ma riga Baba prof fita...

★★★

Har ƙarƙashin zuciyarsa kewarta yake ji. Amma girman kai bazai barsa zuwa ya nemeta ba. Sosai yaji zafin damunsa da tayi jiya akan Hajiya Mammah. Har ma tana faɗa masa wai sharri akai mata bayan ga komai a bayyane gaban kowa akayi. Shi ya tsani aitama abu kwana-kwana bayan kuma ansan gaskiya ce a bayyane. Gefe kuma dama zuciyar ɣan mazan a tunkushe take. Dan ya gama samun dukkan bayanai ta kowanne ɓangare game da shirin Baba prof da Hajiya ƙarama tun a daren jiya. Hasalima bayan barowarsa karya Hajiya Mammah yana shiga sashensa aka kira wayarsa. Dukkan shirin Baba prof aka sanar masa. Dan haka hankalinsa ya tashi ya kai zaune cikin kujera shine ita kuma Samraah tazo ta damesa da wani batun Hajiya Mammah can. Yau kuma da safe aka bashi dukkan bayanan Hajiya ƙarama itama. Hatta da allurar data bayar akama Baba prof ya sani. Shi kuma a yanda yake jin zafin Baba prof ɗin baiga dalilin da zai sa ya hana ai masa allurar ba. Ai Hajiya ƙaramar ce dai-dai da shi. Suci kansu su sha baƙin ruwa. Makashin maza ai dama maza ne ke kasheshi.

A ɓangarensa shima ya gama dukkan shiri da team ɗin sa da kuma su Uncle Abdullahi matsayin jami'in tsaro. Bai so wannan taron suna zai kasance a haka ba. Amma babu yanda zai yi dole sai an kai ga hakan dan ya gaji shi kansa. Yafi buƙatar komai ya fito ya kwashi iyalansa subar ƙasar nan suje su hutama ransu ko matarsa tayi rainon cikin nan cikin salama. Ummie ta huta daga gwagwarmayar da ga sha...

Jin bazai iya daurewa ba kasancewar yasan a irin wannan lokacin tana a halin ciwo yasa ya nufi ɗakin nata, sai dai ya samu wayam babu ita. Amma dukkan alamu sun nuna anan ɗin ta kwana. Ransa ne ya ƙara ɓaci da tunanin ina ta tafi kuma. Dan har Bathroom ɗin ta ya duba amma babu ita. Ƙasa ya sakko ɗakin su Ummie nan ma babu ita, sai ma Paah ne kawai ke barci Ummie na bathroom alamar wanka take dan yaji motsin ruwa. Har zai nufi kitchen sai kuma ya fasa. Wayar Falaq yay kira a dake yace ta turo masa Samraah ɗin. Itako sai taji tsoro tace masa ai tana barci ne tun ɗazun. Ɓoyayyen numfashi ya sauke da yanke wayar kawai dan dama wayo yay mata dan ya tabbatar Samraah na wajentan. Daga haka ya sake haurawa saman a ransa yana raya sai ya hukuntata tunda har ta tafi inda bai aikata ba ta kwanta bayan ga ɗakinta ga nashi. Bata san dama yaji haushi rufe masa ƙofa da tai jiya ba. Sam baya son raini, dan shi abinda kawai ya ɗauki rufe ƙofan raini ne. Bai ƙara bi takanta ba yama shirya ya fita a gidan shi da Hayatu.....

□□□□

Kamar yanda zazzaɓin ya saba sakina gabanin azhar yau ma hakanne. Da ƙyar na tashi zuwa upstairs ɗin nai wanka nayi salla. Kasancewar Aunty Falaq ta faɗa min duk abinda ya faru har kiran da yay mata a waya yana nemana yasa bayan na shirya na nufi ɗakinsa. Kimtsashi na shiga yi duk da babu wani datti dan nawa dai an gyara, wannan aikin Mama Balki ne kullum takan zo da masu aiki su gyara ko'ina na sashen tana tsaye ɗakinsa ne kawai nake gyarawa ni dan babu mai shiga. Koda na kammala sai na ƙara ɗan jin ƙarfin jikin nawa. Komawa nai ɗakina na sake gyara jikina, dan sunan kamar wasa yanata tara mutane. Dangin Mama Balki sun zo suna sashensu, hakama na Baban su Hayatu da na mamansa. Saboda ma haka Aunty Falaq ta koma can babu wanda aka bari ya shigo nan sashen Ya Awwab ɗin. Ni kaina kwalliyar tawa sai naga ta burgeni, dan haka na tsaya ina kallon kaina a mirror harda yin hoto. Key na sakama ɗakinsa da nawa sannan na sakko dawn stairs. Na ɗan ji shock ɗin samunsa zaune a falon ƙasan shi da Ummie da Likitanta da Paah. Amma sai murmushin da Ummie tai min da miƙo min hannu alamar naje gareta ya sani sauke ajiyar zuciya. Yanda yay mun kallo ɗaya ya ɗauke kansa nima kallo ɗayan na masa na basar. Paah na fara gaidawa da girmamawa sannan Ummie dake riƙe da hannuna tana yaba kwalliyata. Batare dana kallesa ba shima nace masa ina yini sannan na gaida doctor ɗin shima. A haka Fahad ya shigo ya samemu likitan na cigaba da mana bayanin illar da aka so yima Ummie da alluran da aka dinga mata na birkita mata brain. Ya bata shawarar ƙoƙarin fidda abinda duk ke ranta koda ta hanyar faɗama wani ne, hakan zai sa nauyin da zuciyarta tayi ya ragu har ita brain ɗin ta samu rangwame. Haka dai ya dinga bayani dalla-dalla na matakan da za'a cigaba da bi domin tabbatuwar ingancin lafiyar Ummie ɗin. Tamkar an jeho Mama Balki sai gata ta shigo tana kuka. Mu duka duk miƙewa mukayi a razane. Ummie ta shiga tambayarta abinda ke faruwa. Da ƙyar cikin shaƙewar muryar kuka ta ce, “An ɗauke takwaran Alhaji ƙarami, an tare kuma ɣan Kano da akaje ɗakkowa airport kafin su ƙaras....”

Kiran wayar Maash da akayi ne ya katseta. Uncle Abdullahi ya gani ɓaro-ɓaro. Ɗagawa yay, kasancewar akwai bluetooth a kunnensa saurarensa kawai yake. Daga can a rikice Uncle Abdullahi yake magana. “Awwab tabbas akwai matsala. Dan sun canja wasan da ga yanda ka sani. Sai dai ban san daga cikinsu ta ɓangaren wa aka samu canjin ba”.

Komai Maash ƙin cewa yay sai yanke wayar da yayi kawai, ya wani fincike bluetooth ɗin kunensa yayi wurgi da shi. Gaba ɗaya kamaninsa sun canja jijiyoyin kansa sun mimmiƙe. Dai-dai nan Hayatu shima ya shigo a birkice yana tambayar Mama ina Falaq. Sake rikicewa mukai dan ita kanta Mama ma sai yanzu hankalinta ya kai. Cikin wani sabon tashin hankalin ta ce, “Ba kuna tare ba? Tun kiran da kai mata ai ta fito mafari kenan ma ta ajiye yaron.”

“Innalillahi wa'inna ilaihiraji'un. Wlhy ban kira Falaq ba ni. Tun yaushe kenan akai kiran?”.

“Yau na shigesu ni Bilkisu. Wayarta fa na hannuna mun gama magana da Hafizzullah kiranka ya shigo na miƙa mata na tashi, bai fi minti ɗaya ba ta sameni da yaro a hannu tace kana kiranta shine ta bani shi ni kuma na miƙama Zaituna. Kwata-kwata bai fi mintuna talatin ba yanzu”.

“Hafizzullah! To shi yana ina?”. Na faɗa cikin kiɗima nima, dan sai yanzu hankalina ya kai kansa. Kuka na fashe musu da faɗin, “Na shiga uku, aunty Falaq, Hafizzullah, da Baby kenan duk aka tattare. Dama sun faɗa, ashe sakacin da suka ambata sunyi naƙin bibiyar zuri'ar baban mu suna wani sabon shirin. Shin minene mahaifinmu ya aikata haka mai zafi garesu shi da Abie? Mi suka aikata musu Umm.....” na kasa ƙarasawa saboda wani irin kuka daya taho min ga jiri na neman kwasata...

Rawa jikin Ummie ya farayi itama. Da kyar ta iya ɗaura hannunta akan kafaɗar Samraah dake wani irin kuka mai cin zuciya. Lips ɗin ta na kakkarwa ta ce, “Samraah mahaifin ku?”.

“Yes Ummie, sun faɗa sunyi sakaci da basu bibiyi suri'ar jirgin mota ba kamar yanda suka bibiyi ta Abie.”

“Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un. Kina nufin kema jinin Abdul-wahab ce?”.

Ɗagowa nai na kalleta, cikin kuka nace, “Ummie da ni da Hafizzullah da Yaya Musaddiq da Ya Awwab yakai ƙasar China karatu duk shi ya haifemu. Mu yan uwan aunty Falaq ne na jini”.

Sake rikicewa Ummie tai ta juya ta kalla Mama Balki. “Dama bake ce kika haifi Hafizzullah ba?”.

Kai ta jinjina mata alamar tabbatarwa. Tana hawaye ta ce, “Ɗayar matar Abdul-wahab ce ta haifesu, muma bamu san haka ba sai da Alhaji ƙarami ya auro Samraah.....” nan fa ta shiga bata labarin dalilin haɗuwata da Ya Awwab har zuwa aurenmu. Ai gani mukai kawai Ummie ta tafi zata zube ƙasa. Da sauri duk mukai kanta ALLAH dai ya bama Paah sa'a ya rungumeta a jikinsa. Wani irin kuka ta fashe da shi mai ban tausayi da cin rai. Sai kuma ta ture Paah ta miƙe. Wayar Ya Awwab ta ɗauka. Babu wanda yasan mi take yi ta shiga danne-danne sai kuma ta kai a kunne. Ɗan jimm tai har wayar ta shiga aka ɗaga, bata yi ko da sallama ba a kausashe ta ce, “Kai tsinannen matsiyaci maci amana butulu. Da ni kake TAKUN SAƘAR ka saboda nice jinin Ibrahim. Idan har kai ɗin ɗan halak ne kazo muyi gaba-da-gaba a yau ba kai kidnapping wanda basu da alaƙa da kai ba. Dan haka in har ka cika kai Adamu namiji ne ba mata maza ba. Ɗan halak ne ba ɗan shege ba kazo ka sameni”.

Kitt ta yanke kiran tana mai wurgar da wayar. Kamar an saita kuwa Maash ya cafeta cikin hannunsa. Wayar shima ya kai kunensa yana wani makirin murmushi dake nuna tsantsar ɓacin ransa da fusata. Cikin tashi kakkausar muryar shima ya furta, “Nasan kaji mi tace. Dan haka ni Muhammad Awwab El-Mu'azz zan maimaita maka yanzu. In dai kai ɗin ba matsoraci bane. Shashasha lusari mai ɓuya a bayan mace. Kuma cikakken namiji ne ba mata mazan ba kazo ka sametan a cikin Mansion. Idan ba haka ba ni zan biyoka har inda kake, idan kuma hakan ta faru wlhy, wlhy sai kayi dana sanin kasancewata a cikin ZURI'ARKA tsohon banza!!”.

Babu wanda jikinsa baya rawa yanzu kam a falon. Dan kaf ɗinmu ba yara bane. Mun kuma fahimci waye wannan da ake wayar da shi. Ko kallon inda wani yake Maash baiyi ba ya fice a binsa. Hayatu da Fahad suka take masa baya. Sai nima kawai na bisu dan bazan iya kallon yanda jikin Paah ke wani irin karkarwa ba.....✍

Tofa, yau fa ake yinta

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-two

*_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar

idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauki da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....😉. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□_*.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauki ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....Ganin sun tunkari motoci nima sai kawai na bisu. Yau kam da kansa ya buɗe mazaunin driver ya shiga. Dan haka na buɗe side ɗin gefensa nima zan shiga kawai mukaga an wangale gate. Abin mamaki motocin Baba prof ɗinne ke shigowa. Duk tsayawa mukai har suka kammala shigowar aka maida gate aka rufe. Kawai sai yan iska masu zubin shaiɗanu na dirgowa a motocin riƙe da mugayen bindigu tamkar sojoji sun tafi yaƙi. Harga ALLAH na tsorata, na kuma sake tabbatar da mutumin nan baƙin shaiɗani ne. Sai da yan barandar tasa suka gama zagayemu tsaf sannan shi ya fito. Sanye yake cikin manyan kaya harda hula kamar wani tsohon kirki. Ya

kawo baƙin gilashi ya toshe idanunsa. Wani shegen tsaiwar yɗan iska yayi kafin ɗaya daga cikin yaran su kawo masa kujera tsakiyar compound ɗin alamar zama. Hannu ta ɗaga musu yana masa nuni damu ya wuce ainahin ƙofar babban sashen cike da takun ƙasaita.

Dai-dai nan aka fara fito da mutane daga kowanne sashe na gidan ana maidasu sashen masu aiki mazansu da matansu. Ashe tuni ma yaransa sun gama zagayemu da sunan masu decorretion batare da an farga ba. Sai dai ashe nice mai tunanin ba'a fargan ba. Shi gogan yana sane da duk motsin su tunda suka fara aikin. Sai dai ya barsu a ƙarƙashin nasa shirin shima. Ganin ya nufi ƙofar falon shima a fusace muka take masa baya ni da Hayatu da Fahad. Zaune muka sameshi yay zaman ƙasaita, yayinda yɗan iskansa suka zagaye Maash. Muma muna shiga suka zagayemun. Su Azizat dake falon duk sun rikice suna kallon kakan nasu a firguce.

Fito da duk wanda ke sashen yasa ayi. Kusan su Ummie sune ƙarshen fiddowa. Sai Hajiya ƙarama da tai sumar tsaye. Dan ta fahimci shirin wannan makirin tsohon ya danne nata kenan. Sai dai koba komai ta ribantu itama ai, sannan tanada tata nasarar. Ƙananun kukan da su Arwa keyi a wajen yasa yɗan iskan daka tsawa tare da yin harbi. Sake rikicewa falon yayi sai da ƙyar suka lafa. Ta gefen ido na kalla Maash da aka fi zagayewa da bindugun amma babu ko ɗar a tattare da shi. Sai ma tsaiwar ƙasaita ta yay bayansa jingine da bangon falon ya harɗe ƙafafunsa waje guda hannayensa duka biyu cikin aljihun wandonsa. Gefensa Fahad ne shima dai an zagayesan kamar yanda akaima yayansa. Sai Hayatu da ni ma da akaima ƙawanya tun a farkon shigiwarmu. Daga can ma Ummie sun zagayeta haka ma Hajiya ƙarama. Hajiya Mammah da itace ƙarshen fiddowa kasancewar tana ɗaki kwance tana jiyyar hannunta suna isowa wajen ihu ta fasa da faɗin, “Mun shiga uku Baba!”.

Gilashin idanunsa ya cire yana mai binta da kallo. Bakin baya iya shiru cikin rawar laɓɓa ta sake faɗin, “Baba wai mike faruwa ne haka? Wane kalar bala'i ne wannan kuma ni Nafisatu Adams yɗan fashi da ranar ALLAH. Ni wIhy duk na ma rikice ko kidnapping ɗinmu akayi....”

“Ko kuma yay kidnapping kansa ba”. Muryar Ummie ta ratsa kunnen kowa a wajen a bazata. Duk kallonta akayi dan dariyarta take hankali kwance idonta akan Baba prof.. da mamaki Hajiya Mammah ta ce, “Ummu-Hidaya! Ban gane ba. Baba ne fa taya zai yi kidnapping kansa kuma? Kina ganin mutane sun zagayemu da bindigu kamar babu hukuma a ƙasar”.

Haɗe fuska Ummie tayi da watsa ma Hajiya Mammah ɗin wani kallo. “Kamar yanda kika gani mana Nafisa. Ai uban naku lusari ne ba jarumi bane. Sannan mata maza ne ba namijin gaske bane. Dan namijin gaske a filin daga baya riƙe garkuwa. Amma shi harda yɗan baranda ya zo. Adamu kenan, a tunaninka zuwa da waɗan nan wawayen dake hura hanci da bindigu a hannu zaisa ka amsa sunan NAMIJI a gabana? Ai kazo kai kaɗanka ne zan maka kallon ɗan rakkiyar mazan ma. Ka manta na faɗa maka, na faɗa maka in dai ni jinin Ibrahim ce da izinin UBANGIJI sai ka ƙare

rayuwarka a ƙarƙashin ƙafafuna kamar yanda tun farko kake a ƙarƙashin ƙafafun mahaifina. Ai na faɗa maka dama bazaka taɓa tsira ba, kuma kafin ka mutu mutuwar wulaƙanci sai ka biya bashin CIN AMANAR da kayi ma mahaifina.....”

“Ƙarya kike ƙaramar yar iska ni ba MACI AMANA bane. UBANKI shine ya fara CIN AMANATA. dan haka shine MACI AMANA, BUTULU, MARA ADALCI, mai son kansa kawai. Shekaru ashirin da shida na ɗauka ina masa bauta da durƙusawa ƙarƙashinsa, alhalin dukiyar da yake taƙama da fankama da ita dani aka tarata. NI!! NI!! nan Adams. Yazo ƙasarmu a matsayin matsiyacinsa faƙirin da baida banbanci da mabaratan kan titi kafiri mai bautar gunki. Mune muka tallafesa ya zama mutum, muka buɗe masa idanunsa ya fahimci a inda yake, musamman ma NI! NI ɗin nan. Uwata ta zama sanadin shigarsa musulinci. Babu irin wahalar daban masa ba, duk da shekarun daya bani ba wasu masu tazara bane haka nake kiransa YAYANA ko YALLAƁAI, idan ya buƙaci aikena jikina har rawa yake domin son ganin na cika masa fiye da yanda ya buƙata. Ko kallon banza wani ya masa zafi nakeji a cikin zuciyata har na ɗauki mataki. Nasha yin faɗa da abokan aikina idan suna gulmarsa. Idan yana ciwo nine tsaye a kansa har ya samu lafiya. Hatta da wankin kayansa da gyaran ɗakin barcinsa kullum nine keyi batare da jin komai ba a raina. Kafin ya furta yunwa na sayo abinci na ajiye masa, haka nake girmamashi a duk wani motsinsa tamkar yayana uwa ɗaya uba ɗaya. A duk lokacin da naga wani abun cigaba da zai ɗaga darajar Company bana baƙin cikin kawo masa shi. Kuma haka za'a gwada a samu nasara. Amma duk da wannan hidimta masan dana ƙare ƙuruciyata inayi a matsayi ɗaya yake kallona har a randa zai bar duniya. Wato YARONSA. Yaronsa da darajarsa kawai yayi aiki a biyashi sai idan wani ya taso a sake nemansa yayi ya biyashi da yan kuɗaɗe.

Butulci na farko da tabbatar min shiɗin BAƘON HAURE ne mai rama ALKAIRI da SHARRI shine haɗa baki da budurwata ya turani karatu ƙasarsa bayan tafiyata sukayi aure saboda shi ɗin TSINANNE NE kafirin banza. Na danne zuciyata na ƙyalesa saboda dalilai biyu. Na farko ina masa kallon Yaya ne da zan iya sadaukar da komai a garesa kamar yanda nake tunanin shima zai iya sadaukar min. Na biyu yaci darajar mahaifiyata daya riƙe hannu biyu take masa kallon ɗa jininta. Sai dai nayima kaina alƙawarin komai tsahon lokaci sai na hukunta Rabi'ah da kaina da shi kansa. Dan a lokacin ita nafi kallo a mai laifi, idan shi bai san ina sonta ba ai ita tasan ina sonta. Idan kuma shi bai san ana barin halak dan kunya ba ita ai ta sani. Amma abin duniya ya rinjayeta. Koda yake banyi mamaki ba kasancewar ta yar KARUWA mai TUWO-TUWO kuma KARUWAR.

Wasu irin hawaye ne masu zafi suka silaloma Ummie. Yayinda jikin Maash ya fara rawa na tsantsar fusata. Yana motsawa yan iskan nan suka sake attacking ɗin sa da bindugun. Amma duk da yasan zafa su iya harbin nasa ya mutu har lahira tuni ya watsar da su ta hanyar hankaɗe bindugun ya nufi mahaifiyarsa. Dan a duniya bai haɗa al'amarinta da kowa ba. Da sauri suka ɗana kunamin bindugun su da wanda ke zagaye da ita amma sai Baba prof ɗin ya ɗaga musu hannu yana murmushi. Kamo Ummie Maash yay jikinsa, maganar da babu wanda ke ji yake mata ƙasa-ƙasa

cike da kulawa da tattali. Dariya Baba prof ya kwashe da ita kamar ba tsoho mai shekarun girma irinsa ba. Jinai zuciyata na ƙuna. Bamma san lokacin da nima na furta, “Wawa jahili”. ba

Ai gaba ɗaya waɗanda ke zagaye da ni, da wanda ke zagaye da Maash ɗin sukayo kaina...

“Duk wanda ya taɓa min MATA a cikinku wlhy! Why UWARSA ma sai tayi dana sanin HAIHUWARSA!!!”.

Razananniyar muryar Maash ta ratsa kunnen kowa dake a wajen sai da muka firgita. Dan hatta da kamaninsa sai da suka sauya. Cikin nuna Baba prof da yatsa ya furta, “Kai kuma kafi JAHILAI JAHILCI tunda har kake iya maida FARI ya koma BAƘI. WULAƘANTACCE kawai da bai san girma da kimar HALLACI ba, mai faɗa da ƙaddara ɗan son banza. Kai har kana da bakin zaman yima mutane wannan surutan banzar naka soki burutsu. Duk abinda kake lissafin ka masan ai badan ALLAH kayi masa ba, kayine daman dan ka shiga jikinsa ka cimma wata manufarka baƙin annamimi. Idan kace duk ya maka wannan, inganta rayuwarka data yayanka da yayi fa. Bai kuma ji ƙyashin ɗaukar yarsa ɗaya tilo ya aurama ɗanka da ke a gurɓace ba. Sannan ya kama UWARKA ya riƙe da hannu biyu fiye da yanda ma kai kake riƙon nata. Sai ka gaya min UBAN mi kake so ya maka bayan duk wannan?”.

“Ni kake zagi Awwab?”.

“An zagekan, zan maka ma mafiyin wannan ɗin ne. Dan ni wlhy tuni na daina maka kallon MAHAIFIN UBANA. Na tsaneka”

“Kamar yanda nima ban taɓa maka kallon ƊAN ƊANA ba tun ranar haihuwarka naji bana sonka”.

“Alhamdullahi hakan yamun daɗi ai, dan ka taimaki kanka wajen gane abinda yafi ƙarfinka har abadan yafi ƙarfin naka. Kai ko kunya bakaji ba a duk wannan surutan naka ka faɗi ta inada Abie ya cutar da kai...”

“Oh so kake kasan ta inda ya cutar dani mara kunya. To zakaji yanzun nan kuwa. Dan zan ko gaya maka idan ita uwarka ta gagara sanar maka. Ko aure da kake faɗin ya ɗauka uwarka ya bama Mu'azz ni na sakashi yin hakan ta ƙarfin tsiya ba hallacinsa bane ba.....”✍

Hummmmmmmmmm

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-three

_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍____.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....Dukkan ƙuruciyata a wajen hidimtawa rayuwarsa na ƙarar da ita, amma da yake shi kansa kawai ya sani haka ya tattare dukkan dukiyar da aka tara da gumina a ciki ya rubuce sunan yarsa akai da naka, kai ɗin nan ɗan mitsitsinka dama baka san kanka ba balle waninka. Niko ya haɗani da wani tsohon companyn da ya gama mutuwa ya manna min yan kuɗaɗe wai ya sallaman naje na gyara. Tun daga lokacin na fara tunanin ta yanda zan mallake dukkan abinda ya handame ɗin nima tunda naga kowa kansa ya sani kawai. Haka na shiga na fita na kwaɗaita masa haɗa aure tsakanin Mu'azz da uwarka. Tsabar mutumin nan shi butulune nunawa ma yay kamar bai da wannan ra'ayin. Baya son wannan haɗin saboda Mu'azz baya jin magana. Rashin jinsa yayi yawa. Bazai iya riƙe masa Ummu-Hidaya ba miye-miye. Kai ko ga yar gwal an haifi a Nigeria. Komai bance masa ba a randa ya kawo min wannan zantukan banzar nashi. Na koma kawai gefe na shiga na fita shege a dawowa ta biyu baima san sanda ya amince ba jikinsa na rawa. Suma duk da akwai shaƙuwa a tsakaninsu na sake ƙulle zukatansu a waje guda suka nuna suna son junansu. A zatona wannan haɗin auren zai sa ya dunƙule dukiyar ya bama Mu'azz matsayinsa na mijin yar tasa tilo da yake taƙama. Kokuma ya tattara duka aikin ya bama Mu'azz ɗin. Ya cigaba da jagorantar companyn. Amma shegen mutumin nan sai ya ɗauki yarsa ya ɗorata akan komai. Tana wata ƙasar tare da ɗana da aka maida hoto amma tana juya kan dukiyar duk da ƙananun shekarunta.

Wannan abu ya ƙara ƙona min zuciya matuƙa. Wato ni na ɓata ƙuruciyata a banza wajen hidimta masa ɗana ma zai koma ɗan amshin shata mijin Hajiya. Haba never. Tuni na je na kunno musu wutar da Mu'azz ya fara cin ubanta. Dan a lokacin data samu cikin farko ya jajibemu domin dubata da shirina naje. Na banka masa maganin da Malamina ya bani bamu baro ƙasar ba sai da ya zubar mata da cikin da ake ɗogafi da shi. Da matuƙar farin ciki na dawo a lokacin har kashi biyu kuwa. Na zubar da cikin da Mu'azz yay mata da ƙararshi data kawo min wai bata son ubanta ya sani ai masa faɗa akan neman matan da yake da dukanta da yake yi. A zahiri na

amsa mata da to kawai, amma ko uhun bance masa ba. Yo neman mata sai na hanashi ya more ƙuruciyarsa ya ƙare kanta iya kaɗai kenan ma, ko kuwa tana matarsa bazai jibgi shegiya ba yanda yake so a kuma sanda yake so. A dawowar tamu ma dukkanin baya nai ina samu akan zaman nasu. Ubanta yake ci gwargwadon iko shine ma dalilin da yasa tana kammala karatun ta saka suka dawo Nigeria da zama. Duk da dai tana dojewa wai ta dawo ne tai aiki a kamfanin babanta. Ƙaryar banza kenan. Koda ta dawo ɗin nasan Mu'azz na aikata duk abinda yake acan bai fasa ba. Ban kuma tsawatar masa ba. Babban abinda ya fara saka min tsanar shegiyar yarinyar nan bayan wadda nake ma ubanta ta shafeta shine ɓoye zancen cikinka da tayi tare da wannan munafukar annamimiyar da mijinta. (Ya nuna Mama Balki) Ban tashi sanin tana da ciki ba sai da ya shiga watan haihuwa, shiyyasa ashe ubanta ya tura Mu'azz wata ƙasa aikin watanni har shida. Ni kaɗai nasan a halin dana tsinta kaina a wannan lokacin, dan haka na nutsu domin nemo mafita akan yanda ko ta haihu za'a maida abinda ta haifa lahira dan ubansa. Ƙawarta da naga tana yawan zirga-zirga a gidan ce tazo min rai. Dan haka na nemeta amma sai taƙi bani haɗin kai a lokacin da yake Lawisa shegiyar makira ce. Tata yawo da hankalina duk da barazanar da nake mata da kurari, sai da ta latsani da ƙyau har bayan an haifeka sannan ta yarda mukai magana. Wannan shine mafarin alaƙata da Lawisa duk da bata da wani ƙarfi sai idan dalili ya taso. Jawota jikina yasa na fahimci itama shegiyar tana kwana da tashi da baƙin cikin Ummu-Hidaya ɗin. Amma tana dannewa kullum tana jikinta. Kamar dai yanda nake ma ubanta wahala, itama tanata yima yar wahala. Duk da mun haɗe kai da Lawisa tako ina mun gagara samun nasara akan kauda kai a duniya. Dan koyaushe idon baƙar matar nan da mijinta na kanka. Ya nuna Mama Balki cikin tsana.

Tako ina sun rufe komai sun katantane. Daga baya ma sai na fahimci shi Abdul-wahab kamar ya sakama motsina ido. Dan bawai ga Ummu-Hidaya ba hatta da uban gidan nasa wanni kaffa-kaffa yake da shi idan har ina waje. Rana ta farko dana zuba ma Ibrahim wasu ƙwayoyin da Lawisa ta samo mana ta kuma tabbatar min da in har Ibrahim ya shasu bugun zuciyarsa zai ƙara ƙarfi da ga ƙarshe ta buga ace heart attack ne ya kashesa bayan na gama wahalar zuba maganin a cikin shayinsa kawai matsiyacin yazo da wani salo ya ɓarar da shi as mistake. Ya kuma katantane shi da kansa ya haɗo masa wani ya bashi a gabana. Wannan abu yamun ciwo na fara ninka tsanar da nake masa a raina tare da saka masa alamar tambaya. A karo na biyu ma dana haɗa wutar lantarki a office ɗinsa kawai bamma san ta yanda akai ba kawai shi yaje ya kama wayar ya hana Ibrahim kamawa. Satinsa guda a asibiti yana jiyya a maimakon Ibrahim. Wannan ma ta wuce bance da shi komai ba na sake kafa wani tarkon a cikin gidansa da fetur nan ma Abdul-wahab ya wargaza min. Haka ya dinga bina kafa da kafa yana wargaza min ayyukana akan Ibrahim. Daga ƙarshe na fito ƙuru-ƙuru na masa gargaɗi da barazana. Amma da yake shi taurin kai ya masa yawa sai ma ya maida abun rainin hankali, har yana wani sanar min cikin gadara wai in ma ina wani tunani a kansa ne na canja dan TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE shi ɗin ba kanwar lasa bane. Idan kuma zan shekara dubu ina ƙulla makircin kashe Ibrahim zai kasance a bashi kariya da izinin

UBANGIJI. Kar kuma na ɗauka zai faɗa masa ne ya ɗauki matakin hukuma shi da kansa zai cigaba da bashi tsaro da tsarewar ALLAH batare da ya taɓa sanar da shi wanene ni ba har sai idan shine ya gano da kansa. Alwashi na ɗauka masa kan nima mu zuba ɗin, ni da shi ɗan halak ka fasa. Muka ko zuba ɗin ba tare da sanin Ibrahim ba. Tabbas Abdul-wahab ya nema zamenim bala'i a rayuwata. Dan haka na shirya shirin ƙarshe da shi a ciki dan ya cancanci irin hukuncin Ibrahim shima.

“Innalillahi wa'inna ilaihiraji'un, Baba yanzu har wannan ya kai ka kashe Abie da ya inganta rayuwarmu. Shine fa sanadin barowarmu ƙauye”. Hajiya Mammah ce ke maganar cikin matsanancin kuka. Hakama Hajiya Mama da Paah kansu kawai suka duƙar suna hawaye.

Cikin kaushin murya da zafin rai Baba prof ya daka mata tsawa da faɗin, “Oh dan yayi sanadin barowarku ƙauye bada wahalar ubanku bace Nafisatu. Ko a banza yasa na kawo kun badan ya cigaba da amfanuwa da ƙuruciyar mahaifinku bane. Kar wanda ya sake katseni ki bari nakai ƙarshen zancena mana kafin kiyi alƙalanci!!!”. Ya ƙare maganar a tsawace yana wani irin huci kamar bajimin sa. Kafin ya cigaba da magana a zafafen nasa.

“Sai da na gama shirya komai sannan na tunkari Ibrahim da sigar neman alfarmar aron kuɗi da zan inganta bussines ɗina. Amma shi da yake butulu ne, kansa kawai ya sani sai shegiyar yɔar nan tasa da kai dake matsayin jikan da ni nama fisa matsayi da ƙarfi a wajenka domin ubanka na haifa. Haka ya nuna min baida waɗan nan kuɗin. Sannan ko yana da su ma bazai bani ba dan sunyi yawa. Naje na cigaba da juya na hannuna wai fara kasuwanci da kaɗan yafi albarka. Kuji min shegen makiri, shi bada manyan ya fara ba. Na zafafu ranar da ƙyar nai controlling kaina. Ban sake masa magana ba sai bayan wasu kwanaki na sake zuwa masa dai da wannan buƙatar amma na rabin abinda na nema a farko nan ma ya nuna min sam shifa bazai bani ba tunda ya sallameni. Idan ma dukiyar da nake kallo a hannunsa ce shima ba tashi bace mallakin yɔarsa ce da jikokinmu. Kam babbar bala'i kenan. Wai abinda aka tara da gumina ake min gadara da shi hahaha yaro bai san wuta ba kenan sai ya taka. Daga haka ban sake masa batun ba sai bayan kusan wata ɗaya naje masa da tayin sayen Shere a companyn nawa dan nayi amfani da kuɗin na tada companyn da ke neman durƙushewa. Abin mamaki wai azzalumin nan a wannan ɓangaren babu musu ya amince. Ya sayama yɔarsa kaso ɗaya bisa uku na Shere ɗin company na. Ya kuma biya akai duk abinda ya dace ya amshi takardu a gabana ya damƙa mata. Daga wannan ranar nai alƙawarin sai na ɗanɗanama Ummu-Hidaya azaba da wutar dalma a tafin hannunta. Matakin farko kuma shine kashe ubanta. Anyi haka da yɔan kwanaki kawai a bazata akace min wai tana naƙuda. Imagen matar ɗana nada ciki ban sani ba a karo na biyu. Hakan na nufin akwai abinda take shiryawa kenan itama ko ubanta ya kitsa mata a kaina, domin idan babu rami miya kawo rami? Ta ɓoye na farko na biyu ma haka.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-four

Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😉□□.

.....Banyi magana ba dai sai shi Mu'azz ɗin na samu na ci masa ƙaniya sai da ya koma yana rantsuwar shima wai bai san da cikin ba sai da ya kai watanni kusan huɗu. Ta kuma roƙesa kada kowa ya sani idan kuma ba hakaba zata gudu tabar gida har sai ta haihu ta dawo saboda ta fahimci baya son haihuwa shine ya zubar mata da cikin farko. Na Awwab ma shiyyasa ta saka mahaifinta ya turashi wani aiki na watannin rainon cikin nata da tayi bayan ta tabbatar mai idan wani abu ya samu cikinta sai ta kaisa kotu. Sosai raina yamun zafi da lusarancin Mu'azz. Dan a zahiri baya jin magana, sannan yana da zafin rai idan aka ƙuresa amma bashi da yawan hayaniya da kwaramniya tamkar ba mune muka haifesa ba. Kaf halayensa na mahaifiyata ne ya kwaso shi. Barshi dai da fitinar neman matansa kawai. Takaicinsa ya sakani korashi dan mun gama shirya kawai tafiya matakin ƙarshen ni da Lawisa. Sai dai dole sai mun sami point. Munata neman point bamu samu ba har sai da tafiyarsa jihar Katsina ta taso. Amma zaiyi landing a Kaduna ya ƙarasa Katsina ta mota. Hahaha wannan abu yay min daɗi matuƙa. Hakama Lawisa. Babu ɓata lokaci ta samar mana wanda zai mana aiki a kaduna. Abinda ya ƙara sakamu a farin ciki da tafiyar ta kasance da shegen makirin driver ɗinsa mai cika bakin zai iya ƙare rayuwarsa yana bashi kariya. Anyita ta ƙare, raina yayi sanyi FANSA ta tabbata akan Ibrahim da Drivern sa Abdul-wahab, sai dai wai Ibrahim bai mutu ba. Hakan bai wani ɗaga min hankali ba, dan nasan zan iya ƙarashi da hannuna abu mai sauƙi. Amma kuma zan iya bashi damar rayuwa koda a kwancen ne ta yanda yana kallo ina juya abinda ya cutar dani a kansa amma babu yanda zai yi dan ubansa.....

“Wlhy kai jahili ne. Wato ɗauka ma kake rayuwarsu da mutuwarsu duk a hannunka take?”. Fahad ya faɗa a matuƙar zafafe yana kuka. Cikin tsawa Prof... Ɗin ya watsa masa harara da faɗin, “Nace a daina katseni sai naje ƙarshe. Kai yaushe ma aka haifi uwarka balle kai zaka katseni. Idan kai baka san rayuwarsa a hannun nawa take ba ita uwarku ta sani dan taga kaɗan daga abinda zan iya bayan tamun

irin wannan gadarar. Haka shima uban nata. Ni ɗin dai daya wulaƙantar ni ne na shiga na fita aka kawosa Lagos ɗin yana a tsakanin rayuwa da mutuwa. Inda naso da tun a can zan kashesa amma ba haka nake buƙata ba alokacin. Ni na tsaya tsayin daka akai treatment ɗinsa har ya fara samun sauƙi. Kaga ko ai rayuwar tasa a hannuna take mara kunya (Wa'iyazubillah😭). Naje masa da jarabawar ƙarshe, wadda da ace ya cita da har yanzu yana rayuwarsa dan ba itace a gabana ba ni. Yana a gadon asibitin naje masa da batun duk halin da yake a ciki nine na sanya shi, na kuma gaya masa kuskurensa, tare da tabbatar masa idan har ya mallaka min abinda nake so a lokacin tofa zai tsira, hakama yaɗarsa zata tsira. Hakama jikokinsa. Idan ba kuma ba haka ba, zan kashesa kamar yanda na kashe uwar matarsa da matarsa. Na kuma kashe yaɗarsa da jikokinsa abinda ya hana nin ya dawo nawa gaba ɗaya dan babu mai cin gadonsa sai ni. Hhhhhh!!! Kun san miya faru? Da yake mutumin nan ƙasurgumin shegen Bature ne kai tsaye yace min bazai bayar ba. Har ma yana iƙirarin idan ya bar asibitin nan sai ya wulaƙanta rayuwata. Dan sai ya kaini hannun hukuma na faɗa masa dalilin kashe masa mata da mahaifiyarta. Hahaha ni sai ma ya bani dariya, dan haka na haɗa masa da abinda naso barinsa a duhu saboda wasu dalilai, amma tunda zai iya ɗaukar fansar matarsa da uwarta nashi iyayen fa?. Dan haka na fito na faɗa masa ai suma ni ne na kashesu. Nayi hakanne kuma a dalilin hukuncin auren budurwata da yayi, cikin sauƙi na shirya matsalar data zama gobara har yau ake ɗauka daga sune. Tofa wai wanda ke a gadon asibiti a tafin hannuna ke nuna fusata har gado na jijjiga. Sai famar hura hanci yake shi a dole sai ya ɗau fansa. Kaji Bature ɗan balaja'u. Kazo ƙasata kace zaka nunan gadara. Barinsa nai ya gama bige-bigen nasa sannan na siburbuɗa masa allurar poison. Hhhhh karfa kuga laifina dan alokacin bata mutuwa bace. Ina da makarinta a hannuna, na kuma nuna masa idan har yay min abinda nake so zan masa ita mu rabu lafiya ya cigaba da rayuwarsa zaɓinsa ne. Na koma gida ina jiran feedback. Washe gari kuwa na samu kira daga wajensa. Ganin yaɗarsa da jikansa a wajensa har ma da lauyoyinsa yasa na fahimci gargaɗina ya amsu kenan. Dan haka na samu gefe naci dariyata son raina sannan na koma. Sai dai tun a farkon zaman meeting ɗin na fahimci baifa sallaman ba, lallai taurin kai baiyi ba, da ace mutumin nan yasan mizan iyayi da wlhy baiyi jayayya ba. Da bai zaman tattare komai da komansa a gabana ya mallakama yaɗarsa da jikokinsa ba. Da bai ajiye shaidu akan hakan ba har kuma ya gayyaceni zaman. Dan wannan shine mafi girman kuskure daya taɓa aikatawa a rayuwarsa da shima yasan ya tafi yabar BAYA DA ƘURA. Dan nayi alwashin sai na tabbatar masa da TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE koda yana kwance a cikin kabarinsa. Yanda bai saka ni cikin zancen ba an ajiyeni ne matsayin hoto ko dan yamun gadara ne oho mas nima sai banyi magana ba har akai zaman meeting ɗin aka tashi. Abu ɗaya nai masa shine lokacin da zan fita a ɗakin nai masa kallon (Kayi kuskure) nai ficewata. Dan banda sauran kuma dil da shi wasan ya koma tsakanina da yaɗarsa ne. Yes ni da yaɗarsa dan allurar poison ɗin da nai masa kawai ta wadatar ta ƙarasa min rayuwarsa. Hakan kuwa ce ta kasance, washe gari aka shafe babin rayuwarsa. Ya zama tarihi. Alonso Ibrahim ya shuɗe kamar bai zo ba.

Adalcina yasa na tsaya akan komai na jana'izar sa komai akayi yanda ya kamata. Ai koba komai baƙonka Annabin ka inji masu iya zance. Baƙunta yazo ƙasarmu, ya kuma tattara ya bar mana miya rage ai gaba ta ƙare kuma sai wadda aka barma JINI. Banyi ƙasa a gwiwa ba dan bana son na cigaba da jan al'amarin na samu Ummu-Hidaya da batun ta bama mijinta komai na dukiyarta ya cigaba da juya mata a matsayinta na uwa ta cigaba da tarbiyyar yaranta da kula da mijinta. Kun san buɗar bakinta mi tace dani kuwa? Hahahhhh!!! Kawai sai cewa tai wai (Baba karka damu, zan cigaba kamar yanda na fara wannan shine burin mahaifina). Banyi fushi ba na cigaba da nuna mata tayanda zata fahimta amma ina. Imagen like father like daughter. Kai harma tafi ubanta taurin kai da tsaurin ido. Koda yake ai jini biyu ta haɗa, Rabi'ah ma badaga nan ba a taurin kai. Iya son fahimtar da ita nayi cikin hikima amma ta tabbatar min da itafa tana akan bakanta, idan dai Mu'azz zai zo ya nema aiki ne a companys ɗinta yazo ƙofa a buɗe take, yayi kamar yanda kowa keyi a biyasa albashi, amma batun ta bashi ragamar komai ko ni ta bani sam bazatayi ba. Kai harma da fa su zagina ita ga BOSS LADY jinin Alonso da Rabi'ah masu kuɗi ko. To Rabi'ah ɗin ma dan ubanta saurana ubanta ya samu dan sai da na gama shanye romon a waje kafin shi ya aura abinka da karuwa yar mai tuwo-tuwo.....

A zafafe Ummie ta ture Maash ta miƙe tana nuna Baba prof da yatsa, a matuƙar kaushin harshe ta ce, “Karya kake baƙin azzalumi annamimi. Oh surutun da aka barka kanayi taaa!! taaaaaa!! Tun ɗazun yasa kake jin kamar bakinka ne kawai ya iya magana har kake da kalmar yima mahaifiyata sharri. Ka kira Abie ɗina da maci amana, butulu, azzalumi, baƙon haure, kafiri da mine. Yanzu kana son aibanta mahaifiyata da zina. Ƙarya kake yi Adamu. Dan uwarka da bakinta ta faɗi mutunci da martabar da mahaifiyata taje da shi ga mahaifina. Idan kana gani bata raye yanzu ALLAH shine shaida kana da damar ƙaryatata dan dama ba daraja da mutuncinta ka sani ba ai. Sannan kana maganar na zageka, ai sai ka fito ka sanar musu dalilin da yasa na zageka bunsuru ɗan akuya wanda bai san mutunci da kimar kansa ba”.

Ta share hawayenta da nuna shi.“Jama'a kunga wannan, in har bai tuba ba ya mutu, idan har wanda ya kashe basu dawo duniya ya nema gafararsu ba, idan har waɗan da ya zalunta ciki harda mahaifiyarsa da matarsa harma da yayansa basu dawo duniya ya nema anfuwarsu ba, to tabbas idan kuka gagara ganinsa a WUTA ranar sakamako maybe garwashi ne ya lulkuβesa acan ƙasan wutar jahannama.....✍

“Ya rabba😭. ALLAH ka rabamu da son zuciya. Wace irin rayuwace wannan ka ƙare rayuwarka a bibiyar ta wani. Mutane dan ALLAH mu canja, dan yanzu mafi yawanmu wannan itace rayuwarmu shiyyasa HASSADA take ƙara ƙarfi a zukatanmu wlhy.”

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

*_ALLAH ka gafartama iyayen

mu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-five

Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😉□□.

.....Bari na faɗa muku wani abu, duk da ya fito ya nunama mahaifina ainahinsa har yabar duniya bai nuna min wanene shi ba. Ko zaman meeting da mukai ana gobe zai bar duniya abinda kawai ya nuna min shine yana son ya tattara komai gareni, dan akwai wasu abubuwa daya ware na Muhammad da Fahad a cikin dukiyarsa. Sauran kuma nawane a matsayina na mai gadonsa. Ya ƙara da min nasiha game da kulawa da duk wanda zanyi mu'amala, ya tabbatar min dana tsaya akan gaskiyata, na kuma rungumi yaƴana na horar da su ta yanda sune zasu zama gatana kuma garkuwata koda anan gaba. Ya faɗakar da ni kada na cuci kowa, koda ma'aikaci na ɗauka mai hidimta min a cikin gida na sauke hakkinsa na kuma bashi darajarsa irin ta ɗan adam. Yace dani na cigaba da girmama wannan wawan, dan shi ɗin kamar ubane a wajena, yana kallonsa matsayin ƙani jininsa kodan riƙon da mahaifiyarsa ta masa da raino irin na uwa. Sannan mijina, duk rintsi kada na barsa, kada na masa ɗagawa, kada na ƙasƙantar da shi. Na ƙyautata masa, na masa biyayya matsayin sa na miji, shugaba, uban yaƴana, ta wani fanin tamkar yayana. Ya nuna min yasan halin Azz na neman mata, karna damu na cigaba da masa nasiha da addu'a watarana zai daina in sha ALLAHU. Daga ƙarshe ya bani amanar Bilkisu da Falaq tare da ɗora min nauyin nemo sauran iyalin Abdul-wahab na haɗasu na riƙe tare da ɗaukar nauyin rayuwarsu. Sannan ya danƙa min takardun Companynsa na robobi yace na bama iyalan Abdul-wahab ya mallaka musu duniya da lahira. Dan bazai taɓa iya biyan mahaifinsu abinda yay masa a rayuwa ba koda da dukkan abinda ya tara ne. Na amshi komai da hannu biyu, tare da masa addu'a da fatan samun lafiya.

Daga nan mukayi zaman meeting komai lauyoyinsa suka saka hannu muma muka saka ni da Muhammad. Fahad kam da pinger print ɗin sa akai amfani dan bashi da wayon yin abinda ya kamata. Takardun Company daya mallakama zuri'ar Abdul-wahab akwai saka hannun Abdul-wahab ɗin sai dan ban san lokacin da ya sakashi yayi ba. Shima dai lauyoyi suka saka hannu na ajiye akan sai na samo sauran iyalan nashi sannan na damƙa musu. Nayi mamakin rashin cewar Adamu komai a wajen, da kuma yanda Abie bai sakashi a maganar ba ko sau ɗaya. Dan har muka gama cike-ciken takardun nan kallonmu kawai yake yi. Wannan abu ga tsaya mun a rai har na ƙudiri aniyar tambayar Abie idan mun kasance mu kaɗai. Amma sai labarin ya canja washe gari na rasa Abie na. Mai yankewa ta raba a gaɓar da nafi buƙatarsa.....”

Kuka ya sarƙeta. Da yawan wanda suke a wajen suma hawaye suke najin tsananin tausayinta. A hankali na rarrafa inda take na rungumeta, sai shima Maash yazo ya haɗamu ya rungume mu duka. Ƙwacewa shima Fahad yay yazo ya rungume Yayansa. Haka mukai kuka sosai idan ka cire Maash da idanun ne kawai suka juye sai jijiyoyin kansa da suka tashi sosai. Hakan yasa na sake tabbatar da taurin kansa. Da ƙyar Ummie ta cigaba da faɗin....

“Na shiga ruɗani matuƙa na rashin Abie, amma haka nai tawakkali ina addu'a da fatan dangana wajen UBANGIJI. Badan zuciya ta saba ba, ba kuma dan gangar jiki da ruhi sun haƙura ba na fara dawowa dai-dai. Kwatsam sai ga azzalumin nan yazo min da fuskar yaudara akan na mallaka komai a hannun Azz yana kula da shi. A lokacin ban kawo komai a raina ba, sai dai ina akan nasihar mahaifina. Sannan bazan iya mallaka komaina ahannun Azz ba kodan halinsa akan mata. Za'a iya amfani da wannan damar a lalata komai dan nasan matan banza da dukiya basa taɓa rayuwa a muhalli guda. Dole wataran sai an rasa guda a ciki. Kodai dukiyar ta kakkaɓe a dalilin matan, ko matan su gudu a dalilin ƙarewar dukiyar. A zatona ya fahimceni zai bar ni, amma sai ya cigaba da kawo wasu hanyoyin cikin salon damuna. Kawai sai na fara shan jinin jikina, anya kuwa mutumin nan babu wani abu a ransa. Musamman idan na haɗa yanayinsa da zaman meeting ɗin da akayi na rashin cewarsa komai, da yanda ko wata mahaifina baiyi da rasuwa ba amma yake wannan kai-kawon na son na mallaka dukiya ga ɗansa duk da yasan hallayarsa. Kai akwai abinda ya kamata na sani. Na ɗauki ƙudirin wannan bincike kawai sai ma ya sauƙaƙa min ta hanyar fitomin da mummunar manufarsa. A wata ranar juma'a da na gama kammala shirin komawa office a litinin ɗin satin da zamu shiga ina falo zaune Muhammad na kusa da ni yana homework ina gyara masa, sai Hayat, Falaq, Fahad dake ta tsalle-tsallensu kawai sai gashi ya faɗo mana. Nayi mamakin hakan, babu neman izini babu sanarwar irin wannan shigowa haka. Duk da abin ya sosa raina sai na daurema zuciyata saboda Abie yace na masa biyayya tamkar ƙaninsa na jini, sannan koba komai shi ɗin mahaifin mijina ne. Hijjab dake ajiye a gefena kawai na ɗauka na saka ina masa sannu da zuwa. Bana jin ya amsa min yanda ya kamata, dan ko gaisuwar da su Muhammad sukai masa bai kulasu ba. Fahad ma da ya nufesa yana murna bai taɓa yaron ba ya waske. Nan ɗin ma dai bance komai ba,

sai Muhammad nama magana akan ya tattarasu suje wajen Mamansu Fateema (Maman Hayatu) dan lokacin Bilkisu bata da lafiya.

Yaran na gama fita na maida hankalina kansa. Cikin sauƙaƙa harshe na ce, “Baba lafiya dai kuwa? Yanzu nake zancen zuwa ni da yara gida mu muku barka da juma'a na sanar maka zan koma zuwa office in sha ALLAHU Monday”.

Wani mummunan kallo ya jefeni da shi, cikin ɓacin rai ya ce, “Ummu-Hidaya kina son nuna min kema mai taurin kai ce kenan?”.

Cikin nuna mamaki na ce, “Baba taurin kai kuma? Mizaisa na maka taurin kai. Kai fa uba ne a wajena. Ka cancanci sakani ko hanani akan abinda kaga zanyi ba daidai ba. Karka manta ko sanda Abie na raye yakan saka kamin faɗa ko gyara akan wani kuskure idan nayi balle yanzu da banda kowa sai ALLAH sai ku”.

“Ƙarya kike Ummu-Hidaya, in da abinda kika faɗa haka yake da baki bijirema umarni na ba. Da baki nunama duniya ni ban isa ba. Idan ma wani abu ne a ranki to bara na fito miki a mutum. Baki da ƙarfin hanani abinda nayi niyya. Na biyo miki ta hanyar lalama ne domin na baki damar rayuwa cikin salama ke da yaɣanki. Dan haka zan miki gargaɗi ba ƙarshe da zai iya taimakonki. Kada kice zaki bijirema umarnina. Idan kuma har kikai hakan kiyi kuka da kanki akan abinda zai iya biyo baya. Ban kuma amince da komawarki office ba ranar litinin ɗin, idan har kallon uban kike min da gaske”.

Sosai raina ya sosu da waɗan nan zantuka nashi. Bamma san fushi ya taso min ba na furta masa, “Baba ai baka da hurumin hanani zuwa aiki, inaga Azz ne kawai keda wannan damar matsayinsa na miji. Shima idan naga akwai tauye hakki a cikin al'amarinsa bai zama lallai na masa biyayya ba saboda tun farko ya ɗaukama mahaifina alƙawarin barina, nima kuma ya ɗauka min, idan har yasan hakkin alƙawari da muhimmancin sa kaga bazai bijire ba”.

Dariya ya ɗan yi da mun kallon sama da ƙasa, cike da gadara ya furta, “Ga fili ga mai doki”. Yay ficewarsa. Wannan al'amari ya gigitani ya kuma ƙwaɓe min lissafi. Gaba ɗaya komai naji ya ƙwace min. Hankalina yay matuƙar tashi. Mutuwar Abie ta dawo min sabo fil a zuciyata. Nayi kuka irin wanda bazai misaltu ba a wannan yini. Dole na keɓance kaina daga kowa domin yin nazari. Sai ya zamto gaba ɗaya weekend ɗin ya koma min na bincike da nazarin manufarsa. Duk da gargaɗin nashi a monday ɗin haka na tashi da shirin fita aiki. Amma mi sai Azz ya birkice min a wannan safiya kan bazan fita ko'ina ba. Na tambayesa dalili yace ban isa ya faɗa ba. Fita dai office ya soketa har abada. Ko dai na bashi komai ya cigaba da kulamin da shi, ko kuma na bama Baba. Murmushi nayi kawai na takaici, dan na fahimci ɗora shi akai akan keken ɓera. Sai kawai ban kulashi ba na cigaba da shirina. Na gama zan fita ya hanani fita ta hanyar kulle ƙofa. Da farko roƙonsa na farayi da son fahimtar da shi kuskuren da yake neman yi. Amma yaƙi saurarena sai ma sake hawa da yayi. Hakan ya baƙantan rai da zuciya nima na hau sama muka fara rikici. Kamar yanda ya saba duk da tunda muka dawo Nigeria hakan bai sake faruwa ba

ya ware ƙwanji ya hau dukana. Da ƙyar na shiga bathroom na rufe kaina ina kuka. Abinda yasa kowa bai sani ba saboda yaran duk sun fita makaranta. Bilkisu kam tana wajen mahaifiyarta saboda damuwar abinda ya faru na zuwanta can dangin Abdul-wahab suka ƙi saurarenta bata da lafiya ma. Abinda yasa a lokacin ban shiga maganar ba akwai shirin da nake yi ya kuma haɗa da nima ina a cikin damuwar ne. Ya cigaba da banbamin masifarsa akan na buɗe ƙofar na masa banza naci kukana sosai a toilet ɗin sannan na wanke ciwukan daya jimun. Haka ya gaji dan kansa ya fita ya bar gidan batare dana fito ba. Nima sai da naji fitar motarsa sannan na buɗe na fito. Bana son yarana su fahimci baƙar rayuwar da nake ciki tsakanina da mahaifinsu na tsawon shekaru, musamman ma Muhammad mai fushi da ƙin duk abinda zai taɓa ni. Dan haka na daure na gyara komai na gyara jikina nasha magani na fita zuwa office ɗin cikin ƙarfin hali kamar yanda nayi niyya tun farko.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-six

*_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya ƴan yayi cikin farashi mai sauƙi da

rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers □□□□□□□□_*.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku□□□._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba □□□.

.....Wannan shine mafarin komai. Fita ta office kuma ta sake fusata shi ya cigaba da kunnomin Mu'azz da abubuwa iri-iri ya zamto a tsakanin nan sam babu zaman lafiya ko tausayi a tsakanina da shi. Duka, zagi, gori, har akwai wani dare da yazo min da w.....

Kuka ya sarƙeta ta kasa ƙarasawa, sai da tayi sosai sannan ta cigaba da faɗin, “Da wata har ɗakin barci na, ya hanani fita a ɗakin sukai abinda suka so. Zan iya cewa ban kai wayewar gari da numfashi ba. Dan sume musu nayi tsabar tashin hankali, mijina da wata a ɗakina gadon mu na aure. Lokacin dana farfaɗo naga

Fatima (Maman Hayatu) da Lawisa a kaina. Tambaya ɗaya na musu ina yarana? Suka bani amsa da suna lafiya kawai na maida idona na rufe. Wannan kuma shine ya zama tushen fara fitar damuwata. Daga kuka sai tasa yarana gaba naita kallo dan na fahimci a wannan gaɓar sune kaɗai gatana. Sune kaɗai abinda ya rage min na kalla naji daɗi kamar yanda mahaifina ya sanar min. Sai kuma matsanancin tausayin rayuwarsu da nake ji, dan bana jin nima zanyi tsawon rai batare da nabi bayan mahaifina ba. Saboda ina jin yanda ƙirjina da zuciyata ke mun nauyi. Bani da wata madafa, na rasa wanda zan fiddoma ainahin damuwata. Duk da kuwa bazanyi butulci ba Mahaifiyar Bilkisu tsaye take a kaina. Itama kuma Maman su Azz a ɗan tsakanin ta jani jikinta sosai. Kasancewar nayi shiru da bakina ban taɓa cewa kowa komai ba akan abinda ke damuna yasa kowa ke fassara al'amarin nawa da kasa yin tawakkali da rashin mahaifina da nayi. Ni kuma ni nasan ainahin matsalata. Bilkisu ta dawo saboda kwanciya ciwo da nayi a tsakanin, sai yazam ita da Lawisa da Fatima ke kula da ni da yaran, jin na yarda da su a raina saboda yanda suke nuna damuwarsu a kaina yasa na damƙa musu amanar yarana batare da su sun san dalili ba ashe Lawisa munafukata ce. Jiyyar kusan sati ɗaya na fara ƙarfafa kaina kodan yayana, bazan so na tafi na barsu a ƙananun shekarunsu ba. Lokacin Azz yayi tafiya, sai dai ban san takamaiman inama ya tafi ba, kamar mahaifinsa ya barni sai gashi ya dawo a kwanakin dana fara murmurewa. Ni yanzu ganinsa baya bani wani mamaki ko ɗar dan na gama sakashi a layin da ya dace da shi. Ashe ma ya wuce hakan dan sai a ranar yake tabbatar min. Banko kalli inda yake ba na gaisheshi da tambayarsa ko yau kuma miya kawoshi?. Kai tsaye yace dani cika alkawarinsa. Banji komai a kalmarba na ce, “Humm”. Shima Humm ɗin yace min tare da cigaba da faɗin, “Kin mun taurin kai da tunanin babu abinda zan iya gareki saboda baki san wanene Adams ba. To bari na fiddo miki da saninsa. Ni ba kanwar lasa bane ba yarinya. Dan shi kansa mahaifin naki ya buga da ni na kaisa ƙasa balle ke ƙaramar ANT. Na biki ta lallami da hanyar sulhu ta yanda zaki rayu cikin aminci da yayanki amma kin tabbatar min baƙya buƙata. To abinda na saka Mu'azz yake miki yanzu ƙarami ne. Ni nawa kashe ki zanyi kamar yanda na kashe uban naki, na kuma kashe uwarku da uwar uwarki da iyayen ubanki. Je kabarin Abdul-wahab drivern ubanki ki tambayesa labarin yaya karon battarmu da shi. Alwashi ya ɗauka zai ƙare rayuwarsa a kare rayuwar ubanki shiyyasa na haɗa da shi na kashe a randa nai shirin kashe uban naki. Sai ko gashi shine ya rigashi tafiya batare da ya karesan da ya ɗaukar min alwashi ba. Dan haka zaɓi ya rage naki, tattaro dukkan dukiyar ki danƙa min yanzun nan a hannuna. Ko kuma na ƙwata ta ƙarfin tuwo bayan na kashe ki, na kashe waɗan nan yan kuyi-kuyin yaran naki.”

Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un. Harga ALLAH bazan iya ma fassara muku halin dana tsinta kaina a wannan lokacin ba. Dan kalaman wannan baƙin azzalumin ba ƙaramin dukan zuciyata sukayi ba. Duka mai girma da gigita brain da tarwatsa zuciya. Cikin rawar jiki na ce, “Kai ne ka kashe Mamana da mahaifiyarta? Sannan ka kashe mahaifina da iyayensa? Ka kuma kashe Abdul-wahab?”.

Dariya ya bushe da ita harda buga ƙafa. Sannan yay min kallon sama da ƙasa ya ce, “Saura ma ke cikason su tare da yaranki biyu idan kika cigaba da mun gadara da taurin kai akan abinda aka tara da gumina aka bar miki da sunan gado. Da kike ganina cikakken ɗan hau ne wlhy, sannan gagararre ne a ƙauyenmu ki bibiyi tarihi na, taƙadaranci yasa na baro gida, samun ubanki yasa naji a raina kakata ta yanke saƙa amma ya nuna min shi ɗin ma shege ne kansa kawai ya sani. Ko karatu dana daure nayi nayine saboda na fahimci baka amsa sunan wane sai da shi. In da yay ma kansa adalcin bani abinda yake hakkina tun farko da yanzu yana rayuwarsa, amma ya nuna min shi wani kwallon shege ne. Hhhh yanzu yana ina? To kema kinada zaɓin rayuwa ko bin bayansa. Na baki daga nan zuwa dare na ga saƙo”. Ya ƙare maganar yana wata shegiyar dariya da miƙe....

Wani irin abine ya tokare min kafar numfashi, sai dai nayi jarumtar fisgoshi cikin azaba da ƙunar zuciya. Dai-dai yana saka ƙafa zai fita na dakatar da shi da faɗin, “Kai matsiyaci maci amana azzalumi, fasiƙi. Naji kaci nasarar kashe zuri'ata bisa dalilai daban-daban. Sai dai na maka alƙawarin ni Ummu-Hidaya Ibrahim ko zaka dinga yankan naman jikina wlhy bazaka mallaki wannan dukiyar da kake kwaɗayi ba. Kuma koda nima ya kasance ƙaddarar mutuwata a hannunka take sai na zamewa rayuwarka bala'i ta inda bakai zato da tsammani ba. Ka kira kanka taƙadari ko, to ai kan naka kawai ka sani, kuma na maka alƙawarin jinin zuri'ata daka salwantar bazai taɓa tafiya a baza ba sai ka biya da FANSA. FANSA a lokacin da baka da madafar dafawa, FANSA a gaban alƙalin alƙalai. FANSA a ranar da gangar jiki ke amsa tambayoyi ba baki ba. FANSA a ranar da ake roron ayyukan alkairi. FANSA a ranar da ake biyan bashi da aiki bada abinda aka karɓa a duniya ba. Idan babu aiki za'ai FANSA da zunubin mai hakki. Kamar yanda wannan dukiyar ta gagareka amsa a hannun mai ita duk da kanada damammaki da gadarar kai shege ne a hannun UMMU-HIDAYA ta ƙara maka nisa ne, nisa mai matuƙar tazarar da sai dai yaro da babba su hangi sararin SAMANIYA a samanta badai taɓawa da hannaye ba. Ai kai matsoracine ma tunda kashewa kake, cikakken namiji fili yake sharewa a gwabza yaƙin nuna ƙwanjin NASARA, Gwarzo na gaskiya ya ɗauki KAMBUN IKO!!!. Na faɗa, na kuma sake maimaitawa, zan kuma sake shelantawa. Ka kuma rubuta ka ajiye kona mutu a dalilin ƙaddarar mutuwata a hannunka take sai an maimaita maka hakan. Kuma koda bana raye wannan dukiyar tafi ƙarfin mallakar ka kai da kaf ZURI'ARKA baƙin TSINANNE, sai dai ku ƙare rayuwarku a ƙarƙashin ALFARMAR ZURI'AR MAHAIFINA”.

“Hahhhhh!! Lallai yaro bai san wuta ba sai ya taka. Oh ya TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE kenan. To bari mu gani ni da ke waye shegen. Bazaki mutu ba. Zan barki a raye kuwa ta yanda sai na ɗanɗana miki azabar ruwan DALMA a tsakkiyar tafin hannu. Zakiyi rayuwar da gara mutuwa da ita. Zakiyi rayuwar da ke kanki sai kin tsani kanki da kanki. Zakiyi rayuwar da yaɣanki sai sunji sun tsaneki fiye da komai a rayuwarsu. Zan nisanta su da ke, na rainesu raino irin na bawa da uban gidansa. Fiye da irin rainon da UBANKI yay min. Dan sai na maida su KARNUKAN farauta ta da zan dinga jefama NAMA suna bi da gudu suna ɗauka tamkar wulaƙantatu.

Dukiyar da kike gadara da ita ɗanki ne zai juyata ni da kaf ZURI'ATA muna kwance muna ci a cikinta. Sai ya ƙare ƙarfinsa da ƙuruciyarsa akan bauta min kamar yanda na ƙare nawa ƙarfin da ƙuruciyata akan naki uban. Sannan daga ƙarshe na miki alƙawarin zan shinfiɗe miki gawarwakinsu a gabanki bayan koman da kike taƙamar da shi ya dawo hannuna. Muje zuwa wasan yar Alonso". Ya faɗa cike da gadara yana ficewa kafin nace komai. Bamma san yanda akai ba, yanke jiki kawai nayi na faɗi a wajen. Ban tashi farkawa ba sai bayan kwana biyu kamar yanda Bilkisu ta sanar min kwanana biyu a halin suma shiyyasa suka kaini asibiti. Halin da naga Muhammad a ciki ne ya ƙara ɗaga min hankali. Cikin kwanaki biyu duk ya fita a hayyacinsa. Dan haka na tambayeta shine take sanar min ai shima yana dawowa a makaranta lokacin ina sume kasancewar shi ya fara cin karo da ni sai ya ɗauka na mutu ne, shine ya yanke jiki ya faɗi shima. A tare ma aka kawomu asibitin. Sai dai shi bai jimaba ya farfaɗo. Tunda kuma ya farfaɗo basu sake gane kansa ba. Baya cin abinci sai ruwa kawai. Magani kam dama ya tsaneshi sai da ƙyar ake danna masa shi. Kamasa nayi na rungume ina hawaye. Shima yana kuka. A zancen nan da nake muku fa Azz baya gari, tun abinda ya faru na kawo min wata ɗakin barci daya gudu ban sake ganinsa ba har lokacin. Bamma san inda yake ba. Kuma har cikin raina ina son sani kodan jin abinda babansa ya faɗa da saka hannunsa yake mun komai tun farkon auren mu. Waɗan nan damuwar ta Muhammad da Azz ta sake ƙarfafa ciwona har nai jiyya kusan ta sati uku. Daga lokacin kuma komai ya canja daga yanda yake. Ummu-Hidaya ta gaskiya ta gushe. Ciwon HAUKA ya maye gurbi. Tun abin na buga min na ɗan dawo hankalina a wasu lokutan har komai ya rincaɓe ta yanda bana gane komai sai tsananin tsanar Muhammad. Gashi dai shine a mafarkina da ƙasan zuciyata. Amma a duk sanda ya tunkaroni ji nake tamkar na kasheshi na huta. Bana taɓa samun nutsuwa har sai na raunatashi... Kuka ya sarƙeta. Maash ta kamo ta rungume tsam a jikinta.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

.....Kowa a falon kuka yake fiye da zaton mai zato. Idan ka cire prof da muƙarrabansa sai Hajiya ƙarama da tai tagumi kawai. Sai Maash da ke kukan zuci dan babu ɗigon hawaye akan fuskarsa. Sai da kowa yay mai isarsa kafin Ummie ta cigaba da faɗin, “Kuji tsoron ALLAH duk da anan mafi rinjayenku zuri'arsa ne, kuyi alƙalanci na gaskiya. Minene laifin mahaifina ga wannan mutumin? Shin dama ALKAIRI kan zama SHARRI? Ta ina mahaifina ya tauye mutumin nan? Minene laifin su Muhammad idan yace ni na masa ko mahaifina ya masa. Adamu baka tunanin ALLAH yay maka talala ta tsahon rayuwa har zuwa wannan lokacin da kaci alwashi a kansa ba? Ko a tunaninka isarka ko gadarar taka ce ta jagiranceka zuwa yau? Lawisa mina miki a rayuwa? Wane mummunan abu na taɓa aikata miki da aka haɗa hannu da ke wajen cutar da ni. Ke ɗin fa yʼar uwa na ɗauke ki. Jawoki nayi daga rana a lokacin da kike matuƙar buƙatar hakan zuwa cikin inuwa. Na haɗu dake a secondary school first ranar da aka kaini nima kema aka kaiki. Yanda kike ƙazama daga ganinki anga jigatacciya yasa kowa a ajinmu baya son haɗa mu'amularsa da ke. Kin bani matuƙar tausayi dan koba komai rana guda aka kawo mu. Hakan yasa na janyoki jikina hatta da kuɗin break ɗina tare mike rabawa. A randa kika bani labarin aikatau aka kawoki garin Lagos kasancewar baki gane komai baki jin turanci gidan da kike aiki suka sakaki a makaranta yasa na ƙara jin tausayinki. Haka na kaima Abie kuka a kanki. Na roƙesa ya amsoki a gidan da kike ki dawo gidanmu. Soyayyar da yake min tasa bai musa ba ya amsa min ya kuma aiwatar. Sai dai wadda ta kawoki aiki ashe yʼar uwarki ce ta jini dan haka ta nuna bazata bamu ba dole mukai haƙuri. Amma Abie yace zai cigaba da ɗaukar nauyin karatun naki kibar aikatau ɗin. Haka akayi kuwa, duk abinda Abiena yay min a fannin karatu sai ya haɗa da ke, hatta da sutura a lokuta da dama idan aka siyamun nakance kema a saya miki. Haka zai saya miki batare da ƙorafi ba. Hatta da yʼar uwar taki yakan hidimta musu duk dan soyayyar dake tsakaninmu. Hatta da karatu da taimakonna kike yinsa dan baƙya gane komai ba gori ba. A haka muka kammala secondary. Duk da Abiena ya mun aure da Azz mun bar Nigeria bai daina ɗaukar nauyin rayuwarki ba. Kina zuwa masa da batun komawa karatu a fannin lafiya ya biya miki bayan ya tallafa miki kika fara. A haka na dawo na sameki kin zama ma'aikaciyar jinya. Abin ya birgeni na fara tunanin buɗe miki asibiti. Ina gayama Abie ya bani goyon baya ɗari bisa ɗari. Haka ya bani kuɗi na zuba aka gina ƙaramin asibitin shan magani da karɓar haihuwa kawai aka damƙa miki. Sai dai ƙarancin ƙwarewa yasa nai ƙoƙarin sake turaki ƙaro karatu, kafin ki dawo aka sake faɗaɗa asibitin. Ya zama kowa zai iya jiyya aka ƙara sabbin ma'aikata da kayan aiki da bako ina zaka iya samunsu ba aka shugabantar dake kula da komai na asibitin. Abubuwa da yawa kin sani a kaina Lawisa. Rayuwar aurena da sirrina da mahaifina ne kawai bana shering ɗin sa da kowa a rayuwata. Dan haka har mahaifina yabar duniya bai taɓa sanin a halin ƙuncin da nake a gidan aurena ba, na saka a raina watarana komai zai zama labari. Domin ina ƙyautatama mijina zato da fatan watarana girma zai sa ya ajiye wasu

abubuwan kodan yaransa dake tasowa. Ko'a lokacin dana dawo a hayyacina na shakera kusan ɗayar nan na buɗe ido na ganki matsayin matar Azz ko sau ɗaya na taɓa canja miki fuska? Kona taɓa bincikarki yaya kika auri mijina? Gashi nan shima da ransa da lafiya Azz na taɓa tuhumarka ya akai ka auri Lawisa? Na taɓa nuna maka ba kayi dai-dai ba har na koma a halin ciwo?. Bama kuba ga yayana nan, ga Bilkisu nan da ake ganin inada kusanci da ita fiye da kowa akwai wanda na taɓa tambaya yanda akai Lawisa ta auri mijina?. Ba kuma dan banji zafi bane ko banyi mamaki bane, kawai na bar al'amarin matsayin ƙaddara kuma aurene ai ALLAH ya halasta muku dammi ni kuma zan butulce masa bayan yamun ni'imomi daban-daban a rayuwa da ban san adadinsu ba, sannan a halin da nake ciki dolene Azz yay aure ai. Zaman Lawisa da Azz matsayin ma'aurata bazai ƙaran da komai ba, ba kuma zai rageni da komai ba. Hatta da wannan yarinyar (ta nuna Arwa) dana buɗe ido na ganta akace yar Lawisa ce har yanzun ban sani ba Azz ne mahaifinta ko wani daban. Dan a sanina nasan gab da rasuwar Abie Lawisa tazo mana da zancen ta samu mijin aure acan garinsu. Sai dai har Abie ya rasu ba'ai auren ba ni kuma nazo na shiga halin dana shiga. To ban sani ba ko tayi wancan auren ko batayi ba, da kuma na dawo hayyacina ganinta matsayin matar Azz ban tambayeta komai ba. Lawisa a cikin wannan duk dana faɗa ta ina na cutar da ke? Minene laifina a gareki? Minene laifin mahaifina da har kika iya bada gudummawar aka halakar da shi akan abinda yake hakkinsa. Ki faɗa min Lawisa! Ki faɗa min....”

Kuka yay bala'in sarƙeta har bata iya jan numfashi da ƙyau. A mamakin kowa sai muka ji Hajiya ƙarama na dariya. Babu wanda bai zuba mata ido ba a cikinmu dan mamaki. Sai prof ne ya wani taɓe baki da jan tsaki mai ƙarfi yana gyara zaman ƙasaitarsa shi a dole ga tantirin tsoho. Sai da Hajiya ƙarama tayi mai isarta sannan ta miƙe tana tafa hannaye da yima Ummie wani kallon zako ki sani yau. A gadarance ta ce, “Ummu-Hidaya kenan. Naji duk lissafinki da gorinki akan abinda kika min ke da babanki. Na kuma gode da gori. Dama kuma nasan irin wannan ranar zata zo, gata kuwa tazo. Dalili dai kike buƙata ko, to gashi zan faɗa miki yanzun nan. Komai ya faru ne a dalilin MAHAIFINKI. Tun a ranar farko da aka kaini makaranta kema aka kaiki na gansa son sa ya shige min zuciya sururuf....”

Kaff falon nan hatta da Prof a wannan gaɓar sai da ya kalla Hajiya ƙaramar. Cikin halin ko'in kula ta ce, “Eh ku kalleni da ƙyau abinda na faɗa shine gaskiyata. So ne na gaskiya na aure ya shiga cikin ZUCIYATA a ranar farko dana fara ganinsa. Ban damu da zai iya haifata ba, danni ba shekarun na kalla ba NAGARTA da jin soyayya ta gaskiya. Sai dai abin kaico da tashin hankali a gareni ban san ta yaya zan mallakesa ba. Dan haka na shiga ƙulla ta wace hanya zan samu? Kwatsam sai kika shigo rayuwata kika jani jikinki. Nayi farin ciki da hakan domin son da nake ji inama mahaifinki kema ya shafeki. Ƙaunarki ta ƙara tasiri a raina a lokacin da kika kaini ga Mahaifinki matsayin ya taimaka min ga halin da nake a ciki. Bai kumayi musu ba ya amsheni, kinyi ƙoƙarin ganin na dawo gidanku da rayuwa amma innata ta hana hakan. Naji zafin abinda tai min amma na ƙyaleta da tunanin a hakanma zan iya mallakar babanki, idan ta hanani zama ai aure zai maidani zaman din-din-din. Na

ɗan fiddo da hanyoyin nuna masa manufata duk da ƙarancin shekaru na amma ya nuna baima san minake yi ba. Banji haushi ba, na kuma ɗauka har cikin raina bai fahimta ɗin ba kasancewar Bature. Idan baki manta ba a cikin hikima nazo miki da labari makamancin irin namu gab da zamu gama karatu. Na nuna miki ƙawar na bala'in son baban ƙawarta amma buɗar bakinki sai kika ce wai bata da tarbiyya ne da kunya. Idan da kece kuma wannan ƙawar wlhy sai kin rabu da ita. Har misali kikai da ni da ke akan naga dai babanki baida mata ko, a misali nace ina sonshi wlhy sai kin rabu da ni har abada. Dan sam abun babu mutunci a ciki babu tarbiyya. A lokacin dariya kawai nai miki amma naji zafi har ƙasan raina. Na kuma fahimci aikine a gabana tuƙuru kenan. Daga ranar ban sake miki maganar ba har aka sha bikinki da Mu'azz. Nayi farin ciki matuƙa jin zaku bar ƙasar ne, a ganina damace agareni. Hakanne kuwa yasa kuna wucewa banyi ƙasa a gwiwa ba na fara aikama babanki sakwanin wasiƙu ta hanyoyi da dama. Amma bai taɓa amsa min ba. Ganin wankin hula zai kaini dare lokaci na wucewa na sameshi har office na fayyace masa sirrin zuciyata cikin roƙo da kuka. Ganin yanda ya shagala a kallona sai na ɗauka zai tausaya min. Amma ina gamawa ya balbaleni da masifa ta inda yake shiga bata nan yake fita ba. Sai da yay mun tass da tabbatar min ai ko aure yake buƙatar yi bazai auri yʻar cikinsa ba, yʻar cikin tasa ma ƙawar yʻarsa da itama yakema kallon yʻa. Ya nuna min nama cire wannan tunanin daga zuciyata har abada kada na sake dawo da shi. Shi kallona yake dai-dai da Ummu-Hidaya, zai kuma cigaba da mun irin wannan kallone har abada. Dan haka idan inaso na shirya na koma makaranta, na kuma zaɓi kowacce nake so zai biya min.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-eight

.....Ba wannan nake buƙata ba, dan haka na baro office ɗin cikin ɓacin rai. A tsakanin har jiyya na kwanta kusan na wata biyu. Da ƙyar aka samo kaina na dawo dai-dai. Na ɗauka nisantarsa da nayi zai canja komai, sai dai sam ba haka bane komai ma kamar ƙaruwar yake yi. Dan haka na yanke hukunci zuwa nace masan zan koma makarantar ko hakan zai sa ya koma fuskanta ta. Nayi mamakin daya amsan da hannu biyu ya kuma kaini makarantar yay min komai, sai zuciyata ta sake ƙarfafani akan zan iya shawo kansa wataran. Haka na cigaba da karatu ina cigaba da bibiyar rayuwarsa har kika dawo. Dawowarki taso canja wasu abubuwan dan na sake samu kusanci da shi fiye da sanda baƙya nan, na kuma sake fito masa da har lokacin ina kan bakana ya taimaka min ko bazai aureni ba yay tarayya da ni koda sau ɗaya ne. Amma sai ya karta min rashin mutuncin da yafi na farko, ya saka drivern sa yamun kora irin ta kare. Suka wulaƙantani mafi munin wulaƙanci da banyi zato daga garesa ba. Da yake so na gaskiya zuciyar take masa banyi fushi ba ko yanke mu'amula da ke har kika buɗen asibiti. A zatona lokacin kin mallaka min asibitin ne, wataran zaki mallaka min takardu matsayin nawa. Dan haka na ɗan ragema kaina damuwa akan mahaifinki. An kai matsayar da kika shawarceni da sake komawa karatu, ban musa miki ba na amsa da hannu biyu na tafi wata ƙasa karatu, ban kumayi wasa ba nayi karatun na dawo, abin farin ciki da kika fara tabbatar min da shi shine faɗaɗa asibiti, na takaici shine kawo wasu ma'aikatan matsayin wanda zamu haɗu mu kula wai da shi. Ni a lokacin zuciyata ta gama bani wannan asibiti mallakina ne, ba wai shugabancinsa nake buƙata ba. Ga soyayyar mahaifinki da maimakon raguwa kullum sake faɗi take a raina duk da inada masoyana gwargwado amma naƙi bama kowa muhimmanci. Anyi bikin buɗe asibiti a daren na bankama mahaifinki ƙwaya na kuma je garesa batare da kun sani ba kasancewar kuma duk barci na sakaku a gidan saboda anan na kwana wajenki. Sai da ya fara sakin jiki mukai nisa ga abinda nake matuƙar buƙata a garesa kawai ya tureni kamar wanda ya tuna wani abu. Ya jefeni da maganganu masu matuƙar zafi da ciwo, amma na danne na duka ina roƙonsa ko sau ɗaya ne ya taimakeni amma mutumin nan ya hankaɗoni waje bayan ya shashsheƙa min maruka da tabbatar min ya min mafi munin tsana a rayuwarsa. Ya kuma bani lokaci nayi gaggawar fita a rayuwarki gaba ɗaya idan ba hakaba zanga matakin da zai ɗauka a kaina. Na nuna masa kada yay wannan gangancin ni mai sonshi ce ta gaskiya, har tayin kashesa an kawo min ban amsa ba kuma wanda ke jikinsa ne daya yarda da shi. Amma sai ya nuna ƙarya nake yana sake wankeni mafi munin wanki ya sake saka Drivern sa a daren ya bar gidan da ni.

Wannan zafin da ciwon yasa a washe gari na samu Adams da batun amsar tayinsa. Dan na fahimci bazan samu abinda nake so ba, to kuwa kema da yake komai domin ke sai kin rasa shi gwara ace bana ganinsa a duniyar gaba ɗaya. Wannan ne dalilin dunƙulewar mu da Adams, duk da ban wani saki jiki da shi ba shima sosai. Na kuma amshi umarnin iyayena akan mijin da duka zaɓa min duk da bana jin sonshi bamma taɓa ganinsa ba. Na kuma amshi tayin abokina da muka haɗu a karatuna mai suna Marcel. Na fara masa safarar yara mata kaɗan-kaɗan daga ƙauye mu, sai kuma yazo da buƙatar neman ƙoda. A tsakanin ne babanki yay

accident, zan ma iya cewa da ƙodarsa muka fara a wajen treatment. Bayan mutuwarsa dil ɗina da Adams ya ƙare dan haka na buƙaci shere ɗina dan lokacin idanuna sun fara buɗewa da kuɗi. Amma sai ya sake kwaɗaita min batunki da kuma yanda kukayi da shi. Banyi mamaki ba dan ni nasan kina da taurin kai, zama ki iya faɗa masa abinda yafi hakan. Ko musu banyi ba da wannan sabon dil na amsa kuwa, mukai cinikin Shere ɗina akan zamuyi 60-40 muka fara aiki. Sai dai a tsakanin anyi aurena da Sabilu, mukai zaman shekara biyu da shi ya rasu. A randa kikai sumar farko na shock ɗin da kika shiga kan batun Mu'azz da budurwarsa ni na fara miki allura. Shi kuma ya bizne asirin daya amso akan ki tun daga ƙasar Togo. Daga baya kulawar da ɗanki ke baki ya nema wargaza mana aiki, dan duk wanda yasan Awwab tun yana yaro hatsabibin kansa ne. Shi kansa Adams ɗin wlhy yana jin shakkarsa da wasi-wasin karfa wataran ya zame maka ƙayar kifi. Dan akwai lokacin da yay niyyar ya kashesa na dai lallaɓashi akan koba komai zai mana amfani, dan yafi Fahad ƙarfin zuciya. Haka dai ya barshi badan yaso ba. Sai dai mun sake hanyar maidosa tafin hannunmu shima, muka saka ƙiyayya tsakaninku, hakama tsakaninsa da ɗan uwansa. Ni kuma na zama matar Mu'azz saboda aikinmu ya tafi yanda ya kamata, tunda mijina ya mutu na gama takaba. Sannu a hankali abubuwa suka kankama, maganar Adams ta fara tabbata, dan kuwa Awwab ya koma juya dukiyar, duk inda zai shiga ya fita ya sani akan kasuwanci. Har yama fi mahaifinki da ke zafin nama, ga shi da nasibi komai ya taɓa kafin wani lokaci ya zama kuɗaɗe. Tun muna ɗaukar abun ƙarami sai muka fahimci babbane fa, dan dukiya nata hanƙoro da bunƙasa. A tsakanin mukai tunanin warware asirin kanki domin gwadaki ko kin saduda ne, Adamu yazo da malaminsa na Togo, wanda shine yay ainahin asirin dama matsayin mai magani. Ya warware asiri a zuwan magani ya baki, kowa nata farin ciki lafiya ta samu gareki, yayinda mu kuma muke ta shirin kammala dil ɗin mu. Abin mamaki abin tsoro, koda bayan samun lafiyarki Adamu ya tunkareki sai gadararki tafi ta farko, kamar ma an ƙaro miki izza ne. Dan maimakon ki risina ƙaimi aka ƙara kunna miki. Kin saka ɗanki yin katafaren company a garin kano. Kin kuma fara wannan katafaren gidan dake a jerin gidaje na farko da ake alfahari da su a garin Lagos. A babbar anguwa irin wannan. Hakan ya sake haukatamu, dan mun sake tabbatar ba ƙananun kuɗi kika mallaka ba. Hankalinmu ya tashi, mun kuma fahimci idan fa har lafiyarki ta ɗore tofa mu wankin hula ne zai kaimu dare ne. Dan mun gano shirye-shiryen da kike akan Adams saboda shi kaɗai kika sani. Bamuyi ƙasa a gwiwa ba kuwa muka garzaya Togo, muka sake sabunta aiki, muka kuma canama mai maganin wajen zama dan mun san zaku nemeshi. Hakan kuwa akayi, kun nemeshin kamar yanda mukai zairgi, rashin samunsa kuma ya ɗaga muku hankali matuƙa. Ko'a kwalar rigarmu mukam. Bayan kun gama bige-bigen neman maganin asibiti da mutumin, dan babu kalar kai-kawon da baku sha ba daga baya dai kuka haƙora da tunanin mutumin ya mutu ne ma. Bayan shuɗewar watanni Awwab ya ƙarasa gina gidan nan, ɗakkoki ku dawo nan yasa abubuwa suka ɗan fara mana nisa. Dan sai dai kawai nazo sau ɗaya a rana da doctors ɗin ta damu sukema aiki kawai mu dubaki. Dan haka dole muka sake sabon lale musamman daya zama zuwa lokacin shi Awwab ya gama yarda da sakin jiki da ni, ta ɓangaren kakansa ma babu matsala. Shine ya masa magana da nuna masa

muhimmancin dawowarmu kusa da su saboda al'amarinki. Da farko yaso ɗan tirjewa, sai daga baya kuma miya gani oho masa ya dai amince. Mun dawo Mansion, Nafisa ta dawo, Mama ma ta dawo, hakama Abdullahi da iyalansa, wannan duk cikin burin kakanku ne daman. Dan haka bai taɓa damuwa ba game da hakan duk da bashine yace duk sauran su dawo ba, saboda ya miki alƙawarin dama sai zuri'arsa sun zama suna kwance ya bautar da ɗanki wajen nemo musu suci su hutama ransu. Shi kansa baida aiki sai yawon bin ƙasashe yana hutawarsa duk da tsufar nan nashi da kike gani matsiyacin. Da kike maganar na auri Mu'azz ban taɓa sonshi ba. Ina zaune da shine kawai dan cika manufa..

Duk da a farko-farkon aure zuciyata ta fara karaya, amma bawai na miƙa wuya bane, soyayya ta gaskiya har yau har gobe mahaifinki kawai nake ma ita Ummu-Hidaya. Tabbas tako ina Mu'azz baida daɗin zama. Dan ko matan da yake bi a waje bawai suna jin daɗin mu'amula da shi bane saboda bai ɗauki mace da wata daraja ba. Kawai dai idan akace kuɗi to ƙarshen zance kenan. Suma kuɗin sukema biyayya. Shiko bin matansa mujarrabu ne a garesa ko nace hakkinki, dan akwai lokutan da sam baya so saboda tsoron Awwab da yake ji. Dan zan iya ce miki wannan ma shine dalilin fara shirina da Awwab, tun da ya gano halayyar sa sai ya fara tausaya min, dan ya fahimci nima bawai zaman daɗi nake da shi ba. Sosai shirinmu na tafiya yanda ya kamata, sai dai maganar buɗe Companyn Kano ne ya fara hargitsa mana lissafi. Dan na kula Adamu sam baya ƙaunar hakan a ransa da gaba ɗayan rayuwarsa. Ga kuma Awwab ɗin ya nuna masa taurin kai a bisa umarninki. Ban fahimci abinda yake jima tsoron ba sai da matashiyar budurwa yar jarida mara tsoro ta saka Awwab magana a karo na farko na rayuwarsa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page eighty-nine

Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yɜan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....😉□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....Koni na tsorita, dan duk wanda yasan Awwab yasan baya yarda yay hira da yɜan jarida. Hakan kuma nada nasaba da al'amarin ki, idan har kikaga yayi magana da

yan jarida akan abinda ya shafi Bussines ne a kuma filin bussines ɗin kawai. Amma a wannan gaɓar bayan wani kallo da yama yarinyar irin wanda mu kammu shaida ne bayama mace irinsa koma ace bai yaɓa ba kai tsaye ya amshi gayyatarta. Hankali tashe nai kiran Adamu na tura masa faifan video ɗin dan yanata yawo, shine ma latest topic a wannan satin gaba ɗaya. Shima hankalin nashi tashi yayi, dan a ranar ya baro India zuwa Nigeria. Ko gida bai shigo ba daga airport yay Kano. Ba wannan bane kaɗai ya ɗaga mana hankali, akwai yaron Adamu mai suna Commondo dake masa dukkan ayyuka na sharri, kasancewar a gidan nan munada masu naɗar mana bayanai tako ina hatta Fahad dake ƙasar waje sai muka haɗa Awwab da wani yaron Commondo ɗin mai suna Jaga, Jaga irin mutanen nan ne masu wayo matuƙa. Ta duk yanda zasu shiga jikinka ka amince da su ya sani, dan haka duk rashin yarda irin ta Awwab sai da Jaga ya zama makusancinsa, muna murnar zamu samu nasara akan Awwab ta dalilin Jaga na jikinsa sai wasan ya canja, wasu halaye na Awwab suka rinjayi Jaga ya fara daina kawo mana bayanan komai akan duk motsin Awwab, idan ma muka takura sai ya dage mana akan shi bai samo komai ba. Dan haka muka fara sanya masa alamar tambaya. Commondo ya saka aka masa bincike akan al'amarinsa. Sai ko gashi an gano masa Jaga ya koma tsagin Awwab ne. Ya saka ko aka sato masa shi, dan kawai mun yanke shawarar a kashesa. Haka ɗin kuwa akayi, Ni da Commondo mukaje da Jaga har Kano a halin suma cikin companyn da Awwab zai buɗe a ranar buɗe Companyn, zan iya cewa ma har aka fara taron muna a cikin companyn a gabana da kansa ya caka ma Jaga wuƙa. Motsi da mukaji yasa muka shiga maɓoyarmu cikin ɗakin tarkacen machines da suka ajiye. Tacan muka fice dama mun tanadama kammu hanya ta dalilin sabon informer ɗin mu. Muka bar Jaga na shire-shiren mutuwa, mun kuma tabbatar kafin asan da shi ya mutu, idan aka ga gawar kuma a cikin companyn aiki ya tashi, dan dole ne Awwab ya shiga bala'i maganar fara aikin company ya tsaya, a shiga kai-kawon bincike mukuma muyi amfani da wannan damar mu cika burinmu dan mun fahimci abinda muke bibiyarfa sun nuna saura tsinka. Sai dai kuma me, har dare babu wani labari akan al'amarin, har jami'an tsaro mukai ma shune sukazo mana da batun babu wani abu daya faru makamancin wanda muke zargi, sai ma neman ɗora mana wani abu suke daban muka dai sha da ƙyar, ga kuma batun yarinyar nan dole Adamu ya shigo Nigeria. Koda ya isa Kano a can ya samemu, sai dai iya bincike bamu gane komai ba akan al'amarin yarinyar, hakama Jaga bincikenmu ya tabbatar mana ya mutu, Awwab ya saka an fidda gawa ta yanda babu wanda zai iya samun kafar zarginsa. Bamu so haka ba, amma ba komai ai akwai wata damar, koba komai kuma mun kawar da Jaga ɗin dake neman tona mana asiri. Mun cigaba da harkar gabanmu hankali kwance. Sai kuma shigowar yarinyar nan matsayin ƴar aiki ya sake wargaje lissafinmu. Kada kuyi mamakin da ban gane ta ba, saboda a wancan karon bawani kallo na mata sosai ba, akwai kuma facemask a fuskarta eyeglasses, hakama lokacin da tayi hira da Adamu da shi kansa Awwab ɗin ni ban wani maida hankali a kammaninta ba saboda zuciyata ba'anan take ba kuma lokacin ma dai da gilashi. Tabbas Samraah ta wargaza mana komai. Dan yarinyar nan kamar an karanta mata daki-daki ta dinga tafiyar da al'amuran har zuwa wannan gaɓar.

Tabbas you are smart, I love you”. Taƙare maganar tana wani kashewa Samraah ido cike da salo...

Harara na watsa mata cikin takaici na ce, “Ni kuma Kinga na tsaneki. Tsana mafi munin tsana da nake jin zan iya ɗaukar makami akanki wlhy. Jaka jahila butulu kawai. In sha ALLAHU ƙarshenku bazaiyi ƙyau ba. Ummie kuma ta muku nisa mai tazarar zango da har gaban abada bazaku taɓa iya kamota ba. Jinin iyayenmu kuwa daya rataya a kanku in sha ALLAHU bazai barku sake zaman lafiya ba a rayuwarku daga nan har ranar mutuwarku. Dan yana da nasaba da rashin nasarar ku kuketa wahala na shekara da shekaru har zuwa yanzu kun gagara cimma abu guda. Ciwon da Ummie tayi kuwa ƙaddararta ce wawaye, hakama rabata da yayanta ƙaddararsu ce. Yanzu da UBANGIJI yaso yaye musu ba gasu ba kukuma har yanzu kuna a ƙasan ƙafafunsu. Kai a tunaninka ka bautar da Ya Awwab yana nema muku duniya kuci kai da zuri'arka ko. Hhhhh baka fahimci ƙarshen labarin naka ba yanzu? Shi da kake tunanin ka bautar, da ku yan kwanciya a kawo muku kuci matsayin iyayen gida waye ta ƙaremawa? Waye ya faɗi ƙasa wanwar? Dawa ta ɓare? Da ku, ku ɗin nan marasa tawakkali ga UBANGIJI, marasa tauhidi da yarda da ALLAH ba abin wasan wani banza bane. Idan dai har ƙyautatawa zata iya zama wa irinku mutum bazai taɓa fatan ƙyautatama kowa ba. Dan kune kesa bayin ALLAH tsoron ƙyautata ma mutane a wannan ƙarni, kuke saka a gagara banbance na ƙwarai da butulallu irinku. Kaicon bawan da za'a ƙyautatama da tarin alkairi ya maida da sharri. Kaicon bawan da zai dinga kallon hidimarsa ga wani kamar ta fi ƙarfin ƙyautatawar da yake masa koda ya fitar da hakkinsa. Kai kana ganin kun tallafa ma Abie ya tashi saboda ya shigo ƙasarku matsayin baƙo. Ka hidimta masa, ka masa miye, ka masa miye, miye, ko. To amma malam mai hidima idan har da kunya a tare da kai kuwa ya dace ka zauna bamu wannan labarin ma?. A wannan hidimar da kai masa fa, shima shine ya ɗauki nauyin karatunka har zuwa wata ƙasa. Ya baro iyalanka daga ƙauye suma ya ƙyautata rayuwarsu, ya ɗauke su ya kai su ƙasar da kake ya inganta musu rayuwa da ilimi....”

“Ilimi kodai ya lalata musu rayuwa, ta sanadin hakan ɗana ya lalace da neman mata....”

A fusace na ce, “Ban gama magabata ba kada ka sake katseni!!!!”. Babu wanda bai kallan ba a falon, dan nayi magana ne fa like wata boss lady, ni kaina naga ƙarfin hali na. Fahad ya kwashe da dariya tare da faɗin, “Duk wanda ya ƙara katseki Aunty Sam ALLAH sai na kwashe miki ƙafafunsa. Cigaba da basu bayani.”

Jinjina nai masa da satar kallon Maash, zaune kawai yake kansa a ƙasa ya dafe shi da duka hannayensa. Ummie kam kallona take tana murmushi. Murmushin na mata nima da cigaba da faɗin, “Abie bai lalata maka ɗa ko ɗaya ba. Baƙin halayyarka ce ta lalata su. Ko baka san masu iya magana kance TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE ba. To ka binciki kanka da kanka kaine amsar tambayar abinda ke zagaye da zuri'arka. Abie ya baka gida bayan dawowarka, ya baka motar hawa. Ya ɗauki company guda sukutum ya baka tare da kuɗaɗen da zaka kafa Bussines. Ya

ɗauki yarsa ɗaya tilo ya bama ɗanka aurenta. Duk da wahalar da take sha bata taɓa iya gaya masa ba ta shanye tai haƙuri, har ma tana tattali da fatan haihuwa da shi, a hakan da yake sonshi take. Duk da halin daka nunama mahaifinta na banza, ka kuma fiddo masa da ainahinka a sanda yake gadon asibiti bai gaya mata wanene kai ba saboda halin dattako. Bai ce ta rabu da ɗan ka ba. Bai ce ta tuhumeka da abinda ka aikata masa ba, sai ma cewa yay duk rintsi ta kasance da shi, duk rintsi ta maka biyayya a matsayin ƙaninsa na jini. Kaji halin manyan ƙwarai masu tauhidi. Dan ALLAH abin bai birgeka ba?. A lokacin da kazoma da Ummie baƙin halinka ɗanta nada wayon da zata sanar masa. Ya ƙullaceka a zuciya har kawo yau. Amma ka duba batace ma kowa komai ba har ka aikata abinda kake ganin damace ta baka ka aikata. Har warkewa tai a lokacin da shekarunsa suka kai yasan komai amma ta shanye bata faɗa masa ba. A hakan bata faɗa masa ba da ilimin da UBANGIJI ya bashi ya gano kai ɗin wanene? Amma duk da haka bai tunkareka ba ya barka da halinka shima. Baka tunanin talala suka maka na barinka da ƙarfin ikon ALLAH har azo irin wannan gaɓar da zaka fallasa kanka da kanka?. Ke ko baƙar tsinanna ai bani ma da abin faɗa a kanki. Dan ke baki da banbanci da dabbobin aladu masu cin kashi matsayin abincinsu. Kuma a cikinku duk ma wanda ya ɗauka min yan uwa ya dawo min da su. Idan ba haka ba ni ba Ummie bace da zata iya barinku da halinku, take a yanzu zan sakaku kuyi nadama wlhy, dan kunga wayar nan, komai da kuka faɗa ta kwashe a ciki, yanzu kuma zan tabbatar muku da sunana yar jarida ne. Bara kuma ku gani”.

Kaf falon babu wanda bai waro idanu a kallona ba. Yayinda prof ya zaburo kaina jikinsa na rawa. Babu zato kawai mukaga Maash a tsakkiyar mu. Kallonsa yake kamar zai cinyesa da idanu. Cikin matuƙar fusata ya ce, “Mi zakayi”.

A fusace shima prof ɗin ya furta, “Duk abinda zuciyarka take tunanin zan iya. Har yaushe aka haifi ubanta ma balle ita da take tunanin wani abu”.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page Ninety

.....“Ai ko da kayi mafi girman kuskuren data faɗa zakayi, dan daka taɓa koda kayan jikin wannan wlhy Gara kaje ka ringume transformer kasan dama tsautsayi ya kaika. Oh kai da tunaninka zakayi duk wannan surutun naka ya tafi a banza yaranka su kashe mu ka fice salin alin zuwa airport ka hau jirgin zuwa Saudia daka gama shiri ko, daga can ka wuce ƙasar da kake so. To ai ka makaro. Dan wannan TSUTSAR NAMAN ITAMA NAMA CE. Idan taƙadaranci kakeji ka iya kada ka manta jininka ne ni, na ɗebo daga wasu ɗabi'unka, sai dai ina bi dasu ta hanya mai ƙyau domin maganin irinka. Idan kuma dattako ne, jinin Ibrahim nake, kaga ko gidan ka taras. Bari na faɗa maka abinda baka sani ba. Tun daga randa na gane kai wanene duk wani motsinka a tafin hannuna kake yinsa. Kaf ma'aikatan gidanka da kake gani aikina suke yi.” ya ƙare maganar da kallon ƙofa ya ce, “Bismillah”.

Ba prof ba mu kammu sai da zukatanmu suka girgiza. Duk da ni Bama sanin ma'aikatan nai ba tunda ba taɓa zuwa gidansa nayi ba. Isma'il Kuku ne farkon shigowa. Sai maigadi, amintaccensa, drivernsa daya taɓa karyawa, bai san sanda ya bar hannun Commondo ba sai dai har yanzu akwai ɗaurin karaya a hannunsa. Amintaccensa, mai bayin filawa, masu share-share da goge etc. Taga-taga prof yay zai zube ƙasa sai da Hayatu ya taresa yana faɗin, “Hankali dai Baba hankali”. A yanda yay maganar kowa yasan akwai shaƙiyanci a ciki. Aiko Fahad ta bushe da dariya da faɗin, “ALLAH Yaya Hayat dama ka barsa ya ɗan sha ƙasa”. Mangare kan Fahad Ummie tayi kaɗan.

Dafe ƙirji Baba prof ɗin yayi. Abin mamaki fuskar Maash da murmushi ya ce, “No no ai lokacin bugawar zuciyar baiyi ba da saura ɗan dakata min.” juyawa yay ya kalla masu bindugun dake zagaye da mu. A take suka sauke bindugun suna murmushi. Sai kuma suka haɗe hanayensu waje guda suka ɗan risina wa Ummie alamar ban haƙuri, nima suka juyo suka rissina min, sukaima Fahad da Hayatu ma haka... A razane Baba prof ya ce, “What?! Ozee. Ni zaku cima amana? Na ɗauki nauyin zuwanku tun daga ƙasarku kuce wani kuke ma aiki ba ni ba?.”

“Dama can bakai mukazo yima aikin ba old man. Dan tun kafin kazo garemu shine ya fara zuwa”. Ozee yay maganar cikin nuna girmamawa ga Maash da harshen turanci. Idanu kawai ya lumshe musu ya buɗe su akan Prof da ya gama diriricewa yana kalle-kalle. Murmushi Maash yay da faɗin, “Oh Mr Paul daya ɗakko maka hayarsu kake nema. Hayat!”. Da sauri Hayatu yay salute ɗin Maash ɗin cike

da girmamawa yana fita, sai ko ga Mr Paul bayansa da police biyu ya shigo. Maimakon ya kalla Prof sai ya rissina ya gaishe da Maash.

“Kuturun bala'i, Yaya kana aljanna ina binka da addu'a wlhy, harma Ministar guda a ƙarƙashin komarka yake. Shegiya nera duniya ce”. Fahad ne da wannan maganar yana miƙewa zaram. Ba shi ba mu kammu abin ya matuƙar razana mu. Mr Paul fa da kowa ya sani Minister mai faɗa aji a ƙasar. Eh kam gaskiyar Fahad Naira maganin wata magana. Yanzu kam Baba prof sai da ya kai ƙasa yana nuna Mr Paul da hannu, murya da bakinsa na rawa ya ce, “Kaima munafukina ne dama Mr Paul?”.

Cikin halin ko'in kula Mr Paul ya ce, “Professor magana ce ta kuɗi fa. Sannan magana ta gaskiya Maash yafi ƙarfina, ya wuce da sani na. Bani da zaɓin da ya wuce goya masa baya. Kadai san ni akan kuɗi Mamana ma zan iya badawa”.

“Kutumelacy babarka fa? Shege Ministar yasan takarda hhhhhh!!”. Fahad ne da iskancin nan yanzu ma. Yanzu kam kasa daurewa nayi sai da na murmusa ina mai girgiza kaina. Yayinda Hawaye suka ɓallema Prof a bazata. Nan ma murmushin Maash ya sake saki da faɗin, “Inaa ai lokacin kuka ma baiyi ba. Hayat next level.”

Sake fita Hayatu yayi sai gashi ya shigo da Jaga. Sai wani takun ƙasaita yake ana bubbuɗewa cikin tsadaddun suit Dan yanzu kam Maash ya ɗaure masa ƙugu. Baba prof zai zabura Jaga ya dafesa yana dariya da faɗin, “No tsoho kwantar da hankalinka ba Fatalwa bane JAGUS ne”.

Kalmar JAGUS ɗin nan daya faɗa ita ta sakamu dariya. Dan hatta Maash ɗin sai da yay ɗan girgiza kansa. Cike da izza Jaga ya cigaba da faɗin, “Kun zata na mutu ko? To kwana basu ƙare ba old man. Kasan mu yan gidanmu ALLAH ya bamu tsahon rai. Kakana na goma ance shekara ɗari huɗu yayi a duniya, hakama na tara dana takwas dana bakai. Na shidda ne yay ɗari uku da uku, na biyar kuwa ɗari uku da arba'in. Na hudu yay ɗari biyu, na uku kuwa ɗari da hamsin, shine ya fara rage mana mudu. Wanda ya haifi ubanta ɗari da arba'in yayi, babana kuwa har yanzu yana raye ya kusan cika ɗari da hamsin shima. Ya kake tunani akan ni JAGA, ai maybe ma kakana na goma zan gado nayi four hundred inji turawa, larabawa kuma sukace أربعة مئة.

Wani tsugunne gayu yay a gaban Baba prof ya kamo gemunsa yana wasa da shi fuskarsa da murmushi ya furta, “To ya kake ganin zaku kasheni tashi ɗaya na tafi tsoho? Abinda fa baku sani ba shi wannan bawan ALLAHn KAINUWA ne, sannan DUTSENE na rimi bashi fargaba ko ta ruwa. KWAI NE kuma CIKIN KAYA ajiyar ALLAH. Idan har munanan hallayarku zaku iya jan ra'ayinmu ku lalata mana rayuwa da bamu kuɗi da kayan maye, ta yaya kuke tunanin adali irinsa dake ƙoƙarin ƙyautata rayuwarmu bazai iya janye ra'ayinmu daga gare ku ba. Kai ka godema ALLAH a Muktar nazo nan ba Jaga ba, da wlhy sai na jajjage maka hanjin cikinka tsaf da wuƙa. Kasa a kasheni kai da yaronka da waccan yar iskar karuwar yar karuwa”. Ya nuna Hajiya ƙarama. Idanu ta waro waje da faɗin, “Ni ce karuwar yar karuwa?”. Muryarta na rawa. Murmushi Jaga yay yana miƙewa cikin wani ɗan iskan rangaji ya

isa gabanta, sai da yay mata wani kallon sama da ƙasa sannan ya furta, “Oh maimaici kike buƙata kenan. To aike kin wuce karuwa ma. Matar datai aure kan aure jama'a miya kamata a kirata”. Yay maganar yana juyawa ya kalla kowa a farlon. Cike da shaƙiyanci Fahad ya ce, “Sai dai Uwar ƙaruwar Ya Muktar”.

“Oh oh I love you my ƙani. Nima na zama babba”.

Jaga ya bama Fahad amsa yana wani tsuke baki kamar zai yi kiss da girgiza kai like yanama ɗan yaro wasa. Dariya mafi yawanmu a falon mukayi, dan hatta Ummie sai da ta murmusa. Uban gayyar dai yanzu ma kai kawai ya ɗan girgiza. Jaga ya cigaba da faɗin, “Yawwa to kinji sunanki MAGAJIYAR KARUWAI. Bara na baku labarin wannan matar, dan nasan da yawanku baku sani ba hatta shi ogan nata kansa. A ƙauyenmu akan haifeta, kuma bata da uba, dan tsohuwarta a yawon tazubar ta samota itama. Bayan ta haifeta aka rirrima akama uwar aure da wani saurayinta da aka laƙama yar duk da shi ya rantse ba yarsa bace. Oho musu dai haka suka zauna taren ita lawisa na girma, tsangwamar mutane da hantarar da ake mata duk inda ta gitta ana kiranta yar shege, ko talla ta ɗakko babu mai saya yasa, a makaranta yara dunya dukanta kenan ƙanwar uwarta da itama take zaman tazubar ɗin anan Lagos ta ɗakkota ta taho da ita aka nema mata gidan aikatau. Tana fara aiki taga yaran gidan na zuwa makaranta itama tace tana so, haka mai gidan ya sakata amma da sharaɗin bazasu na biyan kuɗin aikinta ba. Tako amince, daga ita har ƙanwar uwar tata. Da yake tayi primary a ƙauyen namu, sai dai bata kammala ba. Amma shi mai gidan nan yay duk yanda yay aka sakata a aji ɗaya na sakandire. Daga nan ƙaddara da tsautsayi suka haɗata da Ummien mu ALLAH ya ƙara miki lafiya da nisan kwana. Ya rissina yana haɗe hannunsa wa Ummie. Murmushi ta sakar masa. Yayinda Fahad ya ce, “SARAUNIYA UMMIE YAR IBRAHIM MAMAN MUHAMMAD AWWAB DA SAMRAAH DA FAHAD ta amsa maka babban Yaya”.

“Godiya nake my ƙani”.

Cewar Jaga. Sai kuma ya cigaba da faɗin, kada na jaku da nisa. Tunfa Lawisa na aji biyu ta fara sanin maza, shiyyasa ma ta laƙema kakanmu Alhaji Ibrahim ALLAH ya gafarta masa. Sai dai bata samu nasara ba. Yawon tazubar ɗin nata ya fara yawa bayan ta gama makaranta. Wanda ya auri babarta tana zuwa ƙauye yace ya mata miji da Laminu, idan kuma har bata amince ba zai saki uwarta. Itako uwa bata son barin gidan miji, tacema Lawisa idan bata auri Laminu ba zata tsine mata. Da alama dai bata son tsiniwa, dan haka ta amshi Laminu da hannu biyu akan zata aure amma sai ta gama makaranta. Babu wanda yace a'a, dan a lokacin shima Laminu yana makarantar almajirci bai koma gida ba. Bayan kamar shekara huɗu sai ga Laminu ya dawo, lokacin Lawisa na nan Lagos wai ta zama a malamar asibiti, da akace tazo batun aure ya taso sai ta bijire, ai ko dai aka ɗaura mata aure da Laminu, sannan innarta ta ɗauketa da ƙarfin tuwo takai ƙauye. To abin mamaki kuma bamu san yaya akai ba Lawisa na zuwa ta faɗa soyayyar Laminu, wasu dai na ganin aikin asiri ne ba wani abu ba. Haka dai aka tarkatasu suka taho Lagos dan tace bazata bar aikinta ba. Abinda Lawisa da danginta basu sani ba shima Laminu

shegen kansa ne, dan a inda yake ma ya addabi mutane matuƙa, aiko tana kawoshi Lagos idonsa ya buɗe ya fara mu'amula da manyan mutane a riga irinsu su Prof sai ya sake bushewa, dan kuwa wanda ya kashe yaje prison kamashi yay da Lawisa suna ikkanci a ofishinta na asibiti, shine ya bisa har can garinsu ya kashe aka kamashi aka kaisa kotu daga can aka wuce dashi magarƙama. To nadai takaice muku Lawisa taje ƙauye tace Laminu ya mutu a haɗarin mota. Haka akaita kuka da yan sadake-sadake musamman iyayensa harna kwana bakwai. Ita kuma ta shiga takaba wai. Bayan ta dawo ta cigaba da harkokinta daga ƙarshe ta auri ɗan oganta". Ya nuna prof. "Abinda Lawisa da Prof basu sani ba shine. Laminu shine ya koma Commondo kuma yaron prof ne, ita kuma Lawisa mijinta ne uban yarta waccan". Ya nuna Arwa. Wani mugun zabura kuwa Arwa tayi jikinta na rawa. Hannunta dafe da ƙirjinta ta ce, "Na shiga uku ni ɗin?".....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-one

*_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya ƴan yayi cikin farashi mai sauƙi da

rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍____*.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

_Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍__._

....."Tabbas ke kuwa. Da aka faɗa miki Ubanki ya mutu ƙarya akai miki, yana raye yana prison an yanke masa ɗaurin rai-da-rai a lokacin, ita a azaton Lawisa ya tafi kenan, tana son kumaa binne ainahinta ga wanda take tare dasu wato jama'ar wannan gida dake kanki yar tata shine tace ya mutu. Sai kuma ga oganta prof yaje ya cirosa a prison ɗin bayan wasu shekaru. A lokacin kuma tana auren ɗansa. Lawisa ta shiga ruɗani da ganin Laminu, yayinda shima hankalinsa ya tashi amma ya dake, sai da suka bar gaban prof ya buɗe mata aiki. Sunci uwar rikici sosai, daga ƙarshe ya barta ta cigaba da rayuwa a wannan gida amma tana bashi wata Share. Da kuma sharaɗin idan an samu abinda suke ma dakon wahalar nan ma zata raba

abinda ta samu kaso uku ta bashi ɗaya. Duk dan ya rufa mata asiri ta amince. Sai dai har kawo yau shi Prof fa bai san da wannan alaƙa ba sam. Dan haka suka koma ta bayan fage suna cimasa dun-duniya.”

Ai prof baima san sanda ya tafi zai kife ba a karo na biyu Isma'il Kuku ya taresa. Muryarsa na rawa ya nuna Hajiya ƙarama da faɗin, “Lawisa, dama duk zaman da nake da ku ke da Commando kun san juna? Ashe ma Ni dukan jaki kawai nake nabar taiki a kusa da ni. Na gode ALLAH da yasa nayi maganinki a gaɓar da ya dace”. Harara Hajiya Ƙarama da jikinta ya gama sanyi ta zuba masa itama muryar tata na ɗan karkarwa ta ce, “Daga baya kenan. Ji da abinda ke gabanka. Magani kuwa idan ma baka sani ba nine nayi naka”.

“Mi kike nufi?”.

“Abinda kake nufi”.

Dariya Baba prof yay yana wani ɗan buga kansa ya ce, “Abinda ni nake nufi bazai taɓa miki daɗin ji ba wawuya. Ina fatan baki manta lemon da kika sha ba a jiya cikin mota ta kafin mu wuce wajen ɗan iskan mijin naki. To lemo ne mai ɗauke da gubar da zata dinga zagwanye jikinki a hankali bayan ya ruɓar da ke. Ai dama na faɗa kiki sai na kawar da ke, dan ba'a cin amanata a kwana lafiya, yanzu kin yarda ko hhhhh?”.

Rawa jikin ta yake har sai da ta kai ƙasa. Sai kuma ta ƙyalkyale da dariya tana nuna shi da faɗin, “Tsohon banza ai TSUTSAR NAMA ITAMA NAMA CE. Naji ka bani lemo mai guba, nima kuma nasa an maka allura mai guba daka biya da hannunka zakaima Awwab. Kaga idan jikina ya zagwanye kaima naka zai kasance a kandare kar ka zagwanye ɗin wawan tsoho kawai. Ni da kai ai CUTA CE TA ƊAU CUTA ƁARAWO YA SACI AKWATIN MACIJI hhhhhhh”.

Nan ma murmushi Maash yayi da katsesu ta hanyar faɗin, “Har yanzu dai ai ba'a gamaba, lokacin rikicin naku da aibanta juna baiyi ba. Kalla nan”. Ya ɗauki remote ya kunna television. Tar tar kuwa hoton Commondo ya fito, hannunsa sanye da Handcuff, gefensa Jannifer ce itama sanye da Handcuff ɗin. A gabansu akwai kayayyaki iri-iri na makamai da wasu kwaleye dake a rufe. Sai yara yammata a gefe zaune kawunansu a ƙasa an basu facemask sun saka. Sai ta gefensu kaɗan Marcel ne shima da nashi yaran gabansu zube da tarin makamai. Sai kuma yaran Hajiya ƙarama na asibiti. Ga su Rubayya a kusa da su ita da su Falila.

Ba baba prof kawai ba, hatta da Hajiya ƙarama a firguce take gaba ɗaya. Ga Arwa tunda ta zube ƙasa ta kafa mata ido taƙi ta janye hannunta dafe da ƙirjinta. Sai da Commondo ya fara magana da jin ya ambaci sunansa da Commondo sanan Arwa ta juya tana kallonsa jikinta na rawa da lips ɗinta, alamar magana take son tayi amma ta kasa. Kan Commondo ƙasa aka fara masa tambayoyi yana amsawa.

“Minene sunanka”?.

“Laminu, amma anfi sanina da Commondo yanzu”.

“Miye sana'ar ka?”.

“Dabaru ne kawai”.

“Kamar wane iri?”.

“Akan sakani aiki kamar su kisa, fyaɗe, sai saida kayan maye da sauransu.”

“Shekara nawa ka ɗauka kana wannan aikin?”.

“A ƙalla ashirin da uku”.

“Kana da uban gida ne?”.

Ɗan jimm yay shiru kamar bazai amsa ba. Jikin prof nata rawa kamar idanunsa zasu faɗo cikin tvn. Sai da aka sake maimaitawa Commondo maganar sannan ya amsa da, “Eh inada uban gida”. Sai kuma yay murmushi

“Shike sakaka duk waɗan nan abubuwan kenan?”.

“Eh kusan hakan, wasu lokutan kuma aikina ne koma abokan huɗɗarsa”.

“Minene sana'asa?”.

“Sana'arsa kam bata da iyaka. Amma dai babban mutum ne a ƙasar nan mai faɗa aji. Yana safarar miyagun ƙwayoyi, yana safarar mata zuwa wasu ƙasashe. Yana kuma shigo da makamai. Yanada kamfanin sarrafa magungunan bogi. Sannan yana da alaƙa da manyan mutane da yawa da in na kira sunansu sai an razana. Kaɗan daga sana'oinsa na ɓoye kenan. Na zahiri kam rataye yake a bayan inuwar matar ɗansa da jikansa da yaci amanar mahaifinta bayan ya masa rana shi kuma yay masa dare. Idan zan buɗe muku aiki akan wannan mutumin zakusha mamaki. Amma kafin na ambaci sunansa zan baku sunayen wasu gurare yanzun nan jami'anku suje su yi binciken wajen in har aikin gaskiya zakuyi akansa awa ɗaya tayi yawa gareku, shiyyasa ma bazan faɗi sunansa ba sai kun gama binciken.”

Cikin jinjina kai jami'in dake masa tambayiyin ya miƙe, inda ogansu yake yaje, suka ɗan yi magana ya sake dawowa. Takarda da pen aka bama Commondo, sai dai ya nuna musu bai iya rubutu ba. Dole jami'in ya bashi kunne ya gwargwaɗa masa abinda suke son ji.

Murmushi Maash ya saki tare da ciro wayarsa a aljihu yay ɣan danne-danne yana kai hannu ya gyara bluetooth ɗin kunnensa alamar waya ya kira. Ana ɗagawa daga can kai tsaye ya furta, “Lokacinka”. Daga haka ya yanke...

Zubewa kawai Baba prof yay a jikin kujera wata irin zufa na jiƙesa a dukkan illahirin jikinsa. Kamar yanda Commondo kuwa ya ambata in dai aikin zasuyi sai gashi basu wuce mintuna talatin ba kasancewar duk inda ya basu direct address ne ana zuwa ake ganin abinda ya faɗa ɗin. Na farko companyn Baba prof da Abie ya bashi, zuwa yanzu ya jima da faɗaɗashi sosai ana sarrafa magunguna, sai dai acan ƙarƙashin ƙasa ƙwayoyin mayene kawai iri-iri masu hatsarin gaske. Sai expire magunguna da ake loda ana kaisu arewa da drips, wasu ma ba expire ɗin bane basu da inganci sam. A wajen aka samo cocaine da yawa. Waje na biyu gida ne na marayu da kowa yasan Baba prof ɗin na ɗaya daga cikin masu bada gudumawa a cikinsa ashe yara ne ake safara zuwa ƙasashen waje. Wasu kuma anan ma cikin ƙasar ake kaisu wajen manya suna lalata musu rayuwa. Da yawan yaran da aka bincika akwai alamar daga arewacin ƙasar suke, ƙalilanne yaran kudanci. A dai cikin gidan marayun aka fitar da tarin makamai dake ajiye a cikin wani ɗaki.

Hankalin mutane yay matuƙar ɗagawa sosai. Wannan wace irin masiface. Zuwa yanzu kafin ma aji ta bakin Commondo da yawan mutane sun gane prof ɗinne, kasancewar duk wajajen da akaje ɗin yanada muhimmiyar alaƙa da su ta bayyane. Kafin su dawo itama Madam Jannifer aka mata nata tambayoyin, ita kam babu kwana-kwana ta kwashe duk laifinta ta ɗora akan Hajiya Ƙarama da Baba prof ɗin. Ashe itama tana kawo masa mata daga arewacin, ita kuma Hajiya ƙarama ƙoda take sayar mata. Ta kuma tabbatar da Marcel uban gidanta ne ada, yanzu kam Bancy ne. An je binciken ina Bancy yake amma ya gudu. Sai yaran asibitin Hajiya ƙarama da suma suka buɗe aiki da tabbatar da cirar ƙoda da wasu sassan jikin mutane idan sun mutu, wasu turawa ke zuwa su saya. Sai su Falila da suka kasance yaranta. Itace ta kaisu Maash Mansion da sunan aikatau amma aiki suke mata. Ko mazajen da suka aura a gidan duk auren na bogi ne suma yaranta ne. Hasalima mijin Falila so yay ya bijire mata shine ta haɗa tarkon kasheshi a randa sukai kidnapping Paah. Ta sha sakasu abubuwa a gidan musamman ɗaure mahaifiyar Maash dake fama da rashin lafiya da sarƙa a toilet. Sai ta dai-daici zai dawo gida sai ta saka su kwanceta. Sukace ɗauri na ƙarshe da asirinta yaso tonuwa shine sanda matar Maash ɗin ta fara shiga sashen ta sameta a ɗaure har sarƙar taci jikinta. Shigar bazata tayi shiyyasa basu sani ba har sai da abin ya faru, a lokacin sunsha maruka a wajen Hajiya ƙaramar, ta kuma tabbatar musu idan bakinsu ya buɗe wlhy sai ta kashesu.

Bayan dawowar jami'an da sukaje binciken sirrikan Baba prof aka buƙaci Commondo ko zai sake cewa wani abu. Murmushi yayi da jinjina kai, ya ce, “Kusan duk abin faɗa ya ƙare, sai dai ga saƙo zan bama professor Adams Isa K/Mashi, akwai wani ajiyayyen sirrinsa a hannuna da shine makasudin fara aiki na a ƙarƙashinsa. A lokacin da nazo Lagos ta sanadin aurena da matata Lawisa da iyaye suka haɗamu acan ƙauye mu. Abinda kowa bai sani ba mijin babarta ya haɗamu aure ne domin na binciko masa wani mutumi dake a jikin wani hoto. Wannan mutumi shine yay cikin Lawisa. Yaje ƙauyenmu ne yin aikin noman wiwi da ake masa a ɓoye. Ita kuma babar lawisa na kai musu tallan yar tsala a gonar, shine yay

amfani da damar ya dinga amfani da ita har yay mata ciki. Lokacin daya gama harkar nomansa yabar gari ciki bai bayyana ba, sai bayan kusan wata biyu da hakan aka gane tana da cikin, maimakon ai bincike sai aka laƙama ƙanin babata dake matsayin saurayinta, shine aka sakashi dole ya aureta bayan an haifi Lawisa. Shi harga ALLAH yana sonta, amma yayi alƙawarin sai ya binciko wanda yay wannan aika-aika dan ya wanke kansa, wannan shine dalilinsa na sakani aurenta bayan ya samu tabbacin baban nata na anan Lagos ya zama babban mutum, kai tsaye ma ya bani inda zan sameta saboda akwai cikin yan garin namu da shi mutumin ya taho dasu nan birni suna masa aiki shine ma ya sanar da mijin babar ita lawisa ainahin gaskiyar yanda aka samu ciki. Sai dai yana jin tsoron bayyanawa ya saka kansa a damuwa dan ya tabbatar ubantan hatsabibine. Bari dai kada na kaiku da nisa. Da taimakon ɗan garin namu nazo jikin Prof.. ɗin, na kuma tabbatar da lallai shine na jikin hoton nan, a kuma cikin hikima na dinga bin hanyoyin dana tabbatar da shi ɗinne ubanta bayan ya fiddoni a prison saboda yana son na kashe masa wani babban ɗan siyasa a lokacin. Dan haka Lawisa ɗiyar Professor Adams Isa K/mashi ce. Idan kuma ya musa hakan inada cikakkun hujjoji bila adadin dazan iya kawowa akan hakan musamman daya kasance uwarta na raye wadda sukai abin tare, wanda akai komai a gabansu suma wasunsu suna raye. Hotonsa ma da aka samu bai san ita uwar lawisa ta ɗauka a cikin kayansa ba dan ita sonshi take a lokacin na gaskiya ta kuma zata shima son nata yake kamar yanda yake mata daɗin baki zai aureta. Sannan itama bata san mijinta ƙanin babata ya ɗauki hoton ba ya bani. Wannan shine saƙona. Sauran kuma tsakanin ni da shine idan mun haɗu a jail.....✍

Bantan uban can kai. Kenan auren Hajiya ƙarama da Paah a wace matsaya yake? ALLAH ka rabamu da ruɗaɗɗiyar rayuwa.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-two

.....A yanzu kam kaf ɗinmu a cikin falon nan sai da muka miƙe tsaye. Mafi yawanmu jikinmu rawa yake yi. A kaf abubuwan nan saboda mu dai mun san wasu a cikinsu babu abinda yafi girgiza mana zukata irin wannan kalma ta ƙarshe daga Commondo. Hajiya ƙarama ɗiyar Baba prof ce. Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un. Wata gigitacciyar ƙara kawai mukaji Hajiya ƙarama ta saki tana mai zubewa a wajen wanwar. Hakama Baba prof kifowa yay ƙasa daga kujera. Yayinda shima Paah ya zube a wajen sumamme. Hajiya Mammah ta daddage ta banƙara ihu da ambaton “Mun shiga uku baba! Yarka kuma???”. Hajiya Mama (Mashi'a) itama dai taga-taga tai zata zuben ta dai samu ya dafe kujera hawaye tuni sun wanke mata fuska. Uncle Abdullahi ne kawai ke tsaye ƙyam akan ƙafafunsa sai dai shima kansa a ƙasa yake. Da alama kodai kuka yake, ko kuma kan nasa ne ke juya masa. Fahad kam jikin Ummie ya shige yana wani bala'in waro idanu waje bakinsa a hangame kamar wanda yaga abin tsoro. Itama Ummien suman zaune tayi tana nuna Baba prof da Hajiya ƙarama dake ƙasa wanwar a sume. Yayinda Maash da ni da Hayat su Mama da ma sauran duk wanda ke falon duk mukai sumar tsaye kawai tamkar an dasa mu a wajen tsabar razanin jin wannan batu..

Gaba ɗaya gidan ya gama rincaɓewa. Hayaniyar zuwan jami'an tsaro da yan media ya dawo damu hayyacinmu. Burin yan jarida kawai su shigo gidan, sai dai jami'an tsaro dake zagaye da mu sun hana hakan. Ga Hajiya ƙarama na aman jini tana nuna Baba prof tana kuka. Shima kallonta yake da duk sauran yayansa yana kukan, musamman ma Paah da tunda ya yanke jiki ya faɗi shi baima farfaɗo ba. A haka aka fita dasu compaund aka saka cikin ambulance maimakon motar jami'an tsaro dan dukansu likita suke buƙatar gani. Muda aka bari gida zaune kawai muke jugum-jugum babu mai iya cema ɗan uwansa komai. Sai jami'an tsaro daketa faman kai kawo a lungu da saƙo na gidan da sunan bincike. Musamman ma sashen Hajiya ƙarama. Sun samo gwalai-gwalai ɗan kitt guda, sai ruwan allurar poison ɗin nan da taima Baba prof sauran ta ajiye da shirin yina Maash da Ummie. Sai magunguna da alluran data dingama Ummie nau'i daban-daban. Sai tarin wayoyi da take ɓoyewa da numbers ɗin abokan huɗɗarta ke a ciki. Bayan hakan akwai abubuwa da yawa da mu kammu da su kansu jami'an tsaron basu san ma'anarsu ba. Da ga ƙarshe dai aka tattare sauran yaransu dake aiki a gidan maza da suka rage su huɗu aka wuce da su. Maash, Hayatu, Jaga, Uncle Abdullahi suka bi bayansu dan har yanzu ba'a san ina su Hafizzullah suke ba, ana dai kan bincike.

Dole ne a wannan gaɓar Hajiya Mammah, Hajiya Mama su baka matuƙar tausayi, kodan su ɗin mata ne shiyyasa Uncle Abdullahi ya fisu dauriya. Su Azizat kansu kuka suke iya iyawarsu. Dan tunda suke basu taɓa ganin tashin hankali makamancin wannan ba. Ni kaina ban taɓa gani ba. Ummie ce ma ta bani matuƙar mamaki, ko ɗigon hawaye babu a fuskar baiwar ALLAHr nan yanzu. Itace ma ta kamani ta tayar muka nufi sashen mu. Da taimakonta nayi sallar la'asar dan wani irin zazzaɓi mai zafi ne ya gama rufe ni. Mun idar mukaji hayaniya, sai ga Falaq ta shigo da gudu tana kuka. Duk miƙewa mukai kanta, cike da farin ciki. Koda muka fito waje sai muka samu har su Hafizzullah. Ga baƙin Kano da banyi zaton gani ba. Gwaggo Gudidi, Abba, Kawu Musa, Kawu Lurwanu sai Sheikh Muhammad ibn Khalipha Al-Hussain da yay musu jagora. Ashe bawan ALLAH har da shi aka ƙwamushe. Ai bamma san na kwasa zuwa jikin Gwaggo Gudidi ba. Kuka na sakar mata kawai, itama sai ta rungumeni tana sharar hawaye.

Masauki aka fara kaisu dan su watsa ruwa suyi salla. Badan sun so hakan ba saboda matsuwar zama da Mama Balki suka je duk suka aiwatar. Badai a samu zama ba sai bayan sallar isha'i har su Maash sun dawo gidan. Dama suna asibiti ne wajen su Paah. Sai da suka ga komai ya daidaita sannan suka taho. Baba prof da Hajiya ƙarama na ƙarƙashin kulawar hukuma da likitoci. Sai Arwa da Paah da suke a kulawar asibiti dan su basu da alaƙa da jami'an tsaron. Har lokacin ina nane da su Abba. Sai tambayoyi nake zuba musu akan kowa da bayan tahowata. Cikin ƙarfin hali Abba ke amsa min, dan ya kasa kallona saboda kunya. Nima na fahimci hakan, amma sai ban nuna masa ba. Gwaggo Gudidi kam bakinta ya kasa rufuwa da yaba gidan ita da Kawu Lurwanu. Shi kansa kawu Musa na fahimci na manya kawai yake dan sai faman jinjina kai dai yake kasancewar yanzu duk muna a sashen Maash ne.

Kallo ɗaya da nai ma Maash da suka shigo na fahimci a matuƙar gajiye yake. Koma nace alamominsa sun nuna tamkar ma bai da lafiya. Dan sai faman kai hannu yaje saman goshi time to time. A haka yay dauriyar zama suka gaisa da su Kawu Musa. Naji daɗin yanda ya girmama iyayena. Ga Ummie nata ɗawainiya da su itama kamar babu abinda ya dameta. Nan ko itama ɗazun ina kallonta tana sharar hawaye sai dai tana jin motsina ta goge fuskarta ta dake. Sai lokacin na fahimci ɗazun ma saboda mu take dakewar ashe. An gaggaisa da yima juna godiya da addu'oi kafin su Kawu Musa su bama Mama Bilki da Falaq haƙuri, sun amshi laifinsu da kuskurensu ƙwarai da gaske. Sun kuma nuna nadamarsu tun a wancan lokacin dan har Lagos ɗin sunzo nemanta rashin ina zasu kama yasa suka haƙura suka koma. Hatta gadonmu da aka raba da sunan Falaq a ciki, sun kuma tabbatar da yana nan ajiye basu ci ba. Wannan magana ta karyarwa Abba zuciya ya hau sharar hawaye shima. Haka ya shiga bamu haƙuri har Yaya Musaddiq da Maash ya kira a waya video call tun fara zaman. Yanda yake kuka yana faɗa mana wlhy duk Mom ce take cewa su sayar tunda shike wahala da mu, ko yaso bijire mata baya iyawa, wani lokacin sai sun ɗaga abu sun sayar ta dawo yayta kuka da ga baya a ɓoye. Baya jin daɗin abinda ke faruwa da mu a gidan musamman ma ni, amma bai san miyyasa

baya iya tsawatar mata ba. Shi kansa yasan an zalunceni fiye da kowa a cikinmu, dan badan tsarewar UBANGIJI ba da kuma tsayawar Yaya Musaddiq akan tarbiyyata dana lalace kamar yanda Mom taso, sai dai shi ALLAH ba'ai masa dole, a ƙarshe dai gashi nan komai yana neman juyewa a kansu. Yanzu haka ba'a san inda Baby take ba. Sun je har dangin mijin nata satin da ya wuce suka musu korar kare akan sanda akai auren ai basu sani ba. Suje can su nema yaɗar su suma tuni sun fidda mijin nata a cikin jerin yaɗayansu. Ashe sauran matansa ma dake tare da shi zaman yaɗayansu kawai suke yi tuni an raba aurensu tun sanda yayma amaryarsa fyaɗe ta baya ta tona masa asiri. Shine ya gudu yabar ƙasar, daga baya ya dawo ya auri Baby bada saninsu ba. Ƴan uwansa tsiraru da aka gani wajen bikin nasu na binsa ne saboda kwaɗayin abin duniya. Wannan al'amari ya ɗaga mana hankali. Yanzu haka Jalilah na asibiti yau kwana biyu kenan. Ga Abbas sun daki wani yaro a makaranta babansa babban mutum ne yasa an kamasu an rufe yau kwana biyar kenan shima. Munyi yawon bashi haƙuri babu adadi yaƙi sauraren mu ni da sauran iyayen yaran...” kuka ya sarƙe Abba. Daga ni har Hafizzullah da Yaya Musaddiq kukan muke muma. Yayinda gurin kowa yay tsitt, sai ma Ummie ce ke lallashin Hafizzullah dake kusa da ita da Fahad. Niko ina jikin Gwaggo ne da itama ke kukan. Hakama Falaq kuka take sosai ganin muna kuka.

Maash ne cikin ƙarfin hali yay gyaran murya. Duk kallonsa mukai, cikin dakewar nan tasa ya furta, “Inaga kukan ba shine mafita ba. Addu'a ne kawai. Sannan in babu damuwa ina son sanin sunan shi mutumin dake tare da yarinyar”.

Cikin kuka da zabura Abba ya faɗa masa. Kansa kawai ya jinjina yana miƙewa. Sai da yay ɗan taku biyu a hankali ya furta, “Sai da safen ku”. Daga haka ya haye sama. Da kallo duk muka bisa. Sai da ya ɓacema ganinmu Sheikh Muhammad ya ce, “Abubuwa sun masa yawa. Zuciyar ce kawai a tsaye. Inaga muma ya kamata duk muyi haƙuri mubar komai zuwa safiyar gobe idan ALLAH ya kaimu. Dan ita kanta mahaifiyarsa likitocinta sunzo ganinta. Muma kuma muna buƙatar hutu. Ɗiyata tashi kije ga mijinki kinji”. Ya ƙare maganar yana nuni da ni. Ji nai kamar na nutse a wajen dan kunya. Sai da Gwaggo ta miƙar da ni. Sum-sum na wuce zan tafi Mama Balki Sarkin ƙarfin hali ta dakatar da ni. Kwandon data shirya abincin Maash ɗin ta bani, haka na amsa babu musu na haura saman nima da ƙyar. Na jima tsaye a bakin ƙofar batare da nasan miya kamata nayi ba. Komai da kowa tausayi suke ban a gidan. Hatta ni kaina tausayin kaina nake ji da kaina. Kusan mintuna biyu sannan nai ƙarfin halin buɗe ƙofar na shiga da sallama a bakina.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_

Typing□

Typing□

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-three

_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai..... Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers _.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....A kwance na sameshi rai-rai saman kujera idanunsa a lumshe hannunsa dafe da kansa. Ƙafarsa ɗaya a ƙasa ɗayar a saman kujerar ya ɗan dogareta. Har na ajiye basket ɗin saman table na ƙarasa gabansa bai ko motsa ba. Babu alamar ma yasan da shigowata, dan kallo ɗaya zaka masa kasan ya mutaƙar yin nisa a cikin tunani. Gwiyawuna na kai durƙushe ƙasan carpet ɗin saitin inda fuskarsa take. Idanu na zubama ƙaramin pinkish lips ɗinsa da suka bushe na wasu sakanni. Kafin a hankali na kai hannuna saman nashi daya sa a kansa na janye. Har lokacin bai buɗe idanunsa ba, sai na ƙara jin gaba ɗaya zuciyata ta karaya. Mutum mai kaarfin hali irin Ya Awwab kaga yanayinsa ya canja haka ai ba ƙaramin abu bane ba. Bance da shi komai ba na ɗaura hannuna akan botiran shirt ɗinsa na fara ɓallesu. Har sai da na gama duka kafin na miƙe, saman jikin nasa na haye na kwanta gaba ɗayana na kwantar da kaina a ƙirjinsa. Sai kawai na saki masa kuka, dan jina a jikin nasa sai naji wani irin raunin zuciya ya sake mamayeni. Komai daya faru a ɗazun da yanzu ya zame min kamar yanzu-yanzu yake kan faruwa.

Nafi minti ɗaya a hakan batare daya tanka min ba kafin naji saukar hannayensa a saman bayana. A hankali muryarsa can ƙasan maƙoshi sosai ya furta, “Miya faru kuma?”.

Sai kawai na sake ƙanƙamesa nima, a hankali na furta, “Nayi kewarka”.

Rungumeni ya sake yi da ƙyau shima yana wani jan nannauyan numfashi da busa min iskar cikin kunnena. Yanzu kam mun ɗauki tsawon lokaci a hakan da har mu kammu bamu san adadi ba, har na daina kukan na koma jan ajiyar zuciya kamar yanda shima yake yi. Muryata acan ƙasan maƙoshi na furta, “My Hot”.

“Uhhyim”.

Ya amsa min shima a ƙasan maƙoshin. Kaina na ɗago ina kallonsa. Idanunsa dake lumshe na shafa kaɗan. Sai ya shiga buɗesu a hankalin. Har cikin raina sai da naji

tsoron ganin yanda suka canja, sai nai ƙoƙarin rissinar da nawan ina sauke ajiyar zuciya. Haɓata ya kamo ya maido da fuskar tawa, dole na sake kallonsa cikin idon. Alama yay min cikin yanayin ɗan ɗage kai da gira. Sai kawai na sake marairaice masa fuska zan saki kukan. Kansa ya girgiza min yana lumshe ido alamar kar nayi. Baki na taɓe hawayen na sakkowa da gudu. Sake rungumesa nayi na sakar masa shi.

Motsawar ƙirjinsa naji kaɗan, sai kuma hannunsa daya tura a cikin gashina. A cikin kunnena ya furta, “Ni dai kar a haifa min yarinya mai saurin kuka”. A yanda yay maganar ne ya sani fara kai masa yʻan ƙananun duka, sai yay ƙoƙarin riƙe hannun nawa yana murmushi. Daga haka ya tashi zaune da ni a jikin nasa. Bathroom ya kaini, da taimakonsa mukai wanka muka fito. Mu duka mukai shafa'i da wutri. Ganin ya ɗauki Alkur'ani ya hau karatu nima sai kawai nayi amfani dana wayarsa. Sosai yin karatun Alqur'anin ya kawo mana sauƙi a zukatanmu. Harna ɗan samu ya sha tea da abincin Mama balki lauma kusan biyar. Nima na ɗan ci, da ga haka ya ɗan zauna dube-dubensa a laptop wanda nasan kawai yana yine badan hankalinsa na a wajen ba. Ni dai dake kwance a jikinsa tun ina kallonsa har barci ya ɗaukeni ban san sanda ya gama ta kwanta ba...

Washe gari na tashi da zazzaɓina kamar yanda na saba. Nai yʻan amaye-amayena ya dai taimaka min nayi wanka na kwanta sai barci. Lokacin da nake farkawa rana ta ɗaga. Haka na kimtsa na fito neman abinci dan yunwa nake ji. Shi ko da'alama ma ya jima da barin gidan. Ina sakkowa su Ummie na shigowa da Mama Balki da Fahad sai Hafizzullah. Ashe daga asibiti suke duba jikin Paah da su Baba prof. Jikin Arwa dai kam babu daɗi, dan yarinyar nata aman jini. Wai da safen nan Commondo yake ta roƙon a kaisa ya dubata ta ganshi ya ganta koda sau ɗaya ne matsayin mahaifinta. Abin ƙaddara anama shirin sallamarta dan tun dare ta dawo hayyacinta ita sai kuka data kwana yi kawai. Tana yin ido huɗu da Commondo ɗin babu wanda ya lura ta finciki almakashin hannun nurse ɗin dake canja mata bandage ɗin goshinta sakamakon faɗuwar da tayi a jiya taji ciwo a wajen kawai ta cakamasa a gefen wuya. Kʻoƙarin riƙeta akeyi amma ina sake zarewa take tana caka masa tana kuka da yimusu ALLAH ya isa shi da uwarta. Da kyʻar aka iya riƙeta aka ƙwace almakashin, shine kawai ta hau tari sai aman jini, yayinda aka kwashi Commondo zuwa taimakon gaggawa rai a hannun ALLAH. Shine fa akai kiran Maash ya tafi asibitin shi da su Ummie hankali tashe. Yanzu dai haka Commondo sakamakon abinda Arwan ta caka masa wata jijiyarsa ta tsinke. Ita kuma da ƙyar aka shawo kan aman jinin da take yi suka sakata barci. Baba prof kuwa tun a daren jiya allurar da Hajiya ƙarama ta masa ta fara nuna kanta. A yanzu haka daga ƙafarsa zuwa ƙugu duk sun sandare sun daina aiki. Dama Allurar bata mutuwa bace. Zata sabdarar da mutum ne ya zama babu inda ke motsi a tare da shi sai kansa kawai. Da yake gaɓa-gaɓa take bi yanzu haka ta sandarar da ƙafafun zuwa ƙugunsa. Itama Hajiya ƙarama data farka a barcin da suka sakata tana jin abinda Arwa taiwa mahaifinta ta sake rikitowa a gado batun da ake paralysis dai ta tabbata

gareta bayan abinda Baba prof ya shayar da ita da bai fara nuna kansa ba dai ita. Al'amarin dai babu daɗin ji sam.

Yʼan suna kam dama yau duk suka kama ganansu da safe. Yʼan Kano ne kawai dake shirin wucewa gobe idan ALLAH ya kaimu suma. Naso nace zan bisu, na dai daure saboda halin da gidan ke'a ciki. Ummie ta musu alƙawarin in sha ALLAHU da zarar Falaq tayi arba'in ita da kanta zata ɗaukemu da su Maash duka muje garesu dangi suga Falaq su kuma ga mazajenmu suma mazajen namu suga dangin namu. Gwaggo Gudidi taji daɗin hakan, tace maybe ma sannan Halime amaryar Abba ta haihu dan cikinta ya fara tsufa. Jin hakan Ummie tace to shikenan hakan ma yayi kawai. Suma dai washe gari suka wuce gida ya koma da ga mu sai mu.

Hajiya Mammah dai wasan ɓuya take da kowa. Garama Hajiya Mama ta shigo sun gaisa da yʼan Kano har sau biyu. Yau kuma dana tashi jikina babu daɗi sosai dan har ruwa sai da aka sanya min shima ta shigo ta dubani. Sai dai daka ganta kasan bata cikin walwalarta. Duk ta zube a kwana uku kacal idanunta a kukkubure alamar taci kuka sosai. Bama su kaɗai ba mu kammu kowa ya kallemu yasan dauriya ce kawai, shiyyasa ko tattauna zancen abinda ya ke faruwar kowa ya kasa zama yayi da ɗan uwansa. Ga yʼan jarida na damunmu sai dai kowa yaƙi cewa komai a gidan dan uban gayyar bai kula ba. Ya Awwab ɗin ma kwata-kwata ya daina yini a gidan. Sai a yau ɗin da bani da lafiya daya kasance dani na fahimci shima bashi da lafiyar. Dan zuwa yamma duk dauriyarsa sai da ya kai kwance dai. Dole hayatu yazo masa da likitansa. ALLAH sarki Ummie duk ta damu. Shawara da likitansa ya bada akan ya kamata ya samu hutu gaskiya, idan dama hali yay nesa da ƙasar kona ɗan wata ɗaya ne dan jininsa ya hau sama sosai, har yanama zuciyarsa barazana. Hankalinmu ya tashi matuƙa. Duk da yace shi babu inda zai je bamu bi takansa ba Hayatu ya fara shirye-shirye bayan sun tattauna da Uncle Abdullahi. Ɗari bisa ɗari Uncle Abdullahi ya bada shawarar gaba ɗayanmu ya kamata mu wuce ɗin, batun Paah kuma a barshi a hannunsa dan yanzu kunya da tashin hankalin abinda Baba prof ya aikata ma Ummie da iyayenmu da wanda shima ya aikata yasa hatta da shi kansa ƙarfin hali kawai yake na fuskantar gidan. Amma idan akai ɗan nesa da juna zukata suka huta koba komai a tattauna wasu abubuwan. Da wannan shawarar Hayat da Ummie suka amince, cikin ƙanƙanin lokaci akai duk abinda ya dace musamman ga ni da Hafizzullah da Bahijja da Ummie ta amshe da bamu taɓa ƙetare ƙasar ba. Mama da Falaq da su sauran hakan ba komai bane. Haka kuwa akayi sati biyu ciff da faruwar komai muka ɗage zuwa ƙasar Spain kamar yanda Ummie ta buƙata, dan tana son kaima kufan mahaifinta ziyara, inda itama idan za'ace inane tushenta dole tace can ƙasar dan ba'a ado da ƙasar mahaifiya. Naso ace munje asibiti kafin mu wuce. Amma Uncle Abdullahi ya hana hakan. Hajiya Mammah ma bata yarda mun ganta ba. Ita ko Hajiya Mama dama ta koma a satin daya gabata.....✍

Ku ƙara hakuri dani dai kunji bayin ALLAH, ni kaina bana gane kaina saboda rikicin gidan Yayanmu maash😂😂😂.

Barka da juma'a. Ina fatan kowa na lafiya. Fataken dare ga shi nan na baki ƙyauta

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

Typing□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-four

.....A randa suka wuce a ranar mahaifin su Azizat tsohon mijin Hajiya Mammah ya iso Nigeria shima. Ya zo da buƙatar amsar yaransa. Hankalin Hajiya Mammah yay matuƙar tashi, taita roƙonsa amma sai buɗar bakin Azizat ɗin da ƙanwarta sukace su gaskiya mahaifinsu zasu bi. Dama tunda abin nan ya faru suka koma sashen Uncle Abdullahi. Damuwa da kukan da suke sha ya sakasu shiga kamar a halin depression. ALLAH sarki ɗan uwa rabin jiki, sai Malika ce ke ƙoƙarin kwantar musu da hankali ita da mahaifiyarta. Ganin yanda suka tubure zasu bi mahaifinsu yasa dole Hajiya Mammah ta sallama. Tana ji tana gani suka tattara kaf kayansu suka bisa zuwa ƙasarsu, ko kallonta basuyi ba sai itace ke famar kuka.

Bayan wucewarsu washe gari itama Maman Malika ta bama Uncle Abdullahi shawarar barin Mansion su koma nasu gida tunda aikinsa ya ƙare. Ta kuma bashi haƙuri bisa zargi data dinga masa da magana mara daɗi akan hakan. Dan sunsha

tafka rigima akan dawowarsu Mansion batare da kowa ya sani ba. Saboda ita sam ba'a san ranta suka dawo ba a lokacin, sai dai da yake yafi ƙarfinta dole ta haƙura ta sallama ashe shi da tasa manufa.

ALLAH sarki rayuwa, duk abinda ya sakaka dariya watarana sai ya saka ka kuka. Hakama wanda ya sakaka kuka zai iya sakaka dariya watarana. Yau ga Hajiya Mammah dake so da burin mulkar Mansion ita kaɗai ƙwallin ƙwal a cikinsa. Sai securitys da aka bari da wasu tsirarun ma'aikata maza. Amma kaf masu aikin nan mata sai da Uncle Abdullahi ya sada kowa da iyayensa da alkairi mai tsoka daga Ummie. Kuka sosai Hajiya Mammah tayi a wannan rana, ta dinga zagaya gida tana sambatu da surkulle kamar wadda ta zare. Kwana biyu dai ta fahimci kanta na neman kwancewa ta tattara itama ta nufi tsohon gidansu na gado inda Baba prof yake rayuwa, tunda shi bai kai ko kaso ɗaya bisa goman girman Mansion ba. Nan ɗin ma dai ba daɗin take ji ba sam. Dan kowa ya watse babu masu aiki ko ɗaya a cikinsa hatta maigadi ma. Ga jami'an tsaro sunma gida kaca-kaca saboda bincike. Haka dai ta raɓa ta zauna dan babu yanda zatayi. Idan ma tace zata bar nan ɗin ina zata je? Ita dai yan kuɗaɗen da take samu dama kullum cikin fallasar dasu take da lissafin ai Azizat zata auri Awwab su mallake dukiya. Shiyyasa ɗan abinda take da shi yanzu bawani ya taka kara ya karya bane ba. Dukiyar dake tsakanin Mansion da nan kuwa karo na farko a rayuwarta taji ko tsinke bazata iya taɓawa ba dan ba nata bane ba. Tana matuƙar jin kunyar tace zata koma gidan Uncle Abdullahi kuma kodan cin kashin data dinga ma matarsa da shi kansa. Saboda ita dama ba kowa ta ƙyale ba ko sanda suna Mansion.

Tsanantar da jikin Paah yay ya saka Uncle Abdullahi zuwa ya sameta kan ko zataje tai jiyyarsa. Dan shi gaskiya yana matuƙar jin kunyar sanarma su Awwab halin da yake ciki. Balle ma shima Awwab ɗin yana can yana fama da jiyya. Ita kuma Ummue doctors na ƙara treatment ɗin ta yanda ya kamata. Batayi ko jayayya ba ta amsa masa. Haka ta shirya ya ɗauke ta ya kai asibiti batare da sun iya cema junansu komai ba. Dan su a karan kansu ma shakkar tada zancen abinda ya faru sukeyi. Sun fara shiga suka duba Hajiya Ƙarama da ɓarin jiki ke a shanye, sai Arwa da itama ke a kusa da ɗakinta yarinyar na cikin matsanancin depression abin tausayi. Sai Baba prof da komai baya motsi a jikinsa sai kai da idanu, ɗaki ɗaya suke shi da Commondo da Arwa ta tsinkema jijiya shima dai gashi nan ne kawai kwance sai idanun. A yanzu su duka huɗun suna a ƙarƙashin kulawar jami'an tsaro ne. Su asibiti ke kula da komai nasu shiyyasa ba'a buƙatar masu jiyya. Sai Paah ɗin ne kawai, amma duk da haka Uncle Abdullahi yana raba lokacinsa a tsakaninsu musamman Paah da Baba prof ɗin da suka zame masa dole...

□□□□□

A ɓangaren su Abba kam tunda suka isa gida Abba yayma Mom bayanin Maash ya amshi sunan mijin Baby yace zai bincika ta ɗan fara samuwa. Duk da dai a ƙasan ranta tana jin wani iri, dan koba komai dai Maash ɗin nan mijin Samraah ne. Yarinyar data ɗauka ba komai ba. Koda yake miye ma na ɓatama kanta rai, tasan dai matsayi irin na Maash da dukiyarsa mizaiyi da ita. Ƙilama ko ganinsa batayi balle ya mata kallon macen aurensa. Wannan batu na zuciyarta ta sata samun sassauci. A washe gari aka sallamosu asibiti. Suna zaune ita da Ummanta da Bibaa a falo Halime dake fama da ƙaton cikinta ta shigo tana ɗan hakki. Yanda cikin nata yay girma dole kayi mamakin kamar ba cikin fari ba. Da ga tsayen ta gaishesu da yima Mom ɗin yaya jiki dan bata iya zama sai da taimakon wani. Umma ce kawai ta amsa mata. Mom kam bama ta kalleta ba, yayinda Bibaa taja tsaki ta tashi ta bar falon. Ita kaɗai tasan zafi da raɗaɗin da take ji a zuciyarta a duk sanda ta kalla cikin yarinyar nan. Babu abinda basuyi dan ya zube ba amma ko gezau. Babu komai ai yanzu sun samo abinda zai musu maganinta. Dan teacher ɗinta ya tabbatar mata tayi ƙoƙari ta samo mahaifar Halimen a randa ta haihu. Shiyyasa yanzu ranar haihuwar kawai suke jira.

Halime da yanzu ita abinda ma ya isheta shine ya isheta tana gama gaishesu ta fito abinta. Ɗakinta ta koma inda Abba ke jiranta dan yana gidan shima. Yau kuma ranar girkinta ne. Kamata yay ta zauna yana mata sannu. Cike da shagwaɓa ta amsa masa tana miƙa masa ƙafarta da tayi fushi. Amsa yay yana danna mata a hankali suna yɑr hirarsu. Hirar data saka Abban kwasar dariya dan Halimen nata zuba masa shirmen turancinta ne data dage tana koyo. Duk da ma dai a tsakanin nan makarantar ta gagareta saboda bata jin daɗi...

Kullum sai Abba yayi waya dasu Samraah yanzu. Ƙoƙarin jawosu jikinsa yake yi domin ya kwaranye abinda ya cusa musu a baya. Su kuma sun saki jiki da shi da alama sun jima suna buƙatar hakan daga garesa amma ya gagara musu. Har dai ranar da su Samraah zasu wuce Spain Mom bata sani ba. Dan Abba ya daina sanar mata komai daya shafesu. Idan ma shawara yake nema Halime ce. Saboda zai iya cewa itace ta dawo dashi kan hanya akan batun su Samraah ɗin. Tunda ta fahimci komai kullum cikin masa nasiha take kamar ba yarinya ƙarama ba. Tun yana fushi da ganin ta shiga hurumin daba nata ba har ya fara fahimtarta. Sannu a hankali ya fahimci kuskuren da take ƙoƙarin nuna masa. Shiyyasa yanzu wani bala'in ƙara son yarinyar yake. Gata dai da ƙarancin shekaru sai hankali da sanin ya kamata. Fatansa dai ALLAH ya sauketa lafiya....

□□□□□

“Wai yaushe ne batun tafiya Lagos ɗin nan Daddyn Attahiru. Tunda abubuwa sun lafa inaga ya kamata muje muyima bawan ALLAHn nan godiya. Na kuma sake

neman gafararsa akan kuskuren dana tafka. Wlhy gaba ɗaya ko'a zuciyata na tuna kunyar kaina da kaina nake ji”.

Murmushi Dad dake zaune idonsa a television yayi, sai kuma ya ɗan kalla Mamyn tare da amsar kofin black tea ɗin da take miƙo masa. Sai da ya kai shayin bakinsa ya ɗan sha sannan ya sauke numfashi. “Karki damu zamuje, sai dai tama ƙara tsayi. Dan yau dana bincika ake sanar min shi da iyalinsa da mahaifiyar tasa duk sun wuce Spain. Dole muyi haƙuri har ALLAH yay musu dawowa.”

“Tofa, ba kwana biyu daya wuce kake cemin kun gama magana da PA ɗin nasa ba zamu je a satin nan ba. Yaya akai hakan to?”.

“Kin san manyan nan barin ƙasa tamkar zuwa bayi ne su fito suka maidashi. Balle shi Maash dake da jiragen kansa ma. Haka dai zamuyi haƙurin har ALLAH ya maidosu lafiya. Yanzu yaya batun shi Mansoor ɗin? Kin tuntuɓesa akan batun yarinyar nan ya amince? Dan so nake a haɗe bikin nan dana ɗan uwansa kawai a wuce wajen kowama ya huta naji da yarana mata suma”.

Murmushi mai ƙayatarwa Mamy tayi, muryarta a sanyaye ta ce, “Ni kasan har yanzu baya wani sakin jiki da ni. Daga gaisuwa dai shike nan. Amma Attahir yace min yaga suna waya sosai da ita. Har yana cemata a weekend ɗin nan zai sake shiga Maidugurin su gaisa. Kaga kuwa idan bai amsheta ba ai bazai ce zai koma gidansu ba bayan zuwan da mukayi muduka ko”.

“Eh gaskiya hakanne kam. ALLAH to ya ƙara daidaitasu. Haka zamu cigaba da masa addu'a ALLAH ya cire masa son ita waccan yarinyar. Dan ta masa nisa sosai sai dai haƙuri kawai. ALLAH kuma ya bamu ikon gyara kurakuranmu baki ɗaya”.

“Amin” Mamy ta amsa muryarta na sake rauni. A haka Attahir da Mansoor suka shigo falon. Da alama daga wani wajen suke a taren. Kowannensu ledar hannunsa ya ajiye. Kafin su gaida iyayen nasu. Da kulawa suka amsa musu, Attahir ya cigaba da faɗin, “ALLAH duk mun gaji. Yanzu ni da ɗan gata ne Mamy sai ki bani shayin nan na Dad mai zafi nasha na more. Amma nasan ba'a sha miki shayin miji”.

Dariya Dad da Mamy sukayi saboda yanda Attahir ɗin ya ƙare maganar abin tausayi. Yayinda Mansoor yay ɗan murmushi kawai dan yanzu ya koya miskilanci. Kofi Mamy ta ɗauka ta saka masa shayin tana faɗin, “A'a babana ai sai na baka. Nasan mika sayo min nima. Ai ba'a hana mai badawa. Man kaima zaka sha ko?”.

Ta maida hankalinta akan Mansoor. Kai kawai ya girgiza mata alamar a'a. Sai ma ya yunƙura zai tashi Attahir ya kamasa ya maida yana hararsa. Badan yaso ba ya koma ya zauna yana sauke ajiyar zuciya. Cikin tsaresa da ido Attahir ya ce, “Yaya mukai da kai ne?”.

Kai Mansoor ya ɗan sosa, sai kuma ya haɗe hannayensa biyu alamar ban haƙuri. Murya a karye ya ce, “In sha ALLAH zan gyara kayi haƙuri”.

Kai kawai Attahir ɗin ya jinjina masa, shi kuma ya maida hankalinsa ga Mamy murya a sanyaye ya ce, “Mamy zan sha”. Murmushi ta sakar masa idanunta na cika da ƙwalla. Haka ta zuba musu kowa ta bashi cike da kulawa. Daga haka suka cigaba da hira. Tun Mansoor na jefa ɗaɗɗaya har dai ya fara sakin jiki. Harma hirar ta koma fannin shirin auren Attahir, daga haka shima Dad ya takalo masa nasa batun da Salimah. Da farko ya ɗan nuna shi ba sonta yake ba, sai da suka dinga masa nasiha da lallashi sannan yace zai ƙara nazari. Abinda ya yanke zai sanarma Attahir. Sun jin daɗin hakan, suka kuma bisu da addu'a su duka.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-five

Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....Isowar mu ƙasar Spain bata zame mana cikin daɗin rai ba. Dan daga airport ma asibiti aka wuce da Maash. Abu kamar wasa ashe dai ciwo ke cinsa sosai yana dannewa. Sai ɗan jigatar tafiyar nan ta sake ruɓu-ruɓu da shi. Koni mai fama da ciki ban kaisa takwarkwashewa ba. Duk da nima dai sai da suka bani gado ba wasu awwani. Bayan komai ya dai-daita muka wuce gida aka barsa nan dan dokarsu babu mai jiyya. Dan nima ina buƙatar nutsuwar. Gida ne a cikin estate da ya amsa sunansa gida. Gida na farko muka shiga, hakan ya sakani sauke ajiyar zuciya, dan in ba haka ba wannan ai sai ka rikice saboda ginin duk iri ɗaya ne ya tafi reras abin sha'awa. Yay min ƙyau da tsari sosai. Katon falone a farko sai gefen haggu da dama daya zama gidan kamar wani sashe biyu. Sai upstairs. Mun sami masu aiki biyu, mace da namiji, cikin girmamawa suke mana sannu da zuwa. Kafin su mana bayanin tsarin gidan. A take Hayatu yace ni na wuce sama, dan nan ne ɗakin Maash yake. Sai Ummie da dama tana da ɗakinta itama dan sun ɗan taɓa zaman jiyyarta anan ama lokacin ne Maash ɗin ya sai gidan. Itama ya rakata nata a side na hannun dama dake dauke da bedrooms huɗu, sama biyu, ƙasa biyu. Ita zata zauna a saman ne, ɗayan ɗakin kusa da ita tace Falaq ta zauna nan ita da Bahijja, dan tace cikakken wankan jego zata fara mata ta gaji da wannan gantallen jego nata kadama Ya Hayat ya saka ran zata bashi yanzu. Dariya muka saka sosai yayinda Hayat ke

faman shafa ƙeya. Ɗakunan ƙasa kuma Mama Balki da Baba suma aka basu. Sai Fahad da Hafizzullah suma a side na haggun aka basu sama. Hayat kuma ɗakunan ƙasa koda dai Ummie ta bashi yar matarsa ga inda zai fake nan. Hakan yayi sosai. Dan haka babu wanda yaja zancen kowa ya tafi inda aka bashi.

Sosai saman yay min ƙyau da ƙyatar da ni. Falo ne madaidaici sai bedroom guda ɗaya tal. Babu kuma ta inda muke da alaƙa da side ɗin bedrooms ɗin su Ummie da nasu Fahad. Komai tsaf yake kuma fari tas kamar kaci. Na dai samu nayi wanka na kwanta dan barci ne a idona sosai. Dama kuma likitocin sun ce a barni na huta sosai. Ban samu nutsuwar fahimtar gidan yanda ya kamata ba sai washe gari. Alhamdullah na tashi jikina yay daɗi ba kamar jiya ba. Sai kuma kewar mijina da son zuwa na ganshi amma ina jin kunya. Haka dai na daure a munafunce na tambayi Yaya Hayat. Shine yace na kwantar da hankalina zuwa anjima zai kaimu mu gansa. Naji daɗin hakan. Haka kuwa akai zuwa yamma muka je muka dubashi, yanama barci. Haka muka sakance kullum muna zuwa mu dubashi, wataran yana ido biyu wataran barci. Randa yake ido biyu ya dage nice zan masa komai, babu yanda na iya haka nake yi ina jin kunya har mu taho. Satinsa ɗaya aka sallamesa ya taho gida shima, dan ya matsa likitocin su sallamesa kin san ya tsani zaman asibiti. Murmushi kawai na ɗanyi lokacin da Hayatu ke sanarma Ummie ina mai jin daɗi a raina. Nima nafi son ya dawo gidan na bashi kulawa da kaina ai. Kamar ko yanda Hayatu ya faɗa da yamma sai gasu da shi. Kowa ya nuna farin cikin ganinsa. Bayan sun gaisa da su Ummie muma muka gaisheshi da masa yaya jiki. Da kai kawai yake amsa mana kafin ya tashi ya haura sama. Kasa tashi nayi dan kunyar idon su Ummie sai da Mama Balki tamin wayon maya tace na tashi ga abincinsa can an shirya na kai masa.

A bakin gado na samesa zaune ya zubama ƙofar ido kamar dama ni yake dakon shigowa. Ina shigowar ya wani ɗan lumshe idanunsa da sake buɗesu a kaina. Hannu ya miƙa min alamar nazo garesa. Banyi musu ba kuwa. Saman cinyarsa ya ɗaurani tare da rungumeni muka dinga sakin ajiyar zuciya. Mun jima a haka sannan cikin raɗa nace masa, “Yaya jikin?”.

Maimakon amsa min sai ya ɗagoni yana kallon fuskata. Tare da kai babban yatsarsa saman lips ɗina ya ɗan shafa. Idanuna na lumshe a hankali, dan yanda yake zagaya yatsar tashi sai nake jin tsigar jikina na tashi. Saukar hannunsa saman cikina ya sani buɗe idon. Muryarsa a ɗashe ya furta, “Yaya little Ummu-Hidaya?”.

“Tana lafiya, tare da yima Abbunta addu'ar samun lafiya mai ɗorewa. Ta yi kewarsa kuma matuƙa”.

Wani ɗan langaɓar da kai yayi gefe yana sake ƙanƙance idanu. Jinai sam bazan iya jurar kallon ba na faɗa jikinsa kawai na ƙanƙamesa tare da haɗe lips ɗinmu waje ɗaya....

Rayuwa a Spain wata irin rayuwace da kowa a cikinmu bazai manta da ita ba. Dan mun haɗu ne mun gina wani farin ciki a zukatan junanmu da har abada bazamu manta ba. Idan ka gammu bazaka taɓa ɗauka mu ba jini ɗaya bane. Mama da Ummie sun zama iyaye. Baba ya zama Uba. Maash da Hayat sun zama manyan yayye. Fahad da Hafizzullah sun zama garkuwa. Mukam ƙanne masu matuƙar biyayya gana gaba dasu. A cikin ɗakin mijina kam ni da shi sai sambarka da alhmdllh. Dan dukkan wata soyayya da kulawa ina samu daga garesa harma wadda banyi zato da tsmani ba. Hafizzullah da Bahijja sun koma makaranta. Yayinda Fahad aka fara shiga harkokin Bussines shima. Yaya Musaddiq yazo mana hutun sati ɗaya. Na shiga matuƙar farin ciki da wannan ziyara ni da yan uwana da su Ummie duka. A wannan zama ne Ummie ta bamu takardun Company da Abie ya bada a bamu. Munyi kuka munyi godiya sosai. Mun kuma tattauna abubuwa masu yawa da suka jima suna damun kowannenmu. Bayan wucewar Yaya Musaddiq Falaq ta koma ɗakin mijinta dan tayi arba'in. Little Awwab nata wayo Masha ALLAH. Ya Awwab ma jikinsa yayi sauƙi sosai. Kamar yanda Ummie ke sake samun lafiya yanda ya kamata. Dan yanzu haka itama zata fara cigaba da kula da wasu harkokin Bussines ɗin ne anan. Saboda Maash da Hayatu sun koma gantalinsu na ƙasashe. Har Nigeria ashe suna kaɗawa idan ta kama. Sai dai basu taɓa sanar mana ba. Cikina ya fara fitowa ɗan kif da shi, sai dai kunya tasa kullum bana rabo da hijjab in har zan sakko ƙasa wajen su Ummie, ko na saka riga mai burun-burun da ba'a ganewa.

A hankali soyayya da shaƙuwa ta fara shiga tsakanin Fahad da Bahijja. Wannan abu yama kowa daɗi, sai dai ita Bahijja na dojewa saboda kunya. Ni da Aunty Falaq muna sake fanfata kuwa. A haka Jaga shima yazo yay mana hutu na sati biyu ya koma Saudiyya. Bayan wucewarsa bai fi da sati uku ba Abba ya kira yake sanar mana Amaryarsa ta haihu yan biyu duk maza. Murna sosai muka dinga yi dan mun san lokacin zuwa Nigeria yayi kamar yanda Yaya Awwab yay mana alƙawari. Gashi a ɗan tsakanin shima Yaya Musaddiq zai je ya musu hutun sati biyu. Sai abin ya sake mana dai-dai. Ganin har ana saura kwana uku suna babu Maash babu alamarsa a Spain jikinmu ya fara sanyi. Idan muna waya ko video call nai masa batun tafiyar kuma baya cewa komai sai ya basar ma. Dana fahimci hakan sai na daina masa batun gaba ɗaya. Mun daiyi ɗan gyare-gyaren muna jiran ikon ALLAH. Sai ana gobe suna da safe suka iso Spain shi da Hayat da Fahad. Munyi farin cikin dawowar tasu, amma harga ALLAH na fidda ran zuwanmu Nigeria a lokacin kam. Amma mi sai kawai yace mu shirya jirginmu zai tashi washe gari zuwa Nigeria. Tsabar farin ciki bamma san na rungumeshi agaban Ummie da Mama Balki ba harda manna masa sumba a lips. Sai da naji Hafizzullah da Fahad na dariyar shaƙiyanci sannan na farga. Ai da gudu na sakesa na bar wajen. Ummie na kirana cikin dariya ban waigo ba.

Har ta gama haye stairs ɗin yana tsaye a inda ta barshi, ta kuma gefen ido yake kallonta. Ba yau ta saba rungumeshin ba. Sai dai koda kwatance bata taɓa yi a gaban Ummie ba. Sai ma idan shi yaso yin hakan ta doje. Jiyay gaba ɗaya ta saukar masa da kasala. Karo na farko sai yaji nauyi da kunyar Ummie da Mama Balki.

Amma sai ya dake abinsa yama cema Hafizzullah ya bashi coffee. Tashi Fahad yay yabi Hafizzullah kitchen ɗin, sai da suka gama iya shegensu wai yayan nasu na borin kunya sannan suka kawo masa coffee ɗin. Yana amsa ya miƙe ya haura sama da shi a hannu. Ai ko suka gimtse bakuna suna dariya sai da Mama Balki ta korasu sashensu. Shigowarsa dai-dai da fitowata wanka. Dan ina shigowa bathroom na wuce dama. Alhamdullah yanzu kam laulayi yayi sauƙi sosai, dan tunda na shiga wata na shidan nan kam sai dai kwaɗayi da ciye-ciye nake. Amma ciwo-ciwon nan da jinin da nake gani duk wata kaɗan-kaɗan duk sun bari. Sai kuma ƙulafucin miji abin har kunya yake sakani. Yanda yake bina da kallon ƙurilla yasa na tura masa baki da kauda nawa idon a kansa.

Murmushi ya saki kaɗan da laluba aljihunsa ya fiddo min chocolate ɗaya da indai yana gari ko yay tafiya ne ma zai shigo sai ya shigo min da ita. Bamma san nima nayi murmushin ba da nufosa. Kofin hannunsa ya ajiye yana mai ware min hannayensa duk biyu. Shigewa nai jikin nasa ya ɗagani cak yana juyi dani. Dariya na shiga yi ina ƙanƙamesa da faɗin, “Wayyo My Hot juwa. Juwa my Hot ka bari”.

Saman gadon ya sauke ni tare da rungumeni da ƙyau shima yana murmushi. Nima ina ƙanƙame da shi ina faman sauke ajiyar zuciya. Daga haka lissafin ya canja. Tako wane fanni cikin nan baya hanani bashi dukkan kulawar data dace a zahirin rayuwa da shimfiɗarsa. Hakan ke ƙara saka shaƙuwa ta musamman a tsakaninmu da soyayya mai ƙarfi duk da har yanzu daga ni har shi babu wanda ya taɓa furtama ɗan uwansa kalmar (I love you) sai dai a aikace. Hakan kuma ya gamsar da mu ya kuma wadatar. Dan soyayya a baki ba'itace soyayya ba. Soyayya ta gaskiya ma ta wuce batun faɗi da bakin ai sai dai lokaci da yanayi su tabbatar....

WASHE GARI kamar yanda ya faɗa jirginmu ya wulla zuwa ƙasarmu ta haihuwa bayan barinta kusan watanni huɗu kenan. Mun sauka a Lagos inda motocinsa da guards ɗin sa na amana suka zo ɗibarmu airport. Da taimakonsu muka shige motocin dan yan jarida da bamu san ta yanda akai suka san zamu shigo ƙasar ba tuni sun kewaye mu. Ga jama'ar gari da muka zame musu yan kallo. Ni da shi mota ɗaya muje, dan tunda muka fito a jirgin yana maƙale da hannuna cikin nashi kamar za'a ƙwaceni. Sanye yake cikin ƙananun kaya da suka masa ƙyau sosai. Ni ko abayace a jikina baƙa data mun ɗas, tare da ɗan ɓoye cikina ɗan watanni kusan shida. Ni kaina nasan na ƙara ƙyau da cikar kamala ga ƙibar da ciki ya sani fatata sai ɗaukar ido take mai birgewa. Mun sha matuƙar mamaki da ganin yanda akai ma Maash Mansion gyara. An canja fentinsa da komai na cikinsa. Su Mama Balki an maidosu ainahin sashen da Ummie ta fara mallaka musu sanda take ginin gidan. Haka itama an gyara mata ainahin sashen da tayi da sunan nata. Sai Fahad shima da Hafizzullah, a kwai kuma ainahin sashen da in yayi aure zai zauna da matarsa. Sai Hayat da Falaq Ummie tace nan zasu dawo suma tafi son ganinmu a tare waje guda. Sai kuma mai gayya mai aiki muna dai anan nasa sashen na fil azal. Sai dai yanzu daga ni sai shi ne. An kawo sabbin masu aiki maza da mata. Kowa ya yaba

Ummie harda hawayen farin ciki, dan Maash Mansion ya koma ainahin wanda ta tsara a rayuwarta. Bamu wani hutaba sosai a washe gari da safe jirginmu ya sake ɗagawa zuwa Kano ta dabo tumbin giwa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-six

.....Motocin da suka ɗakkomu daga airport na shigowa gidan da suka kawomu na ganesa. Kallonsa nayi kawai, ganin ni yake kallo shima yasa na ɗan hararesa kaɗan. Sai ya saki mun ƙaramin murmushi. Murya can ƙasa ya ce, “Kin gane gidan ne?”.

“Hummm taya zan mance sa. Gidan da akayi kidnapping ɗina”.

“Harda sharri abun”.

Kwantar da kaina nayi a jikin hannunsa ina murmushi. Na ce, “Babu wani sharri sai gaskiya. Ai kaida Yaya Hayat ko humm”.

“Miza'a mana?”

Ɗan far nayi da idanu na, cike da shagwaɓa na ce, “Sai na bama yaranku labarin rashin jin da kukayi”.

Murmushi yayi kam yanzu sosai har haƙoransa na bayyana. Yayinda na shagala da kallonsa dan in yay irin murmushin nan ba ƙaramin ƙyau yake masa ba. Kaɗan na kaima kumatunsa sumbata. Kafin yace wani abu na buɗe motar na fice abuna. Ashe ma kowa ya fito mune kawai a mota. Duk sai naji kunya ta kamani. Haka dai na dake. Shima fitowa yay fuskar nan a haɗe kamar ba shi ya gama murmushi ba

yanzu yana ƙoƙarin gyara rigar suit ɗinsa. Ido muka haɗa nai saurin ɗauke nawa na maida ga little Awwab dake hannun Hafizzullah.

Duk da gidan ba wani ƙatoto bane ba dan ko kashi ɗaya bisa takwas ɗin Maash Mansion bai kaiba shima dai yayi ƙyau. Kuma yana da nasa girma gwagwado da zai ɗaukemu mu dukanmu. Duk a falo muka zube kowa na maida numfashin gajiyar tafiya duk da ba wani nisa bane. Amma kasancewar ta jiya bata gama sakinmu ba sai duk gamu nan dai. Shi dai uban gayyar bai zauna ba ya shige bedroom ɗinsa. Sai TJ da Hayatu ne keta ɗawainuya da mu. Bamu wuce mintina goma ba aka kawo mana abinci daga gidan su Bahijja. Hameed ne da wannan aikin. Ya zauna an gaisa aka ɗan taɓa hira yace zai wuce. Aiko Bahijja ta maƙale masa dan tana kewar gida. Ba'a hanata binsa ba dan tayi ƙoƙari ma.

Muma dai abincin kawai mukaci na marairaicewa Ummie kan zamu fara gaba ni da Falaq da Hafizzullah kafin su taho anjima. Dan har yanzu tara ma batayi ba. Hanyar bedroom ɗin da Maash ya shiga Ummie ta nuna min. Ta ce, “Maza jeki mijinki ne da wannan ikon. Idan ya amince ni nawa addu'a ne daughter. Kema tashi ki gayama naki”. Tai nuni da Falaq. A kunyace duk muka tashi, yayinda Fahad da Hafizzullah ke faman mana dariyar shaƙiyanci. Samarin nan sun ishi kowa. Bare mu da suka sama ido ALLAH ya aurar da su mu huta dai. Idan kuma da mai so a fans ɗinki bily yazo na sayar masa😂.

Banyi mamakin samunsa yana barci ba hankali kwance. Dama nayi zargin hakan tunda naga ya shiga bai fito ba kusan awa ɗaya da rabi. Ashe shi barcinsa yake sha hankali kwance. Kayan daya cire ya zube a kujera yana cikin duvet abinsa ya ƙure ac ya rage fitilar ɗakin kamar dare. Kusa da shi na ɗan zauna dan harga ALLAH na matsu naje naga yɗan uwana bazan iya haƙura har sai ya tashi dan kansa ba. Sai da na ɗan zubama fuskar tashi ido na kusan mintuna biyu kafin na kai yatsana saman girarsa mai cike da baƙin gashi na shafa. A hakankali na gangaro har saman hancinsa na sauka kan mitsitsin bakinsa. Sosai barcin ya masa nauyi dan bashi da alamar motsawa. Sai kawai na rankwafa na sumbaci lips ɗin nasa. Ina ƙoƙarin janyewa caraf aka riɓe nawan. Idanu na waro sosai dan mamaki. Ashe idonsa biyu yay likimo. Mintsini na dinga kai masa amma kota kaina baibi ba, sai ma jawoni da yay saman gadon ya sakani cikin bargon. Duk shagwaɓa da roƙon da nake masa yay kunnen uwar shegu dani ya shiga yin yanda yaso dani. Bamma san na bada kai bori ya hau ba. Dan mutumin nan ku barni da abuna kawai ni nasan sirrin kayana.

Cike da shagwaɓa nake kallon agogo tamkar zanyi kuka. Shiko ko'a kwalar rigarsa gashinsa yake tsanewa tamkar bai san inayi ba. Haka na ɗauka mai na shafa na gyara fuskata inata faman kumbure-kumbure. Rasa yaya ma zanyi nayi, dole na ɗauka waya na kira Aunty Falaq nace ta taimakeni da akwatin kayana. Dariya ta dingamin da tsokana, sai da taji zan mata kuka tace gashi nan a kofar

ɗaki ta ajiye. Haka na leƙo na ɗauka. Shiri nayi cikin siket da rigar lass da duka min ƙyau sosai na fito a matar Maash ɗina. Shi dai yana zaune yana kallona. Sai da na gama nazo inda yake, cikin sanyin murya na ce, “Yaya to waye zai kaimu?”.

“Ina?”.

Ya tambaya cikin halin ko'in kula. Idanu na waro ina kaiwa zaune kusa da shi. Cikin sake marairaice wa nace, “Dan ALLAH my Hot kada kasa na maka kuka. Kafa san gidan Abba zamuje yaufa ne sunan. Ɗazu ma tambayarka Ummie tace nazo nayi shine.. shine kai kuma...”

Na kasa ƙarasawa.

“Uhhm Ni kuma! Ni kuma mi?”.

Ya faɗa cike da salon ɗage gira sama. Hannayena duka biyu na saka kan fuskata na ce, “Ai ba saina faɗa ba. Dan ALLAH kace muje ALLAH so nake naje naci shinkafar sunan irin saukewar farko ɗin nan kaga fa har sha biyu saura”.

“Ohhh kice kwaɗayi ma zaki je ashe?”.

“ALLAH Yaya Awwab bazaka gane ba. Tunfa muna Spain nake sha'awar cin shinkafar suna, kaga tunda yanzu ga dama ai sai naje naci ko”.

Idanunsa da ya kafeni da su ya ɗan jaa luuu yana jinjina min kansa. Sai kuma ya kalla agogon ɗakin. A saman lips ya furta, “Sai yaushe zaku dawo?”.

“Lah Yaya bacan zamu kwana ba wai?”.

Kansa ya girgiza min alamar a'a. Sai kuma ya miƙe ya nufi akwatin ya ɗauka kaya. Sai da ya kammala sakawa sannan ya dawo inda nake da wani ƙaramin kit a hannunsa. Sarƙace ya ciro a ciki da kansa ya saka min harda yan kunnenta da zobe da abin hannu. Tayi ƙyau sosai daka ganta kaga diamond. Kallonsa nayi idanuna cike da ƙwalla. Sai ya ɗauke kansa tare da faɗin, “Let's go”. Baki na buɗe zanyi magana ya ce, “Shiiiii!!! Bana son surutu”. Daga haka yaja hannuna muka fice. Falaq da Fahad da Hafizzullah kawai muka samu a falo wai suna jirana. Sai Hayatu dake waya a gefe Little Awwab a hannunsa. Gaisheshi suka shiga yi, ya amsa musu da kai, kafin ya tambayesu su Ummie. Falaq tace sun kwanta suna hutawa wai kar a tashesu sai lokacin tafiya gidan suna. Murmushi kawai ya ɗan yi da maida kallonsa kan Hayat daya gama wayar ya nufo mu, sai da ya amshi little Awwab a hannunsa sannan yay masa nuni da mu. “Waɗan nan ya za'ai da su?”.

Murmushi Hayatu yay da amsa masa da “An gama shirya motocin tafiyar tasu. Hafiz da Fahad sunce zasu iya kaisu sai guards da zasu musu rakkiya, idan sun ajiyesu sai su dawo”.

“Okay yayi hakan ma”.

Daga haka yaja bakinsa yay shiru. Sai Hayat yace muyi himma. Sosai dukanmu farin ciki ya kama mu. Musamman ma su Fahad da aka samu ƙafar gantali, dama a matse suke tun ɗazun. Banyi zaton zai biyomu har wajen ba. Amma a mamakina sai naga ya miƙe riƙe da little Awwab ɗin ya kama hannuna muka fito. Har jikin motar da zamu shiga ya buɗe min da kansa yay min nunin na shiga. Tsayawa nai kawai ina kallonsa kamar yanda shima yake kallona. Sai da mukaga hasken camara kammu sannan muka dawo hayyacinmu. Duk juyawa mukai, Hafiz da Fahad ne ashe ke ɗaukar mu hoto. Da sauri suka shige mota suna shafar kawuna. Nima sai kawai na shiga inda ya buɗe min ɗin na zauna. Ɗan duƙowa yay ya gyara min gyalena da ya ɗan sauka sannan ya saka mun little akan cinya ya sumbaci gefen kumatuna. Cikin kunne ya raɗa min, “Banda rashin ji babyna bata gama ƙwari ba”.

Kafin ma na ɗago na kallesa ya janye jikinsa ya rufe ƙofar. Kallonsa nayi idanuna a narke. Kafin na motsa lips ɗina a hankali na furta, “Zanyi kewarka”.

Wani ɗan iskan Murmushi ya sakar min da ƙanƙance idanunsa ya ɗan ɗage min gira ɗaya. Sai kawai na duƙar da nawa kan nima ina murmushi ganin Hayatu na kallonmu. Sai da muka fita a gate ɗin Fahad dake gefen Hafiz dake driving yay gyaran murya da faɗin, “Gaskiya mudai Aunty a dinga sassautawa kar a ƙona mu”.

Daga ni har Falaq kallonsa mukayi, duk da nasan baya cema Falaq aunty. Yayinda Hafizzullah ke dariya ya ce, “Faɗa musu dai. In ba haka ba ALLAH ban komawa school sai da mata”.

Dariya Falaq ta saka, yayinda na riƙe baki ina kallon Hafizzullah ɗin ta mirror. “Lallai yaron nan zama da Fahad yasa kaima ka fetsare ko? Aiko duk zanyi maganinku. Bari mu dawo zan faɗa masa duk abinda kukace a motar nan”.

Da sauri har hada baki suke wajen bani haƙuri. Falaq dai nata dariya...

Mun iso anguwarmu lafiya. Ban san nayi kewarta ba sai da muka shigo cikinta. Komai yana a yanda na barsa. Ɗan cigaban da aka samu a shekara ɗaya da wasu watanni da bana nan ba wasu masu yawa bane. Murmushi kawai nake saki har motocinmi uku sukai parking a ƙofar gidan Abba. Ta farko data bayanmu duk guards ɗinsa ne. Sai mu a motar tsakkiya fara tass dako makaho ya laluba yasan an sayeta da kuɗaɗe masu tsokar gaske. Tunda muka shigo anguwar aketa kallonmu. Barema cikin layinmu wasu har biyowa sukai suga su wanene a ciki. Kafin Hafiz da Fahad su fita guards ɗin har sun fito. Sune suka buɗe mana ni da Falaq, kamar yanda suka buɗema Fahad da Hafizzullah.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-seven

_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍____.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....Jinai ma hawaye na neman cika mun ido. Amma haka na daure na dake abina dan yanzu fa ba da bace. Matar Muhammad Awwab El-Mu'azz Maash nake. Amsar handbag ɗina guard ɗin ɓangaren da nake yayi da sauri, yayinda ni kuma na saka little Awwab a kafaɗa na zuro ƙafata dake sanye cikin takalmi mai ƙarancin tudu silver sai sheƙi yake, ya wani masifar haska yʻar ƙafata da tai cas a ciki. Cike da ƙasaitar da ban san ta fara bin jinina irin ta matan manya□ ba na fito. Ni kaina a yanda nai action ɗin fitowar nasan nayi barazana a wajen Bily. Dan a take shock ɗin mutane da yawa ya bayyana saman fuskokinsu. Aunty Zakiyya dake tsaye tare da wasu mata da alama rakosu tayi kota tarosu ce tai wani masifar zabura da ƙwala kiran sunana cike da farin ciki tazo ta haɗa ni da little ta rungume. Kafin kace mi yara sun fara cillawa da gudu cikin gida suna faɗin ga Samraah. Ya ALLAH da ƙyar muka samu shiga cikin gidan. Hafizzullah riƙe da handbag ɗina daya amsa hannun guard ɗin nan. Mu huɗun duk muka shiga har Fahad. Cikin lokaci kaɗan gida ya yamutse, na ɗaki nata fitowa. Ni dai ina rungume jikin Gwaggo Gudidi da itama ta fito. Hango Mom da tai kamar mutuwar tsaye yasa na saki Gwaggo Gudidin na nufeta na rungume. Dan harga ALLAH wani irin kewarta nake ji, na yarda da batun masu iya magana da sukance sabo akewa kuka ba mutuwa ba. Farin cikin da nake ciki da yʻan uwa da suka lulluɓeni yasa sam bamma fahimci halin da Mom ɗin ke ciki ba. Da ƙyar aka sarara min saboda Gwaggo Abu datai maganar su barni na zauna bani kaɗai bace ina fama da kaina sai jagwalgwala ni suke. Kai tsaye kowa ya fahimci inda ta dosa, dan koba'a fada ba duk mai hankali ya ganni yasan inada ciki. Anan tsakar gida muka zauna a tabarma dan na samu damar gaisawa da kowa. Yʻan uwan, maƙwafta dama yara nan fa aka shiga gaisuwa. Yayinda yaran keta shigowa da kayayyaki. Ashe Hayatu ne ya lodosu a motar bisa umarnin uban gidan nashi batare da saninmu ba. Cike da shaƙiyanci abokan wasa ke tambayar wai cikina wata nawa ne. Hararsu kawai na dinga yi naƙi faɗa, da naga zasu takura min ma sai na gabatar musu da aunty Falaq. Ai ko nan take aka koma murnar ganin yʻar uwa, dan akwai dangin ɓangaren babanmu da yawa da sukazo daga Gwarzo

kasancewar dai akwai zuminci a tsakaninsu da dangin mahaifiyar tamu su Abba. Sai kuma aka koma koke-koken yima iyayenmu addu'a. Kiran sallar azhar ya taimakemu muka samu sararawar mutane. Sashen Mom da ban sake gani ba tunda na rungumeta ɗazun muka shiga. Babu mutane sosai dan wai bata gayyaci kowa ba. Hasalima tun ɗazun tana ɗaki ihun zuwane ya sa ta fito har mutane suka ganta a yau ɗin. Zaune muka sameta ta zabga tagumi. Zama nai kusa da ita na sake rungumeta. Koba komai dai ita muke ma kallon uwa dan itace ta rainemu. Sai da na ɗan jima a jikinta sannan na ɗago cike da kulawa da girmamawa na gaisheta. Muryarta na rawa ta amsa min, ban damu ba na tambayarta ina su auta naga banga kowa ba sai ita kaɗai sai Ummanta da itama na gaisar. Umman tata ke sanar min ai sun ɗan fita ne. Kaina na jinjina da faɗin, “Mom bari muyi salla yau akwai labari, so nake ki bani labarin duk abinda akayi bana nan nayi kewarku sosai. Hanun Aunty Falaq naja muka wuce tsohon ɗakina dan Little Awwab na hannun su Gwaggo an goyesa, su Hafizzullah kam tuni sukai gaba abinsu. Mun ɗauro alwala zamu fara salla Aunty Falaq ke faɗin, “Sis... Matar nan kamar batai murna da ganinki ba. Da fa muka shigo kamar kuka take”.

Murmushi na mata da faɗin, “Kai aunty maybe na murnar ganinmu ne. Kin san fa itace ta riƙemu”.

Humm kawai tace badan ta yarda ba ta kabbara sallarta. Nima sai na kabbara tawan. Bayan mun idar na ciro wayata a jaka dake ruri. Ganin Yaya Awwab ke mun video call da sauri na ɗaga. Tar-tar kuwa ya fito akan screen ɗin kamar na taɓashi na kama. Ganinsa zaune kamar a bedroom yasa na ɗan waro idanu. A shagwaɓe na ce, “Salla fa?”.

Sai da ya ɗan kalla agogon hannunsa tare da lumshe idanun ya buɗesu a kaina sannan ya motsa lips ɗinsa ya furta, “Yanzu kikayi naki ke kenan?”.

Kai na jinjina masa. Shima ɗan taɓe bakinsa yay da jinjina kansa ya ce, “Yayi. A ina kike nan?”. Back camara na maida na haska masa ɗakin kaf sannan na maida ta gaba fuskata da murmushi na ce, “Tsohon ɗakina ne munyi salla da aunty Falaq”.

Zaune ya tashi da ƙyau yana faɗin, “Sake haskawa na gani”. Babu musu na tashi tsaye ina haska masa da nuna masa wardrob ɗina na bango ni da su auta, inda nake ƙwana. Harma da wasu abubuwa nawa da har yanzu ba'a fita dasu a ɗakin ba. Maido da camaran nai kaina ina murmushi, shima sai ya murmusa da silent muryar nan tashi ya furta, “Ɗakin matar Maash ya ƙayatar da ni, zanso wataran nima nayi barci a cikinsa tana jikina”.

Sosai na waro idanuna, sai kuma na kalla inda Aunty Falaq take. Wayam ta fita, na ɗan sauke ajiyar numfashi da kallonsa. Gira ya ɗan ɗaga min alamar miye ɗin nan. Nima sai na tura masa baki na ce, “Aunty Falaq fa na nan, a gidan namu kuma zaka kwana harma na kwanta a jikinka”.

“To minene? Kuma zan ƙi magana da Matana saboda Falaq na nan? Yanzu dai yashe zaku taho. Ina buƙatar ɗumin matata”.

“Kai Yaya ko awa biyu fa bamu yi a gidan nan ba. Bammaga Abba ba? Kuma su Ummie zasu zo idan anyi la'asar. Kai bazaka zo ba?”.

Shima fuska ya ɓata, da yar shagwaɓa ya ce, “My Tiger ana ga ƙura kina ga yaƙi, ni mizan zo nayi taron mata, sai gobe in sha ALLAHU zamu zo mu duka gaida Abba sai muga babys.”

“To Please mu kwana nan. Kagafa yan uwa duk suna nan sunzo da yawa musamman yan gwarzo. Ga shi duk basu san Falaq ba”.

Kai ya girgiza min alamar a'a yana lumshe idanunsa. Idanuna cike da ƙwalla na ce, “Miyasa?”.

Kamar bazai ce komai ba sai kuma a hankali ya furta, “Sabida mijin Samrh bazai iya barci ba sai da Matarsa a jikinsa”.

“Kaida kake tafiyanka fa sai ma kai sati ban ganka ba”.

Murmushi ya ɗan yi kawai yana kallona hannayensa harɗe a ƙirjinsa. Ganin yaƙi magana na sake tura baki da faɗin, “Shike nan amma fasa hiran da kai, kuma namayi yaji yau anan zan kwana”. Na katse kiran. Nayi hakan ne saboda shigowar su aunty Zakiyya da suka kasa haƙuri. Dole na biye musu muka fita. Babu su Mom a falon yanzu, dan haka muka fice tsakar gidan dake ta sake cika da yan suna. Sashen amaryar Abba muka shiga mai jego kenan. Haka kawai naji tamun a rai, gashi dama bazamu wuce sa'anni ba. Daga ita har yan uwanta sai haba-haba suke damu. An zagayemu da kayan ciye-ciye kamar mune kaɗai baƙin sunan. Yara na hannunmu Masha ALLAH daga gani dai sun kwaso ƙyawunta. Muna a sashen Abba da Kawu Jafaru da abokansa suka shigo. Shima kasa ɓoye farin cikinsa yayi, babu kunya ya dinga yima abokansa bayanin ga yarsa dake aure a Lagos tazo. Tuni sun ɗau haske. Niko da Falaq munata gaidasu da girmamawa. Anan muke jin ai walima zasuyi, nima sai na sanar masa ai Yaya Awwab ɗin ma na zuwa idan anyi la'asar harda mahaifiyarsa. Kasa rufuwa bakin Abba yay dan farin ciki. Ganin yanda yake ta farin cikin na ɗauka waya na turama Yaya Awwab ɗin roƙon dan ALLAH ya biyo su Ummie.

Sam banyi tunanin zai zo ɗin ba. Bayan la'asar gida ya gama cika matuƙa mun zama abin kallo tako ina sai ƙusƙus mata suke da nuna ni, ta wajema anata shirin fara walima wasu ma har sunje sun zazzauna sai ga wasu zuƙa-zuƙan motocin har huɗu. Biyu dai na guards ɗinsa ne da suka rakomu ɗazun suka koma. Biyu kuma ɗaya Ummie ce da Mama balki da uwargidan Sheikh Muhammad ibn Khalipha Al-Hussain ce. Sai ɗayar Tj da Hayatu a gaba, uban tafiya a baya. Ina da ga bakin gate muna magana da wasu yan islamiyyar mu da aka kaima labarin zuwana dake nan

layinmu sun zo tabbatar wa na ɗan rakosu akan gobe zamu haɗu yau taro yasa bazamu gaisa da ƙyau ba motocin suka tsaya. A take kallo ya koma kansu kamar sanda muma muka iso. Number motocin yasa na gane nashi ne, sai nai tunanin su Ummie ne kawai. Su na nufa cike da murmushi zan tarbi su Ummie sai kawai aka buɗe masa. Fitowarsa ta saka mutane da yawa ambaton Masha ALLAH. Dole nima na tsaya cak ina kallonsa kallo irin na mamaki. Dan sanye yake da bugaggiyar shadda data ji ɗinki ɗan ubansu da yay masifar zauna masa a jiki tamkar dan shi kaɗai aka halicci shadda a duniya (Tofa namu mazan fa😏) ga wani arnen takalmi da hula daya murza a sama. Yana masifaffen ƙamshin nan nasa daya mamaye wajen gaba ɗaya yama danne namu. Karo na farko dana ganshi sanye da manyan kaya a rayuwata. Kullum daga suit sai ƙananu kawai. Gira ya ɗan ɗage min da kashe ido ɗaya cike da salon nan nasa na isa da ƙasaita. Sai kuma yamun alamar wai nazo garesa. Kafaɗa na maƙe masa da nufar Ummie na rungume. Hannu biyu ta riƙeni itama tana murmushin da masa daƙuwa dan kowa a wajen kasancewar idanu na kanmu yaga abinda ya faru a tsakanin namu. Kansa ya ɗan rissinar da kai hannu ya shafo wuyansa. Tuni kuwa waje ya fara ɗaukar ƙusƙus. Yayinda su Abba suka taso cike da farin cikin tarbar babban mutum irinsa kuma surukinsa. Yanda yake ƙoƙarin girmama iyayena sosai yake ƙara saka min ƙaunarsa da kgirmansa a zuciyata. Nima sai naja su Ummie muka shiga cikin gidan da tuni har an kai musu labarin mijina da iyayensa ne suka zo. Shigowar su Ummie ya saka gidan ɗaukar tsitt, kowa na yaba sunan UBANGIJI a ransa. Dan duk wanda ya kalla Ummie yaga cikakkiyar baturiya a kayan hausawa. A falon Mom Gwaggo Gudidi sukai musu masauki. Babu wani alamar wulakanta kowa ga Ummie. Kowa yazo cikin girmamawa da mutuntawa take gaishesa. Kamar yanda suma suke mata gaisuwa irin ta girmamawa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-eight

.....Cikin ƙanƙanin lokaci aka gama shirya musu abincin suna kala-kala a farlon Mom ɗin data fito ta gaishesu cikin dauriya da dakewa. Da alama dai mahaifiyarta ta kwakwkwafeta ne. Dan kallo ɗaya zaka mata ka fahimci a susuce take. Bare ma ganin su Ummie ta sake firgicewa. Bata ma ida susucewa ba sai da Maash suka shigo shi da Hayat da Abba har cikin gidan a falon da muke na sashen nata. Da ga can tsakar gida Abba yabar bakin kowa buɗe dan kai tsaye ya sanar musu wannan mijin Samraah ne, wannan kuma Falaq. Anan kuma tsabar neman magana irin na Yaya Awwab Ummie ta bani Babys na miƙa musu kawai ya haɗa da hannuna ya riƙe yaƙi kuma saki dole na kai duƙunne gabansa hannayena da nashi tallafe da Babys ya ɗaura saman cinyarsa a haka. Niko ina ta duƙunne a gabansa like na dafa gwiyawunsa. Cikin ɗan iskan salon kallon nan nashi dake kashe min jiki ya kallan fuskarsa da ɗan murmushi muryarsa very soft da kowa baya ji sai ni ya furta, “Kamar ace namu ne ko My helf”.

Tamkar zan nutse dan kunya, danni gani nake kowa na jinsa na marairaice masa fuska. Cikin magana ƙasa-ƙasa na ce, “Yaya Awwab su Abba fa da Ummie, ka saki min hannu na tashi Please”. Ɗagowa ya ɗan yi da alama shima dai ya shagala da mantawa da su ɗin, fiiii ya ɗan kalla kowa sai kuma ya dawo da kallonsa kaina. Cikin sake maida muryarsa Low ya ce, “Ya Rabba. My tiger dama bamu kaɗai bane?”.

Hararsa na ɗan yi, sai kuma nai ƙoƙarin janye hannayena dan nama fara gajiya da durƙuson. Ina samu na zaresu na miƙe a wajen batare dana kalla kowa ba. Kamar munafuka sum-sum na koma kusa da Mama balki na zauna kaina a ƙasa. Har aka gaisa aka gama ban sake kallon kowa ba. Sai da Abba yace nazo na amshi yaran a hannunsa zasu tashi sannan na miƙe dan dole. Koda naje sai ya bani ɗaya wai na bari zai tayani da ɗaya. Ya zanyi dole na bisa a yanda yake so muka fito a falon dan na ƙara fahimtar yana matuƙar son yara. Kamar an saita sai ga su Fahad da mai hoto. Ai kawai taremu sukai mu tsaya a mana hoto a haka. Yau dai naga takaina, dan dole na tsaya aka ɗaɗɗala mu babu ko kunyar taron mata dake cike da gidan nan ga su Abba Yaya Awwab ya rungumeni ni da Babys ɗin aka mana hoton nan. Ina samu wani ya amsa na nufi fecewa a wajen amma ya damƙe hannuna dole a haka muka fito har ƙofar gida. Sai da yaga matasan anguwa da abokan Abba dama magidantan sun zagaye motarsa sannan ya barni na koma ciki badan yaso ba. Naji daɗin hakan dan na fahimci take-takensa so yake ya gudu dani gida wai hayaniya namun yawa ga babynsa.

Cikin gidan na koma aka cigaba da hotuna. Sai ga yara na shigowa da labarin wai mijin Samraah da ƙaninsa (Hayatu) nata rabon kuɗi wa matasa da magidantan anguwa a ƙofar gida. Kamar wasa ana haka sai ga Hafizzullah da sukai kira a waya shima ya shigo shi da Fahad suka farama matan cikin gidan rabo. Zo kaga gyuɗa, wasu ma kaina sukazo sunayin gyuɗar ana zuba min kirari. Humm kuɗi! Kuɗi!

Jama'a kuɗi dabbane. Badai zance komai ba, na bama kowa damar ya auna a cikin ransa kawai....

Suna kam dai Alhamdullah, dan yayi matuƙar armashi fiye da zato da tsammani. Dan daga ƙarshe dai su Maash basu tafi ba sai da akai sallar magrib muka tafi tare akan gobe in sha ALLAHU zamu dawo a gaisa sosai gobe idan ALLAH ya kaimu Yaya Musaddiq ya shigo sai mu shiga gwarzo. Badan naso ba na bisu muka tafi. Ni da shi a mota ɗaya ina jikinsa inata faman fushi an hanani kwana. Nan ko jikina harda su zazzaɓi abinda na jima banyi ba. Nasan wannan hayaniyar ce da daƙunar dana sha wajen mutane. Gwaggo Gudidi harda bani tofi nasha wai maganin baki. Ni har dariya ta bani dan har ɗaga rigata tayi ta shafe cikin da shi. Kafin mu isa gida nayi barci, sai kawai jinai kamar an ɗaukeni ana tafiya dani, sanda nake buɗe ido har mun iso falo gasu Ummie da kowa sai kawai na fuske naƙi buɗe ido dan bazan iya yarda na haɗa ido da kowa ba a wannan yanayin wlhy. Sai da ya shiga ɗaki dani ya dire a saman gado na buɗe idanuna. Tsayawa kawai yay a rankwafen yana kallona cikina ido, irin dama kin tashin nan ashe kikai likimo.

Kaina na kauda gefe ina murguɗa masa baki. Sai ya saka hannu ya dawo da fuskar yanda take cikin ɗage gira da motsa lips kaɗan ya ce, “Naga wannan”.

Zanyi magana kawai ya rufen baki ruff da nashi. Daga haka salon wasan ya canja sai tsintar kaina nayi a ruwan wanka. Ai ban sake cewa komai ba dan nasan dai da gudunmawata akaje inda akaje ɗin....

Washe gari ɗan zazzaɓin dana tashi da shi yasa na tashi a kasalance. Da ƙyar na iya taimakawa Falaq da Ummie da Mama balki mukai break fast, duk da Yaya Hayat yace mu bari za'ai order muka ƙi, sai da muka kusa kammalawa sai kuma gashi an kawo daga gidan Sheikh ma. To baiyi yawa ba, tunda dama akwai guards da securitys ɗin gidan, sai hakan yasa abincin ma ya sake wadatar mu sosai. Sai da akai zaman ci wasu ma sun fara sannan mai gayya da aiki ya fito. Dan barcin daya hanamu yi jiya yay ramuwa da safen bayan sun dawo daga jogging shi da su Hayatu. Da kayan barci ya fito jikinsa alamar ma ko wanka baiyi ba. Kujerar kusa da ni Fahad ya ja masa ya zauna. Batare da ya kalla kowa ba yace “Ummie, Mama good morning”.

Da kulawa suka amsa masa. Yayinda muma muka shiga gaishesa. A fakaice ya amsa mana sau ɗaya ya ɗauka tea ɗin gabana ya fara sha. Ummie ce tai magana tana kallonsa. “A'a Muhammad ya zaka shanye mata tea, ba gashi zata haɗa maka ba.”

Cikin langaɓe kai da marairaice murya ya ce, “Ummie yunwa. Rabona da abinci fa tun jiya da dare”.

Kanta ya ɗan girgiza da faɗin, “Ai laifinka ne. Ace mutum bazaicin abinci ba sai yunwa ta cimasa ciki ta cinye. Shiyyasa gaka nan ko ɗan tumbin nan na matasa bakayi sai uban ƙirji kamar zaki. Ni Ulser ma nake tsoritar maka”.

“Humm Ummie ai ta jima da kamashi fa”.

Cewar Hayat cikin damuwa. Hararar Hayat ɗin ya ɗan yi da ɗaukar tea spoon ya jefa masa. Sai ko a saman kansa. Dafe wajen yay da faɗin, “Ummie shike nan ya fasa miki kan ɗa”. Yanda Hayatun yay maganar da yanda Ummie taima Maash ɗin daƙuwa da jifa masa tea spoon ɗin itama ya cafe yasa muka hau dariya. Sai da ya ɗan harare mu musamman su Fahad sannan muka gimtse. Sai Ummie da Mama ke kayarsu da su babu damar a hanasu dai. Haka dai muka ci abincin cike da nishaɗi, yaƙi yarda na zuba masa wani dole a plat ɗaya muka ci ni da shi. Duk da bama wani na kirki yaci ba, shine ya fara tashi wai ya ƙoshi. Duk lallaɓawar da Ummie ta masa sai ya marairaice wai a hakan ma yayi over feeding cikinsa zai fashe. Ni tausayi ma ya fara bani, na fara jin ya kamata likita ya dubashi ko hanjin nasa sun naɗe ne shin. Falo ya ɗan zauna har lokacin da muka fara kammalawa muma. Kafin ya tashi ya sake komawa bedroom ɗin namu. Muma bamu zauna a falon ba kowa ya tafi ɗakinsa domin kimtsawa. Dan Yaya Hayat yace fita zamuyi mu dukanmu....

□□□□□

“K yanzu kina ganin wannan kukan zai fisheki Jalilah? Tun fa jiya kike abu ɗaya bayan na kwana takwas da suka wuce. A gabanki kuma likita ya sanar mana idan fa baki nutsu ba zaki iya yanke jiki ki faɗi ƙarshe da paralysis ce.”

Hawayen da suka cika idon Mom ɗin ne suka sake sakkowa a guje. Bata iya ta share ba. Sai magana data farama mahaifiyarta muryarta na sarƙewa. “Umma yaya kike son nayi, miya rage mun idan ba kukan ba. Ki duba fa ki gani komai neman ƙwacewa yake yi kamar a mafarki. Mun gagara samun mahaifar shegiyar yarinyar can yar ƙauye amma tazo ta addabemu. Tsabar munafunci mun rasa a ina tsohuwar can takai ta bizne. Muna ji muna gani munga samu munga rashi. Bamu gama fita a wannan magagin ba sai ga wannan shegiyar yarinyar. Kiga fa, ƙamshinta ma kawai abin firgitarwar ne a garemu. Ki kalla lass ɗin jikinta wlhy irin na miliyoyin kuɗin nan ne. Sarƙarta ta diamond ne Umma. Diamond da muke ji a labari, dan Gara zinare kanzo hannayenmu koda na ƙaramin kuɗi. Umma handbag ɗinta da mayafi da takalmar ƙafarta ba kannanun kayan kuɗi bane. Ga ciki a jikinta, kiga yanda yaron nan ke mata kamar ita kaɗaice mace a duniya ko kunyar uwarsa baya ji kai tsaye yake nuna mata kulawa da tattali. Itama uwar kuma ko'a jikinta ko irin ɗan kishin nan na uwar miji babu a tattare da ita. Ƙamshin turarenta kawai ka shaƙa kasan irin na manyan turaren nan ne da talaka sai dai yaga hoton kwalayensu a net idan yay searching. Why Umma why hakan ta kasance ne? Umma

Baby da Bibaa na naima tanaji da fatan irin wannan rayuwar ba sakaran yarinyar nan da ko hasken kirki na fata bata da shi ba. Ina ganin Mansoor yafi ƙarfinta ashe wanda ya takesa ya shanye ne zai maye gurbinsa. Umma taya hankalina zai kwanta ni ko sanin inda tawa yar take banyi ba ma. Ga Abbas na hannun yan sanda. Gaba ɗaya Imam bai damu damu ba yanzu. Yanda yake rawar jiki akan yayan nan da aka haifa masa sai ki ɗauka ba'a taɓa masa haihuwa a gidan nan ba. Umma wlhy ji nake kamar na kashe kaina na huta kawai da ganin wannan baƙin cikin. Wai waɗanda ke ƙasan ƙasan ƙafafuna, na fisu da komai na rayuwa a da sune suke kokawa da turareniyar hayewa can sama ƙololuwar ƙurewa suna shirya alamomin zubar da ni da mun ɗagawa. Kamar ni Jalilah Ummie. Ni ɗin nan dai Jalilarki.....”

Kuka mai ƙarfi ya sake sarƙeta. Kamota Umma tayi jikinta ta rungume itama idanun nata cike da hawaye. Dan abinda yar tata ta faɗa duk gaskiya ne. Ita kanta dauriya kawai take ta manya amma jiya ko wani barcin kirki batayi ba saboda tunani da damuwa. Zuwan yarinyar nan Samraah ba ƙaramin hargitsa musu lissafi yayi ba. Ga lissafin Halime da basu gama ba. Ganin wanene ai nahin Maash ɗin a zahiri yau ba hoto ba, da yanda ya dinga ɓarin kuɗi kamar ba nemansu yake da wahala ba ya sa komai ya ƙwace mata ma. Ga yarinyar da ciki itama, idan ta haifi Namiji fa shike nan ta gama mallakar komai. Har zuwa yau da safe ta gagara komawa dai-dai yanda ya kamata.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page ninety-nine

*_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram

da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan😣. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....😉. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍____*.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

_Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😉__._

.....A tsare motocin da muke ciki suke tafiya saman titi tamkar an zana su. Duk ta inda muka gitta sai kaga idon mutane na binmu. Ni dai ina kwance a jikinsa ina game da waya yana kallona hannunsa a saman cikina yana shafawa. Jakin babangida da muka ɗan hau ya sa na cije baki da miƙewa zaune da ƙyau saboda

motsin da cikina yaya babu shiri, ƙoƙarin tambayata yake lafiya ni kuma hankalina nakan mai agwalina dake bakin titi cike da barrow da idona ya hango min. Har mun ɗan gota nace ma TJ ya tsaya. Tsayawar kuwa yayi, ni kuma na kalla ogan nasa daya zuba min ido. Batare da damuwa ba na ce, “Ya Awwab Please bara na sayi Agwalima ɗin can”. Nai maganar ina zaro 1k a handbag ɗina. Ƙoƙarin buɗe ƙofar motar nake ya riƙo hannuna. A marairaice na juyo na kallesa kamar zanyi kuka. Baice komai ba ya ɗauke kansa tare da sakin hannuna ya buɗe side ɗin da yake ya fita. Cikin rawar jiki TJ ya fita shima yana faɗin ya bari ya sayo amma ya ɗaga masa hannu. Hakama Hayat da su Fahad ganin ya fito duk suka fito suma amma sai bai kalla kowa a cikinsu ba ya tsallaka wajen mai agwalima ɗin. Tashin bal, gaba ɗaya mutane sun zuba masa ido musamman ganin yanda yaje gaban mai agwalima ya tsaya. Shi kansa mai agwalima duk ya rikice dan duk wanda dai ya kalla wannan ɗan gayen yasan baiyi kalar shan abun titi irin wannan ba, barema wai agwalima. Hannu ya bama mai agwalima alamar busabaha. Jikinsa na rawa ya waro idanunsa waje zai ɓoye hannun, amma sai bai damuba ya riƙo hannun nasa shi kuma. Cikin dakewar nan tasa da silent voice ga hausa bai cika ba ya ce, “Ina son shi duka saka a leda”.

“Agwalima ɗin ranka ya daɗe?”.

Mai agwalima ya faɗa cikin waro idanunsa waje fiye da ɗazun. Cikin halin ko'in kula ya jinjina masa kai. Sake ruɗewa mai agwalima yayi ya shiga kwasheta yana zubawa a bako. Yayinda masu wayoyi aka samu abin ɗauka kasancewar wani ya ambaci sunan Maash ɗin a wajen. Yana gamawa ya laluba aljihun farar shaddarsa da yau ma Samraah ta dage sai ya saka ya zaro kuɗi. Bai wani damu da dubawa ba ya ajiyema mai agwalima ya ɗauka bako ɗin zai wuce. Cikin sauri TJ da Hayat, Fahad, Hafizzullah suka zo dan su amsa amma nan ma ya hanasu sai da ya kawota har mota ya saka a sit ɗin gaba ya cira guda biyu ya buɗe side da nake ya ɗauka roban ruwa ɗaya ni dai ina binsa da kallo kamar wata sakara ya wanke a gwalimar fes sannan ya miƙo min.

Kasa koda motsawa nayi, sai idanuna na ne da suka cika da hawaye ke binsa da kallo, ɗan duƙowa yay ya hure min idanun tare da kamo hannuna ya ɗaura a gwalimar sanan ya rufe murfin ya zagaya nasa side ya shiga. TJ na gama rufewa na faɗa jikinsa kawai na ƙanƙamesa hawayen da nake riƙewa na gangaro min. Ku gane bawai yayi abinda maza da yawa bazasu iya bane ba ko basu taɓa yi ba, kawai dole ne abin ya bani shock musamman da na sani kuma da kuke biye da labarin nan kuka sani Maash yayi makamancin hakan abun mamaki ne.

“Shagwaɓa ba”.

Naji saukar soft muryarsa cikin kunnena dai-dai yana ɗagoni zaune da ƙyau. Ɗagowa nai na kallesa idanuna na sake cika da hawayen zanyi magana. Kansa ya girgiza min tare da kai yatsarsa ya ɗauke hawayen. Sai kuma ya ɗago hannuna dake ɗauke da agwaliman ya ce, “Ya ake ci?”.

Murmushi na sakar masa ina ɗan langaɓe kai na ce, “Bafa ci ake ba sha, bari ka gani”.

Ban jira amsarsa ba na luguyguyta agwalima ɗin yay ruwa sannan na sha shi, wani irin lumshe idanu nayi dan jinai tamun daɗi fiye da koyaushe. Jin an riƙo hannuna yasa na buɗe idanun, kan bakinsa ya kai agwalimar dana sha ɗin shima ya sha. Da sauri ya saki hannun nawa yana dafe bakinsa. Cikin ɗan waro idanu na ce, “Miya faru?”.

“Tsami”.

Ya faɗa fuska a yamutse kamar zai fasa ihu.

Bamma san dariya ya kwace min ba. Sai da ya dungure min kai yana faɗin, “Mugunta ba”. Sannan na tsagaita. A haka muka iso gidan Abba. Tarba muka samu fiye data jiya. Dan yau iya danginmune kawai sai na Aunty Halima amaryar Abba dake shirin tafiya gida, dan har suyar namansu sun kusa kammalawa. Cike da farin ciki auta yazo ya ƙadandaneni harda kukansa yana faɗa min yayi missing ɗina, miyyasa na tafi na barsa Bibaa nata dukansa. Bata masa homework bata masa wanka. Murmushi nayi ina mai lallashinsa, na kalla Bibaa da tai sumar tsaye kawai tana kallonmu. Hannunta na kamo itama na rungumeta a jikina. A mamakin kowa sai kawai ta saki kuka da babu wanda yasan dalilinsa.

Haka dai bayan an nutsu a falon baƙi iya manyan damu aka gaggaisa ni da Falaq muka fito, dama su Fahad basu shigo ba suna ɗakin Yaya Musaddiq abinsu. Sashen Mom muka shiga gaisheta. Dan tunda ta fito taga mune ta koma. Tana kwance a kujera ta juya ma ƙofa baya. Koda muka gaisheta Ummanta ta amsa wai barci take. Dariyama abin ya bani ni kam. Dan na fahimci bata san na ganta ne kawai, alhalin sanda muke shigowa suka fito suma, daga baya ne suka koma dakin. Ban wani damu ba muka fito. Sashen Aunty Halima muka shiga. Nan ne kam muka baje anata shan hira har ƙanwar mijin Aunty Zakiyya da tai min ƙunshi biki tai mana ƙunshi ni da Aunty Falaq. Sai ga Hafizzullah ya shigo da waya a hannu ya nuna mana wai mutane sun yi video ɗazun wajen sayen agwalimar da Yaya Awwab yayi gashi nan yanata tranding anata comments. Ni abun ma sai ya bani mamaki irin wannan rashin aikinyi haka har ina. Kowa yaji da sabgar gidansa amma sun zauna damuwa da abinda bai shafesu ba. Wannan nunawa ta Hafiz tasa yʼan uwa da basu san abinda ke faruwa ba suma duk suka gani. Nanfa abokan wasa suka tasani da shaƙiyanci aunty Falaq na kare ni da Aunty Halima.

Sosai kasancewa a gidan Abba yau ta sakamu a farin ciki, bayan sallar azhar sai ga Yaya Musaddiq ya iso. Fahad da Hafizzullah sunje airport sun ɗakkosa. Sosai gidan ya sake rikicewa da farin ciki, sai lokacin ma nasan ashe su Yaya Awwab meeting sukayi akan batun auren Yaya Musaddiq ɗin. Shi Abba da bai san Yaya Musaddiq nada budurwa ba yace ya bashi Bibaa. Sai da Yaya Musaddiq ya iso aka tambayesa kafin a sanar masa batun Bibaa yace ai yanada matar aure. Gaba ɗaya sai jikin Abba yay sanyi, Gwaggo Gudidi zatai batun Bibaa yay mata alamar ta bari.

Haka dole tai shiru. Bayan la'asar muka bar gidan. Companyn sa mukaje. Daga inda labarin Muhammad Awwab El-Mu'azz Maash da Samraah Abdul-wahab Gwarzo Sam-G ya fara kenan. Sai da naji hawaye sun cika min ido. Dan komai dawo min ya dinga yi tamkar yanzun ne yake faruwa, barema da muka shiga hall na meeting aka saka mana footage na ranar taron. Hatta da inda nake ɗaukar video a wajen gawar Jaga da bai mutu ba. Rungumeni Ummie tayi tana hawaye. Yayinda Maash ya haɗamu gaba ɗaya ya rungume shi kuma. Bamu baro cikin company ba sai goma da kusan rabi na dare. Muna fitowa daga Company tafiyar tamu ta rabu. Su Ummie akai gida da su mu kuma wata hanyar daban. Ƙoƙarin tambayarsa nayi ya hana, dole naja bakin nai shiru har muka iso. Wani irin mugun waro idanu nayi ganin gidan da aka fara kawoni amarya matsayin matar Maash, ni kuma ina ɗauka matar Mansoor. Rasama abinda zance masa nayi, na saki baki da hanci kawai ina kallonsa. Ido ya ɗan kashe min tare da jan mayafina ya rufe min fuska sannan ya ranƙwafo ta bayana hannayensa duk saman kafaɗata cikin kunne ya furta, “Idan za'a kawo amarya rufe fuskarta akeyi”. Ban iya nace masa komai ba. Face murmushi dana saki ta cikin mayafin. Hannuna ya kama har ciki, bai ajiyeni a falo ba ya kaini har bedroom ɗin nan da tarihi bazai taɓa mantawa da shi ba. Sai da ya zaunar da ni a saman gadon sannan ya furta, “One minute” ya juya ya fita. Mayafin na ɗaga ina bin bedroom ɗin da kallo idanuna cike da hawaye komai na dawo min tamkar yanzu yake faruwa. Sai da naji motsin zai shigo mai maza na maida mayafin yanda yake. Abinda ya shigo da shi ya ajiye, na fahimci hakanne saboda ƙamshin daya cika ɗakin. Cikin nutsuwar nan tasa ya kai zaune kusa da ni, batare da yayi magana ba ya kamo hannayena cikin nashi, kaɗan ya murza yatsun da suka sha lalle yau wajen ƙanwar mijin aunty Zakiyya, sai kuma ya ɗagosu duk ya kai mitsitsin bakinsa ya sumbata. Hannayen ya saki ya kama gyalen ya buɗeni ya saka kansa ciki shima, sannan ya sake maidawa ya lulluɓe mu. Cikin wata irin murya mai taushi da sanyi ya furta,

“Mrs Muhammad Awwab!”.

Har cikin tsakkiyar kaina naji wannan kira. A wani irin slowly na ɗago manyan idanuna da ruwan hawaye ya jiƙe na zubasu cikin dara-dara ɗin cat ɗin nasa da blue ɗin ya fito sosai da ɗigo-ɗigon gold. Idan har kaga idanunsa haka to yana cikin matuƙar farin ciki ne babu wata damuwa a tattare da shi.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page Hundred

Kai jama'a 100 fa 😭

.....Kallon juna muke tsakkiyar ido tamkar zamu cinye kanmu. Ga numfashin juna muna shaƙa a lokaci guda. Cikin matuƙar sanyin murya ya furta, “Samrh! Kece ALJANNAR DUNIYA TA”.

“Nima haka Yaya Muhammad”. Na bashi amsa cikin karyewar murya. Kamoni yay gaba ɗaya na ya saka cikin jikinsa ya rungume tsam-tsam. Kafin ya shiga laluben lips ɗina ya haɗe da nashi. Wani kalar salo yake min mai gigita zuciya da matuƙar nuna sallamawa ga abinda ka yarda kake kuma matuƙar so da bege. Ban wani zauna ɓata lokaci ba na bashi dukkan amanna nima. Sai da ya tabbatar da kansa ya samu yanda yake so kafin ya barni muka sake rungume juna muna mai sauke ajiyar zukata a jere. Munja tsahon lokaci a haka kafin ya ɗagoni yana kallona. Murya a dasashe ya furta, “ALLAH yay miki albarka kinji”.

“Amin ya rabbi, tare da kai Yaya Muhammad”.

Idanu kawai ya ɗan lumshe min ya buɗe murya a ɗashe ya ce, “Salla”. Ban musa masa ba muka shiga toilet. Yanda nake ganin ko'ina ƙal nasan sakawa yay akazo aka gyara. Alwala muka ɗauro kawai muka fito. Kamar yanda ya ambata muka gabatar da salla har raka'a huɗu. Addu'a ya mana sosai dana sake tabbatar da yanada ilimin addini. Bayan mun idar ya buɗe ledar nan daya ajiye. Sai ga gasassun ƴan shila da akaima gyara na musamman a cikin takeaway. Kun san Sam-G ɗin taku yanzu babu abinda ta iya sai kwaɗayi, ai ƙagara ma nayi a fara ci. Da kansa ya dinga bani, shima yana ci, sai da mukai ƙat barema ni (Su Sam-G anga banza). Fuskarsa da ɗan murmushi ya ce, “Na biya bashin kazan al'ada ba?”.

Idanu na lumshe ina murmushi na furta, “Harda gyara ma”.

Sai kawai ya jinjina kai yana sake faɗaɗa murmushin sa shima. Taimaka min yay na cire kayan jikina shima haka muka tafi bathroom wanka. Dan na fara hamma barci kuma yazo. Baya wasa da hakan dan Doctor ya tabbatar masa ina buƙatar dinga samun isasshen barci a ƙalla na awa goma sha ɗaya kowace rana. Bayan munyi wanka da brush mun fito ya ciro kayan barci a wardrobe ya saka min, sannan

shima ya fita. Babu wani jimawa ya dawo cikin nasa kayan barcin harna kwanta ma ni. Fitilar ɗakin ya rage shima ya hawo saman gadon yana mai kwantar da kansa a saman filon da nawa yake. Tare da rungumoni jikinsa sosai. Ajiyar zuciya na sauke a hankali, dai-dai lokacin da yake kai hancinsa saman wuyana yana busa min numfashinsa da shinshinar wajen. Da sauri na ƙanƙame hannunsa dake saman cikina.

“Kin fara barci ne?”.

Kaina na girgiza masa.

“Bayan an kawo amarya ɗakinta, angonta ya bata kazan al'ada. Sunyi sallan godiya ga UBANGIJI miya rage kuma?”.

Jinai gaba ɗaya na daburce musamman yanda yake maganar a cikin kunnena da shinshinar sa yana kuma busa min numfashi duk a lokaci ɗaya. Muryata na rawa na ce, “Ba komai sai suyi barci su huta gajiyar biki”.

“Faɗi gaskiya dai?”.

A shagwaɓe na ce, “Da gaske”.

“Bashin kazan shi fa?”.

Ya sake faɗa cikin salon ruɗa min jiki. Da ƙyar na iya furta, “Ai ba bashi bane ƙyauta ne na tarba”.

“Ni dai nawa bashi ne a biyani”.

Ya bani amsa yana birkitoni jikinsa gaba ɗaya. Bamma san na shige ba kawai na ƙanƙamesa ina masa kukan shagwaɓa da faɗin wannan ai wayone kawai....

□□□□□

Tari ne ya hanata sukuni cikin dare, ga barci ta kasa saboda abubuwa sunma zuciyarta yawa matuƙa gaya. Gashi yau Ummanta ta wuce gida, tayi zaton Abba zai shigo ya kwana anan sai dai har yanzu babu shi babu alamarsa. Tashi tai ta shiga bayi, kawai sai tarin ya sake sarƙeta. Sai da tayi sosai hannunta a saman bakinta. Tana samu ya tsagaita ta janye hannun mi zata gani. Jini a cikin hannun nata. Wani irin tsargawa zuciyarta tayi. Tai tsai tana kallon jinin al'amarin kamar a mafarki. Jini fa? Mike nan? Mi hakan ke nufi?. Jitai gaba ɗaya tana neman susucewa ma. Tuni ta zame jaɓar ta zauna a ƙasan bayin wani zufa na keto ma illahirin jikinta dake tsumar rawa. Ta jima zaune a wajen batare data san makama ba. Kafin tai ƙarfin halin tashi ta wanke hannunta da bakinta da fuskarta ta fito. So take ko kuka tayi

kam yanzu amma hakan yaƙi yiwuwa. Haka ta ɗauki waya batare da duba ƙarfe nawa ba tai kiran Ummanta. Cikin alamun mai barci ta ɗaga daga can, sai kawai ta sakar mata kuka. Hankali tashe Umma ke tambayarta lafiya. Da ƙyar ta iya mata bayanin abinda ya farun. Ita kanta Umman daga can duk ta gigice. Sai maimaita kalmar, “Jini! Jini fa da Jalilah. Miya kawo jini kuma daga tari. Innalillahi wa-inna ilaihiraji'un na shiga uku ni Larai. Kinga yanzu dai ki kwantar da hankalinki dare ya riga yayi, kuma ko mijinki kada ki faɗawa da sassafe zanzo muje asibiti kinji ko”.

Mom na sharar hawaye ta ce, “To Umma sai kinzo”.

Koda ta yanke wayar sai ta faɗa saman gado kawai ta saki kuka, dan bata da abinda ya rage mata kuma sai dai kukan kawai. Al'amarin yaran nan su Samraah da Haihuwar nan ta Halime yayi masifar tsaya mata a zuciya fiye da komai. Dan shi kansa Musaddiq yaron gaba ɗaya ya sauya ya canja tamkar bashi ba. Sai ka ɗauka ama can ƙasar wajen yake rayuwa ba watanni kawai yay da tafiya ba. Hafizzullah ƙaraminsu na baya-baya da bama ta damu da shi ba shi kansa yaron baka gajiya da binsa da kallo yanzu. Balle kuma babbar giwa. Yarinya ƙarama jiba yanda take gara kan babban mutum irin Maash da manyan ƙasa ma ganinsa garesu aiki ne babba. Ai dolene ma a wannan al'amarin akwai aikin asiri. Bata yarda da tsohuwar nan ba Gwaggo Gudidi. Akwai abinda suka nemawa yarinyar nan ta mamaye Maash da danginsa. Kuma wlhy sai ta tona mata asiri dan sai inda ƙarfinta ya ƙare auren nan sai ya tarwatse. Bari dai tasan inda Baby take tukunna”. Sai kuma hawaye sharrrrr.....

Hummm Mom! Mom!! Mom!!!!!!

❣❣❣❣

Barci na sha sosai da safe dan tun bayan sallar asuba dana koma ban tashi farkawa ba sai sha ɗaya. Nayi mamakin ganinsa gefena shima yana barcin. Sai duk ya bani tausayi. Babu wanda baya buƙatar hutu a rayuwarsa. Sai dai kawai dan babu yanda za'ayi dole a haƙura. A gefe mutane sha'awarsa suke ya tara, a rayuwarsa kam cike take da ƙalubale da buƙatu kamar kowa. Na tabbatar inda zai samu dama zai kwanta a gida ya huta koda na tsawon sati ɗaya ne. Amma sam bashi da wannan damar. Koda ya gwada yin hakan bashi yiwuwa garesa, ni kaina matar tasa lokacinsa ƙayyadajjene a gareni. Numfashi na sauke a hankali, tare da kai lips ɗina saman small nashi na sumbata. Sai kuma na shige jikinsa kawai na rungumesa sosai. Saukar hannunsa a saman kaina, da yanda ya tura yatsun cikin gashin yasa na sauke ajiyar zuciya mai nauyi. Muryarsa a raunane cikin yanayin wanda ya tashi a barci ya furta, “Kin tashi?”.

Kaina na jinjina masa tare da sake shigewa jikin nasa na ce, “Amma kai bana son ka tashi yanzu”.

“Why?”.

“Saboda ina son ka huta Please. My Hot wlhy jikinka na buƙatar hutu sosai. Ka duba hanlin daka shiga wata huɗu da suka wuce saboda stress. Shike nan kullum kai ina zaka neman kuɗi, ina ka dawo neman kuɗi. Daga jirgi sai zaman mota. Ko lokacinka bana wani samu. Please kuna hutawa mana, duka rayuwan nawama yake wai. Mu gama nema da tara dukiyar mutuwa ta zo ta tsamemu a cikinta mu tafi kamar ba'a taɓa yinmu ba. Sai ma mun dace da haihuwar yaya na ƙwarai ne zamu tafi mubarsu da dukiyar su mana addu'a, wasu bishashar gabansu kawai itace damuwarsu. Please mu kasance tare kawai ni basai kaje ko ina ba”.

Na faɗa ina sake shigewa cikin jikinsa sosai. Shima sake ƙanƙameni yay yana sauke wasu irin ajiyar zuciya a jajjere. Kamar yanda nai tsammani baice komai akan batun ba. Sai taimaka min da yay mukayi wanka. Bayan mun gama kimtsawa falo muka dawo, banyi mamakin ganin an kawo mana abinci ba sai dai naji kunya dan daga gani daga gida ne. Haka na zauna muka karya koma nace ni na karya dan shi kam bana ɗaukar cin abincinsa cin abinci. Yanda bai nuna zamu bar gidan ba nima sai nake jin daɗin zama a cikinsa. Salla kawai ke fitar da shi. Ina ganin kiran su Aunty Falaq naƙi na ɗaga dan nasan tana can ta haɗa kai da Fahad iya shege zasu min. Hafizzullah dai gida muka barsa yaga Yaya Musaddiq ya nane masa.

Ba ƙaramin farin ciki na tsinta kaina a ciki ba da zaman gidan nan na yau. Sai la'asar muka fita, nazata ma gida zamu koma sai naga mun nufi wani waje daban. Ashe gidan Sheikh Muhammad ibn Khalipha Al-Hussain muka nufa. Acan muka samu su Ummie. Aiko sai naji duk na daburce. Ga Aunty Falaq ta sakani gaba da tsokana. Ummie dai da Mama murmushi kawai suke. ALLAH ya taimakeni Fahad ya shigo tare da Bahijja sai tsokanar ya koma kansa. Har dare muna a gidan Malam, koda muka baro can gidan dai muka koma ni da shi su Ummie kuma suka wuce can. Yau kam a ɗakinsa muka kwana, katifa ce kawai a cikinsa ƙatuwa. Nan ɗin ma mun kasance cikin farin ciki sosai. Washe gari babu barcin safe mukai shirin tafiya Gwarzo. A gidan Abba muka haɗu da su Ummie, nayi mamakin ganin harda Mom, sai dai daga gani bada son ranta bane ba. Dan ina ganin Abba na mata masifa, ga Ummanta tsaye galala tana bin Abban da kallo.

Mota duk muka shiga, dama shi Maash tunda ya fito ya gaida Abba ya koma ciki abinsa. Su Ummie kam bama su fito ba. Wajensu Gwaggo ta shiga. Aunty Falaq da mijinta sai Yaya Musaddiq. Hafizzullah da Fahad motarsu daban. Ni da uban tafiya sai TJ dake jan mu. Abba shi da Mom da su Bibaa sai Kawu Jafaru da muka ɗauka a hanya. Gaba da bayanmu motar guards ce. Ɗan kwanciya nayi a jikinsa dan shi yanata aikinsa ne a laptop. Tun ina kallonsa ina cin chocolate ɗin hannuna harna fara barci. Sai da ya ɗan motsani zai gyara min kwanciya na ɗan buɗe ido. Lumshe

mun nasa yayi ya sake buɗewa da faɗin, “Sleep” akan lips ɗin sa. Maida idanun mai kawai na rufe dan barcin nake ji sosai.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page Hundred & ***one***

Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....😉□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😉□□.

.....Mun iso tushe asali abin alfahari. Tarbar da muka samu ya sake tabbatar min da ansan da zuwanmu. Dan mun sami gidan Kawu Musa cike da dangi yayya da iyaye kamar ba safiya ba. Bayan gaishe-gaishe da yan koke-koken tuna mahaifinmu suka sake neman gafarar Mama Balki da Falaq. Kai tsaye sukace su sun yafe komai ya wuce. Suka kuma nuna farin cikin kasancewa a cikin yan uwa da yanda aka musu tarba ta mutuntawa da nuna ƙauna. Falaq nata kuka dan ita kaɗai tasan a kalar farin cikin da take a ciki yau ɗin nan. Abinda ta gama fidda rai da samunsa yau gata tsundum a cikinsu wato dangin mahaifinta, kuma kowa na nuna mata soyayya da ƙauna kamar za'a cinyeta dan kulawa, hakama little Awwab kowa nata ma yaron addu'a.

Su Kawu sun damƙa mata gadonta a hannu, yayinda Ummie ta damƙa mana alƙawarin mahaifinta. Sai zuciyar Abba ta sake karaya yau ma harda kukansa yana bamu haƙuri akan kuskuren da yay na salwantar mana da namu hakkin dake a hannunsa na mahaifinmu dana mahaifiyarmu. Dan gona ɗaya ta rage itama dan tana a hannun Kawu Sabi'u ne yana nomata shiyyasa Abban bai sayar ba, Mom kuma bata san da ita ba. A gaban kowa ya faɗi Mom ce duk ta dinga saka shi yin hakan, shi kuma a lokacin wlhy baya gane komai sai bin umarninta da sabon faranta ma zuciyarta. Kuka ta sanya masa wai ya kawota cikin danginsa dan ya tozartata ashe su sake ɗaukarta a wulaƙance. Babu wanda yabi takanta dama tunda muka zo duk ta kasa sakewa saboda da can ba zuwa take cikinsu ba, ba barin yayanta take su zo ba. Idan kuma su sunje ta wulaƙantasu da nuna musu ƙyama.

Dangin su Mamanmu ma da mukaje kasa sakewa tayi. Can ma mun samu tarba ta mutuntawa da girmamawa. Haka muka kasance cikin farin ciki a tsakkiyar danginmu. Sai naji kamar a barmu muɗan kwana amma nasan uban gayyar ba yarda zaiyi ba. Dan koda naima Ummie magana sai tace nayi haƙuri idan na haihu ita da kanta zata tsaya har sai nazo nayi sati da ga ni har Falaq. Na ɗan ji sanyi da jin hakan, falaq ma nata murna dan tana son zuwa ta kwana ɗin ko dan sanin kowa yanda ya kamata.

Yini guda muna a can, dan sai bayan sallar la'asar muka barosu suna kewarmu muna kewarsu. Ga uban alkairi naban mamaki da Maash yay musu. Ni kaina sai da naji hawaye sun cika min ido da alkairin nasa. Gashi an tsaida magana gobe idan ALLAH ya kaimu su Kawu zasu zo akai komai na Yaya Musaddiq dan Abba yaje yayi magana da iyayen Ruƙayya sunce su babu wata damuwa suzo kawai tunda dama sun san da maganar Musaddiq ɗin. Sai da muka raka su Abba har gida sannan muka wuce muma. Yau dai kam wajen su Ummie muka wuce. Gajiyar da kowa ya kwaso yasa ba'a zauna falo ba duk muka shige ciki. Ni wankan ma sai da tainakonsa nayi, dan barci kamar zan zube ƙasa nake ji..

WASHE GARI muka samu baƙuncin abokan aikina su Ruƙayya. Abin mamaki harda MD da kansa. Hayatu ne ya saukesu a falon baƙi. Aka kai musu kayan tarba kafin na kimtsa na fita tare da boss. Naji daɗin hakan da yay min, gashi maƙale da hannuna har muka shiga falon ko kunyarsu bai ji ba. Har su Ruƙayya sun miƙe da nufin zuwa su rungumeni suna ganinmu tare sukai surrender. Murmushi na musu cike da nuna jin daɗin ganinsu. Mutuniyata dai sai sinne kai take nasan kunya ce ta isheta. Niko sai na basar na haɗa su duka na nuna jin daɗin ganinsu. Cike da girmamawa MD da su Usman suka gaida Maash, nima muka gaisa harda cemun wai ranki ya daɗe. Ɗan hararsu kawai nayi bance komai ba. Kada na tanka cibi ya zama ƙari dan kafin mu fito harda gargaɗi a kan na kula yanzu ba da bace kada naje ina musu murmushi tunda harda maza. Ni dariya ma ya bani, amma dai na amsa dan a zauna lafiya. Mun ɗan taɓa hira da duk dai mai alaƙa da aiki ce. Shi dai baya saka mana baki sai idan yaso dan kansa. A hirar ne suke sanar min ashe MD yanzu baya wajen, an ɗan samu rikice ne ya ajiye aikinsa. Station ɗin ma yanzu neman durƙushewa take saboda sabon MD ɗinsu bashi da aiki sai wulaƙanta mutane. Ga son yaɗa labaran sirrin mutane, yanzu haka muma wai akan video da yake yawo a media na sayen agwalima da Yaya Awwab yayi yana nan yana shirya abu a kansa. Shiyyasa ma sukai azamar zuwa su gammu tun kwana biyu da suka wuce amma basu samu damar hakan ba sai yau.

Maimakon Maash ya tanka akan batun sai ya shiga yima MD tambayoyi akan ainahin masu companyn. Cike da girmamawa ya dinga bashi amsa. A mamakin mu da zasu wuce sai kawai yace MD ya fara shirin komawa aiki on Monday. Ba su ba hatta ni sai da na kallesa. Amma sai ya basar. Bayan wucewarsu naso muyi maganar sai bata yiwu ba saboda zuwan Yaya Musaddiq. Shi kuma suka fita shi da

Hayatu. Bayan la'asar koda suka dawo ya shigo ɗaki na biyosa da ruwa sai na samu ya shiga wanka. File ɗin daya ajiye a side drawer na ɗauka ina dubawa dan haka kawai yaja hankalina ganin tambarin gidan TV ɗin mu. Ba ƙaramin razana nayi da ganin sunana ba matsayin mamallakiyar gidan tvn. Zufa naji tana keto min, da ƙyar na iya controlling kaina na maida na ajiye yanda ya ajiye abinsa. Koda ya fito ban nuna masa na gani ɗin ba sai taimaka masa da nayi ya kimtsa muka fito falo dan yace zai ci abinci. Koda ya kammala cin abincin kuma hira da su Ummie dake falon ya ɗauke hankalinsa. Sai kuma ga kiran Uncle Abdullahi yana sanar musu ai ALLAH yay ma Arwa rasuwa yanzu babu jimawa. Ashe yarinyar jiyya take sosai zuciyarta ta kumbura. Sunƙi sanar mana ne saboda kunya da nauyin abinda mahaifinsu ya aikata mana da nata iyayen. Shi kuma Maash ko shigowa yay ƙasar baya zuwa asibitin ta yanda zasu gansa. A ɓoye yake zuwa ya duba Paah kawai ko shi Paah ɗin ma bai san da haka ba. Harga ALLAH bai taɓa maida hankalinsa kan yarinyar ba dan shi yama manta da ita sam. Iyayenta kuwa dama bai yaɓa sha'awar dubasu ba da Kakansa. Paah ɗin ma dan ya zame masa dolene yana kuma fatan sauke hakkinsa dake kansu matsayin mahaifi. Shiyya dukkan ɗawainiyar asibitin shike ɗaukar nasa batare da shi kansa Uncle Abdullahi ya sani ba. Dan bai hana a amshi kuɗinsu ba, amma yace su ajiye duk randa aka sallami Paah ɗin su basu abinsu.

Wannan rasuwa ta shigemu. Dan haka a ranar muka fara shirin wucewa dan Ummie ta roƙo Uncle Abdullahi da a jinkirta jana'izar har zuwa safiya ayi a Mansion. Ita yarinya bata da laifi, bata san komai ba akan abinda ya faru itama tsintar kanta tayi a tsakanin hakan. Idan ma za'azo dubi ta wani fannin ita aka cutar Haka kuwa akayi bayan sallar isha'i jirginmu ya wuce Lagos badan mun shirya hakan ba. Dan sati guda muka zo da niyar yi a Kano. Sai dai kana naka ne ALLAH yana nashi. Daga airport dai duk gida muka wuce, kowa kuma makwanci ya nema domin hutama rayuwarsa. Sai washe gari bayan sallar asuba aka kawo gawar Arwa gidan. Dangin iyayenta guda biyu sun iso daga ƙauyensu kasancewar tunda wancan zancen ya fasu ashe sunzo dama. Sai dai Uncle Abdallahi ya hanasu zuwa Mansion, da suka dawo kuma a lokacin mu mun wuce Spain. Mama Balki tai mata wanka da kakarta data haifi Hajiya ƙarama. Aka shiryata aka kaita makwancin ta na gaskiya. Duk da Arwa yarinya ce sannan uwarta kawai ta sani a gidan mutuwar ta shigi su Mama Balki sosai. Ita Ummie ba wani shaƙuwa sukai ba amma taji rasuwar. Ni kaina da ban taɓa damuwa da shirgin yarinyar a gidan ba sai da rasuwar ta dakeni. Hakama Maash bai dai ce komai ba face yimata addu'a amma nasan koyaya zai ji, dan yarinyar harga ALLAH tana masa kallon ɗan uwane kamar uba ɗaya. Duk da itama ya jima da fahimtar take-takenta na son shi. Abin mamaki sai ga su Azizat sun zo daga Niger suma a washe gari. Azizat tayi kuka sosai dan kowa yasan a gidan suna shiri matuƙa da Arwa. Duk da shirin nasu baya wuce akan a ƙuntatama Malika ko yanda za'a shawo kan Maash dai. To koma dai yayane ita dai ta tafi ta huta kuma. Sai fatan ALLAH ya gafarta mata kurakuranta da namu dana iyayenmu baki ɗaya...

Rasuwar Arwa tayi matuƙar jijjiga iyayenta. Musamman ma Hajiya ƙarama. Dan a wannan ranar likitoci kwana sukai kanta tanata wani irin kuka da aman jini. Ɗayan

ɓarin jikin ya ida mutuwa. Dama ga allurar poison ɗin da Prof yay mata ta fara aiki kaɗan-kaɗan kamar yanda wadda tai masa shi tuni ma ta gama masa illa. Haka dai aka sakata barcin dole har washe gari da aka bizne Arwa bata farko ba. Shima dai Commondo yaci kuka rurus. Dan duk da bai taɓa nuna damuwarsa akan yʻar tasa ba yana matuƙar sonta da ƙaunarta. Yana gani ko wahalar da ya sha a rayuwa zata tafi a banza a ƙalla dai ya bar mai masa addu'a. Dan koda ta masa abinda ya sakashi shiga a wannan halin bai taɓa jin soyayyarta ta ragu masa a zuciya ba. Ashe itace zata fara tafiya ta barsu, inama shine ya tafi ba ita ba. Kaicon wannan mummunar rayuwa tasu mara ƙyaƙyƙyawan tarihi da alƙibalar gani a koya.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page Hundred & two

.....Har akai sadakar uku jikin kowa dai a sanyaye babu wani ƙarfi. Dangin su ma sukai shirin kama gabansu. Dan sun san anmusu halacci. ALLAH sarki Ummie, bata barsu haka ba sai da ta musu alkairi. Suka tafi suna mai sanya mata albarka da addu'oin fatan alkairi har ma damu kammu. Sun wuce da safe gidan ya sake komawa shiru. Dan su Azizat dama ba'a nan suke kwana ba can wajen mahaifiyarsu gidan Prof da safe su zo su koma can da yamma. Batare da mun sani ba washe gari akace mana sun wuce. Ita dama Hajiya Mammah tun randa akai jana'iza da tazo bata sake zuwa ba saboda kunya ne ko munene dai oho mata. Da yammacin ranar tafiya ta tasowa Yaya Awwab, haka ina fushi da kumbure-kumbure suka wuce shida PA ɗinsa da ƙandarariyar baturiyar nan dana tsana. Yanda take wani kwarkwasa da iyayi agaban Yaya Awwab na ƙona min zuciya. Bandai ce komai ba amma ALLAH idan bata kiyayeni ba sai na mata zanen yarabawa. Bayan wucewarsu gidan sai ya

sake koma mana shiru, sai kawai na tattara na koma sashen Ummie dan bazan iya zaman sashen ni kaɗai ba. Ashe can ma Aunty Falaq ta gudo wajen Ummie ɗin. Dariya Ummie taita mana wai mu ragayen mata ne. Daga maza sun tafi sai mu gudo wajen Mamanmu. Shagwaɓa muka dinga mata tana biye mana. Ita dai Mama ido kawai take saka mana.

Muna waya da yan Kano, Musamman Yaya Musaddiq da Hafizzullah da Abba. Sai aunty Halima sabuwar ƙawarmu. Dan yanzu mun ɗinke da ita kamar ba matar Abbanmu ba. Bahijja ma na Kano maƙale bata dawo ba. To batun dawowar tatama dai sai da aure a kanta. Dan an gama tsaida magana bikinsu za'ai kawai da Fahad a huta kafin mu koma. Sai yanzu ne ma nake jin batun komawar tamu Spain. Harga ALLAH na ɗauka mun dawo gida kenan. Kasancewar a gari ɗaya Abba ke cemin an saita bikin Yaya Musaddiq da na Fahad ɗin rana ɗaya. Nan kuma da kwana goma ne idan munada rabon kaiwa. Ba ƙaramin farin ciki na tsinta kaina ba da wannan labari. Na kira Ruƙayya naita mata tsiya, dan yanzu muna waya kullum da chart amma bata sanar min ba. Shima Yaya Musaddiq ɗin ya mun bayani duk yanda sukai da Yaya Awwab. Ya ɗauki komai na bikin ko naira ya yace baya son wani ya sanya. Harda hawayensa dan video call muke a lokacin, sai nima kawai na sanya masa kukan. Dole ya danne nashi ya koma lallashina.

Kasancewar biki a ƙurarren lokaci mukai tunanin fara shirye-shirye ni da aunty Falaq. Dan ango dai Yaya Awwab ya tasa ƙeyarsa da shi aka tafi. Sai dai kwanansa uku sai gashi ya dawo. Maimakon Lagos sai ya sauka a Kano. Da daddare sai gashi tare da Hafizzullah. Mamaki ya kama mu dan munsan dai Hafiz na Kano. Sai cewa Fahad ɗin yay yaje ya ɗakkosa ne su fara shirin biki. Cikin harara nace “Wannan ɗan yaron? ina abokanka”.

Sai kawai ya nuna Hafiz ɗin, wai ai shi shine babban abokinsa. Rasama abin cewa mukayi, sai Mama da Ummie ne ke mana dariya. Babu yanda muka iya dole muka shiga hidimar tsare-tsaren bikin tun a ranar. Washe gari da yamma Yaya Awwab yay kirana wai mu shirya za'a kaimu airport zuwa dare. Da mamaki na ce “Airport kuma Yaya Muhammad yin me?”.

Kai tsaye ya bani amsa da, “Zaku same mu a Dubai ke da Falaq”.

Rasama abin cewa nayi nikam. In ba masu abu da abinsu ba irin wannan yanke wannan hukunci kamar wanda ke Katsina zashi Kano. Babu yanda muka iya muka shiga shiri. Ummie nata faɗa wannan wace irin tafiya ce ni ina fama da kaina falaq ga ƙaramin yaro. Mama dai ta bata haƙuri akan tunda sunce muje mu tafi ɗin kawai. Haka dai Ummie ta barmu. Babu abinda muka ɗauka daga mu sai kayan jikinmu da handbags. Hafizzullah da Fahad suka kaimu airport. Fahad sai lallaɓamu yake wai mu zaɓoma matarsa kaya na kece raini. Muna isowa bamu fi mintuna talatin ba aka ɗauke mu. Banyi mamakin ganin mu kaɗai ba a jirgin sai wasu tsirarun mutane.

Dan zuwa yanzu na sake fahimtar wanene mijina. Tabbas ALLAH ya musu baiwa ta dukiya, sai dai fatan ALLAH ya kaimu aljanna kuma...

Mun iso Dubai lafiya. Sai dai ni naɗan jigata kaɗan dan banda juriya yanzu sosai, dama kuma tun jiya bana jin daɗi dauriyar kawai. Hayatu ne yazo ta ɗaukemu, sai naji haushin rashin ganin ogan nasa. Amma dai bance komai ba har muka iso gida. Gidane mai ƙyau sosai da yaji kayan more rayuwa. Shima Hayatun na ajiyemu yace zai koma wai meeting suke can ma ya bar ogan nasa kuma yana jiransa ne. Takaici yasa naƙi tanka masa. Sun san basu da lokacinmu suka kwasomu zuwa nan kara tsaye. Yanda nake kumbure-kumbure yasa Aunty Falaq tambayata lafiya. Cikin ɓacin rai na amsa mata da, “Aunty dan ALLAH wane kalar wulaƙanci ne haka. Sun san suna da abin yi suka kwasomu. Nifa ALLAH bazan jure wannan abun ba. Kayi aure dan ka kasance da mijinka akoda yaushe amma sam bashi da isashen lokacinka. Yau yana wannan ƙasa, gobe waccan, jibi meeting, gata taron ɣan kasuwa. Citta kaza, kanumfari kaza”.

Dariya sosai ta sanya min, ta ce, “Oh oh little sis.. irin wannan lissafi haka. Lallai akwai aiki kenan. Ashe ke bazaki iya jure abinda na jure ba. To wlhy Yaya Hayat ko satin amarci bai cika mun ba suka bar ƙasar nan. Kwanansa biyar inaga. Da ya tafi ban gansa ba sai bayan sati uku. Nana ma sukai kwana ko huɗu ne da ƙyar suka sake tafiya. Nifa a ɗan zaman rikice-rikicen nan ne ma zance miki mun taɓa zaman sati ciff yana gida sai dai ya ɗan fita ya dawo sabgar wuni. Ya xamuyi tamu ƙaddara kenan, mata a waje gani suke mun gama morema duniya da komai na cikinta. Nan ko mu muka san ƙalubalenmu. Samraah kafin nayi aure babu abinda nake buri kamar naga koyaushe ina tare da mijina muna tattalin juna. Sai dai da safe na shiryashi ya ɗan tafi harkokinsa zuwa la'asar ace ya dawo mun kasance tare har wata washe garin, weekend kuwa ya zama salla ce kawai zata fitar da shi. Amma a satin farko na fahimci wannan burin nawa ya zama tarihi ba kuma mai tabbata bane. Tun ina damuwa da yawan fushi harma na haƙura dan bani da yanda zanyi. Dan haka kema haƙuri zakiyi, a hankali zaki saba da duk wannan rashin kasancewar tasu tare damu mu itace babbar ƙaddararmu a gidan aure. Muma godema ALLAH da ya kasance yanzu gamu a tare, ga kuma iyayenmu guda biyu ga Baba suna ɗebe mana kewa.”

Ta ƙare maganar tana ja min kumatu na. Baki na sake tunzurawa, dan nikam gaskiya bana jin zan iya dauriyar nan. Kawai azo ayita da wajewa ga lokacin tafiya gana zaman gida. Amma dai bance mata komai ba. Wanka muka farayi muka ɗan tsakuri abincin da muka samu an kawo mana. Ni kawai ma sai na kwanta abina dan barci nake ji sosai.

Ba ƙaramin ƙarin takaici naji a zuciyata ba sanda har na tashi naga babu shi babu alamarsa. Sai ma Aunty Falaq ce ta shigo tace na shirya wai Yaya Hayat ya

kirata nan da awa ɗaya za'azo a ɗauke mu mu sameshi kasuwa. Baki na buɗe kamar zanyi magana sai kuma nai shiru saboda ƙwallar da suka cika min ido. jinake kamar nace babu inda zanje sai dai na daure kawai nai shirin cikin doguwar rigar data kawo min. Amsar little Awwab nai a hannunta muka fito, babu wanda yay magana a cikinmu bayan amsa gaisuwar Balaraben da yazo ɗaukar mu ya buɗe mana bayan motar muka shiga. Tafiya ce ta yɝan mintuna ta kaimu haɗaɗɗe kuma makeken shagon da baida iyakar labartawa. A can muka samu Yaya Hayat. Bayan mun gaishesa ya amshi Awwab a hannuna yana tsokanarmu. Murmushi kawai nayi ni dai bance komai ba, sai aunty Falaq ce ke kare mana. Saka Awwab yay a irin yɝar jakar goyon nan ta yɝan gayu a ta cikinsa, mu kuma muna biye da shi har cikin shagon.

Bayan ya mana bayanin kayan lefen Yaya Musaddiq da Fahad zamu haɗa da wasu kuma daban aunty Falaq ke tambayarsa “Wai Yayana fa? Tunda muka iso bamu ganshi ba”.

Cikin ɗan shafa kai ya ce, “Ai wlhy yama bar Dubai ɗin nan awa ɗaya data wuce. Amma dai zai dawo kafin mu wuce dan tare da shi zamu wuce Nigeria. Jinai hawayen da nake ƙoƙarin riƙewa sun zubo min, da sauri na kauda kaina gefe na share su. Komai ban ce musu akan batun nasa ba, suma kamar sun fahimci yanayina sai suka bar maganar muka fara abinda ya kawo mu. Yin komai nake zuciyata babu daɗi, yanzu na yarda da batun mutane da kance da zarar ka samu ciki mazan nan sun bar batunka, musamman masu kuɗin nan sunfi bama dukiyarsu muhimmanci fiye da matansu. Banda ma wulaƙanci irin na mutumin nan, ina cikin wannan halin ya raboni da ƙasata cikin gaggawa babu shiri, nazo kuma inda yake yana garin bawai baya nan ba, amma bai nema inda nake ba balle ya kira yaji yaya muka iso, bai kuma zo inda nake ba bayan ya gama uzirin da yake ya sake taka jirgi ma yabar ƙasar. Harga ALLAH na tsani wulaƙanci, ni mace ce mai son kulawa. Bawai dukiya da samun duk abinda nake so ne matsalata ba. Ina buƙatar tattali a koda yaushe da nuna damuwa ga abokin rayuwata, idan kuma abinda ya kamata na fahimta ne a fahimtar dani zanyi uziri. Munyi siyayya sosai, gajiyar da jikina ya nuna yasa Yaya Hayat yace mu bari haka sai gobe in ALLAH ya kaimu. Muna zuwa gida kobi takan abubuwan daya saya mana na ci banyi ba na wuce ɗaki na kwanta. Sai da aunty Falaq taga ban fito ba ta biyoni da shi. Kin motsawa nayi sai ta ɗauka barci nakeyi harda gyaramin blanket ta fita. Shigowarta biyu ina mata haka, daga ƙarshe dai ta haƙura ta kawo min duk abinda zan buƙata ta tafi itama ta kwanta. Har cikin dare sosai ina kallon waya da tunanin zai kirani ya bani haƙuri da faɗa min uzirinsa, amma shiru. Sai kawai na sanya kuka. Sai da nayi mai isata sannan na tashi zuwa bathroom nai wanka na fito, daurewa nayi naci abinda Aunty Falaq ta ajiye min dan yunwa nake ji sosai. Ina kammalawa na ɗauki wayar kamar zan kirashi wata zuciyar dai ta gargaɗeni na ajiye na kwanta. Sai kuma dai na ɗauka na kira shin har sau biyu ba'a ɗaga ba. Haushine ya sake ƙuleni na ajiye wayar..

Washe gari ma har mukai shirin sake fita babu kiransa. Na kai ƙololuwar shiga ɓacin rai musamman lokacin da muke tafiya a mota da naji Hayat na waya da shi. Wato nice mara amfani kenan. Shike nan zan nunama mutumin nan na haifu nima. A ranar muka gama sayyar duka. Yaya Musaddiq da Fahad set uku-uku na akwatina. Sai kuma set huɗu daban da bamu san kona waye ba. Sai muma muka ɗauki abinda muke so ko nace Aunty Falaq da Yaya Hayat suka zaɓa mana ni takaici yasa ma komai baya birgeni. Tun aranar sukam kayan aka wuce da su Nigeria. Mu kuma Yaya Hayat ya tafi damu yawo. Ni sam ba daɗin yawon nake ji ba. Nadai dake ne kawai ban nuna musu koda a fuska ba.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page hundred & three

Ina miƙa saƙon ta'aziyya ta ga yan uwa masoyan mu dake ƙoƙarin bibiyarmu ta rasa yar uwarmu da mukayi RAHAMA NALELE. Ya rabbi ka gafarta mata, ka yafe mata kurakuranta, kasa kabari ya zama wajen hutu a gareta, da iyayemu baki ɗaya. ALLAH ya raya abinda ta bari ka albarkaci rayuwarsu. Ka bama iyayenta da yan uwanta haƙurin rashinta da mu baki ɗaya. Ida tamu tazo muma ALLAH kasa mu cika da imani. Dan girman ALLAH, dan girman ALLAH, duk wanda yake ji a ransa ta taɓa masa ba daidai ba ko wani kuskure da ita bama tasan ta masan ba ko akan sani muna roƙonsa ya yafe mata. Ko sau ɗaya ne kuma a matsayinki na masoyiyar mu dan ALLAH ki mata addu'a a cikin sallarki, idan kin samu dama kiyi sadaka da fatan yaje gareta koda kaɗan ne 😭□. ALLAH ya gafarta mana baki ɗaya.

.....Yau ɗin ma a gajiyen muka dawo, dan ni harda ma ɗan guntun zazzaɓi na. Shayi kawai nasha na tafi na kwanta na barsu anan falo. Haka na tashi har washe gari zazzaɓin na damuna. Ban gaya musu ba, sai aunty Falaq ce data ɗan fahimci kamar bana jin daɗin take tambayata. Murmushi kawai naɗan mata da bata amsa da, “Kawai dai yanayin ne Aunty”.

“Uhm yanayi, ko kuma Baby na ne dai? Ko Yayana ake kewa”.

Murmushi kawai nayi yanzun ma ina ƙoƙarin kai fruit ɗin da ta yanka min sukai ƙyau a cikin bowl baki na. Dai-dai nan Yaya Hayat yay sallama. Itace ta amsa idonta a ƙofa, ni kam a zuciya na amsa ina mai gyara zaman gyalen dana yafa saman kaina ya sakko min har kafaɗa. Bai shigo ba sai da tace, “Bismillah”.

Yana buɗe ƙofar ƙamshin turaren da ko'a barci nake najisa nasan na waye. Sai da zuciyata ta motsa. Amma na dake batare da na ɗago ba na cigaba da shan fruit ɗina. Yayinda Aunty Falaq ke masa sannu da zuwa da gaishesa. Amsa mata yay da kulawa, yana tambayar Awwab. Da girmamawa tace masa barci yake yi. Da ga haka ta miƙe ta nufi kitchen. Jin kaifin idanunsa a kaina yasa na kasa jurewa, kaɗan na ɗago sai na samu idon nasa ne kuwa a kaina. Yana sanye cikin wandon jeans navy blue da hi neck riga black data masa ƙyau sosai ta kuma kama masa jiki, sai black jacket ɗinsa a saman kafaɗarsa ya ratayeta da hannunsa. Cikin abinda bai fi sakan biyu na masa kallon ba a kaikaice ta yanda shi kansa bai zama lallai ya lura shi ɗin na kalla ba na maida kan Yaya Hayatu. Gaishesa nayi ya amsa min da kulawa yana tambayata gajiya nace Alhmdllh. A dai-dai nan Aunty Falaq ta fito da tray ta ajiye gabana, batare da tayi magana ba tabi bayan mijinta daya kama ƙarfen stairs zai haye. Tare suka haura, niko na cigaba da shan fruit ɗina kamar ban san da mutum a wajen ba, sai bayan kusan minti ɗaya da wucewarsu na ce, “Ina yini”.

A mamakina sai kawai naji an gittani an wuce batare da ya amsa ba. Ta gefen ido na bisa da kallo wani irin tuƙuƙi na riƙe maƙoshi na, ɗakin da nake kwana ya shige abinsa. Ƙofar na ɗan harara na cigaba da shan fruit ɗina. Sai dai me, gaba ɗaya kuma sai naji ya fita a raina. Dangwarar da bowl ɗin nayi na zame a kujerar na kwanta. Tun ina ƙirga mintuna zai fito harna koma lissafin rabin awa. Jinai zuciyata ta ƙara yin ƙunci, lallai mutumin nan ɗan wulaƙanci ne. Amma bari naga iya gudun ruwansa dai kafin na yanke masa hukunci. Minti talatin ta zama awa guda, sai ma barci ya kwasheni a wajen batare dana shirya ba....

Ransa a dagule ya dawo Dubai ɗin nan kamar yanda ya barta cikin ɓacin rai. Dan akwai kayansa daya kamata tun six days ago ace suna Nigeria kawai ake sanar masa wai an riƙesu a ƙasar Camaroon. Yayi iya ƙoƙarin sa ta hanyar waya dan ganin kayan sun isa saboda muhimmancinsu da mabuƙata kayan dake jira amma sai wani banza ke raina masa hankali. Gashi anan Dubai ɗin ma abu mai muhimmanci yake yi. Ga matarsa na hanyar tahowa. Duk da yaso ace da kansa yaje tararta hakan bai yiwu ba, dan yayi zaman meeting da wasu manyan ƴan kasuwa

na duniya akan wasu matsaloli. Yana cikin meeting ɗin ya samu saƙo wai ana neman juyar da jirgin kayansa inda ya fito an hanashi ƙarasawa Nigeria. Dole yay excusing kansa daga wajen Meeting ɗin cikin abinda bai fi awa ɗaya ba yabar Dubai ya nufi Camaroon ɗin. Tunda yaje can bai huta ba, yanata faman kaiwa da komowa shi da lawyers nashi dan ƙulli ne babba ake neman masa da gwamnatin ƙasar. Sai a yau ya samu kansa kayan suka wuce Nigeria, ko tabbatar da tashin nasu baiyi ba ya fallo ya koma Dubai ɗin dan hankalinsa duk hana kanta. Shine ya iso da ɗokin ganinta amma ko ɗaga kai ta kallesa ma batai ba. Yaso mata uziri sai yaga kawai ta ɗago ta gaida Hayatu batare da shi ko ma kallonsa tayi ba. Wane kalar wulaƙanci ne hakan, matarsa, da ya ɗauka dukkan kansa ya bata da kowane irin matsayin girmamawa. Kai ina baya son raini kuma sam. Koda wani laifi ya mata ya kamata ta haɗiye a gaban koda Ummiensa ne sai sun keɓe ita da shi ta faɗa masa ko ta nuna fushin da shi, idan ba ban haƙuri ne zai bata, idan na ya fahimtar da ita ne zai yi ƙoƙarin hakan. Amma har yanzu bata san wanene shi ba.

Wankansa yayi ya haye gado yay kwanciyarsa. Dan kwana biyun nan sam baya ko isashen barci, ga wata yunwa da yake ji mai tsanani amma yafi buƙatar barcin dai first. Barcin kusan awa biyu yayi alerm ya tada shi, ganin lokacin salla yayi ya miƙe da ƙyar zuwa bathroom. Ruwa ya sake watsama jikinsa dan ya warware da ƙyau, yay alwala ya fito. Yana ƙoƙarin saka kaya ta shigo ɗakin, bai nuna yasan da shigowar tata ba kamar yanda itama ta nuna bata san da shi ba tai waucewarta bayi. Sai da ta shige ya zubama ƙofar cat eyes ɗinsa da suka sauya kala. Komai baice ba ya saka sallaya ya kabbara salla. Bayan ya idar tana daga gabansa tana tata ya ɗauka waya yay kira. Cikin harshen larabci yay magana da bata wuce ta sakan huɗu ba ya ajiye yana miƙewa. Bakin gadon ya koma ya zauna yana latsa wayar, mintuna kusan goma aka danna door bell ɗin gidan, tashi yay ya fita, babu jimawa ya dawo ɗauke da ƙyaƙyƙyawan kwando a hannu. Cikin set na kujerun da aka ƙawata bedroom ɗin dasu ya koma ya zauna, bayan ya mata kallo ɗaya ya ɗauke kansa, dan har yanzu tana a saman sallayar bata tashi ba. Abincin da aka kawo masa ya ɗan tsakura kaɗan ya ture...

Dai-dai nan na tashi daga zaman sallayar daya ishe ni. Veil ɗin kaina na warware, yanzun ma batare dana kala inda yake ba na nufi ƙofa zan fita amma sai na jita a rufe. Mamaki ya kamani dan nasan dana shigo dai ban kulle ba. Numfashi na ɗan furzar na koma kawai saman gadon nai kwanciyata. Ina kwance kamar mai barci sai dai idanuna ne kawai a lumshe naji alamar tsaiwar mutum a kaina. Sai ƙamshin turarensa daya cika min hanci matuƙa. Kamar zan share sai dai na buɗe idanun. A kansa na sauke su, ganin yanda ya wani kafe cikina da ido yasa na yamutse fuska. Kamar na balla masa harara sai dai na daure na sake maida idanun na rufe. A matuƙar mamaki naji saukar muryarsa a kaina wai yana da buƙata..

Kutumelecy ban taɓa sanin guy ɗin nan tantiri bane sai yau. Kasa jurewa nayi na buɗe idanuna a kansa jin ya kwanto gefe na. Sai kawai na yunƙura zan bar masa gadon. Ya maida ni ya kwantar. Ƙoƙarin turesa na shigayi sai dai ko gezau. Ƙarshe takaici yasa na sakar masa kuka. Amma hakan bai sakashi fasa abinda ya ambata

ɗin ba. Sai dai duk yanda yaso ya samu haɗin kai daga gareni bai samu ba. Bai kuma fasa bina a cikin nutsuwa ba. Niko tunda ya barni sai na juya masa baya kawoi ina raira kuka. (Wato bily fushin mai ciki sai addu'a kawai, dan har cikin ƙasan raina haushinsa nake ji). Yanzun ma komai baice min ba ya ma tashi ya wuce bathroom abinsa. Aiko na sake hawa fummm...

Haka yayo wankansa ya fito, sai da ya kammala gyara jikinsa cikin bada umarni ya da dakewar nan tasa a daƙile ya furta, “Five thirty zamu wuce”. Daga haka yay ficewarsa. Yau na sake tabbatar da rayuwar aure haƙuri ce kawai. Duk kuma daɗinka da miji sai ya baka wannan maɗacin. Nima ji nake ƙasar kawai nake son bari, sai kawai na miƙe na gyara jikina na shirya. Sai da nai sallar la'asar na ƙarasa kimtsawa na fito duk da da sauran lokaci. Babu kowa a farlon sai television, na wuce na ɗauka ruwa na koma na zauna a kujera. A haka su Aunty Falaq suka fito suka sameni suma cikin shiri. Damuwata na haɗiye na ɗauka Awwab dake ƙusha ƙushin kuka. Batare da mun zauna ba duk da saura kusan mintuna arba'in Hayatu yace muje anzo ɗaukar mu. Nayi zaton shi yana waje, amma sai naga mu kaɗai ne muka shiga motar, koda muka iso airport ma babu shi, sai da muka shiga jirgi bayan cikar lokaci mun zauna sai gashi ya shigo shi da Juliet. Dama a wuya nake, ga shi kuma da wannan shegiyar ƙandararriyar baturiyar. Su duka ban kallesu ba, sai da ya zauna a kusa da ni cike da iyayi ta ce min, “Good evening” tana ranƙwafowa da tab a hannu wai zata nuna masa abu.”

Ai bamma san na buga mata wata tsawa ba cikin rufewar ido na furta, “Hy bar nan!!”.

Ba ita ba har shi uban gayyar sai da ya kalleni. Na watsa musu harara su duka yayinda ita jikinta ma ke rawa. A daburce ta shiga bani haƙuri da ƙoƙarin mun bayanin abu zata nuna masa mai muhimmanci. Nima sai na sake fusata na ce, “Okay bazaki tafin ba kenan ko?”.

Zata sake magana yay mata nuni data wuce. Sim-sim ta tafi har tana waigena. Na sake balla mata harara sai ta zabura da sauri ta ƙarasa ficewa a wajen. Ƙwafa nayi da faɗin, “Da ki tsaya mana. ALLAH da sai an fitar da ke a karye daga jirgin nan. Ki cigaba da shiga mun hanci karki fasa ramammiyan banza jiki duk ƙashi ko ƙyan kallo babu subi su nanewa mazan mutane da sunan aiki mayu”.

Gyaran murya ya ɗan yi. A fusace na juyo ina hararsa. Na ce, “Oh ko zaka shigar mata ne?”.

Kansa kawai ya ɗan jinjina min alamar a'a, idanunsa dake wani lullumshewa a kaina ƙyam. Cikin masifar dai nace, “Aida ka shigar mata duka zan iya daku”. Na ɗauke kaina nama kwanta ina wani buɗewa da ƙyau yanda zanji daɗi.

Ta gefen ido yake kallonta sai yaji abin ma ya koma bashi dariya. Ya dai dake baiyi ba, sai ya ɗan murmusa kaɗan da girgiza kansa yana ɗaukar tab ɗin gefensa ya shiga daddanawa, dan akwai abinda yake son bincika a google.....✍

😂 ALLAH sarki Yayanmu Sarkin haƙuri. Dangin Sam-G magana ta gaskiya ku sake mata karatun aure, mu bama son Hayaniya da raini😊.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page hundred & ***four***

Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....😉□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😉□□.

.....Har muka iso Nigeria ban shiga sabgarsa ba bai shiga tawa ba, koda yake ma ni barcina nasha sosai har muka iso. Su Fahad ne sukazo tarbar mu da Guards ɗinsa. Ɗan barcin da nayi yasa jikina duk babu wani ƙwari, dole na bari ya riƙo min hannu muka fito. Muna shiga motar ma idanu na rufe kawai har muka iso gida. Kafin kowa ya fito ni na fita, na shige jikin Ummie da Mama da suka fito tarbar mun. Faɗan yanda jikina ya ɗauki zafi amma suka taho da ni haka Ummie da Mama keyi. Falaq tace ai ban faɗama kowa banda lafiya ba fa, har Yaya Awwab bata tunanin ya sani. Kallonsa Ummie tayi cike da tuhuma. Sai maimakon yace wani abu akan hakan sai cewa yay, “Ummie good night”. Ya wuce warsa. Duk binsa sukai da kallo, na balla masa harara da murguɗa baki.

Babu wanda yace komai Ummie tace muma muje mu huta kowa tasa an kai masa abinci bedroom. Ni dai badan naso ba na tafi sashen namu, ɗakina kuma na shige, komai fes an gyara min, wanka kawai nayi abuna nai shirin barci. Yunwa nake ji amma bazanje ɗakinsa ɗibo abinci ba dan na fahimci can Ummie tasa aka kai. Sai nayi kwanciyata. Ko minti huɗu banyi da kwanciyar ba ya shigo ɗakin, ƙin

motsawa nayi balle yama san idona biyu. Babu zato kawai naji an ɗaukan camak an fice. Watsal-watsal nake da ƙafafu ina kaima ƙirjinsa ƙananun duka da faɗin, “Ni ka sauke ni, ALLAH zan maka ihu”. Ƙin kula ni yay yaƙi kuma cewa ko ci kanki har sai da ya kaini bedroom ɗinsa ya dire a gado. Kuka na fara masa yaƙi kulani sai abinci ma da ya ɗibo ya dire a gabana.

“Ni banzan ci ba. Kuma ka buɗen ƙofa na koma ɗakina dan bazan kwana anan ba.”

Ƙafarsa ɗaya dogare da gadon ɗaya a ƙasa ya kamo haɓata yana mai ranƙwafowa kaina. Cikin wani ɗan iskan salo idanunsa sarƙe da nawa a saman lips ya furta, “Garama kici, dan rashin cin bazai hana na nema hakkina ba. Ɗaki kuma na ɗaureki ne?”. Ya ƙare maganar cikin ɗage gira. Baƙin ciki yasa ni kaima hannunsa wawura zan ciza. Ai babu shiri ya janye jikinsa da waro idanunsa waje. Na balla masa harara da murguɗa baki na ce, “Da ka tsaya mana”.

“ALLAH ya shiryeki”.

Ya faɗa yana tura hannayensa duka cikin aljihun wandon pyjamas ɗin sa. Baki na tura da jawo abincin na hau ci ban sake kulashi ba. Ina jina nayi dam na sauka nayo brush. Gadon na haye nai kwanciyata ban kulashi ba. Shima baice min komai ba yana zaune yana kallona kawai. Cikin barci na jisa a gefena ya sakani a jikinsa. Sai kawai na sake shigewa nima. Da safe kuma ba kunya na ɗora da fushina nama bar masa ɗakinsa sai a sashen Ummie muka haɗu wajen breakfast...

Shirye-shiryen biki sun kankama sosai. Muna shirin wucewa Kano saboda Ummie tace gara kawai muje can ɗin ayi komai tunda muɗin duk anguna ne. Hakan yamun daɗi sosai. Dan har gyaran jiki nake son muyi aunty Zakiyya ta gama shirya mana komai. Har yanzu ni da mutumina dai ana ƴar share juna. Sai dai shifa hakan baya hanashi zuwa yasha bidirinsa a jikina. Duk kukan dazan masa kuma bazai kulani ba. Randa su Ummie zasu wuce Kano sai ya nuna wai suyi gaba ni daga baya zamu taho tare da shi. Aiko na sanya kuka sosai. Harararsa Ummie tayi, amma ya fiske abinsa yaƙi cewa komai. Daga ƙarshe ma ya tashi ya fita a falon dama muna a babban falo ne mu duka. Zan ɗaga hankalina Ummie tace karma na damu kaina na barta da shi. Ban san yanda suka ƙare ba washe gari muka wuce da su Ummien. Mun isa Kano cikin aminci, bamu wani zauna ba muka hau gyaran jikinmu dan nan ƙanwar mijin Aunty Zakiyya tazo ta same mu. Ta kuma zuba mana wani shegen lalle daya amsa suna lallale tamkar ka cinyesa saboda ƙyau. Da dare sai ga su Fahad da ɗinkunanmu. Nayi mamaki sosai dan ni bamma san an kai ba. Ashe wannan aikin Ummie ne. A ranar da yamma dole naje can gidan Abba ni da Aunty Falaq. Can ma dai shirye-shirye sun kankama. Dan su Gwaggo Gudidi na gidan ita da aunty Halima ke komai. Wai Mom taƙi shiga tace tun farko ai ba'aso a ganta a ciki ba tunda ba'a sakata ba. Kobi takanta banyi ba ma ni kam yau dan al'amarin nata ya fara bani takaici. Muka zube musu kuɗaɗe masu yawa ni da Falaq domin

amfani. Hakama Abba mun bashi isasun kuɗi da zai yi hidima, sai ya kama hawaye yana sanya mana albarka. Bamu baro gidan ba sai da muka tabbatar duk wata ɓaraka mun toshe kayarmu duk da Yaya Awwab yace zai ɗauki nauyin komai muma yana da ƙyau dai aga zabuwa da zanenta kawai. Yaya Musaddiq ma dai komai normal, dan shine ma ya dawo damu gidan tare da TJ ya gaida su Ummie da musu barka da zuwa. Gefe Ummie ta jashi da Mama Balki da Baba suka tattauna abinda bamu sani ba, ko faɗan aure aka masa kuma oho mudai an ware mu. Ummie ta kawo akwati guda ƙatoto na ɗinkunan biki data musu komai iri ɗaya sai color kowa da wadda yake so shi da Fahad nacin amarci. Jinai gaba ɗaya mutanen nan nama rasa mizan ce dasu a rayuwa...

Washe gari gida ya fara amsar baƙi. Wasu a ɓangaren dangin K/mashi suka iso. Sai dangin su Mama Balki da suka nuna kara. ALLAH sarki Ummie duk da itama nasan tana son taga a irin wannan ranar a nuna wasu tawaga matsayin nata dangin na uwa da uba amma bazaka taɓa ganin damuwar hakan a fuskarta ba. Ta rungume duk wanda yazo a matsayin nata na jini. Can ma su Hafiz sun sanar min yan Gwarzo nacan cike da gidan Abba. A daren ranar su Yaya Awwab ma suka iso. Kasancewar isowar dare sukai ni har namayi barci, sai da asuba na ganshi. Idanu na zuba masa ya wani ɗage gira irin na kallon fa. Baki na taɓe da faɗin, “Miye ma abin kallo anan mutum duk tsufa ya taso masa”.

Hannu ya kai zai cafkoni na fice da ɗan gudu ina masa gwalo. Ya jinjina kai alamar zan kamaki ɗin nan. Ban sake zuwa inda yake ba dan mun zama busy. A ranar muka kai lefen Bahijja, daga can muka wuce gidan Abba kuma zamu kai na Yaya Musaddiq tare da iyayenmu dake jira dan tun jiya da dare akwatinsa na gidan Abban. Mun samu cakwakiya a gidan, ashe kawo wannan kaya ya birkice Mom nata tsiya harda su gori. Abu kamar wasa har Abba ya mareta, kaɗan ya rage ai ɗanyen aiki ya saketa Gwaggo dai ta dakatar da shi ALLAH ya taƙaita. Shine ta shige ɗaki ta rufe kanta. Bata buɗeba sai da Ummanta tazo. Sai kuma sukaga an kawo likita alamar dai akwai damuwa. Amma ba'ace musu komai ba. Oho muma dai bamu matsawa kammu sai mun sani ba muka tafi kai lefe. Tarba muka samu acan ma ta girmamawa, yayinda gidan su Ruƙayya ya rikice da ganin lefen nan kamar yanda dangin Bahijja sukai murna. To da yake su sun fisu ƙarfi, itama kuma Ruƙayya irin rayuwarmu tayi a hannun kishiyar uwa sai abin nata yafi ɗaukakuwa. Dan can ɗin ma wata drama ɗin muka gani da tafi ta Mom. Matar baban Ruƙayya harda su suma sai da aka yayyafa mata ruwa. Kai jama'a kowane gida dai akwai irin waɗan nan ashe. ALLAH ya ƙyauta ya tsarkake mana zukatanmu. Haka dai muka barosu akan sai yamma kuma an haɗu, wajen kamu dan ranar za'ayi a hall ɗin da Ummie ta kama kasancewar dai komai za'ayisa a tare ne domin sauƙaƙama juna kai-kawon.

Muna dawowa gida babu zama. Shirin kamu aka fara, ni da Aunty Falaq muka koma can gidan. Mun dai zama busy body abin tausayi. Acan ɗin ma ba zaman mukayi ba. Shirin tafiya kamun da ɗan abinda baza'a rasa ba mukayi kafin cikar

lokaci. Bamu sami su Yaya Awwab a gidan ba. Ni sai hakan ma yamun daɗi, dan in yana nan wani abun zai iya cewa bazanyi na wahalar masa da yarinya ba. Sai da muka kammala shiri ne ina zaune a ɗaki ina shan complex ya shigo. Daga ni har bowl ɗin dana haɗa complex ɗin yake kallo. Ni dai na masa sannu kawai na cigaba da shan kayana dan har yanzu ba'a wani shirya bane gaba ɗaya. Kamar zai shareni shima sai kuma dai ya magantu.

A daƙilen nan nasa yace, “Babu abinci a gidan ne?”.

“Akwai mana”.

“Shine kike shan wannan shiriritan bayan kin san bake kaɗai bace. Zama da yunwa ko. Aiko zaki nutsu waje ɗaya dan dama wannan kai-kawon ya fara isata. Gaba ɗaya kun maida kanku daga nan zuwa nan kamar kun manta ma akwai aure a saman kanku. Jiba fita zakiyi amma kin zauna har ana miki wani banzan makeup a fuska. Irin ma kin maidani shashashan nan da ban san ciwon kaina ba kowane banza idonsa akan matata.....”

Gaba ɗaya na zuba masa ido kawai dan ya rikice sai masifa yake. Fahimtar neman dalilin da zai sa ya hanani fitar nan yake yasa yau ni na sauke tawa zuciyar. Dan kishi tsababa a kan fuskar bawan ALLAH zai hau min bori. Haka dai yaci ya tsire ni dai na daure dan in ALLAH ya yarda bazai samu sanadin hanani rawar gaban hantsi ba. Ina ganin ya shiga bathroom sum-sum na kwashi abubuwana na gudu wajen su Ummie. Banko sake yarda mun haɗu ba har muka tafi. Sai a hanya naga ran aunty Falaq a ɓace itama nake tambayarta lafiya.

Kamar zatai kuka tace, “Yaya Hayat mana. Su duk yawon da suke kana jurewa amma yau kishi ya rufe masa ido sai jaraba yake mun wai dan mi zan yi kwalliya haka alhalin fita zamuyi. Na masa bayanin wajen nan babu maza sam duk matane fa, hatta da masu video mata ne. Amma sam yaƙi fahimtata. Daga ƙarshe ma wai wlhy na damesa da tsari nabar ganin bikin Yayyena ne sai ya hana yaga abinda za'ayi. Shine kawai na masa shiru nidai ALLAH ya taimaka kikazo kika kirani na samu na fito”.

Rasama mizan ce nayi, dan al'amarin nasu sai naga kamar wani haɗin baki. Shi wancan da bamma gudu ba ban san a wace matsaya nake ba yanzu. A hakan ma nasan yana can fam ALLAH yasa kada ya fanshe a gobe wajen walima da kuma dinner da sai anje Lagos za'ayita ita. Hakuri kawai na bata naja bakina nai shiru..... ✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

TSUTSAR NAMA....!!

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page hundred & five

.....Wajen kamu ya matuƙar ƙayatuwa. Ya kuma tara mutane fiye da zaton mai zato. Dan ta kowanne ɓangare amare da angunan yan dangi ne. Babu wani hayaniya masu kiɗan ƙwaryane aka ɗakko sai mawaƙiyar nan khairat da taima amare da angunansu waƙar aure. Mufa mune amararori, tako wane ɓangare akwaimu. Shigowar amare hannayensu riƙe da juna cikin shiga iri ɗaya komai ya sake kankama. Bayan an kaisu har masaukinsu aka buɗe taro da addu'a kafin a fara abinda ya tara mutane. Dan so ake kafin magrib dai in sha ALLAHU a kammala kada a tauye hakkin kowa. Ko maƙiyi yaga wannan kamu yasan yay matuƙar ƙayatarwa. Alheri tv sun nuna komai live, sai wasu gidan tv da aka gayyato daban sai kuma masu ɗauka a wayiyi dan yanzu kowa ya zama mai ɗaukar hoto da video sai dai addu'a. (ALLAH ya hanamu ɗakko abinda zai zame mana damuwa wataran).

Tiɓis muka koma gida ga kaina na ciwo. Kai rainon ciki ma dai sai addu'a. ALLAH ya ƙarama iyayenmu rahama da gafara. Samun oga na gida ya sani jin shakkar shiga ɗakin, sai da ya fita Masallaci na lallaɓa na shiga. Kafin ya dawo har na kwanta. Koda ya dawo kuma saina lafe kamar mai barci, dan ni kaina nasan na taro Match. Washe gari aka tashi da shirye-shiryen ɗaurin aure. Tako ina gidajen a ɗinke suke da yan uwa. Duk da ina son tafiya cikin yan uwana haka na daure. Baƙin daketa shigowa daga sassa daban-daban dan gayyatar ɗaurin auren nan ta zaga fiye da inda ba'a zato, auren ƙannen Maash ba wasa ba, tun daga sallar asuba bai dawo gida ba sai kusan sha biyu. Ina ɗakin ina shirin ya shigo. Gaishe shi nayi dan da safe bamu gaisa ba. Ciki-ciki ya amsa kamar yanda yake yi yan kwanakin nan. Kamar na watsar da shi sai kuma na tambayesa na kawo masa tea? Dan nasan bai ci komai ba har yanzu. Idanu ya zuba min sosai yana kallona. Nima kallon nasa nake yi, sai kuma na janye ina ƙoƙarin wucewata. Cak na tsaya sakamakon riƙonin da akayi, kafin ma nace wani abu ya jawoni ya zaunar saman jikinsa ya rungume. Daga ni har shi ajiyar zuciya muka saki masu ƙarfi. Cikin kunnena ya furta, “Ni na gaji da wannan faɗan haka nan”.

Maimakon bashi amsa sai kawai na sakar masa kuka. hawayen da suka cika min ido suka shiga gangaro min suna sauka saman ƙirjinsa. Murmushi ya ɗan yi da har naji alamunsa. Sai kuma muka sake ƙanƙame juna sosai.

“Humm miyasa kike son bamu wahala. Gaba ɗaya kin zama mafaɗaciya.”

“To ba kaine kake sakani yin faɗan ba. Kamun laifi kuma ka fini fushi harda ringa mun mugunta.”

“Nima ai kin mun laifin, na shigo gida ina ɗokin zuwa na ganki kawai ki wani shareni kina gaida wani a gabana ni kamar baki san da ni ba. Kin san ko zafin da naji, da ƙyar na danne zuciyata ban hukuntaki ba”.

“Amma kaifa ka fara min laifin, sai kuma ka fini jin haushi. Ina fama da kaina ka tasoni babu shiri zuwa wata ƙasa. Babu tarba, babu kiran waya, ban ganka ba, da ga ƙarshe ma akace min ka wuce wata ƙasar irin ma ni bana cikin tsarinka ɗin nan. Na kiraka a waya baka ɗauka ba, baka biyo kiran ba kace min koda uzirine ya riƙeka baki sanyi a raina. Ka dawo kuma kana wani shashasha min ƙamshi. ALLAH naji ranar kamar na baro ƙasar nan ko'a ƙafa ne”.

“Ya rabba! Yanzu dai duk misunderstanding ne ya shiga kawai. Bayan Ummie na a duniyar nan kece mace ta biyu mai matsayin da babu mai irinsa a gareni Samrh. Gaba ɗaya abinda kike tunani ba haka bane ba.....” tsaf ya zayyane min komai daya faru, tare da tabbatar min wayarsa lokacin a Dubai ya manta ta tsabar hankalinsa ya tafi ga wancan uzirin, shima sai daya dawo a randa ma zamu wuce yaje ya ɗauka wayar a office daya barta yake ganin miss calls ɗin. Yayi niyyar mun bayani a jirgi yaga na sake tunzura har inama Juliet masifa.

Sosai na sake rungumesa da faɗin, “Kayi haƙuri, ni kawai na ɗauka tsabar muhimmancin harkokin ka ne suka fini. Ita kuma ALLAH bana sonta, taita maka wani iyayin banza. ALLAH wataran sai na karya mata ƙafafun nan kamar na sauro”.

“Trouble maker, kawai sai ki karya mata ƙafafu?. Yanzu ni dai tashi time zai ƙure, idan na dawo ma ƙarasa faɗan”. Yay maganar yana ɗaukata camak zuwa bathroom. Da kansa yay mun wanka nima na taimaka masa yayi. Koda muka fito a gurguje na fara taimaka masa ya shirya dan su Uncle Abdullahi nata kiranshi ashe har sun iso tun ɗazun. Matuƙar ƙyau yayi a cikin manyan kayan dan yau harda babbar riga. Ga gyaran fuska mai ƙyatarwa yasha. Haka na gyara masa gashin nan na ɗauresa sannan na saka masa hula ta yanda ba'a ganinsa. Ni kaina bamma san lokacin dana furta masa, “Mijina kai ƙyaƙyƙyawane”.

Wani silent murmushi yay da jan kumatuna ya kashe min ido ɗaya da faɗin, “Duk ƙyauna na kai wannan SARAUNIYAR MATAN”.

“Uhm, saika sa mata sun zaneni ta ina na zama sarauniyarsu?”.

“A fadar Muhammad Awwab mana”. Ya faɗa cikin soft murya da sumbatar lips ɗina. Ya kuma ɗan duƙa ya sumbaci cikina da ya fito sosai ɗan kif da shi. Hoto na masa a gurguje ya fice dan kiran su Uncle Abdullahi yaƙi daina shigowa. Yana fita nima nai nawa shirin inata faman sakin murmushi. Na yarda kam mata da miji sai ALLAH. Duk iya ƙololuwar fushin da za'a ɗauka da juna sai kaga na lokaci ne, da zarar an huce kuma an manta shike nan...

A gurguje Please .

★★

Alhamdullah bayan sallar juma'a ɗunbin al'ummar MANZON ALLAH suka shaida ɗaurin auren Yaya Musaddiq da amaryarsa Ruƙayya. Yaya Fahad da Bahijja. Ɗaurin aurene da ya tara manyan mutane ƙasar da wajenta, yan siyasa, sarakuna, yan kasuwa daga ƙasashe daban-daban. Wasu ma dai suna Lagos suna jiranmu zasu halarci dinner ne. Shugaban ƙasa da kansa ya halarci wannan aure (Amma fa shugaban ƙasa Ramadhan nake nufi). Ko garin Kano yasan yau ana ɗaurin auren masu hannu da manda. ALLAH sarki Paah ma da jiki ya fara sauƙi yazo, sai da za'a ɗaura aure Maash ya gansa. Tunda suka haɗa ido da Maash yay ƙasa da kansa bai yarda sun sake ba. Sai Maash ɗin ne ya danne zuciyarsa ya gaishesa da girmamawa. Bai kuma tambayesa yaya jiki ba. Uncle Abdullahi dai shi yay waliccin Fahad, Kawu Lurwanu kuma na Yaya Musaddiq. Bayan ɗaura aure aka ɗunguma ƙaton Hall ɗin da aka tanada domin ƙwarya-ƙwaryar liyafar da su Hayatu suka shirya domin ciyar da baƙinsu abinci. Anci kuwa ansha kowa ya godema ALLAH. Yayinda mu ma anan muketa namu hidima. Mansoor da Attahir da suma next week nasu bikin da Dad ɗinsu sun halarci ɗaurin auren. Bayan kammala cin abinci manyan baƙi suka fara kaucewa. Na jirgi na nufur airport na mota na nufar masauki, wasu kuma Lagos ma suke wucewa tun yau ɗin kasancewar can akai musu masauki.

Sai bayan la'asar anguna suka shigo mana da manyan yayye. Ummie ta rungume Fahad tana hawaye, kowa yasan na farin ciki ne. Shima dai hawayen yake yi, mutane da yawa na tayasu. Koda ta sakesa Yaya Awwab dake tsaye kawai yana kallonsu shima ta kamo ta rungume tana mai sanya musu albarka. Daga haka akai hotuna, Paah dai bai zo gidan ba sai su Kawu Abdullahi. Dama matarsa da Malika suna nan tun jiya, Hajiya Mammah ce dai sai yau tazo a ɗarare, itama Hajiya Mama tana nan yau kwana biyu ita da duka yaranta. ALLAH sarki Ummie, ta dake zuciyarta komai daya shafi uba su take sakkowa gaba, tun Hajiya Mammah na nuƙu-nuƙu dai harta fara ɗan warewa. Ana hotuna Ummie na maƙale da ni da Aunty

Falaq. Babu ko kunya shima uban gayya ya rungumeni aka mana, harda inda yake sumbatar goshina, hannunsa kuwa na saman cikina ko'a jikinsa.

Bayan kammala hotuna anan muka ɗunguma can gidan Abba kuma. Cikin namu yan uwan da gayyar dangi. Nan ɗin ma dai anyi hotuna na kece raini, Mom dai taƙi ko fitowa. Tanama bedroom babu wanda zai ce yazo wajen bikin nan ya ganta daga jiya zuwa yau. Ita dai Bibaa da taga babu sarki sai ALLAH saita ware abinta cikin dangi. Auta kam yana nane da Yaya Musaddiq.

Sai da aka ɗakko amarya Yaya Musaddiq sannan aka ɗakko ta Fahad, gida ne mai ƙyau da tsari aka kai amaren su duka anan anguwar da muke. Yaya Musaddiq a can sama, Fahad anan ƙasa. Duk da ba zama zasuyi ba su duka kowa yasan haka duka iyayen amaren sunma yaransu jere gwargwadon ƙarfinsu. Babu shiri daga gidan amaren na fito a ƙafa saboda babu wani nisa na koma gida. Dan ji nake kamar zan zube dan gajiya. Aiko ban nema kowa ba na shige nai wanka da ƙyar na kwanta. Bamma san lokacin da Yaya Awwab ya dawo gidan ba, sai cikin dare da yunwa ta sakani farkawa na gansa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page hundred & ***six***

.....Washe gari tun safe wasu aka wuce Lagos da su, dan jirage uku na Maash aikin jigilar ɗaukar mutane sukayi□. Su Ummie suna cikin masu tafiyar farko, ni dai da Aunty Falaq da amare da angwayensu sai namu mazan dole sai yamma. Dan Fahad ya buɗe aiki. Babu ɗaya ƙafa a daren ya maida Bahijja amaryar gaske. Baiwar ALLAH tana ta ɓarzar kuka. Babu shiri Ruƙayya ta kirani tace nazo akwai matsala ta

rasa yanda zatai da Bahijja itama duk ta firgice. A lokacin ina jikin nawa angon, cikin mamaki yake tambayar lafiya dan na roƙesa zanje can.

Abinda ta gaya min na faɗa masa. Zai kira wayar Fahad dan shi bai ma fahimci komai ba na dakatar da shi. “Yaya karka kirashi, bafa wani abin tada hankali bane ba.”

“Kamar ya kada a kira shi, kika sani ko wani shirmen ya aikata. Kin san fa Fahad baya jin magana”.

Dariyama ni abin ya bani, na ce, “Ai wannan karon rashin jin nashi na manyanta ne. Kawai inaga ya angwance ne fa”.

Idanu sosai Maash ɗin ya zaro da faɗin, “Samrh! Anya yaron nan nada hankali? Ya bari a gama bikin mana”.

Dariya kawai na shiga yi. “Kai yaya mutum da matarsa. Nidai yanzu bara naje...” bamma gama rufe baki ba sai ga kiran Fahad ɗin ya shigo min. Muryarsa a sanyaye ya ce, “Aunty dan ALLAH kizo yanzu. Amma kada ki faɗama kowa nan zaki zo har Yaya Please. Wlhy ina cikin matsala”.

Dakewa nayi ina ƙoƙarin danne dariya nace masa gani nan kada ya damu. Koda na yanke kiran sai Yaya Awwab da duk ke jinmu yay ƙwafa kawai. Ni dai na ɗan taɓe baki da faɗin, “Idan ma dai babu batun kwanciya asibiti da ɗinke-ɗinke irin na wasu ai da sauƙi. Shi yayi da ƙyau”.

Harara ya zubo min kamar zai cinyeni da idanu. Na fita abina ina dariya dan nasan ya gane da shi nake dai....

Sosai Bahijja ta bani tausayi, kai maza dai duk sai abarsu. Ita kanta Ruƙayya duk tayi laƙe-laƙe. Haka na taimaka mata da ruwan zafi tanata faman kuka. Dole Yaya Musaddiq ya samo mana wata Nurse yar anguwar mu ta dubata. Alhamdullah dai tace ɗan ƙarin data samu baida yawa. Adai kula da shigarta ruwan zafi sosai wajen zai haɗe da kansa. Ta kuma bata magunguna. Ban baro gidan ba sai da taci abinci tasha maganin ta kwanta. Na fito na samu Fahad a falo ya zabga tagumi. Dariya nayi a zuciyata. Amma a zahiri fuskata a dake na ce, “Ta samu barci, ni bari naje na samu Yayanka dan dole tafiyar mu ta koma sai ko zuwa six ne. Idan ta tashi ka kula da ita ta shiga ruwan zafi yanda ya kamata”.

Kansa dake ƙasa ya jinjina min, kafin murya a sanyaye ya ce, “Amma aunty babu matsala ko?”.

Hararsa nayi. Ya sake duƙar da kai yana sosa ƙeya.

“A yanzu dai babu, amma idan ka kuma batare data warke ba akwai. Ka kuma san duk yanda zaka lallasheta ta nutsu kar Ummie ko yayanka su fahimta, kaga dai

wajen taro za'a shiga. In ba hakaba kai da su ne ni babu ruwana kaga tafiyata. Sai na shigo anjima". Daga haka nai ficewata. A ƙofar gida na samu Maash jikin mota yana waya. Na ɗan tsaya ina masa kallon mamaki har ya kammala ya katse.

"Lafiya kuwa na ganka anan? Ba barci kace zakayi ba?".

Fuska ya ɗan yamutse, "Na kuma kasa tunda kika fito. Idan akwai matsala inaga ki fito da yarinyar nan muje asibiti".

"No babu wata matsala fa. Ai shi bai jawo magana da yawa ba kamar wasu".

"Suwa kenan?".

Ya faɗa yana wani bina da kallo a dake. Kafaɗa na ɗan ɗage da taɓe baki na ce, "Ni dai ai ban faɗi suna ba a zancena ba ko".

"Kin san ALLAH yarinyar nan kina shiga mun hanci kwana biyun nan, amma zan kamaki ne. Zaki san ni kika tasa a gaba".

Dariya nayi da faɗin, "Oh oh kaji tsargar kai. My Lion kaji na ambaci sunanka a maganata. To kodai kaima haka kayi ne?".

"Zo muje sai na faɗa miki yanda nayi ni, dan har farkawa nayi aka ɗinke". Yay maganar yana ƙoƙarin cafkoni. Da sauri na zille ina dariya nai hanyar gida. Tsaye yay kawai hannayensa duka biyu riƙe da ƙugunsa yana kallona harna buɗe gate zan shige. Sai da na saka ƙafata ɗaya na ɗan leƙo kaina na masa gwalo na ida shigewa ina murmushi. Kusan karo mukaci da Aunty Falaq a ƙofar falo.

"Ke kuma daga ina haka?".

Dariya na saki da nuna mata gate. Nace, "Daga gidan amare. Na leka nemanki da zan fita naga kuna tare da Yaya Hayat a baya shine na wuce. Yayanki ne ya jiƙa aiki".

Idanu ta zaro sosai da faɗin, "Wanne daga ciki?".

Dariya na sake kwashewa da shi da kai bakina saitin kunnen ta na raɗa mata. Ta riƙe baki tana dariya da fadin, "Kai ALLAH ya shirya Yaya Fahad wlhy. Shi babu ɗan kawaici mu yan biki mu tafi sannan. Muje ni dama nemanki nake fa Aunty Maijidda ce ta kirani yanzun".

"Okay muje to".

A gurguje Please .

□□□□□

Bamu bar Kano ba sai shida na yamma. Abinka da jirgi mun isa akan lokaci, dan Alhamdullah sallar magriba ma a gida ta mana. Mansion fa yayi masifar cika ta ban mamaki. A hakama wasu suna hotels. Na ɗan ji sanyi ganin sashenmu babu wannan hayaniyar. Dan sai da ma ya buɗe sannan muka shiga. Bamufi mintuna biyar ba Ummie ta shigo ta samemu a falo dan bamu kai ga haurawa sama ba. Mun gaisheta cikin girmamawa. Ta amsa mana da kulawa tana tambayata babu dai damuwa ko? Babu inda ke mun ciwo kuma.. Nace mata eh babu komai.

Sosai na waro idanu waje jin wai harda mu fa a wannan dinner. Dan Uncle Abdullahi ya dage akan dole mu kasance cikin anguna da amare tunda mu a namu bikin babu abinda akayi. Abubuwan da suka faru kuma Yaya Awwab bai taɓa magana ba ya kamata a wannan gaɓar duniya ta sake tabbatar da aurenmu.

A marairaice na ce, “Amma Ummie ALLAH ai shine shaida. Idan ta mutane zamu bi ko UBANGIJI bazamu bautamawa ba yanda ya kamata. Kawai a barsu su cigaba da shirmensu watarana sa gane da kansu. Bayanin da Abba yay musu kuma a wancan karon mutane da yawa sun fahimta”.

“Hakane Daughter. Amma ku fahimci zancen Abdullahi nakan gaskiya. Anji duk wancan ta wadatar, amma watarana ake gudu musamman ga masu tasowa da su bamu san wazai iya rarrabe musu gaskiyar ba. Sannan yaranku nan gaba wani zai iya amfani da wannan damar ya saka musu ruɗani a zukatansu”.

“Hakane Ummie”.

Na faɗa a sanyaye kaina a ƙasa. Jin shiru uban gayyar bai taka ba na ɗan ɗago na kallesa. Itama Ummie shi take kallon. Itace ta katse shirun namu da faɗin, “Muhammad bakace komai ba”.

“Ummie toni mizance tunda kun gama magana. Duk hukuncin da kuka yanke ai dai-dai ne. Kawai dai kamar yanda ta faɗa ne maganar mutane ba abin biyewa bace. Tunda mu mun san kammu fine”.

“Duk da hakan dai kawai ku shirya. Ga kayan da zaku saka can a ɗakinta an ajiye muku. Mai kwalliya zata zo ta mata”.

Da sauri ya ce, “No Ummie abar batun kwalliyar nan. Kayan ma idan basu min ba zan iya canjawa”.

“Kai kuma ka sani wannan uban yaɗan kishin tsiya”.

Ta faɗa tana miƙewa ta fice abinta. Shiru da ga ni har shi babu wanda yay magana. Sai ma wani kicin-kicin da yay da fuska alamar sam baya ra'ayin abin kawai yayi biyayya ne. Nasan dama bazai masa ba shiyyasa naso tun farko Ummie

ta fahimta. Gudun karma ya juye bala'in a kai a sai na miƙe kawai ina faɗin, Bara nayi fitsari” na gudu abina. Nafi minti talatin da shiga sannan ya shigo. Ina kwance a gado kawai ina ƙullawa da kwancewa. Nasan mutumin nan da kishi kada ayi abun nan ya zame min baya da ƙura. Box ɗin da kayan ke ciki dako motsasu banyi a inda suke ba ya ɗauka ya shiga buɗewa. Sai da ya fito da kayan ciki tas ya gama kallonsu kafin ya zubesu a saman gadon ya kai zaune yana wani shafar fuska da furzar da huci mai ƙarfi.

Shiru kusan na minti ɗaya kafin cikin sanyi nace, “Uhmm Yaya Awwab kodai kawai nacema Ummie banda lafiya. Nasan hakan zai sa tace nai zamana. Kaga shike nan an rabu lafiya”.

Shiru kamar bazai tanka min ba sai kuma ya juyo ya kallani. Sai da ya ɗan lumshe ido ya buɗesu a cikin nawan kafin ya sake furzar da numfashi a slowly. Fuskarsa a yamutse ya ce, “Bayan ta tambayeki kince lafiya kike. Kawai ki tashi ki shirya ɗin”. Daga haka ya tashi ya fita abinsa.....✍

□□Mufa mun wuce airport. Wanda bai shirya ba sai ya taho a mota babu ruwana. Bikin Fahad guda ai sai mun zubar😂□□□.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

—

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page hundred & ***seven***

*_Wai ni Balki ina duk masoyan Bilyn Abdull ɗin nan dake a manhajar Instagram da TikTok ne?□? Kai jama'a gaskiya da kunya ace account na Bilyn Abdull a Instagram

da TikTok iya kar fallowers ɗin kenan□☹. Ina masoyan facebook ɗin nan dana WhatsApp, Please a fito mana ai fallowing ɗina. Accounts ne na Bussines ko bazaki/zaka saya ba zakaga abinda ya burgeka ko kalarka ka nema a inda kake. Maza ku garzayo BILYN ABDULL ONLINE SHOPPING kodan kashe kwarkwatar idanunku ku more kallo iya kallonku da kaya yan yayi cikin farashi mai sauƙi da rahusa. Muna bada sari, muna adashen gata, muna sai da ɗai-ɗai. Ka gani su burgeka, ka saka ka birge mai kallonka sai Bilyn Abdull online shopping. Bari muga akwai ƙaunar kodai-kodai....☺□. Ga link nan naga accounts ɗin nan biyu kamar zasu fashe da fallowers 😘😘😘😍😍□□□□_*.

*_BILYN-ABDULL ONLINE SHOPPING_* _Duniyar cancaɗa ado da kwalliyar birgewa. Kar ku bari ayi babu ku😘😘😘._

*_My account on TikTok_*

https://www.tiktok.com/@bilynabdull?_t=8mfvWuXADVF&_r=1

*_Instagram_*

I'm on Instagram as @balkissaibrahimmusa. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=fc2g6shv1k6u&utm_content=p17zzzv

Ina masu son zuwa ganin likita ko yawon buɗe ido ƙasar Egypt?. To ku garzayo munada hanya mai sauƙi ta sama muku sauƙin tafiya cikin ƙa'ida da bin dokar ƙasa. Katafi anan cikin aminci, ka dawo kuma cikin aminci. Wajen kwananka a can zamu tanada, asibitin da zakaga likita duk zamu tsaya maka da tsayawar UBANGIJI. Hakama yawon hutawa zamu zame maka jagora. Kai ko hanyar zuwa domin sayo kaya duk muna da ita. Kai dai kawai kazo garemu kaga aiki da cikawa da iznin ALLAH. 09032345899. A nememu tanan ga masu buƙata, dan ALLAH serious bama son latsi ko wasa dan ba wasan muka fito ba 😂😍□□.

.....Ajiyar zuciya kawai na sauke nima na tashin. Sai da na fara yin wanka nazo nai sallar isha'i sannan na hau shiri. Lass ne ko material zan kirashi bamma sani ba nikam. Amma yayi masifar haɗuwa. Ga wani uban stones work yasha na musamman. Rigace doguwa har ƙasa fitet datai bala'in bin jikina ta fito da matashin

cikina ɗas hannunta dogo sosai. Sai akai wani shegen flay jacket data sauka ta rufe har mazaunaina ta gaba kuma ta ɗan gota cikina ta yanda ba'a ganinsa sam. Sosai pitch and black color ɗin lass ɗin ya fita da fitarsa ta haƙiƙa. Ɗinkin kuma ya sake ƙawatashi. Tunda ya hana mai kwalliya dole ni na zauna naima kaina ɗan light makeup da na tabbatar yama fi wancan da za'a canja min kamanni. Dan nan a ainahina nake komai cif-cif. Ɗan ƙwalin kaina ɗauri daya sake ƙawata kwalliyar sannan na saka jacket ɗin da ɗan turare kaɗan na saka sauran tarkacen yɑn kunne da sarƙa da suka kasance zinari. Nasan nayi ƙyau koda ba'a faɗa min ba. Ya Arrahaman na faɗa a zuciyata ni kaina fa nake kallon kan nawa ta mirror. Kwalliya dai kam itace mace. Komai muninka indai zaka gyara sai an kalla an sake kallo. Bare kuma Alhamdullah muna da dai ɗan ƙyan nan dai-dai mu ma. Balle a yanzu da ciki ya sake ƙawatani da fiddoni fam. Flat shoes ɗin da aka haɗo da kayan na sakama ƙafata mai ƙawace da dan kyalli da baƙi. Kafin na haɗa yɑn tarkacena a handbag. Ina warware mayafin ya shigo shima cikin shirinsa. Shaddace baƙa data masifar fiddo da ainahinsa. Sai kawai na tsaya ina kallonsa kamar yanda shima yake kallona. Na buɗe baki zanyi magana sai shima ya buɗe zaiyi muna ƙoƙarin haɗa baki. Duk shiru mukai muna ma juna murmushi. Sai kawai nai ƙasa da kaina har ya ƙaraso inda nake.

Kamar mai tsoron a jisa cikin silent voice ɗin san nan ya furta, “Anya kuwa zan barki fita a haka My Samrh”.

Kaina a ƙasa ina murmushi na ce, “Sabida mi?”.

“Kinyi ƙyau ne fiye da yanda kike tunani”.

“Kaima ai hakan. Dan komai ka saka a jikinka ƙyawunka ƙawatashi yake yi”.

“Ai ke kin mafi ƙyawun ƙyau My helf”. Ya faɗa yana rungumoni jikinsa. Ni dai addu'a kawai nake kada yace na cire ko yace an fasa. ALLAH dai ya taimakeni akai kiransa a waya kan mu ake jira kowa ya tafi har angwaye. Gyalen ya amsa da kansa ya yafa min. Batare da ta sake magana ba ya ɗauka handbag ɗina a hannunsa na haggu na damar ya kamani muka fita. Gidan shiru sai securitys kawai. Sai motar dake fake fara tass mai shegen ƙyau da kuma ta guards ɗinsa guda biyu. Da sauri TJ dake neman faɗuwa saboda kallonmu ya buɗe murfin da sauri, yayin da shi Uban gayyar ya zagaya da ni ta ɗaya side ɗin ya buɗe da kansa ya taimaka min na shiga sannan ya sake zagayowa inda Tj ya buɗe masa ya shiga.. kallona ya ɗan yi ya sakar min murmushi. Nima sai na sakar masa murmushin tare da kwantowa gefen hannunsa....

□❤□❤□

A ɓangaren anguna da amaransu kwalliya ce ta kece raini da ko makaho ya kalla yasan naira tayi aiki a wajen. Dan rigunan amare da suka kasance pitch sun musu masifar ƙyau. Hakama angwaye dake sanye da fararen suit kamar ka sace su ka gudu dan ƙyau. Manyan motocin da aka sakasu sabbi ƙal ko ledojinsu ba'a ɗaye ba sunyi matuƙar sake ƙawatasu. To magana ake ta aljihu da manda fa. Ƙannen Maash sunfi gaban wasa a wannan gaɓar.

Hall ya cika iya cika taban mamaki duk da kuwa duk wanda ya shiga wajen yana da lasisin hakanne. Harka ce ta manyan mutane da yʻayʻan manyan. Ga ƙawayen amare sun fito cikin nasu kalar ta musamman da nunama tsara. Kamar yanda al'adar biki yake bayan sanar da isowar anguna da amare ƙawayen amarya da abokai suka jagoranci shiga dasu cikin tsari da nutsuwar data ƙayatar da kowa. Yaya Musaddiq shine babba. Dan haka yana a gaba shi da amaryarsa Fahad biye da shi maƙale da tasa amaryar da makeup ya ɓoye yanayinta na gumurzun da tasha a jiya hannun angon nata. Dan yanda tafiyarta ma bata gama daidaita ba Falaq ta canja takalmanta zuwa flat gudun matsala. A hakanma dai dan hannunta na cikin nashi ne ya taimaka mata da rufa asirinta. Babu wanda zai ce waɗan nan angwaye da amare basu birgesa ba. Ga shi an musu ɗinki na mutunci da sam bai fidda tsiraicinsu ba. Hasalima maimakon naɗa ɗan kwali a saka net su rolling ɗinsa akai musu ta yanda ya sake mutuntasu matuƙa. Wajen hawa steps Bahijja ta kasa saboda azabar data ratsata. Dan tun takun farko ta tsaya cak. Ai kawai Fahad na fakar ido ya ɗauka kayarsa camak ya ƙarasa da ita har saman kujerar da zasu zauna. Miko za'ai inba dariya ba. Dan yanda yay ɗin dole ya burgeka kuma ya baka dariyar. Shiko ko'a jikinsa fatansa dai asirinsa ya rufu a gama harkar nan lafiya Ummie ko Mama ko Hajiya Mama wani bai ramfosa ba. Dan Hajiya Mammah ma shi zaima iya gaya mata da bakinsa har yanzu ba wani mutunci take da shi a idonsa ba. Wajen zama uku aka tanada. Su suna gefe da gefe na tsakkiya na babban yaya. Sai dai ba kowa ya sani ba, ana daita mamakin ma rashin isowarsa akan lokaci wajen dan har aka gabatar da addu'a da ɗan wasu abubuwan bai iso ba. Sai bayan kusan mintina talatin aka sanar da isowar tashi.

Anan fa wanda basu san Maash ba suka fara baza ido domin ganinsa. Wanda kuma suke wasi-wasin batun aurensa na son tabbatarwa da gaskiyane ko kuwa. Saboda an san dai babu yanda zai ya halarci wannan dinner babu matar. Bayan mc ya gama kirari da wasa shi ya shigo cikin gakun nan nasa na ƙasaita da rakiyar bajiman guards ɗin sa abin zabbirgewa. A gefensa ƙyaƙyƙyawar matarsa da suka gama dacewa a gefensa hannunsa sarƙe a cikin nata ɗayan hannunsa ɗauke da handbag ɗinta.

“Masha ALLAH”.

Kalma mafi girma data dinga fita a bakunan mafi yawan mutanen wajen kenan, dan duk iya hassadarka kasan wannan haɗi ya haɗu. To sai muce mai abu da abunsa ne ya shigo. Dan kuwa dai bakin mc ya gagara rufuwa sai washi yake iya washi kamar zai haɗiye garshensa. Abu mafi birgewa ga anguna guda biyu kuma

ƙanne da duniya ta shaida ga MAASH yana taka step ɗin wajen suka miƙe domin girmamawa a garesa. Sai kawai ya tsaya kallonsu shima da murmushin da mutane da yawa zasu iya rantsuwar basu taɓa gani akan fuskarsa ba. Dan har cikin rai yake jin alfaharin kasancewarsu ƙannensa, tare da cika burin kakansa da har ya koma ga ALLAH bazai taɓa mantawa da shi ba. Sai kuma ƙyau da sukai masa matuƙa dan da kansa ya bada design ɗin kayan da ke jikin nasu musamman ma suit ɗinsu. Nuni yay musu da su zauna kafin ya ƙarasa shi da tasa zinariyar mazauninsu. Kamata yay da kansa ya zaunar sannan shima ya kai zaune ya kuma jawota jikinsa da ƙyau tamkar za'a ƙwace masa ita. Aiko abokansa sai kawai suka hau salute nashi.

Farin cikin Ummie baya musaltuwa a wannan rana. Sai da ta share hawaye ta sake sharewa sau babu adadi. Yayinda ita ke kukan farin ciki anan acan asibiti Baba prof na ƙunar zuciya yake yi shi da yaɾsa Lawisa. Dan kuwa saboda su Maash ya ɗauki nauyin gidajen tv masu yawa suke nuna wannan dinner live. Ya kuma saka aka saka musu tashoshin dan su gani kamar yanda kowa ke gani.

Wani irin zafafa da hanƙoro zuciyar prof keyi a cikin ƙirji. Sai dai babu damar motsa ko ɗan yatsa dan shi da dutse basu da banbanci a yanzu ƙasancewar sai an motsashi dan haka yake turum. Rashin makama ya sakashi fashewa da kuka kawai. Hawaye masu azabar zafi da ƙona zuciya suka dinga bin fuskarsa. Yayi kiran azo a kashe masa tvn amma babu kowa a kusa. Sai faman taunar lips yake yana fasasu da gaƙori tare da antayi ashariya manya-manya kamar ba tsoho ba.

A ɓangaren Commondo kam dariya ya dinga yi, dan shi ba taron bane ya zame masa abin kallo prof ne. A kwanakin nan dama a tsakaninsa da shi sai dai yaɾ tsinema juna da yin ALLAH ya isa. Prof ɗin yayi-yayi a raba musu ɗaki anƙi ko kulashi. Daya damu mutane ma dan bakinsa ras na magana da ga shi har commondo ɗin. Sai securitys ɗin dake tsare da su sukace bashi da wannan isar ai a yanzu. Kalmar nan ta masa masifar ciwo. Ai ko ya dinga surfa musu zagi a wannan rana amma babu wanda ya kulashi...

★★

A wajen dinner bayan mc ya gabatar da isowar Maash da tashi amarya aka sake addu'a. Kafin aunty Mama ta fito ta gabatar da kanta matsayin ƙanwar mahaifin anguna. Ta kuma buƙaci nutsuwar kowa dan acewarta tana da bayani mai muhimmanci da babban saƙo ga duk wanda ke a hall ɗin dama wanda ke gani a wajen ta hanyar television. Tsitt kuwa hall ɗin ya sake yi fiye da da. Itama sai ta sake nutsuwa da juyawa ta fuskanci Maash dake gyarama Samraah mayafinta suna magana ƙasa-ƙasa. Cike da kulawa ta kira ainahin sunansa.....✍

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

*_ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□_**_Typing□_*

□TSUTSAR NAMA....!!□

(Itama nama ce)

Bilyn Abdull ce

Book three

Page hundred & ***eight***

.....Dara-dara ɗin cat eyes ɗinsa ya ɗago ya kalleta. Tare da motsa lips ɗinsa a hankali ya amsa mata da girmamawa. Da sauri mc ya kawo masa mic dan kowa na buƙatar jin abinda zai faɗa. Hakan ya sake gamsar da mutane. Hajiya Mama ta cigaba da faɗin, “Muhammad Awwab wacece a tare da kai?”.

Juyawa yay ya kalla Samraah da tai ƙasa da kanta. A hankali ya ɗaura hannunsa saman haɓarta ya ɗagota. Kallon juna sukai cikin ido kafin a hankali ya kai mic ɗin saitin small pinkish lips ɗinsa ya motsasu cike da ƙasaita idanunsa a cikin na Samraah ɗin itama nata a cikin nashi har lokacin ya furta, “Aunt! Ita ɗin MATATA CE!”.

Ya Arrahaman, irin wannan salo haka mai kashe zuciya. Sai kawai hall ɗin ya ɗauki tafi. Da ƙyar aka samu ya lafa. Hajiya Mama ta sake faɗin, “Yaushe ka fara sonta?”.

Yanzun kam idanunsa ya lumshe tare da sake juyawa ya buɗe su akan Samraah da ita kanta wannan tambaya ta sakata jin zumuɗi tana kallonsa. Cikin tsakkiyar idonta ya sake saka nashi. Cikin wani irin soft voice ya furta, “Ranar dana fara GANINTA”.

“Yaya akai haka bayan kowa yasan Maash ba ma'abocin shiga sabgar mata bane?”.

“Saboda ita ta kasance ta MUSAMMAN”.

“Uhmmm Masha ALLAH ta musamman kam. Muma shaida ne. Amma zamu so musan yaya akai haka da sauri?”.

“Saboda tayi abinda wani bai taɓa kwatanta yi ba a sunan ma'aikacin jarida harda Mazan. _(“Sir a matsayinka na matashi da za'a iya shiga mamakin ganin yanda ka gina katafaren kamfani irin wannan da ya zama na farko a Africa, a duniya na uku kuma bama shi kawai ka mallaka ba, akwai wasu manyan cibiyoyi daka kafa a ciki da wajen Africa ma ba Nigeria kawai ba, ko nace duniya, shin ko zaka iya jan hankali matasa irinka dake tasowa dangane da neman na kai da asalin tarihinka dan su san kaima ba daga kwance ka kai wannan matsayin ba, sai da kai aiki tuƙuru, tare da tsallake ƙalubale masu yawan gaske kuma duk kai haƙuri ka jure har gashi a yanzu ka zama wani babban ginshiƙi tauraron duniya dake haska yankinsa da ƙasarsa, yarensa harma da addininsa?)_

Sune kalmomin data furta masu girgiza zuciya da rarrabesu suka zama masu wahalar gaske da sanya razani, tare da jan hankalin Muhammad Awwab El-Mu'azz Maash gareta. Dan shine lokaci na farko, kuma karo na farko da naga tsantsar JARUMTA da iya aiki da ƙwarewar iya sarrafa harshe na ɣan jarida a tare da yarinya ƙarama kamarta. Idan nace muku TSORONTA naji, har na amince batare dana shirya hakan ba karki musanta min”

Kutumaddu-madu. ai wani irin sowa da ihu da hall ɗin nan ya ɗauka na matasan samarin dake wajen dama abokan uban gayyar su kansu kai kace wata gagarumar ƙwallo da duniya ta dasa ma idanu gaba ɗaya ce a kaci. Ya ilahil alamin. Maash ya gama buɗe aiki yau. Ita kanta Samraah jikinta tsuma yake yi. Babu shiri ta shige jikinsa ko zata samu nutsuwar fuskantar mutane. Sai da aka samu hall ɗin ya lafa bayan mc ya warware sautin waƙar da aka rairama Maash ɗin da Samraah sannan tambaya ta koma kanta.

Cikin tsareta da ido Hajiya Mama ta ce, “Daughter Samraah wanene wannan tare da ke?”.

Kallonsa na ɗan yi sai kuma na duƙar da kai ina murmushi. Mic ɗin ya kawo gab da bakina, a hankali na furta “Mama Miji”.

“Oh Woow Masha ALLAH. A ina kuka fara haɗuwa?”.

“Wajen taron buɗe Company naje a matsayin mai ɗaukar rahoto.”

“Kenan kema tun a ranar ki ka faɗa a soyayyarsa?”.

Shiru nayi kamar bazance komai ba. Hakan yasa hall ɗin yay tsitt sosai. Sai da Hajiya Mama ta sake furta, “Muna sauraren Mrs Maash”.

Ɗagowa nayi na ɗan kallesa sai naga ya wani tsareni da shanyayyun idanunsa. Ɗan hararsa nayi kaɗan na maida kaina na rissinar. Kamar mai koyon magana na ce, “Mama kawai dai....”

Sai kuma nayi shiru. Sai da na sake jan wasu sakanni da saka ƙaguwa a zuciyar kowa na kuma ji a raina ajin da naja ya jawu. Dan shi kansa uban gayyar a ƙagare yake sannan na furta, “Addini, nagarta, Ƙyawawan ɗabi'u, kama mutuncin kai, yakana sune suka fara jan hankalina bayan aure. Aduk wanda ke gefe idan akace masa Maash abinda zai faɗa ko ya fara kawoma ransa, ko ya kallesa a bangon mujallu ko jaridu da fuskar television matsayin matashi da ake makallo da wasi-wasin dukiyarsa ko ta halak ɗin ce ko kuwa akwai wasu dabaru. Tantiri da baya jin magana, mai izza, fariyya da dukiya. Mai tsananin ɗagawa da girman kai wanda baya son arewa da mutanen yankin. Sai dai kuma sam ba haka bane, na fahimci hakanne nima a lokacin da muka kasance kusa da juna. Maimakon waɗan can halayen da ake masa kallo da ga nesa. sai naci karo da kishiyarsu a tattare da shi. Hasalima da matasanmu zasuyi koyi da halayensa da sun matuƙar ribantuwa. Mutum ne mai addini da kula da shi fiye da yanda muke zato. Yana da ilimin addinin sosai. Mutum ne mai sauƙin kai da son sauke hakkin na ƙasa da shi cikin tausayawa. Mutumun ne jarumi ba malalaci ba. Akoda yaushe ƙoƙarin neman nakansa yake ta hanyar HALAL da kuma guminsa. Sannan ba arewa bace baya so manyan arewan ne da ya kamata su jawosa jikinsu arewar ta amfanu da shine ruɓaɓɓu. Dan ta aljihunsu kawai suke yi su. Wannan nagartar tasa itace tushe kuma mafarin komai. Idan har za'aso MAZAN da basu da ko quarter ɗin waɗan nan halayen nasa shi mizai hana a so shi”. Na ƙare maganar a hankali ina mai ɗago idanuna na kallesa. Shima ɗin kallona yake, dan haka na ɗan kashe masa ido ɗaya kamar yanda yake min ina wani sassanyan murmushi. A hankali na motsa lips ɗina idanun nawa a cikin nasa na ƙarasa furta, “Dan haka shine ALJANNAR DUNIYA TA”.

Sosai hall ɗin ya kaure da tafi, yayinda dj ya saki cool music na masoya mai ratsa zukata. Shiko jikinsa kawai ya jawoni ya rungume sosai. Tare da faɗin, “NIMA ITACE ALJANNAR DUNIYA TA”.

Sake hargitsewa hall ɗin yayi kuwa. Kusan mintuna goma kafin komai ya nutsa. Aunty Mama ta cigaba da faɗin, “Nasan wasu dayawa zasu ce muda mukazo taron sabbin amarya da ango mun ƙare kuma ga tsaffin aure. To ayi haƙuri, suma wannan taro harda su. Dan nasan mutane da yawa kafin sanin Maash yayi aure sukan saka a ransu duk ranar da zata kasance ta bikinsa sai ya nema fasa Nigeria da wajenta na ban mamaki. Sai kuma komai ya faru batare da an sani ba, hakan yasa daga baya da abin ya fito wasu suka shiga ruɗani. Shiyyasa mukai amfani da wannan damar domin tabbatarma da mutane gaskiyar da suke son sani. Muhammad Awwab El-Mu'azz Maash dai mijin Samraah Abdul-wahab Gwarzo ne. Wadda akafi sani da Sam-G. Muna musu fatan alheri da zuri'a ɗayyaba tare da dawwamammen farin ciki. Yanzu zamu dawo kan angunanmu da amarensu suma. Mc bissmillah”.

Taro ya cigaba da gudana cike da birgewa da ƙayatarwa. Tarihin angwaye biyu dana amarensu sai san barka. Yayinda aka warware sautin mawaƙa da aka gayyato daga arewaci da kudancin ƙasar. Kai da kaga yanda ake zuba liƙi da manyan

kuɗaɗe zaka san bikin na girma ne. Su Alhaji Fahad babu yakana babu ɗaga ƙafa yasha rawarsa. Yayin bada cake ya tsotse lips ɗin Bahijja tsaf dan sai da ya saka a nashi bakin sannan ya bata. Lokacin da Ummie tazo tana musu liƙi su dukansu bayan an saka mata waƙarta ta girma itama Mama Balki da Hajiya Mammah biye da ita Maash da Samraah sukazo suka fara liƙeta da daloli itama. Ai tuni suma aka zo ana zuba musu nasu. Yayinda Ummie ta juyo garesu suma. Hakama Yaya Musaddiq da Fahad da amaren biyu suka fara zuba musu. Falaq da Hayatu da Jaga Hafizzullah suma ba'a barsu a baya ba. Waje dai kam sai sambarka kawai.

Duk fa wannan al'amari dake faruwa a idanun su Mom ne da tun ɗazun da suka iso taci karo da Mansion illahirin jikinta ya dakata da aiki. Sai hawaye, wani abu daya dinga yunƙuro mata a ƙirji yasa babu shiri ta bukaci shiga toilet. Toilet ɗin kusan neman gigita mata lissafi yayi, ta hau tari sai ga jini. Kuka sosai taci a bayin tana kallon jinin data tara a cikin hannunta. Ita kaɗai tasan abinda take ji a zuciyarta. Wannan wane irin al'amarine haka mai ban ruɗani. Shiyaysa tacema Ummanta bazata zo ba. Amma ta takura akan su zo kodan suga tsiyar da za'ayi. Damunta da Umma tai da knocking yasa dole ta buɗe bayan ta wanke fuskarta ta fita. Data fito ɗin ma ta samu an baje musu tarin abinci na alfarma da sai a gidan girma. Sai abinda kake so zaka ɗiba kaci, ga Halime sai dai zuba santi take ta kasa zuane ta kasa tsaye. Ashe ba'a nan abun ya tsaya ba, aka kwaso su kuma zuwa wajen nan daya ida gigita tunaninta. Harda matar shugaban ƙasa fa. Bama wannan ba, yanda aka ɗaukaki al'amari Samraah na bata mamaki da tsoro, koyaya ta motsa Maash na ankare da ita. Hakama mahaifiyarsa. Yaya Musaddiq kam duk abinda sukema ɗan su Fahad basu babbanta shi ba. Suna ɗaya ake kiransu da shi, ƙannen Maash. Ana cikin taron mahaifiyar Maash taje har inda su Samraah suke ta kamo hannunta ta dinga zagayawa da ita wajen manyan matan dake wajen suna gaisawa. Tsabar wulaƙanci tana ata gefen wata matar Minister amma ko kallonta Samraah batai ba kamar ma bata ganta ba, alhalin har haɗa ido sukai. Sai kuma can ta hangosu inda Halime take har Ummie na ɗaukar yaro ɗaya a cikin yaran suna dariya cike da nishaɗi. Akazo wajen liƙa kuɗi, Samraah da Maash fa daloli suka liƙa su. Akazo kuma aka lulluɓesu suma da liƙin. Ga kalaman da Maash ya dinga zubawa akan Samraah ɗin kansa tsaye cikin tsananin kulawa da tattali. Itama kuma ta zuba a kansa. Jitai ma gaba ɗaya idan ta cigaba da lissafin zuciyarta zata buga. Sai kawai ta tashi ta fice a hall ɗin idanunta har kamar ma basa ganin hanya da ƙyau...

Ba Mom kawai ba, acan asibiti jikin Baba prof da Hajiya ƙarama rikicewa yayi. Dan shi jijjiga ya fara kamar irin na mace mai naƙuda ya dinga taune lips suna jini kumfa na fita ta bakinsa ta hanci. Ga idanunsa ƙyam akan television. Itako Hajiya ƙarama kuka take iya ƙarfinta tana jama mahaifin nata ALLAH ya isa. Itama dai daga ƙarshe sai da doctors ɗin suka mata allurar barci.....✍

Kuce dani ina Paah□□□?.

Masoya ina ƙara gaya muku kada ku bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR ta 2024 babu ku. Dan wannan karon komai fa na musamman ne. Sabuwar Shekara, sabon zubi da babu irinsa.

GUDA DAYA:400

BIYU:700

UKU:900

HUDU: 1200

BANK NAME:KEYSTONE

BANK ACC NO:6019473875

ACC NAME:MUSAA ABDULLAH SAFIYAH

ATURA SHEDA ZUWA;09166221261

__

IDAN KATI NE KUMA MTN/VTU A BIYA DA TURA SHEDA ZUWA GA:09134848107

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din*

09033181070

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!

MARABA DA LALE GA MASOYAN ZAFAFA BIYAR□□□ALLAH YA KARA ARZIKI... ZAFAFA BIYAR NAKU NE□

ALLAH ka gafartama iyayenmu 😭□